*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

Bisimillahi Rahmanir Rahim

*001*

Ya zuba wa likitan jar fuskar shi yana binsa da kallo da manyan idaunshi waɗanda suka rine daga farin su na asali zuwa jajir har wani ruwa ne ya kwanta acikin su gaba ɗaya jijiyar dake kanshi ta miƙe, shi kanshi likitan bai iya haɗa ido dashi ba sabida yadda halittar idanun nashi ta sauya ta jirkice kai kana kallon shi kasan yana cikin tashin hankali ba ɗan kaɗan ba.
A hankali likitan ya ɗauko gorar ruwa daga cikin frij ɗin dake office ɗin shi ya ɓalle murfin ya miƙa masa, bai musa ba ya amsa ya kafa kanshi a saman gorar wadda bai ajeta ba sai da ya shanye ruwan tas! wanda gumi ya sami damar yanko masa ta kowa ce kafa ta jikinsa tamkar babu na'urar Ac acikin office ɗin.
Sai dai har lokacin idanun nashi basu sauya launi ba wani ƙaton abu ne ya zo ya tokare masa maƙoshin sa zuciyar shi tai rauni a lokacin yasan kuka ma rahma ne in da zai iya da yayi sai dai taurin dake cikin zuciyar shi irin na jaruman maza sadaukai Masu tawakkali da yarda da ƙaddara shine ya bashi damar yin dakiya acikin wannan lamari da ya kuma afkuwa a gare shi.

"Doctor kana nufin wannan karon ma nayi asarar Beby na a karo na Huɗu?"
ALIYU ya faɗa cikin Sanyi murya kamar ba tashi ba.
Doctor ya dube shi.
"Kayi haƙuri yallaɓai haka Lamarin Allah yake, Ka ɗauka haka ya tsara maka ma a wannan karon"
A hankali ya shafo tulin sumar dake kanshi wadda take a nannaɗe irin ta fulanin asali ɗinnan baƙa irin wadda tai kamar an shafa mata relacxa bai ce komai ba har wajan mintuna goma. Kafin yace.
"Muje doctor a ɗibi jinin nawa a ƙara mata ina fatan tana cikin ƙoshin lafiya?"
Likitan ya miƙe yayi gaba yana cewa.
"Har yanzu bacci take, bata riga ta tashi ba"
ALIYU bai ce komai ba yabi Likitan zuwa ɗakin ɗiban jinin sai da aka ɗibi leda uku a jikinshi sannan likitan yace masa ya kwanta a wani ɗan gado dake ɗakin dan ya sami Hutu.
A hankali ya miƙe yana rangaji yabar Ɗakin batare daya tankawa Likitan ba, a harabar rantsatstsan asibitin Kuwa Jama'a ne Burjik mafi aka sarin su ƴan uwan ALIYU ne na jini sai ƴan uwan Matar tashi.
Da sauri Musa Yaron shi ya taso ya kamo shi yana cewa.
"Sannu oga ai da ka kirani dana zo na taimaka maka"
Idanun ALIYU da suka fara rufewa ya ɗago ya dubi Musa murya a hankali yace masa.

"Musa kaini gida please"
Jikin musa na rawa ya ɗaga murya ya kwaɗawa drivern ALIYU kira wanda ya taso da sauri ya shiga cikin wata baƙar jeep wadda tsayawa faɗin tsadar tama Ɓata baki ne ya ƙaraso gaban su Musa ya taimakawa ALIYU ya shiga cikin motar ya kwantar da kanshi jikin Kujerar motar ya lumshe idanun shi driver yaja motar ƴan uwan ALIYU suna ta ɗaga mai hannu duk jikinsu a sanyaye.

Motar bata tsaya a ko ina ba sai a ƙofar gidan Shugaban kamfanin sayar da manyan motoci da ƙananu wanda ke garin kano da kuma lagos da abuja mai suna *MADAKI MOTOR'S* kuma shine mai bawa gwamnati mai ci a yanzu shawara a ɓangaran *MATASA* Ko ina ka duba pasta ce mai hoton ALIYU tun daga farkon Titin Gidan wanda ke unguwar ƙofar Na'isa,har zuwa jikin ginin gidan wanda aka rubuta *HASKEN MATASA TALLAFIN MATA DA ƘANANUN YARA*
Da gudu masu gadin gidan suka wangale ƙaton gate ɗin wanda motar da ALIYU ke ciki ta kutsa kai cikin ƙaton filin adana motocin dake gidan wanda yawan motocin wajan kaɗai in ka gani sai ka shiga ɗimuwa, Masu gadin da sauran ma'aikatan gidan tuni sun zagaye motar kowa Burin shi Yaga halin da ALIYU yake ciki sannan yayi masa jaje akan abin da ya same shi Musa ne ya taimaka mashi zuwa part ɗinshi wanda ko masu hidimar gidan basu sami Zarafin yin magana da ALIYU ɗin ba.
A hankali ya nufi haɗaɗɗan Parloun shi wanda ya gaji da haɗuwa Ko ina ƙamshi da sanyi ne ke tashi ga masu hidimar part ɗin suna ta kaiwa da komowa baya amsa gaisuwar da suke masa haka yaja ƙafafun shi da sukai masa sanyi ya haura saman shi kai tsaye bedroom ɗinshi ya nufa ya faɗa ƙaton katafaran gadon shi idanun shi ya rufe ruf yana sakin numfashi.

Gaba ɗaya masu hidimar gidan jikinsu yayi sanyi na yadda suka ga uban gidan nasu duk da bamai yawan magana bane amman sanyin shi na yau kaɗai yafi na koda yaushe.

A Ƙaton parloun ta tana ta sintiri hannunta goye a bayanta taka sa zaune ta kasa tsaye tana ta faman kiran Numbobin ALIYU bai ɗauka ba cikin sauri wata dattijuwa ta shigo parloun ta dubi Matar dake sintiri a parlon babbar macece sosai dan ta manyanta a shekaru sai dai a fuska da jiki zaka ga ba sosai shekarun nata suka fito ba sabida yadda take cikin hutu da jin daɗi Kallo ɗaya zakai mata kasan ita ce mahaifiyar ALIYU sabida yadda kamannin nasu ya fito sosai kamar tayi kaki ta tofar haka suke da ALIYU bata da jiki sosai fara ce tas kana kallonta kaga Bafulatanar asali.
"Ranki ya daɗe Alhaji ya dawo sai dai jikinsa duk a sanyaye yake wanda bamu san halin da hajiya ƙaramar take ciki ba"
A hankali Matar ta juyo ta kalli dattijuwar wadda tai saurin yin ƙasa da kanta fuska babu walwala tace.
"Nagode Hajja jeki kitchen ki ɗora mana abincin dare"
Daga haka ta Nufi ɗakinta wanda tsayawa faɗin tsaruwar sa ma ɓata baki ne Mayafi ta ɗauka ta fita daga Part ɗin nata ta nufi wanda ALIYU ya shiga Tun farkon shigowar sa Duk masu hidimar sashin ALIYU sun shiga nutsuwar su sabida ratsowar Ammi mahaifiyar ALIYU Ɓangaran sai zubewa suke suna miƙo mata gaisuwa bata amsawa hasali ma ko kallo basu ishe taba haka ta wuce babban parlon shi ta haura saman kanta tsaye ta shiga ɗakin baccin sa.

Ta ja ta tsaya a kanshi tana Mai zuba masa idanunta tsananin tausayin yaron nata na ratsa dukkan Jikinta.
"Yanzu kai ba da ban ma'aikatan gidannan sun gayan Mami bata da lafiya ba, da ba zaka gayan ba haka kuka wuce asibiti tun safe ina matsayin mahaifiyarka amman baka gaya min ba?"
Firgit!
ALIYU ya miƙe zaune yana zuba mata ido wanda har lokacin basu dawo daidai ba.
"Allah ya baki haƙuri Ammi tsananin ruɗewa ce ta saka ban gaya miki ba, Suma Ƴaƴan gidan su Mamin, ita ce ta shaida musu, Sannan Mun haɗu da Khalil a asibitin shi ya faɗawa cikin gidan Baba Madaki, yanzu haka duk mun baro su a asibitin"
Har ALIYU, ya gama maganar Ammi bata ɗauke idanunta daga kallon shiba inda abin da Ammi tafi tsana a duniya bai wuce gidan Baba Madaki ba wanda Yake gida ne na kakannin su ALIYU waɗanda suka haifi Mahaifin su, dukkan ƙannen mahaifin ALIYU  anan cikin gidan Baba Madaki gidajen su yake wanda suke a bayan gidan su ALIYU ɗin wajan galadanci Mahaifin ALIYU kaɗai ya tsallako ya fito daga cikin gidan amman dukkan sauran Ƴan uwan shi suna cikin gidanne.
Wanda Ammi sam bata shiri da Ƴan uwan mahaifin su ALIYU.
"Ka kyauta min da abin da kayi"
Ammi ta faɗi tare da barin ɗakin nashi.
ALIYU a hankali ya koma saman gadon shi ya kwanta sai Lokacin ya tuna da wayoyinshi dake wajan Musa tuni ya kashe wayoyin sabida yasan yadda mutane zasu dame shi da waya shi kuma baya son Magana a halin da yake ciki a yanzu.

Bai tashi ba sai gab da magariba ya shiga toilet ya watsa ruwa ya fito ya sanya jallabiya fara ƙal yay ɓarin turare mai kamshi sosai ya fita masallacin dake harabar gidan nasu yaɗan sami nutsuwa anan ya dinga Gaisawa da ma'aikatan gidan daga nan ya wuce part ɗin Ammi sai dai bai same ta ba wai tana asibiti cewar ƙannen shi ƴammata sajidah da safnah  daya tarar suna kallo a parlo suma dawowar su daga makaranta kenan inda suke karatu a jami'ar bayero dake kano suna lavel 2

Cikin wata ƙaramar honda civic fara ya shiga
A hankali yajata yana driving kanshi bayan ya sanya p cap ya kare fuskarshi sabida gudun idanun jama'a Masu gadi suka hangame ƙaton gate ɗin gidan ya fita da motar dandazon matasan daya gani a ƙofar gidan ne ya bashi mamaki da gudu yaja motar yabar harabar gidan yana gudun kada su gane shine cikin motar.
Cikin ƙanƙanin lokaci ya ƙarasa asibitin yay horn aka buɗe masa gate ɗin ya shiga cikin harabar asibitin yay parking motar ya fito gudu gudu sauri sauri ya shiga ɓangaran da aka kwantar da Mami matar shi Ya tura ƙofar ɗakin ya shiga ciki tana kwance har Lokacin ga ledojin ƙarin jinin da akai mata sun ƙare an cire Ammi zaune ita da Maman Mami sai ƙannen Mami ɗin duk sun yi tagumi Kallo guda zaka ma Maman Mami kaga suna
yanayin kama da Ammi kasancewar yayarta ce Mahaifin su ɗaya.
ALIYU ya tsugunna ya gaida Maman Mami wadda ta amsa mai cikin kulawa tana mai tashi ta fita daga ɗakin Ammi data masa kallo ɗaya itama tabi bayan maman mami sauran  ƙannen

Mami  miƙewa sukai suka fita ɗakin yayi saura daga ALIYU sai Mami dake kwance a saman gado.
*Idan kina buƙatar na tallata miki kayan siyarwar ki a ƙasan shafikan littafin nan kimin magana kai tsaye duk shafi 2 500 naira ne 09022260850*
*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*002*

Cikin sanyi jiki ALIYU ya ƙarasa Bakin gadon da Mami take kwance ya zauna a gefenta, Hannun shi mai taushi ya sanya ya tallafo kanta ya ɗora saman jikinshi ya zuba mata ido tsananin tausayinta ne yake ratsa masa cikin zuciyarshi wanda har yake huda dukkan sassan jikin shi.
Mami idanunta ta lumshe wanda ruwan hawaye ke ta firfitowa da gudu babu ƙaƙƙautawa a wannan karon raunin ta yafi na ko da yaushe bayyana wanda ganin hakan ya ƙara Razana Aliyu sosai ya firgita da yadda yaga ruwan hawayen dake fitowa daga idanun mami Sai dai tsabar kawai ci bai sanya ya bayyana wannan razana tasa a fili ba.

"Kiyi haƙuri Mami, wannan kukan bai da amfani"

Aliyu ya faɗa cikin tattausan lafazi.

Ta ɗago ƙwayar idanunta wadda tai jajir ta kalle shi tana mai ɗauko hannun nashi ta ɗora akan cikinta muryarta wadda ta dashe sabida tsabar kuka ita ke shiga cikin kunnen shi.

"Yayah Aliyu wannan karon ma cikina ya zube, cikin dana ƙwallafa raina akan shi cikin da nake mafarkin na haife shi....."

Sai ta kuma fashewa da kuka!
"Shitt!"
Ya ɗora yatsun sa a saman bakinta ya lumshe manyan idanun shi aran shi yana jin dama shima zai sami damar kukan daya koka dan yaji sanyi acikin zuciyar shi.

Muryar shi mai cike da taushi nagarta gami da haiba ita ke fita ƙasa ƙasa kamar yana yin raɗa, dama shi tun tuni bamai buɗe murya bane in zai yi magana.
"Mami ki shuru wannan kukan naki yana ƙara min zafi acikin zuciyata, Allah ne ya bamu ya kuma nufa bamai rayuwa bane shiyasa ya amsa mu duka haƙuri zamu yi"
Yafaɗa cikin dakiya da jarumta.

Ƙofar aka turo da sauri Mami ta sauke kanta dake jikinshi ta gyara ɗaurin ɗankwalinta Maman ta ce.

Cikin alkunya ta ƙaraso Wajan su taja kujera ta zauna wanda Aliyu yay tsam ya miƙe yana sosa kanshi.
"Aliyu sai fa haƙuri mami taƙi kwantar da hankalin ta, Ni ina ganin wannan kukan kamar harda wauta sabida ba wanda ya isa ya tsaida Allah acikin dukkan al'amuran daya riga ya saukar"

Aliyu ya saki murmushin daya fi kuka ciwo.
"Mama ki barta tai kukan May be, zata ji relief acikin zuciyarta"
Yana faɗin hakan yayi saurin barin ɗakin Ya fita waje ya sami Ammi zaune a saman kujera tana ganin shi ta miƙe.
"Bara nayi musu sallama sai mu wuce"
Daga haka ta kama handle ɗin ƙofar ta shiga Maman Mami tana ta aikin rarrashin Mami Ammi tai musu sallama ta baro ɗakin.

Ƙannen Mami cike da ladabi sukai wa Aliyu sallama, Maman Mami har wajan Mota ta biyo Ammi suna ƙara tattaunawa wanda Maman Mami sai mita take na yadda Mami duk tabi ɗaga hankalin ta.

Ammi ta shiga motar wadda Aliyu ya buɗe mata Ta zauna sosai sannan shima ya shiga Bisimillah ɗauke a bakin shi yaja motar yana ɗagawa masu gadi hannu suka buɗe masa gate ɗin ya cillah hancin motar shi titi.
Motar tayi shuru Ammi ce ta katse shurun nasu ta hanyar ce masa.

"Kadai ci abinci amman kafin ka tawo nan?"
Ya shafa kanshi kamar koda yaushe yace mata.
"A,a ina son sai nayi sallar isha'i sannan sai na ɗan haɗa coffee In sha dan ina son gobe da sassafe zan je Abuja"
Ammi tai jimm kafin tace.

"Ya Kamata ku ƙara komawa wajan wannan Likitan Na ƙasar india akan matsalar ɓarewar cikin nan na Mami ni abinnan har tsoro yake bani ace daga ta samu ciki ana murna kuma sai aga ya ɓare ba wani dalili"

Ta cikin Madubi ya dubi fuskar Ammi wadda ta bayyana da damuwa ƙarara.

Cikin nutsuwa ya furta.
"Ammi babu wata dubara da za'ai akan abin da Allah ya ƙaddara bamai rayuwa bane, wannan rubutu ne tun asali haka Allah ya ƙaddara in muna da rabo Allah zai bamu"

Ammi tana jinjina wa Aliyu ta ɓangaran tawakkali bai taɓa dangana matsalar matar shi da wani abu ba ko wancan karon ma ita ta tilasta musu fita ƙasar india akan matsalar ɓarin da matar sa

ke ta samu amman shi koda yaushe fadin sa ɗaya shine Komai muƙaddari ne daga Allah.

"Shikenan Allah ya baka wani mai albarka ya kuma inganta"
Ammi ta faɗa a hankali.

Shima a ƙasan laɓɓansa ya amsa da.
"Amin"
Motar ta ɗauki shuru titin nasarawa gidan gwamna dama ya gaji haka har suka ƙaraso cikin gari babu wanda ya kuma magana acikinsu dama shi bamai yawan magana bane yawanci shurun sa yafi maganar shi yawa shiyasa wasu ke masa kallon Miskili.

A daidai ƙofar gidan shi yayi parking wasu matane cunkus wasu da goyo wasu ma sunyi bacci akan dakalin Ƙofar gidan Ammi takai duban ta ga matan.
"Kasan dai wannan duk jama'ar kace nidai taimaka ka shigar dani sai ka fito"
Yayi lallausan murmushi ya danna Horn masu gadi suka wangale masa ƙaton gate ɗin ya tura hancin motar shi zuwa harabar adana motocin gidan yayi parking da sauri ya fito ya buɗe wa Ammi motar ta fito ya take mata baya har zuwa part ɗinta.

A parlon ya tsugunna har ƙasa ya dube ta.
"Ammi zan fita na sallami matan waje ko kina buƙatar wani abu ne?"
Ammi taji wani irin farin ciki ya nunku acikin zuciyarta ciki da kulawa tace.
"A,a kaje Allah yayi maka albarka"
Ya miƙe bai koma part ɗin shiba ƙofar Gidan ya koma Da sauri matan suka miƙe suna gaishe dashi babu ƙyama bare nuna cewar shi mai kuɗi ne ya janyo kujerar roba fara ya zauna yana facing ɗin matan.

Ta farko ce ta ƙaraso gaban shi.
"Yallaɓai tunda ga ɗorayi unguwar Bello na tako da ƙafata ina fatan Allah ya haɗani da kai mijina ne ya rasu ya barni da marayu bakwai ina sana'ar wankau yau da gobe sanyi yaci ƙarfin jikina ina ta wahalar magani ga yarana ƙananu ne, takai ta kawo bamu da abin da zamu ci"

Ya dube ta kullum a  cikin irin waɗannan al'amura yake kashe lokacinsa.
"Tom shikenan zan baki jarin da zaki sami abin da zaki dogara da kanki sabida ki taimaki yaran ki, ba zan baki kuɗin da bazaki sana'a dasu ba dan zan kashe miki zuciya kuma kinga in yau mune gobe bamu bane ba ina ganin na baki abin da zaki tsaya da ƙafafun ki yafi na baki kuɗin da zakici abinci"
Ya faɗa cikin muryarshi ta dakakkun Maza.
Nan da nan matar ta soma goge hawaye.
"Allah yayi maka albarka, Allah yasa ka gama lafiya, naje gidajen masu kuɗi yakai talatin da wannan buƙatar babu wanda ya dube ni, tabbas in da za'a sami jajurtattu irinka da yawa acikin al'ummah da tabbas bara da sace sace da maula da sun ƙare Allah yasa kafi haka"
Murmushi yayi kawai ya ɗaga mata hannu batare daya ce komai ba.
Ta biyun itama ta matso gaban shi.

"Ni kuma mijina ne, yake aikin saka roɗi agarin ɗora dakin gaba ɗaya ginin ya faɗo masa sama da shekara biyar yana kwance yana jinya duk abin da muka tara ya ƙare"
Ta faɗa tana kuka.
"Share hawayen ki Allah ya bashi lafiya"
Ya faɗa da tausayawa A hankali sauran matan keta ƙaraso wa gaban shi ko wacce da kalar tata damuwar.
Sai da ya gama dasu sannan ya miƙe ya shiga cikin gida jim kaɗan ya fito Da leda a hannun shi ko wacce sai da ya sanya wani daga cikin masu hidimar gidan ya ɗauki sunanta da kwatancenta aka rubuta akan kuɗin da zai bata Kuɗi ne masu kauri ya babbasu yace ko wacce taje ta sami sana'ar da zata tsaya da kanta.

Aliyu yasha godiya wajan matan ya miƙe da kujerar da ya zauna ya shiga cikin gidan yana mai jin farin ciki a zuciyar shi burin sa kullum ya bayar shiyasa Allah bai taɓa hana shi ba.

Yana ƙoƙarin shiga sashin sa Musa dake zaman jiran shi yasha gaban Shi yana rage tsayin sa.

"Musa mai kake har yanzu baka tafi wajan iyalin kaba?"
Musa ya shafa kai yana zaro wayoyin Aliyu daga Aljihun sa.
"Yallaɓai dama wayoyin kane a waje na"
Ya miƙa masa, sallama sukai da Musa Ya kama hanyar part ɗin shi.
Yana shiga wanka yayi ya sauya kaya zuwa singlet da boxer ya sauka ƙasa sanin ba wani ma'aikacin dazai shigo masa Parlo a wannan lokacin tunda gejin su daga magariba ne zuwa Bayan magariba sun jere musu abinci sun bar part ɗin sun koma nasu sai kuma da safe.
Ya shiga kitchen ya haɗo coffee a cup sai turiri yake yana daga tsaye ya shanye shi tas ya aje cup ɗin ya koma saman shi alwala ya ɗauro yay sallah isha'i tare da shafa'i Wuturi sai ya tashi cikin dare ya idar ya jima yana addu'a sannan ya shafa ya cire kayan jikin shi yayi saura daga shi sai dogon farin wando wanda dama baya saka riga in zai kwanta bacci ko takan wayoyin shi baibi ba ya zube su a gefen gadon shi.......*Idan kina so na tallata miki kayan sana'arki a ƙasan shafukan littafina Duk shafi biyu 500 naira kimin magana kai tsaye domin a fara tallata miki hajarki*
09022260850
*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*003*

Pillow guda ɗaya ya matse a saman ƙirjinshi bai rufa da komai ajikin shi ba, dama haka tsarin shi yake duk sanyi baya rufa idan yana bacci kuma baya sanya riga iya kacin shi dogon wando

kaɗai, baccin shi yake cikin nutsuwa sabida yadda gajiya ta zirga zirga ta kashe masa jikin sa damma namijin duniya ne wajan gwagwar mayar rayuwa.

Ammi ta ƙarasa bedroom ɗinta bata zauna ba alwala ta ɗauro ta fito daga Toilet Sadiƙ Yayan Aliyu, Aliyu shike bin sa yana zaune a Garin lagos yana kula da kamfanin ALIYU na lagos,Tare yake zaune da matar shi acan Aunty sakinah da yaran shi guda uku mata, yayi sallama cikin ɗakin nata.
Fuskarta a sake ta amsa tana cewa.
"Kaikuma zuwan dare kayi kano kamar korarre"
Sadiƙ ya shafa kai yana dariya.
"Hajiya Ammi tamu, to ki fara bani abinci naci sai muyi maganar data kawo ni"
Ammi tayi murmushi.
"Bari nai sallah tukunna sai na ji dakai"
Ta shinfiɗa darduma a nutse take sallar wadda taja lokaci mai tsayi dama Duk sun san yadda sallar Ammi take ɗaukar Lokaci Sadiƙ har sai da yakai ga yana gyangyaɗi a ƙasan carpet.
Muryar Ammi yaji.
"To sarkin bacci tashi mu fita daga falo sai kaci abincin"
Ta faɗa tana fita daga ɗakin Sadiƙ ya bita suka zube nan ƙasan carpet.
"Lah Yaya Sadiƙ yaushe ka shigo bamu sani ba?"
Cewar sajeeda wadda ta buɗe ƙofar ɗakinsu ta fito tana murnar ganin sadiƙ sabida shi mai barkwanci ne da sakewa ba irin Ya Aliyu ba mai tsare gida sam in ya shigo sashin su basa sake wa har sai ya fita.

Buɗe hannunshi yayi yana dariya yana cewa.
"Zo mana autar Ammi ina safnah?"
Da sauri sajeeda ta ƙarasa jikin Sadiƙ ya rungumeta suna dariya Muryar Bashir Ce ta karaɗe Falon shima Dariyar yake shigowarshi kenan gidan.
"Babban yaya kaine da tsohon daran nan?"
Bashir ya faɗa yana dariya.
Sadiƙ yace.
"Ina naga ta zama mai gida ya kirani ɗazu naji muryar shi babu daɗi dama kullum abu a cunkushe babu fuskar far'a"
Bashir dariya ya saki sabida yasan da wa yake yana nufin Ya Aliyu.
Ammi ma dariyar tayi tana cewa.
"Ina ruwan ubana nina rasa wannan rashin far'a na wa ya ɗebo"
Sadiƙ yayi dariya yace.
"Ammi ke ya gado danni Ammi wani bin in kika ɗaure fuska wallahi har tsoron yi miki magana nake"
Gaba ɗaya Falon dariya aka saki Ammi ta ɗauki Pillow ta jefawa Sadiƙ Ya cafe yana dariya Safna ta fito itama Tafiya tai wajan Ya Sadiƙ tana Murnar ganin shi dan shi yake iya ɗaukar duk sangartar su saɓanin Aliyu da yake cin Ubansu babu sauƙi.

Ammi ce ta miƙe ta nufi kitchen ta haɗowa sadiƙ abinci yana ci ana hira har wajan Sha ɗayan

dare Bashir ne ya fara miƙewa yayi musu sallama sabida Gobe zasu je Abuja shida Aliyu dan duba wasu motoci da aka kawo sabbi kamfanin Aliyun na can.

Su safna kuwa anga yaya sadiƙ ai sai ma miƙe ƙafa da sukai suna ta zuba masa zance kala kala suna bashi labarin makaranta shi kuma sai jansu yake yana ta sakin far'a Ammi wani irin daɗi take ji aranta gaba ɗaya ƴaƴan nata kansu a haɗe yake haka suke in sunga junan su kamar su haɗiye kansu Aliyu ne kaɗai bai da sakin fuska sai dai shi ɗin yafi dukkan Ƴaƴanta son ƴan uwanshi Kawai miskilancin sa ne da zafin zuciyarshi yasa ba'a fahimta.

Sai da sadiƙ ya sanya su Safna suka kai Kayan abincin kitchen yasha ruwa sannan yace musu su tafi su kwanta dare yayi.

Sallama sukai masa suka nufi ɗakunan kwanan su.

Falon yayi shuru daga sadiƙ sai Ammi ya gyara nutsuwar shi ya kalli Ammi sosai cikin sakewa dan Ammi bata alkunyar ɗan fari da Sadiƙ gaba ɗaya ta sake da ƴaƴanta yadda ba'a zato sabida sune sanyin idaniyarta Sune garkuwa a rayuwarta tun suna ƙananu take gwagwarmaya dasu Sabida suna ƙananu mahaifinsu ya rasu yabar mata su duka duka lokacin Sadiƙ baifi shekara goma sha biyar ba Aliyu sha Huɗu dan tsiransu da sadik shekara ɗaya ne Salma ce suke da ɗan tazara da Aliyu na kusan shekara Biyar ita lokacin tana shekara tara Bashir shekara bakwai Safna shekara huɗu sajeeda shekara Ɗaya haka Allah ya ɗauki ran mijin nata yabar mata waɗannan ƙananun ƴaƴa wannan tasa ta shaƙu da ƴaƴan nata taja su ajikinta fiye da ƙima.

"Ammi tun safe Aliyu ya kirani a waya wai Mami ta tashi tana ta zubar da Jini haka yace sunje asibiti a gigice hankalina ne yaki kwanciya shine na biyo jirgin dare nazo akan wannan batu"
Sadiƙ ya faɗa cike da nutsuwa yana fuskantar Ammi wadda ta bada dukkan nutsuwarta a tare dashi.

"Nima bai gaya min ba sai a wajan masu aiki naji, Amman dan shishshigi har ƴan cikin gidanku sun cika asibitin"
Sadiƙ ya kawar da abin da Ammi tace dan har ga Allah baya jin daɗin yadda Ammi take wa ƴan uwan mahaifin nasu.
"Ammi ni ina ganin kamata yayi kawai Aliyu ya ƙara aure, Dan wannn matsalar tayi yawa"
Ammi ta watsawa Sadiƙ wani kallo.
"Haka ya aiko ka waje na kenan? saƙo ya baka?"
Sadiƙ ya gigice dan yasan Halin Ammi inta botsare musu.
"Wallahi Ammi ko ɗaya kawai dai ni tausayi yake bani ne kinga fa tare akai mana aure dashi yanzu haka Minal shekarun ta goma a duniya kinga shima in da Allah ya bashi da tuni yana da sama da ƴaƴana"

Ammi ta dube shi.
"Sadiƙ zaku ga kamar ina takurawa Babana ne akan Lamarin auren shi, Ko ɗaya ni tsorona kada ya auro matar da zata rabamu dashi Na san Baya son Mami ko kaɗan tsananin biyayya ce ta sa ya aureta Ni kuma na haɗa shi da Mami ne sabida Duk tsiya mahaifinmu ɗaya da Mahaifiyarta Kaga Mami tamu ce bamu da matsala da ita Kuma auren su zai ƙara ƙarfin zumuncin mu da mahaifiyarta"

Sadiƙ ya sunkuyar da kanshi a ƙasa Duk wannan fa ba Masalaha bace A zuciyar shi yake faɗin haka duba da yadda Ammi take Takura Aliyu akan abubuwa da dama ko lokacin auren su ma shi direct daya kawo sakina Ammi bata musa ba Amman shi Aliyu daya kawo wata Najuwa wadda sukai B.U.K tare da ita yace ita zai aura Fafur Ammi ta rufe ido tace bata yarda ya auri Najuwa ba, Haka yace yana son wata ƴar nan galadanci itama Ammi taƙi daga haka yay fushi yace shi yama fasa auren kwata kwata katsam Ammi taje gidan Yayarta dake fagge ta kawo masa babbar ƴarta Mami tace ala dole sai ya aureta Duk da ba wani sonta yake ba amman haka ya auri yarinyar.

"Ammi Wannan fa duk ba Mafita bace, Kowa yana son yayi aure dan ya haihu shima ya sami ɗansa na kanshi tunda Mami tana da matsala wajan ɗaukar ciki yakamata abar shi ya ƙara aure wataƙil Allah ya bashi rabon a jikin wata"
Ammi ta sunkuyar da kanta ƙasa kafin tace.
"Mami yarinya ce mai ladabi ka duba dukkan Mu babu wanda bata ganin darajar shi, uwa uba mahaifiyarta ma mace ce mai son zumunci, bana son ya auro wadda zata tarwatsa mana gidannan sannan yadda matan nan suke da wankakken ido ba kowacce bace zata aure shi dan Allah wata ma dan dukiyar shi zata aure shi, Muyi addu'a  Allah ya bawa mami dan ita ce tamu Kome zata zama agidannan tamu ce ba bare ba"

Sadiƙ yabi Ammi da kallo ya kasa fahimtar maganar Ammi kawai yadai fahimci Ammi tana tsoron kada Aliyu ya auro matar da yake sone tazo ta rabasu shiyasa ta aura masa mami sabida tasan baya son mami biyayyace yake mata sannan kuma bayan haka tasan kome mami zata zama ta tace tunda ƴar yayarta ce.

Sallama yayi mata ya nufi masaukin shi ya kwanta Cike da tunani kala kala sai da Asubahi suka haɗu da Aliyu a masallaci.

Cikin barkwancin da yake jan Ya sadiƙ dashi dan in kana son kaga Aliyu ya sake sosai to Sadiƙ na wajen sabida shaƙuwar da sukai da Sadiƙ Aliyu baya Ɓoye wa Sadiƙ komai nashi kamar yadda Shima sadiƙ ɗin baya ɓoye masa tun asali basu da abokai awaje su biyu ne aminan juna wanda ko Ammi bata san wani sirrin nasu ba.

"Ah Babban yaya kaine agidan namu?"
Aliyu ya faɗa yana murmushi.
Sadiƙ yace.
"Ba dole ka ganni ba tunda kai min waya hankalina bai kwanta ba wallahi yaya mamin?"

Aliyu yayi murmushin gefen baki haka suka jera zuwa sashin Ammi a falo sukai zaman shan baƙin shayi har wajan takwas suna tare da sadiƙ Aliyu ya miƙe yaje yay wanka ya dawo cikin shirin tafiya Bashir ya fito Musa ne ya kaisu airport Bayan sunyi sallama da Sadiƙ wanda zai je ya dubo mami sai ya wuce lagos shima..........
AUTA 09022260850

*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*004*

Baƙa ce sosai irin baƙin nan mai ɗaukar ido dan fuskarta har maiƙo take yi ga wasu ƙuraje da suka cika fuskar tata ƙananu Tana da Kananun ido marasa girma da gajeran hanci ba zaka sanya ta cikin Mata masu tsananin kyawu ba Bata da tsayi sosai ƴar ƙarama ce kamar zaka hureta ta faɗi sabida ƙanƙantarta sai dai daga samanta acike take dam haka zalika ƙasanta ma ta wajan hips ɗinta a cike yake dam amman tafarar ɗaya ba zaka hango hakan ba har sai ka ƙura mata ido Tana da wani irin jiki Wanda ake ce masa karuwan Jiki mai ɓoye halittar jikin mutum, Yanayin jikinta shiya ɓoye mata shekarunta wanda tana cikin shekaru Ashirin da huɗu da haihuwa amman in ka dube ta sai kace ƴar shekaru goma sha shidda zuwa sha bakwai ce, sabida ƙanƙantarta yawanci Kawayenta basa kiran sunanta sai dai suce mata bakwaini wannan suna In taji sun gaya mata shi faɗa ake da ita sosai sabida kowa yasanta bata barin kota kwana ƴar hayaniya ce FARHA kenan wadda sunan ta na Asali shine Fatimah Ƴar gidan Malam Abubakar Mai Bulo dake Ɗandago wanda jama'a kewa gidan laƙani da gidan Cida kai ko gidan yawa sabida tsabar yawan ƴaƴan babansu Malam Abubakar mai Bulo shine tasa kowa a gidan yake fafutukar abin da zai ci dan tuni Mahaifin nasu ya sallamawa kowa ce mace nauyin kanta ita da ƴaƴanta sabida tsabar yadda nauyi da rashi yayi masa yawa Mata uku ne agidan su Farha Babar su Hadiza Nada Ƴaƴa Goma Babar su Ruƙayyah nada ƴaƴa Goma babarsu farha nada Ƴaƴa Biyar Gaba ɗaya ƴaƴan gidan su ashirin da biyar ne cif.
Malam Abubakar mai bulo mutum ne mai son ya kyautatawa iyalinshi ada sanda yana dashi anji daɗi agidanshi dan wadatar sa ma ita ce ta saka ya tara mata har uku da ƴaƴa batare daya ji wata shakka ba, sai dai yau da gobe ga girma ga nauyi yasa abubuwan suka caɓe masa hakan tasa yaja tagumi ya zubawa matan sa ido yanzu haka suke buga buga dan asirinsu ya rufu wani bin inya sa mu yakan ƙoƙarin wajan yaga ya kawo gida mai girki ta sarrafa sai dai akan Shinkafa Rabin kwano ana iya bawa hammata iska acikin gidan Musamman da Farha wadda ita bataƙi tai dambe da ɗan ƙaramin yaro akan shinkafa loma ɗaya ba, in suna faɗa akan abinci agidan tamkar basu taɓa cin abincin ba haka suke cika gidan da hayaniyar su har maƙota sai sun shigo rabo ga matan ko wacce ba haƙuri daga ana faɗan kowacce ɗanta take tare wa Malam Abubakar mai bulo ( kawu ) mutum ne mai zafi manyan ƴaƴan sa  da ike mata ne suna gama primary ya aurar dasu suma sauran ƴammatan sabida yadda zamani yazo ne da ƙyar aka

shawo kanshi ya barsu suke karatun bokon waɗanda suke duk ƙannen farha ne Don ita farha ma ta kammala karatun ta a F.c.e kano  inda ta sami diploma a ɓangaran mass communication kuma Cikin ikon Allah ta sami nasarar amsar result ɗinta wanda bata da wata matsala sabida tana da hazaƙa sosai, amman in kaga ƙannen farha sai ka rantse Yayinta ne.

Ƴaƴan ɗakin su farha Yaya sadiya tai aure Yaya Nafisa tai aure Fa'iza tai aure wadda farha take bi yanzu haka daga farha sai ƴar ƙaramar ƙanwarta mai suna ikram wadda ita ce autar umman su farha.
Suma ƴaƴan ɗakin Babarsu Hadiza wadda take itace uwar gida matanta takwas ta aurar da uku saura biyar hadiza ce Babba yanzu a ƴammatan tana shekarar ƙarshe a secondry sai ƙannanenta mata da suke tawosa sai maza samari guda biyu waɗanda suka girmewa Farha sai ƴaƴan babarsu Ruƙayya itama ta aurar da biyu yanzu haka akwai shida agabanta Ruƙayya ce Babba a ƴammatan gabanta sai sauran sai maza biyu suma samari Ɗaya ƙanin farha ɗaya yayanta  Umma mahaifiyar farha bata kai sauran matan gidan jin jiki ba sabida bata da nauyi da yawa sosai tana kuma sana'arta ta wankau sai dai yawanci kuɗin basa zama daga an samu ake kashewa Musamman Lokacin da Farha na makaranta sabida umma ce ke hidimar taimakon farha akan karatun nata wanda ta ƙwallafa rai akan sai ta karanci aikin jarida, Haka Umma ta tsaya akan karatun farha da taimakon Salim saurayin farha ɗan Abokin kawu wanda tun kafin farha ta taso Salim ke hidima da ita suna son junan su sosai Salim yana kashewa farha kuɗi sabida ɗan kwari ne anan yake sayar da atamfofi Yayi nacin ya kawo kuɗi Gidansu farha Lokacin da tagama karatu tace ya bari ta sami aiki sabida taga yadda Iyayenta mata ke shan wahala agidan su akan neman abinda zasu ci ba ason ran kawu farha ke zaune ba aure ba ga zabga zabgan ƙannenta nan duk sun taso sun cika gida yafi son ya soma aurar da ita kafin ya aurar dasu Ruƴayya waɗanda zasu kammala karatun su na secondry a wannan shekarar Kawu mutum ne mai zafi abu ƙanƙani in yaji ɗansa yayi yakan iya kullo ƙofar gida ya zane shi tas ya huce dukkan baƙin cikin talaucin sa akan ɗa bai ƙi ya karya ɗa ya aje uwar sa tai jinya ba shiyasa duk hayaniyar ƴaƴan gidan daga kawu ya shigo zakaji sunyi tsit kamar Ba Wani ɗan adam dake rayuwa acikin gidan.

Ta shirya cikin baƙar doguwar riga wadda ta yane kanta da baƙin mayafin doguwar rigar ta ɗauki jakarta bayan ta dubi ƙanwarta Ikram wadda bata fi shekaru goma ba tana zaune a saman tabarma tana shan koko.
"Ikram jeki ɗakin kawu kiwa ummammu magana ni zan fita"
Ikram ta tura baki gaba tana hararar Farha.
"Kutss ni kike harara Auta? dan ubanki ni sa'arki ce dan wa nake fafutukar fita neman aikin, idan danni da Umma ne sai mu sha ruwa mu kwanta jiya ina ba haka kikai ta mana kukan yunwa ba"

Ikram ta miƙe aguje ta fita daga ɗakin sanin halin farha na rashin haƙuri yanzu sai ta hau jibgarta.
Ummah dake ɗakin kawu taje kai masa kokon karin kumallo ita ta dubi Ikram wadda ta faɗo ɗakin tana nishi.
"Auta meye haka zaki shigo ɗakin Kawunku da gudu?"
Ikram data san halin kawu wanda ta haɗa ido dashi yana zaune saman darduma da sauri ta

koma da baya tana cewa.
"Ummah wai yaya ce zata fita shine tace in gaya miki"
Ummah ta dube ta.
"To kuma sai kin yi gudu daga ɗakin zuwa nan"
Ikram ta koma bata bawa umma amsa ba sabida yadda taga kawu na zabga mata harara.
"Nifa Hasiya na gaji har ga Allah, lamarin ku keda ƴarki ya isheni haka tace candy na barta tace cigaba da karatu na barta wai mai kuke nufi da Salim ne?"
Bai jira amsar ummah ba ya cigaba da cewa.
"Maganganu ko ina nata tashi a cikin unguwa ance cin kuɗin sa muke alhalin ba bashi ƴarmu zamuyi ba, To ni Allah ya gani kuma shaida ne ban taɓa amsar ƙwandalar yaron nan akan Fatimah ba, Hasalima sanin danai wa mahaifinsa a matsayin sa na aminina yasa naji yaron ya ƙara shiga raina amman kun kafe sai tai karatu ta gama kunce sai ta kama aiki to nikam na gaji wallahi kuna kaini bango sai dai ta nemi wani uban bani ba dan nagaji inji dana gabana ma mana haba jama'a"
Umma tai ƙasa da murya sabida ƴan laɓe dan sana'ar matan gidan ne.
"Kayi haƙuri ka ƙara mana lokaci in sha Allah daga lokacin da zaka ƙara ba zamu haura ba"
Kawu yace.
"To kice mata na bata wata guda salim ya aiko na aurar da ita inta ƙara haura hakan to ta nemi wani uban ba Habubakar ba"
Daga haka yaja rediyon shi ya kunna yabar umma riƙe da haɓa.
Tashi tai ta fita tsakar gida cin karo tai da Babarsu Hadiza wadda tai saurin Komawa da baya tana sosa kai Umma tasan labe tai musu anjima kaɗan kawu na fita zata kwaza maganar a tsakar gida yanzu shakkar kawun ce ta hana tai mata habaici.

Umma ta ƙarasa ɗakin.
"Umma ni fita zanyi sabida na gaya miki wannan ƙawar tawa tace yau yayansu yace zamu ga mutumin nan mai gidan rediyon kin san sabuwa ce tashar ana  buƙatar sabbin ma'aikata"
Ummah ta bita da kallo.
"Ke ko ɗan man leɓe da hoda ba zaki saka ba? gaki baƙa kin ɗauki baƙaƙen kaya kin lafta babu wani armashi a shigar taki..................
09022260850
*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*005*

Farha ta tura baki gaba ta cinno shi sosai nan da nan ta fara sosa ido kamar zatai kuka.
Muryarta a shaƙe ta soma magana.
"Haba umma wani irin ba armashi a shigata  nida zan je wajan neman aiki kwalliyar me zanyi,

nifa umma ba kyakykyawa bace koda nai kwalliyar ma ba kyau zata min ba nafi son fuskata a haka nidai fatana Allah yasa yau na dace dan wallahi har na gaji da zirga zirga"
Ta ƙare maganar tana langwaɓar da kanta kamar wata ƙaramar yarinya koda yake in ba Sanin shekarunta kai ba tabbas zaka ɗauka irin ƴar ƙaramar yarinyar nan ce.

Umma takai duba wajan kofin kokon data ajewa farha wanda bata shaba tace mata.
"Ga kuma kokon naki baki sha ba, kin san dai ba wani kuɗin abinci zan baki ba iyakaci na baki Kuɗin mota daga nan zuwa ƙofar nasarawa nawa zasu kaikin?"
Farha tace.
"Ki bani ɗari biyar inda canji sai na dawo miki dasu, sannan kokon nawa ki rufen inna dawo zan siyo awara wajan Babar su Ruƙayya na haɗa naci yanzu sauri nake kada na makara"
Ta kai maganar tana buɗe handbag ɗinta.
"Kinga umma bani da canji a jakar tawa ma, bari nai sauri zan duba agogo a ɗakin su Ruƙayya tunda ba waya a hannuna yanzu tunda tawa ta faɗa rijiya shikenan"

Umma ta kunce Haɓar zaninta ta ciro Tsohuwar Ɗari biyar ta miƙowa Farha tana ce mata.
"Ni gwarama da wayar taki ta faɗa rijiyar sarai kin san abin magana bayawa kawun ku kaɗan, tunda ya saka dokar hana riƙe waya gwara kin haƙura in kinyi auren kya riƙe ta sannan kuma ki sauri yau karki kai yamma dan jiya baki je Islamiyar dare ba nan yazo kamar zai kawon duka sabida faɗa kin san dai halin sa"

Farha ta rufe handbag ɗinta, Bayan ta saka Kuɗin aciki.
"Umma duk su Ruƙayya da wayoyin su nima Salim yace zai kawon in ya dawo daga lagos nina san zagon ƙasa ake min a wajan kawu ba da ban an kai mai rahoto ba ina yasan ina da wata waya Munafukan banza"
Tana faɗin haka ta sanya kanta tabar ɗakin Ummah ta bita da addu'ar nasara.
Ta ɗaga labulan Ƙofar ɗakin su Ruƙayya Tana cewa.
"Mutanan ɗakin nan suna kusa a duba min agogo?"

Babar su Ruƙayya ta Ɗago kai tana wa Farha wani kallo.
"A,a manyan ma'aikata yau kuma ina aka cillah?"
Sarai farha tasan magana ta gaya mata sabida haka sai tace.
"Alkairi muka nufa kuma dashi zamu dawo ƙarfe nawa?"
Babarsu Ruƙayya ta Cije baki tana cewa.
"Ki shigo ki duba mana sai kace ɗakin baƙon kine"
Farha ta Ƙaraso cikin ɗakin ta kalli agogon dake bangon ɗakin sannan ta ƙarasa gaban madubin Su Ruƙayya ta ɗauki Hoda ta shafa ta fesa turare, dan su Ruƙayya ƴan kwalliya ne saɓanin ita da ko hodar ma sai dai ta bi ɗakunan su ta shafa tasu dan bata da ita sabida kwalliya sam bata dame taba.

"Keko farha ko ɗan caro white ɗinnan na zamani ba zaki siya ki goga ba wannan baƙi naki har yayi yawa ki duba kaf ƴaƴan gidannan Kamannin kawun ku suka ɗauko farare tas kyawawa amman ke wallahi kamar ƴar gudun hijira nina rasa mai salim ya gani a tare dake keba Tsaho

ba keba wata cikar ƴa mace ba"
Babar su Ruƙayya kenan mai gaɓa gaɓa ita kai tsaye take Nuna ƙyashinta akan farha kuma duk maganar data fito daga bakinta haka zata faɗe ta babu batun ta tauna ta saɓanin Babar su Hadiza mace ƴar bariki sam ƙaryane ka gane inda ta dosa sai dai farha tana lura da kowacce kawai sai dai ka zauna da mutum ne da halin shi kuma ba komai bane ya tsone musu ido ba illah son da Salim yake mata suna ganin duk yafi mazan ƴaƴan su rufin asiri sai kuma karatun datai musamman wannan aiki da take nema ya tsone musu ido shiyasa ko wacce ta dage sai ƴarta tai karatu sabida suma su sami aiki in sun gama baƙin cikin su ƙiri ƙiri baya ɓuya Wanda suka haɗewa Umma kai su biyun ba'ajin kansu Gwarama ƴaƴan babu ruwansu ta wani bin amman wataran in iyayen suka zugo su haka za'aita bala'i agidan har sai kawu ya tsawatar in kuma aka shirya shikenan.

"To babar su Ruƙayya in dai kawu ne ya haife ni ai shikenan kyau kuma tunda su rukayya nada shi na bar musu suje suyi gasar shi"
Daga haka ta ɗaga labulan tabar ɗakin tana gab da kaiwa soro taci karo dasu humaira Ƙannenta ƴaƴan su babarsu rukayya suna dambe akan kwaɗan kwaki tsaki farha taja aranta tana takaicin wannan ɗabi'a ta yaran gidansu a kullum tana addu'ar Allah ya bata abin da zata wadata gidansu da Abinci.

Har takai bakin titi wannan takaici bai bar ranta ba Suke nan kullum cikin dambe akan abinci kamar wasu mayunwata har ƴan layi sun shaida su tana nan tsaye a bakin titi Allah ya bata adaidaita sukai ciniki dashi akan zai kai ta ƙofar nasarawa akan naira ɗari biyu tafiyar ba wahala sabida babu cunkoso a titi bayan ta sauka ta bashi kuɗin sa ya ciro canji ya bata layin gidan su ƙawarta shema'u ta shiga tana tafe tana sauri haka ta shiga gidansu shema'u ta tarar da ita Itama tana shiri tana ganinta ta washe baki.
"Ƴar halak yanzun nan ya gali yake maganarki dafatan dai kinzo da komai naki?"
Farha tai dariya.
"Da takarduna nake kwana fa a jaka sabida kiran kota kwana, ina mamanku?"
Shema'u tace
"Tana wajan aiki bara na masa magana sai mu tafi"
Shema'u ta faɗi tana ɗaukar mayafinta Jim kaɗan suka fito tare da Ya gali Farha ta rissuna ta gaishe dashi ya amsa yana sakin murmushi suka jera zuwa bakin titi ya samar musu adaidai ta zuwa Inda Gidan rediyon yake a titin audu baƙo way ne A bakin gate mai ɗan sahun ya sauke su suka bashi kuɗin shi, Farha ta kalli saman gate ɗin inda aka rubuta GARKUWA RADIO da manyan harufa ya gali ne agaba su kuma a bayan shi.

Haka suka shiga cikin gidan radion sun jima a zaune kafin suga Md ɗin wanda yace su shigo office ɗin shi bayan sun gaisa ya fara duban shema'u yana cewa yaga takardun nata ta miƙa mai sannan ya karɓi na Farha.
Ya jima yana duba takardun nasu kafin ya dubi Ya Gali.
"Gali kasan fa wannan tashar tamu sabuwa ce gaskiya muna buƙatar gogaggun ma'aikata waɗanda suka san kan aiki su waɗan nan yaran da alamu ma basu taɓa yin harkar ba"
Caraf farha tace.

"A,a wallahi lokacin da muke school an taɓa tura mu gidan radio kuma ba laifi mun sami gogewa a wani ɓangaran"
Md yayi murmushi kafin yace.
"To shikenan babu matsala In sha Allah gobe da safe ku dawo domin muyi muku screening, In mun sami abin da muke nema a tare daku shikenan"
Farha harda zamowa daga saman Kujerar da take zaune.
"Dan Allah ka taimaka mu sami aikin nan musammam ma ni dana ke ta zarya kaga yau zuwa na kusan uku kenan Ban sami ganin kaba, sai yau da Ya Gali yace mu tawo tare dashi"
Daga Md Har Ya Gali da shema'u dariya suka sanya mata sabida yadda tai kamar zatai kuka.
"Karki damu Fatimah Ko?"
Da sauri ta ɗaga kanta.
Sannan Managern director ɗin ya cigaba da cewa.
"Mudai fatan mu wannan tasha tamu ta sami karɓuwa ta ɗaukaka tai suna wannan shine burina"
Da sauri farha tace.
"Wallahi zamu yi iya yinmu ko kasuwa ka turani nikam zuwa zanyi"
Sosai aka ci dariyarta a wajan haka sukai sallama suka baro Office ɗinsa A bakin gate suka rabu Ya Gali ya basu kuɗin adaidaita shikuma ya tafi Inda zashi har suka rabu da shema'u dariya shema'u kewa farha sabida yadda tai ɗin kowa ya gani sai yaci dariya.
Bata damu ba ita dai burin ta Allah yasa ta sami wannan aiki haka ta wuce gida a bakin titi ta sauka ta ƙarasa Cikin layin su da ƙafa ga uwar ranar data ƙwalle sosai. *09022260850*

*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*006*

Idanunta Jajir ta shiga cikin gidansu da gudu ta suri buta tayi cikin banɗaki sai dai taja ta tsaya a ƙofar banɗakin sabida yadda ta tarar da Salima Ƴar ɗakin su Ruƙayya a saman masai tana kashi.
"Dallah ke salima ki maza ki fito kinje kin sami banɗaki kin zauna kamar ɗaki"
Cewar farha tana rawar diskon Fitsarin daya kama mata marar ta.
"Ba zata fito ɗin ba ai ba gidan Babanki bane ke ɗaya aikin banza aikin wofi Baki iska kin takura taba"
Cewar Habiba wadda take bin Ruƙayya tana bakin rariya tana wanki.
Farha dama mai jiran ƙiris juyowar da zatai ta ɗaga bokitin wankin Habiba ta zubar tare da wanka mata mari.
Wata ƙara Habiba ta saka wadda ta sanya sauran matan gidan Yowa kansu nan da nan dambe ya kaure da ƙyar aka shiga tsakaninsu.

Babarsu Ruƙayya data kama habiba masifa ta soma yi tana cewa.
"Ai ba habiba bace takar zomon haka kawai kinje yawon gantalinki kin fake da neman aiki ba nasara shine zaki huce masifar ki akan ƴata to kije Allah ya isa"

Halifa daya shigo gidan ɗan ɗakin su Ruƙayya ne shima kuma yayan farha ne a wajan uba Muzurai yahau yi yana tambayar ƙanwarsa mai akai mata take kuka! ƙarya da gaskiya Habiba take gaya masa nan da nan yayo kan farha wadda tai ɗammara da mayafinta tana girgiza jikinta Duka ya kawo mata.
Tai tsalle tayi baya tana cewa.
"Wallahi Halifa in ka taɓani sai na maka illah danni ba ƴar ɗakin ku bace shine zakuyo min taron dangi toni ɗaya ce amman gayya"
Umma ce ta fito da sauri ta kama hannun Farha sukai ɗaki Halifa na zagin farha Babarsu Ruƙayya nayi Habiba nayi dama haka al'adar ƴaƴan gidan da matan gidan take muddin ana faɗa kowa nasa yake karewa sai dai fa a wajene ƙaryarka ka taɓa guda ɗaya gaba ɗayansu sai sun rufu akanka amman acikin gida kamar zasu kashe kansu.

Huci farha take Tana faman Hawaye dama ita akwai saurin kuka in ranta yana ɓace magana ma bata iyayi har sai ta huce tukunna.
"Nace ki daina shiga sabgar yaran gidannan haka kawai ni ba zaki dinga jamin magana ba in ba dama ki wuce gidan Nafisa kawai ki kwana biyu ni bana son tashin hankali"
Farha taiwa umma shuru sai faman ajiyar zuciya take saki.
Kafin ta miƙe ta koma tsakar gidan fitsarin da yake cinta tayo ta ɗauro alwala ta dawo ɗaki.

Har lokacin Umma faɗa take ita dai ta Shige uwar ɗaka ta shinfiɗa darduma ta tayar da sallah, Kwanciyarta tai tana Jin takaicin abin da Habiba da su Halifa sukai mata.

Har wajan La'asar Umma tana leƙa ta kota tashi sabida bacci ne ya ɗauketa ba itace ta farka ba sai wajan magariba a gurguje tai sallah ta fito rumfar Umma ta tuɓe rigar dake jikinta tai saura daga ita sai under skirt taja shi saman ƙirjinta.

Umma data shigo ɗakin zata ɗauki kuka ta dubi Farha.
"Sai yanzu kika tashi? wai ba na hanaki wannan shigar banzar ba tashi kije ki saka kayan ki Kizo ki alwalar magariba ki shirin makarantar dare"
Turo bakinta tai gaba.
"Umma ni gaskiya yau ba zani dare ba sabida ban biya kuɗin wata ba, Malam Alhazai duka na zeyi a banza"
Umma tace mata.
"Bana ce zan bada kuɗin ba nidai tashi kije ki alwalar ga abincin kinan yau ko karyawa baki ba"
Tsananin tausayin umma ne ya kama Farha Umma uwa ce Jajirtacciya akan ƴaƴanta Duk wiya bata bari karatun su ita da Ikram ya salwanta saboda tace su Fa'iza basu yi ba dole ta tsaya akan su Farha Ga mazan su Fa'iza bama su ƙarfi bane duk wata fafutuka ta umma akan Ƴaƴan nata take dan wani bin har aike take bawa Farha takai musu gidajen su duk dan asirinsu ya

rufu.

Ta fita tsakar gida bayan ta sanya Hijabi ta ɗebi ruwa ta watsa ajikinta sannan tayo alwala ta koma ɗaki taci abinci Tana kammala cin abincin ta fita tsakar gida bakin Murhun da Umma ke fama da wuta duk idanunta sunyi jajir na hayaƙin itace taimakawa umma tai har wutar ta kama sannan ta soma taimakon ta da tankaɗe sabida kwana biyu Kawu ya kawo abin girki wanda umma ce keda girkin a kwana biyun.

Sai da aka kira sallar magariba sannan ta koma ɗaki Lokacin ankawo wutar nepa sallah tayi bayan ta idar tai azkar ta ɗauko Hajabin dare Ta fito taiwa Umma sallama ta fita makaranta Harta mance ma da maganar Kuɗin wata sai da ta dawo ta karɓa sannan ta koma ƙarfe tara ake taso su tana Zuwa bakin ƙofar gidansu taga Salim zaune saman Babur ɗinsa yana zaman jiranta Da murna ta dube shi.
"Yaushe ka sauka bawan Allah? bara naje na aje kur'anina na dawo"
Gida ta shiga ta aje Jakarta sannan ta shaidawa Umma salim ne ya zo Ta ɗauki tabarma ta fita Ƙofar gida a dakalin Ƙofar gida ta shinfiɗa Tabarmar Salim ya zo ya sauna ta gaishe dashi.

Fuska a sake yace mata.
"Ɗazun nan na dawo sai sauri nake nazo naga Farin ciki na!"
Dariya tai tana rufe fuska Harga Allah tana son Salim kodan yadda yake Nuna mata soyayya mai cike da kulawa da tattali.
"Nidai nayi mamaki tunda a lissafi naji kace sai kayi sati naga kuma yau kwanan ka uku"
Murmushi yayi a karo na barkatai.
"Wallahi Farha ba zan iya kaiwa wannan lokacin ba, Shiyasa na dawo ga wayarki ma nazo miki da ita"
Ya faɗa yana ɗauko ledar wayar daga aljihunsa.
"A,a Salim kabar wayar nan kaga waccan ma Kawu sai da yayi faɗa Ka ajemin idan mukai aure ka bani"
Dariya yayi harda riƙe ciki.
"Idan banda abinki in mukai aure ai wadda tafi wannan zan saya miki, Ni zan sami kawu Na bashi haƙuri Ki riƙe wayar saboda tana taimaka mana wajan jin motsin junanmu"
Fafur Farha taƙi amsar wayar kuma ta hana Salim tunkarar kawu da batun ta riƙe wayar sabida tasan Halin kawu akan hakan zai iya saɓa mata.
Hira suke mai cike da so da ƙaunar Junansu Duk kuma maganar bai wuce akan Salim yana son ya turo Iyayen shi a kawo kuɗin auren su ba sai naci yake mata yana Kwantar da kanshi shidai Allah ya ɗora masa soyayyar Farha a zuciyar shi.
"Salim ka min haƙuri Gobe wannan gidan Radion suka ce muje nasan In sha Allah akwai nasara a zuwan namu Kaga zuwa sati na sama sai Muyi maganar zuwan iyayen naka Nafi son na riƙe aikina ne a hannu sabida ina gudun na aureka kace kai baka san zancen aikin ba"
Yadda tace hakan yabi sabida baya son Ɓacin ranta lallaɓata yake yi Sun kai har wajan ƙarfe Goma suna hira kafin ya mata sallama Dubu Biyar ya bata yace tai kuɗin Mota da ƙyar ta amsa ta shiga cikin Gida.

"Fatimah nifa nagaji da wannan gantalallan zancen naki koki cewa yaron nan ya turo kona sami uban nashi da kaina ai ba baƙona bane ba"
Cewar kawu wanda ya shigo gidan yanzu.
Muryarta cikin tsoro tace.
"Ai abin da yama kawo shi kenan yace in baka haƙuri zasu magana da Baban nashi"
Ta faɗa tana Addu'ar Allah yasa kada Kawu yace ƙarya take.
"To yanzu naji batu danni bana son ai min kallon ƙaranta"
Daga haka ya haska Fitilar shi ya shiga ɗaki saboda Lokacin an ɗauke wuta.
Da sanyin Jiki ta shiga ɗaki umma tana kallonta tace.
"Kin kyauta da kika wa Babanki ƙarya dan nasan ƙarya kike Salim mai jiran ƙiris kedai ki amfani da damarki kada ta wuce ki"
Farha ta kalli umma.
"Munyi magana dashi ai cikin wani satin zasu zo"
Daga haka tai ɗaki ta aje tabarmar Kuɗin ta miƙawa umma.
Umma tabi kuɗin da kallo kamar tana tsoronsu.
"Nifa bana son yawan amsar kuɗin bawan Allan nan taimakon daya miki ma lokacin kina makaranta kaɗai Allah ya saka mai da alkairi"

"Umma tun da shi ya bani yaya zanyi gobe kinga zamu koma screening kinga na sami na zaryar Mota"
Umma ta Ɗaga Filo ta aje kuɗin farha tai Uwar ɗaka ta haye gado ta kwanta bayan tayi sallar isha'i.

*************

Maman mami ta dubi mami bayan ta raka Ammi mota.
"Dole ki kuka Mami nima Dan zuciyata a dake take ne ace sau huɗu kana samun ciki yana ɓarewa babu wani dalili, Ni babban Burina ki haihu da wannan yaro daga nan ƙaryar Hajiya Amina ta ƙare"
Ta faɗa tana cije bakin ta.
"Mama nagaji ne wallahi Nima na matsu na haihu, wallahi duk biyayyar da nakewa Ammi dan dai kawai ban haihu bane Shasha sha suke mayar dani ita da ƴaƴanta nima sai na maida kaina kamar ban san mai nakeyi ba, Amman wallahi da zarar na haihu da Aliyu duk sai na rabasu sai na soke duk wata facaka da suke da dukiyar shi Ta mayar dashi saniyar tatsa duk wata lalurarta akan sa take ƙarewa Hatta Ƴan uwan shi Dashi suke gadara Lamɓo nake musu kada taga ita ta haɗa auren mu wallahi Sabo da kaza baze hana in yanka taba"
Maman mami ta saki dariya.
"To dama mai nace miki, Cewa nai ki mayar da kanki wawiya ki nuna duk abin da yake musu bai dame ki ba har Allah ya baki Ƴaƴa da ɗanta daga nan kashinta ya bushe, Haba Amina kinyi wauta tun da muka taso Mahaifinmu ya fifitaki akaina duk da mune ƴaƴan shi kaɗai a duniya Ya so mahaifiyarki fiye da tawa, Kika fini Da miji kika fini da ƴaƴa to ni kuma nai alƙwarin sai na ƙwace Goriba a hannun yaro Wannan Aliyun da ya zama garkuwarki sai na rabaki dashi wannan shine babban Burin daya sa Nai miki kwanton Ɓauna na Haddasa Auren Mami dashi"

Maman Mami ta faɗa tana wata irin dariya ta basawa.
Mami ta saki murmushi ta koma ta kwanta aranta tana jin soyayyar Aliyu mai tsanani tare da kishin dukkan Biyayya da Hidimar da yakewa Mahaifiyar shi da ƴan uwanshi sun mai dashi kamar bai san ciwon Kuɗin shiba....... *09022260850*

*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*007*

Washe gari Farha da wuri ta shirya cikin riga da skirt na atamfa ja ta yafa baƙin mayafi ta fesa turare ta ɗauki handbag ɗinta ta dubi Umma wadda ta zuba mata ido tana kallon ta.
"Umma ni zan tafi ai min addu'a"
Umma ta dube ta da kulawa.
"Allah ya bada nasara, yau ma baki karya ɗin ba zaki tafi?"
Tai murmushi mai ƙayatarwa.
"Umma sai na dawo zan karya ɗin"
Acikin kuɗin da Salim ya bata jiya umma ta ɗauki dubu ɗaya ta bata tana mata fatan alkairi.
Ta fita tsakar gidansu batare data kalli matan gidan dake hada hadar ɗumaman tuwo da dama koko ba.

"Manyan ma'aikata sai ina?"
Cewar Babarsu Hadiza cikin sigar zolaya.
Farha data sa kanta a soro ta ɗaga murya sosai tace mata.
"Gidan nasara da sa'a na nufa in Allah Ya yarda"
Daga haka tafita daga gidan titi taje ta sami abin hawa sai da ta biya ta ɗauki shema'u sannan suka wuce.
Suna tafe suna hira inda shema'u take bata labarin da ya gali ya bata jiya na cewa ashe Gidan rediyon na wannan mutumin ne anan ya galin su ya fara aiki kafin ya bari wai kuma in dai zaka samo wa md rahoto tofa zai ta ƙara maka albashi.
Farha tai zuru kafin tace.
"Ya Allah kasa mudai muna da rabo"
Haka suka ƙarasa bakin gate ɗin bayan sun sallami mai Adaidata sahun daya ɗauko su, Suka shiga cikin gidan Rediyon zaman jiran Md ɗin sukai har wajan takwas da rabi kafin ya ƙaraso.
Da far'a ya dube su.
"A,a su fatima ne da wuri haka, Ah lallai ba zamu dinga samun matsala daku ba ku biyoni ciki"
Suka miƙe suka shiga office ɗinsa.
Zama sukai a saman kujerun office ɗin shima ya zauna sannan suka soma gaishe dashi.
Ya dube su Yana ɗaga takardun su.

"To Alhamdulillahi duk abin da nake buƙata a tare daku na samu, sai dokar gidan rediyon nan da zan faɗa muku, Bana son fashi sannan labarai na hausa da turanci ko wanne ya faɗo kanku zaku iyayi"
Duk suka bashi nutsuwar su sannan ya ɗora.
"Ni dai fatana duk inda labari yake mai daɗi wanda zai ja hankalin jama'a ina maraba dashi ku kawo mana Mu watsa tashar mu ta sami karɓuwa, Albashin ku dubu ashirin ne a wata, sannan babu taka maiman lokacin tashi ya danganta da yadda duty yazo muku wanda ake kafewa a waje kowa ya duba lokacin shi"
Farha a wannan karon ma sai da ta zube ƙasa tai masa godiya ya umarce su dasu tashi ya rakasu su zaga wajan da yakamata haka suka bishi ya nuna musu ko ina hatta ɗakin yaɗa labarai da sauran su Ma'aitan tashar basu da yawa abin har ya bawa su farha mamaki, Haka suka gaggaisa da sauran ma'aikatan sannan ya baro su anan domin suga yadda ake gudanar da aikin.
Ranar su Farha basu tashi ba sai wajan la'asar kuma ba komai sukai ba kawai ganin yadda ake labarai ne da yadda ake ɗauka da yadda ake yaɗawa Wanda kafin kace me Farha harda daɗa ganewa sosai.

A gajiye liƙis ta shiga gida wanda tana zuwa ɗakin umma ta zube Fa'iza sai dariya take mata wadda tazo gidan ta wuni Da ƙyar Farha ta miƙe tayo wanka taci abinci dama sunyi sallar su acan Da gayya ta fita tsakar gida ta leƙa ko wani ɗaki ta shaida musu ta sami aiki Sai dariyar yaƙe suke mata Haka ita dai ta koma ɗaki tana bawa su umma labari.
**********

Sadiƙ bayan ya shirya Ya nufi Ɗakin Ammi har ƙasa ya tsugunna ya gaishe da ita sannan yace mata zai je ya Dubo Mami sai ya wuce lagos dan jirgin sha biyun rana yake son yabi Ammi tayi masa fatan alkairi sukai sallama ya shiga mota drivern gidan ya kaishi asibitin da aka kwantar da Mami.
Da sallama ya shiga Ɗakin da mami take Hajiya Tajira maman mami ta saki fuska sosai tana cewa.
"Wa nake gani a cikin asibitinnan kamar Abubakar sannu da zuwa"
Sadiƙ ya zube har ƙasa yana gaida maman mami kafin ya tashi ya zauna kujerar da take kallon Mami wadda take zaune ta miƙe ƙafa tana shan tea fuskarta fayau duk ta rame.
"Sannu Mami yaya jikin ashe haka Allah ya aiko?"
Sadiƙ ya faɗa cikin jajantawa.
Mami tai ƙasa da kanta tana kallon Ƙarfen gado bata ce komai ba.
"Kiyi haƙuri kada ki sanya tunanin komai aranki In sha Allahu zaki sami wani ingantacce"
Maman mami ta karɓe zancen cikin kwantar da murya.
"Haka ne fa Abubakar nima haka nake ta gaya mata, Amman daga ita har Alin sun ɗaga wa kansu hankali musamman ma shi daya ce ya ƙagu yaga magajin shi"
Sadiƙ ya cije leɓe yana murmushi yasan wannan faɗi ne Ba yadda za'ai Aliyu ya faɗi haka amman sabida kada ya ƙaryata ta yasa yace.
"Dama ai haihuwa ita ce ribar aure Mama muma fatan da muke Allah ya bashi ɗan kanshi"
Daga haka ya miƙe ya zaro 20k daga aljihun sa ya direwa Mami yayi mata fatan Allah ya bata

lafiya ya fita yana ƙoƙarin Fita daga ward ɗin su Sajeeda suka shigo hannun su ɗauke da ƙaton Basket na Kayan Break fast ya dube su.
"Ku yanzu dan sakarci kun san zaku zo amman baku bari mun tawo tare ba?"
Dariya sukai a tare suka gaishe dashi sannan yayi musu sallama driver ya nufi airport dashi dan yayi jiran jirgin daze bi bai bari maganar Maman mami ta sami gurbi a zuciyar shiba sabida yasan mata basa rabo da kace nace shiyasa ya kawar da maganar bayan yayi wa ɗan uwan shi zato mai kyau.
Su Safna sun gaisa da Maman mami sannan sukaiwa mami sannu suka dire mata Basket ɗin sabida sauri suke suna da lecture suka bar ɗakin Mami ta bisu da harara tana jan tsaki.
"Wallahi Mama na tsani sadiƙ ɗinnan inna ganshi kamar na shaƙe shi sabida a duniya ba maganar wanda Aliyu yake ji sama data sadiƙ komai nashi ya ɗora shi akai"
Hajiya tajira tace.
"Ina sane ai na yaɓa masa magana kuma nasan ya fahimta kedai sha kurumin ki wallahi ba zamu barsu haka ba dole ma mu raba wannan alaƙar"
Mami ta kuma jan tsaki.
"Suma waɗannan ƴan iskan yaran sai iyayi da girman kan tsiya wancan satin fa wayoyi ya sai musu masu uban tsada sannan yace wai ana fara visar umarar azumi zasu tafi Wallahi mama saura kaɗan na faɗi sabida takaici kuma bara na koma nima sai an tafi dasu Hassana"
Haka suka lalace a wajan suna ƙulla sharrin su kafin Likita tazo taga jikin mami jim kaɗan tazo ta basu sallama da yake da driver nan da nan sukai Gida a maimakon ya wuce da ita gidanta sai Hajiya tajira tace su wuce Fagge inta ƙara jin ƙwari sai ta koma Basu bi takan Aliyu ba Bare a tambayi izininshi.
******

Ranar Farha ta wuni ta kwana cikin farin ciki kuma washe gari babu sanya ta fita wajan aikin ta Alhamdulillahi ta sami wani daga cikin ma'aikatan yana ƙara nuna mata komai Taji daɗin Wajan aikin nata Haka ta cigaba da Fita aikin wanda tuni ta goge har tana ƙoƙarin shiga ɗakin watsa labarai Babban Burin Farha ya cika a sati ɗayan datai a Garkuwa Radio Duk inda ka zaga Muryarta ce raurau ke fita cikin labaran Yammaci wanda duk wanda ya kunna Radiyo ya kamo tashar garkuwa zaici Karo da Muryar Fatimah Ɗandago dan sam batai amfani da Abubakar ɗin ba Dole tasa Salim ya ƙara ɗaga mata ƙafar kawo kuɗin sabida da kanta tace yaje ya bawa kawu haƙuri ta roƙe shi daya bari tai kamar wata guda da fara aikin sai ai maganar auren nasu kuma Salim bai musa ba sabida yana sonta haka yaje wajan kawu da batun wanda kawu yay faɗa amman ya ce daga wannan lokacin baze kuma ƙarawa ba damma daga wajan salim ɗinne aka sami tsaikon.

Cikin rufin asiri farha take aikin ta sabida bama kowa ne yasan ita ce fatima ɗandago ba sabida yawanci da farha aka santa Wani bin haka zataji kawu na sauraron labaranta taita dariya tana jin farin ciki sam bata da matsala a wajan aikin ta kuɗin mota kuwa wannan dubu biyar ɗin umma tace ta aje ta dinga ɗauka tana fita aikin Abu ɗaya ne ta kula a wajan aikin shine Md babu ruwan shi da ingancin labari shidai kawai a kawo masa ya ɗora a kafarshi dan Rediyon shi tai farin jini sam ba ruwan shi sabida Allah ya bashi jarabar son kuɗin tsiya sabida yasan In dai Radion shi tai suna da talla ma kaɗai zai iya biyan ma'aikatan shi.

Tana jin ƴan uwanta ma'aikata na ƙorafi da wannan matsala don zata iya jawo wa gidan rediyon barazana Ita dai da yake Allah bai sa taci karo da wata matsala ba yasa ta saki ranta Shema'u tana sashin labaran wasanni na safe ita kuma tana sashen watsa labarai na yamma wannan tasa sam bama sa haɗuwa da shema'u sabida lokacin da shema'u zata tashi ita kuma lokacin take zuwa Daga gidansu ma bata da lokacin kowa kullum tana ɗaki tana Rubuce rubucenta na labarin da aka bata wanda zata watsa shiyasa wani bin ma sai kaji Ana cigiyarta acikin gidan.
*ABUJA*

*09022260850*
*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*008*

Ya lumshe idanunshi yana shafa kwantacciyar sumar da take saman kanshi kwance yake a katafaran gadon dake cikin hotel ɗin IBETO tunda yazo garin Abuja bai sami zama ba zirga zirga yake akan ƙoƙarin ganin Motocin daya yi order daga kwatano sun shigo kamfanin shi. Wayar shi dake gefen shi ce take ringing ya lalubo ta da dogon hannunshi mai cike da gargasa ya ɗago idanunshi yana duba screen ɗin wayar AMMI sunan dake ta yawo a saman screen ɗin wayar tashi sai da ya bari ta katse sannan ya kirata.

"Assalamu alaikum Ammi ya kuke?"
Daga Ɓangaran Ammi ta ce masa.
"Lafiya lau, Nace Mami fa tana gidan su ashe da aka bata sallama can suka wuce kai ma Babana mai yasa baka leƙa sanda zaka wuce Abujan ba"

Zazzafar iska ya fesar.
"Ammi kinsan Sadiƙ yazo so mun ɗan jima dashi ne na ƙure lokacina"
Ammi tace.
"To naji yakamata Ka dawo sabida ka samu ka leƙata ta dawo ɗakinta"

Kansa a ƙasa yace.
"Dama gobe Nake son na dawo sabida ƙungiyar matasan gwale da suka gayyacen wasan ƙwallon ƙafar su, Amman shi Bashir zai zauna ne har sai anyi clearing ɗin komai"

Daga ɓangaran Ammi fatan alkairi tare da addu'ar nasara tayi masa Ya lumshe idanun shi bayan sunyi sallama da Ammi wata iskar ya kuma fesarwa.
Ya lalubi Numbern Mami.
Tana zaune a ɗaki tana shan farfesun kan rago taji wayarta tana ringing My One and only sunan

data masa saved dashi kenan shike yawo a saman screen ɗin wayarta ta kalli Ƴan biyu ƙannenta suka miƙe suka bar ɗakin Da sallama ta ɗaga wayar Muryarta a narke.

Dakakkiyar muryar shi mai cike da taushi ita ta karaɗe cikin kunnenta.
"Mamy waye ya baki izinin tafiya gida?"
Ya tahume ta.
Inda inda ta soma yi tana kame kame.
"Dama Mama ce tace na biyota sabida jikina ba ƙwari"
Aliyu yaji ranshi ya ɓaci da wannan shashancin da mami tayi.
"To ki koma gida"
Daga haka ya katse wayar shi ya cillata can saman gado ya miƙe ya nufi toilet ruwa ya sakarma kanshi kafin ya ɗauro tawul ya fito gaban dressing Mirrow yana goge Ruwan dake ɗigowa daga jikinshi.

Ya shirya cikin ƙananun Kaya Wando Nevy blue mai santsi sai riga Polo kalar wandon ya feshe jikinshi da haɗaɗɗan turare Ya ɗauki wayar shi ya fita daga ɗakin

Kai tsaye Katafaran kamfanin shi dake kan titin Ibrahim Badamasi Babangida dake garki area 11 ya nufa sukai magana da managern shi sannan ya dawo ɗakin Yau gaba ɗaya jin shi yake wani irin kasala da Buƙata Sun taru sun masa katutu shi namiji ne mai lafiya Ya fahimci yawan takurar da yakewa Mami ne yake sanya cikin dake jikinta samin matsala tun sanda Likita yayi masa bayanin nan yaji hankalin shi ya tashi Sabida shi indai zai ci zai sha tofa ba ze taɓa ganin Matarshi ya kauda idanu ba Babban abin daya ɗaga masa hankali shine yadda Likita ya bashi shawara akan cewa inda hali ya ƙara aure sabida Mami ta dinga samun sassauci daga yawan buƙatarshi Wannan bayani da likita yayi mashi tunda yakai Mami asibiti shike damun shi a tsarin shi Babu neman matan banza dan ba'a haɗa arziƙi da zina sannan kuma shi bai da ra'ayin ƙara aure to wama zai aura Dama Najuwa yaso ita kuma da Ammi taƙi Ya haƙura tuni tai aurenta Mami kuwa zaɓin Ammi ce.

Tsaki yaja lokacin daya miƙe tsaye ya shiga Toilet ya ɗauro alwalar sallar magariba anan ɗakin yayi sallah Ya jima a zaune har akai Kiran sallar isha'i Ya tashi ya gabatar yana idarwa yayi waya a kawo masa Black tea Ba'afi Minti Biyu ba yaji kwonking Ya miƙe ya amso tea ɗin wanda yake ta tururi Ya zauna saman stool yana sha Bayan ya kammala ya cire kayan jikin shi ya kwanta ba jimawa bacci yayi awon gaba dashi.

Da sassafe yayi shirin komawa kano wanda kai tsaye daga airport Gidan mai girma gwamna Driver ya wuce dashi sabida meeting ɗin da aka kirashi na gaggawa akan kawo ƙarshen zaman banza ga matasa wanda gwamnati zata bada tsarin Jari na musamman domin a taimakawa matasan.
*****

Wannan satin aka dawo da Farha tsarin labaran safe kuma cikin Hukuncin Allah an haɗesu da shema'u wanda daga farha har shema'u sunyi murna da wannan abu sai dai yadda Md ya

buƙaci su soma fita Kasuwanni da titina dan ɗauko rahoto abin baiwa Farha daɗi ba dan Yau sai ƙafarsu ce ta kawosu sabida Sunje ɗauko Rahoton faɗan daba anan warure wani ɗan daba daya Biyosu da zabira ƙafar kowace ta kaita gida Daran ranar Farha ta kasa bacci tai ta juyin gajiya ga ƙafarta tai tsami.

Umman farha data gama jin labaran ƙarfe Goman dare Wanda Mai bawa Gwamna shawara a Ɓangaran Matasa *Aliyu Audu Madaki* ya sami ganawa da gwamna a yau domin bada jari na musamman ga matasan dan kawo ƙarshen zaman banzan su wanda yace shi kanshi yana buƙatar matasan da suka kammala secondry Guda Hamsin N.c.e zuwa degree guda ɗari gaba ɗaya Ɗari da Hamsin da suzo Kamfanin shi Mai suna *MADAKI MOTORS AND SERVICES* dake kan titin lawan danbazau don a tantance su ya basu aiki a kamfanin don ya tallafa musu wajan rage zaman banza.

Kabbarar Umma ce tasa Farha ta buɗe idanunta da suka ƙanƙance sabida Gajiyar gudu.
"Umma danna mini ƙafata"
Farha ta faɗa tana hamma.
"Ke rabu dani ina jin abin alkairi ya Allah kasa wannan alkairi yazo mana gidannan Su Halifa su sami aikin kamfanin nan tunda har gyaran motoci naji ance ana yi wannan bawan Allah Ubangiji ya biya shi da gidan aljanna"
Farha da bata fahimci Komai ba tace.
"Umma keda wa haka kike ta Kabbara?"
Umma tai murmushi.
"Wallahi farha inda haka za'a sami masu kuɗi masu taimako irin wannan mai bawa gwamna shawara akan matasa da an sami ci gaba sosai naji ance shima matashi ne kuma da kuɗin sa gwamna ya ganshi dan yadda yake taimakon matasa da Kula dasu ne ma ya jawo hankalin gwamna ya haɗa tafiya dashi wanda aka ce da ƙyar ma ya yarda ya karɓi SA ɗin"

Farha bata fahimci komai ba taja Mayafin rufarta bata farka ba sai asubah tana yin sallah tai wanka ta soma shiri Ƙarfe bakwai tabar Gida Har tausayi take bawa umma a sati Biyun datai har ta ƙara ramewa ta koma ƴar firit Kullum takance Umma burina naga Kin daina wahala daga na ɗauki albashi zan baki Ki sai komai na buƙatarki.

Tare da shema'u suka ƙarasa Cikin Gidan rediyon Suna gaisawa da sauran ma'aikata Md ya aiko Kiransu.

Cikin ladabi suka gaishe dashi yana zaune, Yana cike takardu.

Ya dubi Farha.
"Fatima wani labarin Kika ji mai Fusgar hankali acikin wannan satin?"
Farha tai jimm can sai batun Data ji umma nayi jiya ya faɗo mata.
"Yallaɓai Naji Dai Maganar SA na gwamna a ɓangaran matasa wanda zai basu tallafi na Musamman wai ko a kamfanin shi Oho dai"
Md ya ɗaga waya ya kira ɗaya daga cikin Abokan aikin su farha.

Da sauri Taj ya ƙaraso suka gaisa da Md.
"Kaji abin da yake ta Yaɗuwa a gari shine batun bada aiki na kamfanin SA na gwamna a ɓangaran matasa nima naji wannan labari kuma naso daga tashar mu ya soma fita dan hakan zai calling attention ɗin jama'a zuwa tashar mu tunda hakan bai samu ba Taj ina son Mu nemo Wani labarin akan shi wanda zai Jawo hankalin Mutane zuwa tashar mu nidai suna nake so kamar yadda kuka sani"

Office ɗin yayi shuru Farha da shema'u na raba ido Taj yace.
"Gaskiya yallaɓai nidai a sanina Yadda naji ana Faɗin alkairin Madaki zai wuya ka sami wata matsala daga ɓangaranshi kuma idan har ka lalubota ƙarshe abin akanka zai ƙare dan Babban mutum ne a garin nan Kaje Ƙofar na'isa zuwa galadanci zuwa gwangwazo zuwa gudundi Mandawari gidan sarki kaga yadda matasa suke Yinsa kaga taɓa irin waɗannan akwai Bala'i"

Md yayi dariya.

"Nifa taj baka fahimta ni babu wata matsala data taɓa haɗani dashi, Hasalima a pasta kaɗai nake ganin shi kawai yadda yanzu zancen shi ya cika gari nake son na samo Koma meye da sunan shi dan nasan tashata zatai farin jini kaga daga nan zan soma amsar manyan advert a wajan mutane"

Tajjuddeen yayi shuru.
"Eh to yallaɓai yana da Special Issue amman wannan na familyn sane Naji ance bai taɓa haihuwa ba duk cikin da matarshi ta samu zubewa yake"
Jikin Md har rawa yake wajan cewa.
"Serious taj? wajan wa kaji?"
Taj yay murmushi.
"Ah Kasan Babban mutum ne shi to dole wani bin koda yana son Sirri hakan baze yuwu ba dole maganar shi ta dinga fita more especially daya soma siyasa"
Md yace
"Haka jeka taj zan nemaka"
Md ya dubi su farha bayan fitar Taj.
"Yawwa ina son ku juya wannan labarin nashi ya koma cewar Tsafi yake da duk Cikin da matar shi take samu domin yayi kuɗi"

Zufa ce ta soma karyowa daga Jikin farha da Shema'u.............
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*009*

Duk da uban raɓar na'urar A'c data ke kaɗawa a office ɗin, Hakan bai hana Gumi wanke musu Jikin suba.
Shema'u ta kalli Farha wadda take ta faman ƙifta ido kamar zata fasa ihu.
Maganar Md ce ta karaɗe Office ɗin.
"Wannan labari zai jawo hankalin Mutane zuwa wannan tashar tamu uwa uba manyan ƴan kasuwa zasu san da zamanta har ma su fara bamu manyan tallika sannan Ƴan hamayyar jam'iyarsu Suma zasu neme mu ƙila ma su ɗauki Nauyin fili na Musamman dan tattaunawa akan Harkar siyasa"

Md ya faɗa hankalinshi kwance.
"Gaskiya nidai bazan iya ba sabida taɓa Babban Mutum irinshi akwai matsala kamar yadda Taj ya faɗa Kuma ma hakan ya zama kamar Ɓata masa suna zamuyi hakan zai janyo mana babbar matsala"
Cewar shema'u wadda ta faɗa kanta tsaye Md ya ɗaga mata hannu.

"Ƙin Amincewar kowacce acikinku shine Tikitin Barinta aiki a wannan tasha kuna nufin zan ɗaukeku na baku Dubu ashirin duk wata a banza ne Jiya ma kaɗai dana tura ku ɗauko rahoto Guduwa kukai sabida haka wannan Labari dana buƙata shi nake so ku watsa Ƙin amincewa kuma kora ce Amincewa kuma Karin albashine tare da Karramawa ta musamman danna san ba ƙaramin alkairi zamu samu ba"
Ya faɗa yana girgiza ƙafafun shi Farha ta bishi da ido Duk yadda Allah ya rufa mai asiri Amman bai godewa ba yake hango abin da zai saka shi acikin matsala, Har ta ɗaga kai zata ce ita ma bazata iyaba sai ta tuna da yadda aurenta zai zo ga hidimar Kayan ɗaki wanda da wannan aikin Ita da umma suka laru domin su rufawa kansu asiri dan tasan kawu ba abin da zai Sannan matan gidansu kowa ya sawa aikinta ido idan har ta daina wannan zai basu ƙofar Yi mata habaici da dariya sannan zata jefa zargi a zuciyar umma na dalilin daya sa aka koreta tasan kota faɗi dalili ba lallai a yadda.

"Yallaɓai zanyi ni zan iya"
Ta faɗa Muryarta na rawa.
Md ya washe baki yana cewa

"Yawwa ƴar gari To shikenan Gobe zamu fitar da tsarin Komai Yau na sallameki da wuri tafi gida ke kuma ga takardun kinan kada ki kuma dawo min Tasha"
Yana faɗin haka ya miƙe ya watsowa shema'u takardunta yabar Office Ɗin Shema'u ta ɗebe su ta zuba a jaka ta Miƙe tana bala'i
"Dama irin kune kuke ɓatawa ƴan jarida suna kuma in sha Allah wannan labari sai ya wargaza maka farin cikin ka, kawai dan biyan buƙatar kanka zaka ɓatawa Bawan Allah suna mutum mai taimako mai tausayi Allah baze baka nasara ba"

Tana gama faɗin haka ta fice Sauran ma'aikata na mata magana suna tambayarta ƙanwar Gali mai ya faru tai musu banza Ta tari Abin hawa da ƙyar Farha ta cimmata suka shiga adaidaita zuwa gida.

"Ke yanzu Farha akan abin da bai taka kara ya karya ba zaki zaɓi abin da zai ja miki matsala dan wallahi ƙarshenta ta rufta dake, Ki zauna ki karatun ta nutsu shi Md mai kuɗi ne ƙila ma ya ɗauke iyalinshi subar ƙasar ke kuwa fa? baki da tsuntsu baki da tarko wagairahun Ai a kano"

Farha tai murmushi.
"Shema'u baza ki gane ba nidai Allah yasa hakan ya zama alkairi Md ya ƙara min kuɗin nan dan na kashe matsalolin gabana"

Shema'u ta mata wani sakaran kallo kafin tace.
"Farha kenan mai yasa mu mutane muke da son kammu ne? kin zaɓi ki ɓatawa wanda nauyin sama da al'umma dubu suke ci a ƙasan shi dan ki kauda matsalar gabanki? kin zaɓi ƙuntata zuciyar wanda yake taimako domin Allah dan ki kauda taki matsalar lallai kin taro faɗan da baki da ƴan wasa Allah ya baki sa'a"
Duk wannan Maganganu na Shema'u basu saka farha taji wata karaya akan Ƙudirinta ba haka ta rufe ido tana Tunanin yadda zata kaya gobe.

Ba yadda shema'u batayi da farha ba akan ta janye amman taƙi daga ƙarshe haka suka rabu baram baram Farha a zuciye ta shiga gida Sabida yadda shema'u ta gaggaya mata magana har tana ce mata Shi mai kuɗi ne zai iya sawa a ɗaure kaf Familyn su Farhan.

Tana shiga cikin gidan ta tarar da su Umma a tsakar gida kowa farin ciki yake ta aje Handbag ɗinta ta nufi randa ta ɗibi ruwa ta kafa kai tana sha.
"Farha kinga Allah ya karɓi addu'ata Yau dai su Halifa sun sami aiki a kamfanin SA ɗin jiya"
Gaban farha ya faɗi tai murmushin dole tai Musu fatan alkairi ta wuce ɗaki.

Yau gidansu Farha gwanin sha'awa su Halifa anƙi fita konan da can suna gida ana taya su Murna Shi Halifa yana ɓangaran gyaran motoci Nura kuma sune masu Duba motocin da suka shigo da waɗanda suka fita dama an gama karatu ba aikin yi Ga zafin talauci ga Samartaka Wannan samun aikin Nasu Yayi wa kowa na gidan Daɗi hatta kawu sai da ya shiwa SA ɗin gwamna Albarka Abin daɗin Kuma shine Kowani ɗan ɗaki ya samu aikin Halifa ɗan ɗakin su Ruƙayya Nura kuma ɗan Ɗakin su Hadiza ita dama Umman Farha bata da ɗa namiji amman harta fi Iyayen yaran murnar samun aikin nasu.

Gaba ɗaya Farha jitai bata da sukuni Taƙi sakin Jikinta a gida sai faman Juyi take a saman gado Ko tsakar gida taƙi fitowa duk Murnar da ake agidan tana ɗaki a ƙunshe har magariba.

"Wai Farha meke damunki kada kija ace kina baƙin cikin samun aikin su Halifa kinsan halin Gidannan ba'a raina magana"

Farha taja Abin da ta rufe Jikinta dashi.
"Umma bana jin daɗin Jikina ne"
Umma ta dube ta da kulawa sosai.
"Allah yasa ba ciwon marar ki bane zai tashi ba, ga ba kuɗi a hannuna"
Farha ta dubi umma
"A,a lokaci bai yiba kuma ina neman sauƙi wajan Allah"
Ranar Ko makarantar dare ma bata jeba Umma kuwa yau hirar tsakar gida ce ta Ruɗe a gidan wanda Halifa ya baje yana ta basu labarin Yadda Mai Kamfanin Madaki Motors ɗin ya karramasu Kuma da kanshi ya Duba takardun kowanne acikinsu ya kuma raba musu aiki da albashi mai tsoka Halifa ya ƙara da cewa.

"Ai wallahi sanda naji labaran jiya ko bacci banyi ba Muna tashi Da asubah muka tafi Sai wajan azahar layi yazo kammu Mutum Ɗari da hamsin ya nema amman Mutum yakai Dubu da sukaje lallai ana zaman banza a garin nan"
Babarsu Ruƙayya tace.
"Allah dai yayi masa albarka yadda ya fitar damu daga takaicin rayuwa shima Allah ya yaye masa dukkan matsalolin shi"

Babarsu Hadiza tai caraf tace.
"Tab su masu kuɗi ina suka ga matsala zasu sha madara suci kaji Kai dai talaka mai neman na masara kaike da matsala"

Halifa yayi dariya sannan yace.
"Tab yadda naji fa ance bai taɓa haihuwa ba Mama ke kin ganshi kamar shi yayi kanshi dan kyau yadda kika ga Tumatur sabida ja wallahi ban taɓa ganin Mutum mai kyau irin nashi ba Kamar ka taɓa jini ya fito"
Ya ƙare yana kallon Babarsu.
Babarsu Ruƙayya tace.
"Lallai duk wadda Allah yasa ta haihu dashi ta girmi talauci Allah ya bashi ɗan kanshi"
Ire iren waɗannan hirar sukai tayi har kawu ya shigo shima ya saka baki ranar gidan dai ya wanzu cikin farin ciki ita kam Farha bata san wainar da suke toyawa ba haka tai kwanciyar bacci mai nauyi yayi gaba da ita.

***********

Ammi ta dubi Aliyu wanda shigowar shi kenan Falon nata dan tunda yazo bai sami damar zuwa wajanta ba, Yaje gidan gwamna yau kuma ya ɗebi ƙananun ma'aikata a kamfanin shi dan ko wajan wasan ƙwallon ƙafar matasan gwale bai jeba sai saƙo ya bawa musa yakai musu.

"Sannu babana mai za'a kawo maka?"
Ammi ta faɗa da kulawa.
"Ammi ni yanzu bazan iya cin komai ba dare yayi adai haɗo min Baƙin shayi kaɗai ma is ok"

Ammi ta kalli Sajeeda da duk ta shiga taitayin ta ganin dodonsu ya shigo falon.
"Auta maza haɗowa Hammanki shayi a ƙananun Kofuna"
Ya turɓune fuska.

"Ammi kinsan bani son yarannan na taɓa abu kina bani"

Ammi ta kama haɓa tana dariya.
"To sarkin tsafta na manta ne ai, Bara na haɗo ma da kaina, Niko nace yaya Kaje ka dubo Mami kuwa? ɗazu na kira yaya tajirar ma bata ɗauka ba ina ga bata kusa da wayar tata ne"

Wanni kallo ya watsawa Sajeeda ba shiri ta Miƙe har tana haɗawa da Gudu tabar falon.

Kafin yaɗan kalli Ammi............

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*10*

Ya fesar da zazzafan huci murya can cikin ƙasan maƙoshi ya furta.
"Ammi tun ina Abuja nai mata waya bata dawo ba kenan?"
Ammi ta bishi da kallon mamaki.
"Ban gane bata dawo ba kenan? kai da kuke haɗe waje ɗaya tayaya zaka zo kana tambayata"
Ya saki wani Miskilin Murmushi sannan yace.
"Ammi ai ban sani ba ko anan ta kwana tunda ni banbi takanta ba bacci yasha kaina jiya yau kuma tun sassafe nabar gidan"
Ammi bata Masa magana ba sai da taje Kitchen ta haɗo masa haɗaɗɗan Baƙin shayi wanda yaji citta da na'a na'a sai ƙamshi yake ta ɗora ƴar Butar shayin a saman tray sannan ta jero ƙananun Kofuna a gefe ta nufo Parloun dasu a hannunta.

Da sauri ya miƙe ya karɓi tray ɗin yana cewa.
"Sannu Ammi"
Ya janyo center table ya ɗora tray ɗin akanshi.

Ya koma ya zauna a saman kujerar da take facing ɗin wadda Ammi take zaune akanta.

"Wannan wace irin magana kake Babana? yanzu ace kai kana a matsayin Mijinta ka kasa leƙawa ɗakinta har ka kwana ka wuni agidan amman baka san ko ta dawo ba ko bata dawo ba?"
Ya ɗaga butar shayin ya tsiyaya a kofi sai faman turiri yake yi da zafin da komai yake kurɓa yana lumshe ido zafin na ratsa mai ɓargon Jikinshi.

"Ammi kimin uziri jiya ban shigo ba sai 12 na dare bayan na gama meeting da mai girma gwamna na shiga gidan Radio mun gana da Ƴan jarida, yau kuma kinga shigowata kenan yanzun nan nai sallar isha'i sai yanzu na sami kaina duba ƙarfe kusan goma da wani abu"

Ya faɗa yana ƙara tsiyayar shayin.
"Kaga irin abin da nake nuna maka wannan shine yake ƙara sanyawa nake ƙaunar mami har raina, Sabida ba kowace mace bace zata jure auren irinku sam baka da lokacin kanka, Yarinyar nan bata taɓa ƙorafi ba wallahi bata taɓa kawomin, Ƙarar kaba Kaga Tana gadon asibiti haka fa ka tsallake ka tafi Abuja Bana jin ka dubo ta yanzu kamata yayi kaje ka duba lafiyarta sai ku tawo tare"

Ya lumshe idanu yana sauraran Ammi harta gama maganar tata.
"Ammi tun ina can na mata waya ta dawo tunda bata dawo ba a rabu da ita May be hutawa take, Nidai nasan duk wani haƙƙi ina ƙoƙarin saukewa"
Ammi tabi sa da kallo yana da kafiya duk abin da yace zeyi to baya fasawa.

"Dalilin haka Ammi nake son na ƙara aure Kin san Bahaushe yace mai Mata ɗaya Aminin gwauro, bada ban kin gayan bata nan ba ni kam bamma san bata dawo ba"
Ya faɗa yana murmushi dan tsokanar Ammi yayi da batun zai ƙara aure Aiko nan da nan ta haɗe girar sama data ƙasa.
"Idan ma sabida haihuwa kake son ƙara aure in ka kwantar da hankalin ka kwana nawa ne matarka ta sake samun wani, Tunda Zaku fita India a duba matsalar yawan ɓarewar Cikin nata, kuma nan ma na saka ana ta addu'a kayi haƙuri kada ka ƙara aure sabida ina tsoron matan wannan zamani ba kowace mace bace zata aure ka dan Allah wata ma Da burin ta wargaza gidannan zata shigo ita kuwa mami duk tsiya tamu ce matar Rufin asiri ce duk abin da kake mana bata taɓa ɗaga ido ta duba hakan da suffar baƙin Ciki ba ina burin Allah ya albarkace ka da samun zuri'a daga Mami sabida nagartarta"

Ya jinjina kai duk maganganun Ammi haka suke shima kanshi yana mamakin Mami sam bata da matsala Haƙurinta har yayi yawa tundaga kan Ƴan uwanshi Har zuwa kan Ma'aikatan gidan suna yabonta Duk yadda zai Buzance mata yayi mata masifa inta masa laifi bata ko duban sa haka Duk nacin sa wajan Buƙatar aure bata raki Bare Ta ƙosa.

"Ammi mai ƴa nima dama wasa nake ni yanzu Ɗayar ma Bani da lokacinta bare har Biyu, Ina naga Lokacin ma duba matar Ina nan dai ina addu'a Allah ya bamu ingantacce ƙarshan watan nan ma doctor yace za'a mata ɗaurin mahaifa wanda yace In sha Allah Da zarar an kwance Kuma mahaifarta zata iya ɗaukar Ciki"

Ammi ta washe baki cike da farin ciki tace.
"Allahu yasa Ya Rabbi ya nunan wannan rana, Babana a yanzu ba abin da zance wa Allah sai godiya duk wata ni'ima yayi Min ita Burina naga Ɗanka Ko ƴarka A duniya yadda na matsu da wannan burin ban matsu naga auren su Bashir ba, Wallahi bada ban sharrin matan wannan zamani ba dani dakai na zan Ƙara nema maka wani auren a karo na biyu ko Allah yasa a dace, To Ina tsoron Sharrin matan wannan zamani Kuma sannan Mami ba juya bace Ɓari ne kaɗai matsalar ta shima Allah zai daidaita Gata ƴar uwarka ta jini gata da kyawu da biyayya Ni banga aibun taba Sabida haka ka ƙara damƙe matarka Koda wasa bana son ka kuma min maganar ƙarin wani aure"

Aliyu yayi Murmushi ya rasa mai Yasa Amminsa ke masifar son Mami wata irin soyayya Ammi kewa Mami sosai, Sannan yana ganin tsoro a fuskar Ammi ƙarara duk sanda yace zai ƙara aure Kullum batun ta akan hakan shine tana tsoron sharrin matan wannan zamani amman mami ita tata ce tasan ba tada Matsala.

Ya miƙe yana zube dukkan hannayen shi cikin aljihun Farar shaddar Jikin shi "Ammi ni zan kwanta mu kwan lafiya"
Daga haka ya juya yabar Ɗakin Ammi ta bishi da kallon tausayi Duk kawaicin sa wannan karon ya shiga damuwar Ɓarin Mami.

Koda ya koma ɗaki Shafa'i yayi ya kwanta ko kallon wayar shi da Mami ke faman Kira baiyi ba Daga ƙarshe ma kasheta yayi inta matsu dan kanta ta dawo shikam baze Je ba.
***********

Sukuku Farha ta miƙe yau har umma na ce mata ko ba zata aikin bane jiki ba ƙwari ta Shirya tai sallama da Umma ta fita Gabanta tun Jiya yake faɗuwa Haka ta ƙarasa Tashar tasu Md ya tareta da Murna yau har ɗakin yaɗa labarai ya rakata yana ƙara bata Hope akan Labarin da zata watsa a safiyar yau Ɗin.

Bayan sunyi sallama da Md ta duba doguwar takardar daya Miƙo mata sunan SA na gwamman a ɓangaran Matasa ne ya fita ɓaro ɓaro Jikin takardar.
Murya ta gyara bayan ta maƙala headphone  tare da sanya ƴar ƙaramar loudspeaker a bakin ta

Cikin zaƙin Muryarta sautin maganarta ke Fita.
_Barkam mu da safiyar laraba ga labaran namu daki daki karku manta kuna tare da tauraruwar tasharku mai farin Jini GARKUWA RADIO mita goma da ɗigo tara, Da farko zamu fara leƙawa sashin siyasar Kano, zakuji cewa mai bawa gwamnatin jaha shawara ta musamman a ɓangaran matasa Alhaji Aliyu Audu Madaki, Wanda ya Ƙware a fanni bada tallafi taimakon yara mata marayu matasa wanda sunan shi yayi fice tun ma kafin gwamnatin ta bashi Muƙami, Ya ƙara rasa cikin da matarshi ke samu a karo na Huɗu nasan dai mai sauraro zai mamaki tare da aljabin yadda duk cikin da mai ɗakin mai bawa gwamnan shawara take samu yake ɓare wa, To

ba abin mamaki bane in ka duba yadda yake shiga da fice da facaka da dukiya wadda wata majiya mai tushe ta tabbatar da Yadda yake salwantar da cikin matar tashi ne ta hanyar bawa matsafa Yaƴan cikin domin ai masa tsafi Kuɗinsa ya ƙara hauhawa wanda hakan shine maƙasudin arziƙinsa,wannan kenan sai kuma ɓangaran wutar lantarki wadda ta wadata acikin wannan jaha kada ku manta kuna sauraran wannan labarine daga wannan tasha tamu mai farin Jini dan kawo tallanku ko Gayyatar taron suna biki kuna iya ziyartarmu a shafikanmu na Facebook Ko adireshin mu dake Kan titin audu baƙo way_
Farha ta ƙarasa bayan ta yarfe zufar data wanke mata Jikinta kowa na ɗakin watsa labaran kallonta yake Jiki ba ƙarfi ta ɗauki jakarta kanta ciwo yake mata sai da ta gama labaran ma ta mance Ko sunanta bata faɗa ba Ga wata nadama na Cin zuciyarta.

Ko Bitakan Office Ɗin Md batai ba tayi hanyar titi sabida yadda idanunta ke Lumshewa.

Haka ta koma gida zuwa rana zazzaɓi mai zafi ya rufeta har haɗe haƙora takeyi.

Daga cikin garin kano duk wanda ya saurari labaran safiya na tashar Garkuwa yaji wannan ƙazafi da akaiwa Hasken matasa wasu sun yarda wasu sun ƙaryata kafin kace me labari ya cika gari Ƙofar Gidan Aliyu ya cika dam da matasa waɗanda suka zagaye Gidan domin bashi kariya koda wasu zasu yo zanga zanga dan barazana gare shi, Matasan Ƙofar na'isa kuwa Tuni sunyi zuga zuwa Gidan Radion garkuwa wasu da kalanzir wasu da ashana da taya Ba wata Sanya suka cinnawa Gidan Radion wuta wanda da ƙyar ma'aikatan suka sha Zuwa wani Lokaci gari ya ruɗe ƴan sanda sun cika titina sabida zanga zangar matasa waɗanda suka Fito suka nuna ƙin Goyon bayansu akan wannan ƙazafi da akaiwa Aliyu.
MD da gudawa ya ƙarasa gidanshi ya kasa zaune ya kasa tsaye tsoro nadama suke cin zuciyar shi yasan Ba Aliyu ba hatta ƙungiyar ƴan jaridu ta ƙasa sai ta tuhume shi akan wannan labari da tashar shi ta fitar sabida doka ce ga duk gidan Rediyon da bai tace labari ya tabbatar da ingancin shiba kafin ya fitar dashi, ga shinan son zuciya da bala'in Neman suna yaja masa bala'in da bai san Lokacin fitar shiba.

A guje Ammi ta nufi sashin Aliyu wanda duk ma'aikatan Sashin nasa sunyi cirko cirko wasu ma kuka suke sabida zuwa wannan Lokacin kowa yaji abin da ke faruwa.

Ta ƙarasa falon Musa na durƙushe agaban shi ga sautin maganar mai labaran nan raurau ya karaɗe Falon wanda Musa ya ɗauki Recording ya kunnawa Aliyu.............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*11*

Zagaye Ƙaton Parloun shi yake hannun shi Goye a bayan shi Sam ba zaka fahimci inda Halin da yake ciki ya dosa ba Idanun shi ya rintse Har yanzu sautin Muryar yarinyar da take Labaran bai bar amsa kuwa acikin Dodon Kunnen shiba.

"Iya sanina bani da abokin faɗa a Wajan sana'ata Bani da Abokin Gaba bani da wanda na taɓa Musayar Harshe dashi a ko ina Why zaku Min haka mai nayi Muku zaku ɓata min suna a idanun al'ummah idan wasu sun yarda wasu ba zasu yarda Ba"

Da sauri ya Zube a gaban Ammi wadda ta tallafe haɓa da hannunta hawaye nabin Idanunta. Ya kamo ƙafafunta ya ɗora kanshi akansu.
"Ammi ki yarda dani wallahi bani da Hannu a zubewar Cikin Mami, Arziƙi Allah ne yayi Minshi nima ina mamakin Yadda duk abin da na taɓa sai Allah ya saka mai nasibi Ke shaida ce ammi kinsan yadda Muka taso"
Yana fara maganar Muryarshi ta shaƙe ya soma tari da gudu Ammi Ta buɗe Frij ta ɗauko ruwa ta ɓalle Gorar ta fara bashi Musa na masa sannu.

"Nina haife ka Nina san waye kai Allah ya tsareka daga dukkan wanda ya nufoka da sharri Allah ya kare ka daga dukkan sharri"
Ammi ta faɗa cikin kuka.

Da gudu ɗaya daga cikin masu gadin Gidan ya shigo falon Ammi ta zaro ido tana cewa.
"Sun shigo su kashe min shi ko? ku taimaka Ku Ɓoye min shi kada a far masa"
Mai gadin yayi Murmushi.
"Hajiya ku godewa Allah, Haƙiƙa baka Alkairi ka taɓe kamar yadda baka sharri ka gama lafiya, Dama zaki fito waje da sai Kin mayar da kukan ki Dariya sabida Ilahirin matasan Dake garinnan sunyi dafifi a ƙofar Gidannan domin bawa mai gida kariya, Yanzu haka mai girma gwamna ya turo da Motocin Ƴan sanda kusan Goma suna nan tsaye da Bindigu domin su bawa wannan Bawan Allah kariya Sannan matasan gari sun Je sun ƙona gidan Radion yanzu haka neman Mai gidan Radion suke ruwa a jallo dan dai basu sami Mutum Ko ɗaya bane daga cikin ma'aikatan sabida kowa ya gudu"

Ammi ta sauke ajiyar zuciya tana shafa kan Aliyu wanda ya kwantar dashi akan cinyarta.
Ya kasa magana Har Ammi ta sallami su Musa Falon yayi saura daga shi sai ita.
"Ka ɗauka hakan wata nasara ce daga Allah in sha Allah hakan ba ze zama sharri gareka ba sai Alkairi kuma bana son kai fushi ka daina taimako wannan ma ya zama ƙara ƙarfin ka wajan taimakon al'umma domin kaga ranar hakan da idanunka inda baka taimako da bamu san yadda abin zai zama ba, amman albarkacin al'ummar Annabi gashi kana ta samu kariya"
Aliyu yaƙi magana sabida zuciyarshi yadda take a karye ta yaya za'a ce shike salwantar da Cikin Mami dan ya ƙara arziƙi ta yaya za'a dangana dukiyar shi data tsafi shida ya sha wahala

kafin ya tarata.

Duk yadda ake kiranshi a waya ya kasa ɗagawa Ta ya sadik kaɗai ya ɗaga data bashir waɗanda suka ɗaga hankalinsu akan Labarin da suka ji ya tabbatar Musu da cewa yana lafiya ya kashe wayar sai ta mai girma gwamna wanda ya bashi haƙuri yace kada ya saka abin aranshi hakan ma matakin nasara ce Kuma gwamnati zata ɗauki mataki akan shugaban Gidan radion dan zata binciko shi harma wadda tai labaran.

Bayan ya gama jin jawabin gwamna yayi godiya sai dai yace wa gwamna yabar Batun tuhumar mai gidan Radion shida kanshi zai Bibiyi Lamarin dan ya ɗauki matakin daya dace sosai sukai magana da gwamna kafin yayi masa sallama bayan yace ga Jami'an tsaro nan ya Turo masa dan su kare lafiyar shi data iyalin shi yayi Godiya ya katse wayar.

Yawan ƴan jaridar dake ƙofar Gidan  ya kai ya kawo dan ƴan jarida kamar su fasa gidan su shiga su ɗauko rahoto haka suka taru ga jama'a kota ina wannan tasa aka rufo gidan ma gaba ɗaya ya zama ba shiga ba fita daga gidan Madaki ma sosai ƴan uwan su Aliyu suka girgiza nan da nan Baba Usman Kanin Mahaifin Aliyu ya saka malamai aka hau sauke alkur'ani mai girma.

Mami kuka take tana kiran layin Aliyu dan hankalinta gaba ɗaya yana kanshi Ko kaɗan bata yarda da wannan labari ba sabida tasan waye Mijinta har ya fita damuwa akan asarar Cikin da suke yi Suma gidansu Mami sai rufe Ƙofa sukai sabida Yadda jama'a ke dafifin shigowa jaje.

Yana rangaji ya miƙe da sauri Ammi ta taimaka masa ya haye saman shi ya faɗa saman gado yana Lumshe idanunshi Ammi ta rufo masa ƙofar Ta nufi sashin sa da ƙyar ta rarrashi su sajeeda waɗanda suke Kukan abin da aka wa yayan nasu.

Wayar shi dake Ringing a karo na ba adadi ya laluba ya ɗaga Muryar mami ke sauka cikin kunnen shi.
"Yaya dafatan kana lafiya? wallahi ni na yarda dakai Mijina sabida haka ka kwantar da hankalin ka wannan shiri ne na maƙiya"
Da.
"Umm"
Ya amsa mata ya kashe wayar yayi shuru yana sauraran Bugun zuciyar shi.

Ƴan jarida da sauran jama'a gajiya sukai suka bar ƙofar gidan har zuwa dare ba aji ɗuriyar shiba amman an tabbatar yana cikin Ƙoshin lafiya dama shi haka tsarin sa yake in yana cikin damuwa shuru yake In yana cikin ɓacin rai shuru yake ya killace kanshi wannan tasa Ammi bata sake komawa wajan shi ba tasan yana tunanin mafita ne na wannan matsala data afko masa.

***********

Gaban Farha ne ya faɗi sanda taji kawu na Allah wadai da Wannan tasha ta garkuwa wadda ta

ɓata sunan Aliyu Matan gidansu kuwa masifa suke suna kumfar bakin cewa baƙin ciki ne yasa akai masa sharrin ba wani abu ba Ƙara jan abin rufa tai tana Sakin Hamdala da Allah yasa babu wanda yasan a tashar take aiki kuma ba sunanta a labarin sannan bata can aka ƙona gidan rediyon kamar yadda taji labarin a tsakar Gida cewa an ƙona gidan rediyon.
Damuwar ta ɗaya wannan sharrin data ja gaba wajan yaɗawa Ina zata sami wannan bawan Allah ta roƙe shi gafara tsananin tsoro da damuwa sune suka ƙara haddasa mata zazzafan zazzaɓi zuwa dare Jikin Farha ya ƙara rikice wa wanda hatta Ƴan gidansu sun tsorata dan kuka take tana cewa umma ta yafe mata mutuwa zatai Duk zafin kawu sai da ya ruɗe Salim ne ya kirawo Nurse aka saka mata ruwa aka mata Allura Wanda bacci yayi awon gaba da ita.

***********

Daran ranar Aliyu bai bacci ba yadda yaga dare haka yaga rana, Ba abin da yake sai sallah yana ƙara neman gafarar Allah akan dukkan laifukan sa tare da neman tsari da kariya daga dukkan sharri sai da yayi sallar asubah sannan ya sami bacci Karfe goma ya farka ba laifi ya sami nutsuwa sosai harya fito Parlou yana amsa jajen ma'aikata yana kuma ɗaga wayar mutanen sa masu yi masa jaje.
Ƙarfe sha ɗayan safe Musa ya ƙaraso Parlon nashi bayan sun gaisa ya dubi Musa........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*12*

Muryar shi a kausashe wadda ta nuna zallar Ɓacin ran daya kwana dashi.
"Musa ina son lallai a yau ka gano min  inda mai gidan radio ɗinnan yake inda hali katafi da jami'an tsaro cikin fararen kaya, su Kama min shi tabbas sai ya gaya min meye nufin shi akaina zan nuna masa ni ɗin wanene in aka shiga gona ta"
Ya faɗa yana fesar da numfashi mai ƙarfi.
"Sannan ita ma yarinyar datai labaran lallai ina son sanin wacece"
Ya faɗa yana jingina kanshi a jikin kujerar da yake kan ta a zaune.

A hankali ya furta.
"i will not leave them"
Ya ɗago ya kalli side ɗin da musa yake ya furta.
"kuma a yau nake so ka ai watar da komai ba sai gobe ba"
Musa daya tsorata da yanayin mai gidan nashi jiki na rawa yace.
"I will do my best for that"
Daga haka ya ɗaga ma Musa hannu yana cewa.

"Thank you very much Musa"
Da hannu ya dinga cakuɗa sumar data ke kanshi Duk ranshi a ɓace yake mai yasa mutane suke haka tabbas inda sun san girman laifin da sukai masa da idan ance su ƙara ma wani irin sa baza suyi ba.
Ya cije baki.
ya tashi ya koma bedroom ɗinshi yau ko wajan Ammi bai leƙa ba yana jin wayar shi na ringing bai bi takanta ba.

Musa yana tafe yana tausayawa Mai gidan radion sanin waye Aliyu Sarƙa ne faɗi kirikice Sarƙa ne mai rikicin gangan Dangin zaƙi ne Layin zuma.

Direct police station ya nufa sannan ya buƙaci a bashi  ƴan sanda Guda biyu Batare da sun saka uniform ɗinsu ba Haka suka nufi Gidan Radio Ɗin Abin yayi matiƙar bawa musa Tsoro na yadda yaga an ƙona gidan Radio ɗin Ƙurmus ba wani abu na mora aciki Wajan ba kowa sai Mai gadi wanda su Musa suka ƙarasa wajan sa yana zaune a saman Banchi su musa suka ƙarasa suka mai sallama.

Mai gadin Irin Iyamuran nan ne Bayan sun gaisa bai da hausa sosai ya dubi Musa yana tambayar shi.
 "What do you need here"
Ɗaya daga cikin Police ɗin ya kalli mai gadin yace masa.
"We will ask you a few questions"
Mai gadin ya zuba musu ido sabida dama tun jiya a tsorace yake dandai kawai son kuɗin shi na albashi shine ya zaunar dashi Kowa yasan ƙabila akwai riƙo da aiki baya wasa dashi.
"I hear you,what is your quesion?"
Ya faɗa yana kallon ɗan sandan daya masa magana.
Musa yaɗan dube shi.
"Gidan mai wannan gidan radion muke son ka nuna mana?"
Mai gadi ya zaro idanu cikin hausar da bata ishe shi sosai ba sabida yana jin hausar sosai amman Mayar da amsar ne take basa wiya.
"i don't know his house"
Ya faɗa yana mayar da radion shi kunnen shi ganin zai Ɓata musu lokaci yasa Ɗaya daga cikin Jami'an tsaron ya buga Masa tsawa tare da Nuna masa Id card ɗinsa Jikin mai gadi ya soma rawa Zufa tana karyo masa Nan da nan ya miƙe yana cewa.
"Let me show you"
Suka bi bayan shi Sai da suka hau Adaidata sabida da ɗan tazara daga nesa da gidan ya dakata ya nuna musu da ya tsansa yana cewa.
"That house with a black gate"
Daga haka ya juya da sauri, Suma basu wani takura mai ba suka nufi Inda ya nuna musun Gidan a rufe yake sai da suka buga Da dutse Md ya Fito yana cewa.
"Waye?"
Musa ya maƙale Murya kamar ta mata yace.
"Nice Hafsa"

Md yayi tsuku daga ciki kafin ya zare sakata caraf Ƴan sandan suka damƙe shi batare da sun masa magana ba suka tura ƙeyar shi Titi suka sami adaidaita suka tafi dashi station Gaba ɗaya Md zare ido yake Jikinsa na rawa wata irin nadama ce ta rufeshi dama tunda ya shiga Gida hankalin shi ba a kwance yake ba Burinshi yaranshi su taso daga Islamiyya ya tarkatasu su gudu Matarshi ta fita Ɗauko yaran duk zaton shi itace ma dayake sunan nata kenan Hafsa wanda Musan yaci sa'ar Ambata shiyasa ya buɗe Iya azaba Md yaji a wajan jami'an tsaron Amman Amsar shi ɗaya ce wallahi ba wanda ya saka shi ƙirƙirar labarin shidai kawai yayi ya saki ne dan tashar sa ta sami Suna.

D.p.o ya dube shi.
"Wato irin kune ɓata gari masu tada zaune tsaye acikin al'umma kawai dan son zuciyar kanka da biyan Buƙatar kanka zaka Ƙirƙiri labarin ƙarya dan ka sami ɗaukaka a tashar ka"
Ya kalli ɗan sanda guda ɗaya yace.
"Officer ku shigar dashi Bayan kanta har sai ya bamu amsar abin da muka nema a wajanshi ta yaya za'a ce babu wani dalilin shi na fitar da labarin kuma an tabbatar shine mai tashar"
Md cikin magiya yake cewa ai masa afuwa.
Musa bai bar station ɗin ba sai bayan sallar magariba Kai tsaye Waya ya kira Aliyu ya tabbatar masa da cewa an kama Mai gidan Radion an ɗamƙawa hukuma.
"Ita yarinyar fa?"
Cewar Aliyu.
Shaf Musa yama manta da wannan Sabida haka komawa yayi cikin station ɗin ya nemi daya ga Md.
Bayan ya shiga Inda Md ɗin yake tambayar shi yayi ina ne inda Wadda tai labaran take matar aure ce ko budurwa.
"Wallahi Ranka ya daɗe nina tirsasata bata da laifi yarinya ce ƙarama"
Musa ya buga masa tsawa.
"Ba wannan na tambayeka ba kwatancan ta kaɗai na tambayeka?"
Md yace.
"Gaskiya ni bazan ce ga inda ta fito ba amman Yarona daya taɓa min aiki ɗan nan ƙofar nasarawa ne duk inda ka tambayi gidansu Gali anan layi na Biyu cikin ƙofar nasarawa za'a nuna maka gidansu Tare da ƙanwarshi ya kawo min su tun last week"
Musa yace.
"Na fahimta"
Ya miƙe ya fita daga Wajan kanshi tsaye adaidaita ya kuma hawa sabida yadda Aliyu ya bashi tsoro ne yasan ya ko mota bai ɗauka ba Ƙofar nasarawa ya sauka yaci wiya kafin ya sami gidan wanda Ya sami Gali zaune da matasa a ƙofar gida ana hira Hannu ya bashi suka gaisa sannan yace.
"Da Allah ina son ganin ƙanwarka"
Gali bai kawo komai aranshi ba ya shiga gida ya kira Shema'u duk zaton shi Ko Musa saurayin shema'u ne.

Shema'u cike da mamaki ta ɗauki Hijabinta tabi bayan Gali Jingine da bango taga musa ya ƙaraso suka gaisa tana masa kallon rashin sani.

"Na san zaki mamakin ganina, Sunana Musa ɗaya daga cikin yaran mai Kamfanin Madaki Motors Kuma amintaccen yaron shi"
Shema'u tai jimm dan sunan ya kwanta mata musa yace.
"Ehemm Ina nufin special adviser na gwamna a ɓangaran matasa"
Zabura shema'u tai da sauri sabida ta gano nufin sa yanzu.
"To meye ni nawa acikin case ɗinsu tunda bani nai labaran ba,itama farha duk Nacin danai kada tayi gashi nan son zuciya ya kaita tayi abin zai zama masifa"
Musa ya fito da wayar shi ya saita recording.
"Ko zaki iya gaya mana gaskiyar abin da ya faru?"
Shema'u cikin tsoro tace.
"MD ya nemi ɗaya daga cikinmu akan tai labari akan Shi SA na gwamna ɗin wai muce duk cikin da matarshi ke samu shine yake dalilin zubewarshi ta hanyar bawa matsafa cikin, Ni direct nace bazanyi ba sabida ina gujewa kaina matsala sannan ni ƴar ƙofar nasarawa ce nasan waye shi tunda ina jin labaran alkairan shi a wajan mutane Ƙawata Farha ita tace zatai ba yadda ban da itaba daga ƙarshe ma har faɗa mukai da ita"
Musa ya gyara tsaiwa tare da cewa.
"Ita ƴar ina ce Farha, Kuma budurwa ce ko matar aure?"
Shema'u tace.
"Tare mukai karatu da ita indai ka shiga Lungun Ɗandago kace Gidan Malam Abubakar mai Bulo ba wanda baze kaika gidansu ba, ko kace Gidan cida kai ko gidan yawa Budurwace amman an kusa bikinta a yadda take gaya min akwai wanda yake sonta tun tana ƙarama"
Musa ya mayar da wayarshi Aljihu yana mata godiya.
Shema'u da gudu tai cikin Gida kai tsaye sai banɗaki ta fara fesa gudawar tsoro.
Musa bai koma wajan Aliyu ba sai da ya Je Ɗandago ya sami wanda ya nuna masa har Ƙofar Gidansu Farha sannan ya nufi wajan mai gidan Nashi.
Sai da Musa yasha zaman Jiran Aliyu sabida ƴan uwan mahaifin su da suka cika ɓangaran nashi domin suyi masa jaje Har sai da Aliyu ya sallamesu sannan Musa ya sami damar shiga parlon nashi.
"Musa yaya?"
Ya faɗa yana ɗage girarshi.
"Yallaɓai Mun sami nasarar cafke mai gidan radion duk da yana ƙoƙarin guduwa ne yabar garin, yanzu haka yana wajan ƴan sanda"
Aliyu ya cije baki yace.
"Da kyau musa"
Musa ya ɗauko wayarshi ya kunna yadda sukai da shema'u Aliyu ya Mai da Nutsuwarshi yana sauraran mai shema'u take faɗa.
Murmushi yayi na mugunta bayan ya gama sauraran abin da shema'un take faɗi.
"Yallaɓai gaskiya yarinyar ƴar talakawa ce Irin waɗannan shari'a dasu ma akwai wiya dan in za'a kasheta ba lallai a sami mai belinta ba"
Aliyu ya wara idanunshi.
"Waya ce maka shari'a zanyi da ita musa? ba kace an kusa bikinta ba?"
Musa ya jinjina kai.
"Yawwa Musa ka shiryan tafiyar sirri Gobe In sha Allah zuwa gidansu Yarinyar"

Ya faɗa yana wani irin Murmushi.
Musa daya camfa murmushin uban gidan nashi dana mugunta ya miƙe yana cewa.
"Angama ranka ya daɗe"
Aliyu ya tura hannu cikin aljihun wandon shi ya nufi saman shi bayan sunyi sallama da Musa.
*********
Washe gari Farha ta miƙe da ƙwarin Jiki har Mutan gidansu suna tsokanarta na yadda taita neman yafiya Jiya Tun magariba ta tsala kwaliya sabida salim yace mata zaizo Burinta yazo yau ɗin suyi maganar aurensu tunda dai yanzu ba batun aiki sabida an ƙona gidan radion tasu bababn tashin hankalinta ma shine yadda zata sanar da umma cewar an dakatar da ita a wajan aiki wanda faɗin hakan shine mafitarta, dan kota sha giyar wake bazata dangana kanta da gidan radion da aka ƙona jiya ba, gwara tai aurenta ta huta.
A wayar Umma salim ya kirata akan tai haƙuri baze sami damar zuwa ba jifa tai da wayar tana tura baki gaba.
Umma ta dube ta.
"Ai sai ki tashi ki tafi makaranta tunda baze zo ba"
Takaicin Salim yasa taja hijabin ta tai waje ko jakar makaranta yau bata ɗauka ba.
Adaidai wannan Lokacin Aliyu ya fito cikin Shirinsa jallabiya ya saka Brown Colour wadda tai masifar yi masa kyau ya fesa turare ya Rufe fuskarshi da face mask.
Ya fito compound ɗin gidan musa yana cikin mota yana jiranshi yana shiga motar musa yaja suka bar Gidan masu gadi suka buɗe Musu gate.
A bakin layin su Farha musa yay parking sabida motar ba zata shiga cikin layin ba, Aliyu ya fito daga cikin Motar yana mamakin ƙanƙantar cikin layin ko ina dumɗum ba wutar nepa Musa na gaba Aliyu yana binshi Daga nesa musa ya nuna masa ɗan ƙaramin gidan su farha.
Aliyu ya ƙarewa gidan kallo ya taɓe bakin shi lallai yarinyar nan tai gangancin shiga Hurumin shi dan sai ya tarwatsa mata dukkan wani farin cikinta kamar yadda tai silar shigar shi damuwa shida dangin shi da dukkan masoyan shi.
"Musa koma mota ka jirani"
Da mamaki Musa ya koma Da baya duk da bai san Ƙudirin Uban gidan nashi ba amman Lamarin ya bashi mamaki.
Aliyu ya ƙarasa ƙofar gidansu Farha Adaidai wannan Lokacin ta sako kanta ta fito Ƙofar gidan Ikram ta biyo ta tana cewa
"Yaya Farha umma tace ga jakarki"
A zuciye ta juya.
"Dan ubanki sai ki kai min ita aji munafuka"
Ta faɗa batare data lura da Aliyu dake tsaye a wajan ba ya zuba mata ido yana kallonta tsananin ƙanƙantar Yarinyar ita tafi komai ɗaure masa kai sai dai ya kula ƴar bala'i ce ta a mutu, Taɓe baki yayi yana nazarin yadda take surfawa wadda ta biyota masifa Ikram ta juya gida a guje sabida yadda Farha ta kawo mata duka.
Adaidai nan kuma Farha ta Juyo zata cigaba da tafiya ƙafarta ce tai mata nauyi sabida wanda tai arba dashi a tsaye a gabanta ya zuba mata ido babu Ko ƙiftawa............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*13*

luuu ta tafi zata faɗi Aliyu yayi saurin tarota jikinsa da faffaɗan hannunshi Ya wani rungumeta a cikin ƙirjinshi Ƙifta idanu Farha take tana Ƙoƙarin zamewa gaba ɗaya Jikinta rawa yake sosai tunda take a rayuwa ba namijin daya taɓa raɓata da jikinshi sai wannan bawan Allah da bata san kowa ye shiba.
Cikin Nutsuwa ya zamar da ita daga jikinsa yana sakar mata mayaudarin Murmushi.
Da sauri ta tattare Ƙasan skirt ɗinta zata Koma gida da gudu Aliyu ya kuma saka hannunshi a karo na biyu ya janyota gabanshi.
Ko Rabin tsayin shi bata kai ba ganinta yayi ƴar ƙarama a gaban shi Ya Sunkuyo sosai gabanta ya rage tsayin shi ya ƙura mata idanunshi waɗanda ya lura Suke mata kwarjini a tare dashi fiye da komai.
Lumshe idanu Farha tai Jikinta yana rawa ƙirjinta yana bugawa bata taɓa Ganin Halitta Mai kyau kamar ta wannan Bawan Allah ba, Dan ko kaɗan bata ɗauka ma bahaushe bane.
"Amincin Allah da rahmar sa su tabbata agare ki My princess"
Muryar Aliyu mai taushi ta doki dodon kunnen Farha.
Ƙara raɓewa tai Duk jikinta yayi sanyi atake anan wani irin BAKON LAMARI Ya ziyarci zuciyarta.
"Nasan zaki mamakin yaya akai nazo har gidanku? Ba mamaki abin da kake so shi kake bibiya Naje har gidan Radio ɗin da kike aiki wanda anan hanyar na ganki amman Naga gidan Radio ɗin a Ƙone mai ya faru da shi?"
Gaban Farha ya faɗi waige take Ko wani zai zo wuce wa daga cikin ƴan gidansu ganin babu kowa yasa taja ajiyar zuciya.
"Bawan Allah kayi haƙuri dan Allah, Nima ban san mai ya faru da gidan Radio ɗin ba, Kuma kabar Ƙofar Gidannan sabida Kawun mu in yazo ya tarar dani da wani raina zai ɓaci"
Aliyu ya zubawa ɗan ƙaramin bakinta ido wanda take sarrafa shi wajan yi masa magana dashi ya wani Lumshe ido tare da warasu akanta Kana yace.
"Ina son ki kuma ni da maganar auren ki nazo in baba ma ya ganni zan sanar masa Naga matar aure agidan shi"
Farha ta firfito da idanunta waje cike da tsaro.
"Dama ana aure batare daka san Mutum ba Bawan Allah?"
Aliyu yayi Murmushi yana danne Abin da ke taso masa a ƙasan ranshi.
"Sunana Bawan Allah anan cikin gari nake nagaya miki in zaki fita aiki nake ganin wucewar ki gashi ma baki gayan dalilin Ƙona gidan Radion naku ba"
Farha ta dafe ƙirjinta dake barazanar faɗowa ƙasa dan tsabar yadda yake Luguden duka.
"Kayi haƙuri Dan Allah, Ina da wanda zan aura in Babana yazo ya ganka sai ya halaka ni"

Aliyu ya wani zaro ido wanda ya ƙara haska zatin kyansa wanda ya kuma ruɗa farha.
Yace.
"Nima ai mijin aure ne serious ina sonki kuma da gaske in da hali zan maye gurbin wancan"
A wannan karon muryar farha da ɗan tsiwa tace.
"Zaka biya dukkan hidimar daya ɗauka shekara da shekaru yana mini Idan har na Rabu dashi ai naci amanarshi na yaudare shi Kuma zan sanya Ƴan uwana da iyayena cikin damuwa"
Aliyu ya cije leɓe.
A zuciyar shi yana Cewa Ni kuma silar labarin ki ɗaya a jiya ya cillah dukkan ahalina cikin matsala ya sanya Mahaifiyata zubar hawaye Wallahi bama zan barki ba sai nai amfani da ƙarfin soyayyata na ruguza dukkan farin cikin ki yadda kika min.

Gani yaƙi cewa komai yasa ta juya zata shiga gida, Hannun shi ya ɗora a saman ƙafaɗunta ya juyo da ita tana kallon Fuskar shi.
Ya matso gabanta har yana fesa mata Hucin Numfashin sa

"Ni ina son ki, Kuma auren ki zanyi ina son ki min list na duk abin da yayi Miki ni zan ninka masa"
Daga haka ya turata soron gidan da ƙarfi ya juya yana tafiyarsa mai cike da burgewa.
Zubewa tai a wajan tana Mayar da Numfashi wata sabuwa!
Da ƙyar ta shiga cikin Gida duk maganar da Umma kewa Farha sam taƙi bata amsa gado ta haye tana tunanin anya ba aljani bane ba Ita dai bata san shiba sannan kuma bata taɓa ganin Mutum mai kyanshi ba ɗan gayu ga ƙamshinsa ya cika mata hancinta Tsintar kanta tayi da Lulluɓe Jikinta duk rufe idanun da zatai hoton shine ke yawo acikin idanunta tashi tai ta Zabga tagumi Ganin hakan baze fishsheta ba ta miƙe ta fita tsakar Gida ta ɗauro alwala ta soma nafila.

********
Yana murmushin samun nasara ya shiga Motar Ko kaɗan batai masa ba hasalima bata burge shiba kawai zai aure tane dan ya ƙuntata mata ya kuma sanya takaicin ta acikin zuciyar mahaifanta ya fahimci daga ita har mahaifanta suna bala'in son wannan saurayin nata sabida haka zai amfani da ƙarfin Soyayyar shi wadda zai cusa mata ta ƙarfin tsiya dan ya wargaza dukkan farin cikinta ita da mahaifanta kamar yadda tai jagaba wajan Yaɗa sharrin sa.
Sam baze miƙata ga Hukuma ba aurenta kaɗai da zeyi shine dorinar dukan dukkan laifi kan data masa Sabida ta yaya ma zai tsaya yana shari'a da mace.
Gumi ya share sanda ya tuno da Ammi yasan ko yasha giyar wake baze tari Ammi da batun zai auri yarinyar nan sabida Hukunci ga laifin data masa ba to meye mafita zai boyewa Ammi auren sane Girgiza kai ya shigayi ammi bata cancan ci haka daga gareshi ba Sannan kuma yasan inta sani bazata yarda ya auri yarinyar ba Shi kuma ta hanyar aure kaɗai ya zaɓi Ƙuntata mata dan shi ba mazinaci bane bare yay amfani da wata dama dan ya tarwatsa mata Farin cikinta Kuma shi ya tabbatar wa zuciyar shi cewa baze taɓa barin Wannan yarinya ba wallahi sai ya ɗauki fansar Abin da ta masa.
Har suka ƙarasa gidan shi bai sami mafita ba sallama sukai da Musa wanda bai san yadda Aliyu Yayi da yarinyar ba kuma bai sami fuskar tambaya ba bare ya tambaye shi.
Part ɗin Ammi ya nufa ta tirsasa shi akan dole sai yaci abinci yana ci tana masa Bayanin

Maman Mami tazo da Ƴaƴanta Dan su masa jaje, Sannan ta buƙaci Daya Musu alfarma Mami zata ɗan kwana biyu agida ta huta.
Taɓe baki yayi tare da cewa.
"Nifa Ammi cikin satin nan ma zanje chaina dan zan shigo da sabbin Motoci kamfanina dake lagos sabida haka bani da matsala da zamanta agidan nasu"
Daga haka ya tashi yayi mata sallama yabar part ɗin.
Kwanciya yayi akan gadon shi yana hasko fuskar yarinyar Ƙaramar yarinya ce sosai Shi dariya ma ta bashi yadda yaga duk ta tsorata in banda Abin shiri na zuciyar mace ina ita ina shi Ya kuma gyara kwanciya yana hasko ƙanƙantar ta Lallai wannan ma in yace zai haɗa ƙirji da ita tabbas Mutuwa zatai dan yayi mata girma shi bai ma taɓa ganin Halitta ƙarama kamar ta wannan yarinya ba komai nata ƙarami hatta yatsun hannunta daya kalla ƙananu ne.
ALIYU KENAN.
Yaja Bargon shi ba jimawa bacci yay awon gaba dashi.
Da safe ya fita kamfanin shi tuni ya watsar ma da batun wannan yarinyar ya shiga sabga da ma'aikatan shi wanda yawanci Jaje ne suke masa akan abin da ya faru Dan nacin Ƴan jarida har can suka bishi akan suna son jin ta bakin shi fafur ya hana ma'aikatan shi barin ƴan jaridar su shigo masa haka ya wuni a office yana saka hannun a takardun Motocin da aka tura wasu jahohin bai tashi ba sai wajan Magariba ƙofar Gidan shi ma ba masaka tsinke tun yana magana muryarshi tana fita har muryar tashi sai da ta dashe sabida amsa gaisuwar jama'a bai shiga gida ba sai wajan 12 na dare Yana mai jin farin cikin yadda al'umma suka nuna rashin jin daɗin su na abin da ya same shi lallai ya yarda jama'a rahma ce Kuma alkairi Daɗi gare shi wanka yayi ya kwanta jikinsa fal gajiya Hutu kaɗai yake buƙata..........
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*14*

Juyi kawai take yi a gado jikinta sanye da ƙaramar riga mai hannun shimi hannunta dafe da daidai ƙasan mararta wanda take dannawa sai Nishin azaba take Kukan ma yaƙi zuwa tun bayan datai sallar Asubahi take jin ciwon Marar ta na taso mata kaɗan kaɗan adaddafe tai sallah ta koma gado ta kwanta tana faman Juyi
"Wai yau ba zaki fita aiki bane Farha? jiya dai baki da lafiya amman yau ya kamata ki fita kada suce kina wasa da aikin ki"
Cewar umma da take tsaye a kanta.
Ɗago idanunta tai wanda yayi jajir sabida azaba Murya can ƙasa tace.
"Umma nai wa ogan waya na gaya mashi bani da lafiya bazan iya fita ba"

Umma tabi ta da kallo tana nazarinta.
"Yaya naji muryarki a haka Ko jikinne?"
Cikin tsananin azabar zafin marar tace mata.
"Umma marata ciwo ji nake numfashina yana fita da ƙyar"
Ta faɗa cikin azaba Umma ta ɗauki wayarta ta soma haska saman sif ɗinta Maganin farha ta lalubo wanda saura ɗaya ya ƙare ta miƙa mata fita tayi waje ta ɗebo mata ruwa lokacin data dawo har ta miƙe zaune.
"Ungo kisha kafin Ikram ta tashi sai ta amso maki wani"
Ta amshi ruwan ta watsa maganin cikin bakinta Tashan ye tana mayar da Numfashin wahala Jim kaɗan ta miƙe tai tsakar gida aguje tana kwarara amai wanda shine ya Tada jama'ar gidan su.
Babarsu Ruƙayya ce ta tsaya akanta tana mata sannu Babarsu Hadiza kuma ta wanke mata Aman Ƙannenta sai sannu suke mata tana amsawa da ƙyara Duk abin Matan gidan da ƴaƴan gidan in abun jaje ya samu suna ƙoƙarin karantawa Amman in tashin hankalin su ne ya motsa ba sauƙi.

A wajan ta kwanta har rigarta na yayewa Ƴan cilli cillin cinyoyinta Suka bayyana a waje Kawu ne ya fito yana kallon ta.
"Wannan kuma lafiya ko jikinne?"
Umma data ke ɗagota Zuwa jikinta tace.
"Ciwon marar tane ya tashi shine tasha magani take amai"
Kawu ya koma cikin ɗakin sa.
Can jimawa ya fito da ɗari Biyu.
"Ga wannan ku tafi asibiti a dubata Allah ya sawaƙe"
Umma tabi Naira Ɗari biyun da kallo tana cuɗa yadda zata musu Kuɗin mota har da ganin likita ba abin kai magana ba yayo maka caa.
"Allah saka da alkairi"
Daga haka ta ɗaga Farha suka nufi ɗaki da taimakon umma ta shirya Suka fito domin zuwa asibiti.
Da ƙyar aka kaisu bakin asibiti a naira ɗari Layi suka tarar sosai a asibitin Farha na zaune tana jin yadda wasu mata suke magana ɗayar ce tace.
"Ai tuni an ƙona gidan radion tun ranar, Naji ance ma an kama mai gidan radion ita kanta yarinyar datai labaran an kamata, Wai gwamna da kansa yace zai ɗauki mataki akansu shi kuma Hasken matasan yace a,a abar shi da kanshi zai ɗauki mataki"
Farha tai tsuru tana jin wannan ƙarya wai an kama wadda tai labarin bayan gata a zaune.
Tana jin yadda matar take ta zabga wa mutanan wajan ƙarya akanta alhalin gata a zaune kuma tana wa Allah godiya abisa rufin asirin dayay mata daya sa babu wanda ya kama sunanta har yanzu.
Haka layi yazo kansu suka shiga ganin likita wanda ya rubuta musu magani Daga asibitin Zage suka shiga Gidan yayar umma anan suka ci abincin rana da ƙyar ma umma ta yadda ta zauna sabida tasan halin kawu da faɗan tsiya.
Ita kam farha bacci ta samu bayan taci abinci wanda Umman zage tace wa umma tabar farha zuwa yamma sai ta tawo gida Haka umma tai wa Umman zage sallama ta tafi gida.

Koda Umma taje Gidan kawu faɗa ya kamayi akan me zata baro masa ƴa a wani waje ta kamo hanya ta tawo umma tasan za'a rina sabida yadda tasan shi mutum ne mai taka tsantsan akan ƴaƴanshi.
Shuru tayi masa ta shige ɗaki sai ya bita yana cewa ta mayar dashi mahaukaci Umma dai bata yi magana ba tazo ta tarar da gidan A bushe ba ai abinci ba inda bata biya zage ɗin ba da haka zasu dawo da yunwa damma ta tarar da Ikram ta tafi gidan fa'iza.
Zuwa yamma Halifa ya kawo garin tuwo kwano Biyu yace a tuƙa sabida yau Mai gidansu yasa an musu kyautar Dubu goma goma Shi kuma nura ya bada dubu biyu yace ayi cefane.
Amman Fafur Babarsu Ruƙayya tai ɗakinta da garin, tace babu wanda zata tuƙawa tuwo da garin Ganin haka yasa itama Babarsu Hadiza ta bada Dubu biyun da Nura ya bata tace Zuhuriyya ta siyo musu taliya da mai da Kayan miya haka kowacce ta saka tukunyarta tare da ƴaƴanta dama umma tasan za'a rina shiyasa bata fito tsakar gidan ba har wajan Marigaba tana ɗaki Sai da aka kira sallah Ikram ta dawo daga gidan Fa'iza Lokacin data shigo ɗakin Hannunta riƙe da fulas wanda Fa'iza ta ciko shi da awara da naira ɗari biyar tace a kawo wa ummansu.
Kawu ne ya ƙara zuwa bakin Ƙofar Umma.
"Hasiya wai har yanzu fatima bata dawo ba kinga bana son irin haka kada ki ƙara bar min Ƴaƴana a wani wuri"
Umma data zuciyo dama da taƙaicin matan gidan a ranta duk da tasan cewar kawu bai san abin da sukai ba.
"wai kai dan Allah in farha ta zauna acan gutsirar namanta za'ai? ina ba wajan yayata taje ba in ta zauna anan wani abun zaka mata nan maganine aka rubuto mata kazo ka tambayi kuɗin sai aikin tambayar ta dawo"
Bala'i ne ya kaure a tsakanin Umma da kawu abin da bai taɓa faruwa ba haka ya fita ƙofar gida ya tsaya yana sauraran ta inda farha zata fito har ya gaji ya nufi Bakin titi wajan zaman shi sai dai a ranshi ya ƙudiri aniyar sai ya mata arnan duka idan ta dawo gida.

Farha sai Bayan magariba tai shirin dawowa gida bayan sunyi sallama Da umman zage wadda ta bata kuɗin Mota katin ta na wajan Likita daya rubuta mata magani ta ɗauko ta fito daga gidan cikin ikon Allah tana fitowa ta sami abin hawa.

Yau Aliyu bai wunin Office ba yaje wajan visa ɗin sa ta fita chaina wadda yay cuku cukunta yana dawo wa gida kuma ya wuce cikin gidansu mahaifin sa rabon kuɗi yayi Musu kamar yadda ya sanya musa ya rabawa kaf ma'aikatan sa dake kamfanin shi Kuɗi Ya jima wajan ƙannen mahaifinshi Kafin ya fito Yaja face mask ɗin shi ya rufe fuskar shi sabida mutane Ya laluba aljihun shi da ƴan canji Napep ya tare yace masa ɗandago A bakin layin su Farha ya sauka ya shiga cikin layin lokacin gari ya fara duhu.
A ƙofar gidan ya tsaya ba yaron da ya fito daga gidan sai dai Yana jiyo kukan yara da hayaniyar matan gidan ya jima a wajan duk sauro ya gama cije masa jikin shi.
Yarinyar jiya ce ta fito da kuɗi a hannunta daga gani shago zata je yay saurin matsowa kusa da ita.
"Ke ina masifaffiyar yayarki ta jiya?"
Ikram da bata gane ko waye bane sabida abin kare fuskar dayay amfani dashi ta soma ƙifta ido

cikin tsoro tace.
"Farha bata nan tana zage"
Ta faɗa cikin sauri tare da tsoro.
Ya nanata sunan
"Farha"
Lallai kam.
"Sunan ta kenan Shi ake gaya mata?"
Da sauri Ikram tace.
"Eh ko kace fatima ba"
Jin Muryar Halifa dake fitowa yasa Ikram ta Nufi hanyar shagon aguje Halifa yabi Aliyu da kallo wanda bai gane ko waye bane Aliyu ma baiwa halifa magana ba ya cigaba da tsaiwar shi a wajan Har Ikram ta dawo daga aiken ta ta shige cikin gida.

Adaidai nan kuma farha ta shigo layin sanye take da hijabi har ƙasa ja Wanda ya rufe mata har tafin ƙafafunta Daga hannunta ma yatsun hannunta kaɗai ake gani.

Tana ƙoƙarin Hawa dakalin gidan wanda bata lura da Aliyu dake tsaye ba Taji yo muryar kawu wanda garin saurin ta shiga gida har faɗuwa tai ta miƙe tana kaɗe hijabin sai dai kafin ta shiga har kawu ya ƙaraso wajan Aliyu yay saurin matsawa daga jikin gidan ya zuba wa Tsohon ido wanda yaji muryarshi yana cewa.
"Fatima sai yanzu kika dawo to ki jira zuwana daga ke har uwar taki data ɗaure miki gindi ni kinsan ba'a yawo a gidana ba zan lamunci wannan ɗabi'a ba Shiyasa na matsu wannan yaro ya turo ni koba lefe aurar dake zanyi"
Takaicin tijarar kawu ya kama farha shi haka yake in yaso cin mutuncin sa a ko ina yi maka yake yanzu meye abin wannan maganar a ƙofar gida damma ba kowa a layin.
Kawu ya juya ya koma titi Ita kuma ta nufi Gida zata shiga.

Da sauri Aliyu ya sha gabanta.
"Kinga shima ya matsu ki aure to mai kike jira ga miji a hannun ki kin samu"
Taji muryar BAWAN ALLAH a cikin dodon kunnenta cikin taushin murya yayi mata maganar.
Yana zare face mask ɗin daya rufe fuskar shi da ita.

Da sauri ta ɗago kai tana kallon shi.........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*15*

Lumshe idanunta tayi ta saki wata irin ɓoyayyar ajiyar zuciya, Yayi mata masifaffan kyau Ƙura masa idanu tayi babu ko ƙiftawa sanye yake da wani irin lallausan yadi Coffee colour wanda ya haska farar fatar jikin sa sai yanzu ta kuma ƙare masa kallo dogo ne sosai dan yadda ya mata tsaye akan ta har rumfa tsayin shi yayi mata Yana da manyan lumsassun idanuwa masu kama dana wanda yake jin bacci Yana da cikakken gemu wanda ya haɗe da ƙasumba ya cika fuskar tashi Sai Ƙaton tabon Abin sallah wanda yay baƙi sosai a saman Goshin sa.
Numfashin ta ne ya kusan ɗaukewa lokacin da taji ya hura mata iskar cikin bakin shi mai ƙamshin Mint.
"Kallon fa?"
Ya faɗa da tattausar Muryarshi.
Tsintar kanta tayi da jin matsananciyar kunyar shi.
A hankali ya furta.
"Do you feel what I feel when you are with me?"
Ya kuma matsowa gabanta ya maimaita mata abin da yace da yaran hausa.
"Kema kina jin abin da nake ji atare dani?"
Matse katin asibitin dake hannunta tayi gam aranta tana cewa.
Wannan Bawan Allah zai halaka ni.
Jikinta ko ina rawa yake muryarta na rawa sosai tace.
"To ka matsa baya sai muyi magana"
Aliyu ya zira hannunshi saman nata hannun ba zato taji ya fisge katin asibitin data riƙe a hannun nata.
Zubawa katin idanu yayi yana gama karantawa ya saki murmushi.
Bai miƙa mata katin ba ya zira shi acikin aljihun shi.
Hannun nashi tabi da kallo wanda yake shinfiɗe da wata irin baƙar suma tai luf kamar ka taɓa jini ya fito.
"How do you feel about your body?"
Ya faɗa yana ƙoƙarin saka ƙwayar idanun shi cikin tata wadda ita kuma taƙi yarda ta haɗa idanun dashi sabida duk kunyar abin da ya gani ajikin katin  tagama kamata.
"Shike nan tunda baza'a min magana ba oya shiga gida"
Kamar jira take da sauri ta kama ƙofar gidan nasu zata shiga ciki.
Hannu ya zira cikin Aljihunshi tare da fesar da iska mai zafi.
Tsadaddiyar wayarshi wadda bai cika amfani da ita wajan hulɗa da jama'arshi ba ya fito da ita ya damƙa ta a hannun Farha wadda harta kai da shiga soron gidan nasu.
A hankali ya rage tsayin shi ya Sunkuya daidai kunnenta ya raɗa mata.
"Saura ki ƙi ɗaga wayata, zan kira ki anjima"
Daga haka ya juya ya fice daga soron gidan yabar mata ƙamshin turaren shi.
Gaba ɗaya Jikin farha rawa yake sai faman kaiwa da komowa numfashinta yake Ta kasa jan ƙafafunta zuwa cikin Gida gefe guda ga tsoron wannan waya daya bata Ya cika mata zuciyarta.
Da ƙyar ta aro jarumtar jan ƙafafunta da suka mata nauyi ta shiga cikin Gidan Duk matan gidan da ƴaƴan suna cikin ɗakunan su yanayin sallamar datai ne a hankali yasa ba wanda yaji sallamar tata.
Ta ɗaga labulan ɗakin umma ta shiga ɗakin da sallama, Umma ta zuba mata ido cike da

tausayinta zaton umma duk jikin nata ne yasa ta koma haka.
"Sannu farha ina nan ina tunanin ki Yaya ƙarfin Jikin naki?"
Ta damƙe wayar tana Cewa.
"Alhamdulillahi Umma"
Daga haka ta nufi uwar ɗakan su ta aje wayar a saman sif gudun kada Umma ta gani, Ta zare hijabin Jikinta Ta fita tsakar gida banɗaki ta shiga ta gyara jikinta sabida priod ɗinta daya zo mata a yanzu.
Tana shigowa ɗaki taji Muryar yaro yana cewa.
"Wai ina fatima?"
Umma ce ta ɗaga murya tace.
"Shigo mana menene"
A lokacin Farha ta zauna a gefen tabarmar ɗakin yaron ya shigo da ƙatuwar leda a hannun shi fara mai ƙyalli.
"Wai wanine yace in kawowa Fatima amman ya tafi"
Umma tace.
"Wani yaya kamannin sa yake?"
Sabida duk ta ɗauka ko Salim ne.
"Dogo ne sosai fari amman banga fuskar shi ba"
Umma tai jimm dan Salim baƙi ne kakkaura.
"Ka mayar masa da ledar kace ba'a nan gidan take ba"
Yaron yace.
"Ai ya riga ya tafi tunda ya bani"
Daga haka yaron ya aje ledar yayi tafiyarshi.
Ikram ta buɗe baki cike da Ɗaga murya tace.
"Wallahi umma da gaskiyar yaron nan nima tunda kika aiken siyo suga ɗazu na ga Mutumin a ƙofar gida wai yace ina Masifaffiyar yayata, Kuma Umma mutumin kamar balarabe Duk da fuskarshi a rufe take"
Umma tai shuru ta zubawa Farha idanu wadda tai ƙasa da kanta Jikinta na rawa.
"Farha wanene kuma wannan Mutumin kada ki Ɓoye min gaskiya?"
Farha tace

"Wallahi Umma ban sanshi ba nima, Yace min wai a hanyar wajan aiki yake ganina in zan tafi, Amman umma ni ban sanshi ba Allah da gaske nake miki"
Umma ta janyo ledar ta buɗe.
Magungunan da aka rubutowa farha ne masu tsada amman ba a sako katin ciki ba, Sai Kaji manya gasassu Guda Uku da Lemuka masu sanyi.
"Baki san shiba ta yaya kika bashi katin maganin ki? Farha ba zaki jamin Cin mutuncin mahaifin kiba wallahi sai na tattare kayana na bar muku gidan in banda ke da Ikram da tuni na mance da barin wannan gida Salim bai cancanci haka daga gareki ba kada ki bari ruɗin Shaiɗan ya shiga zuciyar ki, Maza ki tattare masa kayanshi Kisan yadda zaki ki mayar masa dasu ni babu ruwana kuma ki kuka da kanki idan mahaifinki yaji"
Farha tahau kuka tana bawa Umma haƙuri.
"Allah umma ki yarda dani shine ya ƙwace Katin a hannuna ɗazu"

Umma miƙewa tayi tabar mata ɗakin.
Farha tasha kukanta Daga ƙarshe ko kallon ledar bata yi ba ta miƙe ta shige ɗaki ta kwanta.
Umma banɗaki ta shiga bayan ta fito Ikram tai musu shinfiɗa a rumfa suka kwanta dama su a rumfa suke kwanciya Farha ce ke kwanan Cikin uwar ɗaka dan komi zafi bata fitowa.
Umma ta jima batai bacci ba tsoron ta Ɗaya shine kada Allah yasa wannan Mutumi ya yaudari Farha ya rabasu da Salim dan so wani bin shu'umi ne Musamman ga zuciyar mace mai rauni.
Cikin baccinta taji Nishin wayar daya bata wadda ita Fushin umma ma yasa ta mance da ita.
Da sauri ta miƙe ta ɗauko wayar ta katse kiran.
Can wani sabon kiran ya kuma shigowa Numbern ba suna sai dai special number ce ta ƙurawa Numbern idanu kafin  a hankali ta ɗaga kiran.
Wata irin Ajiyar zuciya Aliyu ya saki ta cikin wayar.
"So kike yau na kasa bacci my princess ina ta kiranki baki ɗaukar Min kirana ba Why?"
Ƙara damƙe wayar tayi tana Zare idanu tsoronta ɗaya kada Umma ta jiyo ta.
"Dan Allah ka rufamin asiri bawan Allah kazo ka amshi Abin da ka aiko kasa ummata tana fushi dani"
Ta faɗi Murya can ƙasa Kamar mai yin raɗa.
Aliyu ya Narkar da Murya kamar zai mata kuka ya soma Gaya mata mayaudaran kalamai wanda shi kanshi bai san ya iya suba Luf Farha tai tana ƙara nutso a saman gado Wayar kare a kunnenta wani irin Baƙon lamari ke bibiyar dukkan sassan jikinta.
Aliyu sai da ya tabbatar ya mata illah a zuciyarta sabida yadda yaji tana sakin Numfashi da alama kokawa take da zuciyarta Manna wa wayar Kiss yayi ya kashe kiran.
Tashin Hankali Farha a zaune ta raba dare ta kasa bacci duk motsi hoton Aliyu da yadda yake mata magiya ne yake mata yawo acikin idanunta zuwa asubah wata irin Mahaukaciyar soyayyar Aliyu tai mata mugun kamu Ko Motsi tayi shi take gani bata kallon ko wani namiji a zuciyarta sai shi taji ta aminta da Salim  kawai kula shi take, amman soyayya yanzu ta fara yi da bawan Allah kamar yadda ta raɗa masa dan bata san sunan shiba.

Aliyu kwanciyar shi yayi ranshi fes batare daya ji dukkan wasu kalamai daya yiwa yarinyar yayi tasiri a zuciyar shiba.
Washegari haka ya shiga harkokin sa batare daya tuna da Farha ba Ranar Alhamis wadda ta kama rabon shi da farha kwana uku jirginsu ya ɗaga ƙasar chaina.
Harga Allah ya mance da ita tunda ya je chaina zirga zirga yake akan yadda sabbin motocin daya siya su zo Kamfanin shi wannan tasa baya samun Lokacin kanshi bacci ma baya isarshi sosai tsayin sati ɗaya ya ɗauka a chaina daga nan kuma ya wuce saudiyya.

Tuni soyayya da tunanin Aliyu sun huda dukkan sassan jiki da zuciyar Farha dama tun washegari da bai zoba Umma Ala dole tai amfani da Kajin ta bawa farha magungunan sai dai sam ta daina sakarwa farha fuska maganar aiki ma umma da kanta tace ita gaskiya farha ta haƙura da fita Tunda dalilin fita aikin wani ya fara biyota ita bata son Su shiga haƙƙin salim wannan hukunci yayi wa farha daɗi sabida haka bata ɗagawa kanta hankali ba suma mutan gidan duk sun ɗauka rashin lafiyar farha ne yasa Bata koma aikin nata ba.
Ba abin da Farha take sai aikin kwanciya Sai kuma zubawa wayar data ɓoye ido kullum Tunanin ganin Kiran Bawan Allah take tun tana sanya rai har ya cika sati ba shi babu wayar shi dole tai

shahadar kiran layin nashi sai dai baya tafiya haka zata haɗa kai da gwiwa tana kuka ita kaɗai a ɗaki tana Allah wadai da zuciyarta data kamu da son wanda ko sunan shi bata sani ba ƙila ma Ƙarya yake mata yaudarar ta kawai yazo yayi.
"Ni farha meke damun kine? wannan jarababban bacci da ƙunci ke kaɗai ya isheni idan ma dan na hanaki fita aiki ne to kisha Kurumin ki ɗazu Mahaifin Salim ya turo Ƙanin sa nan da jibi zasu kawo kuɗin auren ki"
Farha bata ɗaga kai ta dubi Umma ba Hawaye ne ke gudu acikin Idanunta Ta kife a saman gado ranar wuni tayi kuka da magariba Salim yazo haka ta fita a zuciye duk haushin salim ya cika mata zuciyarta.
Duk maganar da salim ya gaya mata baƙar magana ce take Biyo baya Cike da mamaki salim ya dube ta dan hakan bai taɓa faruwa a tsakanin suba.
"Farha lafiya kuwa kodai wani ya ɓata miki rai ne?"
Ta ɗago a fusace.
"Kaga salim dan Allah ka rabu dani, Kaga in ka takura sai ka aure ni wallahi zan kashe kaina kowa ya huta"
Daga haka ta shige Gida da Ihu wanda yaja hankali mutan gidan tambayar duniya an mata taƙi cewa komai addu'a Umma ta dinga tofa mata zaton umma ko gamo farha tayi

Abin mamaki kwana tayi tana kuka ta wuni Kawu duk zafin sa sai da ya sauko yana tambayar ta Meke damunta.
"Kawu kada ka aura min salim bana son shi wallahi idan aka aura Minshi zan kashe kaina"
Salati Umma dasu Babarsu Ruƙayya suka ɗauka.
Kawu ya miƙe.
"Zan tanaji likkafani da makara wanda ina ɗaura Miki auren zan haɗaki da kaina na kaiki kabari amman ki sani ko gawarki ce sai taje gidan salim Butulu Dama nasan za'ai haka tunda uwarki ta ɗaure miki gindin aiki To duk baku isaba ni ba ƙaramin Mutum bane"
Kawu yabar ɗakin
Umma a zuciye ta rufe Farha da duka tana cewa.
"Ni zaki wulaƙanta to bara na kashe ki da kaina kafin Ki kashe kan naki"
Da ƙyar aka ƙwaci farha a hannun Umma Babarsu Hadiza ta kaita ɗakinta Ranar kowa ya wuni ba daɗi agidan.
Salim durƙushe a gaban Babansu wanda ya kirashi akan Batun kai kuɗin auren shi gidan su Farha.
"Baba ina ganin abar batun kai kuɗin nan"
Baban salim yace.
"Dalilin ka kana son naji kunyar aminina?"
Salim yay ƙasa da kanshi.
"Baba muna jin case a radio da kasuwa na illar auren dole Jiya naje wajan Farha da kanta taci alwashin na aure ta zata kashe kanta"
Subuhanallahi.
Baban Salim ya faɗa yana tafa hannun shi.
"Jeka zan nemeka"
Babar salim dake bakin Kofa tahau bala'i

"Tsinannu dama nasan za'ai haka sun gama ta tsar shi shine zasu zugata to Allah ya isa"
Baban Salim ya dube ta.
"Amman baki da hankali In da kin san waye Abubakar akan ƴaƴan sa da baki ce haka ba, Ɗane ka haife shi baka haifi halin sa ba mu dai addu'a zamu yi duk abin da yafi alkairi Allah ya zaɓa bama son ai abin da za'a zo ana kuka"
Baban Salim Mutum ne mai sauƙi wanda halin shi salim ya ɗauko ba irin mahaifiyar shi masifaffiyar mace ba.
A ranar Baban Salim ya sami kawu a Gida bayan sun gaisa yace masa.
"Malam Abubakar nazo ne da maganar yarannan ɗazu salim yace Min fatima tace in ya aure ta zata kashe kanta, To duk maganar haka bata taso ba ka zaunar da ita ta gaya maka wanda take so in yaso sai ayi dashi ƙila rabo ne ke kiranta in aka ja za'a iya rasa rai"
Kawu ya dubi Baban salim.
"Duk wanda aka rasa kwanan shine ya ƙare nifa ba zata mayar dani ƙaramin Mutum ba Munafurci ne nata dana uwarta Sabida haka bama kawo Kuɗi ba gobe gobannan ina son ka turo da sadakin salim na ɗaura musu aure da fatima"
Baban salim yace.
"Nagode nasan duk ƙauna ce ta saka kace haka ni nafi ka hange akan wannan matsalar, saboda haka ayi haƙuri a tuntuɓi yarinyar wa take so a bata shi ni dai nine mahaifin salim to in dai daga wajena Auren shi zai Ɗauru da fatima to na janye Allah ya haɗa kowa da rabon shi"
Duk yadda kawu ya kafe Baban salim yaƙi sabida Yaji tsoron furunci Farha haka sukai sallama da Kawu abin ba daɗi dan kawu ya zuciya haka yayo gidan ya faɗo ɗakin Umma A ranar anga tashin hankali agidan dan kawu cewa yayi umma sai ta bar masa gidan shi ita da Farha da ƙyar su Halifa dasu Babarsu Ruƙayya suka janye kawu Daran Umma kuka Farha kuka Ikram kuka umma taiwa farha dukan da har sai da tai mata tarkaɗe Amman zuciyar farha bata saduda ba zuwa asubah kawu ya tara kaf Matan shi.
Da Yaƴan ya dubi farha.
"Na baki daga yau zuwa gobe Kiwa wanda kike so magana yazo gobe da sadaki na ɗaura muku aure idan ya wuce gobe kuma zan bawa duk wanda naga dama sadakar ki Burunku ya cika keda mahaifiyarki"
Daga haka yabar wajan.
Umma bata ko kalli farha ba tayi ɗaki Farha ta rasa yadda zatai Haka ta shige ɗaki taita gwada numbern Shi yaƙi shiga.
Har Yamma abu ɗaya take taƙi fitowa waje sabida tana tsoron Hararar umma.
Kamar da wasa Ana kiran magari ba ta kira Numbern tana ringing amman ba'a ɗauka ba.
Aliyu daya sauka yau da rana tunda ya shiga part ɗin shi da yayi wanka bacci kawai yake bai tashi ba sai la'asar yayi sallah Ya Nufi Gidansu Mami abisa tirsasawar Ammi har Magariba suna tare da Mami yana kallon wayar shi na ringing da tsohon layin shi daya bawa wannan yarinyar wadda ya manta ta kiranta ne ma ya sanya shi tuna ita ɗin wacece yana kallo kiranta yana shigowa amman yaƙi ɗauka sai da yayi sallar magariba sannan ya baro gidan su mami wadda tace cikin satin nan zata dawo ɗakinta.
Yana driving yaga wani kiran nata ya ƙara shigowa wayar shi yayi parking a gefen titi ya ɗauki kiran.
Muryar Farha cikin kuka take cewa.

"Ina ka shiga bawan Allah ka barni cikin bala'i dan Allah ka dawo gare ni"
Kuka ne yaci ƙarfin maganar tata.
Kukan mace yana ɗaya daga cikin abin da yake san yashi Jin rauni fiye da zato.
"Ki haƙuri bari na zo"
Daga haka ya katse wayar ya tada Motar yayi unguwar su a bakin layin su yayi parking Yaja Face mask Ɗin shi ya rufe fuskarshi ya taka da ƙafar shi har bakin Ƙofar gidan ya fito da wayar ya kira ta.
"Gani nazo"
Daga haka ya kashe.
Sum sum Farha ta fito daga ɗakin su tayo ƙofar gida wajan shi da sauri............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*RABO YA RANTSE...!!*🌹

*NA*
*AUTAR MANYA*

ADABI WRITTER'S ASSOCIATION

*16*

Tana zuwa gaban shi ta zube a ƙasa tana sakin marayan kuka, Hankalin shi a matiƙar tashe ya tsugunna a gabanta ya sanya hannun shi ya kamo Tattausan hannunta ya zuba mata Girman idanun shi batare daya ce mata ko mai ba sai binta yake da kallo kamar zai cinyeta ɗanya.
Kukan take Babu ƙaƙƙautawa Tuni Kan Aliyu ya fara juyawa in da abin da yafi tsana a duniya bai wuce kukan mace ba sabida tafarar ɗaya yake sanya masa Rauni.
Da ƙarfi ya damƙe hannunta wanda Hakan ya sanya ta sakin wata irin ƙara tana yarfe hannun sabida tun Dukan da umma tayi mata take zaton Hannun nata Ya sami targaɗe.
Kula da yayi hannun na mata zafi ya sanya shi ya sakar mata shi.
"Shiii Be quiet and let's talk"
Ya faɗa yana sakin numfashi mai ƙarfi.
Sannu a hankali take rage sautin kukan nata kamar yadda ya buƙata.
Muryarshi can ƙasan maƙoshi ya furta mata.
"What made you cry?"
Goge idanunta take da hannunta mai lafiya muryar ta a dashe ta soma yi masa magana.
"Kawu ne yace in baka aiko an ɗaura min aure da kai gobe ba, zai ba dani sadaka"
Aliyu ya zare ido with full surprise.
Kafin yayi magana ta cigaba da cewa.
"Tun jiya umammu take dukana har targaɗe tai min"
Tana faɗin haka ta kuma fashe masa da kuka.
Yayi ƙasa da murya kamar mai raɗa Ya ƙara matsowa gaban ta a yadda yake a tsugunnen.
"Duka garin yaya akai haka? dama shi kawu ya sanni ne?"

Ƙunshe fuska tai Cikin jin kunya tace.
"Dan nace bazan auri Salim ba"
Cikin Tattausar Muryar shi yace.
"Dalilin ki? kodai kina sona ne kema?"
Ƙasa tai da kanta ta ɓoye fuskarta da hannunta wanda ya bashi tabbacin zargin dake zuciyarsa na ta bijirewa mahaifan tane akan shi.
Ya saki wani ƙasaitaccen Murmushi ya Leƙa fuskarta data ɓoye.
"Baki sanni ba Fatima, Ko sunana bani tunanin Kin sani bare anguwar mu bare sana'ata kawai tashi ɗaya ki bijirewa wanda da bakin ki kika ce tun kina ƙarama yake miki hidima Why are you doing this, Fatima?"
Ya faɗa mata hakan cike da mamakin ta tare da jinjina girman wauta da ƙuruciyarta.
Muryarta har zuwa lokacin bata Dawo daidai ba may be kukan data sha ne yayi Mata haka da muryar tata.
"Bawan Allah! Koda acikin Bukka kake rayuwa namun daji suna kewaye ka ni zan bika mu rayu tare, Ni dai na san ba zaka cutar dani ba, Kawu yace in baka aure ni ba zai bada ni sadaka kuma kai da bakin ka kace kana sona zaka aure ni"
Shuru Aliyu yayi gaba ɗaya ta gama kashe masa jiki da kalamanta wani irin tausayi yarinyar ta bashi amman daya tuna yadda tai jagora wajan ɓata sunan shi sai ya kawar da tausayin nata a zuciyar shi, Amman kuma mamakin yadda tace tana son shi batare data san koshi waye ba, abin ya bashi mamaki sau da dama yasha Cin karo da ƴammata su tare shi suce suna son shi wanda duk ba domin Allah bane sai dan kawai yana da kuɗi amman ita ta miƙa wiya ko sunan shi bata sani ba amman ta bashi dukkan zuciyarta.

"Kukan ya isa fatima, kawu ɗin gobe yace?"
Da sauri ta ɗaga kanta.
"So nake ki min magana da baki bana son magana da ka"
Ta fahimci yana da son a girmama shi.
"Eh haka yace"
Shuru ya kuma yi gaba ɗaya kanshi ya ɗauki zafi.
"Tom shikenan kice masa zan turo ƙanin mahaifina goben, Amman ni bani da abokai Kuma ni bazan zo wajan ɗaurin auren ba amman zan turo Waliyi na tare da sadaki hakan yayi?"
Ga mamakinsa sai yaga ta saki ranta har tana murmushi batare data tambayi ina zai kaita ba.
"Fatima baki tambayi ina zan kaiki ba inna aure ki?"
Fuskarta cikin farin ciki tace.
"Nina san ba zaka cutar dani ba"
Murmushi ya saki na dole dan ya ɗauki alƙawari mai wiyar cikawa.
"Tashi Muje a gyara maki hannun sai na maido ki gida"
Ta zaro ido wanda hakan ya ƙara fito da kyanta wanda ba kowa ne yake gane hakan ba.
"So kake ai gunduwa gunduwa dani agida"
Ya wani kashe mata ido ɗaya.
"To niba mijin ki bane,Hurry up and let's go back"
Miƙewa tsaye yayi kafin ta tashi har yay tafiyar shi bin bayan shi tayi Allah yasa har suka je bakin layin basu ga kowa ba ya buɗe mata front seat ta shiga shi kuma ya shiga driver seat

Lumshe idanu tai Sabida wani mahaukacin sanyin Ac tare da ƙamshi daya cika motar ita sai tace tunda take a rayuwa bata taɓa ganin mota mai kyan wannan mota ba, ( hhh to farha ai masu abu da abun sune da mai kamfanin madaki motors kike tare a rashin sani ) tafiya suke kamar ta kurame shi yana can duniyar tunanin dalar daya ɗaukowa kan shi ba gammo, ita kuma sanyi da ƙamshi da fargabar gida sun sa tai tsuku.
Jifa jifa yake ɗaga wayarshi wanda duk maganar da yake bada hausa yake yiba da turanci yake yinta.

A daidai ƙofar Ɗan agundi Yayi parking ya kashe motar ya ɗauki face mask ya saka wadda ta lura kamar sakata ya zama ƙa'idar shi.
"Muje ko"
Daga haka ya sauka daga cikin Motar.
Yayi gaba tabi bayan shi gidan sarkin Ɗori Suka shiga kai tsaye ɗakin dake soron gidan ya shiga bayan ya tuɓe takalman shi Dattijo suka tarar a zaune yana shan shayi Suka gaisa dashi Aliyu yace.
"Na kawo ta Baba a duba hannun ta"
Dattijon ya aje Kofin shayin.
"Allah sarki yarinyar kace kenan? matso mugani jikata"
Aliyu yayi murmushi yana ayyana lallai ƙanƙantar Yarinyar tayi yawa.
Farha ta ƙarasa gaban Dattijon.
"Ki cire hijabin ki fito da hannun"
Da sauri Aliyu yace.
"A,a zata fito dashi a haka ai yana da hannu, Fatima fito dashi ta cikin hannun shi"
Tayi yadda yace ɗin.
Addu'a Dattijon yayi Kafin ya cafki hannun da sauri yana Matsa shi.
"Wayyo Ummata Washhh zafi"
Ta faɗa tana cije bakin ta.
Kafin a gama Gyaran ta gama Jigata da gumi da hawaye.
Ana gamawa ta sunkuyar da kanta tana Kuka wiwi
Aliyu ya cire kuɗin da bai san adadin yawan suba ya aje wa Dattijon.
Godiya dattijon yayi tare da cewa.
"Wannan yarinyar taka akwai rigima bari na shiga daga ciki Allah ya bata lafiya.
Daga haka ya miƙe ya fita daga ɗakin.
"Ki shuru dare nayi, Ki tashi na kaiki gida"
Kukan take bata kula shi ba.
Ya miƙe tsaye ya nufi hanyar fita.
Da sauri ta miƙe agarin saurin ta take Hijabinta aiko ta faɗi ƙasa tim.
Cikin azama ya juyo ya ɗagota.
"Kema gaki ƙarama kina sanya wannan abun yayta kayar dake"
Hijabin ne ya cukurkuɗe dole ya sanya hannu ya zare mata shi yana warware wa.
Farha tai saurin sanya hannu tana kare Jikinta sabida daga ita sai doguwar rigar atamfa wadda ta kama jikinta sosai Daga saman Kirjinta ya bullutso yayo sama dama duk ƙanƙantar ta Allah ya bata sama da ƙasa ba laifi kuma masu fusgar hankali.

Aliyu cikin mamakin Halittar Jikinta wadda ya kalla a rashin sani lokacin daze miƙo mata hijabin Ya bata Hijabin Ya fita daga ɗakin Har ya ƙarasa Cikin mota tana laƙai laƙan tafiya Haka ta shigo Cikin motar duk kunya ta gama kamata.
"Raguwa sarkin raki"
Ya faɗa batare daya kalleta ba yaja motar suka bar wajan, a wani haɗaɗɗan restaurant yay parking.
Ya juyo ya kalleta.
"Wait for me, I'm coming now"
Daga haka ya buɗe motar ya fita.
Minti kusan goma sai gashi nan da Ledoji Manya guda Biyu a hannunshi ya zaga Back Seat ya aje su.
Sannan ya dawo ya shiga motar ya zauna ya tayar da motar suka cigaba da tafiya idanunshi akan kwalta.
"Are you waiting for me? be patient"
Taji muryar shi acikin kunnenta ba tare daya kalle taba.
Har suka Karasa bakin layin su.
Babu wanda yayi magana acikin su.
Ya kashe motar ya Fita ya kwaso ledojin Itama ta fito.
"Muje na rakaki"
Ya faɗa, tana gaba yana binta a baya har suka ƙarasa bakin Kofar gidan wanda yayi daidai da lokacin da kawu ya fito daga gidan.
Farha taja da baya ta koma bayan Aliyu cike da tsoro.
"Bawan Allah ga kawu nan na shiga uku"
Ga mamakinta sai taga ya tunkari kawu ba tare da wani tsoro ko fargaba ba.
Ba tada zaɓin daya wuce tabi bayan shi haka tabi bayan shi kamar kazar da ƙwai ya fashewa aciki.
Har ƙasa taga tsugunna yana gaida kawu.
Da gudu tayi cikin gida Kai tsaye ɗaki ta nufa ta haye saman gado.
Jim kaɗan kawu ya shigo yana ƙwala mata kira.
Jiki na rawa ta fito ta tsugunna a gaban shi.
"Allah ya taimake ki, Gobe zasu zo a ɗaura aure amman ki sani duk abin da ya faru dake kada ki nemi gidana"
Daga haka ya juya yabar wajan.
Tana shiga ɗaki Zuhuriyya ta biyota da ledoji.
"Wai gashi inji wani a waje yace wai Allah ya baki lafiya"
Umma ko kallonta batai ba jiki a sanyaye ta ɗebe ledojin ta shige ɗaki.

Aliyu daga wajan Farha gidan Kakannin shi inda ƙannen mahaifin shi suke ya nufa Bayan sun gaisa da baba usman Aliyu ya zaro kuɗi kimanin dubu ɗari ya zube a gaban ƙanin mahaifin shi.
"Baba in Allah ya kaimu Gobe da misalin ƙarfe goma Musa zaizo ya kaiku ɗandago na nemi auren wata yarinya Mahaifinta sadaki kaɗai ya buƙata daga wajena, Amman dan Allah baba wannan magana ta zama sirri bana son Kowa yaji inba sauran kawu naina ba"

Baba usman ya cika da farin ciki addu'a yahau yiwa wannan aure yana saka mai albarka kuma ya tabbatar wa Aliyu da cewa in ba sauran ƙannen shi da zasu je tare ba ko matansu ba zasu ji ba, Aliyu yayi masa godiya yabar Gidan.
Kanshi tsaye gida kuma ya nufa yaje part ɗin Ammi bayan sun gaisa ta kawo masa shayi.
"Ammi nifa gaskiya aure zan ƙara Mami tace sai ta huta zata dawo"
Ya faɗa yana son ya gwada yanayin ta idan har ta amshi maganar sai ya fito fili ya gaya mata gaskiyar shi.
Haɗe ranta tayi kamar yadda ta saba duk lokacin daya zo mata da batun aure.
"Ban amince ba"
Ta faɗa.
"Ammi dalilin ki? shin aurena zai saɓawa shari'a ne ko kuma ƙarin aure haramun ne?"
Ta haɗe ranta kamar bata taɓa dariya ba.
"Ko ɗaya Malam zaka ƙure ni, auren ne kawai banga damar ka ƙara ba ka jira har Allah ya bawa Mami rabonta in ma dan shine kake cewa zaka ƙara aure"
Ganin ta ɗau zafi yasa ya sassauta Murya.
"Allah ya baki haƙuri Ammi ya huci zuciyarki"
Daga haka ya miƙe ya fita daga parlon, Ammi ta bishi da kallon tausayi sai dai ba zata taɓa barin shi yayi aure ba domin tana gudun sharrin matan wannan zamani sannan uwa uba tana taya mami kishi kasancewar ta ƴar yayarta wadda kuma ita ta haɗa auren sabida haka ba zata so ai wa mami kishiya ba.

Daran wannan rana Daga Aliyu har farha sun kwana cikin zulumi.
Washegari gidansu farha ba'a tashi da shirin komai ba kamar ba auren budurwa ba,kawu yace baze gayawa kowa a dangin shiba kuma yace baze kayan ɗaki ba haka umma ma tace ficikarta bazatai ciwon kai ba wajan ƙarfe Goma Baƙin suka ƙaraso Ƙofar Gida Halifa ya kira kawu, Musa sarai ya gane Halifa amman shi Halifa bai gane musa ba dalilin kuwa daya sa Musa ya gane Halifa sabida rabon kuɗin daya yi musu a kamfani, Shi kuma Musa da face mask a fuskar shi wannan tasa Ba kowa zai shaida shiba

Iya maƙota kawu ya kira aka shinfiɗa babbar tabarma a ƙofar gida bayan addu'oi aka ɗaura auren FATIMA ABUBAKAR MAI BULO DA ALIYU AUDU MADAKI, Akan  sadaki naira dubu ɗari addu'a akai aka shafa gaba ɗaya mamaki ya cika musa wanda dama tunda Aliyu yayi mishi waya ya sanar masa acikin mamakin yake.

Buhun goro da alawa Baba Usman daya siyo ya miƙawa kawu aka rarraba Musa ya Ɗebi su Baba usman a mota dan ya mayar dasu gida.
Bayan ya cewa kawu zai zo ya ɗauki amarya su wuce kamar yadda Aliyu ya bashi umarni.

Cikin mamakin sunan wanda aka faɗa da angon farha Halifa yake naɗe tabarman da suka zauna, sai dai tunanin da yayi na suna ai da yawa wanda ake cin karo dashi iri ɗaya yasa ya watsar da mamakin nashi ya shigar da tabarmar gida ya shiga sabgar shi.

Kawu yana shiga cikin gida ya watsawa umman farha sadakin farha.

Tare da cewa.
"Burunku ya cika, Ke kuma maza ki haɗe kayan ki yanzu Mijin ki zai zo ya ɗauke ki, kuma koda wasa kada ki zo min gidana da kowace irin matsala"

A wannan karon umma tai magana Sabida ta riga ta saduda da lamarin.
"In sha Allah wannan aure alkairi zai zame mata, Ni mahaifiyarta ce ya Allah ka kare min ita aduk inda take aduk inda ta tsinci kanta Allah ka sawa mijinta son ta da tausayin ta"
Umma ta faɗa tana hawaye dan jiya nasihar umman zage yayarta ta ratsa mata Jiki wanda tace mata kada ta yarda taiwa ƴarta Mugun baki ko fata.

Bayan musa ya kai su baba usman ya aje su Aliyu yayi masa waya sun jima suna magana kafin Musa ya nufi Gidan su farha cike da mamakin maganganun Ubangidan nashi.

Musa ya ƙarasa har ƙofar gidan yasa yara su masa magana da kawu wanda kawun yace ba inda ze fita farha kawai ta ɗauki kayanta tabi shi Farha kuka Umma kuka da sauran ƴan uwanta wanda kawu yace ba mai binta rakiya itama kuma baya neman tazo masa gida haka Su Ikram suka ɗauki jakar kayan farha wadda suka haɗa mata suka fitar mata da ita wajan mota da ƙyar Babarsu Ruƙayya ta ɓamɓare farha daga jikin Umma wadda take kuka kamar ranta zai Fita. Tana ji tana gani aka saka kayanta cikin Mota itama ta shiga Musa yaja Motar suka Nufi Gidan Mijin nata.

Suna tafe tana kuka har zuwa sanda suka ƙarasa Kofar gidan masu gadi suka Wangale Ƙaton Gate Ɗin adaidai nan farha ta ɗaga kanta tana kallon aljannar Duniya.
Musa ya dube ta.
"Alhaji yace a gaya miki, Sunan shi Ali Madaki wanda kikai jagora wajan Yaɗa labarin shi akan ƙarya sannan yace koda wasa kada ki Kuskura ki nuna kina da alaƙa dashi In kina son zaman lafiya acikin Gidannan"
Jikin farha rawa ya kama tsoro nadama fargaba sune suka rufeta Ruf Auren ɗaukar fansa yayi da ita kenan ashe yaudarar ta yayi ya haɗata da iyayenta ya rabata da saurayin ta Kukan ma kasawa tai a wannan Lokacin tasan kuka ma rahma ne, Tana tuna furucin kawu gabanta ya kuma faɗuwa daya ce kada ta nufo masa gida da ko wace matsala, Lallai Bawan Allah.
Ta faɗa a zuciyarta tana Jan ajiyar zuciya ta kalli gabas da yamma ko ina na gidan akwai jami'an tsaro babu damar guduwa to ina ma zata je
"Fito Muje Ciki"
Musa ya faɗa Bata da zaɓi illa sauka tabi bayan shi hannunta ɗauke da jakar kayanta.
Babban parlon daya fi girman Gidan su suka shiga.
Tsayawa faɗin kyan parlon da tsarin shi ɓata Lokacine Musa ya zauna a ƙasan Carpet itama ta zauna.
Ya kalli dattijuwar dake jera kayan abinci dining.
"Hajja dan Allah ki mana magana da Ammi"
Hajja ta juyo da Far'a kana ta nufi wata hanya Jim kaɗan ta dawo tace masa tana zuwa.
Ƙamshinta ne ya fara yi musu sallama Kafin ta ƙaraso Wajansu Kallo ɗaya farha tai mata ta gane itace mahaifiyar Aliyu dan ga kama nan sosai.

Gaban farha ya faɗi haka kawai taji tana Masifar shakkar Ammi.
Musa ya gaishe da Ammi cikin ladabi itama farha tayi yadda yayi Ammi ta dubi Musa da kulawa.
"Musa kwana biyu Ka Ɓuya?"
Ya shafa kanshi.
"Ammi ayyuka ne suka sha kaina, Dama Ammi Nazo da alfarma wajanki ne wannan ƙanwata ce daga ƙauye Ƴar ƙanin mahaifina babanta ya rasu Shine nazo da ita koda aiki a wajanki a bata"
Farha sakin baki tai tana kallon Musa cikin mamaki.
Ammi tai Jimm.
"Ni ina da masu aiki, Amman Naji Aliyu yana cewa Mai girkin part Ɗinsu tayi tafiya jiya, To zata zauna a ɓangarena Ga ɗaki nan a falo ta saka kayanta zata dinga Min gyaran ɗakina dana su Sajeeda, Sannan ta dinga zuwa part Ɗin Aliyu tana musu girki ina fatan ta iya girkin, albashin ta zamiyi magana da ita anjima naji nawa za'a bata"
Musa ya hau godiya kamar zai ari baki.
Sannan ya tashi yayi musu sallama yabar parlon.
Ammi tace.
"Yaya sunan ki?"
Muryar ta tana rawa tace.
"Fatima"
Ammi tayi murmushin ƙasaita.
"To fati saka kayan ki a wancan ɗakin"
Daga haka ta miƙe ta koma in da ta fito.
Farha Kwantar da kanta tayi a saman kayanta tana sakin wani irin Kuka mai Ban tausayi..........
*LAST FREE PAGE*

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

Wannan shine ƙarshen shafin kyauta base na zauna na rubuto Muku abin da zai faru ba kuma kun san akwai cakwakiya acikin wannan labari In sha Allah duk wanda ya saya zai alfahari da karantawa Nagode masoya sai najiku Allah ya baku ikon siya ya hore muku Amin.
*RABO YA RANTSE*

*17*

*A LOVE STORY 17*
Kuka take da iyaka cin ƙarfin ta Falon babu kowa Bare ta sami mai rarrashinta wata irin nadama marar amfani ce ta rufe ta.
A hankali Hajjo data gama jera kayan abincin ta ƙaraso wajanta.
"Ƴata wannan kuka, Bashi ne ze miki ba haƙuri zaki Kowa da yadda Allah ya tsara masa rayuwar shi"
Share hawayen tayi tare da ɗaukar Jakar kayan nata ta nufi cikin ɗakin da Ammi ta nuna mata a

matsayin nata.
Babban ɗaki ne Mai saitin gado da Wardrobe sai madubi tare da banɗaki acikin sa Kayanta ta aje agaban Wardrobe ɗin ta nufi ƙofar banɗaki Da komai na amfani acikin banɗakin Wajan tap ɗin ruwa ta nufa ta wanko fuskarta.
Ta dawo gefen gado ta zauna tare da zabga tagumi, A fili take furta.
"Bawan Allah ban zaci haka daga gare kaba Dama Ramuwa ce ta sanya kazo kace zaka aure ni, Na yadda dakai na amince dakai na rabu da Salim na ɓatawa umma da kawu rai, Ya Allah ka farkar dani daga wannan mafarki"
Ta faɗa tana fashewa da wani irin marayan Kuka mai cin zuciya darai.

Jin kiran sallar azahar wanda yake nuni da cewa masallacin acikin gidan yake ta miƙe ta shiga banɗaki ta ɗauro alwala tazo ta shinfiɗa ɗan kwalinta Sallah tayi tana zaune tana Tunanin Gidansu Hajjo ta turo ƙofar tare dayi mata sallama.
Ta ɗago idanunta tana amsa sallamar Hajjo.
"Ƴata har yanzu kukan bai ƙare ba, Allah sarki naji Musa yace marainiya ce ke kagi ƴar ƙarama Taso Muje Ɓangaran masu aiki, kici abincin rana ai ke ki godewa Allah ma da Hajiya Ammi ta baki ɗaki a ɓangaransu"
Ita dai Farha bata cewa hajjo Komai ba haka ta miƙe suka fita har Lokacin Falon babu kowa kayan abincin ma Babu alamar an taɓasu.
Suka fita daga Falon wata kwana suka sha wadda sukai tafiya mai ɗan nisa Kafin su ƙarasa wani waje wanda aka zagaye da Doguwar katanga Ɗakuna ne reras har guda Biyar Abin da ya bawa farha mamaki mata ne kusan su Biyar har da yaran su wasu na wanki wasu na tsifa.
Hajjo ta nuna mata wajan zama matan suka bita da kallo.
A hankali tace musu.
"Sannun ku ina yinin ku?"
Suka haɗa baki suka amsa mata Gaisuwar.
"Wannan sabuwar mai aikin hajiya Ammi ce, To ƴata ga ƴan uwanmu ma'aikata nan wannan sunanta tabawa Sharar Falon Hajiya Ammi ne aikin ta, wannan sunan ta Ɗahare Goge Falon Hajiya Ammi ne aikin ta wannan kuma Su ukun suke dafawa masu gadi da masu bawa fulawowi ruwa da masu Sharar harabar Gidan da masu Goge mota Abinci. Ni kuma ni nake Dafa abincin sashin Hajiya Ammi dukkan mu nan A ɓangaran Hajiya Ammi Muke aiki shima Alhaji yadda kika ga nan haka ɓangaran masu aikin shi yake"
Ita dai farha bata gane Maganganun da Hajjo take ta faɗi ba haka ta sunkuyar da kanta ƙasa Hajjo ta shiga ɗaki ta fito da ƙatuwar Roba

Shaƙe da shinkafa da miya da salak da nama ba zaka ce cimar ƴan aiki bace dan ruwa ma na jarka ta ɗauko sai hucin sanyi yake.
Hajjo tace mata.
"Ki saki ranki ƴata kici arziƙi ki barshi a mazaunin shi tunda naji Musa yace ke marainiya ce naji ina ƙaunarki, Kinga ni nan ban taɓa haihuwa ba sama da shekara ashirin nike wa Ammi aiki tun Marigayi nada rai muna tsohon gidan shi na baya kafin Alhaji Ali ya gina wannan komai kike so ki saman zan baki"
Farha taɗan sami nutsuwar maganar Hajjo dan ko ba komai ta sami uwa ta ɗan tsakuri abincin

kaɗan ta miƙe ta Nufi famfo ta wanke hannunta Sauran matan wajan nata kallonta Suna son magana amman daga gani shakkar Hajjo suke sabida da alama Hajjo Boss ce acikin masu aikin gidan.

Zama tayi tana kallon yadda suke harkokin su Gefe guda tana jin yadda Hajjo ke bawa Ɗahare Labarin, Cewar Ammi tace wannan hajjin da ita za'aje Alhaji ya biya mata.

Har wajan la'asar tana zaune can dai Hajjo tace mata ya kamata ta koma ciki koda aikin da zata wa Hajiya Ammi sai da tayi sallah sannan tayi Musu sallama ta tafi.
Ɗahare ta dubi Hajjo.
"Hajjo ina kika samo wannan ƙanƙanuwar yarinyar kuma?"
Hajjo tace.
"Wallahi Musa yaron Alhaji ne ya kawota ɗazu taiwa Hajiya Ammi aiki Ni tausayi ta bani naji yace marainiya ce"
Ɗahare tai jugum.
"Kai hajjo ƙanƙantar yarinyar tayi yawa amman daga gani tana da shekaru damma Allah ya kawo ta hannu na gari matsalar ɗaya ce Ƴammatan Ammi suna da takurawa Mutum Musamman Bashir bai da Kirki gaskiya"
Ire iren maganganun sukai tayi har zuwa sanda suka miƙe domin suyi sallah.
Farha tana shiga Falon Ammi Sajeeda da Safna suna cin Abinci tai sallama Bata kalli saitin suba tayi hanyar ɗakin ta.
Sajeeda ce ta ɗaga Murya sosai.
"Village girl come here"

Sarai ta san da ita suke amman bata waigo ba ta cigaba da tafiyarta.
Safna da wani irin sauri ta ƙarasa wajan Farha ta finciko Hijabin ta.
"ke ƴar ƙauye kina ji ana miki magana dan rashin ɗa'a zaki tafiyarki?"
Farha tabi Safna da kallo doguwa ce sosai fara tana yanayi da shi, Daga gani ba zata wuce sa'arta ba.
"Kiyi haƙuri ban ɗauka dani kuke ba"
Dariya safna ta kwashe da ita sajeeda dake saman dining itama ta taya ta adaidai nan Ammi ta fito falon

"Ku kuma dariyar me kuke Allah ya shirya min ku"
Har Lokacin dariya suke.
Kafin Sajeeda dake dining tace wai Mun mata magana ne da turanci shine wai bata san da ita muke ba Ammi ita ce sabuwar mai aikin namu?"
Ammi itama dariyar tayi tana zama a saman kujera.
"Ita ce, Yarannan baku da dama ke fati Kibi waccan corridor ɗin zaki ga two bedroom nawa kije ki gyara min ki wanken toilet"
Ammi ta faɗa hankalinta kwance batare data tsawatar wa yaranta abin da sukai wa Farha ba.
Jikinta a matiƙar sanyaye ta nufi inda Ammi ta kwatanta matan Ɗakin farko ta shiga ta gyara shi tsaf Na biyun kuwa wanda take zaton na ƴammatan ne taci azabar gyara domin komai a zaune

yake hatta panties ɗinsu sai da ta ɗauke har magariba tana faman Abu ɗaya sabida bata da saurin aiki.

Aliyu tunda ya tashi ya je station ɗin da aka kai Md Direct kotu aka miƙa md Aliyu ya kira lauyan shi suka ɗanyi maganganu dashi sannan aka tsaidar ranar shari'a ranar monday tunda Md har Lokacin yaƙi bada Shaida cikakkiya akan dalilin daya sanya ya yiwa Aliyu wannan Sharri.

Bayan ya rabu da lauyan shi gidan Kakannin shi yaje ya amsa Kiran Baba Usman wanda ya tabbatar Mishi da an ɗauro auren shi Godiya yayi wa Baba usman sannan ya baro gidan Bai shiga gida ba sai bayan sallar magariba kai tsaye kuma Ɓangaran Ammi ya nufa........
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*RABO YA RANTSE*

*18*

*A LOVE  STORY 18*
Sallama yayi a falon Ammi tana zaune A falon bayan ta idar da sallah Safna da Sajeeda suna kwance a saman cinyarta suna charting da wayoyin su a hannayen su Gefe guda ga ƙatuwar Tv tana faman yi.
Ammi ta amsa mai sallamar cikin kulawa ya sami Saman kujera ya zauna da sauri su safna suka tashi zaune suna gaishe dashi fuska babu walwala ya amsa batare daya kalli inda suke ba.
"Ammi wannan abin da kike wa yarannan sam ba dacewa ta yaya yaran da suka isa suyi aure fisabilillahi zaki na ɗora su a saman cinyarki wani ma in ya shigo sai yayi dake"
Ya faɗa yana zabga musu harara sum sum suka Tashi suka nufi hanyar ɗakunan su.

A zuciye suka Faɗa ɗakin nasu Lokacin Farha tana Wanke Toilet ɗinsu Harara sajeeda ta maka wa farha.
"Dallah wuce ki bawa mutane waje jaka! har yanzu kina abu ɗaya gaskiya sai kinbar gidannan dan ba zamu shirya dake ba"
Safna ce ta tankaɗa ta waje suka datso Ƙofar Ran Farha ya Ɓaci, Nan da nan kuka ya tawo mata wanda ta durƙusa a wajan tana yinshi ba ƙaƙƙautawa ta jima tana kuka kafin ta nufi Hanyar ɗakinta sam bata lura da waɗanda suke falon ba ta shige ɗakin faɗawa saman gado tayi tana Cigaba da kukan ta dan abin da su safna sukai mata ya ƙona mata ranta harda ce mata jaka.

"Nace kaji ɗazu musa ya kawo Min mai aiki?"
Aliyu ya sosa kanshi bai nuna alamun ya san da maganar ba.
"A,a ni kam ta yaya zan sani Ammi"

Ya faɗa a taƙaice.
"Yace marainiya ce, ya kawo min ita nidai gaskiya ina da masu aiki da Lagos zan sa akai ta gidan Sadiƙ Ko Sharaɗa gidan salma"
Da sauri Aliyu yace.
"A,a Ammi ki duba ai ba zaki rasa abin da zata yi agidan ba, Tunda yace marainiya ce ai beci ace Kin kaita wani wuri ba shima Musa yaji hakan ba zeji daɗi ba"
Ammi tai murmushi tare da cewa.
"Ni ma tunanin haka dana yi yasa kawai nace zata dinga Muku girki a part Ɗinku tunda ɗazu salamatu tazo Min da batun zatai tafiya ƴarta ta haihu"
Aliyu ya wani haɗe rai kamar bai taɓa dariya ba.
"Gaskiya Ammi ni bana son ƙazanta kawai daga kawo yarinya daga Ƙauye sai ta hau yi mana girki, Duk dani bana cin abincin kowa sai Na Mami ko naki amman bazan so Mami tana cin abincin wadda bamu sani ba"

Ya faɗa yana wani lumshe ido.
"Ai daga gani yarinyar tana da tsafta haƙuri zakai tana muku, Tunda ita mami koda ta dawo ɗin Jikinta bai ƙarfi sosai ba, Sannan kuma ba wai iya girkin zatai kaɗai ba zata Dinga gyara min ɗakina dana su auta tare da wanke mana Toilet"

Aliyu bai ce mata komai ba harta gama maganar tana cewa bari na kirata sai a ji nawa za ake bata a albashin wata.
Ammi ta ɗaga Murya sosai tana kiran.
"Ke Fati zonan"
Cikin hanzari farha ta dafe ƙirjinta dake faman duka.
Ta gyara hijabinta ta fito falon daga nesa dasu ta tsugunna muryarta a dashe wadda take nuni da taci kuka ta Ƙoshi tace.
"Gani"
Ammi ta bita da kallo.
"Matso mana nan dallah malama wa ze ɗaga muryar yi miki magana"
Da sauri farha ta matso daidai saitin Kujerar da Ammi take saman ta wanda ya bata damar kallon inda Aliyu yake zaune ya Fito da wayar shi yana dannawa ya nuna kamar bai san da ita a wajan ba.
"Ka ganta sunan ta fati"
Murya can ciki yace.
"To ni ammi ina ruwana da jin sunan ta duk ma'aikatan dake gidannan nasan sunan su Wasu ma ban san dasu ba, Gaskiya"
Ya faɗa idanun shi akan wayar shi.
Farha takaicin sane ya kamata ta sanya hannu tana share hawayen dake faman zubo mata wai Bawan Allah ne yake nuna mata Ko in kula.
"Nima abin da yasa na gaya maka sunanta har na kirata dan naga Musa ne ya kawota Shiyasa, Fati nawa kike ganin za mu dinga biyan ki?"
Farha tai shuru Aliyu yaja tsaki mai ƙarfi yana Danna wayar Hannun shi.
"Kin min shuru malama, wannan kuka naki baze Fishsheki ba in ma zaki haƙuri ki haƙuri ki

dangana in kuma kukan zaki zan kira Musa na gaya masa"
Da sauri Farha tace.
"Ni dama zaki gaya masa ɗin dan Allah yazo ya fitar dani daga gidannan wallahi bazan iya aikin nan ba na haƙura zan koma ƙauyen kawai"
Daga Aliyu har Ammi zuba mata ido sukai ita ammi tana, tunanin ko sangartata iyayenta sukai da rashin aiki Suka mutu suka barta da aiki, shi kuma Aliyu jinjina ƙuruciyarta yake ko in ta bar gidan ina zata je oho mata.
"Wato ke ba zaki zauna ki nemi na kanki ba Kin saba rashin aiki ƙila iyayenki sun sangarta ki gashi sun Mutu sun barki da aiki To shikenan zan gaya wa Musan in yazo sai ki bishi ɗin baki da rabo"
Aliyu yayi saurin cewa.
"Ammi kada ki biye mata da ƙuruciya a tare da ita, Ki barta a haka zata saba"
Kuka farha ta saka.
"Ni babu abin da zan saba gaskiyata na faɗa akira sa ya mayar dani gidanmu bazan iya wannan aikin ba daga farawa yau har yaran can suna cemin jaka ni ko agida ina da ƙannen da suka fisu girma Duk talaucina ba zan zauna inda ba'asan darajar mutane ba.......bata ƙarasa ba ammi ta wanke mata fuska da mari.
Kafin ta janyota zata rufeta da duka Aliyu yayi saurin janyo farha yayi bayan shi da ita.
"Haba ammi me kike son aikatawa ne baki san amana Allah ya baki ba ita ɗin marainiya ce in kika cutar da ita Allah zai saka mata, Bayan nan akwai Hukumar kare haƙƙin ɗan adam dan tana mai aikin ki baze yuwu ki na dukan taba gaskiya ammi wannan ba daidai bane ba, Ina zaton yarannan zaginta sukai shiyasa take wannan kukan kin san ba kowa ne yasan aci zarafin shi ya haƙura ba dole zata ma gidannan kuɗin goro tunda bata sami karamci daga mutan gidan ba"

Ammi da ranta yakai ƙololuwar Ɓaci bata iya ce masa komai ba sabida ammi mace ce mai jarabar son ɗa ko kaɗan bata ƙaunar laifin ƴaƴanta Musamman waɗannan Biyun da kata ɓasu gwara ka taɓa kowa agidan shiyasa suke cin karan su babu babbaka suke taka uban kowa a ma'aikatan ɓangaran nasu kowa haƙuri yake dasu Aliyu kaɗai suke shakka shine yake cin Ubansu kai tsaye.

"Wuce ki bani guri ƴar ƙauyen banza in baki saita bakin kiba wallahi kafin kibar gidannan sai na miki Illah akan ƴaƴana ke har wace da zaki zo gabana kina magana yadda ranki yake so, Karkiga Musa ne ya kawon ke duka zakici kamar jaka"
Da gudu Farha tabar wajan tana wani irin Kuka.
Aliyu zeyi magana Ammi ta ɗaga masa hannu alamar bata buƙatar maganar shi sai da ta ɗauki lokaci kafin tace.
"Ka kira min musa yazo ya ɗauki wannan yarinyar"
Kai tsaye yace.
"Ammi ki haƙuri gaskiya ba zan iya cewa musa mahaifiyata ta kasa riƙon ƴar uwarshi ba sabida Musa mutum ne mai sona mai ƙaunata ya ɗauke shekaru yana min hidima ganin mun zama ɗaya ne yasa har ya kawo miki ita a ganinshi zaki iya Riƙonta"
Ammi miƙewa tayi bata ce komai ba tabar falon tayi hanyar ɗakinta ta shiga ciki ranta a mugun

Ɓace.

Aliyu ya jima a zaune kafin ya miƙe kanshi tsaye ɗakin da farha ta shiga ya nufa.
Rufo ƙofar yayi tare da zira key kwance take a saman gado kuka take mai sauti ya janyo stool ya ɗora ƙafarshi ɗaya akai ya zuba mata ido kafin yayi gyaran murya.
"Idan kika ce rashin kunya zaki wahala zaki sha a gidannan koni da Ammi ta haifa ina mata ladabi wajan furta magana"
A ƙufule ta ɗago ta zuba mai jajayen idanunta.
"Ni kuma da aka siyo jaka ba zan mata ladabi wajan maganar ba daga nan suyi ta dukana har mahadi ya bayyana"
Ta murguɗa mai baki ta juya mai baya tana cigaba da kukanta.
Can ta kuma cewa.
"Kuma Allah zai saka min abin da kayi min, Bazan ji ko mai akan duk wata matsala da zata sameni ba tunda nina ƙi bin maganar iyayena kuma alhakin salim ma baze barni ba amman daɗina ɗaya addu'ar umma ba zata taɓa barina na sha wahalar da kake son ganina cikin taɓa"
Ta faɗa cikin kuka har da shashsheka!
Murmushi yayi mai sauti.
"Burina na ganki kullum kina kuka masifaffiya, Kin yi jagora wajan jefani acikin matsala sabida ƴar ƙaramar Buƙatarki wadda in da zaki biyo jerin Masu Roƙona na taimaka musu dana baki ninkin ta amman kika gwammace kiɗa akan karatu"
Cikin kuka tace.
"Allah ya kiyaye nazo na roƙi abu a wajan wanda bai san darajar ɗan adam ba mai karya alƙawari wallahi mutane kallon Kitse suke wa rogo amman kai asalin Mugune mayaudari"
Wata irin tsawa ya buga mata cikin har gagi kamar ze doketa ya ce mata.
"Be quiet to me ke har kin isa ina magana kina magana dan baki da mutunci ni sa'anki ne? kada ki ga nai miki maganganun soyayya a baya ko kaɗan maganar ce kaɗai a harshena amman ko Haƙorina bata taɓa ba ban taɓa jin son ki araina ba kamar yadda kika sani na aure kine danna Hukuntaki akan laifin ki, wanda son zuciya ya sanya kika aikata shi gaba in aka ƙara yi miki tayin Aiki irin nawa ba zaki ƙara yi ba stupid"

Cikin kuka tace.
"Ai aiki nayi ba maula ba kuma wallahi ko yanzu nabar gidannan sai nayi maka abin da yafi wannan Mayaudari macuci wallahi na tsanake Allah ya saka min"
Yayi murmushi wato rashin kunya a jininta yake ya lura bata tsoro tana da kafiya irin su basa Saduda barin hali sai Mutuwa.
"Ke har kina tunanin barin gidannan? to bari kiji Naga alama baki san ciwon kanki ba shiyasa naga kinfi dacewa da wanke wanke da sharar gidannan dan baki kama da ƴan jarida ba sai Ƴar aiki sabida ɗan jarida mutum ne mai nutsuwa mai ilimi mai bincike da hangen nesa Amman ke asalin jahila ce marar kan gado ke in banda baki da hankali ko igiyar takalmina kin kai matsayin ki riƙe bare Kiji nace ina son ki har ki yarda lallai rashin tunanin ki yayi yawa Duhun kai da jahilci yasa kikai gigin aurena zaki mutu da igiyar aurena akanki Ko Ƙofar gida ba zaki Ƙara leƙawa ba zaki zauna ki dawwa ma anan kina mana bauta nida mahaifiyata da matata in kinga kin fita daga gidannan to gidan zoo aka kaiki ganin dabbobi ƴan uwanki"

Daga haka yaja ƙofar da ƙarfi yabar mata ɗakin.

"Innalillahi wa'innah ilaihirraju'un"
Farha ta faɗa da ƙarfi tana sakin wani irin kuka tashin hankali ba'a saka maka rana.......
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*RABO YA RANTSE*

*19*

*A LOVE STORY 19*

Farha tayi kuka har ta godewa Allah gashi babu mai rarrashinta ga wani irin tsoro daya cika mata zuciya sabida ta lura ɗakin tane kaɗai a falon su ɗaku nan su yana cikin wannan corridor ɗin data je ta gyara musu Haka ta ƙudundune Jikinta waje Ɗaya Har bacci ya fara ɗiban ta sai ta tuna batayi sallah ba ta miƙe taje toilet tayo alwala ta shinfiɗa Ɗankwalin ta tayi sallah ta jima tana addu'a Akan Allah ubangiji ya kawo mata mafita acikin halin data shiga kafin ta shafa addu'ar ta jingine kanta ajikin gado Bacci Ɓarawo ne ya sace ta wajan.

Aliyu yana shiga part ɗinshi tuɓe kayan jikin yayi ya rage daga shi sai Dogon wando fari da single ƙasa ya sauka ya haɗo coffee sai tururi yake ya zauna a saman sopa yana sha ya kammala ya jona system ɗinshi a charging, ya rage hasken ɗakin ya kwanta tare da janyo ƙaramin Pillow ya matse shi.

Duk rufe idanun da zeyi Hoton fuskar yarinyar yake gani tana kuka, yadda Ammi tai mata abin ya dame shi sosai yadda ƙannen shi suka cimata mutunci abin ya taɓashi sosai ya mirginawa gefe yaji Muryarta tana amsa kuwa acikin kunnen shi lokacin da take ce masa tasan baze cutar da ita ba.
Tashi yayi zaune tausayin tane ya rufe shi sabida shi mutum ne mai tsananin tausayi duk zafin ranshi da kafiyar shi yana da saurin tausayi.
Miƙewa yayi tare da ɗaukar jallabiyar shi daya rataye ya ɗora ta a saman Wandon jikinshi ya zira slipers, Ya sauka ƙasa Ya buɗe ƙofar falon ya fita gidan yayi shuru sosai sabida dare daya soma yi, Kai tsaye ɓangaran Ammi ya nufa ya Buɗe Ƙofar Falon ya shiga hatta Tv ɗin ba'a kashe ba Hasken falon ma haka da alamun tun tashin da Ammi tayi ta shiga ciki bata kuma fitowa ba kashe hasken falon yayi ya kashe tv Sannan ya shiga ɗakin Farha Hasken ɗakin yana kunne Tana zaune akan ɗankwalinta da alamun sallah ta idar bacci ya ɗauketa a wajan Ya ƙarasa gabanta ya tsugunna ya zuba mata ido murmushi ya saki Aranshi yana Jinjina ƙanƙantar ta sai Masifa da rashin kunyar tsiya.
Ɗagata yayi cak ya ɗora a saman gadon ya zare mata hijabinta ya ƙara mata Ƙarfin Fankar ɗakin sannan ya kashe mata ƙwan ya rufo Kofar ya fita Mayar da ajiyar zuciya yayi ganin tayi

bacci bata cigaba da kukan ba.
Shima koma yayi bai kwanta ba alwala ya ɗauro ya cigaba da sallah har wajan ukun dare sannan yayi sha'i da wutiri ya kwanta bacci ana asubahi kuma ya farka yay raka'atul fijir ya fita masallaci daga masallaci Kayan training Ɗinshi ya zo ya saka ya fita Filin motsa Jiki wanda ya kwana biyu baiyi Morning training Ɗin nashi ba, Bayan ya dawo kuma wanka yayi ya kwanta bacci kafin zuwa anjima ya fita office

Bacci take mai cike da firgita haka kawai take firgita acikin baccin nata wataƙil ko sabida rashin sabon kwanciyar kaɗaici ne oho! sabida ta saba da kwanciyar Gidansu duk da ita kaɗai take kwana a uwar ɗakin umma amman Tana jin hayaniyar Mutan gidan nasu.

Sam bataji kiran sallar asubahi ba haka taita bacci har rana ta fito batayi sallah ba dama al'adar Ammi da sunyi sallar asubah baccin su suke koma In  su safna basu da lecture ma har wajan 12 bacci suke Hajjo zata jera musu abincinsu masu gyaran falo su gyara Su kuma duk sanda suka ga damar Fitowa zasu fito suyi break ɗinsu su kunna kallon su batare da wata damuwa ba.

Sai wajan 11 wayar bashir ta farkar dashi wanda yake masa bayanin motocin sun iso kamfanin shi na abuja duk kuma abin da ya dace sunyi shida manager sabida haka gobe ko jibi ze tawo kano.
Suna gama wayar da Bashir ya miƙe Ya kuma shiga bathroom ya jima aciki kafin ya fito da ruwa ajikin sa alamun wanka ya sako, Ya shirya cikin black trouser tare da white shirt mai dogon hannu wadda ta fito da zatin Ƙirar Jikinshi Ya fesa turare ya maƙala Baƙin agogon fata a tsintsiyar hannun shi ya ɗauki Black shoe mai Buɗaɗɗan sama ya sanya ya ɗauki wayarshi kai tsaye Part Ɗin Ammi ya nufa domin su gaisa ya fita Office Duk inda ya gifta ma'aikatan gidan na zubewa suna gaishe dashi har ya shiga Falon Ammi abin mamaki babu alamun sun tashi daga bacci ya ɗaga kai ya dubi agogon bangon dake ɗakin Ƙarfe sha ɗaya har da Mintuna arba'in.
Zama yayi a saman one seater har wajan 12 babu motsin kowa miƙewa yayi ya shiga ɗakin Farha abin mamaki ya bashi yadda ya kwantar da ita haka yazo ya same ta a sheme baccinta take sosai da alamun Kuma baccin yana mata daɗi dan da alama ko sallah bata yi ba.
Toilet ya buɗe ya taro ruwa a hannunshi yana zuwa daidai fuskarta ya yayyafa mata ruwan Firgit ta Miƙe tana sosa fuskar tata da alama Sanyin ruwan ya ratsa mata Jikinta.
Ya koma jikin Kofa yayi folding hannunshi fuskarshi a ɗaure ya dube ta.
"Why are you sleeping like this until it is time for prayer?"
Da sauri ta kalli saitin window, ah lallai yace baccin me take haka har lokacin sallah ya wuceta, Sai dai ta ɗan tsorata sanda taga inda take a kwance ita dai tasan a saman ɗan kwalinta ta kwanta to waye ya hawo da ita saman gado.
Ta juyo ta kalle shi ganin yadda ya ɗaure fuska Ya haɗe girar sama data ƙasa ya sanya tai maza ta sauko daga saman gadon shaf ta manta babu hijabi ajikinta ta wuce shi ta shige toilet alwala ta ɗauro harta fito yana nan tsaye aranta tace ko soja ya rufa maka baya kai dai baka gajiya da tsaiwa kamar yasan abin da take faɗi kenan azuciyarta sai jin muryarshi tayi yana cewa.
"Why are you looking at me or you are not praying?"
Ɗankwalin ta shinfiɗa a ƙasa ta tayar da sallah har ta idar yana tsaye ta jima tana addu'a kafin

ta shafa ta juyo Ta kalle shi Tai ƙasa da kanta cikin rawar murya tace masa.
"Ina kwana"
Bai amsa ba ya cigaba da magana.
"Ina wayar da na baki ki saita alarm amman No Need ki dinga Missing jam'i bayan akwai masallaci acikin gidannan,Take care that I don't catch you again and don't pray early"
Ya faɗa mata hakan lokacin da yake ƙoƙarin Buɗe ƙofar ya fita.
"Amman dan Allah in ka fita ka sa azo ayi sauka a ɗakinnan"
Cikin mamaki ya juyo ya dube ta.
"Sauka kamar yaya I don't understand you"
Hawaye ta matso da yawa muryarta na rawa.
"Nidai na san a ƙasan ɗankwali na nayi sallah na kwanta amman dana tashi na ganni a gado"
Ta faɗa tana sakin kuka mai ƙarfi.
Dariya ta bashi amman bai yi yadda zata ga dariyar tashi ba.
"Toke mai yasa kika yi salla a ƙasan bayan akwai carpet a ɗakin?"
Shuru tayi masa tana cigaba da kukan ta da gaske dai tsoron ɗakin takeji.
"Shikenan dama nine na gayama aljanun ɗakin su dinga hawar dake saman gado in kinyi bacci har bakin masifa ma zasu dinga Yankewa"

Da sauri ta miƙe ta biyo shi tazo gab dashi kamar zata Rungume shi hawaye take.
"Dan Allah kayi hakuri ba zan kuma maka magana ba daga yau"
Duk yadda yake Kunshe dariyar sai da ta fito Ya ɗan yi dariyar kaɗan wadda ta ƙara haska zatin kyan shi.
"Tom naji jeki ki gyara kayanki ki jera su kije ki break ba zasu kuma ba"
Daga haka ya fita daga ɗakin Bakin gado ta koma ta zauna tsintar kanta tayi tana murmushi sabida yadda yayi mata magana yanzu cikin sigar son ya kwantar mata da hankali.

Lumshe ido tayi tunanin Ummanta da Missing ɗin ƴan gidansu ya kamata.
*WACECE FARHA* ?
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*20*

*A LOVE STORY 20*
Malam Abubar ɗan asalin ƙaramar Hukumar gwale dake kano ɗan cikin unguwar Mandawari mazaunin unguwar Ɗandago, Ɗa Na uku a wajan mahaifin shi Malam Abubakar tun asali sana'ar sai da Bilo yake da ita ya tara kuɗi yayi aure inda yake zaune da matar shi guda ɗaya indo Wanda yadda Allah ya hore masa a sana'ar tashi ta siyar da Bilo idan ya yi Sai ya ƙara aure ya auro Hafsatu dukkan su matan nashi Jera haihuwa suke Farko indo ta haifi Adama Sai

Hafsatu ta haifi Samira haka suke ta haihuwar su kufi a kufi har sai da suka haifi ƴaƴa biyar biyar duka mata Ganin haka yasa Hankalin Abubakar ya tashi sabida yana masifar son ya haifi ɗa namiji Sai ya fara neman aure a nan cikin Ƙoƙi ya haɗu da Asiya yaje wajan Abokin shi Asiya itace ƙarama a gidansu yayinta duka matane iyayen su sun rasu tun suna ƙananu Riƙonta sai ya koma hannun yayarta.
Abubakar bai ƙasa a gwiwa ba wajan Neman auren asiya wadda a lokacin ba wata babba bace sabida tana da ƙaramin Jiki sosai Yayin ta da farko sunce ba zata su turata tai kishi da mata har Biyu ba sabida yarinya ce amman yadda Abubakar ya dage Haka suka bashi Asiya ya aura ya kawota gidan shi wanda Hafsa da Indo suka haɗe wa Asiya kai suda ƴaƴan su Faɗin irin Wahalar data sha agidan ba ɓata baki ne dan hatta wankin su dana ƴaƴan su ita take Musu a wannan Lokaci haka zalika Ranar girkinsu ita ke Musu girkin a wajan Mijinta kaɗai take samun sassauci dama kuma sai baya nan suke gana mata azabar.
Cikin haka mahaifin Abubakar ya rasu Dama mahaifiyar shi tuni ta jima da mutuwa ranar sadakar bakwai haka matan gidan sukai tafiyarsu Umman zage Babbar yayarsu Asiya tazo gidan kamar an jefo ta taga Asiya gurfane a gaban ƙatuwar tukunya tana faman hura wuta.

"Sallamau alaikum"

Umman zage tayi sallama.

Asiya ta ɗago ido fal hawaye da majinar hayaƙi.

"Umman zage ce agidan namu sannu da zuwa"

Asiya ta faɗa tana Goge fuskarta.

Ta miƙe tsaye ta shiga ɗaki ta ɗauko tabarma ta shinfiɗa wa Umman zage wadda ta tsaya ta zubawa ƴar uwarta ido cike da tausayawa.

"Umman zage ki zauna bara na kawo Miki ruwa"

Cewar Asiya tana nufar randa ta ɗebowa Umman zage ruwa mai sanyi ta kawo mata gabanta ta ajiye mata.

Umman zage bata ɗauki ruwan tasha ba ta dubi Asiya.

"Auta kinga yadda kika koma kuwa? gaba ɗaya kinyi baƙi kin sake ramewa anya kina jin daɗi acikin gidannan kuwa?"

Asiya ta ƙaƙalo Murmushin dole.

"Umman zage, Lafiya ƙalau kawai Baƙuntar zaman waje ɗaya ne"

Ta faɗa tana ɓoye damuwarta, dan kada ta ɗagawa ƴar uwarta hankali.

"Auta idan kin Ɓoye min damuwarki wa zaki gayawa Mahaifan mu sun Mutu sun bar Min ku har ku Huɗu nice babba acikin ku, Dan haka kada kiji shakkar gayan matsalar Ki Kinji Auta Ba zamu bari ki zauna cikin matsala ba"

Asiyah sai ta fashe da kuka.

"Wallahi Umman zage tun da nazo gidannan nike wa matan gidannan Komai hatta Wankin kashin ƴaƴansu, Yanzu ma sun tafi gidan gaisuwa Basu tafi dani ba sun bar Min girkin su kuma idan yazo faɗa zemin yace banje ba Kinsan shi mafaɗaci ne a wajan sa kaɗai nake samun sassauci"

Tunda ta soma magana Umman zage ta zuba mata Ido ita takaicin Asiya ma shiya fi Komai Ɓata mata ranta.

"Shi Mijin naku ya sani?"

Da sauri ta girgiza mata kanta Alamun bai sani ba.

Umman zage ta Ɗaga waya ta kira Abubakar bayan sun gaisa.

"Abubakar yaya ƙarin haƙuri?"

Daga nasa ɓangaren yace.

"Alhamdulillahi Babbar Yaya ya yaran namu?"

Umman zage tace lafiya lau.

"Dama ina gidan kane in kana kusa kazo in kuma Baka kusa nasan an maka rasuwa to zan rufo maka gidanka na tafi da Asiya Gidana in ka dawo ka biyo zamu yi magana"

Asiya ta zubawa Umman zage ido tana kallon ta dama tasan za'ai haka shiyasa tsayin watannin datai agidan tana fuskantar matsalaloli bata taba kai wa Umman zage Kukan taba sabida tasan halin ta macece wadda ba'a taka mata nata tana da zafi sosai.
Haka zalika sauran Yayin nata suke su Umman ɗorayi suma duk zafi gare su Ita kaɗai ce mai sanyi tana da haƙuri sosai.

Abubakar ya gigice.
"Lafiya Babbar Yaya? Ganinan base kun kai ga tafiya ba"
Daga haka Umman zage ta kashe wayar bala'i ta shiga surfawa ta inda ta shiga ba tanan take fita ba.

"Tirr da wannan sanyi naki ni akwai kishiyar data isa ta juyani wallahi ba'a haifeta ba baki gado muba kina kallona dai sai dana riƙeku har ku huɗu na aurar daku ai ina da kishiyoyin wa kika gani acikinsu tana muku daidai da kallon banza to zama samun guri tafiya rage tsaiwa"

Ita dai Asiya hankalinta duk a tashe yake na wayar da Umman zage tayi wa Abubakar sabida Tasan In Umma ta tafi ƙarshen abin akan ta zai ƙare, Jimawa kaɗan Yayi sallama ya shigo ya janyo kujera ya zauna Yana gaishe da umman zage.

"Babbar yaya ina yini?"

Ta dube shi

"Lafiya ƙalau, yaya daɗin haƙuri?"

Yace.

"Lafiya lau, Ya kuka je gida? angode Allah ya bada lada"

Umman zage tace.

"Amin"
A taƙaice.

"Dama nazo ne domin na kuma yi maka gaisuwa sai na tarar da Asiya ita kaɗai kaga waccan ƙatuwar tukunyar da take akan Murhu matan ka sun bar mata tai musu Girki fisabilillahi ina asiya ina waccan Tukunyar salon Kirjinta ya buɗe"

Abubakar ya haɗe rai a take anan

"To ƙararsu ta kawo Miki kenan? to ai girki ita ya kama tunda su ne masu ƴaƴa dole zasu je Wajan gaisuwa ita kuma tai musu abinci"

Ya faɗa yana hararar Asiyah wadda ta Sunkuyar da kanta a ƙasa.

"Duk ba wannan ba Asiya ta sanar dani irin zaman da take agidannan zamane na bawa da uban gidan shi ita ke wa matan ka wanki hatta girki ita ke Musu to Asiya dai zama dakai bai zame mata dole ba idan Babu hali ka sakar min abata na tafi da ita yanzu base anjima ba"...............

*RABO YA RANTSE! Iittafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya

09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*21*

*A LOVE STORY 21*
Jikin Abubakar ya ɗauki rawa cikin sauri ya dubi umman zage wadda harta Miƙe tsaye yace mata.

"Dan Allah dan Annabi kiyi haƙuri, Babbar yaya kin san ba zan taɓa cutar da Asiya ba"

Da sauri ta katse shi da cewa....

"Cuta ta nawa kuma Abubakar aini ka shani na warke yanzu fa agabana ka rufe ido kana cewa, Girki ita ya kama tunda ita ce marar ƴaƴa to kaga kenan kana goyon bayan Matanka ne"

Shima da sauri ya tashi kamar zai durƙusa mata.

"Wallahi Babbar yaya ba haka bane"

Ta ɗaga masa hannu.

"Haka ne mana Abubakar, Alhamdulillahi tunda kai da bakinka kace bata haihu ba kaga zatai daɗin samun wani Mijin da zarar ka sake ta"

Ya haɗe girar sama data ƙasa.

Muryarshi a kausashe ya dube ta.

"Nidai a mini afuwa idan hakan ta sake faruwa ki ɗauki dukkan hukuncin da kika ga dama, Asiya tana sona ina son Asiya, Na rantse da Allah akaf matana ita nafi so kuma itama ta sani rabani da asiyah kamar Yimin Illah ne"

Ya faɗa kamar zai kuka!

"Naji to amman da sake, Daga yanzu ka dinga saka idanu akan al'amuran gidanka idan ba haka ba gaskiya zaka zo watarana ka tarar na Ɗauke Asiyah dan ba bora bace"

Da sauri yace.

"Naji babbar yaya kuma na Amince, In sha Allah! Hakan kuma ba zata kuma faruwa ba Indai nine mai gidan zan tsawatar"

Daga haka Umman zage ta dubi Asiya wadda har Lokacin taƙi ɗagowa.

"To sakarai saiwa sala, Saura ki zauna tsoro suda ƴaƴansu su cigaba dayi miki izaya Wallahi na kuma zuwa na tarar dake A wannan yanayin tafiya zanyi dake ba soba nina ga laila majunun"

Har ƙofar Gida Asiya ta raka Umman zage Tana kuma jaddada mata akan ta Miƙe tsaye tana karɓar ƴancinta agidan Haka ta dawo Abubakar ya tare ta yana huci kamar zai kawo mata duka.

"Ke ashe baki da hankali da tunani ke sakarar ina ce, Waya gaya miki ana fallasa sirrin aure Kuma ni kin taɓa gaya min halin da kike ciki agidannan?'

Ya faɗa kamar zai mareta.

Jikin Asiyah yana rawa tace.

"A,a ban gaya maka Allah ya baka haƙuri"

Ya ƙara matsowa yana tattare hannun riga da gudu tayi ɗakinta ta rufo ƙofa Ya ƙaraso bakin Ƙofar yana cewa

"To na rantse da Allah kika kuma gayawa wani sirrin gidana sai ranki ya ɓaci marar hankali wadda bata san ciwon kanta ba"

Haka ya ƙaraci bambamin sa da cin mutuncin sa yabar Gidan Yana fita ta fito tana duba tukunyar shinkafar data ɗora Ƙauri ne ya cika hancinta shinkafar tayi Baƙi ta ƙone ƙurmus gashi babu wata dama Girkin Indo ne kuma mai girki ce take riƙe makullin ɗakin adana kayan abincin gidan.

"Wayyo Allah! yau na shiga uku a wajan matan gidannan umman zage dama baki zo ba"

Ta faɗa a fili tana fashewa da wani irin Kuka! har akai la'asar tana kuka gajiya tayi da kukan ta nufi banɗaki ta ɗauro alwala itama yunwar take ji amman tunanin tashin hankalin matan gidan har yafi mata yawa akan yunwar cikinta.

Haka ta wanzu acikin ɗaki har akai magariba tayi sallah ga gidan shuru ba kowa ga ba wuta duk tsoro ya cikata can wajan bayan sallar isha'i suka shigo da koke koken Ƴaƴansu gaban Asiya ya yanke ya faɗi ta kuma shigewa ƙuryar ɗakinta ta Ɓuya.

Hafsatu ce ta ƙaraso bakin ƙofa.
"Ina yarinyar gidannan ina abinci ƴaƴanmu suna ta kuka?"

Asiyah ta kuma ɓuya tana saro ido waje cikin hasala Hafsatu ta kuma ɗaga murya.

"Ke Hasiya su waye sa'annin ki kina ji muna miki magana zaki fito ko sena shigo?"

Cikin sauri Asiyah ta janyo mayafi ta fito waje har ƙasa ta zube tana cewa

"Sannun ku da dawowa"

A fusace indo tace mata.

"Mu ba wannan muke buƙata ba ina abinci? da yunwa muka shigo cikin gidannan"

Asiya ta soma ruwan hawaye

"Wallahi Ban sani ba ya ƙone sai dai na dafa muku wani"

Da sauri indo tace.

"Me kika ce? kina nufin shinkafar har kwano guda ta ƙone kina ubanki?"

Hafsatu ce ta rufe Asiyah da duka indo ta tayata Samira da adama dasuka ɗan fara tasawa suna dariya harda riƙe ciki.

Zuwa lokaci kaɗan Asiyah ta jigata ta fara haki tana wani irin Numfashi sai suka tsorata suka rabu da ita Suna hankaɗata ɗakinta yadda suka daketa haka suka barta kuma itama bata iya tashi ba sabida Jinin dake zuba ta ƙasanta.

Mararta na ƙullewa tana curewa waje ɗaya tuni sun manta da ita sun shiga hada hadar ɗora abincin dare sabo tunda wancan ta Konar suna yi suna mita  cikin haka Abubakar ya shigo gidan kai tsaye ɗakin asiyah ya nufa sai dai yaci karo da ita abakin Ƙofa tana nishi ya ɗagata yana cewa

"Asiyah mai ya same ki?"

Idanu ta lumshe kafin ta fara nuna masa mararta tana Nishin azaba.

Da ƙarfi ya furta.

"Indo zoki taimaka min mu fitar da ita a sami motar asibiti, da sauri kamar gaske tazo ta kama Asiya shikuma ya fita ya samo mota suka sakata aciki suka tafi asibiti Cikin hanzari Likitocin asibitin suna amshi Asiya suka ɗorata a gadon tura marasa lafiya suka shiga wani ɗaki da ita.

Abubakar ya kasa zaune ya kasa tsaye tsoron shi ɗaya shine kada asiyah ta rasu idan ta mutu shima kanshi yasan yayi asarar mace tagari sannan idan ta rasu ta wannan hanyar yasan Ƴan uwanta ba zasu barshi ba ya juyo ya kalli indo wadda tai tsuru kamar shege a rabon gado

"Ke indo mai ya same ta ne?"

Cike da bariki tace

"Muda muka shigo gidan a lokacin mukasan abin da ya same ta"

Ya girgiza kai ya cigaba da safa da marwa a wajan hannunshi a bayan shi yama rasa wani tunani ne zeyi a wannan lokaci Ko wanine ya shigo gidan ya doke ta ko faɗuwa tayi ta buge dan shi tunda ya gama bala'in sa daya bar gidan bai kuma shigowa ba sai yanzu.

Likitan ne ya fito daga ɗakin ya dubi Abubakar wanda ya kasa zaune ya kasa tsaye yace masa.

"Malam in ba damuwa ina son ganin ka a office ɗina".............

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*22*

*A LOVE STORY 22*
Da sauri indo ta matso wajan shi ganin kamar ya damu sosai da kiran da likitan yayi mishi. Dafashi tayi cikin kwantar da harshe wanda ta iya ta furta masa.

"Kawun su kada ka damu, Ba mamaki faɗuwa tayi, dammu ma da muka dawo daga Gidan rasuwa maganar duniya munyi wa yarinyar nan amman muka ji shuru shinkafar ma ta ƙone da alamun tun rana data ɗora bata duba taba"

Ya ɗago idanu jajir ya dube ta.

"Indo naga kamar Asiyah bata Numfashi indo inna rasa Asiyah nima tawa ta ƙare binta kawai zanyi sabida soyayyar da nake wa Asiyah"

Takaici ya kama indo ta fahimci kamar ya mance dawa yake tare yake yabon kishiyarta a

gabanta Bata kuma ce masa komai ba ta koma saman benchi tayi zaman ta shikuma yabi bayan likitan zuwa Office ɗin nashi.

"Salamu Alaikum, Likita na ɓata maka lokaci kayi haƙuri fa"

Kawu ya faɗa yana zama a saman kujera likitan yana ta rubutu a saman farar takarda.

"Wassalam, kada ka damu, dama gashi maganine zaka siyo mata yanzu dai an samu cikin nata bai zube ba sai dai a kula da bata tsoro ko ɗaukar abu mai nauyi da sauransu"

Likitan ya faɗa yana miƙawa kawu farar takardar.
Kawu ya washe baki.

Yana cewa.

"Alhamdulillahi Asiyah ɗauke da cikina kai nagode wa Allah yau sai na raba sadaka Allah yasa namiji ne"

Likitan yabi shi da kallo yana mamakin wannan murna da Mutumin yake yi.

Kawu fita yayi pharmacy, yaje ya siyo magungunan kamar yadda Likitan ya rubuta masa sam baiji tsadar magungunan ba haka ya siyo harda allura ya kawo wa likitan.

Likitan ya amshi alluran ya nufi ɗakin da aka kwantar da Asiyah yayi mata ya dawo.

Da sauri kawu ya tare likitan.

"Likita yaya jikin Asiya ko zan iya ganin ta?"

Likitan yayi dariya! sabida yadda ya hango tsantsar ƙauna da kulawa a wajan Mijin nata.

"Mijin Asiyah jeka gano jikin ta koka barmu mu sarara"

Kawu har yana tuntuɓe wajan nufar ɗakin hangota yayi kwance samɓal a saman gado fuskarta tai fayau idanunta a rufe.
Ya ƙarasa gaban gadon ya zauna yana kamo hannunta.

"Sannu Hasiya Allah ya rabaki da cikin nan lafiya"

Haka ya zauna harta farfarɗo Yana ta zuba mata sannu Ita dai bata ce masa komai ba har Likitan ya dawo ya basu sallama suka tafi gida kawu sai faman riritata yake kamar ƙwai.

Suna zuwa gida ya tara matanshi da ƴaƴan shi yace kada a kuma saka Hasiya komai agidan

yaja musu kunne Baƙin ciki kamar ya kashe su haka sukai ta gunguni sanin halin shi yasa Basu nuna ƙin amincewar su da sharuɗan nashi ba.

Haka rayuwar ta cigaba da tafiya daga ɓangaran Abubakar ( kawu )  kamar ya goya asiyah dan tsabar so da tattali sai dai idan ya fita ne matan gidan suke ƙuntata mata musamman Indo dan tafi Hafsa Iya kirsa da Iya wuri Cikin Asiyah tuni ya fito yana ta girma abinda take so shi take ci.

Ga wani irin buɗe da Allah yayi wa Kawu dan sosai Allah ya wadata shi har gyaran gida yayi musu wanda hakan ya kuma ƙuntata zuciyar matan gidan.

Asiya tana gab da zata haihu ƴar wajan Indo sadiya ta rasu Kuka kamar Indo zata haɗiyi zuciya A daddafe akai sadakar bakwai ranar Allah yasa Asiya ta fara naƙuda wadda Umman zage tazo ta kaita asibiti zuwa dare ta haifo ƴar ta mai kyau jajir kamar mahaifinta sak.

Kawu daya je asibitin ya ɗaga jinjira a maimakon yayi takaici ba namiji ya samu ba sai yahau murna nan da nan yaji son yarinyar ya shiga zuciyar sa.

"Hali dubu komai naki dubu ne Allah ya raya ki Halimatussadiya"

Cewar kawu yayi mata huɗu ba da sunan marigayiya ƴar wajan indo fafur da aka sallame su Umman zage taƙi kai asiyah gidanta haka ta tafi da ita zage domin tace Asiya ina zata iya wankan jaririya kawu badan yaso ba yabar ta haka akai suna yarinya taci Suna Halima Kamar yadda ubanta ya raɗa mata cigaba sukai da wanka har na tsahon kwana arba'in kafin ta zagaya gidan ƴan uwa bayan tayi arba'in ɗin kana ta dawo ɗakin ta in ka kalli Asiya da Sadiya sai ka ƙara kallo sabida kyan da sukai da ƙiba.

Ta ɗan sami sassauci agidan sabida yadda Indo take son sadiya Dan bama ta iya cewa sadiya sai dai tace sadiyata sabida sunan ƴarta da kawu ya sanyawa sadiya.

A hankali sadiya ta Cigaba da girma yarinya mai wayo da dubara koda yaushe tana tare da uwarta dan bata yarda da kowa agidan cikin haka suma su indo suka sami juna biyu Lokacin kuma ana shirin Bikin Adama da samira lokacin yaran sun gama primary Kawu ya ce aurar dasu zeyi iyayen nata kuka akan ƙanƙantar ƴaƴan haka kawu ya samo musu mazaje ƴaƴan abokan shi akai bikin su adama tana agadasawa ita kuma samira tana mandawari.

Ba jimawa su indo suka haihu indo ce ta fara haihuwa sai hafsatu duka maza suka haifa sai dai yadda kawu yay murnar haihuwar sadiya bai murnar haihuwar ƴaƴa mazan ba Yaƴa sunci suna Nura da Salmanu haka rayuwar ta cigaba da tafiya.

Sadiya irin mai jikin girman nan ce dan saida ta kere ƴaƴan su Indo a girma kuma tun tana ƙarama mai kishin mahaifiyarta ce ko kaɗan bata kwaso sanyin Asiya ba ( umma ) sam sadiya mafaɗaciya ce Dan ko abu za'aiwa uwarta to sai dai in tana makaranta amman agaban ta ba wanda ya isa ya taka mata uwarta bayan sadiya umma ta haifi Nafisa ba jimawa ta haifi fa'iza

daga lokacin  kawu kuma a sannan arziƙin yayi ƙasa gidan Bilon shi ma ya ɗaga ya siyar sai buga buga kawai yake.

Lokacin umma ta sami ƴanci dan sadiya ta zama budurwa babu uban daya isa ya taɓa musu uwarsu dan ko kawu ne ya ma umma faɗa to sadiya kwana take kuka kuma ba zata ci abinci ba ga kawu yana masifar son sadiya A hankali Aka fahimci yarinyar aljanu ne suka taɓata dan data soma zama budurwa sosai Nan da nan suke bugeta wanda hakan yana ɗagawa su kawu hankali dan in abun ya tashi babu sauƙi.

Ganin halin da suke ciki ne sadiya ta dubi umman su Lokacin tana ɗauke da tsohon ciki tace mata.......
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*23*

*A LOVE STORY 23*
"Umma ya kamata ki fara yi mini awara ina fitar miki da ita titi danni gaskiya zamannan ya isheni haka"

Umma ta kalli sadiya da tausayawa duka lokacin shekarun ta bama su yawa bane damma dai mai gaɓɓan girma ce.

"Haba sadiya ta yaya kamar ki zanyi wa awara ki bari ƙarfin ki yakai"

Sadiya ta dubi umma.
"Umma kinga su matan gidannan ƴaƴan su suna taimaka musu ke kuma kullum sai dai kita wankau ga sanyi ni dai dan Allah ki min zan saida miki"

Sanin halin nacin sadiya yasa umma ta amsa mata da to daran sadiya bata bar umma ta sake ba haka ta addaba mata sai da ta bata kuɗin wake rabin kwano washegari sadiya ce ta kai markaɗe umma ta dafa mata awarar.

Ta fita can titi tana soyawa da yamma duk wanda yaga sadiya sai yayi sha'awar awarar sabida ƴar mai kyau da ita ga ta tsaf ba ƙazanta kafin magariba awara ta ƙare se kuɗin ta cas babu abun da ya ɓata Sai dai sukai sati suna awarar Kuma cikin hukuncin Allah kullum sai ta ƙare ganin haka yasa Umma ta ƙara ta koma ta kwano ɗaya da wannan ribar awarar suke ci suke sha randa kawu ya kawo su haɗa.

Ganin wannan sai hankalin indo ya tashi sai ta farawa sahura ƴarta lokacin ita ce kusan sa'ar

sadiya sai ta fara mata awarar itama dan gasa

Dan tsokana sai sahura take zuwa kusa da sadiya tana soyawa.

Ranar da sahura ta fara zuwa sadiya bata mata magana ba sai da aka tashi sannan tace.

"Sahura ina baki shawara daki Koma wancan ɓangaran wannan ɓangaran nawa ne in kunne yaji jiki ya tsira"

Sahura tasan Halin sadiya kamar yunwar cikinta.
Tana zuwa gida ta gayawa Uwarta indo ta fito tana cin mutunci akan ba uban daya isa ya hanasu yin awara kuma awara yanzu suka fara.

Sadiya ta fito aguje ta rarumo Muciya tabiyo indo a ranar sun ga masifa dan Indo bata kwana agidan ba Sabida tsoron sadiya umma Aljanun sadiya na damun ta sabida mayar da yarinyar suke kamar wata juju.

Washegari indo ta dawo kawu ya kirasu yace bai amince su cigaba da awarar ba sabida haka ya soke yi sadiya ta kada baki tace masa.

"Kai yanzu kawu idan ka hanamu yin awara kana da abin da zaka bamu su suna da ƴaƴa maza Ita kuma uwarmu bata da kowa sai mu yunwa inta kama su fa'iza tsakar dare umma kuka take nidai gaskiya baze yuwu na dinga ganin ɗigar hawayen uwata ba sabida haka sai na fitar da awara ko umma bazata yi min ba zan amso jari wajan umman zage nayi"

Amaimakon kawu ya hau masifa sai yahau cewa.
"Haba dubu tawa kimin fatan na samu na wadata ku mana, Nima kaina bana son halin nan da kuke ciki"

Duk yadda kawu yaso tabari taƙi awara ta cigaba da fita da ita kuma Allah yasa mata nasibi wannan awara sai da ta koma ta kwano biyar Baƙin ciki kamar ya kashe Su indo gasu su komai suka taɓa narke wa yake.

Haka umma ta haifi Fatima wadda taci sunan mahaifiyar Umma  wadda suke ce mata ( farha ) duk ƴaƴan umma dana sauran matan farare ne tas amman ikon Allah farha baƙa ce ƴar ƙarama Tunda aka haifi farha Sadiya ita ke rainon farha sabida ƙanƙantar yarinyar sadiya ke fita da ita wajan suyar awara ta goye ta kamar ƴar tsana sadiya kewa farha wanka ta wanke mata kayan ta Umma na jinjina yadda sadiya take son Farha yarinyar akwai wayo Bata yadda da kowa daga umma sai sadiya Cikin haka Farha bata fi shekara Biyar ba kawu yace wa Umma zai aurar da sadiya ga ɗan yayan  shi Umma kuka sadiya kuka amman kawu ya rufe ido sadiya tana gama primary Kawu ya aurar da ita duka ƴaƴan yayin shi ya bawa sadiya da sahura  Raziƙa kuma ɗan maƙotan su a tare ya aurar dasu su uku.

Nafisa ta rage da fa'iza da farha nafisa sokuwa mai sanyin hali irin na umma shiyasa komai na umma ya koma baya dama sadiya ce gadarar ta Dan nafisa ko an bata awarar ƙarshe ta saki baki maza su kwashe su gudu haka umma ta haƙura dayin awarar ta zubawa sarautar Allah ido sai dai wani abu ɗaya farha halin sadiya gareta Zafi da faɗa masifa kamar  me ga ƙanƙanta amman akwai zafin zuciya da ƙarfin hali dan bata ragawa duk wanda yayi mata suma su indo sun haifi ƴaƴa mata bayan farha Indo ta haifi Hadiza Hafsatu ta haifi Ruƙayya sai ƙannen su farha faɗan tsiya kuma kayan su baya taɓuwa Tunda aka sanya farha a makarantar primary lokacin ana shirin bikin Nafisa farha ta mayar da kai ga karatu tana zuwa boko da islamiyya daga ta  dawo kuma tayi ɗaki taita bitar karatun ta kaf gidan farha tafi kowa son karatu cikin haka akai Bikin Nafisa lokacin tuni Yaya Sadiya ta haifi mai sunan Umma

Bayan bikin sadiya da nafisa Umma ta haifi Ikram Dole umma ta koma da sana'arta ta wankau sabida ita farha tace ba zata soya  awara ba gaskiya ita karatu zatai sai dai kuma duk wankin da za'a kawowa umma zata zauna suyi tare ta ninke takai gidajen waɗanda suka kawo wankin fa'iza son jikin tsiya bata komai sai ci da bacci shiyasa suke faɗa da farha sosai akan wannan lalacin.

Cikin haka wani hamisu ɗan maƙotan su sana'ar Bugu yake na shadodi yace yana son fa'iza Hamisu shike sangarta fa'iza in ƙwai ne haka zai kawo mata taci tai naƙ kayan toshi kuwa kowa zuwa yake kallon na fa'iza sosai Hamisu yake kula da Fa'iza wadda itama kawu ya haɗa su da sauran ƴaƴan su Babarsu Hadiza ya aurar dasu su Uku Gidan ya rage Farha ce Babba a mata sai Yayin ta maza Guda Uku Halifa Nura Salmanu sai ƙanne da suka taso su ruƙayya dan sunfi farha tsayi da jiki in ka kalleta sai ka rantse sune Gaba da ita.

Farha ta gama secondry kawu ya kirata ɗakin sa.

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*24*

*A LOVE STORY 24*

Farha ta ƙarasa gaban kawu yana ɗaki yana sauraran labarai a radio.

"Kawu naji ance kana kirana gani"

Kawu ya dube ta bayan ya aje radio ɗin dake hannun shi.

"Na ganki fatima, Dama akwai wani abokina da ɗan sa ya ganki yace yana son ki Salim yaro ne mai kirki da sanin darajar mutane, Yana kasuwanci a kantin kwari dama na barki ne kin gama secondry sabida naga kina son karatu kuma zamani ya canza ƴan uwana da abokaina suna min faɗa akan aurar da ƴan uwanki danai da wuri"

Farha nan da nan ta haɗe girar sama data ƙasa murya a shaƙe tace wa kawu.

"Nidai kawu amin afuwa gaskiya bazan yi aure ba sai na Cigaba da karatu har na kai matakin dana zama ƴar jarida"

Kawu ya dube ta.

"To baki isa ba daga ke har Hasiya ƙarya kuke aure zaki naji kuma da na gabana"

Farha ta sanya masa kuka wiwi tana masa magiya.

"Kawu kada ka min haka tun asali ina son karatu na kaf ƴayƴanka baka bar kowa yayi makaranta ba dan Allah ka barni nayi"

Kawu ya dube ta ranshi a ɓace.

"Ita bokon Dole ce na barku kun sami na alkur'ani ko a wajan Allah bani da laifi dan haka na soke batun wata cigaba aure zaki salim zaizo ku daidaita"
Da gudu ta tashi tayi ɗakin su Umma tana masifar son farha sabida sunan mahaifiyarta ne in taga farha cikin damuwa ita ma shiga damuwar take nan da nan umma ta ruɗe tana tambayar farha menene farha na kuka tana shaidawa umma.

Bayan umma ta gama saurararan farha tace.
"Sha kurumin ki wallahi ba mai miki aure yanzu har sai burin ki ya cika kedai bari  na saka Najib ɗan umman zage ya cigiya miki f.c.e tunda takardun ki sun yi kyau"
Daran ranar farha ta kwana da farin ciki.
Wanda umma sai da suka kai ruwa rana da kawu sannan ya bar Farha ta cigaba da karatun.

Lokacin da salim ya fara zuwa wajan farha tana zaune ranar Alhamis babu makarantar dare.

Ikram ta sheƙo aguje.

"Yaya kinyi baƙo akan lifan"

A ƙufule farha ta mako mata mafici.
"Dalla malama gafara ki bani waje baƙon ubanki"
Umma dake Cikin uwar ɗaki tana ninke kayan wanki tace.

"Ni wannan zafin rai naki farha shike bani tsoro ita meye laifin ta ai jakada baya laifi"

Farha ta turo baki gaba ta danno shi.
"Nifa umma ina ga baƙon kawu ne gaskiya ina tsoron fita"

Umma ta ɗaga murya cikin ƙosawa da gardamar farha tace mata.

"In ba zaki fita ba ki gaya masa nidai ba ruwana nagaji kullum maganar baban ki ina ɗaure miki gindi to wallahi babu ruwana gwara ma ki tashi ki fita kije kiji damai yazo"

Farha tana gunguni ta miƙe ta yayi bi hijabi a saman ƙyaure ta ɗora akan ta tafita.

"Farha zonan"

Harta kai bakin ƙofa taji kiran umma da sauri ta ƙarasa wajan umma ta tsaya har lokacin tsinin bakin ta bai koma ba.

"Shafa hoda mana fuskarki sai maiƙo take yi"
Badan taso ba ta shafa powder ta fesa turare dama ita bata san kwalliya haka Allah yayita.

Ta fita ta same shi ɗan gajere ne baƙi kakkaura yana zaune a saman lifan ɗinshi daga nesa ta tsaya ta turo masa bakin ta gaba.

"Gani"
Ta faɗa tana kawar da kanta Salim ya sauko ya ƙaraso gabanta ƙaƙƙarfan ƙamshin turaren shi ya bugi hancin ta.
"Assalamu alaiki ya sanyin zuciyata mandirin ƙalbina tauraruwa a birnin dake zuciyata"
Takaici ya kama farha a ranta tana cewa ji wani ƙauyanci amman bata nuna mai ba sai ta amsa mai sallamar.

"Da farko sunana salim ɗa na farko wajan mahaifan sa muna nan tsallaken ku Babana abokin mahaifin kine na gama ginin gidana a mai dule, Ni da gaske nazo da maganar aure Ina kasuwanci a kantin kwari ina sai da atamfofi da Kayan mata"

Farha ta kau da kanta dan ƙamshin turaren Salim ya soma bugar mata da kanta.

"Naji amman ni gaskiya ba yanzu zanyi aure ba in zaka jira ka jira in ba zaka jiraba ka tafi, Ni kam makaranta zanyi har sai kuma na sami aiki sannan zanyi aure"

Ta faɗa tana harare harare.
Salim ya saki murmushi mai ƙayatarwa.
Yana mata kallon ƙuruciya, Aranshi yana Yaba wautar ta.

"Naji na amince in zaki ga ƙarshen biro da takarda ni zan jiraki farha ina mugun sonki tunda na ganki wallahi na kasa sukuni ji nake kamar ina wata duniya daban ta masoya ki taimakeni Farha kada ki juyawa soyayyata baya ina sonki kamar raina a shirya nake dana fuskanci kowani ƙalubale akan son ki"

Farha ta saki baki babba dashi ya dage yana ta zuba mata kalamin soyayya ita har kunya ya bata haka dai ya tafi bai sami amsa a wajan farha ba.

Acikin satin salim ya dami farha da naci ga lokacin ta soma F.C.E Inda ta sami departement ɗin da take so wato Mass comminucation  a matakin farko na diploma gaba ɗaya farha ta ƙara mayar da hankalinta akan Karatunta sam bata da lokacin kowa sai na karatu ƙawarta ɗaya shema'u ƴar ƙofar nasarawa Dp ɗinsu guda da shema'u farha nada mugun ƙoƙari yawanci ƴan ajinsu bakwaini suke ce mata sabida tsabar ƙanƙantarta.

Soyayyarsu da salim kuma tayi ƙarfi sosai dan salim irin mutanan nan ne masu naci ya nacewa farha, Hidima yake mata yana kashe mata kuɗi sosai dan yawanci Kuɗin da take kashewa na makaranta salim ke bata tun umma na faɗa harta haƙura kawu mutum ne mai zafi shiyasa ma Farha bata fiye amsar abin salim ba haka Farha ta cigaba da makarantar ta koda yaushe salim idan yace ze turo sai tace ya ƙara mata lokaci.

Farha tana da masifaffan ciwon mara wanda umma ke amsar mata magani dan idan ya tasar mata Har suma take Farha bata da haƙuri ga rashin kunya wani bin salim ma inta Botsare masa da ƙyar yake shawo kanshi Umma tayi namijin Koƙari sosai akan farha dan ita ke biya mata kuɗin makaranta duk wata buga buga umma tayi akan farha ta sami ilimi, Sabida yadda umma take son farha sosai Babban farin cikin farha ta sami aikin jarida idan ta gama makaranta.

Zaman gidansu farha ya cigaba da wanzuwa kamar yadda yake sabida Hidimar da kawu ya barwa matansa yasa ake cewa gidan.

Gidan cida kai sabida yawan su kuma wasu suce ƴan gidan yawa.

Faɗa acikinsu kamar me yanzu da ƴaƴan umma suka taso sam matan gidan bamai takata sai dai fa ta ciki na ciki ne kawai gashi kowa yafi son ɗansa yayi gaba yafi na wani Yaƴan gidan nada haɗin kai a waje dan basa taɓuwa amman agida kamar kaji sabida masifa gashi kowa uwarsa ya sani.

Cikin wannan ƙadamin farha ta sami aiki a gidan RADIDON GARKUWA bayan ta gama karatun ta, Ta hanyar yayan shema'u Wanda wannan aiki ne dalilin tarwatsa dukkan Burin farha data ci na ta sami aiki dan taga matan gidansu na shan wahala ta sami aiki dan ta dinga taimakon mahaifiyarta sabida wani bin kwana zasu yi basu ciba Ikram taita kuka Sai dai kana taka Allah yana nashi adaidai sanda ta sami aikin ƙaddarar Auren Aliyu ta tarwatsa mata dukkan waɗannan Burika nata ko yaya rayuwar farha zata kasance?

*WANENE ALIYU*.........

*RABO YA RANTSE! Iittafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*25*

*A LOVE STORY 25*

Marigayi Sale madaki Shine Kakan Aliyu wanda ya haifi Mahaifin shi Allah ya jiƙan shi da rahma Alhaji Abdu Madaki.
Sale madaki haifaffan jahar kano ne anan cikin Galadanci gidan iyayen shi yake mahaifin sale mutum ne mai dukiyar gaske sana'ar saida fata yake shiyasa mutane ke masa laƙani da Madakin fata Kuma sale kaɗai Allah ya bashi aduniya Bayan Rasuwar Dukkan mahaifan sale sai sale ya gyara ƙaton gidan mahaifan nashi yayi aure ya auro matarshi salamatu ƴar nan kusa da gidan su Suna zaman su lafiya da salamatu inda ya cigaba da sana'ar saida fata ya gaji mahaifin shi.

Shuru shuru tunda sukai aure salamatu bata haihu ba tuni abin ya dameta amman shi sale ya dangana yana bata haƙuri koda yaushe akan cewa Haihuwa lokaci ce haka suka shafe shekaru Biyar da aure Amman salamatu ko ɓatan wata bata taɓa yi ba Ganin haka yasan ya ƙanin mahaifin sale yazo har gida ya same shi lokacin sale bai fita kasuwa ba.

"Nazo ne akan maganar matar ka"
Sale ya dubi ɗan uwan mahaifin nashi tare da cewa.

"Allah yasa ba wani laifi tayi muku ba kawu"
Kawun nashi yace.
"Ko ɗaya mu dai mun gaji da ganin ta haka kada kaga ba ran mahaifan ka muma masu tsaya maka ne saboda haka na baka Yata Saude kazo ku daidaita mu irin haihuwa ne dan ba zan so yadda iyayen ka suka haife ka kai kaɗai ya zamana cewa Ka mutu baka da magaji ba"

Sale yayi ƙasa da kanshi yana tunanin haƙuri da nagarta irin na salma idan yayi mata kishiya akan rashin haihuwa bai mata adalci ba.

"Kawu nagode, amman kai hakuri bani da matsala da matata Ni gaskiya ba zan mata kishiya haka kawai babu wani dalili ba"

Kawun sale ya harzuƙa ya fara cin Mutunci.
"To dole ka amshi saude ko kaƙi koka so dan kaga bani na haifeka ba to bari kaji cikinmu ɗaya

da mahaifin ka  ko kaƙi koka so ba'a canzawa tuwo suna sabida haka kazo gida kaga saude ku sasanta a saka ranar ɗaurin aure in kuma ban isa dakai bane ba to"

Saleh yayi ƙasa da kanshi sai faman Haƙuri yake bawa kawun nashi sannan yayi masa alƙawarin zai zo yaga saude.

Kawun sale yayi tafiyar shi batare daya tsaya amsa haƙurin da salen yake bashi ba.

Koda ya koma gida ya rasa ta yadda zai gayawa salamatu maganar da sukai da kawun shi sabida kunyar ma gaya mata maganar yake yi.
Ta lura sam bai da sukuni har dare ganin haka  yasa ta saka shi a gaba da tuhumar meke damun shi? da ƙyar ya aro jarumta ya dube ta.

"Salamatu kin san ina son ki, Kuma ina ƙaunar ki"
Tayi murmushi tace masa.
"Nima in ka cire Allah da ma'aiki da iyayena da suka rasu to sai kai sai kuma ƙanwata Amina da muke shirin auren ta"

Yayi dariya sannan yace.

"To kawu ne ɗazu yazo min da batun cewar zai bani ƴar shi saudatu na aura"
Bai ƙarasa ba ta katse shi cikin murna tace.

"Dama gidannan yayi min girma tsoro nake ji in baka nan Allah ya tabbatar da alkairi kaga na sami ƙanwa"
Duk ta yadda Yaso kushe abin taƙi sai ma ƙarfin gwiwa da take bashi haka ta shige masa gaba akan auren shi da saudat har yaje ya gano saude aka tsaida maganar aure ba da jimawa ba.

Sai dai me Tunda aka saka maganar auren ma salamatu ta soma laulayi wanda ya hanata lafiya gaba ɗaya Sale ya mayar da hankali akan kula da lafiyar matarshi a daddafe ya auri saude wadda tazo gidan da tashin hankali dan saude akwai zafin kishi da zargi haka dai zaman nasu ya cigaba salamatu rabi haƙuri take da saude sabida saude akwai saka ido zargi ga zafin kishi abu kaɗan sai ta kai sale ƙara ƴan uwansa suzo su zage salamatu ba zata tanka musu ba haka Taita cigaba da zaman gidan cikin haƙuri Har Allah yasa ta soma naƙuda wanda sale Baya nan ranar Tana ɗaki tana ta fama Duk ta fita daga hayyacin ta saude tana tsakar gidan ta ware Rediyo tana wanki ko kallon salamatu batayi ba kwatsam Allah ya jefo Amina ƙanwar salamatu ce wadda akai wa aure a kwanakin Cikin su ɗaya kuma su kaɗai ne mata a wajan iyayen su sai yayan su Namiji guda ɗaya da yake zaune anan gidan Da mahaifan nasu suka rasu suka bari.

Ganin halin da salamatu take ciki hankalin Amina ya tashi ta ruga gida ta kira matar yayan su aka saka salamatu a mota suka tafi asibiti Amman saude ko kallo basu isheta ba Koda suka je asibitin matar yayan su ta saka yaron ta yaron yace kasuwa ya kira sale sai dai kafin sale yazo har salamatu ta haifo ɗanta ƙato wanda ko kallon shi batai ba Allah ya amshi ranta iya tashin

hankali wannan zuri'a sun shiga sale kuwa kamar zararre haka ya koma yaja yaro ya rungume yaƙi bawa kowa.

Sai da abokai suke ta masa nasiha sannan ya bada yaron Amina da matar yayan salma sunce zasu riƙe shi amman Sale ya ƙi har da kukan shi sai mahaifin Saude yace a bawa saude ta Dinga bashi madara sai uban sa ya dinga ganin sa a kusa dashi haka akai bakwai aka watse aka bar saude da jariri wanda Amina tai kuka tai kuka akan aka bata yaron aka ƙi.

Sale kewa Abdullahi wanda suke cewa Audu a wannan lokaci, Shike masa wanka kafin ya fita kasuwa ya bashi madara yasha ya wanke masa kayan shi tas Ba tare daya tsaya bin kan saude ba wadda take jin kamar ta jefa audu a wuta Sosai mahaifin shi ke lura da shi ga audu yaro ne mai hakuri da wiya kaji kukan shi haka yayi ta girma ta silar Kula da mahaifin shi yake bashi A haka har yaro yakai shekara biyu Amina na zuwa ganin shi sosai Dan koda yaushe tana hanya ga uban sa na son shi sai dai fa da zarar Sale baya nan Saude zata saka shi a ɗaki ta kulle ya wuni da yunwa amman in uban ya dawo sai dai audu yayta hawaye dan babu bakin magana

A haka ya taso Yakai shekara Biyar saude ta haifi ɗanta itama mai suna Usman.

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*26*

*A LOVE STORY 26*

Bayan usman ta haifi Ashiru daga shi ta haifi sa'adu daga shi sai Rabi'u sai salisu sai suwaiba Lokacin Audu ya zama ɗan matashi zai kai shekara Goma sha biyar wahalar Gidan gaba ɗaya ta koma kanshi komai na su Usman shi yake hatta tsarki kashin su Saude taƙi bashi abinci sai taga uban ya kusan dawowa kuma dan haƙuri irin nasa baze taɓa gayawa mahaifin shi ga abin da take masa ba sai dai yayi ta kuka shi kaɗai tuni an saka su a makaranta shida usman ƙwazo ne da audu sai dai Yadda Usman yake masa mugunta a littafinsa da zarar an sai masa haka ze yaga in Uban ya dawo yay ta masa faɗa yana kammala Firame mahaifin shi ya kaishi kasuwa ya nuna masa harkar fata Ganin haka yasa Saude tace sai an kai usman shima amman uban yace ba yanzu ba sai ya kuma wayo.

Zuwan shi kasuwa ne yasa shi yake ɗan jin sauƙin azabar saude da ƴaƴanta waɗanda suka ɗauke halin ta tsaf ga sharri haka Usman zai hau katifar audu ya maka fitsarin kwance da safe saude ta naɗawa Audu duka.

Watarana mahaifin yayi tafiya sai yace audu kada ya fita kasuwa dan bai san hanya ba dama

kuma abin da yasa yake tafiya dashi kasuwar ma dan ya fahimci yana cin wahalar zaman gidan ne.

Usman da Ashiru sun maka fitsari Saude ta fito da kayan fitsarin ta saka audu a gaba tana duka yana wankin cikin haka Amina ta faɗo gidan da tsohon cikin ta yadda taga ana azabtar da ɗan yayarta har kuka tayi bata tafi ba sai da Audu har da kayan shi ta haɗa bayan sun gama zage zage da saude.

Amina ta saka audu a gaba har gidan ta dake Fagge tana auran miji mai kuɗi tana zaune lafiya da kishiyarta wadda take goyon ƴa mace itama Mijin Amina yayi murnar ganin Audu kuma yayi takaicin Yadda Amina ta bashi labarin wahalar da audu yake sha .

Bayan Sale ya dawo saude ta tare shi da ƙarya da gaskiya haka yazo har gidan Amina yace ta bashi audu fafur ta hana shi abin har yakai su da ba daɗi haka ya tafi yay fushi yace ya bar mata shi ta cinye.

Mijin Amina da ita kanta Aminar sun ɗauki son duniya sun ɗorawa Audu wanda ya murje yayi kyau kuma ya koma makaranta anan faggen Mijin Amina na masifar son Amina wanda soyayyar da yake mata ne yasa ma har take samun saɓani da Kishiyarta wadda take Goyon ƴa mace mai suna tajira.

Haka Amina ta haifi ƴarta mace mai kyau kamar ta fara jajir sabida soyayyar da Mijin ta yake mata ne ya sanyawa ƴar sunan ta itama yarinya taci suna Amina Audu ke renon Amina komai ya samu ita wata irin shaƙuwa ce a tsakanin Audu da Amina wadda komai na yarinyar shike mata Wanda hakan ya ƙara jefa tsana mai ƙarfi a tsakanin Kishiyar Amina da ƴarta wadda taɗan tasa Suka tsani Audu suka tsani Amina da ƴarta Tuni Audu ya mance da rayuwar Gidan su Har ya kammala secondry Ɗinsa Lokacin Amina ita kuma tana Primary ta ɗan tasa ta zama budurwa Bayan kammala karatun Amina na firamare sai tafiya ta kama Babanta da Mahaifiyarta sai suka zauna a wajan Babar tajira ita da audu a hanyar su ta dawowa ne sukai hatsarin mota wanda Amina ƙanwar mahaifiyar audu tare da mijinta waɗanda sune mahaifan Amina Allah yayi musu rasuwa ta sanadin wannan hatsari.

Tashin hankali audu da amina sun shiga ana sadakar bawai yayan salamatu ya ɗauki amina sabida yace baze bawa babar tajira riƙon amina ba sabida itama tana fama da kanta wannan ne sanadin da Riƙon Amina ya dawo wajan Yayan mahaifiyarta shi kuma audu sai ya koma gidansu wanda ya tarar ƙannen shi dik sun girma ba yadda sale yayi haka ya komar da Audu kasuwa wannan tasa wutar ƙiyayya ta ruru a tsakanin saude da ƴaƴanta wadda suke jin kamar su jefa audu a wuta.

Yana fuskantar cin mutunci wajan ta da ƴaƴanta gefe Guda soyayya mai ƙarfi ce ta ƙullu a tsakanin audu da Amina wanda mahaifin audu ya fahimci haka bai ƙasa a gwiwa ba wajan tunkarar yayan su salamatu da batun yana son Audu ya auri Amina ba'ai wani ja yayyaba aka

aurawa audu amina sashe guda sale ya ginawa Audu acikin gidan wanda Amina ta tare aciki.

Bata da wata matsala daga farko sabida audu yana samun Kuɗi fatar ta karɓe shi dan a lokacin batai shekara da auran shiba ya biya musu hajji ita da shi da babansa da yayan mahaifiyar su lokacin saude kamar tayi hauka dan baƙin ciki ita da ƴaƴanta basu jima da dawowa ba Allah ya ɗauki rayuwar Sale mutuwar data girgiza wannan ahali musamman audu.

Haka akai zaman makoki aka watse audu ya koma kasuwa sai dai abu kamar wasa kasuwa ta koma masa baya komai ya taɓa narkewa yake hatta jarin sa saida ya rasa Kawun su yayan mahaifiyar su da ƴaƴansa suke taimakon audu da kayan abinci.

Ga lokacin Amina ta sami ciki ya tsufa komai yazo kuma ya tsaya

Ga cin mutuncin saude da ƴaƴanta a kullum cewa suke sai audu ya tashi anyi rabon gado watarana Amina ta tashi da naƙuda ba yadda audu bai da Saude ba akan tazo sukai Amina asibiti sabida cikin dare ne amman taƙi daga ƙarshe ya fita ya kira matar kawun su suka tafi asibiti Amina ta haifi ɗanta namiji fari mai kyau dashi ƙato suka dawo gida da safe.

Tashin hankalin da suka tarar yafi gaban kwatance dan su Usman da suke samari a lokacin sun watsowa Amina kayanta sun rushe ɓangaran Wai ai rabon gado basu yarda da zaman Audu agidan ba Amina na kuka Kawun su ya bata ɗaki guda agidansa anan suka cigaba da rainon ɗansu Abubakar Sadiƙ.
Sunan yayan mahaifiyar su Audu ya saka.
Rayuwar yau da gobe tai musu zafi Audu yana ji yana gani su Usman suka rabe gidan mahaifinsu kowa yaja sashin sa suka gine Sauran gado gona filaye duk basu bashi ba haka ya cigaba da zama agidan kawu Abubakar yayan mahaifiyar shi da taimakon ƴaƴan kawun shi waɗanda suke yayye garesu shida Amina suka gina masa ƙaramin gida anan ƙofar na'isa ya koma lokacin ne Amina wadda sadiƙ ke cewa ( Ammi ) ta haifi ɗanta Aliyu wanda tsiran su da sadik shekara biyu ranar data koma sabon gidan ta haifi Aliyu wanda aka sanya sunan mahaifin ta Marigayi Alhaji Ali Fagge babanta ita da Tajira.
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*27*

*A LOVE STORY 27*

Aliyu yafi sadiƙ kyau nesa ba kusa ba kuma yafi sadiƙ Girma tunda Audu ( baba ) da Ammi suka ɗora ido akan Aliyu suka ɗauki soyayyar duniya suka ɗorawa Aliyu wanda haihuwar shi tazo wa Baba da nasibi domin ya koma kasuwa Lokacin Aliyu na da wata ɗaya a duniya arziƙin Baba ya

ninka nada tuni ya rushe gidan shi ya sake ginin zamani ya gyarawa yayan mahaifiyarsu gidan shi Lokacin Ammi Ta ƙara kyau hankalinta ya kwanta ta cigaba da rainon ƴaƴanta da suka taso kamar ƴan biyu ga kyau ga farin jini dan duk inda suka shiga ana son yaran.

Duk da yadda su Usman sukai wa Audu ( baba ) hakan bai saka yaƙi suba haka yaja su ajiki koda zasu yi aure shi yayi komai wanda mahaifi kewa ƴaƴa hatta kayan ɗakin suwaiba shine yayi mata yana kyautata musu sosai tuni an saka su Aliyu a makaranta mai tsada Yanayin ƙoƙarin Aliyu ne ya sanya aka haɗe su Aji ɗaya da sadiƙ wanda suka shaƙu sosai sai dai akwai bambancin hali.

Aliyu tun yana yaro miskili ne mai taurin kai marar far'a da son mutane baya da yawan magana sosai Kullum yana jikin mahaifin shi sai dai yadda Baba ke yawan zuwa da Aliyu cikin Gida wajan su Usman yasa Aliyu yake son dangin mahaifin nashi duk da irin abin da sukai wa mahaifin nasu wanda Ammi ta ƙullata aranta amman ikon Allah duk abin Aliyu bai taɓa riƙon su ba wani bin har zuwa cikin gidan yake ya kwana abin Allah saude tana mugun son Aliyu sabida lokacin ta tsufa tuni ta nemi yafiyar audu akan abin da tai masa suma su Usman sun nemi yafiyar shi kuma ya tabbatar daya yafe musu matsalar kawai Ammi ce da ko magana bata shiga tsakaninta dasu usman Sabida tace ita dasu har abada akan abin da sukai wa mijinta.

Komai da su Usman suka mallaka wanda suka dannewa audu yau da gobe ya ƙare tas gidajen sun ma duk sun lalace ajikin Audu suke raɓe a kasuwa shi kuma baya musu Mugunta dan ya tabbata da dama sharri ɗan aike ne Kuma tunda sun tuba sun gane Laifin su shikam ya yafe musu har ranshi dan baka fushi da naka. Allah yayi wa saude rasuwa tsiranta da kawun audu ba nisa haka dama rayuwa take.

Sai da Aliyu ya shekara biyar ammi ta haifi salma mai sunan babar Audu daga salma sai bashir daga shi sai Safna daga ita sai sajeeda.

Lokacin raino yayi wa Ammi yawa sai aka ɗauko mata mai aiki Hajjo wadda suke zaman lafiya hajjo na taya ammi rainon su safna su Aliyu na Secondry Lokacin Jss 1 bashir da salma kuma na primary dan duka lokacin Sadik na shekara sha biyar Aliyu sha huɗu salma tara bashir bakwai Safna huɗu sajeeda ɗaya adaidai wannan Lokacin Allah ya ɗauki ran Audu ya rasu yabar Ammi da waɗannan ƙananun yara bida da bi ya  rasu yabar tarin ƴan uwa da masoya mutuwar data tarwatsa farin cikin Ammi bata da uwa bata da uba bata da Miji yayan mahaifiyarta mai jin ƙanta shima babu sai ta rungumi ƴaƴanta sune komai nata tasaka su agaba tana hira tana dariya tana kuka Hajjo ce mai bawa ammi baki tana rarrashin ta Yau da gobe kayan Allah komai yazo ya ƙare domin zara bata barin dami Ammi ta cinye komai da audu ya rage sai gidansu da suke cikin sa.

Suma su Usman lokacin nauyin ƴaƴa yayi musu yawa ƙananun ƴaƴa garesu dan aure auren tsiya gare su gashi babu Suma basu samu ba bare su taimaki Ammi.

Makarantar su Aliyu suka koro su sabida basa biyan kuɗin term dan makarantar Kuɗi ce Lokacin Ammi tai kuka tai kuka kamar ranta zai fita domin abin da zata ci ma ya gagare ta cikin haka ta fara sana'ar sayar da abinci da goyon Sajeeda Hajjo na riƙe da Safna haka zata fita kasuwa ta siyo kayan girki agidanta take sayar da abincin da wannan ribar suke ci suke sha har ta biya musu Kuɗin makaranta ita dai Burinta ƴaƴanta su rayu cikin farin ciki.

Sannu sannu jarin ma yazo ya ƙare tas Lokacin su Aliyu na Jss 3 Ammi dole tasa tace wa hajjo ta koma gida ta nemi sana'a dan itama ta kanta take yi amman hajjo taƙi tace ita kam ba zata rabu da Ammi ba haka suke zaune Cikin girmama juna dan hajjo nawa Ammi biyayya kamar lokacin da suna da shi bata taɓa sauya wa ba.

Ganin halin da suke ciki yasa Aliyu Kullum in sun tafi makaranta baya zuwa sai yayi tafiyar shi kasuwa dako yake duka lokacin ba wani girma yayi ba zai samo ɗari ɗari biyu sai ya sami banki ya Ɓoye Haka yay tayi lokacin jarrabawa yazo Malamin su yazo har gida ya shaidawa Ammi Aliyu baya zuwa makaranta.

Hankalin Ammi ya tashi Aliyu yana dawowa ta rufe shi a ɗaki tana tuhumar sa tana kuka sabida tana tsoron kada yabi abokan banza dan yafi sadiƙ wayo, Buɗar bakin Aliyu sai yace mata dako yake zuwa kasuwa yayi har ya fito mata da tarin da yake yace zai biyawa salma da Bashir ne Kuɗin makaranta kuɗin Sun kama dubu Uku ammi tai kukan tausayin yaron Haka ta mayar dashi makaranta sai ta sami aikin sharar titi ta dalilin yayanta ɗan wajan kawun ta da sassafe take fita tayo sharar ta ta dawo a wata ana biyanta dubu sha biyar bata cin ko kwabo a wannan Kuɗi haka take biyawa su Aliyu kuɗin makaranta da sauran Hidimar rayuwa.
Ganin wahalar da ammi take yasa Aliyu da safen kafin ya fita sai yaje yayi mata sharar tun tana hana shi harta barshi da wannan Ƴan kuɗin da kuma wanda ƴan uwanta ƴaƴan kawunta suka haɗa mata taja jarin Sayar da manja da man ƙuli a daddafe su Aliyu sukai candy daga nan yace bai san zancen komawa makaranta ba.

Ammin sa na cikin wahala gwara ya tashi ya nemi na kan shi haka Aliyu yake fita kasuwar Ƙofar Ruwa ta ƴan gwangwan wadda wani abokin sa yayi masa tayi a kasuwar ƴan gwangwan ta ƙofar ruwa awon Ƙarafan mota ake a fitar dasu lagos.

Ranar da Aliyu ya fara zuwa kasuwar yana bakin wani shago a zaune.

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*28*

*A LOVE STORY 28*

Wani Babban Mutum yazo zai wuce Sai ya yar da ƴar ƙaramar wata jaka adaidai ƙafafun Aliyu wanda yake gyangyaɗi sabida wanda abokin nashi ya haɗa shi dashi har Lokacin bai zo kasuwar ba Shi Kuma Aliyu tun safe ya dako sammako ya Zo kasuwar dan Burin shi Ko jari Bola ce yayi muddin zai sami Halaƙ ɗin shi.

Da sauri Aliyu ya buɗe idanun shi ya ga jakar sai ya ɗauka yabi bayan Mutumin Da sauri ya tare shi yana ce masa bawan Allah ka yada jakar ka Mutumin yayi farin ciki har ya bawa Aliyu kyauta wanda Aliyu yaƙi karɓa ya koma wajan zaman shi aranar ma dai Aliyu bai sami komai a kasuwar ba haka ya koma gida yana ƙunci dan ko ammi da tana masa magana banza yayi mata kuma yaƙi cin abincin dare haka da sassafe ya koma kasuwar still wannan Mutumin ya kuma zuwa kasuwar yazo ta gaban Aliyu ya wuce har ya yi nisa ya dawo ya dubi Aliyu.

"Jiya na ganka anan yau na ganka lafiya ɗan saurayi?"
Aliyu shuru yayi wa mutumin can kuma sai yace.
"Nazo neman aiki ne"
Mutumin yayi dariya.
"To ban da abin ka matashi ta ina ake samun aiki ana zaune ai sai ka motsa taso Muje Shagona"
Aliyu yabi Mutumin wani shago wanda ake sayar da kayan gyaran Motoci suka zauna mutumin ya kalli Aliyu.

"Ni sunana Alhaji Hamishi, Ni sana'a ta sayar da Motoci da kawo kayan gyaran su daga lagos da kwatano tunda na ganka ka bani tausayi ina zaune anan ƙofar ruwa matata ɗaya da ƴaƴa na mata Biyu Hasina da Hanan"

Aliyu yayi shuru.
"Baka ce komai ba"
Atakai ce Aliyu yace.

"Sunana Aliyu Ni kuma maraya ne da yayana da babata da ƙannena dansu ma na fito neman Aiki dan ina taimakon Ammi nauyi ya mata yawa"

Wannan shine mafarin Buɗewar idon Aliyu akan harkar motoci dan kunsan Komai akwai sila Alhaji Hamishi shine silar Komai na arziƙin Aliyu dan bai wa Aliyu Mugunta ba ya fara ajeshi anan shagon siyar da kayan gyaran motoci na ƙofar ruwa kafin daga baya daya ga amanar Aliyu ya ɗauke shi ya kaishi kamfanin sa dake Kan titin malam ƙato square Aliyu shine ya biya wa sadiƙ kuɗin makaranta a tare suka koma B.U.K Shida sadiƙ inda suka haɗa degree ɗinsu dama tun suna primary sunyi saukar su ta alkur'ani mai girma Suma su Bashir tuni Aliyu ya tsaya musu akan karatun su yana kammala service Ɗinshi ya fara fita kwatano yana shigo da motocin hannu yana siyarwa Ta dalilin Uban gidan shi Alhaji Hamishi  wanda Aliyu ya mayar

dashi uba a gare shi kullum arziƙin Aliyu bunƙasa yake lokaci Guda ya ɗauke nauyin ƙannen shi idanun shi ya bude sosai a harkar wadda harta kai ga ya soma zuwa yana siyo sabbi da kanshi ya ɗora riba ya siyar da kayan shi sabida yadda idanun shi ya buɗe a harkar.

Sannu a hankali arziƙin Aliyu ya bunƙasa tuni yabar kamfanin Alhaji hamishi ya Tsaya da ƙafar shi Haka ya siye ƙaton filin Kusa da gidan su shine ya gina wannan ƙaton gidan da suke ciki a yanzu ya dawo da ammi ciki kuma ya zuba mata ma'aikata Sannu a hankali har gidan su baba usman sai da Aliyu ya gyara shi tsaf lokacin kuma ya mayar da hankalin shi kan ginin kamfanin shi dake titin lawan danbazau wanda ya bawa sadiƙ manager Kuma rabi ma'aikatan shi ƴaƴan su baba usman ya ɗiba amman ba a san ran ammi ba.

Aliyu sun haɗu da musa kamar irin haɗuwar da sukai da Alhaji Hamishi shiyasa Aliyu yake ji da Musa sosai Kuma ya yarda dashi Kamfanin Aliyu mai suna Madaki Motors an services ya bunƙasa wajan kawo sabbi motoci na zamani dana hannu tare da kayan gyaran su Wanda kamfanin yayi suna a garin kano har ma da kewayan ta Aliyu na lagos da kwatano sadik na kano yana lura da wannan kamfani na Aliyu tare da Musa cikin haka Allah yayi wa Alhaji hamishi rasuwa Amman duk da haka Aliyu bai yada zuri'ar Alhaji Hamishi ba yana zuwa sosai matar shi mai Kirki ƴaƴan sane kaɗai sai a hankali Musamman ƙaramar hanan da sam bata da kamun kai wannan kenan.

Cikin haka Aliyu ya buɗe kamfanin sa a lagos wanda sadik ya koma can Taimakon Al'umma Aliyu yake da dukiyar shi musamman mabuƙata dan ya ɗanɗana rayuwar talauci yaji shiyasa bai taɓa wulaƙanta wani dan yana da shiba shiyasa idan yana kano kofar Gidan shi tam da jama'a Haka zalika a dangin su Kowa ya lalubo matsala wajan Aliyu zai tawo Kuma bai taɓa juyawa dangin mahaifin shi baya ba.

Taimakon su yake da su da gidan Kawun Ammi Dan duk matasan gidan daga sun taso Aliyu ke ɗaukar su aiki a kamfanin shi.

Salma tai aure wadda take Bin Aliyu zuwa wannan Lokacin Ammi tace wa su Aliyu su kawo matan aure Sadiƙ ya kawo sakina ƴar nan Ɗiso wadda ammi ta yaba Aliyu ya kawo najuwa course mate ɗin shi a B.u.k ammi taƙi amince wa sabida taga Najuwa wayayyace tace tana tsoron wadda zata raba su da Aliyu still dai bayan najuwa ya kawo wata ƴar nan galadanci nan ma ammi taƙi yarda sai yayi fushi yace ya fasa auren.

Cikin haka tajira yayar Ammi ta kawowa Ammi ziyara wadda rabon ta da ammi tun barin Ammi gidan su Lokacin da mahaifan ammi suka rasu Ammi taje fagge har ba adadi neman tajira amman bata same taba ita ko tajira tana sane da dukkan labarin halin da Ammi ta shiga amman taƙi zuwa sai da mahaifiyarta da mijinta suka rasu Taji labarin arziƙin da Aliyun Ammi  yayi shine tazo dasu mami cikin wahala tana kuka Ammi ta tausaya mata suka jajanta rashin juna kafin ammi ta haɗawa tajira sha tara ta arziƙi tasa aka kaita gidanta wanda take ciki da ƴaƴan ta marayu a fagge.

Kusan koda yaushe tajira tana wajan ammi biyayya takewa Ammi kamar itace ƙanwa Aliyu yaji bai yarda da matar ba sabida biyayyarta da Kirkinta yayi yawa Amman yadda Ammi ta ɗaukake ta tana yayarta ce uban su ɗaya su kaɗai suka ragewa juna shiyasa Aliyu ya zuba musu Ido dan bama cika zama yayi ba dama.

Kamar wasa Tajira tazo wa Ammi da batun haɗin auren ƴaƴan su abin kamar aikin asiri ammi bata musa ba dole tasa Aliyu ya auri Mami ƴar wajan tajira sadik ya auri sakina suka wuce lagos Shikuma Aliyu anan yabar mami a part ɗinsa ba dan yana son mami ya aure taba sai dan Bin Umarnin Ammi amman yadda mami ke masa biyayya yasa ta sami Gurbi a zuciyar shi Ta sami ciki har sau Uku yana ɓarewa yanzu haka shekarar su ta goma da aure sadiƙ ƴaƴan sa uku duk mata salma ƴaƴan ta biyu shiko Aliyu shuru kake ji dan daga Mami ta sami ciki ɓarewa yake.

Matar Alhaji Hamishi Momcy tana ganin mutuncin Aliyu dan duk wata matsala tata data ƴaƴanta shi take Kira ta gayawa Babbar ƴar Alhaji Hamishi Hasina tayi aure ƙaramar ce kaɗai take bawa Momcy ciwon kai dan hanan bata ji kule kulen maza ga shaye shaye sabida kawai uban su ya rasu yabar Musu dukiya ta raina Momcy bata jin maganarta hakan tasa wani Bin momcy ke kiran Aliyu wanda Hanan take masifar Jin tsoron shi dan baya mata ta sauƙi ya ɗauketa kamar su salma dan baya da gate a gidan Alhaji Hamishi kuma komai na abincin Gidan shiya ɗauki nauyi hatta masu gadin Gidan shike Biyan su sosai yake kyautata wa Iyalan Gidan.

Aliyu yana son Ammi yana kyautata mata sosai baya ƙetare dokar ta ko kaɗan Sabida haka ma ko maganar daɗin aure baya wa Ammi dan bata ƙaunar yayi wa Mami Kishiya.

Ammi ita ma tana son Aliyu yadda ba'a zato ɓacin ran Ammi Biyu ne wanda take nunawa Aliyu ƙiri ƙiri in yayi na farko yazo mata da tsokanar zai wa Mami kishiya wannan Rufe Ido take ta nuna ɓacin ranta dan tana son Mami sosai sabida yadda mamin ke mata Biyayya a fili, yadda Ammi ke son mami bata son sakina matar sadiƙ haka dan ƙiri ƙiri Ammi take nuna fifikon soyayyar mami a gaban Kowa Na biyu kuma Ammi taji labarin Aliyu yayi wa dangin mahaifin shi abu yanzu zata rufe ido taita faɗa tace duk abun da sukai wa mahaifinshi baya tunawa shiko sam bai taɓa Ƙullatar dangin uban nasu ba wandaAmmi ko Ɓangaranta bata bari su shigo in sunzo sai dai suje sashin Aliyu Baba Usman ya bata haƙuri amman ta rufe idonta.

A lokacin da Suka cika shekara goma da aure tuni sunan Aliyu yayi fice a garin kano sabida taimakon sa ga al'umma yana da kamfanin sa a kano lagos da kuma abuja arziƙin sa ya Bunƙasa Yadda Aliyu keda farin jini ne yasa gwamnati mai ci a yanzu tai masa tayin siyasa da farko yaƙi amman ammi tace yayi haka ya marawa gwamnati baya wanda gwamna ya bashi Muƙamin mai bashi shawara a Ɓangaran harkarkokin matasa wanda matasan ke masa laƙani da HASKEN MATASA!

A daidai wannan Lokacinne mami ta kuma samun Ciki ya ɓare wanda shine Gidan radio ɗin da farha ke aiki suka zaƙulo labarin suka juya ya koma sharri wanda farha tai jagoran cin yaɗa labarin wanda hakan yasa Aliyu yaji gwara ya aureta kodan ya ƙuntata mata akan abin da tai masa wanda auren farha Shine kaɗai abin da Aliyu ya taɓa aikata wa wanda Ammi bata sani ba

sadiƙ ma bai sani ba Kuma duka Ƴan uwan shi da suke ciki ɗaya basu sani ba mami matar shi bata sani ba, ko yaya zaman farha zai kasance da Aliyu Oho

*DAWOWA CIGABAN LABARI*

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*29*

*A LOVE STORY 29*

DAWOWA CIGABAN LABARI.

Cikin kasala ta miƙe daga saman gadon ta ƙarasa bakin jakar kayanta Zazzago su tayi ta ware su a saman carpet tana Ninke wa, Tana gab da gamawa aka bankaɗo ƙofar da ƙarfin gaske Farha ta saki bra ɗin hannunta tana zaro ido.
Sunkuyar da kanta tayi a ƙasa lokacin da taga Ammi a tsaye akanta fuskarta a haɗe.

"Fati"

Ammi ta kirawo sunanta.
Da sauri tace wa Ammi.

"Na'am ranki ya daɗe ina kwana"

Ammi ta ƙara tamke fuska cikin kakkausar murya tace wa farha.

"Kada kiga baba jiya ya hanani na koreki hakan ya baki damar kawo min iskanci ina son ƴaƴana duk abin da suka ce miki kiyi gaggawar yi in ba haka ba zaki tsinci kanki cikin wahala da ƙunci a tare dani"

Farha ta ƙara yin ƙasa da kanta gabanta yana cigaba da faɗuwa da sauri tace.

"In sha Allah Ammi zanyi muku dukkan abin da kuka ce"

Daga haka Ammi taja mata ƙofar tana mai ce mata.
"Ki maza kizo ki gyara mana ɗakunan baccin mu kafin ranki ya ɓaci"

Aje ninkin tayi tare da bin bayan Ammi Duk suna zaune a dinning suna break fast kallo ɗaya tayi musu sum sum ta nufi corridor ɗin da ɗakunan baccin su Ammi yake sai yau ta ƙarewa

Ɗakin Ammi kallo haɗaɗɗan ɗaki kamar bana dattijuwa ba yasha kayan gado saitin farare masu tsada da kyau sai ƙamshi ɗakin yake yi Toilet ta soma wanke mata sannan tazo ta soma gyara gadon tana gamawa ta shiga ɗakin su Safna wanda anan taci wahala sabida komai yana zaune da gindinsa a ɗakin sai da ta gyara dukkan kayan su da suka birkito toilet ɗinsu kuma harda Jini duk sun ɓata shi Ta toshe hancin ta tana wanke toilet ɗin wanda kamar da gayya ma suka ɓata shi ajigace ta gama sabida tashin zuciyar da ya kamata sabida tana da ƙyanƙyami haka ta fita daga ɗakin tana mayar da Numfashi.

Har lokacin Yammatan suna dinning suna Cin abinci daga tsakiyar falon Ammi ce zaune da Aliyu wanda bai fita ba suna magana da Ammi tazo zata gifta taji yace mata cikin taushin muryar shi.
"Kije dinning kiyi break"
Yi tayi kamar bata jishi ba ta wuce cikin ɗakinta sabida yadda amai yake taso bata Ammi tabi Aliyu da kallo.

"Bangane taje tayi break a dinning ba ka manta akwai girkin su daban da sukeyi a ɓangaran masu aiki?"
Ya shafa kanshi sam yama mance Ammi tana wajan batare da yace wa Ammi komai ba ya cigaba da danna wayar shi dake hannun shi.

Wayar Ammi dake gefenta ce tayi ƙara ganin salma ke kiran yasa Ammi ta tashi ta nufi bedroom ɗinta su safna na ganin Ammi tabar wajan suma suka tashi da sauri ko wacce tayi hanyar Bedroom sabida ganin dodon nasu a wajan.

Miƙewa yayi duk da yana da Meeting da mai girma gwamna sannan kuma Momcy matar Mai gidanshi marigayi Alhaji Hamishi tayi masa waya akan tana neman shi.

Dinning ɗin ya nufa ya ɗauki plate ya zuba soyayyan dankali da Miyar source ɗin albasa da hanta ya haɗa tea mai kauri daya sha Ovaltine da madara ya saka tea spoon aciki ya juya ɗakin Da farha ke ciki ya nufa Bata cikin Ɗakin ya aje mata Break ɗin a saman madubi ya zauna a gefen gadon yana jiran ta fito duk da sauri yake yi amman ya rasa dalilin daya sa yake son yaga taci abincin wanda ya dangana hakan da tsananin tausayi da yarinyar take bashi shi mutum ne da baya son A bashi yarda Ya ci amana tunda tace tasan baze cutar da ita ba shikenan ta sare mata duk wata laka ta jikinsa wadda yaci buri akanta mai yawan gaske.

Tsaki Aliyu yaja yana duba haɗaɗɗan Agogon zallar azurfa na Rolex dake ɗaure a tsintsiyar hannun shi, Kafin ya miƙe ya ƙarasa Bakin ƙofar toilet yaja ta buɗe durƙushe ya ganta ta riƙe wuya tana kakarin Amai.

Ƙamshin turaren shi ne ya sanar mata tsayiwarshi a wajan.

Da sauri ta taro ruwa tana wanke fuskarta da wajan da bata iya aman bama Ta miƙe ya matsa mata hanya ta wuce zaune tayi a bakin gado tana mayar da Numfashi Ya bita da kallo bayan ya

fito daga cikin Toilet ɗin.

A taƙaice yace mata.

"Wai menene hakan? ulcer ce dake kike amai baki ci abinci ba?"

Haushi ya kamata ta juya masa baya tai kwanciyarta tana cigaba da riƙe wuyanta dan har yanzu ƙarnin jinin da kuma ganin shi da tayi zuciyarta bata daina tashi ba.

Ya tako daidai saitin ta yana Facing inda ta kalla ɗin.

"Fatimah wai menene?"

Shuru tayi masa tai kamar Allah bai halittar shi a wajan ba.

Ya zube dukkan hannayen shi cikin aljihun wandon shi, kafin ya juya yabar mata ɗakin.

Yana fita kuma ta fashe da kuka ita kaɗai take magana kamar wata zararriya.

"Ya Allah! ka fitar dani daga cikin wannan hali wannan bawa naka ya cutar dani ina ji ina gani Mahaifiyar shi da ƙannen shi sun mayar dani ƴar aikin su"

Ta ƙare maganar cikin kuka bacci ne ya ɗauketa a haka ba ita ta farka ba sai azahar da wata irin haɗaɗɗiyar yunwa amman bata ko kalli inda taga abincin daya aje mata ba wanka tayi sannan ta sauya kaya ta fita Can sashin su hajjo.

Duk suna zaune wasu na Cire hancin kayan miya wasu na tuƙin tuwo ta ƙarasa tayi musu sallama Da far'a suka amsa mata murya a sanyaye tace musu.

"Hajjo ta nan dan Allah?"

Ɗahare da sakin fuska tace mata.
"Eh ga ɗakin ta can shiga tan ciki hutawa take dan bata jima da shigowa ba"

Miƙewa tayi ta nufi ɗakin Hajjo ta tarar da ita tana sallah, bayan hajjo ta idar da far'a ta dubi Farha.
"Ƴata yanzun nan nake tunanin ki fa araina bari na baki abinci nasan ba lallai kin karya ba"

Hajjo ta zubo mata kunun gyaɗa wanda yaji kwakwa tare da farfesun kayan cikin rago da doya da ƙwai.

"Maza kici ki ƙoshi ki mayar da kuzarin ki, Kinji marainiyar Allah"

Wata ƙwallah ta sauko wa Farha wadda bata bari Hajjo ta gani ba tayi sauri ta share ta ɗauki kunun sha take kamar magani gaba ɗaya tunanin Gida da Yadda tabaro Umma ya tsaya mata azuciyarta

Hajjo ganin datai kamar farha na cikin damuwa sai ta dinga bata labarai na abin dariya wanda kafin wani lokacin har ta shanye Kunun ta ci doyar sosai Anan ta shantake har la'asar tai sallah sannan suka jera da hajjo wadda zata ma su Ammi girkin dare Har Kitchen farha ta raka Hajjo wadda ta zauna tana taya Hajjo aikin Girkin haka kawai taji hankalin ta yafi kwanciya da hajjo taji hajjo kamar ƴar uwarta ta jini, Suna gama girkin wajan magariba Hajjo ta ɗiba musu nasu Farha takai kayan abincin dinning ta jera ta dawo ta gyara Kitchen Ɗin Hajjo nata shi mata albarka.

"To ƴata kije ɗakin ki kiyi sallah zan kawo miki naki abincin kinga magariba tayi"

Cewar hajjo.

"Farha ta tura baki gaba kamar yadda take ma umma in ƴan shagwaɓar suna kusa"

Cikin Muryar tausayi tace

"Dan Allah muje ɓangaranku ni anan tsoro nake ji ni kaɗai"

Hajjo tace mata babu matsala su tafi mana haka suka jera suka bar part Ɗin Ammi suka tafi nasu Hajjo a ɗakin Hajjo farha harda cire Hijabi bayan tayi sallah tayi kwanciyar ta aɗakin tuni sanyin fanka Ya saka taji wani bacci ya kamata Nan da nan ta soma baccinta a ɗakin hajjo ɗin.

Yana tafe cikin sauri sabida ya ɗan makara ya shiga motar driver yaja motar direct gidan gwamna suka je suka gama tattauna abin da zasu tattauna sai yayi kamfanin shi ya saka a hannu a wasu Motoci da za'a fitar zuwa Calaba anan ya zama busy bai sami kan shiba sai wajan bayan sallar magariba ya gaji iya gajiya ko Momcy ma sai waya yayi mata akan gobe yaje Gidan kokuma zai mata waya idan ya nutsu Kai tsaye Kuma gida ya nufa sukai sallah a masallaci ya fita waje ganin masu neman taimako ya kuma komawa masallaci yayi sallar isha'i daga nan part ɗin Ammi ya nufa don ya sha shayin sa na ƙa'ida duk dare Ammi ta haɗo masa shayin suna sha suna hira har ya kammala Ammi tana masa maganar dawowar Mami Wadda zata dawo Gobe a yadda Mamin taiwa Ammi waya ta sanar da ita

"Ammi ni zan je na kwanta na gaji, Ƙila ma gobe Bashir zai dawo fa yayi Min waya ɗazu"

Ammi itama miƙewa tayi tsaye tana cewa.

"Nima ya gaya min ɗazu a waya har ina masa tsiya ya zauna a abuja"

Daga haka sukai sallama Ammi ta nufi ɗakinta shikuma ya Nufi hanyar fita har ya kama Kofar zai fita kuma sai ya tuna da Yarinyar nan ko yaya take ciki shidai baiji motsin taba kuma Ammi bata masa maganarta ba ɗakin ya nufa sai dai yana tura ƙofar yaga wayam bata cikin ɗakin yadda ya aje mata break haka ya tarar dashi da sauri ya iska Toilet nan ma bata ciki Aliyu ya yarfe zufar data gama jiƙa masa Jikin sa kardai Guduwa yarinyar nan tayi to tayaya ma zata iya guduwa.

Sai ya shiga safa da marwa a ɗakin Ta yaya zai iya tambayar Ammi zagaye ya dinga yi a ɗakin Shi kaɗai ganin hakan ba zata masa ba ya sanya shi Fitowa daga ɗakin ya nufi hanyar ɗakin Ammi........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*30*

*A LOVE STORY 30*

Bedroom ɗin su safna ya fara shiga ya zira kanshi ya leƙa ciki suna kwance ko wacce riƙe da waya suna charting gyaran murya yayi wanda yasa ko wacce ta juyo babu shiri ya tamke fuska murya a shaƙe yace musu.
"Why are you not sleeping? salon kuzo kuna samun carry over a makaranta kuzo ku ɗagama Ammi hankali alhalin kune bakwa mayar da hankali akan karatun yanzu ƙarfe nawa amman kun zauna Kuna charting da samarin da ba zasu aure kuba"
Kowacce ta shiga hankalin ta ko tari basu yi ba ya gama cin mutuncin su yaja ƙofar bayan yaja musu kunne akan ya hana su chart ɗin dare yana fita safna taja ajiyar zuciya cike da tsoro ta dubi Sajeeda.
"Sis nifa wallahi in naga Ya Ali gabana faɗuwa yake Mutum kullum sai baƙar zuciya fuska a tamke"
Sajeeda wadda take faman sakin Numfashi tace.
"Hmm nifa har yanzu ban gama dawowa daidai ba wallahi yaya akwai bala'i ko me ya ruwan shi damu oho Ammi ma bata ɗaga mana hankali ba sai shi wallahi nifa nafi son ya sadik akan ya Alin nan"
Safna ta kama baki har tana zira kanta ta window tana leƙan shi.
"Amman sis baki da kirki Nikam ko wanne ina so acikin su shi kawai Ya Ali ya cika takura ne Kin san Allah Ko Aunty mami ma haƙuri fa take da halin shi watarana naje part Ɗinsu Tea ta zuba mai By mistake ta cika masa sugar ke kinga yadda ya rufe ido yana mata bala'i kamar zai dake ta"
Sajeeda dariya take har tana riƙe ciki kafin tace
"Nikuwa har kin tina min dukan da yayi ma Aunty salma kafin tai aure har targaɗe yaji mata, Amman kuma fa ya Ali ya iya love dan ranar dana rakasu Hospital da Aunty Mami baki ga yadda yay ta mata ba nidai ina son Miji Irin ya Ali wallahi irin su nada wahalar samu ko acikin

maza yana da zafi yana da kirki, kawai in baka san halin shi bane zakuyi ta samun matsala amman wallahi yana da haƙuri dan yadda Ammi ta riƙe masa wuta akan Aunty mami kin san Allah ko ya sadik ne baze yarda ba Kina kallo Mai Aunty mami keda aba kamar tsinke ni ban taɓa ganin siririn mutum irin taba Kirjinta yasin kamar na farar babe"

Habawa safna mai zatai inba dariya ba.
"Haba sis ta yaya zakice Kirjinta kamar na farar babe ta yaya kika gani?"
Safna ta faɗi har Lokacin dariyar take yi bata daina taba.
Sajeeda tace.
"Tab in ta dawo ki zuba mata ido an ya wannan akwai size na bra ɗinta ma wannan halitta haka ƙananu gaskiya yaya Ali yana haƙuri, Kuma nina tabbata duk ranar daya samu wadda yake so wallahi ba baki nayi ba amman daga Aunty mami har Ammi kashin su ya bushe domin Mami ba zata same shi irin yanzu ba ita kuma Ammi zai bujere mata ne dan kawai biyayya yake mata"
Safna tace.
"Tab duk soyayyar ya Ali da Ammi ke kina zaton akwai wadda zai bijirewa umarnin Ammi akan ta kema dai sis faɗi kawai kike"
Sajeeda dariya tayi.
"To meye umarnin ammi ɗin in ba son zuciya ba Be patient with what I have to say, gaskiya ce ɗaya Ammi bata kyauta wa ya Ali ba, ki ɗauko mace mai suffar maza ba gaba ba baya ki haɗa ta da jarumin maza sai tsayo Kamar zare fisabilillahi dan kawai kina da ra'ayin kada ya auro wata tazo ta rabaku wani rabo Safna? meye baiwa Ammi ba mu maye bai mana ba kamfani guda ya ɗauka ya bawa ya sadik shike juya shi daidai da gidan da yake ciki nashi ne Ya Bashir shike da matsayin manager a kamfanin shi na kano mu meye bai mana ba daidai da Aunty salma duk shekara tare yake haɗamu Muje Hajji muje umara muje dubai Mu hau motar da muke so musa kayan da muke so mu sai wayar da Muke so Duk kudin waye bana saba? ya kamata Ammi ta rabu dashi ta zubawa sarautar Allah ido IDAN RABO YA RANTSE Fa sai mai shi Rabo dangin ajali ne ta yuwu ba ajikin Aunty mami rabon Ya Ali yake ba amman Ammi taƙi ganewa ko ita mamin tasan meye azuciyarta datake ta wannan haƙilo domin ita oho"

Safna tai shuru tana nazarin maganar ƴar uwarta tabbas komai sajeeda ta faɗi haka ne gaskiya ne maganarta.
"Hakane sis nikam na rasa wace irin soyayya ammi kewa mami Kamar aikin asiri sam kaƙi farin cikin ɗanka akan na ɗan wani shegu munafukai masu kalar Munafurci ni shiyasa kika ga bana mata da sauƙi sosai na riƙe mata wuta damma ammi na min magana ne ke nifa daga Aunty Mami har Aunty sakina wallahi basu Min ba ita ma Aunty sakina matar ya sadiƙ ina taga wani kirki sai jida kai da kallon mutane ɗaiɗai gashi ki lura ƴar bariki ce sam bata ƙaumar Aunty mami ko zuwa sukai nan kiga fa bata sakin jiki da Aunty mami wannan inda a haɗe suke ma da kishin faccalan ci zasu yi kodan kwanaki tace wa ya Ali yaje ya auri ƙanwarta yaƙi ne oho amman naso naji maganar yana gayawa Ammi"

Sajeeda Dariya ta saki.
"Au wannan ƙanwar tata jamila wadda take acan lagos ɗin wadda suke zuwa nan tare hutu ita take son taima ya Ali an cusai da ita haha lallai kam shiyasa naga tanawa Aunty mami gani gani

mai ya Ali zai da jamila ai ba sa'ar shi bace ita kanta Aunty sakinar ai  kamar ta girmi ya sadik"
Haka suka cigaba da hirar su har lokacin baccin su yayi suka kashe ƙwan ɗakin suka kwanta baccin su.

Aliyu yana barin ɗakin su safna wanda dama neman Farha yaje sai ya wayance da musu faɗa ɗakin Ammi ya shiga by lucky tana toilet ya duba bai ga Farha ba yaja mata Ƙofar yabar ɗakin sai da ya fito parlou ma yake tunanin meze kaita ɗakunan su kama Ƙugu yayi tunanin shi ya ɗauke yama rasa meze yi a wannan Lokaci haka yaja ƙafafun shi da suka masa sanyi ya fita daga parloun Ammi part ɗin shi ya koma yayi wanka ya sauya kaya zuwa jallabiya fara mai dogon hannu daga ciki ya saka dogon farin wando mai santsi  ya fesa turare mai ƙamshi Ya sauka ƙasa ya haɗa tea yana sha yana nazari a ƙa'ida yanzu ba abin da yake buƙata sai bacci amman ina yaga  ta yin bacci bega yarinyar mutane ba wadda yasan ko ba daɗe ko bajima Mahaifanta zasu Buƙaci ganin ta in yayi sake tayi wani gurin meze ce musu duk ranar da suka buƙaci ƴar su.
Aje tea cup ɗin yayi a center table ya ɗora dogayen ƙafafun shi a saman Table ɗin ya sanya hannun shi yana cakuɗa sumar kan shi yana hasko Rashin mutuncin daze mata idan ta yarda ya ganta a duk inda taje.
Daga bisani miƙewa yayi ya fita daga parlou ɗin duk inda ya Shiga ma'aikatan gidan maza suna Masa barka da fitowa zagaye ƙaton Gidan yake Har ƙarshen katanga daga ƙarshe yaje wajan masu gadi.

"Salamu Alaikum"
Da sauri masu gadin suka ƙaraso wajan shi suna amsa sallamar.
Ya harɗe hannaye a ƙirji.
"Malam ɗalha baku ga yarinya ƙarama ɗazu ta fita ba?"
Suka ɗan yi jimm kafin malam ɗalha yace.
"Gaskiya yallaɓai bama wanda ya shigo yau a mata bare a fita Ina fatan dai lafiya?"
Girgiza kai yayi tare da juyawa a lokacin ranshi ya soma ɓaci hankalin shi kuma ya soma Tashi a karo na farko daya soma jin Ammi ta sosa masa rai na yadda tai buris da lamarin ƴar mutane wadda inda tana saka idanu akanta ba zata Fita ko ina ba dukkan laifin kuma ya ɗora su akan Ammin sane sai dai baya da yadda zeyi ya Tuhume ta dan an ce wata fuskar tafi gaban mari.

Shi kaɗai a harabar gidan har wajan 11 yakai ya komo baccin ma ya ƙaurace masa da sauri ya nufi wajan mota ze driving yaje gidansu kota je sharf kuma ya manta bai ɗauko key ba ya juya suka ci karo da Hajjo.

"Ɗana barka da dare?"

Ya juyo yaɗan saki ranshi kaɗan.

"Hajjo daga ina da wannan dare baki bacci ba?"
Hajjo tai dariya.

"Bacci ɗana ai har yayi mini yawa yanzu ma fita zanyi titi goro na ya ƙare nasan zan sha faɗa da masu gadi amman haka nan zasu barni kaina har ciwo yake in banci ba"

Aliyu yay murmushi yana cewa.

"Hajjo bada ban goro nada illah ba dana sa an kawo maki hunhu dan ki daina fitar dare bani so hajjo kada watarana Mota ta kaɗe min ke"

Dariya tai tana cewa.

"Allah zai kiyaye bara nai sauri na baro Ƙanwar musa marainiyar Allah kada ta farka daga bacci taji tsoron ɗakin dan duk su Tasallah sunyi bacci"

Aliyu ya sosa kai.

"Hajjo gashi ban fito da canji ba dana baki na goron"

Tayi dariya.

"Kada ka damu, Niko ɗana wannan ƙanwar Musan itama ƴar ƙauye ce ni dai banga tayi kama da mutan garinmu ba ɗazu taita karanta Min sunayen kayan abinci a kicin"

Sai lokacin ya gano Hajjo da wadda take Nufi da kanwar musa Ɓoyayyar ajiyar zuciya yaja kafin ya tamke fuska.

"Hajjo ina zan sani Bana nan ya kawo ta Kije kada dare yayi kinga lokacine na Damuna sabida ruwa"

Hajjo da sauri ta juya tana tafiyarta har da saurin ta.

Juyawa yayi direct sashin su Hajjo ya nufa Sashin nasu babu kowa duk sun rufo ɗakunan su ya gane ɗakin hajjo sabida yafi na duk ma'aikatan tsari ya tura Ƙofar ta.

Ajiyar zuciya ya sauke mai ƙarfi daya hango farha tayi ɗaiɗai a saman gadon Hajjo tana sharar Baccin ta hankalin ta kwance ya jima a tsaye yana kallon ta yay kamar ya rabu da ita tunda yaga inda ta kwanta ɗin sai kuma yaji baze iya ba.

Ya shiga buga gadon Hajjo da sauri yana furta.

"Fatima ke fatima tashi"

Cikin magagin Bacci ta buɗe ido tana cewa.

"Ni dan Allah umma ki rabu dani bacci nake yau ba zani aikin ba"

Yayi murmushi ya rasa ƙaunar fatima da wannan aiki.

"Ke tashi mana kona zuba miki ruwa, Kin san kina son umman kika Lalata aikin ki kika ci amanar aikin ki son zuciya ya kaiki ya baro to nan a kurkuku kike ba'a gidan umma ba"

Da sauri ta watsake ta zuba masa jan idanunta wanda bacci ya sanya ya koma jajir ɗin........

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*31*

*A LOVE STORY 31*
Yana tsaye a kanta fuskarshi ba yabo ba fallasa kamar koda yaushe ƙamshin mayen turaren shi mai azababban ƙamshi ta shaƙa tana ƙoƙarin juya masa baya yayi saurin ce mata.
"Kada ki kuskura ki koma baccin nan ko ni sa'an wasan kine ina miki magana shine zaki koma bacci"
Ya faɗa a hasale.
"Toni me zan maka da tsakar daran nan mutum sai Mugunta na gudo nan ɗin ma ba zaka barni ba"
Ta faɗa tana turo baki gaba wanda ya fito da zallar ƙuruciyarta ta kwaɓe fuska kamar zata zubo da hawaye
Ya gyara tsaiwa ya harɗe hannun shi ido ya zuba mata yana hukunta ta da kallon shi mai azababban saukar mata da dukkan wata rashin kunyarta
Tsit tayi ta sunkuyar da kanta a ƙasa dan ba zata jure wannan kallon nashi ba.
"Don't let me count to three before you wake up"
A kausashe ya faɗi maganar wadda ta sanya farha miƙewa ta ɗauki hajib ta saka Fuww ta wuce shi tana gunguni tana tafe yana binta a baya kamar jela har suka bar part ɗin su Hajjo.
Adaidai Hanyar part ɗin su Ammi taga ƙaton Farin Muzuru zai shiga Falon Ammi ai da wani uban sauri tayo baya direct kanshi tayi ta cakume shi tana sakin ajiyar zuciya da sauri ya Ɓamɓareta daga jikin shi.
"Ke dallah meye haka zaki taɓa min jiki na kamar na sa'anki"
Muryarta na rawa take nuna masa.
"Wani farin abu na gani zai shiga falon Dan Allah kayi gaba in koma bayan ka"
Banza yayi mata dan takaici ta bashi yayi gaba tana binshi da sauri har ya ƙarasa bakin Ƙofar Falon ya tsaya ta Ki tafiya.

"Wai ke kamar wata ƙaramar yarinya tsaiwar me kike ba zaki shige ba"
Turo baki tayi wanda ya zama ƙa'idarta
"Ni ka rakani to tsoron wannan abun nake"
Ya bita da kallon Minti guda ya kawar da kanshi bai ce mata komai ba taga ya juya yayi tafiyar shi.
Wani tsoro ne ya kama farha tattare rigarta tayi da gudu ta shige Falon Ta nufi ɗakin data ke sai mai da Numfashin Tsoro take yi Ƙofar ta sanyawa Key ba kowa a falon Haka ta kwanta ta jima bata yi bacci ba tana ta faman Juyi a saman gadon can dai bacci ya ɗauketa.

Hajjo tana dawowa taga wayam bata ga farha ba aranta tai tunanin ta tafi makwancinta shiyasa bata damu data Bibiyeta ba haka ta kwanta a saman gadonta itama baccinne yayi gaba da ita.

Aliyu tafe yake yana tsaki har ya ƙarasa part Ɗinshi

Ya haura saman shi rigar Jikinsa ya zare ya kwanta a saman gado yana ta jan tsaki har Lokacin Yarinya kamar Ƴar yaye komai sai an mata ga rashin Kunyar tsiya shifa wannan ne dalilin daya sa sam ƙarin aure baya Burge shi itama bada ban taja wa kanta ba da baze aure taba, Shi ina ze iya auran ƙaramar yarinya wadda kullum cikin baka ciwon kai take Shifa ko fushi yayi mami ke rarrashin sa shi bai saba da lallaɓa mace ba shiyasa idan tayi wani abun yake jin kamar ya rufe ta da duka dan takaici.

Ya mirgina yana shafa ƙasumbar data taru a fuskar shi wadda kwana biyu bai yi gyaran fuska ba.

Adaidai wannan Lokacin wayar shi dake yashe a gefe ta soma ringing Ya lalubota ya ɗaga.
Muryar mami a narke tace.
"Aminci da rahmar Allah su sauka a gare ka Mijin Mami"
Kadaran kada hakan yace.
"Tare dake"
Taja ajiyar zuciya.
"Ka soma bacci ne Sweet me?"
Ta taɗa muryarta a narke kamar zatai Kuka.
"A,a"
Ya faɗa a taƙaice
"Me yasa baka yi bacci ba ko tunani na kake yi?"
Ya janyo pillow ya matse.
"Mami inna ce Miki bakya gabana yanzu ba zaki yarda ba?"
Taji gabanta ya faɗi shifa wani bin idan ya saki magana se kace goyon gwauro sam bai iya magana ba duk yadda tazo masa haka yake faɗar ta amman bata sani ba ko ita kaɗai yake wa hakan oho.
"Kamar yaya bana gaban ka ina matarka ta sunna me kake nufi?"
Ta faɗa kamar zata saki kuka!
Ya lumshe ido burin shi ya ɓata mata rai kamar yadda ta ɓata masa.

"Understand me, idan nace zan tunanin ki hakan ze jefani cikin wani hali ai kin san yadda nake Kuma kin san ke kaɗai gareni kika tsallake kika tafi hutu kika barni, Ni me yasa in kina gida ko tafiya zanyi dake nake tafiya amman ni sabida ban da ƙima da daraja a idanun ki shine kika tsallake with out my permission kikai tafiyar ki Mamy"
Gaba ɗaya jitai hankalinta ya tashi.
"Kamin afuwa Hubby Mama ce tace nazo na huta amman hakan baze sake faruwa ba In sha Allah gobe ina tafe da tanadi mai zafi"
Bai wani ji maganar tata ta shige shi ba yace.
"That will be later"
Ya aje wayar.
Ya ja pillow yayi kwanciyar shi batare da ya sanya tunanin Mamy a ran shi ba.

Baki ta saki tana bin wayar da kallo kafin taja tagumi hawayen takaici yana zubo mata a haka Hajiya tajira ta shigo ta sami Mami.
"Ke kuma lafiyar ki kukan me kike haka?"
Mami ta aje wayar.
"Mama yaushe zan sami yadda nake so a wajan Aliyu? me yasa Aliyu bai ɗauke ni da daraja a rayuwar shiba?"
Tajira ta zauna gefen mami.
"Sabida ke matar tushe ce kuma bahaushe yace matar tushe bata daraja"
Mami cikin tashin hankali tace.
"Mama har ladan noma ana bada mata kuma hakan besa mazajen su sun raina musu Aji ba, Amman ni cikin shekara goma da aure ina masa hidima ina ɗaukar cikinsa yana zubewa bai taɓa Nunan Kulawa cikakkiya ba Shi kamar mai Jinnu kullum cikin ƙunci wallahi nina tabbata arziƙin Ammi nake ci a wajan sa nina rasa yadda zanyi Aliyu ya soni Wani irin maganine bana sha na gyara ba amman daga ya gama dani baze ƙara waiwayata ba sai wani Lokacin"
Ta faɗa batare data tuna da wa take maganar ba Jitake kamar da ƙawarta take magana ba uwarta ba

"Kece na gaya Miki abin da zaki amman kinƙi yarda Nifa zuwa yanzu na dena son auren ki da Aliyu burina ya mutu Mu gina kammu"
Mami tayi ƙasa da kanta.
"Mama ina son Aliyu ba zan iya sanadin barin shi duniya ba ada na auri Aliyu da tarin manufofi Amman yanzu manufata da auren Aliyu shine naga na haihu dashi Komai nashi dashi kanshi ya dawo ƙarƙashin Ikona"
Tajira taja tsaki.
"Ki shaƙe ɗan iska ya sheƙa akwai hanyoyin ɗaukar rai kala kala  ya mutu ga maza nan sai wanda kike so kawai Ki kashe shi waze ɗauka kece tunda daga ƙarshe Ki ƙalawa uwar sa kice ita ta kashe shi dan tana baƙin Cikin ya haifi ƴaƴa Su gaje shi, Shikenan fa a baki tuminin takabar ki Kizo mu fantama tunda Dai Boka ya tabbatar ba wani aiki daze ratsa Aliyu Itama Aminar da yaya aikin yaci kanta har ta gigice akai auren naku"
Mami tabi Mahaifiyarta da kallo.

"Mama nidai addu'a zaki min na haihu da Aliyu shine burina Amman bana fatan na ɗauki rayuwar shi wallahi Ina son shi!"
Zagi uwar tahau yi wa mami kafin ta Miƙe tabar mata ɗakin.
"Wallahi mama ba zan iya kashe Mijina akan abin duniya ba Ni burina ya haihu dani na mallake shi yanda ita kanta uwar tashi sai tai shekara bata sanya shi acikin idanunta ba"
Ta faɗa a bayyane kamar wani na Jinta.
Ranar da tunani kala kala Mami ta kwanta bacci rabi na Maman tane ada mamanta tana goyon bayan ra'ayin ta sai dai tun Jiya data je wajan Bokan su ya basu tabbacin ba zasu sami Aliyu yadda suke soba shine Tunanin Mamanta ya karkata ga shawarar da Bokan ya basu akan kawai su kashe Aliyu Ko banza Mami zata ci Tuminin takaba ita Kuma Mami ta turje akan abarta inta koma tasan zata kuma samun wani Cikin wanda take sarai ze zauna ajikinta.

Da Asubah Farha ta Miƙe taje tayo awala tai sallah ta koma baccinta Har wajan 10 tana bacci kafin Safna tazo ta Buga mata Ƙofa............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE*

*32*

*A LOVE STORY 32*

Idanunta fal bacci ta taso gaban ƙofar muryarta sanyi ƙalau wadda ta ɗan dashe irin ta masu bacci tace.
"Waye" a zaton ta shine sabida ƙofar akwai key har lokacin bata zare ba tun jiyan data ma ƙofar key da zata kwan ta bacci.
Ga mamakin ta sai taji muryar ɗaya daga cikin ƴan matan tace mata.
"Ubanki na ƙauye ne taso Ki buɗan daƙiƙiyar banza"
Tashin hankali ƙafar Farha rawa ta soma yi wani irin Ɓacin rai ya ziyarci Zuciyarta.
"Sai dai ubanki na birni ya taso ya buɗe miki jaka dabba wadda bata san darajar ɗan adam ba to nafiki zama ƴar hau"
Ta faɗa a zuciye idanunta har sauya kala yayi.
Ihu Safna ta saka tana dukan ƙofar da ƙarfi tana ɗurawa Farha zagi Ta uwa ta uba tana shan alwashin idan ta buɗe ƙofar sai ta La'anta ta.
A fusace Farha ta buɗe Ƙofar wadda Safna ta janyo Farha Falon su ta watsata a center ɗin falon safna ƙatuwa ce farha ƴar ƙarama rufe Farha tayi da duka wanda Ihun Farha shiya janyo Hankalin Ammi da Hajjo dake Kitchen tana haɗa break fast Sajeeda ma dake ɗaki aguje ta fito Falon wanda yayi daidai da lokacin da Safna ta haye ruwan Cikin Farha tana jibga kamar ta sami jaka.
"Ke Safna kashe ta zakiyi baki da hankali" cewar Ammi tana ƙoƙarin Riƙo safna wadda ta naɗe hannun riga tana dukan Farha.
A zuciye ta miƙe tana tsuma.

"Ammi wai yarinyar nan daga naje kiranta ta wanken Toilet zan wanka shine ta hau zagin Babana me na mata"
Ta faɗa tana wawuro Farha wadda har Fuskarta wajan idanunta ya fashe Sajeeda ita ma kukan kura tayi ta janyo farha tana duka haka suka rufu akan ta duk yadda Ammi take Musu magana basu ji ba Ammi Fushi tayi taja gefe tana cewa idan sun kashe Ƴar mutane hukuma zata ɗaure su a banza Hajjo kuwa kuka take tana a kawo musu ɗauki.

Cikin sauri ya ƙaraso Falon Ammi sanye yake cikin wani azababban lallausan Yadin Tissue mai azabar kyau wanda kyansa ya nuna tsadar sa sai ƙamshin Mayen turaren shi mai kama hanci yake Yana tafe yana duba agogon Fata fari tas dake hannun shi sabida so yake yaje Daura A yau ɗin ya dawo dan ganawa da wani babban ɗan siyasa wanda yake siyan motocin sa.

Abin da Aliyu ya gani shine ya sanya shi ƙarasawa Cikin falon da sauri Idanunshi ne ya hango masa aika aikar da ƙannen shi ke shirin yi wanda sam su idanun su ya rufe basu san da shigowar shi falon ba.
Direct wajan Wayar jikin Tv ya nufa ya ɗano ta irin mai kaurin nan daga safna har sajeeda har ammi da hajjo basu ji takun shi ko maganar shiba sai saukar wayar kawai suka ji yana laftawa su safna ajiki waɗanda sukai saurin sauka daga saman Farha suna Ƙoƙarin guduwa Haɗe su yayi ya gwara kawunan su waje ɗaya nan da nan Goshin su ya fashe abin ka da fararen fata kafin ya saka ƙafa ya kwarfe su faɗuwa sukai ya shiga tafka musu Wayar wadda duk sai da ya fitar Musu da jini ajikin su.
Tun Ammi na kallon Abun a wasa har ta zo gaban shi tana masa magana amman bai saurare ta ba sai da ya tabbata ko hannu basa iya ɗagawa sannan ya cillar da wayar Sai nace tunda mai gani yake ganin idanun Aliyu bai taɓa ganin Yanayi irin na yanzu ba idanun shi har wani ruwa ya tara sabida jaa ita kanta Ammi Baya tayi sai Huci yake Jikin sa yana tsuma.
"Ammi inda ban zo ba kina kallo zasu kashe Musu ƴa nawa take zasu rufu su Biyu akanta suna dukan ta uban me tai musu"
Ya faɗa yana Zaro ido waje.
Sajeeda data miƙe aguje tai ɗaki ta ɗaga Murya tana cewa.
"Ko kai kaji abin da tai haka zakai mata babanmu ta zaga yaya"
Aguje yabi ta wadda yake cewa.
"Ta zagi uban naku ubanku yafi nata daraja ne"
Kamar yasan abin da ya haɗa su ganin yana neman ya cimmata yasa Ammi ta ɗaga Murya.
"Baba kada ka kuma dukan min ita abin ya isa haka ai ba jakai bane akan wannan jarababbiyar yarinyar yau kake wa ƴan uwanka wannan dukan kamar bare to na gaji Wallahi kawai Musa yazo ya tafi da ita dan bazan aje masifa agidana ba"
Bai ko saurari Ammi ba ya ƙaraso gaban Farha wadda take kwance kamar gawa ya ɗagata cak yayi ɗakinta da ita daga Ammi har safna data sha duka da Hajjo sakin baki sukai da hanci suna kallon ikon Allah.

Shikuma yana zuwa tsakiyar ɗakin ya direta sai Lokacin ta sami damar kuka dukan shi take a ƙirji tana wani irin kuka!
Muryarta a shaƙe take ce masa.

"Daka bari ai sun kashe ni mai yasa zaka Duke su ba jaka baiwa ka siyo musu ba ai da ka bari kawai sun kasheni ba zaka tabbatar Min da baka ƙaunata ba har se ka sa sun kashe ni ka kaiwa Iyayena gawata"
Takaicin ta ya kamata Aliyu bai san sanda ya wanke ta da tagwayen maruka har Biyu ba zaman ƴan bori tayi a tsakiyar ɗakin ta saka wani irin Kuka ya juya zai fita daga ɗakin da wani irin Sauri ta miƙe aguje tabi bayan shi ta ɗane bayan shi ta cakume shi gam tana kuka.

"wallahi yau sai ka kasheni nasan nai maka laifi dana yaɗa labarin ka ba akan gaskiya mai yasa ba zaka kaini Kotu ba to in ba zaka kaini kotu ba ka kasheni ai kai mai Kuɗine in ka kashe ni ka kashe banza ba mai maka magana amman ni nagaji da wannan ƙaddararran auren naka gwara kawai anyi ta ƙare"

Juyo da ita yayi gaban sa ya saka hannu ya riƙota cak ya ɗorata a saman Ƙirjinsa ya kaita kan gado ya aje ya sunkuyo daidai Fuskarta har tana Juyo kamshin cikin bakin sa.

"Shiii why are you raising your attention on something that is impossible?"
Ya miƙe tsaye tare da zube hannayen shi acikin aljihun wandon shi.
"Ba abin da ze faru acikin dukkan da kika lissafo kawai abin da na sani kece zaki ci baƙar azaba a wajan su in kika cigaba da rashin Kunya in kin mani na jure su ba zasu jure ba"

Ya faɗa hankalin shi a kwance a wannan Lokacin ya sami Nutsuwa ba kamar lokacin da ya shigo falon ɗazu ba.
Murya cikin kuka tace.
"Allah ya isa tsakani na dakai ko wuta tana cin kabarin ka bazan yafe maka ba"
Ya riƙe baki cikin mamakin furucin ta.
"Baki da ɗa'a fatima baki da tarbiya bada ban ina tuna wasu abubawa ba dana miki abin da zaki Dena min wannan tsiwar amman ba damuwa ai ga basawan Ammi nan sun ishe ki haka zasu yita dukan ki kamar Allah ya aiko su"
Kuka ta kuma fashewa dashi.
"Zan so suyita dukana daga nan har suyi sanadin ajalina"
Yayi Murmushi mai sauti.
"Mu gidannan bama kisa amman akwai horo ga marar Kunya irin ki Kuma daga yau bani kuma tare miki tunda nima Kin riga da kin rainani bakya ganin darajata a matsayina na"
Bai ƙarasa ba kuma kome ya tuna Oho ya lalubo wayar shi dake Ringing acikin aljihun shi.
"Hello Musa Okey ka bani Minti Biyu gani nan ok" ya katse Kiran.
Ya ɗan dube ta.
"Ki sami ruwan ɗumi ki gasa fuskar ki baki ga yadda ta ƙara Miki Muni ba"
Ya faɗa yana Wani ɗan iskan Murmushi.
Pillow ta ɗauka ta cillo masa ya cafe yana dariya ya fita yabar ɗakin................*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 33*

Yana fita daga ɗakin nata ya gyara fuskarshi daga dariyar da yake ta koma a ɗaure tamkar bai taɓa dariya ba har Lokacin su Ammi suna falon bai ko kalli saitin kowa ba ya wuce yana ƙoƙarin fita daga falon Ammi ta kira sunan shi a hasale.
"Baba baka ganni a falon bane?"
Cak ya tsaya duk yadda yaso daidaita yanayin sa abun yaci tira a yadda fuskar shi take ya ƙaraso wajan Ammi ɗin ya sami Kujera mai kallon wadda take akanta ya zauna yana duba agogon hannun shi har Lokacin Bai saki fuskar shi ba wanda hakan da yayi ya ƙara jefa Ammi cikin shakku.

"Ita ɗin Meye haɗin ka da ita da zaka ɗagata Ku shiga ɗaki harka jima a ɗakin nata Me kuke yi?"
Wara ido yayi Wanda hakan ya ƙara haska zatin kyan da Allah yayi mishi.
"Ban fahimci me kike nufi ba Ammi I don't understand what you mean by this statement kimin yadda zan fahimta?"
Ya faɗa yana kuma duba agogon shi ya matsu yabar Falon sauri yake.
"Naga kamar sauri kake ka tashi ka tafi"
Ko motsi ya kasayi sabida dama can in Ammi tana fushi baya iya kataɓus yanzun ma wannan yanayin ya ji a tare dashi.
"Please Ammi Kada na fita kina fushi dani"
Ya faɗa Yana ƙoƙarin ƙaƙalo Murmushi amman ya kasa dan har yanzu maƙogwaron shi a bushe yake tamkar wanda aka gasa da wuta.
"Nidai kawai ka kira Musa yazo ya ɗauke waccan jarabar Tunda kake baka taɓa ma ƴan uwan ka irin dukan daka Musu akan wannan yarinya ba Haka kawai ban san abin da ze faru nan gaba ba sabida haka tun wuri gwara tasan inda dare yayi mata"
Ya zuba mata ido harta kammala maganarta kwantar da murya yayi sosai.
"Ammi sai kawai abar Su, akanta suna dukan ta itama fa mutum ce kamar su meye bambancin su? ƙila ma tafisu Muƙami a wajan Allah wallahi akan wannan yarinyar sai muga ba daidai ba wajan Allah, Gaskiya Ammi bani da idanun dazan tari musa akan yazo ya ɗauki ƴar ƙanin mahaifinsa a gaban mahaifiyata ta kasa riƙeta bawan Allah'n da ƙila ma ya girmeni amman Hidima yake min ba dare ba rana Girmamani yake tare da dukkan wani abu nawa Musa yana min abin da kuɗina ba zasu mini ba I can assure you of that'
Har yakai aya a bayanin sa tana kallon shi dama tasan za'ai haka wani irin kafaffan ɗa Allah ya bata tun yana ƙarami haka yake idan yace Eh hakan ne idan yace a,a da wuya a sauke shi akan wannan tsarin.

Ta ɗaga murya sosai.
"To naji bayanin ka ai kai Ko ɗan jarida bai kaika tsari da tambayar tsiya ba To kajini da kyau bazan lamunci iskancin ta agidannan ba wallahi ta ƙara misayar yawu dasu Safna sai na koreta da kaina ba tare da Neman shawarar kaba baze yuwu yara da gidansu azo a takurasu ba kuma kai ma daga yau kada na kuma ganin daidai da magana ta ƙara haɗaku nan ga Hajjo nan da muka shafe shekaru ai banga kana Janta kamar yadda kake wa yarinyar can ba mai kama da sauro"

Ta faɗa tana wani irin huci.

"Ammi halittar Allah ce dai ba kyau ka haɗa mutum da dabba Don in aka barka kai ba zaka yi dukkan su ba, Amun afuwa tunasarwa ce"
Daga haka ya miƙe yabar mata falon batare daya Yi mata sallama ba.

Ammi tagumi ta zabga kafin ta fara magana da hajjo dake jere abin karyawa a dining.
"Hajjo kinga baba ko An ya zan iya barin yarinyar nan agidannan tunda nake da Baba bai taɓa Yin ja in ja akaina ba sai akan waccan matsiyaciyar mai kama da Tsinken sakace Ina da sake"
Ta faɗa tana Miƙewa tsaye da sauri Hajjo ta ƙaraso.
"Haba hajiya Amina ina tunanin ki ze tafi duk abin da Ɗana ya gaya miki gaskiya ne Kada kije ki faɗa Fushin Allah sanadin yarinyar nan faɗa ne sunyi shi da su Safana sabida haka Ki rabu dasu shi kuma kin san Ɗana yana da tausayi Ta yuwu tausayi yarinyar ta bashi amman ki kwantar da hankalin ki"
Ammi har Lokacin se huci take.
"To ita dasu ɗaya ne gidan uban ta ne da gadon ta acikin gidan Haka kawai bare yazo yafi ɗan gida"
( Hhh hajiya Ammi gidan Mijinta ne kece baki da masaniyar hakan )
Hajjo ta kuma yin ƙasa da murya.
"Ina fa ba gidan uban ta bane wane Mutum da aikin Aljan ai wani kaya sai amale ke ɗauka Allah ya huci zuciyar uwar ɗakina ki mata afuwa mai zuciya da sisin gwal uwar sadiƙ da Aliyu ga bashir a gefe Allah dai ya jiƙan Alhaji da gafara ya raya su salma"
Ammi bata iya furta komai ba ta wuce ɗaki a ranar ba wanda ya kuma fitowa falo sabida ammi a ƙule take an taɓa ƴaƴan gwal tana ɗakin su Safna na cinyarta sajeeda na kafaɗarta ta gama gasa Musu Jikin su sai kuka suke duk Fuska da Jikin nasu ya haye yayi sumtum ita kam Safna data fi Jigata zuwa azahar zazzaɓi ya rufeta har rawar Ɗari take hankalin Ammi daya kuma tashi rasa yadda zatayi da safna tai daga ƙarshe wayar salma ta kira tana sheda mata A gigice salma ta hawo Mota daga asibitin data ke aiki kasancewar ta Nurse Ce ta tawo gidan bayan ta shaidawa Mijinta halin da ake ciki ta cikin waya.

Zuwan salma ne yasa Ammi taɗan sami Nutsuwa Allurai salma ta rubuta da ƙarin ruwa ta bai wa driver yaje pharmacy ya siyo musu.
Minti kaɗan ya kawo ta haɗa alluran cikin ruwa ta ƙara wa safna wadda zuwa Lokacin har baccin azaba ya kwasheta itama sajeeda maganin ciwon Jiki ta samu tasha ta kwanta Salma ta dubi Ammi wadda har tayi wujiga wujiga dan fargaba tace mata.
"Ammi wai meke faruwa ne agidan naki da alama ba normal zazzaɓi bane kamar akwai shatin duka ajikin ƴaƴan naki Allah yasa ba Bashir bane ya sauke gajiyar shi ajikin su?"
Ammi da ta kuma haɗe rai tamau ita ta dubi salma tare da cewa........
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 34*

"Ai inda Bashir ne ya dake su da ba zakiji wayata ba, sabida ina bashir ze iya musu wannan

azababban dukan"
Salma tasha jinin jikinta can kuma tace.
"Ammi Allah yasa ba rashin kunyar tasu suka ma wani a waje ba dan wallahi ba kowa ne ze iya jure halin ƴaƴan kiba Shiyasa kullum faɗan da nake musu kenan wannan tasa yanzu suka min ƙaura suka dena zuwa in da nake don basa son gaskiya"
Ammi tayo kan salma tana cewa.
"Kin fara wa'azin naki ko me shegen iyayi da manyan ce kamar wata uwata to ɗan uwanki ne ya saka waya ya zane su kamar jakai haka ya Mayar min da ƴaƴana wallahi ba dan cikin su ɗaya ba sena maka shi a kotu"
Salma ta kama haɓa kullum Abin Ammi ƙara gaba yake akan su safna su kaɗai ne matsalar Ammin su.
"Ammi akan Su safna zaki maka Yaya Ali a kotu? dan nasan Ya Sadiƙ baya kano tunda kika ce ɗan uwana nina san da Ya Ali kike Ammi meye yayi zafi Ammi Kin san baze dake su There is no reason ba"
Salma takai maganar cikin sanyin halin ta wanda kowa yasan ta da hakan sam bata ɗauki duniya da zafi ba.
"To bari kiji wata matsiyaciyar ƴa musa ya kawon yau kwana biyu wai marainiyace ƴar ƙanin mahaifin sa tunda yarinyar nan tazo gidannan shikenan Ya shiga takura wa ƙannen shi akan ta dan kawai safna zata shiga toilet taje tana buga mata ƙofa akan ta Miƙe ta wanke mata Shine tahau zagin mahaifin safna kin san safna da zuciya koni yaya nake da ita shine fa suka hau kokawa Sajeeda ta fita tana taya safna Wallahi Salama baki yadda ya Dinga dukan ƴaƴan nan ba kalli fa jikin su duk shatin tabon Duka"
Ta faɗa a ƙufule.
Salma taja ajiyar zuciya.
"Ammi Idan na fahimceki Musa P.a ɗin yaya shine ya kawo Maki Ƴar uwarshi amman kamar aiki zata ke Miki Ammi akwai gyara anan shin Kin bibiyi kowa acikin su kin gano me laifin ammi ɗa fa na kowa ne su yanzu su safna ba zasu iya wanke Toilet ba har se me aiki tazo ta wanke Musu kafin su shiga fisabilillahi Ammi wani ɗa namijin ne ze yarda da haka wallahi ni yanzu baban su Dady kafin ya tashi na kammala komai idan ze tafi Office da abincin sa yake tafiya kuma kinga dai ina aiki wani bin har Night duty nake amman Ban taɓa sakaci da hidimar shiba to su waɗannan idan basu saba tun yanzu ba ai ba'a san mijin da zasu aura ba Dan kawai yayan su yana da kuɗi se ya zamana komai se an musu"
Salma ta faɗa tana Hararar gefen su safna.
Ammi cikin ƙosawa da maganar salma tace.
"To idan basu ji daɗi yanzu ba se yaushe zasu ji Da wace irin wiya ce bamu sha ba ke kinga rufa min baki lokacin abu kawai ayi sa idan ya wuce ba za'a yi ba"
Salma tai dariya me ciwo.
"Ammi kenan idan watarana mune watarana ba mu bane mu dinga tina Mutuwa kada ki tafi ba fata nake ba kibar ƴaƴan nan cikin wahala yes wahala mana wallahi Koni ba zan iya Riƙon su da wannan halin nasu ba bare kuma matan Yayye waɗanda basu da tabbas Shi kan shi ya Ali ɗin wani abun ai yana sakar muku ne dan bashi da ɗan kanshi amman bara kiga ya sami matar da yake so da ɗan kanshi idan ance wani ma yayi wani iskancin baze yiba haka kwana ki shima bashir ya kirani yana masifa wai london yake son zuwa ya ƙaro karatu ya Ali yace yayi haƙuri

yaje Jami'atul madina sabida Yafi son bashir ya ƙaro Ilimi akan harkar addini sosai ke baki ga yadda ya dinga cin mutunci ba ni ai naso a gaban yayan yayi da ya ci uban shi Shiyasa naji daɗi daya hana shi fita wajan ma kwata kwata ya zauna anan ɗin yara su dinga rashin Mutunci ana ɗaure musu gindi"
Salma takai aya.
Ammi ta ɗaga mata hannu alamar tai mata shuru.
"Da kike min fatan mutuwa ko yanzu tazo ni nagode Allah Kuma da kike Maganar matan yayye ko ba wanda ze riƙen su mami Allah mata albarka zata riƙe min ƴaƴana har ma tafini basu gata zancen ƴaƴa kuma aini nafi son baba ya haihu fiye da kowa sai dai ki gyara batun wata mace ai daga kan mami babu wata mace da zata shigo gidannan Kina kallon akan waccan Filfiwar yana dukan ƙannen shi ina ga kuma ya samo wadda ya aura yake so take son shi Ina da sake ai kodan haka bama zan bari baba yayo wani aure ba haka nan ze hakuri mami ta zame masa matar ƙaddara mutu ka raba takalmin kaza"
Salma tabi Ammi da kallo.
"Ammi duka maganganun ki se naga kamar kina son kanki ta yaya zaki ce baze yi aure ba bayan da Kuɗin sa da ƙuruciyar shi Allah ya huci zuciyarki Ammi su kuma su cigaba da rashin Kunya da ɗaukar baki sun manta dukan daya taɓa min seda yaji Min targaɗe akan abin da bai ka ya kawo ba Nikam Ammi na wuce su Dady zan ɗauko a school Allah ya basu lafiya"
Salma ta faɗa tana ɗaukar handbag ɗinta tabar ɗakin.

Ammi bata iya cewa salma komai ba sabida ita indai akan su safna ne to faɗa take da kowa Bare kuma ka taɓa Mami.

Salma na fita falon suka ci karo da Hajjo dake Ɗebe kayan abincin safe wanda basu taɓa shiba tana jera na rana.
Har ƙasa salma ta zube tana gaishe da hajjo.
"A,a uwar masu gida kece a gidan namu bara na haɗa abinci"
Hajjo ta faɗa tana dariya.
Salma ma dariyar tayi.
"Wallahi Hajjo tafiya zanyi sabida su Dady suna school zan ɗauko su nima kiran ammi ne ya fito dani daga Hospital da ba abin da ze kawo ni nan sabida yara suna makaranta"
Hajjo tayi dariya.
"Allah sarki su Almustapha sarakan ƙiriniya mutanan su safana amman zasu ƙara zuwa mana hutu ko? dan naga Alhaji Ali yana son yaran nan suzo hutu yayta ɗaukar su suna fita siyayya shima dai Allah ya bashi nasa"
Salma tayi dariya.
"In sha Allah hajjo zasu zo ammi ce bata auren dasu faɗa suke amman zasu zo se anyi Hutun School, ai yaya Ali akwai son yara yakan je min jifa jifa amman ba danni ba se don su Dady Dan har yazo ya tafi ma baifi yamin magana ɗaya zuwa uku ba yana can tare dasu suna wasa kin san in yaga yara"
Hajjo tace.
"Haka ne akwai son yara kam Alhaji Ali shima Allah ya bashi"
Salma ta amsa da "Amin" kafin ta buɗe jakarta ta ɗauko dubu biyar ƴan ɗari biyar ta miƙawa

hajjo.
"Gashi hajjo kisai Goro"
Hajjo tai dariya tana cewa.
"Ke wai bakya gajiya salamatu Da sallah kimin ɗinki duk da wanda hajiya ammi da Alhaji Ali da sadik ke min kema se kinyi ki sai min ragon layya gashi har wannan shekarar zanje aikin hajji"
Sai ta soma ƙoƙarin yin kuka.
Salma tace.
"Haba Hajjo ai kome mukai miki bamu faɗi ba ai shege shike manta alkairi abin da kikai mana dan kawai kin ƙi yarda da zaman sashin nan ne kika ce Kinfi son na ƴan aiki ai ba da ban haka ba hajjo da ba zaki dinga komai agidannan ba makka ba dan kirata bace ai da ba zakije yanzu ba da tuni kin manta da zuwa"
Salma ta faɗa.
Hajjo tace.
"Allah ya saka muku da alkairi yadda kuka riƙeni Allah ya duba ku ya ƙara muku wadata"
Salma tace "Amin hajjo ina ɗakin ƙanwar Musa?"
Hajjo tace "Muje ciki gashi can"
Suka jera zuwa ɗakin da Farha take ciki tare da Hajjo........
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 35*

Salma ce a gaba sabida haka ita ta soma buɗe ƙofar ta shiga kwance ta hango yarinyar sai shashsheƙar! kuka! take ta dunƙule jikin ta waje ɗaya acan ƙarshen gado.
Gyara Murya salma tayi tare da cewa.
"Assalamu Alaiki"
Farha ta ɗago da ƙyar tana kallon meyin sallamar wadda sam bata ji shigowarta ba sai sallamarta kallo ɗaya tayi mata ta kauda kai kamar su har tayi yawa dashi daga gani babu tambaya itama ƙanwar shice.
Da murmushi a saman fuskar salma ta ƙarasa bakin gadon ta zauna.
Hajjo kuma ta tsaya a gaban madubi Fuskarta cike da tausayin farha take ta faman jera mata sannu.
"Zaki iya tashi? naga fuskarki duk ta haye ta suntume"
Cewar salma cikin kulawa.
A hankali Farha ta saka hannunta a saman gadon ta dafa shi tana Ƙoƙarin tashi sabida gaba ɗaya jikinta ciwo yake mata.
Hajjo tazo da sauri ta taimaka mata suka miƙe.
"Hajjo muje Ki samin ita a mota sauri nake so dole zan ɗan dubata idan yaso zan sanya driver ya maido da ita Ki shaidawa Ammi"
Hajjo tasan salma dama akwai ta da tausayi.
"Allah yayi miki albarka yadda kika taimaki marainiyar Allah kema Allah ya taimake ki"
Da taimakon Hajjo ta saka hajib ta riƙo ta ajikinta har parking space salma ta sanya ta a mota tana ƙara jadda dama Hajjo akan ta sanar da Ammi A back seat farha ta kwanta salma ta shiga

driver seat ta zauna ta tayar da Motar suka bar Gidan.

Hajjo cike da bin umarni ta isa ɗakin Ammi bata ciki sai ta shiga ɗakin Ƴammatan wanda ta tarar da Ammi zaune tayi tagumi ta zuba musu ido duk suna kwance kamar zata Shiga Jikinsu sabida kusanci.
"Sannu da hutawa Hajiya Ammi"
Hajjo ta faɗa tana Zama a saman carpet Ɗin Ɗakin

"Yawwa Hajjo salma ta tafi? ga ruwan data sama safna ya ƙare amman tunda ta nuna Min bara na cire"
Hajjo ta kama haɓa cike da al'ajabin langwan ƴaƴan na Ammi kafin tace.
"Wato abin har yakai ga ƙarin ruwa ikon Allah shiyasa yadda na jera abinci haka nazo na kwashe se masu gadi na bawa"
Ammi da take Cirewa Safna allurar Ruwan da aka saka mata tace.
"Hajjo waya ke ta wani abinci ni ai banda kwanciyar hankali har se naga yarana sun dawo yadda suke Kinsan Allah jiri nake ji da ƙyar idan Jinina bai hau ba Yau Baba ya ɓata min rai na ba ɗan kaɗan ba"
Hajjo tayi saurin tare ta tare da cewa.
"Kuma karki sake ki masa baki akan Abin da bai kai ya komo ba dan ke uwa ce"
Ammi dai bata ce komai ba Hajjo ta kuma cewa.
"Dama Uwar masu gida ce tace na shaida Miki ta wuce da ƙanwar Musa zata duba ta dan sunji mata rauni itama amman zata sa driver ya maido miki da ita"
A hasale Ammi ta juyo tana cewa.
"To ina ruwana da ita ni dama daga wannan fitar kada ta dawo Min gidana tsinanniya mai baƙar fuska Tauraruwa mai witsiya ganinta ai baya da alkairi a tare dani"
Aran hajjo tace da yake an taɓa ƴaƴan gwal amman a fili se tace
"Hajiya Ammi shifa ɗa na kowa ne da ɗa da dukiya baka musu Mugunta ki sassautawa marainiyar Allah a ƙa'ida daga ita har Safana basu kyau ta ba duk sun zagi iyayen su"
Ammi ta ɗaga wa Hajjo Hannu tare da cewa.
"Ke kinga sanda akai hakan har da zaki zo kina Faɗin yadda akai da Allah tashi Kije kawai maganar nan ɓata mini raina take"
Hajjo ta kama Haɓa cikin mamakin halin Ammi akan ƴaƴanta.
"To Hajiya Ammi ki haƙuri nayi ba daidai ba meza a dafawa Hajiya ƙaramar Naji kince yau zata dawo"
Bata ko kalli saitin Hajjo ba tace.
"Koma meye ni bata tata nake ba yanzu ta yarana nake"
Adaidai nan sajeeda ta farka tana Jan Numfashi da sauri Ammi tace.
"Hajjo bani ruwan sanyi da ɗan tsumma har yanzu da zafin zazzaɓin a tare da ita"
Hajjo da sauri ta shiga toilet Ɗin su Kaca kaca toilet ɗin ba alamar an wanke ita dai taro ruwan tayi ta kawowa Ammi tare da tsumma fari mai kyau.
Hajjo ce ta taimaka mata ta tubewa Sajeeda riga ta dinga goga mata ruwan sanyin ita kuma sajeedar ta kwantar da kanta a kafaɗar Hajjo tana hawaye.
"Jiba fa hajjo kalla shatin waya har wuyanta kai gaskiya Baba ya cuceni"

Ammi ta faɗa kamar zatayi kuka.
Tana gama gogewa sajeeda Jikinta a hankali ta mayar mata da rigar Jikinta Muryar sajeeda a hankali tace

"Hajjo zan sha tea"

A hankali ta faɗa tana komar da kanta saman pillow ta kwantar Hajjo ta miƙe ta fita dan ta haɗo mata shayin a ranta tana cewa yau fa ba sauƙi an taɓo Kitse a saka ka a rana ka narke a barka a inuwa ka daskare.

Hajjo ta haɗo shayin mai kauri ta kawo mata kurɓa ɗaya tayi tace bata sha agigice Ammi tace "Me kike so a dafa Miki ko asaka driver ya siyo Miki?"
Sajeeda ta girgiza kai alamar bata Buƙatar Komai daga Hajjo har Ammi sannu sukai mata ta koma ta kwanta Safna ma Buɗe ido tayi wanda Ammi ta mayar da kallo kanta tana cewa "Sannu meke miki ciwo yanzu"
Ɓare baki tayi kamar wata yarinyar Goye.
"Ammi ina ga ya karya min hannuna nauyi yake min wayyo Ammina"
Ammi tayi kan safna tana duba hannun ita dai hajjo kama haɓa tai yau tana kallon Ikon Allah safna fatan dankali ta buƙata hajjo ta kawo mata a wulaƙance tasha kaɗan ta ture.

Ammi ta dubi hajjo ido jajir.
"Hajjo jeki ɗakina saman madubi na akwai maganin hawan Jinina ki ɗauko Mini jiri nake ji"
Hajjo ta dubi ammi.
"Haba Hajiya Ammi akan wannan ɗan abu zaki ɗagawa kanki hankali har Jinin ki ya hau Idan Alhaji Ali be dake suba waye ze dake su kada fa ki bada gudunmawa wajan sangarta ƴaƴan ki"
Ammi ta ɗago ido tace wa hajjo

"Ai idan ƴaƴana basu kasheni ba ke kya kasheni da waɗannan maganganun naki zaki ɗebo min kona tashi da kaina"
Hajjo ta Miƙe ta nufi ɗakin Ammi ta kwaso mata magungunan wanda dama tana da hawan Jinin tun bayan rasuwar Baban su Aliyu ta kamu dashi sedai bai fiye tasiri ba sabida tana shan magani Kuma duk ƙarshen wata Aliyu na fita da ita waje ganin Likita waɗannan ƴan watanni nema basu fitan ba sabida tace ita taji daɗin Jikinta ya rabu da ita.

Hajjo ta kawo mata haɗe da ruwan roba ta karɓa ta sha ta kwanta a kusa da ƴaƴanta waɗanda suka sanyata a tsakiyar su.

Hajjo fita tayi ta rufo Musu Ƙofa wato ɗan adam tara yake be cika Goma ba duk yadda Ammi take da Kirki akan ƴaƴanta idanunta rufe wa yake Musamman waɗannan sarakan Guda Biyu basu da mutunci ko kaɗan Kuma baka isa kayi magana akan su ba.
Hajjo ta watsar da tunanin ta Koma kitchen tana cigaba da gyara kajin da zata ma Mami farfesu dan taji ance yau zata dawo.

Bayan fitar Hajjo sajeeda ta Miƙe ta shiga wanka Ammi ta juya tana kallonta "Zaki iya kona zo na taimaka miki?" ta girgiza kai ta shige toilet ɗin ta fito tana Yamutsa fuska "Ammi ba a wanke yake ba toilet Ɗin" Ammi taja tsaki "Ai salma ce da neman suna ta ɗauketa suka tafi Gidanta bada ban haka ba da ba seta zo ta wanke Muku ba" Abin mamaki ammi da kanta ta shiga Toilet ɗin ta hau wanke wa Sajeeda tana tsaye akanta harta gama juyowar da zatai santsi ya kama ƙafarta takwa faɗi tum sajeeda ta ƙwala ƙara tayi kanta tana Ƙoƙarin ɗagata.

Hajjo da gudu data juyo Ihun tayo ɗakin ganin Halin da Ammi ke ciki ya ɗaga mata hankali tana kwance Cikin Kumfar banɗaki da taimakon Hajjo Suka fito da Ammi wadda har ƙafarta ta haye tai sumtum abun ka da farar fata.

"Garin yaya Hajiya ammi Allah ya sawaƙe"

Cewar Hajjo sajeeda tace "Wai Toilet ta shiga ta wanke min zanyi wanka shine fa ta Faɗi"

Ammi ta matse fuska saboda yadda ƙafar ke mata zafi.

"Hajjo ɗauko Min man zafi a ɗakina"

Hajjo ta fita ta ɗauko mata man zafin ta kawo mata.........

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 36*

Hajjo ta rissuna har ƙasa ta miƙawa Ammi man zafin.

Ammi ta rintse ido sabida yadda ƙafar ke mata azababban zafi.

Muryar ta abin tausayi tace wa Hajjo.

"Shafa min daga saman Yatsuna"

Hajjo ta lakato man zafin ta soma goga mata a yatsun ƙafafun nata waɗanda duk sun haye sunyi suntum Hajjo se faman sannu take jerawa Ammi Ita ko Sajeeda wankan ta tashiga ta fito ta zauna gaban madubi ta shafa mai ta zira riga ta kwanta hajjo ta bita da kallo Ammi kwanciya ta kuma yi nan da nan zazzaɓi ya rufeta ruf Hajjo ta baro ɗakin ta wuce kitchen ta cigaba da aikin dake gabanta.

Tunda suka hau kwalta salma ke sharara gudu har ta ƙarasa unguwar sharaɗa Sai da ta biya ta ɗauko Yaƴanta a school sannan suka wuce gidanta Haɗaɗɗan ƙaton gida mai Jan gate tai horn mai gadi yazo ya buɗe mata gate ɗin ta tura hancin Motar ta ciki ta shiga tai parking.

Yaranta farare masu kama da ita suka fito daga gefenta suka tsaya salma ta zaga can back seat inda Farha ke kwance ta buɗe tace mata.

"Ki sauko a hankali mun iso"

Farha ta yunƙura a hankali ta sauko daga cikin motar yaran suka bita da kallo salma ta kama hannunta suka miƙi wata hanya wadda ta kaisu Ƙofar Ƙaton Falon sanyi da ƙamshi ne sukai wa farha sallama a cikin hancinta ta lumshe ido ta nemi guri ta zauna Mai aikin Salma nata zirga zirga daga kitchen zuwa dining wadda ke girki iya na rana sabida yaran salma dake makaranta da sun dawo suci sai wanke wanke da shara amman sauran Hidimar girkin mai gida da gyaran ɗakuna duka salma ke yin kayanta bata yarda mai aikin tata tayi mata ba.

"Maman Dady sannu da zuwa yaya aiki?"
Mai aikin salma ta faɗa mata hakan bayan ta ƙaraso wajan
Salma ta dube ta da kulawa.
"Lafiya lau zuwaira yaya hidimar Gida?"
Zuwaira mai aikin Salma tace.
"Lafiya lau"
Tana kama hannun yaran suka nufi hanyar ɗakin su.
Salma ta dubi farha data zauna a ƙasan carpet tace mata.
"Taso muje ciki bakya zauna anan ke kaɗai ba"
Ta miƙe suka jera zuwa cikin wani ɗaki wanda ƙaramin gado ne acikin sa sai Toilet da carpet shinfiɗe a ƙasan sa.
"Ki zauna anan bari nayi wanka na fito"
Farha ta jinjina kanta Bayan ta zauna a ƙasan carpet ɗin kanta ne ke mata wani irin ciwo har ganin ta na neman juyewa.
Sama sama taji muryar salma akan tana ce mata.
"Me zakici na kawo miki seki sha magani ki kwanta ki huta"
Ta ɗago tana share hawayen ta.
"Dan Allah maman dady ki bani kuɗin mota na tafi gida"
Ta faɗa kamar yadda taji mai aikin nata ta faɗi sunan nata.
Neman gefen gado salma tayi ta zauna ta dubi farha wadda take kuka.
"To yanzu idan na baki kuɗin mota kin san hanyar garin ku?"
Da sauri ta ɗaga kanta tana cewa.
"Na sani maman dady dan Allah ki taimaka mini"
Salma tayi jim kafin tace

"To Amman shi musa daya kawo ki idan har yaji bakya wajan Ammi ai ranshi ze ɓaci"
Kukan farha ta cigaba dayi tana cewa.
"Baze ce komai ba daman nina jawa kaina Nace masa ina son aikatau to tunda abin ya zama haka gwara na koma gida"
Farha ta faɗa har lokacin kuka take

"Ina ne garin naku ni sai na saka driver na ya kaiki amman baze yuwu a sakeki ke kaɗai ki tafi ba sabida hakan ze zama matsala babba"
Gaban farha ya faɗi ita anya ma suna da ƙauye kuwa ita dai a tarihin ta bata taɓa jin kawu ko umma sunce zasu ƙauye ba duk ƴan uwansu suna cikin gari.
Ƙifta ido tai tana inda inda.
Fahimtar Hakan yasa salma cewa.
"Kinga hakan bamai yuwu wa bane tunda naga kamar kanki be waye da hanya ba, Zan kira yaya se ya turo min da number musa sena kira shi yazo nan ya tafi dake"
Gaban farha ya kuma faɗuwa tasan idan har ta gaya masa baze bari ta barta ta tafi ba.
"Maman dady zan fa gane kedai ki taimaka min na tafi ko ma baki bani kuɗi ba ki barni na fita zan san yadda zanyi har naje gida"
Salma ta miƙe ta fita daga ɗakin  batare data yi magana ba.

Bedroom ɗinta taje ta ɗauko wayarta Numbern Aliyu ta shiga kira sedai taƙi shiga sai da ta fito daga ɗakin sannan Number ɗin ta shiga taita ringing bai ɗauka ba.

Haka ta dawo ɗakin da farha take zaune.
Ta ɗaga murya ta kira zuwaira.
Da sauri zuwaira ta ƙaraso.
"Maman Dady kira kike gani"
Salma ta dubi zuwaira

"Dan Allah zuwaira ki haɗo wa wannan baƙuwar tea mai kauri da ɗan Abu marar nauyi, sannan ki bawa su dady abinci su tafi islamiyya"
Zuwaira da ladabi ta amsa kana ta fita daga ɗakin

Minti kaɗan ta dawo ɗakin da ƙaton tray a hannun ta ajewa tayi a gaban farha salma ta dubi farha

"Ci abincin amman ki fara shan tea ɗin kafin kici abincin sabida ya warware miki hanjin cikin ki"
Farha ta ɗaga Cup ɗin tea ɗin ta sanya spoon tana juyawa ta ɗaga shi tana kurɓa kamar maɗaci take jin bakin ta dan kwata kwata babu ɗanɗano ta kurɓi ɗaya biyu uku sai amai ya biyo baya awajan ta dinga kwara amai tana riƙe ciki salma nata jera mata sannu anan wajan ta kwanta tana numfashi salma ta gyara wajan ta taimaka mata suka je toilet ta wanke mata Jikinta saman gadon salma tace tahau jikinta se rawa yake zazzaɓi ne ya rufe ta ganin ta galabaita da yawa yasa salma ta shiga ɗaki ta ɗauko allura da drip ta tsira acikin drip ɗin ta haɗa ta saka mata Allurar harda ta bacci aciki salma ta rufe mata jikinta da bargo bayan bacci ya ɗauke ta taja mata ƙofar tabar ɗakin.

Se wajan la'asar ruwan ya ƙare salma ta cire mata har lokacin Bacci take Bini bini salma zata leƙa amman har aka kira Magariba bata tashi ba salma na idar da sallar magariba taga kiran Aliyu.
Ta ɗaga cikin ladabi tayi sallama tana gaishe dashi.
Cikin taushin muryashi yace wa salma.
"I'm sorry salma naga kiran ki, But kin san kan ƴan mazan a wajan nema ɗaukar zafi yake hope kuna lafiya yaya su Babana?"
Salma tayi murmushi.
"Lah dama nayi zaton haka Yaya Suna lafiya Allah ya taimaka, dan Allah yaya numbern musa zaka tura mini in ba damuwa"
Batare da tunanin komai ba dama shi bai da yawan bincike akan lamarin wani ko ya saka idanu akan Harkar da ba'a saka shi acikin taba.
Yace mata.
"Okey ba matsala amman yanzu haka na fito daga masallaci zan je gida zuwa anjima zan tura maki"
Salma tai saurin cewa.

"Yaya ko kawai bara kaji maganar wannan ƙanwar tashi ce"
Da rashin gane inda ta dosa yace mata.
"Wa kike nufi kenan?"..............
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

Ya matsa kusa da farha kaɗan yaɗan ja bargon ya ɗora hannun shi a saman goshinta babu zafi a goshin nata.
Buɗe Idanunta tayi wanda har Lokacin bai ɗauke hannun shi a goshin nata ba.
Gabanta ya faɗi ta mayar da idanun ta Lumshe.
"Sannu"
Ya faɗa a hankali.
Ta yunƙura zata tashi jiri ya ɗebe ta, ta koma ta kwanta tana jan numfashi hannu ya sanya ya ɗagota ya jinginar da ita ajikin Bango idanunta har Lokacin a rufe yake.
"Kin yi sallah me zaki ci?"
Duka ya jefa mata tambayoyin.
Banza tayi masa dan yanzu bata son magana mai tsaho ta dinga haɗasu sabida ta fahimci ya iya danƙara baƙar magana.
"Wai ke kurma ce ina miki magana kin min banza"
Ya faɗa a hasale.
Adaidai nan salma ta shigo.
"Afuwan yaya ina hidimar babansu ne, yawwa Kin tashi ki ƙoƙari kiyo alwala ki sallah se kici abinci Yaya ina zuwa dan Allah ina haɗawa Baban su abinci ne"
Bai mata magana ba ta fita farha ta miƙe ƙafafunta ta dafa bango ta yunƙura ta shiga toilet ya bita da kallo wato yau ba bakin tsiwa tana rashin lafiya.
Tayo alwalar ta fito juya ta kuma ɗibarta zata faɗi da sauri ya miƙe ya tarota jikinsa kwanciya tayi a saman Ƙirjinsa tana jan numfashi ya kamata har zuwa Tsakiyar ɗakin zamewa tayi daga jikinsa ta zauna a ƙasan carpet tana zubo hawaye.

Ya miƙo mata hijab ɗinta.
"In ba zaki iya tashi ba kiyi sallar a zaune mana"
Ya faɗa mata cikin kulawa.
Ta amshi Hijabin ta saka ajikinta a zaune tayi sallar tana idarwa yace mata

"To me zakici Mu wuce gida"

Kuka ta saka tana rufe fuskarta.
"Ni ka barni anan gidan ni bazan koma gidan kuba"
Shi dariya ma abin ya bashi Ya jingina da bango yana tsaye akanta yana kallonta.

"To anan zaki ta zama bakya ganin itama gidan mijin tane nan waya gaya miki ana gudun Gidan Miji?"
Ya faɗa can ƙasan maƙoshin sa.
"Ni na haƙura da auren ai dama nice na ce ina son ka"
Da sauri yace.
"Yan zufa?"
Tana kuka tace masa.
"Na dena son naka na haƙura koka kaini gida koka barni anan amman na haƙura dakai"
Aliyu dariya yayi sosai har da riƙe ciki.
"Oh fatima kenan danja wutar baya, Ai ƙarya kike kice bakya sona duk bakin daya furta so yazo yace Ƙi to ɓacin rai ne Ni ɗindai ne bana son ki tunda ke kinji kin gani kina sona a haka seki ta haƙuri dani"
Kukan ta ya ƙara ƙarfi fiye dana da.
"To nima nace bana son ka ko ana so dole ne
Ta faɗa tana cigaba da kukan....

Arewabook autarmanya
Paidbook 500 naira into 0078174806 sterling bank evidance of payment 09022260850

https://www.arewabooks.com/chapter?id=6509e2f03057a0e54cceafe1

*RABO YA RANTSE 38*

Aliyu da ranshi ya ɓaci na jiran data saka yake mata ya ɗago yana hangota tana tawowa tsaki yaja ya kunna motar ya buɗe mata kusa dashi harta ƙaraso kuka take kanta a sunkuye da ledar da salma ta bata a hannunta

Zama tayi taja murfin motar ta ɗora kanta a saman cinyarta se kuka take Aliyu ya kunna Motar suka bar Gidan.
Duk yadda ƙarfin radio ya cika motar Hakan be saka yaji sautin kukanta ya ragu ba tsaki yaja a karo na barkatai sam ya tsani kuka a rayuwar shi yaɗan rage speed ɗin motar ya juyo yana kallonta hannun shi riƙe da sitiyarin Motar.
"Wai ke wace irin mutum ce kita wahalar da kanki da koke koke wanda nida ban sanshi dake ba amman yanzu kin koye shi kullum idanun ki cikin kuka me yasa hakan?"

Shuru tayi masa wanda ya ƙara fusata shi aguje yaja motar bai kuma sake yi mata magana ba sai faman Huci yake ta fahimci shurun data masa ne ya fusata shi hakan yayi mata daɗi har ranta ..........
Arewabooks autarmanya
Paidbook 500 naira in to 0078174806 sterling bank evidance of payment 09022260850

https://www.arewabooks.com/chapter?id=650af5e90d776a5748dfe4b4
*A LOVE STORY 39*

Da sauri ta ɗago idanunta ta kalle shi wanda shima ya zuba mata nasa idanun gaba ɗaya sunƙi ɗauke idanun su akan na junan su kuma kowa akwai tunanin da yake saƙawa acikin zuciyar shi A hankali ta zare idanunta daga cikin nashi wanda shi kuma har tallafe fuska yayi yana kallonta kamar ya sami tv ga kuma hannunta daya damƙe mata wanda har ya fara mata zafi sabida riƙon tsauri yayi mata.
A hankali sautin Muryar shi yake fita inda yake ce mata.
"Tell me what he said to you that bothers you in your heart?" ya faɗa cikin ƙaramin sauti mai kama da yana mata raɗa.
Kanta ta kawar sabida kusancin su yayi yawa sosai.
Ta sanya hannu tana share hawayen ta.
Ƙasa ƙasa ya kuma ce mata.
"Tunda ba zaki gaya min ba shikenan, Amman wannan kukan ina son ki rage shi koda baki dena ba sabida wani idan ya gani se yace min ina cutar dake kuma nina san ban maki komai ba Ɓata min raina ma da kikai wanda shine dalilin aure na dake bai saka na cutar dake ba"
Ya faɗa with full Confidence, zuba masa ido tayi san kan shi yayi yawa kafin a hankali tace.
"Shi ai laifi tudu ne, Meye dan kaso kanka cuta kuma tana wa nidai na bar mutum da Allah yana madakata yana kallon kowa"
Bakinta ya kama da hannunshi ya matse wanda har hakan yasa ta saki Ƙara yaja leɓanta na ƙasa da ƙarfi.
"Ko kaɗan fatima baki da kunya wannan bakin zan koya masa hankali, shike nan dai koma me zaki ce ki ce I have no problem with that, tunda dai Allah ne me sheda duk haƙƙin ki ina ƙoƙari wurin sauke shi, Har ɗaki na kawo maki abinci amman dan baki da kirki baki taɓa ba yanzu Baki da lafiya na bibiyeki akan mai zakici nan ma ban isa kin gaya min ba, In ma dan kwanan kine bana baki hakkin ki tanan so mamy ce bata nan yau amman ta dawo daga yau zan raba ma ko wacce nata kwanan there is no problem"
Ya faɗa har lokacin riƙe yake da ƙasan leɓanta.
Ture masa hannu tayi da nata hannun ta zumɓura baki gaba

"Kai ne kake tunanin wannan Ni kam na barwa matarka har abada bana buƙatar kwana da ko wani gardi a ɗakina duk da tsoron da nake ji amman na yafe nida nazo zaman wucin gadi wallahi ina samun hanya sedai ka buɗe ido kaga wayam"

Murmushi ya sauke.

"Fatima nine gardin kenan?"
Ya faɗa yana zuba mata ido.
"Oho ma wanda ya tsargu dashi nake"
Ta faɗa tana hararar shi Murmushi ya kuma saki wato yarinyar ba zatai laushi ba rashin kunya a jinin ta yake Ko babba yana shakkar kallon idanun shi ya faɗi magana amman ita hankali kwance lafiyar Allah take maganarta babu alamar tsoro a tare da ita.

"Shikenan tunda kince haka idan ke kin yafe ni ban yafe ba kuma ki fara lissafi tabbas zanzo ɗakin ki kuma zan baki mamaki wannan rashin Kunyar taki sekin yi nadamar yinta"
Ya faɗa yana ficewa daga motar.

Ita mamaki ma ya bata tasan kawai zance ne ta yaya ze iya zuwa wajanta ya kwana yabar matarshi bayan kuma babu wanda yasan shi Mijinta ne da alama har mahaifiyar shi bata sani ba ta fahimci yana shakkar mahaifiyar shi yana gudun ɓacin ranta sosai taɓe baki tayi kome yasa baya son asan ita matar shice oho ko me yasa ya nemi ya ɓoye auren shi da ita Murmushi tayi ganin yadda ya zuba mata idanu ɗazu kamar tsohon maye Shuru da ɗaure Fuska yana masa kyau sedai ta kula baya son rashin kunyar da take masa ita kuma da ita take ɓata masa rai sannan kuma ta lura bamai yawan son magana bane da alamun ma ita ɗin ma da ƙyar yake mata maganar.

Lumshe idanu tayi tana shaƙar Kamshin turaren daya bar mata a cikin Motar Allah ya sani tana son wannan bawa nashi ita kanta har mamakin son da take mashi take yi ta zaɓi tana ƙuntata masa ne ta hanyar yi mai rashin Kunya dan ta dinga saka shi magana Kuma duk abin da yay mata bata riƙe shi aranta ba sabida soyayyar shi data makantar da ita tabbas so ɗaya tak tana ma bawan Allah.

"When you finish thinking about me, come out, I'm waiting for you" taji yo muryar shi ya leƙo da kanshi cikin motar dama tasan baze iya tafiya ya barta ba sabida yana tunanin kada ta gudu.
Da sauri ya ɗaga kanshi daga cikin Motar ita kuma ta buɗe murfin ta fito tana ƙunƙuni.
"Nifa ba tunanin ka nake ba ehe ina tuna salim ne bawan Allah me zuciyar zinare yana can ko yana wani hali oho"
Har yayi gaba ya juyo ya saki murmushin daya kassara zuciyarta Kafin yaɗan ranƙwafo Gefen Kunnenta a hankali ya raɗa mata.

"Daɗi na dake shashanci in ban da ke sakarai ce, ai ba shi zaki tunani ba iyayen ki zaki tuna da kika bijirema umarnin su sabida haka Think of a situation your parents were in before, sannan kuma ni ba ruwana in kina tunanin wani da aure na akanki ALLAH YA ISA"
Daga haka yayi tafiyar shi ya barta a dashe a wajan Ta faɗi maganar dan ta ƙuntata masa sabida tasan ko wani namiji yana da kishi.
To gashi Kilu taja bau ita bata saka masa takaici ba shiya gasa mata magana mai zafin gaske daga ƙarshe ya bita da Allah ya isa, kai wannan bawa yana da abubuwa na bam mamaki idan ya danƙaro maka magana sai ka rantse Goyon gwauro ne wanda Namiji ya raine shi ba mace ba ya iya baƙar magana wadda zata sanyaka kaji takaici kaji damuwa kaji baƙin ciki lallai matar

shi tana haƙuri dashi.
Haka taja ƙafafunta da suka mata nauyi tabi bayan shi Tuni ya ɓacewa ganinta sabida yana da sauri sosai bata cimmasa ba se a ƙofar Falon yana ƙoƙarin Buɗewa ya shiga cikin falon Ammi..........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 40*

Fuskar shi ta saci kalla yadda taga ya haɗe rai kamar bai taɓa dariya ba gabanta har faɗuwa yayi sosai ya ɗaure fuska ko kallonta kuma beyi ba taga ya buɗe ƙofar ya shiga cikin Falon take masa baya tayi tabi shi ciki Tsayawa tayi daga nesa tana hangen cikin falon wanda shikuma zuwa lokacin Ya riga da shiga ciki har ya zauna.

Jikinta a sanyaye take taka ƙafafunta harta ƙarasa cikin falon kanta a ƙasa batare data kalli mutanan dake zaune a falon ba ta wuce cikin ɗakin ta sum sum.

Aliyu ya kalli Ammi wadda ta ɗora ƙafarta a saman center table Hajjo tana danna mata da ruwan ɗumi.
"Ammi meya sami ƙafafun naki kuma?"
Ya faɗa mata cikin kulawa, Bata kalli inda yake ba ta kauda kanta Hajjo tayi dariya tare da cewa.
"Haba hajiya Ammi Uban ɗakina bai cancanci kiyi fushi dashi ba tunda bashi yakar zomon ba"
Ammi ta ɗagawa Hajjo hannu tana ɗauke ƙafarta Hajjo ta Ɗauki ruwan ɗumin tabar falon, Aliyu ya kuma matsowa gabanta jikin shi duk yayi sanyi murya ya kuma rage wa cikin sanyin jiki yace.
"Ammi badai fushi kike yi dani ba Allah ya baki haƙuri dan Allah ki yafe min ba danni ba"
Ammi dataji zuciyarta tayi sanyi na yadda taga yayi ɗin seta dube shi.

"Daga ina kake da alamun wannan yarinyar tare Kuke, Baba kada ka yaudare ni Ko son yarinyar nan kake nasan halin ka kamar yunwar Cikina"
Shafa kanshi yayi Batare da nuna wani tsoro Ko furgici a maganar ta Ammi ba yace.

"Ammi me kike faɗa haka? nikam ko yarinyar ma da kike magana akanta ban gama gano taba" ya faɗa lokacin da yake Ɗora hannunshi a ƙafar tata yaja yatsan wanda Ammi ta sanya ƙara tana rintse Idanu kawar da maganar yayi yana cewa

"Ammi wai garin yaya ne kika ji ciwo haka?"
Ta yarfe zufar data karyo mata tana kallon shi kafin tace.
"Tsautsayi ne wannan yarinyar bata wanke wa su auta toilet ba to ka gama jibgarsu duk ka jigata min yarana shine ni da kaina naje na wanke Musu harfa na gama ƙaddara Kumfa ta kwashe ni shine na faɗi kaga dai yadda ƙafa ta haye tayi sumtum"
Ammi ta faɗa a zatonta ze ƙara ganin laifin farha yace a sanadin ta mahaifiyar shi ta faɗi ga mamakin Ammi se jin muryar shi tayi yana cewa.

"Sajida safna ku zo nan dan ubanku"

Ya faɗa da ƙarfi kuma babu wasa acikin idanun shi.

Sum sum suka fito daga cikin ɗakin su sabida wunin yau suna ɗaki a kwance Suna ta wa ammi sangarta kala kala batare dasun tausaya mata akan halin da take ciki ba suka zube a gaban sa suna gaishe dashi.
Kawunan su ya haɗe waje ɗaya ya gwara ya sanya ƙafa ya taɗe su a gabansa suka faɗi suna kuka har goshin su ya fashe"Baba meye haka so kake ka kashe min su wai me yarannan sukai maka yau tunda ka tashi kake cin zalin ƴaƴana kada ka bari na maka baki akan su fa"
Ta faɗa tana ƙoƙarin tashi amman ƙafarta tai mata nauyi sabida targaɗan data ji a yatsanta na ƙafa.

Ba tare daya bi takan maganar da Ammi take mishi ba ya miƙe tsaye ya zaro wata ƙatuwar baƙar waya naɗe ta yayi ya shiga lafta musu a gadon bayan su ba ji ba gani Ihu suke suna kiran "Yaya ba zamu sake ba yaya kayi mana afuwa mun tuba wayyo ammi zamu mutu" wannan ihu shiya fito da Farha daga ɗakinta tsorata tayi ganin yadda yake Jibgar su kamar Allah ya aiko shi da sauri Bashir dake shigowa falon ya ƙaraso wajan Aliyu yana Ƙoƙarin riƙe wayar hannun nashi Aliyu ya tankaɗa Bashir ze zuba masa wayar Bashir yayi tsalle yayi gefe yana yarfe hannu dan har ta same shi.

Sai da yaga sun kasa tashi sannan ya yarda wayar yana huci.
"Dan ubanku daga yau idan kuka sake barin ammi tayi muku wankin banɗaki sena karya ku daku saka mata ciwon ɓarin Jiki gwara na karya ku na watsar ai ba ku kaɗai ta haifa ba duk kuma abin da kuke a gidannan na sani tara ku nake, bakwa ganin mutuncin kowa har wasu na tunanin duk haka muke daga yau na dakatar da Hajjo kune zaku dinga girki na dakatar da mai gyaran falo kune zaku dinga gyarawa in na kamaku da saɓa dukkan sharuɗai na wallahi tallahi"
Ya matsa yatsun sa suka bada sautin ƙass da ƙarfi yayi ƙwafa yabar falon fuww kamar kububuwa.

Bashir da shigowar shi kenan Garin ya wuce daga wajan shima Ɓangaran shi ya nufa wanda yake Kusa da falon Ammi ya aje jakar shi ya shiga wanka batare daya bi takan abin da ya gani ba dan yasan ba mamaki laifi su safna sukai wa Ya Ali, wanda shi kam tsoro ya hanashi magana.

Ammi tallafe kumatu tayi tana jin zuciyarta na mata zafi bada ban kukan uwa bala'i bane ga ɗanta yau dase tayi kuka harta godewa Allah da sauri ta isa gabansu tana ƙoƙarin janyo su jikinta "Ni Ammi kada ki taɓani ai kina kallo yana dukan mu amman baki magana ba kamar tsoron shi kike ji" cewar safna babu wata tarbiya acikin maganar tata Ammi jada baya tayi sabida yanayin safna daya bata tsoro se kuka suke kamar ransu ze fita kafin su Miƙe suna jan ƙafafu sukai cikin ɗakunansu.

Farha da hawayen tsoro ya gama jiƙa mata fuska taja ƙofarta zata koma sabida tuni wani tsoron Aliyu ya cika mata cikinta wannan duka ai idan ita yayi wa shi kawai tata ta ƙare Mutuwa zata yi.

"Zonan munafukar Allah"
Taji yo muryar Ammi wadda take kallonta Jikinta yana rawa ta nufi gaban Ammi ta tsugunna.

Ammi ta dube ta.
"Da ina cikin kwanciyar hankalina baba baya shiga harkar ƙannen shi amman daga zuwan ki zaki raba min kan ƴaƴana munafuka bakar kadara wallahi bana ƙaunar ki mai baƙar fuska da muni kamar daran mutuwa idan ba da ban ta dalilin ki ba ta yaya duk haka zata faru Kuma ki buɗe Kunne da kyau Kijini ba Musa ne ya kawoki gidannan ba Ni ko uban musa ne ba ruwana akan ƴaƴana wallahi ko shi Musan zan iya ɓatawa dashi wannan duk wahalar da baba ya lissafa kece zaki Yi ba su ba kuma da kuturin Munafurci inji kin gaya masa wallahi sena karya ki na watsar dake Yaƴana ba kalar wahala bane ba abun da zasu yi kece zaki komai munafuka"
Farha dai se kuka take ta kasa  magana tunda take bata taɓa ganin Mutum wanda ya tsaneta ta farar ɗaya kamar Ammi ba.

"Tashi ki bani waje Munafuka".
Ammi ta faɗa tana saka ƙafa ta ture Farha wadda ta hantsila ta Kifa Har hancinta na fashewa Kuka ta saka mai ƙarfi ta Miƙe ta Nufi hanyar fita daga falon aguje duk tunanin ta ya gushe tama mance hanyar ɗakinta wanda adaidai nan Kuma Bashir ya turo ƙofar ya shigo Karaf suka ci karo da Farha wadda tai taga taga ta faɗa saman Ƙirjin bashir da sauri Shikuma ya tarota Jikinsa ya saka hannun shi ya damƙo Ƙugunta ya riƙe gam........*RABO YA RANTSE! Iittafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 41*

Bashir shagala yayi da kallon Farha tunda yake bai taɓa ganin Macen data fusgi hankalin shi irin taba fatar Jikinta laushi Kuguntа cikakke ya cika masa tafin Hannun shi Bashir wanda idanun shi suke a buɗe tar a harkar mata yaga fara yaga baƙa mayen mata ne Duk samun sa a gindin mata yake tafiya indai mace zata bashi Jikinta shi kuma ze mora mata komai take so kuma ze mata Gogagge ne akan mata ya ƙware sosai a fannin neman mata wanda tun yana yi a ɓoye har Maganar tazo kunnen Aliyu da Sadiƙ sedai duk yadda suka so su fahimtar da Ammi abun yaci tura domin taƙi yarda da maganar tace ƙarya suke masa Wanda suka faɗa ma sharri ne sedai inda Ammi zata saka idanu akan Bashir shine abin da zata fara fahimta ina yake kai Kuɗin sa Aliyu yace ai masa aure Ammi tace har yanzu Bashir yaro ne ita bazata aurar dashi yanzu ba wannan tasa suka tattara batun sa suka watsar tare da zuba masa ido wanda yake cin karan shi babu babbaka dan har labari aka zowa da Aliyu akan Bashir nada gidan sa inda yake kai matan banza ranar daya gayawa Ammi Seda ta kwanta a gadon asibiti tunda ga nan Aliyu yayi fushi ya zubawa Bashir Idanu.

Murza ƙugunta ya shigayi cikin wani irin salo yana kusanto da fuskarsa daidai tata wanda ita

kuma take ƙoƙarin ta ƙwaci kanta gaba ɗaya hankalinta idan yayi dubu ya tashi Kokawa ce ta kaure a tsakanin Bashir da Farha shiya gigice da dirin Jikin farha wadda kallo ɗaya yayi mata ya gano karuwar Jiki gareta a haka zaka ɗauka ƴar ƙarama ce sedai ga wanda yasan mace yasan Farha ƙaramar ƙasa ce da albarkatun man fetur.

A fusace ta ɗago tana ƙare masa kallo Shima fari ne siriri kamar bafulatani sam basa kama da kowa agidan kamannin sa daban Cizo ta gartsa masa a Hannun daya riƙe ta dashi aikuwa ya sake ta yana yarfe hannun aguje ta koma ɗakin ta Lokacin Ammi bata falon key ta murza ajikin Ƙofa ta zube a wajan tana sakin Numfashi idan hankalin farha yayi dubu tofa ya tashi Kukan ma yaƙi zuwa ita tunda take ba namijin daya taɓa ratsa Ƙugunta sai shi Ko Mijinta baya gigin taɓa Jikinta ko salim da sukai soyayya Mai tsarki sukai bai taɓa kai hannu Jikinta ba gwarama bawan Allah daya ɗan riƙe ta Lokacin daya zo wajan ta.

Da ƙyar ta koma saman gado duk a tsorace take Sai da ta ɗan sami Nutsuwa sannan ta shiga Banɗaki tayo alwala ta shiga rama sallolin da suka hau kanta ranar Bacci gagarar Farha yayi tabbas Idan har wannan saurayin a gidan yake tofa zaman ta a gidan akwai hatsari tunda ta Lura Mahaifiyar su Se abin da ɗa yaga dama yake yi musamman ƙananun dan ta lura kamar tafi son su.

Sannan Kuma tana tsoron gayawa Bawan Allah tasan halin shi kada itama yaje ya dake ta, ko kuma babar su taji tace sharri ne ɗaga hannu tayi tana addu'a akan Allah ya kawo mata ɗauki acikin wannan hali se can dare Bacci ya ɗauke ta mai cike da firgici da mafarkai marasa kan gado.

Bashir ya jima a tsugunne a wajan yana yarfe hannun shi kafin ya koma da baya ɗakin shi ya buɗe ya shiga ya faɗa saman gado yayi ruf da Ciki Kamannin yarinyar yana masa yawo Acikin idanun shi Wacece ita me ya kawo ta gidan su.
Tashi yayi zaune yana shafa ɗan Guntun gemun daya tara.
"Ina son ki kuma da aure, ko ke wacece zan aure ki dan na hango kala tace tabbas zatai Juriya ta haɗa dukkan abin da nake so dama bana son mace ta cika kyau bana son mace ta cika tsayi bana son mace ta cika ƙiba bare wannan tana jin maza kyau zatai ta ciko tai Ɓul ɓul kuma zatai daɗin harka"
Shi kaɗai yake maganganun kamar zararre.

Tashi yayi ya shiga wanka dan dole seya shiga wanka sabida ta haɗa masa hazo ƴar wannan rungumar data masa gaba ɗaya jikin shi ya miƙe kawai harka yake buƙata baku ma da kowa ba seda ita sedai ita yana jin a wannan karon ze tunkari ammi da maganar ya sami macen aure, amman baze gaggawa ba seya gama sanin wacece ita kuma yagama sakar mata kuɗi ya ruɗe ta dasu.

Har ya fito wankan tunanin ta yake ya tsane jikin sa da guntun towel ya sauya kaya ya shiga falon Ammi ko ina shuru ya isa bakin Kofar ammi ya tura ya shiga ciki ya same ta zaune a gefen gado.

Da tsananin ɓacin rai Aliyu yabar part ɗin Ammi be shiga part ɗin saba seda yayi sallar isha'i lokacin daya shiga falon shi ya tarar da komai ya sauya alamun matar gidan ta dawo beko kalli setin ɗakunan ta dake Falon ƙasa ba ya haura saman benen shi wanda anan ɗakunan shi suke kayan shi ya shiga tuɓe wa ya faɗa wanka ya fito ɗaure da ƙaton blue towel a ƙugunshi yana tsaye bakin madubi yana fesa turare mami ta turo ƙofar ta shigo fara ce siririya mai tsayi sanye take cikin wasu irin english wears masu tsadar gaske riga ce me hannun vest se guntun skirt ƙafafunta kamar na kaza Ɓingil Ɓingil acikin skirt ɗin wanda idan tai motsi kaɗan za'a iya hango pant Ɗinta ta cikin madubin yake hango fuskar ta wadda tazo bayan shi ta tsaya tare da kwantowa Jikin shi.
"I miss you my hero"
Ta faɗa cikin narkar da murya ta fara Goga fuskarta a cikin kafaɗar shi zameta yayi ya nufi wardrobe ya ciro Gajeran wando da single ya saka agabanta batare data matsa ta bashi wuri ba.
"Yaya baka ce min komai ba nafa dawo tun ɗazu"
Ta faɗa cikin shagwaɓa.
Ya zauna a bakin gado yana ɗaukar wayar shi da sadiƙ ke kira ya katse kiran yana cewa.
"Na ganki mamy sannu da dawowa kawo min black tea"
Ta fita soƙai soƙai ya bita da kallo ya taɓe baki minti kaɗan ta kawo masa tea ɗin ya karɓa yana kurɓa ta zauna a gefen shi tana wasa da sajen shi ya aje Cup Ɗin a bedside drawer ya janyo ta ya ɗorata saman cinyar shi yana buƙatar mace sosai duk da ta ɓata masa rai amman ta gane Kurenta dan wannan baƙin shayi seda Aliyu ya shanye mamy tamkar shi, se kuka mamy take bayan lafawar Komai ya miƙe ya shiga toilet Minti kaɗan ya fito ya tsaya yana sharce ruwan Jikin sa ya dube ta ya rasa yaushe zata saba koda yaushe raki shikuma baya ƙaunar wannan raki duk da dai tana matiƙar Koƙari.
"Ki tashi mana kije ki wanka dan Allah bana son wannan kukan shekara goma Da aure amman dan ragwanci kullum se kin min kuka"
Turo baki tayi tana dira ƙafarta ya wuce ta ya shirya ya nemi Guri ya kwanta bayan ya zare zanin gadon.

Mami ta gaji dan kanta ta Miƙe ta fita zuwa ɗakin ta, ta fahimci baya son raki amman sunyi hira da wata ƙawarta tace wai namiji yana son langwai in ana Auratayya shine dalilin daya sa take wa Aliyu haka wanda shikuma baya son hakan ko kaɗan Itako mami rabi Kirsa ce ta saka rakin ba wani abuba.

Wanka ta shiga tana yi tana danna cinyoyinta domin Aliyu bezo mata da sauƙi ba bata koma ɗakin shiba magani ta sha ta kwanta anan ɗakin nata.

Bashir ya sami guri ya zauna a gaban Ammi yana kallon ta wadda ya fahimci kamar bata jin daɗi kuma ranta a ɓace yake.

"Ammi na dawo kuma na tarar da abubuwa marasa daɗi ko gaisawa bamu yi ba naje nai wanka

na dawo dafatan na same ku lafiya?"
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 42*

Ammi da har lokacin bata sauko daga fushin dukan da Aliyu yayi wa su safna ba ta kalli Bashir da kulawa tana cewa.
"Lafiya ƙalau Bashir, yaya hanya?"
Ya gyara zama ya kuma matsawa gabanta sosai, "Lafiya lau Ammi wai me autras sukai wa Ya Ali ne haka wannan duka it's too much se kace ba ƴan uwan shiba in fa a ƙasar waje ne se anyi shari'a dashi"
Bashir ya sosa wa Ammi inda ke mata ƙaiƙayi nan fa ta soma magana cikin Ɓacin rai har tana fama ƙafarta.
"Wallahi Bashir na rasa wannan baƙar zuciya ta baba se Fushin tsiya fisabilillahi dan na wanke wa su Safna Banɗaki meye ze hau dukan su idan basu Huta yanzu ba yaushe ne zasu Huta to nagaji Gwara ayi ta taƙare na kira ɗan uwan shi na gaya masa sabida haka daga yau ai masa tsakani da ƴaƴana ah to"
Bashir dariya yake sosai cikin ƙara zugata yace mata "Aikuwa dai Ammi Nima na fahimci ya tsani ƴaƴan nan gaskiya ki taka masa Burki Haba mutum se baƙin hali da Ƙuncin Zuciya kamar ta mutanan farko"
Ammi ta Kuma gyara zamanta.
"Kai ma ka Faɗa to daga yau dai yayi auta baze sake dukar Min su ina ji ina kallo ba"
Bashir ya dubi Ammi kafin yace mata "Niko Ammi ɗazu naga wata yarinya a gidannan nace Ko wacece Oho ƴar baƙa haka Marar Jiki?"
Ya faɗa yana ɗage Girar shi Guda Nan da nan Ammi ta haɗe girar sama data ƙasa.
"Anno ba wai kake Nufi Hmm musa yaron Baba ne ya kawo Min ita wai ƴar ƙanin babansa ce Iyayen suka Mutu wallahi ƙaddara ce ta saka na ɗauki yarinyar nan gashi nan ta zame Min ƙajaga"
Da sauri Bashir ya katse mata maganar tata.
"Ammi sabida me Kika ce haka mayya ce ita? ko ɓarauniya? ko Munafuka? But nasan waɗannan Sunfi komai illah ga al'umma tell me wanne ne halin nata acikin su?"
Ammi ta haɗe Fuska kamar Farha na gabanta "Wannan ai duka ta haɗa kaga mayya ce ita ta lashe Kurwar Baba ni bantaɓa ganin mai aikin da yake Kula da ita ba se wannan yarinyar sannan ɓarauniya ce Ni ban yarda da itaba Sannan Munafuka ce Uban wa yasan abin da ta gaya masa yazo ya Huce akan ƴaƴana Allah masani ni wallahi A yau naga Musa ma seta bar Mini Gidana dan ba zan iya riƙon taba ban san me gaba zata haifar ba"
Ajiyar zuciya Bashir ya saki Tabbas tarkon sa zai kama kurciya ashe ma bata da gata ashema ƴar ƙauye ce lallai zeci karan shi babu babbaka zeje ya nemi soyayyarta koda tsiya koda tsiya tsiya yasan se ya nace har Ammi ta aura masa ita.

"Ammi kada ki saka damuwa acikin zuciyarki Ya Ali fa kin san shi da zuciyar sadaukai wallahi tausayin ta kawai yake, Kuma kinga ƙanwar Musa ce kuma shi Kinsan baya wasa da dukkan

wani abu daya shafi Musa wannan shine kaɗai dalilin daya sa kika ga ya damu da ita, Sannan Ammi ki kwantar da hankalin ki Nida kaina zan koreta daga gidannan kada ma ki kulata yazo yana faɗa Kinji Ammina"

Sarai Ammi tasan waye Bashir da tijara seta ji ta yarda da abin da ya faɗa mata ware wa tayi suna ɗan taɓa Hira kafin yabar Ɗakin seda ya Leƙa Ƙofar ɗakin daya ga ta shiga yaja ta yaji akwai key yayi ajiyar zuciya yabar wajan yaso tana buɗe Ƙofar daya shiga ko Leɓanta yaɗan tsotsa yaji daɗi.

Da Asuba farha ta Miƙe ta shiga banɗaki tayo alwala tayi sallah tana nan zaune rana ta fito tayi azkar Fita tayi falon babu kowa shara tahau yi kamar yadda Ammi ta sakata tayi Ta gyara ko ina har Moping ita tayi sannan ta shiga Kitchen ta soma fere doya lokacin wajan ƙarfe takwas da rabi Doya da ƙwai tayi da miyar source seta yi musu Kunun gyaɗa da farfesun Kifi ta kammala ta gyara Kitchen Ɗin ta shiga kai kayan abincin dining ta kai na ƙarshe Bashir ya shigo falon cak ta tsaya da jera abincin ta raɓe ta ɗauke Numfashi tana jiran ya wuce sedai ya tsaya akanta yana sakar Mata Murmushi.

"Amincin Allah ya tabbata a gareki"
Gabanta ne ya faɗi Irin sallamar da ɗan uwan sa yayi mata kenan ranar farkon haɗuwar su.

"Haba baby me yasa zaki min rowar Maganarki Bayan nasan ba kurma bace?"
Ƙoƙarin Juya wa take ta koma Kitchen yayi saurin kamo gefen Hijabin Jikinta gabanta ya faɗi da sauri ta juyo idanunta sukai raurau kamar zata yi kuka.
"Please kada ki kashe ni da kallon ki kigaya min kalma ɗaya tak wadda zata sakani Nutsuwa baby tun jiya na kasa samun bacci akanki nai mafarkin ki kina bani daɗin ki Baby Plsss kimin magana"
Ya ƙarashe maganar yana shan yaji irin na ƴan iskan maza.
Ba abin da farha take nanata wa a zuciyarta se ambaton sunan Allah lallai inda ranka zaka sha kallo lallai Gidan nan akwai Mutane kala kala shi kuma da wannan salon Iskancin Yazo Allah ka kawo min ɗauki ta faɗa a zuciyarta.
"Wallahi in zamu kwana anan in baki mani magana ba bazan saki Hijabin kiba fisabilillah kashe marayan Allah zaki yi ni kawai Muryarki nake son naji" ya faɗa yana langwaɓar da kanshi kamar ze Kuka Irin sune karuwan maza.
"Ni ka sake ni aiki nake yi" daga haka taja hijabin tayi Kitchen ba abin da zatai amman zamanta aciki yafi mata rahma Har rufo ƙofar tayi tunanin ta ze Biyota Cikin haka Hajjo ta shigo Kitchen Ɗin farha ta saki Fuska.
Sosai tare da cewa "Hajjo ina kwana?" Hajjo ta dubi Farha da kulawa "Hmm ƴata jiya Rigimar Gadanga ta hana na tambayeki Yaya jikin naki" farha tayi dariya "Lah hajjo dama kina ciki yake wannan dukan Nima abin yafa bani mamaki da tsoro" hajjo tace "Ina kitchen ina girki dan Hajiya Ammi ta hanani shiga Hurumin ƴaƴanta ne ajiya data min gargaɗi shiyasa nayi Shuru ai shine maganin su yara ba tarbiya ba mutunci basa ganin Girman kowa" Hajjo ta faɗa tana Ƙoƙarin Ɗora ruwan zafi a saman Gas "Hmm Wallahi Hajjo haka ne ni bamma taɓa ganin yara Irin suba amman da alama akwai saka hannun babarsu wajan ɓata su wayyo Inama ƴaƴan Gidanmu ne

da sunci wuya wajan kawu" Da sauri kuma ta rufe bakinta  ta manta zatai suɓutar baki "Me kike cewa ƴata?"  Hajjo ta buƙaci taji abin da farha tace "A,a cewa nayi nafa gama musu abincin karin Kin san ta ce Ni zan dingayi" Hajjo tace "To da kin bari ai nazo Munyi tare amman shikenan Rigimar hajiya Ammi ce tayi yawa amman aikin yayi miki yawa tun jiya ta sanar Min nazo ne dai danna taimaka Miki" Farha tai Murmushi "A,a Ki barshi ai ba yawa ga namu ma na ɗiba mana semu ci abinmu" zama sukai a ƙasan Tiles Suka zuba doyar da Miyar da Kunun Kwano ɗaya suka ci ita da Hajjo Kuma ta saki ranta taci sosai Suna gamawa Hajjo ta mata sallama ta fita Ita kuma wanke wanken kwanu kan data ɓata ta haɗa tana yi Taji ƙarfin Jikinta sosai yau sabida gashi nan ma harta ci abinci Jifa jifa dai take Leƙe Ko wannan matashin ze Biyota ganin Be Biyotan ba yasa ta mayar da hankali wajan wanke wankenta.*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 43*

Ya ware Lumsassun idanunshi akan Ƙaton agogon dake manne a jikin Bangon ɗakin shi.
"Subuhanallahi I'm late today"
Ya faɗa a sanyaye tare da miƙar da dogayen ƙafafun shi wanda har sun dira a ƙasan gadon daya kwanta Wayar shi ya janyo yaga tarin Misscall da aka kira shi Tunda yayi sallar asubah ya kwanta bacci Bai tashi ba se yanzu wanda agogon daya kalla ya Nuna masa har 10:30am, Layin Sadik ya shiga kira wanda daga ɓangaran Sadik yana zaune a dining Sakina na serving ɗinshi break fast yaga kiran Aliyu.
"Gadanga ƙusar yaƙi zaki na Maryama shine dan rashin mutunci jiya kana ganin kirana kake katsewa ko?"
Sadik ya faɗa cikin barkwanci.
Aliyu ya saki tsadaddan Murmushin sa.
"Haba Babban yaya nina  isa kawai Lokacin bani da sukunin ɗaga wayar Ne yaya su Minal da Sakina ina fatan suna lafiya"
Sadik yayi dariya.
"Gata tana Jinka tace tana Miƙo gaisuwa dama Ƙarar ka aka kawo Min fa"
Aliyu ya zaro ido wanda hakan na ƙara fito masa da kyan shi idan yayi.
"Ƙara ta kuma waye?"
Sadiƙ yayi dariya.
"Hajiya Ammi tace a zauna a Kotun Ƙoli babu kai babu autras Ɗinta Inba haka ba Duk abin da tai maka kai ka siya"
Aliyu yayi wata dariyar Rainin hankali.
"Kai kasan me sukai dan iskanci Ammi ke wankewa yaran nan Toilet har faɗuwa tayi tsakani da Allah ya dace?"
Sadik yaɗan Yi Jim kafin yace masa.
"Bai dace ba da se ta saka ƴan aiki ai tunda akwai su, Amman No need ita da kanta tana wanke masu Bayi wani ma seya zage mu"
Aliyu ya ɗage Gira guda yace "To wannan ne silar Dukan amman ita ammi sam taƙi ganin Illar sakar masu Ɗin da take kuma ni ba ruwana ko yanzu naga Sun ƙara laifi zan dake su fa"
Sadiƙ yayi dariya.

"Kaifa matsala ta dakai Mugunta Dan Allah kada ka ƙara dukan yarannan Kaji"
Aliyu yaja tsaki mai ƙarfi.
"To Limamin shagalallu Bazan Kuma dukan suba"
Daga haka yaja wayar ya kashe.

Sakina matar sadiƙ tai Murmushi tana kallon shi.
"Dady kai da waye ne Kuke ta kai ruwa rana?" sadik yayi dariya.
"Nida Ali ne Ammi ce ta kawo Min ƙarar shi"
Taɗan ja tsaki kaɗan, "Ok shine yake maka tsawa a waya nifa wallahi sam bana Jin daɗin abin da yake maka Ɗinnan Kullum nuna maka nake kaima ka gina kanka kabar zama a ƙasan shi kaƙi kai Kenan Kullum kamar shine babban kai ƙaramin"
Sadik ya haɗe rai tare da cewa.
"Look sakina kin san bana son waɗan nan zantukan yaushe Ali ya taɓa min tsawa Ni ba zaki haɗani da ɗan uwana ba Ina Masa kyakykyawar Fahimta Kuma shima yana Mini"
A Ƙufule ta dire Cup Ɗin hannunta tayi ɗaki fuuu "Allah ya rabamu da Mutuwar Zuciya" ta faɗa da ƙarfi yadda sadik zeji yota.
Sadiƙ damo sarkin Haƙuri juya tea ɗin gabansa yayi yana Murmushi ba tun yau sakina ke Ƙoƙarin Nuna ƙyashi ga Ali ba shikam ba ruwan shi yagama shan tea Ɗinsa yabar Gidan ya tafi office batare daya bi takan sakina ba.

Bayan sun gama waya da sadiƙ ya sauka daga saman gadon ya shiga wanka ya jima acikin Toilet kafin ya fito mintuna kaɗan ya shirya cikin jajayen J.c Rigar Mai dogon hannun ce haka wuyanta a zagaye yake haka wandon shima Dogo ne daga wajan ƙasan ƙafar zagaye da adon fari wanda aka Rubuta Adidas da ƙaton harafi ya feshe jikinsa da turare zeje Filin training ne shine dalilin daya sa ya sanya kayan sedai Koda ya sauko ƙasa yama tarar Rana tayi sosai sai ya Nufi dining abin takaici ba abincin akai gashi yunwa yake ji sosai.

Ya kalli mami dake fitowa se baza ƙamshi take.
"Ina abinci na?" ya faɗa yana kallonta, ta ɗan sosa kai.
"Yaya ashe mai girki tayi tafiya ni ban sani ba amman bani Minti Goma zan dafa maka ko Indomie ce"
Ya ja tsaki yabar mata falon sarai tasan baya cin Girkin masu aiki sannan Idan yace ze Jirata nan ma ɓata masa Lokaci zata yi Part Ɗin Ammi ya nufa duk suna saman dining suna yin Break Bai Ko kalli saitin Su safna ba yaja kujera ya zauna yana gaishe da Ammi ba yabo ba fallasa ta amsa masa su safna dama sun gama suka tashi suka bar wajan itama Ammi da ragowar Haushin sa aranta tana gamawa tabar wajan ya haɗa tea ya ɗebi doyar yana zuba farfesun kifin a gefe Bashir ya shigo suka gaisa Shima yaja Kujera ya zauna yana haɗa tea Fuskar Aliyu a ɗaure yake Break ɗin kamar an masa dole.

Sum sum ta fito daga Kitchen duk Gefen hijabinta ma ya jiƙe tazo zata Gifta Bashir yaɗan ɗaga Murya.

"Zoki zuba min doya"
Aliyu ya watsa mai wani kallo bai ce masa Komai ba.
A hankali ta tako gaban Bashir Hannunta na rawa ta ɗauko plate zata zuba doyar Aliyu ya saka ƙafa ya taka mata tata da ƙarfi ta rintse ido yaɗan saci kallonta kafin yace wa bashir.
"Kai baka da hannu ne?" ya kalleta ba walwala a saman fuskar shi.
"Dallah ɓace min daga nan wurin kai ma tashi ka bani wuri"
Da sauri tayi ɗaki shikuma Bashir ya tashi yana ƙwafa yabar falon jiyay abincin ya fita aranshi duk da yana masifar son doya ya miƙe yabi bayanta zuwa ɗakin.

Tana tsaye tana yarfe Jiƙaƙƙen hijabinta ya turo ƙofar ya shigo ciki da sauri tai baya ta ɗauka ko wannan saurayin ne.

Ya jingina da ƙofa bayan ya rufo Kofar yana ƙare mata kallo.
"Me kikai yau agidannan?"
Banza tai masa.
Ya daka mata tsawa yana Kuma tambayarta zumɓura baki tayi ta juya masa baya.
"Daga yanzu kada ki kuma shiga kitchen yin wani aiki, sannan kada na kuma ganin wani ya sakaki aiki kinyi idan ba Ammi ba, Kuma kada na sake ganin Bashir ya miki magana kin kulasa"
Ta harare shi kafin tace.
"Nida nazo bauta bani da zaɓin uban gida duk wanda ya sakani aiki yi zanyi kai meye damuwarka, sannan shi wanda kace sunan shi Bashir nina san shima jiya ne kaɗai da muka ci karo da juna ya rungumeni..........
Da sauri taga yayo cikin ɗakin da sauri kanta yayo gadan gadan wanda ta koma bayan wardrobe ta maƙe tana zaro Idanu janyota yayi ƙiii har Tsakiyar ɗakin.
"Amman ban taɓa sanin baki da hankali ba se yau da auren nawa akanki har kika yarda ya rungume ki akan yaya?"
Tsoro yanayin nashi ya bata tai saurin zubewa a ƙasa tana Kuka.
"Nima fa ban sani ba nidai dan Allah kada ka dakeni ni wallahi tsoron ka nakeji wallahi kamin dukan su ni Mutuwa zanyi"
Ta faɗa tana wani irin kuka Muryarshi cike da takaici yace.
"Ai in ke baki mutu ba zaki lalata min aurena dan baki da hankali meye har zaki yarda Jikinki ya taɓa nashi so kike nai Miki duka shima nayi masa?"
Da sauri ta girgiza kai tana zaro ido tana haɗa hannu.
"Good to daga yau kada na Kuma ganin ko hanya kin haɗa dashi in ba haka ba sena miki dukan da zaki kasa gane gidanku shima Kuma ze same nine"
Ya faɗa da wani irin Fushi yabar ɗakin da gudu ta shiga toilet fitsarine na tsoro har ya fara zubo mata sabida bata taɓa ganin yanayin shi kamar haka ba.

Aliyu wajan Bashir dake zaune a falon ya nufa wanda yake ta danna wayar shi da alamun da akwai abin da yake Jira.
"Bashir kada na kuma ganin ka da waccan yarinyar Duk iskancin da kake a gari yana zuwa kunnen mu to ita ba kalar ka bace, idan ka yarda na Kuma ganin Koda magana ta haɗa ku"
Ya ja ƙwafa yabar wajan ya Nufi ɗakin Ammi duk da har Lokacin ranshi a ɓace yake.

Bashir wani basaraken Murmushi ya saki tare da cewa.
"Haba yaya Ali ai wallahi ko zaka kasheni ba zan bar wannan garar ba nasan ba komai ne yasa kake kaf kaf da ita ba dan kawai ƙanwar Musa ce toni kam ba wanda ya isa ya hanani taɓata tare da Ƙudirina na aurenta Very soon"................*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 44*

Ya shiga cikin ɗakin Ammi da sallama cikin bakinshi ya nemi guri ya zauna a ƙasan carpet Ammi bata ko kalli saitin da yake zaune ba.
"Ammi zan ɗanyi tafiya anjima zanje katsina amman ba lallai na kwana ba in kuma na kwana shikenan"
Se kuma ta juyo batare data bari sun haɗa idanu dashi ba tace.
"Me kuma zakai a hanyar katsina kai da kasan yadda hanyar take a yanzu?"
Murmushi yayi.
"Ammi bafa hanyar katsina ba katsina ɗin zani akwai wanda na turawa motoci basarake ne a jahar katsina to ana bikin ƴarshi wancan satin banje ba shine wannan satin zanje nai masa Allah sanya alkairi"
Ammi da duk ranta a jagule yake tunda taji yace ze tafi katsina sabida yadda labarai ke bazuwa na halin da jahar katsina ke fuskanta ta dube shi.
"Nidai dama zaka tura masa saƙon Barka da arziƙi ka rufa Min asiri kada ka tafi katsinar nan"
Shi dariya ma ta bashi uwa kenan duk yadda take jin zafin sa gashi abu kaɗan yazo kuma ya saka ta firgice cikin sanyin murya wadda tai kamar ba tashi ba yace mata.
"Ammi ki kwantar da hankalinki, Ni Birnin katsina zani ba ƙauye ba Kuma in sha Allah yadda naje lafiya zan dawo lafiya, Yana min ciniki sosai ne bazan iya ƙin zuwa yi masa Allah sanya alkairi ba sabida ni a tsakanina da costumers ɗina akwai Girmamawa da zumunci"
Ya faɗa yana kallon ta har lokacin hankalin Ammi be kwanta ba ta kalle shi tana cewa.
"To meya hana tun Jiya ka gaya min nayi addu'a duk da kullum acikin yinta nake ko Jirgi zaka hau?"
Murmushi yayi.
"A,a Ammi mota ce kuma nida kaina zanyi driving In sha Allah, Addu'a kullum muna yinta ba wani abu Khairan In sha Allah"
Tagumi Ammi ta rafka.
Ya miƙe tsaye.
"Ammi zanje na sauya kaya sannan Kuma dan Allah dan Annabi ba danni ba, Ammi adena saka yarinyar can aiki a kitchen in ma hajjo ba zata muku ba ku ɗauki duk me aikin da Kuke so ni zan biya amman itan ce bana son ana saka ta aiki tayi ƙanƙanta da yawa aikin ze mata yawa kada Ƙirjinta ya bude azo ana samun matsala"
Ammi ta tallafe kumatu tana binsa da kallon tuhuma kafin tahau tafa hannu.
"Kai Allah rabamu da Munafuki au ce maka tayi mun saka ta wani abun?Baba zo zauna ka gaya min tsakanin ka da ƴar ficikar yarinyar can nifa na fara zargin ka anya Baba?"

Murmushi yayi tare da cewa.
"Haba Ammi ita ta isa tazo ta gayan ƙananun maganganu ni ai na girmi wannan kawai I noticed kamar Yau ita tayi duk aikin gidannan ne"
Ammi ta hasalo masa tayo caa akan shi.
"Eh ita tayi sabida su safna suna fita makaranta ni kake so na shiga nayi tunda ka dakatar dasu Hajjo ehe nace Ni zanyi ita ƴar maiƙo ta kwanta tai bacci Su suna da makaranta to wa kake zaton ze in ba itan ba sannan ta gama nawa taje tai wa matarka"
Ranshi ya haɗe Ya kuma tsuke Fuska.
"To gaskiya in hakane Kawai Hajjo ta dawo ɗin, Sannan ni ban amince taje Min part Ɗina ba tai aikin iya kacin nan, Sannan kuma Ammi kicire zargina a ranki bani da wata alaƙa da ita in kika cire dalilin Musa yana daraja ni yana girmamani yana ganin Mutuncin kowa nawa to why shi ba zan daraja nashi ba bare ance marainiyace ta yaya bazan ji ƙanta ba Nina san watarana ya Allah zeyi dani"
Ya faɗa yana kallon Ammi yadda yayi ɗin kokai waye ba zaka ce akwai alaƙa a tsakanin shi da ita ba.

Ammi taja ajiyar zuciya.
"To duk naji yanzu tafiyar zakai kaci abincin kuwa?"
Ya ɗan taka yana fita daga ɗakin.
"Eh Ammi kimin addu'a"
Daga haka ya fita daga ɗakin har Lokacin Bashir yana falon zaman Jiran fitowar Farha Aliyu batare daya dubi setin Bashir ba.
"Malam ka tashi ka fita office zaman uban me kake agidan ok kai sedai duk wata ka ɗauki albashi kenan masu wahala suna can suna yi?"
Bashir ya shafa kai yana cewa
"Ba haka bane yaya dama yau zan ɗan huta kaga Jiya na dawo daga Abuja"
Tsaki Aliyu yayi tare da cewa.
"I don't want to come back and see you sitting here without going to the office"
Daga haka ya fita yabar falon Bashir ya kaiwa Iska naushi yana jan tsakin ɓata mai bajat da Yayan shi yayi haka ya Miƙe ya fita yay shirin Office Ko Ammi baiwa sallama ba ya fita a zuciye sanin waye Aliyu in ya dawo Ɗin bai tafi ba komai na iya faruwa.

Aliyu.
Ya koma part ɗinsa da ike yayi wanka shiryawa yayi cikin wani ubansun Boyel Navey blue wanda yayi masifar yi masa kyau hula da takalmi da agogo same colour ya saka wanda yayi azabar kyau kai kace wajan ɗaurin auren shi zashi ya tsaya yana fesa turare Ya fito daga ɗakin da waya kare a kunnen shi suna magana da Musa Mami tana zaune a falo ta kashe ado Cikin Jan lace riga da skirt.

Da sauri ta taso ta tare shi tana gyara masa lins ɗin gaban rigar shi.
"Yaya kayi kyau sosai"
Ya saki Murmushi ya zauna a saman Kujerar suna cigaba da waya da Musa Mami ta zuba mai ido wannan Mutumin da kyau yake ma sha Allah.

"This look is like you are going to eat me" ya faɗa yana hure mata idanun ta murmushi tai mai.
"Yaya inda zan iya da cinye kan zanyi yadda bamai samun saura"
Murmushi yayi mai tsada yana Kamo kumatunta.
"Ni naga ma kin fara Kumari gaya min sirrin Kinsan Ni ina son mace ƴar lukuta next time gaskiya ƙatuwa zan auro"
Ya faɗa yana mata dariya.
Turo baki tayi tana Ƙoƙarin saka Kuka.
"Haba yaya kalleni fa ƴar cif cif dani, Ni kaɗai nasan na ishe ka ko yaya?"
Ta faɗa tana leƙa fuskar shi Miƙewa yayi tare dayin gaba yana ce mata.
"Kiyi addu'a katsina ta ɗauka"
Daga haka ya fita daga falon yabar mami cikin zulumi da rashin gane maganar tashi............
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 45*

Cikin shiri ya shiga part ɗin Ammi ɗakin ta ya shiga tana zaune saman darduma da alamun sallar walha tayi ta ɗaga hannu tana addu'a suka shafa a tare ya kalle ta da kulawa.
"Ammi na shirya ai min addu' ni zan wuce fa"
Ammi ta ɗan matso gaban shi ta kama saman kanshi ta ɗora hannunta ta jima tana masa addu'a kafin ta ɗauke hannun duk idanunta sun ciko da hawaye ya shiga girgiza mata kai.
"Ammi Don't cry for me  addu'ar dai ita ce in kuma bakya son naje na haƙura"
Ta girgiza kanta.
"Kaje Baba Allah ya tsare"
Jikinsa ne yayi sanyi seya hau janta da hira dan ya kawar mata da tunanin da take yi akan tafiyar tashi, Kafin ya miƙe yana cewa.
"Ammi yau ba'a share Miki ɗakin naki ba ga ƙafar taki har yanzu akwai Kumburi"
Bai jira maganarta ba ya hau kaɗe mata zanin gado ya ɗauki abin shara ya share mata ɗakin tas ya Goge ya ɗauko turaren wuta ya kunna mata nan da nan ɗakin yayi kyau, Ya ɗauko man zafi yazo gabanta ya kama ƙafar yana shafawa Ammi ta zuba masa ido kaf ƴaƴanta ba mai biyayyar shi bamai son ta kamar shi tun yana yaro take jin daɗin sa take alfahari dashi Tuno sanda take fita sharar titi tayi wadda kafin ta fita shi yayi asubancin fita ya share mata sedai taga ya dawo da tsintsiya yana shirin fita makaranta ƙwalla ta taru a idanunta bai taɓa mata Musu a dukkan umarninta ba koda hakan ze jefa shi a damuwa yana bala'in son ta da kishin ta wata irin zuciya gare shi ta sadaukai yana son ƴan uwanshi Komai nashi na sune Bai taɓa mata gardama ba se zuwan Baƙar yarinyar can wadda har ya zage yana dukan su safna  agabanta tana masa magana bai saurare taba wannan gardama kaɗai taga ya taɓa yi mata wadda ta hassasa  Kiyayyar yarinyar a zuciyarta mai tsanani.

"Ammi idan kinga akwai damuwa na haƙura na tafi Office Ni dai nasan In sha Allah lafiya zanje na dawo ina Bin hanyoyin da suka fi wannan hatsari Kuma na dawo lafiya, akaf jahohin kasar nan ɗaiɗai kune bana shiga, Kaduna ce kaɗai ma bani da mutane sosai acan amman sauran

Jahohin nan duk akwai jama'ata kuma ina kokarin shiga"
Taja ajiyar zuciya.
"To shikenan Nima in ƙafar tawa tai min sauƙi zan ɗan leƙa gidan kawu na duba su kwana biyu banje ba ni kuwa mami ta dawo banji ɗuriyarta ba"
Ya kalleta bayan ya miƙe tsaye.

"Eh ta dawo bata zo nan bane?"
Da sauri Ammi tace.
"Zata zo ne hutawa take"
Ya girgiza kai yana cewa.
"Ammi in baki warke ba kada kije ki famo ƙafarki ga inda ma nace kije nan Gidan su Baba kinƙi zuwa anyi rasuwa amman baki je ba Ammi rayuwar ma duka nawa take yau ina Babanmu baya duniya duk wanda ya maka sharri kai bisa da alkairi ƙarshe sharrin nasa akan shi yake ƙarewa duk yanzu ba arziƙin ki suke ciba dan Allah Ammi ki dai na musu haka ko banza ciki ɗaya suka fito da mahaifin mu wannan Jini fa ba za'a iya kwashewa ba"
Ta zuba masa ido.
"To naji baba ku suka zamewa dole bani ba in ka kuma min maganar su Usman zaka fita da ɓacin raina"
Yayi ƙasa da kanshi.
"Allah ya baki haƙuri Ni na tafi"
Ta bishi da addu'a taja ƙaton carbin gabanta tana cigaba da lazumin da take yi.

Direct ɗakin farha ya tura ya shiga.
Tana cikin Banɗaki da alamun wanka take ya janyo stool ya zauna akai lokacin mami ta kira shi awaya kuma adaidai nan farha ta fito daga banɗakin ɗaure da zani ko hijabi babu ajikinta.
"Hello ƴammatana yaya ake ciki?"
Ya faɗa da ƴar tsokanar mami.
Ta karyar da murya tana cewa.
"Nifa ban gane ba wai katsina ka tafi?"
Yayi Murmushi yana cewa.
"In sha Allah ki tanadar min abun daɗi kafin na dawo"
Ta cikin wayar mami tace.
"To Allah ya tsare min kai daga dukkan sharri me zan tanadar maka ɗin?"
Yayi Murmushi "Dukan ki amman kizo ki gaida ammi bata jin daɗi"
Mami tace.
"Subuhanallahi ban sani ba ai jiya ban dawo da wuri ba amman zanzo kai mata sannu"
Yace.
"Ok" yana kashe wayar ya zubawa farha ido tana zaune gefen gado ta yafa wani zanin akan ta ya rufe mata Jikinta tana shafa mai rannan nata a haɗe kamar kace mata ket ta saka kuka.
"Me yasa bakya saka key a ɗakin nan daga an turo ƙofar take buɗewa?"
Tai masa banza ta miƙe ta Nufi wajan kayanta ta ɗauko zata wuce banɗaki ta saka ya taɗota ta faɗo saman Cinyar shi.
"Washh bayana ni ka sakeni"

Ta faɗa tana ƙoƙarin sauka daga saman cinyar tashi.
Yayi mata riƙon tsauri yaɗan kwanto da fuskarsa daidai tata.
"Kawo na sanya miki kayan naki"
Ya faɗa yana kashe mata ido ɗaya harara ta zabga masa ta warce kayan ta shige banɗaki ta jima aciki kafin ta fito har lokacin yana zaune yana aikin danna wayar shi.

Can nesa dashi ta zauna.
"Ya kamata in zaka shigo ɗakin mutane ka dinga neman iso ni har ga Allah ana shiga haƙƙina"
Ta faɗa tana kawar da kanta Murmushi yayi mata tare da dawowa Kusa da ita yana Ƙoƙarin kamo hannunta taƙi yarda ta zame ta zauna a ƙasa.
"Wai meye ne se Guduna kike tunda nazo na fuskanci kamar haushina kike Ji?"
Ƙaramin tsaki tayi wanda ya tsaya mata iya ita kaɗai dan beji taba ta rasa dalilin daya sa taji zafin wayar da ta tarar yana yi kuma ta tabbata da mace yake yin ta.

Ya sunkuyo daidai fuskarta ya ƙura mata ido.
"Naga kin fara haske ko ruwan gidan namu ya amshe ki ne?"
Ta bashi amsa.
"Eh ai wahala ma tana sa hasken dole wai me kake nema ne kazo ka zauna min a ɗaki kuma ni abu zanyi"
Ta faɗa tana matsawa daga setin nashi.
"Tofa Fatima yau kekam lafiyar ki ni kike wa ƙara a kaina?"
Ya faɗa  a hankali.
Saman stool ɗin daya tashi ta koma ta zauna tana facing mirrow tai masa banza ɗakin yayi shuru har tsawon Mintinu ya rasa me yasa take ɗaure Fuska yau take masifa Duk se yaji ya damu ko wani abun ke damun ta ya Miƙe ya isa gabanta ya kamo hannunta.
"Ni nazo sallama ne zan tafi katsina inna kwana to in ban kwana ba yau zan dawo in sha Allah"
Ya ƙarasa gaban ƙofar ya zaro key ɗin ya cire guda ɗaya ya jefa aljihun sa "Ki dinga saka key a ƙofar nan ban yarda na ƙara turowa naji ta a buɗe ba sabida ɗakin kine kaɗai a falon nan kuma keyn ƙofar babbar falo ya lalace shima zan kawo mai gyara to Kina rufe Ƙofar ki" ya faɗa yana aje mata ɗayan key ɗin a saman madubin ta.
Idanunta ne yaɗan taru da hawaye.
"Katsina kuma? to Allah ya tsare"
Daga haka ta soma ƙoƙarin fita daga ɗakin.
Ya riƙota wannan ne karon farko daya rungumeta ajikinsa ƙamshin turaren shi ya kashe mata Jikinta.
"Menene zaki fita bayan baki Min addu'aba ummmh?"
Ya faɗa Lokacin da yake ɗago kanta ya zuba mata ido lumshe nata idanun tayi sabida ba zata iya jure kallon da yake mata ba gaba ɗaya ya kashe mata jikinta.
Kusanto da fuskar shi yake daidai tata ahankali ya furta.
"I kissed your lips" da ƙaramin sauti yayi mata maganar kamar yana mata raɗar magana, kafin ya tallafo kanta a hankali ya ƙara haɗeta da jikinsa sosai ya ɗora harshen sa a saman idanunta ya shiga zagayewa kafin ya gangaro dashi cikin bakinta Rufe bakin nata tayi gam taƙi Buɗe wa Muryar shi can ƙasa cikin maƙurar buƙata yace "Please fatima" yawani ja maganar kamar ze

mata kuka Numfashi mai ƙarfi ta janyo kafin ta Buɗe masa bakin nata ya jefa harshen sa aciki ya soma tsotsar Harshenta da nashi harshen tamkar ya sami alewa har wani tanɗe baki yake kamar maye Goga mata ƙasumbar data cika Masa fuska yake gaba ɗaya tsigar Jikin Farha miƙewa tahau yi tana kuma shigewa Jikinsa kamar wadda takejin sanyi maƙale shi tayi gaba ɗaya ta shige Jikinshi seda ya gaji dan kanshi ya sakar mata harshen nata yaja da baya yana sakin Numfashi itako silalewa tayi ta faɗa saman gado tai ruf da ciki tana Sakin ajiyar zuciya.

Dafe kanshi yayi da sauri yabar ɗakin nata da jajayen idanunshi waɗanda sukai jajir kamar an watsa barkono acikinsu..............*RABO YA RANTSE! Iittafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 46*

Ƙarya ne ka gane wani yanayi Aliyu yake ciki sabida kamewar sa haka ya fita yana sauri ya shiga cikin wata farar mota mai kyau da tsari addu'a yayi yana fita daga gidan ya ɗauki hanyar shi, Bayan ya kashe dukkan wayoyin shi sabida Gudun yawan Kira.

Agigice yaya sadiya Yayarsu Farha ta faɗo gidansu farha idanu jajir da alamu ma kanta a juye yake ba itace ta kawo kanta gidan ba aiko tana shiga tsakar Gidan ta zube nan da nan ta soma iska tana buge buge tana Ihu Hankalin Umma a mugun tashe ta fito ta soma kunce goyon bayan sadiya ta ɗauki ƴar tana Ajewa agefe kawu ya fito shima, Suka rufu akanta suna tofa mata addu'a har wajan awa ɗaya tana iskokin kafin su jirge tai hamma ta miƙe tana jan ajiyar zuciya bata ko kalli sai tin kawu ba ta nufi ɗakin umma tana wani irin kuka wanda ta cika gidan dashi tana shiga ɗakin umma ta soma buga ƙafafunta.

"Yanzu Kawu tsanar taka garemu harta kai haka shine zaka ɗauki farha ka bawa wani wanda bamu san shiba bamu san daga ina yake ba, Wayyo Allah na na shiga uku ƴar uwata"
Yaya sadiya ta faɗa tana wani irin kuka mai ratsa zuciya umma ta zuba mata ido da alamun har Lokacin akwai sauran ƴan wasan ajikinta sadiya tai kuka ta godewa Allah ta koma tai tagumi hawaye yana ta zubo mata umma ta dube ta.
"Wai waye ya gaya miki an bawa wani farha?"
Umma ta tuhume ta sabida tasa gargaɗi kowa akan kada a sanar wa da sadiya sabida matsalar data ke tare da ita.
Ta share hawaye.
"Umma ni kawai Jikina ne ya bani gida ba lafiya, ina zuwa layin nan nai tambaya aka gayan wai an aurar da Farha har yau kusan sati Umma wannan wani irin aure ne aure ba bincike aure kamar na ƴar tsana fisabilillahi me farha taiwa Kawu daze mata haka Ina take da shekarun ma da za'a ce tai Girma batai auren ba"
Tafaɗa cikin Kuka!
Umma ta gyara zama sosai tana cewa.
"Shima kanshi kawun naku abin da yayi ya dame shi dan ko bacci baya samu To sadiya yaya zamuyi farha ta kafe seta auri Mutuminnan Ni kaina bana bacci Kullum zulumina ina yakai mana

ita nifa daidai da dangin shi ban sani ba a yanzu ban san ina yakai min ita ba amman ba ita tajawa kanta ba"
Yaya sadiya ta share hawaye! ta shaƙi majina.
"Ni wallahi umma inda ina nan ba mai aurar da ita haka kawai ma ƙila ɗan yankan kai ne"
Umma tayi murmushi mai ciwo.
"Sadiya baki ga yadda ake yada min magana a cikin gidannan ba Wallahi kullum da kuka nake kwana amman ban san abin da Allah ya ɓoye acikin auran nan ba nidai ina mata addu'a kuma addu'ar mahaifi bata faɗuwa ƙasa Banza nasan Allah yana tare da Farha"
Tagumi yaya sadiya tayi tana sakin ajiyar zuciya umma ta cigaba da cewa

"Ta kafe ta nace seta aure shi, Ranar data bar gidannan dagani har ubanta bamu yi bacci ba dan shi ma kanshi hukuncin daya yanke mata yanzu  damun shi yake ga lalura kullum yana ɗaki a kwance Matan gidannan kullum cikin min dariya suke suna cewa wai ƴan bokon ƙarshen zamani an ɓuge da auren mafatauci"
Umma ta faɗa da ɓacin rai.

Yaya sadiya ta dubi umma cikin tausayawa.
"Umma haƙiƙa kin mana komai a rayuwarmu kin tsaya mana akan komai namu kinci buri akan farha tayi karatu to kuma Allah seya kawo wannan ƙaddara ina so umma ki cire komai aranki Ki cigaba dayi mata addu'a haƙiƙa addu'arki itace makami agareta addu'arki itace garkuwa a gareta amman duk wannan Kuka baze yi muku ba"
Kawu ne ya ɗaga labulan ya shigo duka jikinsa a sanyaye ya dubi Ya sadiya.
"Sadiya ba laifina bane fatima ita ce ta nace seta auri wannan mutumi ni kuma takaicin ta yasa nace yazo a ɗaura musu aure, kuma an ɗaura ɗin hakan dana yi shine ya tsaya min azuciyata ina ganin kamar nahau dokin zuciya na yanke hukunci acikin fushi sedai hakan danai shine zesa jama'a su ƙi zagina domin kowa yasan ba da san raina yarinyar nan ta kafe ba"

Yaya sadiya tayi murmushin takaici.
"Haba kawu ai yanzu an wuce zamanin burge mutane sabida kome zaka ma ɗan adam bazaka burgeshi ba kamata yayi da yarinyar nan ta kafe seka bi komai a sannu amman yanzu ba yadda zamuyi Allah ya ƙaddara hakan addu'ar dai itace mafita"
Kawu ya goge hawayen shi.
"Ni na bi ƴata da mugun baki lokacin da zata tafi shiyasa har yanzu mafarkin fatima nake ya Allah ka kare min fatima har ga Allah fatima tana cikin jerin ƴaƴana dana fi so amman ɓacin rai ne ya saka nai mata haka Yau gashi ina Fegenki fatima"
Kawu ya fara tari Ya sadiya ta kawo masa ruwa da sauri amman duk da haka tarin bai lafa ba wanda yana yi Guntun jini na fitowa daga cikin hancin sa umma ta ƙwala ƙara matan gidan suka fito Su halifa ne suka samo tasi har ƙofar Gida aka saka kawu aciki suka tafi asibiti.

Babarsu Hadiza tai ɗammara tana kuka ta nufi ɗakin da umma take zaune ita da ya sadiya ta ɗaga labulan.
"To Hasiya burin ki ya cika Kawu ya faɗi ciwo Daman babban burinki ai ya mutu a raba gida to bari Kiji koda ya mutun kece a ƙasa dan kece mai ƴaƴa mata waya sani ma ko baƙin cikin farha

ne yakai shi ga fara tarin Jini tana can yawan barbaɗa dan ba namijin daze auri mace irin yadda aka aurar da ita"
Dama Babarsu Hadiza tunda aka aurar da farha take faɗin ƙananun maganganu musamman data ga yadda kawu ya damu Kullum maganar shi daya sani bai aurar da fatima ga wanda bai sani ba.
Yaya sadiya ta miƙe tayo kan Babarsu Hadiza tana huci kana tace.
"Kin manta karon dani ko? har zaki shigo ɗakin mu kina gayawa Uwata maganar banza ke gado ya dama Ko yau kawu ya mutu uwata ba zatai haya ba kuma ƴaƴa mata arziƙi ne ba kowa Allah yake bawa ba Kuma in sha Allah farha tana cikin Koshin lafiya Bayyanarta gareku seta hanaku bacci matsiyata"
Sum sum babarsu hadiza tabar wajan sabida tsoron sadiya Ya sadiya ta azalzali umma akan ta tashi suje asibitin da aka tafi kai kawu umma ta shirya Lokacin yamma tayi amman haka suka wuce asibitin kansu tsaye Wani ƙaramin Private su Halifa suka kai kawu wanda Ya sadiya taiwa Halifa waya ya gaya mata lokacin da suka ƙarasa ma tuni an bawa kawu gado Neman wajan zama sukai Ya sadiya ta dubi halifa "Me suka ce yana damun shi"
Halifa ya sunkuyar dakai ƙasa.
"Wai ciwon zuciya ke barazanar kama shi wallahi yaya sadiya kawu ya saka tunanin auren farha da yayi ne gashi nan ze kashe kanshi abanza ai ba ita kaɗai ya haifa ba"
Halifa ya faɗa cikin ɓacin rai.
Jikin Umma ne yayi sanyi ta fahimci kowa haushin Yadda kawu ke tunanin auren da yayi wa farha yake yi har dare suna asibitin Kafin Suyi wa su halifa sallama su koma gida Ya sadiya tai gidanta umma ma tai gida.............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 47*

Farha ta jima acikin wani irin yanayi tana ta jin kunyar abin da yayi mata lumshe ido tayi tana hango sanda yake kissing ɗinta ta ƙara mirginawa ta janyo pillow lallai namiji bai da kunya ko kunya bai jiba duk girman shi yazo ya wani rungumeta yana kissing ɗinta miƙewa tayi zaune tana Rufe fuskarta da tafin hannunta wani irin Sanyin jiki take ji ga wani irin yanayi dake bin dukkan sassan Jikinta tasan tana masifar son shi Amman ita harga Allah tana jin tsoron duk wani abu daze haɗata dashi dan ita a ganinta ya yi mata ƙato da yawa.

Miƙewa tayi taje banɗaki ta ɗaurayo fuskarta kuma har Lokacin Hannunta akwai ƙamshin turaren shi ɗakin ta akwai ƙamshin turaren shi ta rasa wani irin turare ne yake amfani dashi mai azababban ƙamshi Ƙamshin da baya barin Ka ta daɗi gefen gado ta zauna duk tana jin kewar tafiyar da yayi kuma tana fatan Allah ya dawo dashi lafiya wayar daya bata tana gida cikin ragowar kayanta daba tawo dasu ba jitai ina ma tazo da ita da babu abin da ze hana ta kirashi taji koya sauka lafiya sabida tana jin a labarai yadda jahar katsina ke fama da hare haren ƴan bindiga da sauran su se kuma taji ta kasa samun Nutsuwa har akai azahar tana zaune gajiya tayi da zaman tayo alwala tazo tayi sallah.

Ta miƙe ta fita falo babu kowa a falon ta wuce Kitchen yau marmarin wake da shinkafa take yi sabida ta jima bata ciba ta saba agida koda yaushe umma tana yi musu ta ɗora wake a tukunyar ta duba cikin kayan miya akwai su salak ta ɗiba ta zauna tana yankawa ƙananu ta gama ta wanke ta aje a kwalanda falo ta fita ta ɗauko kayan da suka ɓata na break ta haɗa ta wanke bayan waken ya dahu ta zuba shinkafar Mintuna masu dama ta ɗauka wajan Girkin dan se wajan Biyu da rabi ta kammala ta zuba a flaks ta jera su mai maggi yaji a wasu ƴan kwanuka takai dining ta zuba nata dana Hajja ta fita daga kitchen ɗin Kai tsaye ɓangaran Hajja ta nufa Lokacin da taje Hajja tana wanki a injin wanki Farha tai mata sannu ta shige Ɗakin Hajja ta aje abincin ta fito.

"Hajja kawo na tayaki wankin"

Ta faɗa cikin kulawa.

Hajja ta washe mata bakin ta fal goro.

"To Fati dama na gama ma amman bazan katse kiba ga shanya ta kimin" Farha ta ɗaga Bokitin ta nufi Igiya tana shanyawa hajja kayan nata Hajja wanka ta shiga ita kuma farha ta koma ɗakin hajja ɗin yau ɓangaran ma ba kowa aciki se Hajja kaɗai Hajja ta fito ta shigo ta shirya Ta kalli farha "Yaya kika jere kayan abincin kuma da alama baki ciba?" Farha tayi Murmushi "Hajja ke nake jira ga naki ga nawa" ta faɗa tana buɗe abincin Hajja tayi Murmushi "Ah lallai yau zanci abinci da marmari wake da shinkafa yaushe rabon duniya da ayyaraye su gidannan basa son irin waɗannan abincin kullum se aikin cin nama ni har ya isheni ma" Hajja ta faɗa tana saka hannu ta fara ci itama farha abincin take ci a nutse sedai duk Bata jin daɗin yanayin Jifa jifa gabanta faɗuwa yake ta tsame hannunta ta miƙe tsaye "Hajja zanje na kwanta kaina ciwo yake" Hajja ta bita da kallon tausayi "To ki amshi magani wajan Hajiya Ammi Allah ya sawaƙe" Ta fita ta wanko hannunta ta wuce part Ɗin Ammi ɗakinta ta shiga ta rufo ƙofar da key kamar yadda yace mata ta kwanta bacci ne mai nauyi ya kwashe ta.

Safna tayi tsaki bayan ta buɗe abincin ta nufi ɗakin Ammi wadda ƙafar yau ta saka ta a gaba dan ko falon ma bata fito ba ta tsaya akan ta.

"Ammi yarinyar nan wake da shinkafa tai mana na abincin rana ni gaskiya ammi bazan ciba wallahi"

Ammi ta dube ta.

"To kije ta dafa miki wani abun mana safna rabu dani ƙafata bana jin daɗin ta sam" batare data Ma Ammi sannu ba ta fita ɗakin Farha ta nufa sedai Koda taja akwai Key taja tsaki ta Koma wajan Ammi.

"Ammi akwai key a ɗakin nata" Ammi ta fusato "Ke rabu dani da abin da yake damuna ga ƙafata ga Baba tunda ya tafi nake Kiran shi a kashe ko zakije wajan Mami kiji yo min kota same shi ita" Safna ta turo baki gaba "Ammi lafiya lau sharrin network ne, Ammi rabu da Aunty Mami tunda ta dawo bata neme kiba ai" daga haka fita safna tayi tasan Ammi ba zata saurareta ba hankalin ta a tashe yake har akai Magariba Ammi nata kiran shi bai ɗauka ba Har Bashir ya dawo daga office Ganin yadda ta damu yasa Bashir yay ta bata haƙuri yana kwantar mata da hankalin ta se Bayan sallar Isha'i Aliyu ya shigo gida Ammi ta rufe shi da faɗan me yasa ya kashe waya duk ya ɗaga mata hankali haƙuri ya bata ya Miƙe ya tafi part ɗinsa Mami tayi masa sannu ta gabatar masa da dinner ruwan tea kaɗai yasha ya kwanta bayan yayi wanka.

Damma yayi sallolin shi mami ɗakinta ta kwanta yau dan jiya ta gurzu shiyasa yau ko gigin Nufo inda yake bata yi ba.

Aliyu yaja tsaki ya miƙe ya zira farar jallabiya da slipers ya sauka bayan ya rufo ɗakin shi Ko ina na falon an kashe ƙwai ya nufi sashin Ammi suma da alamun sunyi bacci dan Goma ta wuce ya rufo ƙofar falon Key ɗin daya riƙe na ɗakinta yayi amfani dashi wajan Buɗe Kofar Farha tunda ta tashi dama bata fita ba Sallah tayi tai azkar har aka kira isha'i tayo sabuwar alwala tana nan wajan zaune har Lokacin data idar da sallah mafarki tayi wai kawu ya mutu ana ta kuka agidan su Shine fa tunda ta tashi take ta kuka ga gefen mararta ya riƙe ciwo yake mata kuma tasan ba mp ɗinta ne ze zo ba ta zame ta kwanta anan ƙasan carpet Aliyu ya shigo ɗakin da sallama muryar ta a dashe ta amsa mai sallamar bata miƙe daga kwanciyar data ke ɗin ba.

Ya sami gefen gado ya zauna.
"Yaya baki da lafiya ne? kinci abinci?"
Duka ya jefa mata tambayar yana kallonta.
Ta dafa gadon ta zauna tana Share hawayen ta.
"Ni dai dan Allah kaje ka gano min kawu ne ya rasu"
Ya ɗan kalleta da sauri batare daya gano mai take nufi ba kafin yace mata...........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 48*

"Ki min magana yadda zan fahim ceki mana"
Kanta a sunkuye tace masa.
"Dama ina da wani kawun ne wanda ya wuce mahaifina shi nake nufi"
Cikin rashin fahimta yace mata"Ke waye yace miki ya mutu?"
Ta goge hawayen da yake zubo mata.
"Mafarki nayi wai ya rasu ƴan gidanmmu suna ta kuka"
Takai maganar itama Lokacin Kukan ne yazo mata mai ƙarfi"
Aliyu ya zuba mata ido har wani Lokaci kafin muryar shi cikin sanyi yace mata.
"I'm sorry, dreams are not true, kuma sannan kin saka tunanin gidan ma acikin ranki Amman yana nan lafiyan shi ƙalau"
Ta ɗago ta kalle shi.
"Kai tayaya zaka san yana nan lafiyar shi ƙalau bayan baka je ka gano shiba nidai ko ba zaka ba ka barni naje na gano shi wallahi Ko abinci naci tunanin mahaifa na nake Ummata nasan tana can tana tunani na shima kawun daya ce ze bada ni sadaka Ban san wani hali yake ciba ko ya mutu ne Allah ya nuna min acikin mafarkina"

Ya zuba mata ido kaɗan ya kau da kai sabida tausayin ta daya ji ya fara tasiri acikin zuciyar shi.
"Tam naji zanje na duba shi, Shikenan oya dena kukan haka, sannan ni ban maki alƙawarin fita ba sabida ni bana son yawan fita to yaushe ma kika daɗe da zaki ce zakije gida?"

Ajiyar zuciya ta sauke ta dafe mararta tana rintse ido da kulawa yace.
"To se kuma meye sauran?" kinci abinci?" ta girgiza kanta alamun bata ciba "Kina meye baki ci abincin ba?" ya jefa mata tambayar batare daya tsaya jin me zata ceba ya miƙe ya fita Minti kaɗan ya dawo da tea mai kaurin gaske.
"Ki samu kisha tea na duba baku da abinci kuma dare yayi" ta amsa ta kafa kai ta shanye Cikinta ya hautsina bayan ta aje cup Ɗin da gudu tayi toilet ta dinga sheƙa amai Yana tsaye akanta yana mata sannu ta ɗauraye bakinta ta koma ta zauna tana rawar ɗari Jikinta na rawa nan da nan ta soma Jin zazzaɓi dama tasan za'ai haka ulcer gareta cronic kuma rashin cin abincin ne yaja mata haka.

"Kina da ulcer fatima me yasa kike wasa da abinci me zaki ci yanzu na siyo Miki?"
Ta girgiza kai tana Ƙudundune Jikinta da hijabinta "Ka bar shi na ƙoshi koka siyo ba zan iya ciba ka kawo min ruwan sanyi in sha" ya fita ya kawo mata ruwan ya buɗe mata tasha kaɗan ta jingina da Jikin gado tana hawaye ya koma gefen gadon ya zauna.
"To yanzu meke miki ciwo?"
Ta nuna mai gefen mararta.
"Shine ya ɗaure kamar dutse"
Ta faɗa tana kuka ɗagota yayi ya ɗorata a saman cinyar shi ya cire mata hijabin Jikinta zafi zau kamar wuta ya Ajeta a gefen gadon ya tashi tsaye ya kashe hasken ɗakin rigar Jikinsa ya cire yayi saura daga shi se gajeran wando ya hawo saman gadon ya ɗagata cak ya zare mata doguwar Rigar Jikinta gaban farha ya fadi sabida under wear skirt kaɗai ne ya rage ajikinta Hankalinta bai tashi ba seda taji ta kwance a saman ruwan Cikinsa ya ɗorata akai ya kwantar da ita a saman Ƙirjinsa ta laluba ko zata sami Hijabi ta rufe jikinta ina setaji ta taɓo cinyarshi mai cike da gashi kwance a samanta a hankali taji ya ɗora hannun shi a inda tace yana mata ciwon Murza wajan ya shiga yi cikin kunnenta taji maganar shi ƙasa ƙasa.
"Yayi sauƙi kona sake miki?"
Ta girgiza kai cike da tsoro tace.
"Yayi sauƙi ma sosai ya miƙe zaune ya kwantar da ita hannun shi ya ɗora yana cigaba da murza wajan har seda ƙululun abun ya baje sannan ya saki ajiyar zuciya ya yunƙura ze tashi daga gadon sedai zuciyar shi ta gagara hakan wani Irin abu game da ita ne yake fisgar shi a hankali ya koma da baya ya janyota jikinsa ya haɗe jikinsa da nata waje ɗaya ya rungumeta zafin Jikinta yana ratsa masa nashi Jikin wasu irin al'amura masu girma Aliyu ya tsinci hannun shi na aikawa jikin farha bai Gigice ba seda ya ɗora hannunshi a kirjinta se yaji abun ya wuce tunanin shi ya shiga sarrafa jikinta da zafi zafi.

Kuka take sabida wani baƙon lamari da bawan Allah yake aika mata dashi Jikinta ta zame ta koma can ƙarshen gado tana kuka "Dan Allah ka bari ni wallahi kai min ƙato kashe ni kake son kayi" ta faɗa tana kuka a hankali ya janyota shima kan shi yasan da wahala in zata iya ɗaukarshi ƙanƙantar yarinyar tayi yawa amman yaya zeyi Wutar buƙata bazata bar ƙafafun shi su iya sarrafuwa zuwa part ɗin shiba bare yaje wajan Mami ta kawar masa da ita.

Bakinsa ya ɗora a saman nata ya shiga aika mata da wani irin zazzafan saƙo wanda ya ribace ta baji ba gani ya nufi hanyar da zata sada su hanyar da zata ƙara danƙon dangantakar dake

tsakanin su a wannan Lokacin wani lamari mai girma ya afku a tsakanin su gaba ɗaya hankali da tunanin Aliyu ya gushe ji yake kamar ya sami babbar mace mai shekaru da yawa tunda yake bai taɓa jin Nutsuwa farin ciki dadɗi marar misali kamar na wannan Lokaci ba tuni ya miƙi hanyar shi ɗoɗar wadda shiya fara buɗe wannan hanya a babin rayuwarta, Adaidai Lokacin ita kuma tunaninta ya ɗauke cak numfashin ta na barazanar ɗauke wa wata irin azaba ce take jinta tundaga yatsanta har ko ina na jikinta hawayenta ya ƙafe yawunta ya ƙafe kukan ma yaƙi zuwa se Nishin azaba take tana jin tunda umma ta kawo ta duniya bata taɓa jin mai kama da irin wannan azaba ba dama haka auren yake ita bata da ƙawa bare a bata labari yayin ta kuma basa irin wannan maganar dasu inda tasan haka ake cin wiya dame zesa ta ɗaga hankali wajan auran shi sam babu imani a ranshi duk girman shi ya haye samanta yana mata mugunta. Numfashin tane ya Tsaya na wucin gadi Lokacin da ya sami Nutsuwa ya ƙamƙameta jikinsa yana wani irin rawa nan da nan zazzaɓi mai ƙarfi ya rufeshi janyota ya kuma yi ya matseta kamar ze rabata biyu ya janyo musu ƙaton bargo ya rufe musu Jikinsu ruf dashi................

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 48*

"Ki min magana yadda zan fahim ceki mana"

Kanta a sunkuye tace masa.

"Dama ina da wani kawun ne wanda ya wuce mahaifina shi nake nufi"

Cikin rashin fahimta yace mata"Ke waye yace miki ya mutu?"

Ta goge hawayen da yake zubo mata.

"Mafarki nayi wai ya rasu ƴan gidanmmu suna ta kuka"

Takai maganar itama Lokacin Kukan ne yazo mata mai ƙarfi"

Aliyu ya zuba mata ido har wani Lokaci kafin muryar shi cikin sanyi yace mata.

"I'm sorry, dreams are not true, kuma sannan kin saka tunanin gidan ma acikin ranki Amman yana nan lafiyan shi ƙalau"

Ta ɗago ta kalle shi.

"Kai tayaya zaka san yana nan lafiyar shi ƙalau bayan baka je ka gano shiba nidai ko ba zaka ba ka barni naje na gano shi wallahi Ko abinci naci tunanin mahaifa na nake Ummata nasan tana can tana tunani na shima kawun daya ce ze bada ni sadaka Ban san wani hali yake ciba ko ya mutu ne Allah ya nuna min acikin mafarkina"

Ya zuba mata ido kaɗan ya kau da kai sabida tausayin ta daya ji ya fara tasiri acikin zuciyar shi.

"Tam naji zanje na duba shi, Shikenan oya dena kukan haka, sannan ni ban maki alƙawarin fita ba sabida ni bana son yawan fita to yaushe ma kika daɗe da zaki ce zakije gida?"

Ajiyar zuciya ta sauke ta dafe mararta tana rintse ido da kulawa yace.

"To se kuma meye sauran?" kinci abinci?" ta girgiza kanta alamun bata ciba "Kina meye baki ci abincin ba?" ya jefa mata tambayar batare daya tsaya jin me zata ceba ya miƙe ya fita Minti kaɗan ya dawo da tea mai kaurin gaske.

"Ki samu kisha tea na duba baku da abinci kuma dare yayi" ta amsa ta kafa kai ta shanye Cikinta ya hautsina bayan ta aje cup Ɗin da gudu tayi toilet ta dinga sheƙa amai Yana tsaye

akanta yana mata sannu ta ɗauraye bakinta ta koma ta zauna tana rawar ɗari Jikinta na rawa nan da nan ta soma Jin zazzaɓi dama tasan za'ai haka ulcer gareta cronic kuma rashin cin abincin ne yaja mata haka.

"Kina da ulcer fatima me yasa kike wasa da abinci me zaki ci yanzu na siyo Miki?"
Ta girgiza kai tana Ƙudundune Jikinta da hijabinta "Ka bar shi na ƙoshi koka siyo ba zan iya ciba ka kawo min ruwan sanyi in sha" ya fita ya kawo mata ruwan ya buɗe mata tasha kaɗan ta jingina da Jikin gado tana hawaye ya koma gefen gadon ya zauna.
"To yanzu meke miki ciwo?"
Ta nuna mai gefen mararta.
"Shine ya ɗaure kamar dutse"
Ta faɗa tana kuka ɗagota yayi ya ɗorata a saman cinyar shi ya cire mata hijabin Jikinta zafi zau kamar wuta ya Ajeta a gefen gadon ya tashi tsaye ya kashe hasken ɗakin rigar Jikinsa ya cire yayi saura daga shi se gajeran wando ya hawo saman gadon ya ɗagata cak ya zare mata doguwar Rigar Jikinta gaban farha ya faɗi sabida under wear skirt kaɗai ne ya rage ajikinta Hankalinta bai tashi ba seda taji ta kwance a saman ruwan Cikinsa ya ɗorata akai ya kwantar da ita a saman Ƙirjinsa ta laluba ko zata sami Hijabi ta rufe jikinta ina setaji ta taɓo cinyarshi mai cike da gashi kwance a samanta a hankali taji ya ɗora hannun shi a inda tace yana mata ciwon Murza wajan ya shiga yi cikin kunnenta taji maganar shi ƙasa ƙasa.
"Yayi sauƙi kona sake miki?"
Ta girgiza kai cike da tsoro tace.
"Yayi sauƙi ma sosai ya miƙe zaune ya kwantar da ita hannun shi ya ɗora yana cigaba da murza wajan har seda ƙululun abun ya baje sannan ya saki ajiyar zuciya ya yunƙura ze tashi daga gadon sedai zuciyar shi ta gagara hakan wani Irin abu game da ita ne yake fisgar shi a hankali ya koma da baya ya janyota jikinsa ya haɗe jikinsa da nata waje ɗaya ya rungumeta zafin Jikinta yana ratsa masa nashi Jikin wasu irin al'amura masu girma Aliyu ya tsinci hannun shi na aikawa jikin farha bai Gigice ba seda ya ɗora hannunshi a kirjinta se yaji abun ya wuce tunanin shi ya shiga sarrafa jikinta da zafi zafi.

Kuka take sabida wani baƙon lamari da bawan Allah yake aika mata dashi Jikinta ta zame ta koma can ƙarshen gado tana kuka "Dan Allah ka bari ni wallahi kai min ƙato kashe ni kake son kayi" ta faɗa tana kuka a hankali ya janyota shima kan shi yasan da wahala in zata iya ɗaukarshi ƙanƙantar yarinyar tayi yawa amman yaya zeyi Wutar buƙata bazata bar ƙafafun shi su iya sarrafuwa zuwa part ɗin shiba bare yaje wajan Mami ta kawar masa da ita.

Bakinsa ya ɗora a saman nata ya shiga aika mata da wani irin zazzafan saƙo wanda ya ribace ta baji ba gani ya nufi hanyar da zata sada su hanyar da zata ƙara danƙon dangantakar dake tsakanin su a wannan Lokacin wani lamari mai girma ya afku a tsakanin su gaba ɗaya hankali da tunanin Aliyu ya gushe ji yake kamar ya sami babbar mace mai shekaru da yawa tunda yake bai taɓa jin Nutsuwa farin ciki daɗi marar misali kamar na wannan Lokaci ba tuni ya miƙi hanyar shi ɗoɗar wadda shiya fara buɗe wannan hanya a babin rayuwarta, Adaidai Lokacin ita kuma tunaninta ya ɗauke cak numfashin ta na barazanar ɗauke wa wata irin azaba ce take jinta tundaga yatsanta har ko ina na jikinta hawayenta ya ƙafe yawunta ya ƙafe kukan ma yaƙi zuwa

se Nishin azaba take tana jin tunda umma ta kawo ta duniya bata taɓa jin mai kama da irin wannan azaba ba dama haka auren yake ita bata da ƙawa bare a bata labari yayin ta kuma basa irin wannan maganar dasu inda tasan haka ake cin wiya dame zesa ta ɗaga hankali wajan auran shi sam babu imani a ranshi duk girman shi ya haye samanta yana mata mugunta. Numfashin tane ya Tsaya na wucin gadi Lokacin da ya sami Nutsuwa ya ƙamƙameta jikinsa yana wani irin rawa nan da nan zazzaɓi mai ƙarfi ya rufeshi janyota ya kuma yi ya matseta kamar ze rabata biyu ya janyo musu ƙaton bargo ya rufe musu Jikinsu ruf dashi................
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 49*

Adaidai kuma wannan Lokacin da agogon najeriya ya buga ƙarfe biyun dare tai wata irin razana Sabida mugun mafarkin data yi nan da nan Jikinta yahau rawa idanunta suka firfito Duk sanyin Ac'n daya cika ɗakinta bata Jinsa se tsabar rawa jiki da zafi da zufa da take karyo mata Kuka ta saka tana buga kanta da Jikin gado wanda shine ya farkar da Mijinta daga baccin da yake duk da yayi fushi da ita akan abin da tai masa da safe Amman Tsananin yadda ta ruɗe ta firgice Abin ya ɗaga masa Hankali janyota yayi yana tofa mata dukkan addu'ar data zo masa cikin Bakinsa sedai ina sake Fusga take tana dukan kanta da Jikin gado Ganin haka yasa ya ɗauko wayar shi yana kunna suratul baƙara zaton sa gamo tayi Luf tayi tana sakin ajiyar zuciya Jin kamar tayi bacci yasa ya tofa mata Kursiyu ya koma bacci bayan ya kwantar da ita a gefen shi, Bacci ne mai nauyi ya kwashe shi sabida Jikin magidanci kowa yasan Jiki ne na wahala bare shi mai zirga zirga dan neman halak ɗin shi tana ganin ya kwanta bacci ta zare Jikinta ta fita daga ɗakin wani ɗaki wanda ke nesa da nata ta shiga Shaf ta mance da wayarta haka ta dawo ta ɗauko wayar ta koma ɗakin Zama tai a gefen gado ta saka hannu ta tallafi Fuskarta se kuma ta miƙe tana sintiri hawaye nabin Idanunta sosai kamar famfo.

"Allah ka ƙaryata wannan mafarki dana yi kai ina bama ze yuwu ba"
Ta faɗa kamar mai cutar shigar hauka sabon kamu se kuma ta juya ta ɗauko wayarta to wama zata Kira da wannan tsakar dare haka seta wurga wayar saman gado ta kuma fashewa da kuka.
"Dana ga wannan rana gwara naga mutuwa ta wannan mafarki ba gaskiya bane"
Ta faɗa tana kuka kawai shawarar zuciyarta tabi ta ɗauko wayar ta shiga contact ɗinta ta lalubi Number da take son kira Ringing Biyu aka ɗaga daga cikin wayar wata irin ƙara aka saki ana cewa.
"Jaririya me ye ya hanaki bacci har zuwa wannan Lokaci?"
Ta rintse ido tana sakin Numfashi.
"Uban ɗakina bacci ya gagari idanuna Zafi ya ziyarci zuciyata a taimake ni dan so a taimake ni dan ƙauna"
Dariya aka kwashe da ita wadda ta amsa dukkan cikin wayar har tasaka ta yada wayar ba shiri kafin ta sunkuya ta ɗauka tana cewa.
"Kaina bisa wiyana Ubana uban ɗakina dodo tunkarar ka se Zaki Namiji sa maza gudu"

Wata irin haniniya ya soma yi yana surkulle ta cikin wayar tare da ƙara wadda zata tabbatar da cewa wanda yake riƙe da wayar ba Mutum bane aljanine ya taka kan mutum yayi hawan Bori.
"Jaririya wace buƙata gareki ni zan jirga zan jaya na tafi jangare aiwatar da aikin ƴaƴan bil adama"
Ta share hawaye.
"Wannan aikin dana kawo muku na kwanakin baya dukkan wanda kukai na samu nasara sedai yau na kwanta bacci nayi mafarki"
Dariya ya kaure da ita yana cewa.
"Seni kafiri ɗan kafira mijin kafira baban kafiri gayamin me kika gani cikin ƙananun Mutuwar taki?"
Taja ajiyar zuciya.

"Shi wanda na kawo Muku aikin akan shi na gani da wata yarinya da yara a bayansu suna gudu sedai da suka je bakin wani rami haske ya ɗauke min ganina ya kashen idanuna na koma ganin duhu shine hankalina ya tashi nake tunanin kodai aure zeyi ya haihu wanda bana fatan hakan shiyasa nake sakar Muku kuɗi akan duk cikin da matar shi take samu ya lalace kuma aiki yana kyau iyayen ɗakina domin duk cikin data ke samu ɓarewa yake batare da sun san dalili ba sabida bana ƙaunar ya haihu ƙanin Mijina ne yana da masifar dukiya idan har ya haihu dukkan kaddarar shi hannun matar shi da ƴaƴan shi zata koma nida Mijina haka zamu tashi a tutar babu Kuma da mijina ake wahalar tara dukiyar to kaga idan bai haihu ba mune da gadon sa koda ya mutu kaga bani da matsala Nida ƴaƴana, Kwanaki har ƙanwata na bashi ya aura yaƙi Wannan lamari shine yake ɗaga min hankali a kullum"

Daga cikin wayar aka kwashe da dariya kana aka ce.
"Haba jaririyata nine mugun ɗan muguwa nine namiji me sa maza gudu nine yautai Mugun tsuntsu nine cinnaka bai san na gida ba ko jinsina tsorona suke tunda kika yaran wannan yare na gano kuma nai alƙwarin share Miki hawayen ki na rantse da dutse da dutse na rantse da Dutsen kwatarkwashi na rantse da kan uwata wannan haihuwa ba zata yiwu ba idan kuma ta yuwu niba aljan bane domin na tara jarirai na akan matarshi daga yazo saduwa da ita suke shigewa su zuƙe ruwan Miniyin nasa daze samar da haihuwar su zuba nasu baƙi wanda shike tasiri a mahaifarta idan tazo ta sami ciki ya ɓare a banza suna can suna ta asarar Kuɗin su a wajan ƴaƴan nasara basu san aikin ya wuce tunanin Mutum ba, Sannan maganar ɗamarmara ( aure ) ki kwantar da dolamarki ( hankalinki ) jaririya ta babu ƴar bil adaman da zamu bari ya aura Ke sha'awar ma semun cire mishi ita na rantse da dutse ba zai taɓa ganin ƙwan haihuwar sa a wannan duniya ba sedai a lahira in ana gani dukiya wahalar banza yake Ku yake tarawa da ƴaƴanku dan haka ze Mutu magada su gada ba tare daya sami magaji ba"
Yakai yana dariya.
Wata irin shewa tayi tana masa kirari Tana godiya ta kashe wayar ta zauna jagwab se yanzu ta sami Nutsuwa daga inda ta miƙawa imaninta dan duk abin da suka gaya mata ko suka ce takai bata tsallake wa kuma bata jin daɗi har seta yi.

Sakina kenan matar sadik yayan Aliyu, Haka ta koma ɗakinta hankalin ta kwance Ta koma gaban sadik ta kwanta taja musu bargo bacci ya ɗauke su mai daɗi wanda basu suka farka ba

se asubahi tayi sallah ta koma baccinta.
Sakina ta manta Allah ne da kanshi yace abin da ya ɓoye babu wanda ya isa ya bayyana abin da ya bayyana ba wanda ya isa ya ɓoye ta manta Allah ne yace Idan yaso bawansa ya kasance se yace masa ( kumfa yakun ) ta manta Allah ne yace idan yaso bawansa da samun abu idan duniya da abin da ke cikinta zasu haɗu don su hana basu isa ba, kuma idan ya hana bawan sa abu duk duniya da abin da ke cikinsa in zasu haɗu domin su bashi basu isaba tamanta kowa yana bacci Allah ne baya bacci ta manta kowa yana gajiya Allah ne baya gajiya ta manta kowa na neman mataimaki amman Allah baya neman mataimaki cikin Mulkinsa ta manta da cewa da aljani da mutum duka Allah ne ya halicce su badan komai ba se domin su bauta masa ta manta cewa babu mai ƙarar da Allah kuma babu ragar dashi kuma ta manta Allah ya hana zalunci akan sa kuma ya hana acikin bayinsa ta manta da sallarta da komai nata muddin ta bawa wanin Allah gaskiya Allah baze amsa ba, babu masanin gaibu se Allah shine mai ilimin abin da ze faru yau gobe jibi wallahi ba wanda ya isa yasan gaibun Allah shine mabuwayi masani mai ilimin da babu wanda ya san iyakar shi Shine yaga ƙarshen mulkin kowa nasa kuma ya gagara aga ƙarshen shi To Allah cikin Ilimin sa da ikon shi da hikimar shi ya ƙaddara ƙaddara giftacciya data ƙullah auren Aliyu da fatima cikin hikimar sa a yau yasa suka kasance to koyaya Wannan lamari ze kasance Muje zuwa Mudai Munsan ƙarya sakina da tawagarta suke Ta Allah ce gaskiya cikin mami ma wallahi ba sakina bace ta zubar daman can Allah ya ƙaddara bama su rayuwa bane kawai taje wajan mashirikai ne suna amfani da Kuɗinta suna gaya mata ƙarya dan su ci kuɗinta amman abin da Allah ya ƙaddara babu mai kawar dashi babu mai hana shi Allah ne yasan mai ya Ɓoye dabai bawa mami ciki tsayayye ba Kuma Bahaushe Yace Rabo idan ya rantse se me shi  rabo dangin ajali ne................
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 50*

Zaro idanu farha take tana jan Numfashi da ƙyar sabida itama adaidai wannan Lokacin zazzaɓin ne ajikinta sedai zafin Jikinsa yafi nata sosai Kuma Jikinsa rawa yake wanda har abin yaso ya bata tsoro, Tinawa tai da addu'ar da Manzon Allah ( S.a.w ) yace muddun mutum nayi babu wanda ya isa ya cutar dashi ƙafa uku ce a hankali ta Lumshe idanunta ta soma karanto addu'ar. Bayan tayi Bisimillah seta soma cewa.
"Bisimillahil lazi layadurru ma'asmihi shai'un fil ardi wala fissama'i wahuwassami'ul Alim"
Cikin azaba take addu'ar Kuma idan tayi haka take tofa masa itama ta tofa har takai ƙafa uku Kuma tana tofa masa taji Yana wata irin karkarwa Yana ƙara shigewa Jikinta a Lokacin ta saka kuka tana cewa.
"Ya Allah! na shiga uku wallahi rabani Biyu zakai nifa ƙarama ce ka bari"
Matseta ya kuma yi Numfashin sa yana fita da wani Irin sauri Kafin ya fara cewa
"Fatima please ki rufeni sanyi nake ji Mutuwa zanyi lulluɓe ni wayyo Allah na"
Farha ta ruɗe tana kuka kuma gashi ya matseta ba damar ta miƙe a haka taji ya dena rawar Jikin kuma jikin nasa ya dena zafin Se saukar Numfashinsa taji a saman wuyanta da alama

bacci yayi awon gaba dashi ta sauke ajiyar zuciya sedai har Lokacin hankalinta bai kwanta ba seda ta tabbatar Baccin sa yayi nisa sannan taɗan sami Nutsuwa Kuma lokacin Raɗaɗin ƙasanta ya dawo Fil amman da tashin hankali ya hana taji Bata iya Motsiba sabida daga ta Yunƙura zata Motsa ze ƙara janyota Jikinsa yana sakin ajiyar zuciya kamar ɗan da uwarsa ta Fita ta barshi agida ta dawo ta tarar yasha Kuka ya Ƙoshi shima haka ya koma mata har asubahi yaƙi sakinta duk kafaɗar ta ciwo Jikinta yayi tsami wiyanta ya Sanƙare sabida rashin Juyi.
Har aka tada sallah a masallaci bai iya tashi ba abin da ya bata mamaki Kenan itama baccin ne ya ɗauketa sabida kwanan datai tana gadin sa dan wani Irin tausayi ya bata dama ai babban Mutum kamar shi ze wuya ya rasa maƙiya dan abun da yayi ya bata tsoro.

A hankali Aliyu ya buɗe idanunshi da sukai masa nauyi sukai jajir Jin kansa yayi yay masa nauyi kamar an ɗaura dutse Yaji bakin sa babu ɗanɗano ko kaɗan da sauri ya miƙe Jin an tada sallah da toilet Ɗinta yay Using ya tsarkake kanshi ya Ɗauro alwala This is the first time dayay Missing jam'in asubahi a rayuwar shi.
Ya shinfiɗa darduma a saman carpet ya data sallah bayan ya saka jallabiyar shi ya jima yana addu'a acikin sujjadar shi.
Shidai baze ce komai ba akan fatima tinda matar shi ce ya Lumshe ido ta cika shi da mamaki ta kai shi wata ƙorama mai cike da ruwa mai sanyi Se yace ta shayar dashi ruwan mamaki lallai dukkan cikar halittar mace baga shekaru take ba a baiwarta take ada ashe kallon Kitse yake wa rogo Har Lokacin Jikinsa bai da ƙwari sabida zazzaɓin daya kwana yana yi sam abin yazo masa sama taka ne ba tare daya tanadi wannan ranar ba har rana ta fito yana ɗakin a zaune yana gadinta Allah yasa yayi wa Ƙofar Key abin da bai taɓa yiba kenan Zaman ɗakin mace Ko mami ita ke Binsa

Ƙarfe takwas daidai farha ta farka da addu'ar tashi daga bacci ta yunƙura da Bisimillah zata tashi Ina Cinya da Jiki suka ce lah inji balarabe, suka ƙi miƙuwa dan azabar da suka ci ta Cije baki tana rintse ido adaidai nan Aliyu ya ɗago ya kalleta aka ci sa'a itama ta kallo inda yake ido suka zubawa juna ita ta soma zare nata sabida Kunyar da take ji tasa.
"Sannu kin tashi?"
Tai ƙasa da kanta bata ce komai ba har na tsayin mintina shima hakan ce ta kasance dan bai iya mata magana ba sabida bai san yadda ake rarrashin mace da bata baki ba.
"Kayi azkar ɗin safe?"
Abin da ta faɗa masa kenan.
Shaf shi mantawa yake da azkar sabida daya tashi uziri ɗauke masa hankali yake rabon da ya tsaya yayi azkar har ya manta Sabida uziri sallah ce wannan baya wasa da ita amman bayan ita baya tsayawa yayi azkar.
Ta kuma cewa.
"Ka daina wasa da azkar sabida faɗin Annabi ne addu'a takobin mumini ce akwai addu'oin da in kayi ƙaryar Mutum ko aljan, Sannan ka dinga yawan sadakar ruwa da Niyyar Allah yay maka tsari daga dukkan sharri sannan ka dinga yawan bawa mutane sadaka kana cewa su maka addu'a saboda yawun wani yafi naka a wajan Allah daga yace Allah yayi yin yake sabida akwai manyan bayin Allah wanda ya ɓoye su batare da ansan baiwar da yayi Musu ba, Nasan kai mai

kyautatawa mutane ne wannan ne ma yasa Allah yake baka kariya sabida ta yuwu ma akwai bayin Allah da kake taimako batare daka sansu ba shiyasa aka ce kada ka raina kowa koka wulaƙanta shi, domin baka san baiwar da Allah yayi wa wani ba Amman lamarin ka ya bani tsoro Allah ya tsareka daga dukkan sharri"
Tunda ta soma magana ya zuba mata ido bako Ƙiftawa kuma adaidai Lokacin data furta azkar ya soma karantowa daka wanda tuni ya haddace shi tun yana yaro har ya kammala ya shafa.
"Allah yayi miki albarka ke kam wace Irin mutum ce, Na wahalar dake na baki karatun da baki taɓa shiga ajin sa ba amman Ba burinki ciwon da Kike ji ajikin kiba Burinki ki tunatar dani abin da ze kareni ya zame min alkairi da zaman lafiya a rayuwata wannan magana ta ƙara Miki Ƙima a idanuna Allah yayi Miki albarka"
Ta sunkuyar da kanta a ƙasa a yadda take jin wutar soyayyar shi A zuciyarta Komai ma zata iya sadaukar masa dan ya zama farin ciki gare shi.

Har ya Miƙe ya ɗagata daga saman gadon tunani take seda yakaita har Toilet sannan ya ajeta ya sunkuya yana taro ruwan zafi ya haɗa sosai A ƙaton bawon dake toilet ɗin.
"Oya shiga Ciki ki zauna naji ance haka ake yi"
Tawani narke Fuska tana kallon ruwan zafin dake Huci.
"Dafa zafi wallahi wannan zafi zeyi salon na ƙone"
Yayi wani kalar murmushi.
"Malama bafa a ƙonewa a wannan wajan Pls ki shiga kona danna ki"
Ta soma dira ƙafafunta kamar yadda yara keyi idan sun so rigima batai aune ba taji ya ɗagata cak ya zare skirt ɗin Jikinta ya dannata cikin ruwan yana cewa
"Wannan shine kwanciyar hankalina"
Runtse idanunta tayi tana jin yadda ruwan ke ratsa ta hannu tasa ta kare Kirjinta dan Lokacin babu kaya ajikinta.
Tsugunnawa yayi a gabanta ya zare hannun data kare Ƙirjin nata dashi, ya ɗora nashi hannun akan tudun ƙirjin nata a hankali yace.
"Gaba ɗaya ƴan gidana sunyi jajir sabida yadda na aikace su ko?"
Ya faɗi maganar da wani kalar salo mai kashe ma'abocin da aka wa shi a hankali taji hucin Numfashinsa adaidai dokin wuyanta kafin taji saukar Ɗumin bakin sa a saman Kirjin nata ya shiga sarrafawa kamar mayunwacin zakin daya sami nama.
Lumshe idanu tayi zaman bawon ya kusan gagararta Numfashi yake fitarwa sama sama ganin ze Loosing control ɗinshi ahankali tace.
"Wallahi ban gama warke ba so kake ka kashe ni"
Lokacin hawaye ya soma zarya a saman fuskarta ya ɗago kanshi a wahale gaba ɗaya idanunshi ya sauya kala.
"Zaki iya wankan?"
Ya faɗa a rarrabe da sauri ta ɗaga kanta alamar eh.
Ya tashi ya fita daga toilet ɗin yana rangaji Wankan tayi ta ɗauro alwala ta dafo bango ta fito ɗakin bata ganshi ba da alamun ya bar ɗakin gaba ɗaya a zaune tai salla dan wahala haka ta rarrafa ta koma gado sabida taga ya sauya zanin gadon taja bargo ta lulluɓa zazzaɓi da ciwon Jiki ne suka rufeta a lokacin ko ƙafarta ta kasa juyawa sabida azaba kamar ma bata shiga ruwan Ɗumin ba haka take ji tai kuka harta gode Allah kafin wahalallan bacci yayi awon gaba

da ita.
_Umm Allah sarki ni kowa yana baccinsa a wannan lokacin niko na zubawa waya ido 1:22 na dare ina rubutu 😢 Allah ka ciyar damu da halak ɗinmu neman halak akwai wiya Allah ka bamu da guminmu kasa mu dogara dakai ka rabamu da bara ko maula a wajan wasun ka ya Rabbil Alamin_

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 51*

Cikin sa'a da nasara ya fita daga ɗakin kuma beci karo da kowa ba a falon Godiya yayiwa Allah daya rufa masa wannan asiri kamar iska zata kwashe shi haka yake tafiya jinsa yake sakayau babu ƙarfi yana zuwa part ɗin sa shima kwanciya yayi wanda bacci me nauyi ya ɗauke shi bashi ya farka ba se wajan 12 na rana yana buɗe ido yaga Mami a kusa dashi a zaune duk fuskarta babu walwala.

Ya kalleta yana yamutsa fuskar shi.
"What do you need?"
Yace mata da muryarshi wadda tayi kala data wanda ya tashi daga bacci idanun shi ya ƙara girma sosai goshin sa duk ya tattare.
Hawaye ne ya zubo mata ta miƙe tsaye tana kallon shi cikin damuwa sosai wadda ta gaza ɓoyeta tace masa.
"Yaya haihuwa nake buƙata bana son na mutu ban sami ɗan kaina ba yaushe ne cikina ze tsaya yaushe zan dena ɓari nima naga ɗan kaina a duniya"
Ta faɗa tana wani irin kuka me tsuma zuciya se Aliyu yace tunda yake ganin kukan Mami be taɓa ganin mai yawa irin na wannan lokacin ba.
Ya ware mata hannayen shi muryar shi a dashe take sabida yanayin baccin daya farka daga shi yace mata.
"come here and be quiet, stop crying like that" a hankali ta faɗa saman ƙirjin shi tana wani irin kuka mai tsuma zuciya ya rungume ta cikin kulawa yake rarrashinta.
"I don't like this cry of yours" ya faɗa yana share mata hawayen dake gudana a saman fuskarta Kwanciya tayi a jikinsa tana sakin ajiyar zuciya cikin rarrashin ta yace mata "I think I am worried about this problem and it is bothering me a lot sedai ba yadda zan yi na miƙawa Allah dukkan lamurana tunda Alhamdulillahi bamu da wata matsala daga ni harke to se mu zuba wa sarautar Allah ido muga yadda zeyi damu"

Ta ɗago tare da kallon fuskar shi.
"Yaya zaka iya samun haihuwa daga wajan wata matar tunda ni ga yadda matsala take zuwar min, sedai zanyi baƙin ciki ga wannan rana da bana fatan tazo min na ganta dan nafi son ni kaɗai na zama giwar ka uwar ƴaƴan ka in sha Allah"

Ya shafa kanta batare daya ce mata komai ba ya cigaba da Gaya mata kalaman kwantar da zuciya tare da dogaro ga Allah Mami taji hankalinta ya kuma kwanciya da kalamin dayayi mata kuma tasan yanzu tana da muƙami  a zuciyar sa.
"Bara nayi wanka duk jikina ciwo yake and ki ɗauko min panadol da ruwa marar sanyi" ya faɗa yana zare ta daga jikin sa ya miƙe ya shiga wankan wanda ya jima acikin Bathroom yana gasa jikinsa da ruwa mai zafi kafin ya fito yana tsane ruwan dake sakko masa daga Jikin sa ya shirya kanshi cikin white trouser and black shirt wanda suka ƙara haska zatin kyan shi tare da fito da ƙarfafan surorin jikinsa ya ƙarasa gaban dressing Mirrow yana feshe Jikinsa da turare mami tayo sallama a ɗakin hannunta ɗauke da maganin da ruwa ta buɗe masa murfin gorar ruwan ta miƙa masa ya amsa yasha ya fita daga ɗakin yabar mami aciki domin gyara masa zata yi.
Ya sauka ƙasa dinning ya nufa ya haɗa tea kaɗan da bread ya zauna yana ci har aka kira sallah yana dinning ɗin Lokacin Mami ta sauko ta gama masa gyaran ɗakin nashi zama tai a gefen shi da alamun yau baze fita ba sabida hira suke sosai har tana tsokanar shi da yau ya tsuke wa zece ma yana da aure yayi Murmushi yace.
"Ba su san ni matana har biyu bane ba"
Mami dariya tayi zaton ta wasa yake mata ya duba agogon hannunshi ya miƙe ya fita ta raka shi har bakin Ƙofa alwala ya ɗaura a famfon dake Bakin shiga part Ɗinshi ya tafi masallaci yayi sallar azahar kowa yau mamaki yake me ya hana oga fita Ya jima zaune tare da ma'aikatan gidan yana sauraran Korafinsu Har albashi seda ya yi musu alƙwarin zasu ga ƙari a ƙarshen watan sannan ya bawa mai gadin shi Kuɗi yace yaje ya siyo Pure water Mota guda ya rabawa dukkan Gidajen dake kusa dasu amman kada yace daga shine sadaka ce yana faɗi ya Barsu suna ta masa Godiya Sashin Ammi ya shiga Lokacin Bashir ze fita Office suka gaisa kona ce Bashir ya gaishe dashi ba yabo ba fallasa ya amsa ya Shiga falon Ammi da sallama da ita da su safna suna zaune A falon yau da alamun ƙafar akwai sauƙi a ƙasan carpet ya zauna yana gaishe da ita su Safna suka gaishe dashi Ya zaro wayar shi yana danne danne da alamun yau baya jin yawan magana ne.
"Baba baka jin daɗi ne?"
Cewar Ammi ya ɗaga girar shi yana cewa.
"Me kika gani Ammi Nikam lafiyata lau"
Tayi Murmushi "Baba kenan kai dai zaka ɓoye min amman naga rashin ƙarfin Jiki a tare dakai"
Ya shafa kanshi "Ammi driving danai from kano to katsina shine na gaji amman ba abin da ke damuna"
Ya faɗa yana Murmushin daya ƙara masa kyau.
"Ammi zan sami farfesun kayan ciki wajan ki?"
Ya faɗa yana kallon ta Ammi taɗan tsuke fuska.
"Muma ba wanda yayi karin kumallon sabida kace Hajja ta daina zuwa waccan yarinyar Kuma tun ɗazu Muke dukan Kofarta taƙi Buɗewa waya sani ma kota Mutu"
Gabanshi yayi wani irin faɗuwa yana fatan kada Allah ya amsa maganar Ammi.
Ammi tace "Sajeeda leƙa ko ƴar gwal ɗin ta buɗe ki taso ta" sam ya kasa magana sabida yadda bakin shi yayi nauyin furta komai har Sajeeda ta Miƙe se rakatan da yayi da ido.
Tana zuwa bakin Ƙofar ɗakin Farha By Lucky ta miƙe ta zare keyn jikin Ƙofar ta shiga toilet sabida yadda ta farka da fitsari da ishirwa ta buɗe Kofar ne akan tana fitowa daga toilet ta fita ta sha ruwa sedai tana fitowa taga sajeeda tana faman kallon ɗakin gaban farha ya faɗi hankalinta

ya tashi da sauri tace wa Sajeeda.
"Lah lafiya me me kike nema?"
Ta faɗa har tana raba maganar tata sajeeda ta taɓe baki tare dajan wani wawan tsaki tare da cewa....................*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 52*

"Nida gidanmu har zaki tambaye ni abin da na zoyi a ɗakin nan? to idan na ga dama wallahi seki kwashe kayan ki, Ki koma wajan Ƴan uwanki masu aiki dabba"
Farha tayi ƙasa da kanta tana jin hawaye na shirin zubo mata amman bata bari hawayen ya zubo ɗin ba ta nufi Bakin gado domin tsaiwar ma gagararta zata yi sabida rashin ƙarfin Jiki da take fama dashi.
Sajeeda ta tako har gaban farha ta ɗora ƙafa ɗaya a saman gadon har tana shurin ta tare da cewa.
"Daga yau in kika kuma barin mu bamu karya ba wallahi sena karya ki shegiya da muni kamar daran Mutuwa jaka Kucaka Kizo Ammi na jiranki Mtsss"
Ta tofa mata yawu a fuska tabar ɗakin Farha dan takaici Kuka ta saka seda tayi me isarta sannan ta Gyara Hijabin nata ta fita daga Ɗakin gudun cin mutuncin Ammi, Aliyu ya sauke ajiyar zuciya hangota da yayi tana dafa bango tana fitowa daga ɗakin nata zuciyar shi rawa take Ji yake dama ya ɗaukota ta dena wannan tafiya yasan tayi matiƙar ƙoƙarin iya ɗauke lalurarshi.
Ammi zuba mata ido tayi wanda yasa Aliyu yaji duk hankalin shi ya tashi a hankali ta ƙaraso gabansu ta zauna tana rintse ido kamar ta zauna a saman ƙaya.
"Ke me kike yi haka da baki ɗora mana abincin karyawa ba?"
Ammi ta faɗa tana binta da kallon Tuhuma.
Tayi ƙasa da kanta bata yarda ta kalli setin da Aliyu yake ba Ammi ta kuma daka mata tsawa!
"Ni sa'arki ce da ina miki magana ma kina min shuru kosu yarana bayin ubanki ne da zasu ɗora miki abincin Eye? to saurara kiji wallahi wannan shine karon ƙarshe da zaki Ƙi dafa mana abincin kinji na gaya miki"
Ita dai Farha har Lokacin kanta yana sunkuye tayi shuru A hankali taji muryar shi yana magana
"Ammi ki mata a hankali baki ga kamar bata da lafiya ba, Bara na saka ayo muku takeaway ko yarannan su dafa ai dama su nace su dinga yi amman ammi kika hanasu"
Farha taɗan saci kallon shi Fuskarshi bata nuna yana da alaƙa da ita ba Magana yake hankalin shi a kwance yana danna wayar shi sedai yau babu wannan ɗaure fuskar ba masifa dan ga ƙannen shinan har sun sami zarafin zama a falon wanda da in yana falon ta lura basa iya zama a ciki sabida tsoron shi.
"Baba nifa ba zan saka su Safna girki ba wallahi bama zan ɓoye maka ba tunda ka dakatar da Hajja to sedai ita ta dinga yi mana Dan bazan ajeta ba aikin fari bare na baƙi ba sannan na ɗauki albashi na bata ƙarshen wata Ɗakunan namu ma yaushe rabon data gyara mana ehe"
Ammi ta faɗa tana Hararar Farha data ƙi ɗagowa ta kalleta Murya a hankali tace mata.
"Ki haƙuri Ammi yanzu me zan dafa muku?"
Ta faɗa kamar zatai kuka.

Da sauri ya katseta da cewa
"A,a tashi jeki ɗaki bara a siyo musu kawai lokaci ya ƙure"
Ta dafa ƙasan tiles ta miƙe tana Cije baki ta bar falon Aliyu yayi wa wani yaron shi waya akan yayo masa order abinci Minti kamar talatin yaron nashi ya kawo abincin Da kanshi ya tashi yaje ya amso Ledojin da abincin ke ciki ya miƙawa Ammi wata daban kuma ya bawa safna yace ta miƙawa Farha ta amsa tana tura baki ta nufi ɗakin daga bakin Ƙofa ta wurga mata Ita kam farha kwanciya tayi tana kuka shiyasa bata ma ji shigowar Safna ba bare tasan abin da ta aikata matan.

Gaba ɗaya tunanin Farha shine yaushe zata sami ƴanci yaushe ze dena ɓoye ita matarshi ce abin da ya ƙara fusata ta shine halin Ko in kula daya nuna mata bayan ko wace mace idan ta tsinci kanta a ƙwaryar manya Mijinta yana tsayawa ya riritata ya kula da ita amman ita jiba yadda ya barta kamar ma ya manta abin da ya aikata mata tabbas maganar daya faɗa mata gaskiya ce daya ce mata baya son ta da gasken yake don inda yana son ta baze taɓa yi mata haka ba.

Ammi ta dubi Aliyu cikin faɗa.
"Amman baba me yasa zaka min haka? damu da ita ɗaya ne?"
Ya haɗe rai sosai ya watsawa su safna Mugun kallon daya sa suka miƙe jikinsu na ɓari suka bar wajan ya dubi Ammi har Lokacin Fuskar shi babu walwala.
"Ammi menene abin nuna fifiko ga wanda baka san waye a wajan Allah ba? danna ɗauka mata abinci acikin naku shine matsala to Ammi ki haƙuri Da laifin dana yi"
Ta hayo masa ka da maganarta mai ƙarfi.
"Naga fa abun naka yayi yawa ga Kitchen nan tazo ta girka nata mana dole abin da muka ci shi zata ci salon raini ya shiga tsakanin mu to wallahi ka kiyaye ni Ka shiga taitayin ka ka kama kanka ka fita daga sabgar yarinyar nan tun kafin na saɓa maka"
Ya rasa me yasa Ammi ta ƙi jinin fatima kuma de yarinyar ba rashin Kunya takewa Ammi ba amman baki ɗaya ammi tabi ta tsaneta ya fuskanci har yaran Ammi su safna ma sun Tsaneta.
"Ammi bazan kuma ba ki haƙuri"
Ya faɗa cikin mutuwar Jiki Ammi ta kauda maganar tana cewa.
"Niko me akaiwa Mami ne tunda ta dawo bata shigo Min ba nida ɗazu ma zanje naji lafiyarta"
Ya taɓe baki tare da cewa.
"Nima ban san meya hanata zuwa nan ɗin ba duk tabi ne ta damu kanta akan rashin haihuwa ɗazu ma kuka ta gama yi maybe ko wannan matsalar ce data ɗora damuwarta akai yasa ta ƙi shigowa kin san wani in yana cikin wani yanayi baya shiga cikin mutane"
Ammi tace
"Haka ne ai ba ita kaɗai ba kowa ma burin sa ai ka haihu kaima muga naka ɗan Allah dai ya nuna mana wannan rana in kaje ka turon ita nai mata nasiha"
Ya jinjina kai yana cewa.
"Da aure da haihuwa da mutuwa duk Lokaci ne Allah ya bamu waɗanda zamu iya dasu shi kuma Allah ya iya mana gaba ɗaya Kuka ai bashine ze bata ƴaƴa ba Allah ne mai badawa Ammi ina son haihuwa amman wallahi bana ɗagawa kaina hankali akanta dan nasan daga Lokacin yayi Allah ze bani"

Ya faɗa yana Lumshe ido.
Ammi cike da tausaya mishi tace.
"Haka ne baba Nina sanka akwai tawakkali In sha Allah mami zata cika maka gidannan da ƴaƴa masu Kyau irin ka harma da biyayyarka"
Yayi Murmushi yana shafa kai bai dai ce Komai ba.
Miƙewa Ammi tayi "Bara naje nai wanka naci abinci ka ƙaraso daga ciki mana naga kamar yau ba zaka fita Office ba"
Ya bita da ido be magana ba sabida yadda ya matsu ta tafi yaje Inda zuciyarsa take muradi...........

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 53*

Sakin ajiyar zuciya yayi mai ƙarfi lokacin daya tabbatar Ammi ta ƙullewa ganin sa a hankali ya miƙe tare da nufar ƙofar ɗakin yana murɗa handle ɗin yaji ta a buɗe ya shiga ya sanya key ya rufota yabar key ɗin ajiki a tsaye ya tsaya a kanta hannunsa duka a cikin aljihun trouser ɗinshi kukanta yake sauraro wadda ita sam bata ma san da shigowar shi ɗakin ba, Sannu A hankali ya zauna a gefen gadon yasa hannun shi ɗaya ya tallafe Fuskarshi dashi gaba ɗaya jikinsa yayi sanyi da yadda yaga lamarin nata har Kusan minti ashiri yana zaman jiran ta gama kukan suyi magana ganin bata san yana wajan ba yasa ya matsa Kusa da ita ya janyota jikinsa.

Idanunta har lokacin a rufe suke kuma se ƙoƙarin tashi daga jikin nashi take sedai yadda yabi ya kanainaye ta ya kasa bata damar Miƙewa.
"Shiii fatima, wai meye haka kukan ya isa haka kada kanki yayi miki ciwo"
Ya faɗa yana share mata hawayen nata da tafin hannunshi.
Juyawa tayi ta dena kallon saitin Fuskarshi yayi Murmushi.
"Au wai kukan nawa ne, To naji nayi laifi amin afuwa bazan kuma ba"
Ya faɗa sanda yake ƙoƙarin Juyo da ita facing ɗinshi ya taɓa wuyanta akwai zazzaɓi sosai ajikinta Miƙewa yayi bayan ya sauketa daga jikinshi ya koma toilet ɗin ruwan ɗumin ya kuma haɗawa ya dawo ya ɗagata cak shiya taimaka mata wajan rage kayan dake Jikinta duk Kunya ta gama kamata haka ya kuma dannata acikin ƙaton bawon dake shaƙe da ruwan Ɗumi ta jima aciki shikuma yana tsaye a kanta seda ya sauya mata ruwan har sau uku sannan ya ɗaukota suka fito cikin ɗaki saman gado tahau tana rawar ɗarin zazzaɓi ya ƙarasa gaban kayanta ya ɗauko mata Doguwar riga da ƙyar ta yarda ya saka mata.

Ya sunkuyo daidai Fuskarta cike da tausaya mata.
"Me zaki ci yanzu ina Break fast Ɗin da safna ta kawo Miki?"
Ta zubo da hawaye.
"Ni bazan ci komai ba bakina ma kwata kwata babu daɗi"
Ta faɗa tana jan Bargo ta rufe duk Jikinta.

Ya ƙarasa inda takeaway ɗin take yashe ya ɗauka Doya ce aciki da ƙwai ya tabe baki ya aje a saman Madubi ya fita daga ɗakin tare da rufota da Key gudun kada wani ya faɗa mata yaga halin da take ciki.

Mota ya shiga bayan ya saka face mask ya boye Fuskarshi da kansa yaje ya siyo mata ɗan abinda zata ci marar nauyi ya karɓo mata magani a pharmacy bayan yayi wa likita bayanin halin da take ciki Lokacin daya ƙaraso ana kiran sallar la'asar seda yayi sallah sannan ya wuce koda ya ƙarasa falon Ammi su safna na dinning suna cin sauran abincin ɗazu dan ba'ai girkin ba Ammi Kuma tana ɗakinta ya zauna a falo ya wayance da danna waya ganin yanayin sa yasa suka Miƙe har suna rige rigen barin wajan ya Tashi ya nufi ɗakin farha ya buɗe ya shiga ya rufo Ƙofar tana zaune ta idar da sallah a gabanta ya tsugunna bayan ya aje kayan hannun shi ya taɓa Goshinta yana cewa.
"Yaya yanayin jikin naki?"
Ta ɗan kalle shi gaba ɗaya taga ya sauya mata duk Jikinsa a sanyaye har faɗawa idanunshi taga yayi.
"Da sauƙi Alhamdulillahi"
Ta bashi amsa bayan ta kawar da kanta dan gujewa mayen kallon da yake faman binta dashi.

Ya Buɗe Ledar hannun shi ya fito mata da robar farfesun Kayan cikin rago da soyayyen dankali se kaza Wadda aka gasa mai romo se shinkafa da miyar hanta gaba ɗaya ƙamshin abincin ya cika ɗakin ya zauna a gabanta ya tanƙwashe ƙafafun sa.
"To wanne zaki ci anan Nasan baki ci Komai ba"
Ta lumshe idanu sabida yadda yayi mata maganar cikin kulawa yayi mata ita.
"Shinkafar nake son ci dan yunwa nake ji sosai"
Ta faɗa tan haɗiyar yawu.
Yayi Murmushi.
"Farfesun fa?"
"Shima zanci duka"
Ya ɗauki ƙaramin spoon ɗin cikin abincin ya buɗe robar yana ɗiba yana bata a hankali ta Noƙe taƙi amsa yaɗan harareta da sauri ta amsa tana ci tun tana jin kunya harta ware tana cin abincin ganin ta soma ƙoshi ya tura mata farfesun gabanta wannan karon da kanta taci Kuma taji daɗin bakinta ruwa ya buɗe mata tare da magungunan daya amso mata duka na gajiya ne da rage raɗaɗi ta amsa tasha zata kwanta ya hana yace ta bari abincin ya narke turo baki tayi ta juya masa baya itafa ya soma isarta haka ya hanata ta kwanta seda yaga ta soma bacci a zaune sannan yace taje ta kwanta aiku nan da nan bacci ya ɗauketa wanda bata samu a daran Jiya ba Ƙarfin Fanka ya ƙara mata sabida Ac'n ɗakin ta lalace ya tattare kayan abincin ya aje a gefe ya Rufe mata rabin Jikinta ya fita daga ɗakin bayan ya rufo shi.

Cikin gidansu mahaifin shi ya je Kuma ya sami ƙannen Babansu duka a gida zama yayi suna gaisawa Kuma da alamun sunji daɗin zuwan nashi nan da nan yara da manya sukai ta fitowa suna Mishi sannu da zuwa matan kawunan shi suka fara jere masa kwanukan abinci agaban shi ruwa kaɗai yasha ya fuskanci Hirar da Baba usman keyi masa.
Wadda Godiya yake masa akan hidimar da yake yi musu yaɗan yi murmushi.

"Baba kada ka kuma yi min godiya ai in ban yi muku ba wa zan yiwa Kune fa kuka fito ta tsatso ɗaya da mahaifinmu wallahi Ku nakewa kallon Baba a yanzu"
Albarka suka haɗu suna sanya mashi acikin Gidan sukai sallar magariba wadda Baba Usman yaja su bayan sun idar ganin ba wata matsala a gidan Komai suna da dan hatta sola ya sanya an Musu ko ina haske ga gida yasha gyara.
"Baba zan koma ko akwai wani abun?"
Baba Usman yayi Murmushi
"Haba Aliyu ba komai wallahi dan kayan abincin da ka sa aka cika mana store dashi ko rabi bai ƙare ba Komai akwai shi Alhamdulillah"
Sauran ma suka haɗa baki wajan yi masa godiya ya fita ya shiga Gidan kawun su Ammi nan ɗin ma yaɗan jima dan har isha'i yana cikin Gidan yana fitowa yayi sallah ya koma Gida ya shiga Mota ya kuma siyowa farha abinci da fruit, A mota yabar su seda Ya shiga Part Ɗinshi yayi wanka ya sauya kaya dan duk wanda ke Jikin shi sun dame shi ya sauko ƙasa Mami ya tarar zaune Cikin shiri da ƴar ƙaramar akwati a gabanta.
"A,a mamy lafiya na ganki kamar me shirin Fita wani waje?"
Kuka ta ɗan ƙaƙalo mai sauti.
"Mama ce ta faɗi a napep shine zanje dubata ƙila ma na kwana tunda Ta bugu sosai"
Ya zauna yana cewa.
"Subuhanallahi garin yaya yaushe hakan ta faru?"
Ta goge hawayenta tana cewa.
"Ɗazu nan Hassana take gaya Min gashi suma basa gida suna Ƙauye ita ma Amir ke gaya musu dole Ni zani na kwana dama kai nake jira kazo"
Ya kalleta.
"Ita ma dai ina motar dana bawa Amir ɗin nace ya dinga kaita Unguwa ya kamata ta daina hawa Motar haya"
Mamy da sauri tace.
"Ai ta lalace Motar"
Ya Haɗe fuska"Shine baki gaya min ba me yasa?" ta kama wasa da yatsunta don motar Tuni sun siyar sun Miƙawa Bokaye  Kuɗinta
"Ok Next week Musa ze kai musu wata Kije driver ya kaiki Ki mata sannu kafin nazo Musa ze kawo Muku saƙo Gobe"
Godiya ta fara yi masa ya ɗaga mata hannu dan baya so ta miƙe ta fita daga falon Driver ta kira ya tafi kaita Gidan nasu.

Ya miƙe bayan fitar Mami Saman shi yahau ya gama abin da zeyi ya rufo Ɗakin ya kashe hasken Falo har na ƙasa ya Rufe falon ya fita daga part Ɗin Ya je Mota ya ɗauko abin da ya siyo ya shiga Sashin Ammi ba kowa a falon dama basu fiye zaman falo ba Haka ya Shiga wajan Farha ya rufe Ƙofar ya kunna hasken Ɗakin..................*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 54*

Tana ta baccinta har Lokacin ya aje ledojin hannun shi ya ƙarasa gefen gadon ya zauna bayan

ya zaro wayar shi daga cikin aljihunsa wadda ke faman yin ringing!
Momcy ce matar Marigayi Alhaji Hamishi uban gidan shi rejecting ɗin kiran nata yayi shi ya kirata.
"Assalamu alaikum"
Ya faɗa daga ɓangaren Momcy ta amsa cike da damuwa.
"Wa'alaikassalam, Aliyu baka samu ka shigo ɗin ba kuma ina ta jiran ka"
Ya shafa kanshi kwata kwata ya manta.
"Ki haƙuri in sha Allah zanzo na manta ne"
Momcy tace masa.
"Dama nasan ka manta ne dama maganar Hanan ce"
Aliyu yace.
"Ina sauraron ki ko dai sena zo ɗinne?"
Momcy tayi saurin cewa.
"A,a bari kawai na gaya maka, Yau kwana biyu da Hisba ta kamasu a Wani gidan shaye shaye ita da ƙawayenta dama shine wayar da nake ta yi maka Amman Alhamdulillahi Mijin Hasina yaje da ƙyar suka bada ita"
Aliyu yaji ya kaɗu da wannan magana wato har iskancin Hanan yakai haka.
"Innalillahi wa'innah ilaihirraju'un Allah ka shirya mana zuri'a ki haƙuri kada ki mata baki dan Allah addu"a kaɗai zamu yi mata"
Momcy ta fashe da kuka tana cewa.
"Ina wa Allah godiya daya bani Hanan Amman wallahi lamarin ta ya isheni dama zata mutu na huta"
Da sauri ya katse ta da cewa.
"Kada ki ƙara faɗin haka domin Kamar Kin gaji da jarrabawar Allah ne dan hanan jarrabawace gareki Kuma in sha Allah komai ze zamo labari"
Da sauri momcy tace.
"Aliyu yaushe wannan labari zezo kwata kwata na rasa halin wata ɗauko yarinyar nan mahaifinta Mutumin kirki ne kowa yabon sa yake wallahi Hanan bata yo halin mu ba"
Aliyu yayi murmushi me ciwo kafin yace.
"Momcy sedai ki haƙuri, Tun asali kece da laifi domin Kin sakarwa su Hanan batare da kina kwaɓar su a matsayin ki na uwa ba, Sau tari zanzo gidan Hanan tace Miki zata fita baki taɓa tambayarta ina taje ba Sau tari zaki ganta da ƙawa baki taɓa cewa ina ta samo wannan ƙawar ba sau tari zata fita school baki taɓa Bibiyarta a makarantar ba, Sannan kuma da mahaifinsu ya rasu mai yasa zaki damƙa Musu dukiyar mahaifin su batare dakin saka wani na juya musu ba to Kinga duk ire iren waɗannan Abubuwan sakacin daga wajan kine dama in uwa bata saka ido akan ɗanta irin hakan tana faruwa"
Ya faɗa a hankali.
Kukan ta cigaba dayi domin dukkan maganar shi akan tsari take.
"Haka ne Aliyu Amman yanzu ina kan gyara kai dai ka tayani addu'a"
A tausashe yace.
"In sha Allah ina hanan ɗin bani ita"
Momcy ta miƙawa Hanan wayar.
Shuru Hanan tayi tana hararar wayar.

"Nasan kina jina ko to wallahi Ki shiga hankalin ki kuma lallai acikin ƴan iskan mazan da kike bi ki gaggawar fito da Mijin aure in ba haka ba sadaka zan bada ke Sakarai marar tunani"
Kashe wayar yayi yana jin zuciyar shi babu daɗi bai so wannan ƙaddara ta faɗawa ƴar gidan mutumin arziki kamar Alhaji Hamishi ba.

Tunda ya kunna hasken ɗakin ta farka sedai tai shuru ne sabida tsoron haɗa ido take dashi Musamman daya shigo mata adaidai irin wannan Lokaci Rawar Jikin tace ta ƙaru.
Ƙara kasa kunne tayi lokacin da taji yana wayar ta rasa dasu wa yake wayar wadda tasan bada ƴan gidansu bane Jitai ta damu data san wacece Hanan ɗin data ji ya ambata tunda sunan matar shi Mami.
To wacece hanan meye halaƙar shi da ita da har yake zaƙewa akan lamarin yarinyar.
Taɓe baki tayi a zafafe ta tashi ta dira daga saman gadon toilet ta shiga wanka tayi sabida taji ƙarfin Jikinta ta ɗauro alwala ta fito har Lokacin yana zaune yana danna wayar shi ta sauya kaya a toilet ta fito fuskarta a ɗaure ta shinfiɗa darduma ta tayar da sallah ta idar ta miƙe ta tsaya a saman kanshi ganin bai da Niyyar magana.
"Ka tashi ni zan kaɗe gado na kwanta"
Ta faɗa tana hararar shi.
Bai kulata ba se ji tai ya janyota jikinsa ƙamshin turaren shi ya cika hancinta ta Lumshe ido gabanta yana faɗuwa.
Ya ja hancinta yana aje wayar shi a gefe.
"Fatima sarkin tsiya to anan zan kwana"
Zaro ido tayi tana Jin ƙirjinta yana mata wani irin duka da ƙarfin gaske.
Kafin ta aro jarumtar furta masa.
"Nidai kai tafiyarka dan Allah bana son kwana da Mutum a kusa dani"
Murmushi yayi tare da cewa.
"Sabida me bayan ni bargo zan zame Miki daman yau Garin sanyi ake"
Da sauri tace.
"A,a wallahi zafi ake shiyasa ma nake son kwana ni kaɗai"
Bece mata komai ba ya sauketa daga Jikin shi ya ƙarasa inda ya aje ledojin ya ɗauko su.
"Oya sauko kici abinci ki sha magani"
Turo baki tayi yadda taga fuskarshi babu walwala ne yasa ta sauko ya tura mata Doyace soyayya da miyar kifi se kayan marmari shikam kankana taga yana sha ta ɗan tsakuri Doyar taci Kifin sosai dan ya mata daɗi Miƙewa taga yayi ya shiga Toilet ya jima kafin taga ya fito a gaban Wardrobe taga ya tsaya ya tube jallabiyar jikinshi Daga shi se Gajeran wando ya ƙaraso gabanta taga ya wuce gado ya kwanta Jikinsa duk gashi ne Musamman Kirjinsa Jikinta ne yahau rawa bata taɓa ganin namiji babba a haka ba da ƙyar ta wanko bankin ta da hannunta tana fitowa ta ganshi zaune da alamun Jiranta yake Fisgo hannunta yayi ya ɗora ta a saman Ƙirjinsa ya lalubi Makunnin ƙwan ɗakin ya kashe duhu ya cika ɗakin Laluben Rigarta taji yana yi har ya sami nasarar Cilli da rigar ita dai zaro ido take sabida tsabar Tsoro Gaba ɗaya jitai ya gigice se faman Yamutsa mata Jikinta yake da zazzafan salon shi ya ɗora Harshen shi a dokin wuyanta yana cigaba da ruɗa  ta da salon shi Wani irin baƙon lamari taji a dukkan sassan Jikinta Lokacin daze ɗauki hanyar shi Riƙe shi tayi da ƙarfi hawaye take saki wanda har ya jiƙa masa Kirjinsa.

"Please ban fa warke ba dan Allah kai haƙuri"
Ta faɗa muryarta tana rawa.
Cikin maye da shauƙin wajan taji yace.
"Ummmm zaki ƙara samun goge wa ne a wajan Plsss ki barni"
Daga haka wata irin damƙa yakaiwa Tudun kirjinta yana ruɗa mata Jikinta a hankali ya haɗesu suka zama abu ɗaya Kuka take yana sanya harshe yana Lashe mata hawayen har majinar tata ma haɗiyewa yake shi kaɗai yasan a wata duniya yake gaba ɗaya ya manta kansa ya manta tunanin sa se ita kaɗai yake gani acikin duniyar shi ita ko tun tana kuka har hawayen ma yazo ya dena zuba a hankali taji Kuma ta ɗan dena Jin azabar da take ji dan ba kamar Jiya ba yau bai sarara mata ba se tsakiyar dare kuma ya takura mata sesun yi wanka a daran kuka ta saka masa tace ita duk Jikinta ciwo yake mata bai saurare taba ya ɗagata cak zuwa Toilet shi yayi mata wankan yabarta tai na tsarki suka fito Ita dai bacci ne ya sace ta shiko gani tayi yana ta sallah har zuwa asubah yana kan sallaya seda aka shiga masallaci ya tasheta shikuma ya fita a daddafe tayi sallah dan bacci ne akanta sedai wajan ƙarfe shidda bawan Allah ya ƙara lallaɓo mata da wata sabuwar Fitinar dan cewa yayi se yayi kafi shayi daɗi, wannan karon kuka take tana masa magiya baiwar Allah zuwa safiya tayi wujiga wujiga duk ta ƙara komawa ƴar firit wanka tayo ta koma baccin Gajiya ta barshi a zaune yana waya daga ji da ɗan uwan shi yake wayar ranar kusan a ɗakinta ya wuni motsi kaɗan zece mata Menene Abinci kaɗai ya fita ya siyo musu se Sallah ya kuma Kullo kofar ita har mamaki take ina su Ammi sedai data tuna ba mazauna falo bane setaji ta dena mamakin.
Haka zalika daran wannan ranar ma Farha seda ta kira kaf ƴan gidansu dan Aliyu bai mata ta sauƙi ba kwanan shi Uku a ɗakinta sallah siyo abinci ke fitar dashi dan ta lura baya fita Office shi har ƙiba yayi ita ko se rama kuma babu wani daga cikin Mutan gidan daya zo mata bakin Ƙofa ita ko a falo ma bata jin Motsin su.
Aliyu dubara yayi wa Ammi akan cewa Ze dinga siyo musu abinci abar hajja ta Huta idan yarinyar taji sauƙi zata komo dafa Musu Ammi dama bata fiye son kallo ba kullum tana ɗaki Su safna suna school magariba ke kawo su gida,Hajja bata shigowa yanzu sabida bata da girki se masu gyaran falo kaɗai daga sunyi suke fita  bashir Kuma ya tafi lagos ganin wasu Motoci ga mami bata nan wanda Aliyu tunda ya aika musu da musa ya kai musu Kuɗi be ƙara bi takan su ba wayarshi ma kasheta yake kwanan shi uku yana more sadakin sa.
A rana ta huɗu ne mami tayi masa waya akan zata dawo da daddare yace mata ta bari zezo ya ɗaukota daga nan ya duba mama dan ko Ammi be gayawa ba.
Ranar daya zo wa farha sallama akan ze tafi wajan uwar gida Har ƙaramar rawa tayi sabida tsabar Murna wadda har yaso ya gano.
"Kin san dai sati ake wa Budurwa to zan dawo na ƙarasa kwana huɗu na"
Da sauri tace masa.
"Na yafe wallahi"
Murmushi yayi ya lakace mata hanci ya fita yana jin yana Missing ɗinta dan ta shayar dashi ruwan mamakin Ni'imarta.
Ta bisa da kallo yaci kwalliya kamar zashi zance mayar da kanta saman Pillow tayi ta kwanta yau zatai bacci mai tushe tunda yazo mata a kwana ukun da yayi kusan ajikinta yake wuni da daddare ma haka shiyasa tana sallar Isha'i ta kwanta se bacci.

Aliyu kuwa gidan su mami ya nufa acikin Motar shi domin ya ɗaukota.

Mami kuwa dama ashe..................

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 57*

Ya ɗaga handbag ɗin ya zazzage ta tsaf sega ƙullin ƙananun magani nan ya faɗo ya zaro ido yana dubawa Maganine sedai yayi kala kamar ta curry maganar maman mami ke mai amsa kuwa a cikin kunnen shi inda take jaddadawa mami cewa ki tabbata kin zuba taci ta sheƙa garin da ba'a dawowa gaba ɗaya ya shiga tunanin dawa suke tunda bai ji suna ba sedai ga magani kuma ya gani to koda Ammi suke No! Yadda Ammi take Musu yasan ba yadda za'ai su Nemi rayuwar Ammi gaba ɗaya jiyay komai ya sire masa lallai Mutum abin tsoro ne ko a fuska bai taɓa kawo mami kiyashi zata iya ɗaukar ran shi ba bare kuma ɗan adam mai daraja Hankalin shine ya kuma tashi Lokacin daya tuna Furucin Mami na zata dinga zuwa sashin Ammi suna cin Abincin tabbas Ƙudirin Kisan akan Ammi yake Ko akan ɗaya daga cikin ƙannen shi Ya ɗauki jakar da maganin ya shiga Kitchen Curry ya duba ya tsaya yayi masa ɗauri kamar na maganin ya zuba a jakar Shi kuma maganin ya wurga bayan Kitchen Ɗin ta inda Bishiyu suke ya kashe hasken Kitchen ɗin ya koma ya aje mata jakar yadda take seda ya daidai ta kanshi sannan ya koma ɗakin shi sedai gaba ɗaya Ɗari ɗari yake da Mami abu ɗaya ne ya hana shi ya tunkare ta da maganar rashin cikakkiyar sheda sedai yasha alwashin zeta Bin diddigi har ya tara evidance ɗin sa, Wanda ze iya tunkarar Ammi dashi dan yanzu yasan Ko giyar wake yasha Ammi ba zata kama abin da ze gaya mata ba dan yaga alama akan su Mami bata ji bata gani, Sedai yasha alwashin Tsayawa da saka ido akan Motsin mami dan karta Cutar dashi da mahaifiyar shi.
Ya ƙarasa bakin gado ya zauna wayar shi ce take Ringing mami ta ɗora kanta a saman Cinyarshi jiyay kamar ta zuba masa Wuta amman haka ya danne yana shafa kanta ya ɗaga wayar Bashir ne...........

"Kai meye haka waya da wannan tsohon dare?"
Bashir kamar ze kuka! daga ɓangaren shi yace.
"Dan girman Allah yaya gobe na dawo gida wallahi na saba da kano"
Aliyu yayi Murmushi da biyu ya tura Bashir lagos kuma ko ze yi me baze dawo dashi a wannan Lokacin ba.
"A,a Ka bari ka sami kamar wata Uku acan seka dawo"
Ƴar ƙara bashir ya saki yana daya sanin tafiyar da yayi dan Ko kaɗan Aliyu bai ce masa ze jima haka ba ce masa yayi yaje yaga wasu Motoci wanda yana zuwa sadik ke gaya masa ai Aliyu yace yazo kenan seya kwana biyu ze koma kano.
"Yaya akwai tarin abubuwa a gabana wallahi ka daure ka barni na dawo pls"
Aliyu ya ja tsaki tare da cewa.
"Duk yadda kayi Bashir nidai na gama magana"

Ya kashe wayar yaja mami jikinsa ba jimawa bacci yayi awon gaba dashi da asubahi ya miƙe ya shiga toilet yayi uzurin gaban shi ya tafi masallaci tafiya ce ta dole ta taso masa a yau wadda zeje lokoja ne sabida wasu Motoci daya tura an sami akasi kuma motocin suna da yawa to dole se yaje dan gano matsalar data faru wanda sam bai san da zancen ba se ɗazu Mutumin daya turawa Motar yayi masa waya lokacin yana gab da shiga masallaci Yanzu ma haka wayar ya tawo suna yi da Mutumin wanda yake siyan Motoci wajan Aliyu shima ya saida acan agurguje ya shirya cikin farin yadin Tissue wanda hatta singlet Ɗinsa ta ciki ana iya hangowa ya shirya kayan sa cikin ƙaramar Trolly ya Dubi mami data koma bacci Lokacin har ya ɗauki Trolly ɗin tashi.
Ya bugi Pillown da ta ɗora kanta a saman shi ta buɗe idanunta fal bacci.

"Kinyi sallah kuwa kike wannan baccin?"
Ta mutstsika idanunta tana gyaɗa masa kai alamun tayi ya duba agogon  hannun shi.
"Ni zan tafi airport Lokoja tayi kira yadda ta yuwu ban san ranar dawowa taba ko zan daɗe ko bazan daɗe ba"
Mami ta miƙe zumbur se Kuma ta sauya fuska.
"Yaya lokoja kuma amman baka gaya min ba se yau?"
Yayi Murmushi.
"Nima ban san da tafiyarba taso min tai yanzu zanwa Musa waya yay Min booking jirgi zan shiga part ɗin ammi muyi sallama"
Daga haka ya juya yabar ɗakin Mami kwanciyarta ta koma taja bargo sabida har Lokacin gajiyar Nijar bata sake taba gashi garin akwai sanyi da iskar asubah tunda Lokacin gari bai gama wayewa ba.
Falon Ammi shuru hatta ƙwan falon a kashe yake ya shiga ɗakin farha bayan ya sanya key ya buɗe ya kunna ƙwan ɗakin haske ya gauraya tana Ƙudundune cikin bargo baccin ta take lakadan ya aje jakar hannun shi a ƙasa ya yaye mata bargon yaɗan Bugi Gefen Pillow ɗinta juyowa tayi tana facing ɗinsa har Lokacin bacci take babu alamun tayi sallah ma.
"Fatima tashi mana Kin makara a sallah"
Sama sama taji Muryarshi baccin yayi mata daɗi amman yadda ya takura ta da Kiran sunan ta yasa ta Miƙe tana hamma ta Shiga Toilet tai alwala ta fito ya shinfiɗa mata darduma ta tayar da sallah tana zaune ya ɗan Dubeta bayan tayi sallama.
"Ni zan tafi Lokoja ban san yaushe zan dawo ba"
Se Lokacin ta ɗago ta kalle shi kafin tace masa.
"Allah ya kiyaye hanya ya tsare ya bada sa'a"
A ƙasan laɓɓansa ya amsa mata da Amin yaɗan ƙanne ido guda ɗaya.
"Me zaki bani wanda zan tafi da tunanin shi wallahi a takure nake"
Bata gano maganar tasa ba tace masa.
"Nida ba fita nake ba dana siyo maka koɗan turare ne"
Yayi Murmushi mai sauti kafin ya sauko ya jera kusa da ita ya zauna har kafaɗun su na gogar na juna.
"Nifa ba wannan ba ke nake son kin gano ai"
Ya faɗa yana mata wani ɗan iskan kallo.
Maƙe kafaɗa tayi tana turo baki.

"Ni wallahi na gaji Kullum abu ɗaya kamar Cin tuwo"
Miƙewa yayi ta saki ajiyar zuciya zatonta ma Tafiya zeyi sedai ga saɓanin hakan taga ya hau cire kayansa yana ratayewa ya rage daga shi sai gajeran wando tana kuka tana magiya haka ya ɗagata cak Tun a bakin gado ya soma sauya Salon shi har sanda ya direta a tsakiyar gadon yayi mata rumfa da Jikinsa Ya haye mata ruwan cikinta Zaro ido take tana jan Numfashin dake barazanar ɗaukewa ya sunkuya daidai fuskarta ya zira harshen sa cikin nata ya kama harshen nata yana tsotsa kamar alewa kafin Kiɗan nashi ya sauya rawa ya jima cikin tafkin duniya ta daban kafin ya sami Nutsuwa ya ɗagata cak zuwa toilet da kanshi yayi mata wanka shima yayi se kawar da Fuska take shiko ko ajikinsa haka ya fito da ita dan Rigima har mai ya shafa mata a wajan shafa man ma seda yaja magana ya taimaka mata ta sanya kaya ya wani langwaɓe yana Furta mata zeyi missing ɗinta a zuciyarta tace zadai kai Missing Jikina dan ba sona kake ba haka ya tafi Bayan yayi mata gargaɗi akan kada ta yadda taci abincin kowa a gidan Indai ba na Hajja ba duk abin da take so ta shiga Kitchen tayi amman daidai da ruwa kada wanda ya bata tasha Ita har mamaki furucin nasa ya bata Shiko yayi haka ne sabida sam bai yarda da Mami ba.

Tana ji tana gani ya fita se kuma taji duk ba daɗi gaba ɗaya ya bar mata kewarsa da Ƙamshin turaren shi mai kashe jikin mutum gyaran ɗakin nata tahau yi ta wanke Toilet ta fita falon Ammi ta shiga Kitchen tahau Fere dankali dan haɗa musu abin karyawa wajan ƙarfe taran safe tana Tsaka dayin Miyar source wadda za'aci dankalin da ita Ƙamshin turare na daban yayi mata sallama kafin taji sallama acikin Kitchen Ɗin ta ɗaga kanta a hankali tana amsa sallamar data ji ana yi ɗin.............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 58*

Suka haɗa idanu da wannan farar matar siririya ta jiya wadda take zaton ita ce matar shi kawar da kai Farha tayi tana ƙoƙarin kashe Gas ɗin mami ta saki murmushi mai sauti tare da ƙarasowa gaban farha tana cewa.
"Ƙanwata har kin gama haɗa Break fast ɗin kenan?"
Farha tana zuba Miyar cikin wani ɗan ƙaramin flaks a taƙaice tace
"Ehh na gama, Ina kwana"
Mami ta soma buɗe kayan abincin tana leƙa ko wanne cikin mamakin yadda yarinyar ta iya girki.
"Kinga jeki falo ki ɗauko min wayata Please"
Cewar mami wadda Ƙullin ƙaramin maganin ke hannunta farha tayi Jimm kafin ta fita wanda tana fitar mami tai saurin kunce ɗaurin maganin ta zuba cikin miyar source ɗin ta juya ta rufe Farha ta duba bata ga wayar ba ta dawo mami ta gyara tai kamar batai komai ba cikin Ladabi tace mata.
"Ni banga waya ba"
Mami tace.
"Okey Muje na taimaka miki Mu jera break ɗin" a tare suka dinga miƙa kayan dining har suka kammala Ita dai farha Komawa kitchen tayi ta tattare komai data ɓata sannan ta ɗauki nasu

abincin ita da Hajja ta fita taje can ɓangaran su Hajja ɗin dan rabonta da wajan Hajja yau kwana huɗu dan natau ya nace a kwanakin nan shine yasa bata ga hajja ba da sallama ta shiga ɗakin Hajja wadda take ta faman Ninke kayan sawa.
Hajja ta washe baki tana cewa.
"Ni ai nayi fushi dake Shikenan dan ina hutu seki ƙi zuwar min fatima sam Kin Ɓuya kamar bakya gidannan har naje ƙauye na dawo"
Farha ta zauna tana cewa

"Ki haƙuri Hajja banji daɗi bane nima ina kwance ina kwana?"
Hajja taɗan sauya Fuska cikin alhini tace mata.
"Lafiya lau, Meke damun ki ai ban sani ba ga tsarabar ƙauye na tawo miki da ita ɗazunnan nagama cewa zan leƙa ki"
Hajja ta faɗa tana Miƙowa Farha baƙar Leda mai goriba dasu tsamiyar Biri da gyaɗa mai Gishiri aciki Da murna farha ta amsa tana Godiya Tare da cewa.
"Hajja ga abin kari na kawo Miki ke nasan yanzu Hutawa kike"
Farha ta faɗa tana dariya.
Hajja tace mata.
"Ke rabu da wani Hutu nifa na riga na saba da motsa Jiki ɗan zamannan jikina har ciwo yake bana komai fa shiyasa tun asali da hajiya ammi tace bazan komai ba nace mata a,a ko girki ne nidai zan keyi ai da wannan Ɗakin naki shi aka bani nice naki nafi son wannan"
Farha tai Murmushi tana ɗaukar Goriba ɗaya tana ci.
Hajja ta cigaba.
"Kinsan zamane mukai na amana nida mutan gidannan abin da suke min ƴan uwana ma bazasu min ba kinsan wannan hajjin ma Alhaji yayi min alƙawari"
Farha tai dariya kaɗan tana cewa.
"Hajja azumi fa sauran baifi sati Biyu ba kina kuma zancen Hajji ba umara ba?"
Hajja tace.
"A,a idan azumin ya wuce babbar sallah tazo to shine zamu tafi Hajjin In sha Allah har haƙuri ya bani wai bai biya min da wuri ba niko nace hakan ma nagode"
Farha tai Murmushi tana cin goribarta Hajja kuma abincin taja ta soma ci tana ci tana yaba girkin na farha.
"Yawwa Hajja dan Allah wace hanan a gidannan?"
Farha ta faɗa tana nazarin yadda taji yana waya da Hanan ɗin.
Hajja tai Jimm.
"Kai ba hanan agidannan kodai Mami wata fara matar Alhaji Ali mai kirki zaki ganta ba ruwanta"
Farha ta taɓe baki tare da cewa.
"Ba ita ba"
Daga haka taja baki tai shuru tana zargin Budurwar sace Hanan Ɗin shine daya shigo yake waya da ita a ɗakinta.
Da ƙyar ta kawar da tunanin daya addabi zuciyarta har wajan 12 tana ɗakin hajja kafin tai mata sallama tabaro sashin hajja ɗin, Falon Ammi daga ammi se matar nan tazo har ƙasa ta gaishe da Ammi wadda ta amsa batare data dubi saitin Farha ba farha harta Miƙe mami ta kirata.

"Ƙanwata zo ki rakani part Ɗina da Allah naga kin iya aiki yau kwalema zamuyi ta kitchen dan kwana biyu bana nan yayi datti"
Farha kamar tace wayyo Allah domin ta gaji bacci ma kuma take ji haka tabi bayan mami zuwa sashin nasu Seda ta raina kanta sabida haɗuwar sashin su mami tsarin sa da ƙyansa fadin sa ma ƙauyanci ne bata sare da komai ba seda ta shiga falon lallai Kuɗi yayi kuka jitai ta raina kanta ta kuma tabbata bawan Allah yafi ƙarfinta kawai dai ya mayar da ita mahutar shine. Kitchen din suka shiga Mami ta dinga fito mata da abin da zatai wanda ta zage suna ta aikin har wajan azahar sallah sukai suka cigaba da ikin mami nata janta da Hira ita ko taƙi magana Wajan la'asar suka kammala amman mami ta hanata tafiya tace seta ci abinci mami tana kitchen taji wayarta dake Gefen kujera tana Ringing ta ɗauka ta bita Kitchen ɗin batare data duba wanda yake Kiranba.

Mami ta amshi wayar tana miƙawa Farha Ludayin hannunta akan ta cigaba da juya mata ƴar Miyar Cikin Tukunyar Ita kuma ta ɗaga wayar Cikin farin ciki.
"Dear har kun sauka kenan? Amman kunyi sauri"
Daga ɓangaranshi yana kwance acikin Hotel ɗin daya kama yace mata.
"Eh mun sauka yanzu me kike yi ne naji kamar ƙara a kusa dake?"
Ya faɗi hakanne dan kawai yaɗan Ji ta bakinta sabida yadda ya ɗauki rashin yarda ya ɗora mata shiyasa ya kafa mata matakan tsaro wanda bata sani ba.
"Ba abin da nake Munyi ɗan gyara ne da ƙanwar Musa, yanzu muka gama Girki nake ɗan yi mana"
Yay saurin cewa.
"Wani musa kuma?"
Mami tai Murmushi.
"Musa naka wannan yarinyar ta wajan Ammi"
Ya mayar da ajiyar zuciya.
"Ayya bata ma wayar ni na manta Musa yace a tambayeta ko tayi makaranta wannan term ɗin se a sakata na manta shaf se yanzu na tina"
Mami bata kawo komai ba ta Miƙawa farha wayar tana cewa.
"Jeki falo zakuyi magana bani Miyar na juya"
Farha ta amshi wayar ta fita tana turo baki.
"Kina jina?"
Ya faɗa ƙasa ƙasa.
"Ummmm"
Tace masa tana turo baki kamar yana wajan dan haushin sa take ji na dalilin wannan hanan dataji yana waya da ita.
"Ki wuce ki tafi sashin Ammi ban amince Kicimin abincin part Ɗina ba dan ƙwaɗayin tsiya meye zaki biyota har Take Muku girki bayan abin da ke nan shike part ɗin Ammi"
Ya faɗi hakanne dan baya so taci abincin mami shikuma baya son ya nuna mata abincin mamin ne baya so taci dan bai son ya Nuna akwai wata matsala a tsakanin shi da mami wanda yasan in ba haka yayi mata ba seta ci abincin Shikuma Idan taci hankalinsa baze kwanta ba.

Hawaye ne ke gudu a saman Fuskar Farha.

"Ko baki jini bane Kin min shuru"
Kashe wayar tayi yayi ta kira tana katsewa yasan Haushi taji Kuma yasan ba zata ci abincin ba hakan dayay yaji hankalin sa ya kwanta sabida haka harkokin sa ya cigaba hankalin kwance. Farha kuwa aje wayar tayi ta zubawa Tv idanu tana saƙa wasiƙar Jaki Har zuwa sanda Mami ta fito da Tray da Kulolin abinci jere a saman tray Ɗin ta kawo gaban Farha ta aje ta koma Kitchen ta ɗauko Musu ruwa da Lemo ta dawo kusa da Farha ta zauna ta saka Musu kayan abincin a tsakiyar su........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 60*

Cikin ladabi musa ke amsa wayar wadda ta nuna alamar da uban gidan shi suke yin wayar Musa mota ya shiga yaje ya ɗauko wani Abokin shi wata ƙatuwar Mota ce ta daban ke biye da bayan Motar da su Musa ke ciki wanda take ta bin su har zuwa Bakin Layin su Farha Musa ya dubi Abokin nashi ya ƙara jaddada masa abin da zece kafin ya Buɗe masa Ƙofar motar ya fita Abokin musa ya ƙarasa cikin layin su farha ya kuma sami gidan kamar yadda Musa ya kwatanta masa Yaro ya samu ya aika cikin Gidan akan yana son ai masa sallama damai gidan yaron ya shiga gidan ya faɗi kamar yadda aka umarce shi Nura ne ya fito ƙofar gidan ya bawa abokin Musa hannu suka gaisa Abokin Musa ya gyara tsaiwa yana cewa

"Dan Allah ko nan ne Gidan su farha?"
Nura yayi saurin cewa.
"Ehh nan ne yaya ake ciki?" Abokin Musa yace "Dama saƙo ne Mijinta ya bayar a bawa Babanta ina son ganin Baban nata idan babu damuwa" Nura yaɗan yamutsa fuska cikin Alhini yace "Gashi baban namu bai da lafiya yau kwanan mu biyu da fitowa daga asibiti ma yanzu haka yana kwance Dan Allah ina ne gidan da Farha take aure? ka daure kace wa Mijin nata ya kawo ta Kawu ya ganta dan dalilin aurar da ita da yayi ne ma wannan ciwo ya same shi ance zuciyar shi ce take barazanar kamuwa da ciwo yanzu haka hawan Jini ke damun shi" Abokin Musa ya jinjina lamarin kafin yace wa Nura "To idan ba damuwa ko zamu shiga daga ciki sena duba shi" Nura ne yayi gaba Abokin Musa kuma yana binsa a baya Nura ya shiga ɗakin Kawu Lokacin Umma tana bashi Koko Nura ya kalli Umma kafin yace.
"Ya samu yana amsar kokon?" Umma ta share ƙwalla tace "Ehh amman da akwai ɗan canji da an siyo masa ruwan shayi dan naga baya son kokon bai fiye amsa ba" Nura ya shafa aljihu gaba ɗaya ziro yake sabida albashin Nasu Duk ya ƙare a jinyar kawu yanzu hatta kai su Kansu

Matan Gidan Ko wacce jarin ta ya taɓu sabida siyan magani Yau haka suka tashi Ko ruwa babu agidan dan tsananin Babu shiyasa a wannan lokacin Umma itama kawai dauriya take amman inda za'a gwada Jininta itama tasan yahau sabida yadda ƴaƴan Gidan da matan gidan suka sakota a gaba da habaici da faɗan Ƴarta zata kashe Musu kawu Kullum Umma setai kuka damma akwai Ya Sadiya da take yawan zuwa cin Uban kowa take agidan sedai daga ta fita zasu Ɗora shima kawun Wuni kukan a kawo masa Fatima shiyasa Kullum Jinin sa a haye yake baya sauka Kullum cikin shan magani yake.

"Umma yau se godiyar Allah, Amman zan fita wajan Abokina se a siyo masa" Umma ta kalli Nura da tausayawa yaran ba ƙaramin Ƙoƙari suke yi da mahaifin suba kunya ta kama Umma tasan duk a sanadin Ƴarta Komai yake ta faruwa da Kawu, "A,a Nura ka bari yanzu na aika Ikram Gidan sadiya abin da ta samo se a sarrafa masa" Nura yace "Umma me yasa zaki aika mata Kinsan halin Ya sadiya da Saurin Kiɗima Yanzu seta tawo ta ɗauka ko ciwon nasa ne ya tashi kuma ai tana Ƙoƙari kaf ƴaƴan gidannan bamai kula da kawu kamar ita Kusan Kullum fa seta yo masa Girki"
Umma tai murmushi "To ai ya zama dole Nura, bada ban naga tana sana'a ba da bazan aika mata ba to sana'ar dana ga tana yi ce yasa nake aika mata ai ya zama dole" Nura ya shafa kai yace "Umma ɗan gyara shi ga Baƙo nan yazo wajan shi wai mijin farha ya aiko shi" kawu yana jingine amman se ganin shi akai ya miƙe umma ta kama shi tana cewa "Kabi a hankali" Cewa yake "Nura ina baƙon shine baka gayan ba yana ina ina fatiman take Tazo ta ganni kafin Allah ya ɗauki rayuwata" Ƙwalla ce ta kawo Idon Umma bata taɓa sanin kawu na son ƴaƴan saba se akan farha ashe duk jarabar Faɗan shi ya damu da ƴaƴan sa gashi nan Abin da yayi wa Farha yaja masa ciwo.
Abokin musa ya tuɓe takalmi ya shigo Ɗakin ya zauna a tabarma suka gaisa da Umma sannan suka gaisa da kawu Abokin Musa yace.
"Dama Alhaji ne yace nazo na duba ku, Sannan ga saƙo can A mota yace a baku" kawu yayi saurin cewa "Kai ni babu wani saƙo ina fatima take tana wani gari wani hali take ciki?" Abokin Musa yace "Baba kai haƙuri wannan Ba'a bani damar na sanar dakai ba iya wannan kaɗai aka umarceni shima abin da yasa na faɗa maka sabida kasan yadda garin  ya koma mutanan duniya sun lalace kada kuga saƙo sama taka ku tsorata shiyasa aka ce na bayyana wanda ya aiko ni, Amman garin da take da sauran su wannan ba hurumina bane ni dai nasan ƴarka tana cikin Ƙoshin lafiya Kuma ka godewa Allah ƴarka ta sami Miji na nuna sa'a" Daga umma har kawu ba wanda ya iya magana domin su ba wannan bace Buƙatar su ba buƙatarsu sanin ina ƴarsu take Abokin Musa ya miƙe tare da dire damin ƴan dubu dubu har guda biyar a gaban kawu bai saurari me kawun ze faɗa ba yabar Ɗakin Matan gidan ko wacce tai tsaye cirko cirko suna sauraran abin da Baƙon yake faɗa ko wacce ta cika da mamakin wannan Aike Da Nura da Halifa ne suka bi Abokin musa mota kamar yadda ya buƙata Kaya ne na abinci buhunan shinkafa taliya makaroni mai komai daya danganci abinci akwai shi haka sukai ta fito dasu suna kawowa Gida wanda har ƴaƴan maƙota seda suka taya su gaba ɗaya tsakar Gidan su Farha ya cika da kayan abinci abokin Musa ya shiga Mota bayan sunyi sallama dasu Halifa Musa dabe Fito ba yaja Motar suka bar bakin layin.

Hankalin Umma tashi yayi data ga kayan abincin ta shiga wasi wasin wani irin Mijin farha ta

aura kodai ɗan yankan kai ne da sauri ta kawar da tunanin tana ayyana alkairi Ɗakin Kusa da kicin aka shigar da kayan abincin Wanda kafin kice kwabo Babarsu Ruƙayya ta haɗa wuta an ɗora sanwar safe wadda ba'a ciba kawu kuwa Gaba ɗaya Jikinsa yayi sanyi Nura ya kira ya bawa duka kuɗin da abokin Musa ɗin ya bayar Matan gidan bakin ko wacce ya Mutu Murus sabida al'ajabi Maƙota kuwa leƙowa suke zuwa dare Gida ya cika da ƴan barka barka wasu har cewa umma suke dama sun san watarana kawu ze Huta ajikin wani a cikin ƴaƴan nashi Ikon Allah farha data fi kowa Muni agidan itace mai rabon Jin daɗi yaya Sadiya ma data zo taji kayan arziki Ihu ta saka harda rawa tana cewa Ai alkairi yanzu aka fara gani babarsu Hadiza kuwa ta kasa magana cikin dare ta kama habaici tana ayi dai su gani idan tusa zata hura wuta waya sani ma ko ɗan mafiya ne amman ba yadda za'ai farha ta auri mai kudi irin haka kunjifa Hassada seda kawu ya fito yayi mata cin Mutunci sannan tai shuru Gidan su Farha ya wadata dan Kayan abincin sun haska Gidan ƴaƴan gidan kowa murnar zeyi ci uku ta ishe shi Kuɗin Da kawu ya bawa Nura kuwa Nura bai taɓa su ba zuwa yayi ya zuba a cikin account.

Abokin Musa ne ya dubi Musa yana gaya masa duk yadda ya sami mahaifin yarinyar Musa ya jinjina lamarin tare da ɗaukar alwashin sanar da Aliyu duk yadda ake ciki bayan Musa ya sauke abokin sa waya yayi wa Aliyu ya gaya masa duk yadda sukai musa ya ƙara da cewa.
"Kasan yayin ta suna aiki a kamfanin mu shiyasa ni banje sun ganni ba na tura abokina dan nasan baka Buƙatar su sanka a yanzu"
Aliyu yayi Murmushi daga nasa ɓarin kafin yace.
"Haka ne Musa ina son ka gayawa manager a ƙara musu Kuɗin albashin wannan watan harma da sauran watannin gaba sannan ka koma akai Baba asibiti mai tsada a duba shi sannan ina son a samu Leburori masu aikin sauri Su fara gyara Musu Gidan su inda hali ma har Bene a ɗora sannan wannan kayan abincin duk sati Biyu zaku dinga kai Musu amman na cikin azumi yafi ko wanne son samu ma a ƙara masa mota ɗaya wadda ze rabawa Maƙotan shi musa kada ka Bada fuskar da zasu sanni kasan har yau Ammi bata san nai aure ba wannan shine dalilin daya sa ban so su san ni wanene"
Musa ya amsa cikin bin umarni kuma beyi mamakin hidimar da Aliyu yace ayi ba dan wanda bai haɗa komai dashi bama yayi wa bare surukan sa.

Washe gari Abokin Musa ya koma wajan kawu Asibitin Kuɗi ne mai tsada aka kai kawu aka duba shi aka bashi magani Wani ɗan gida anan kusa dasu Suka koma wanda abokin Musa ya kama musu haya ranar dasu ka kwashe kayan su daga gidan Masu aikin suka fara aiki wanda motar yashi Bulo sumunti ta cika layin su farha Kawu da ƙyar yabar wannan aiki dan seda Su Halifa sukai ta bashi baki da cewa ai ya godewa Allah daya sa ta silar aure farha ta sami wannan cigaba bata silar bariki ba kuma su sun yarda Mijin Farha nagari ne mai gaskiya da ire iren wannan kawu yabari ayi gyaran Gidan ma'aikata suka soma fashe Gida aka fara gyara dakin aka ɗora a ka fara sabon gini a saman Gidan kafin kace Me cikin kwana biyu abin ka da aikin Kudi an ɗora bene agidan su farha Ƙasa kuma anyi ƙaton falo da ɗakuna da Kitchen aciki saman ne ɗakuna uku daga na kawu sena su Halifa ƙasa ne ya zama Ɗakuna Huɗu ɗakin Umma ɗakin babar su hadiza ɗakin babar su Ruƙayya se Ɗakin yara guda ɗaya se wani Kuma ɗakin ɗan ƙarami a gefen na Umma se Store da kitchen Se Katon gate da aka saka cikin kwana Huɗu suka gama aikin aka saka sola akai painti aka saka famfuna idan ka kalli Gidan ba zaka

gane shiba ma'aikatan suna gama gyaran Maƙota da ƴan uwa akaita zuwa gani kowa na santi wasu na murna wasu na ƙananun maganganu Sabbin kayan Ɗaki aka zuba a falon an saka saitin Kujeru labulaye tv da sauran su haka ɗakunan su saitin sabbin kayan gado ƴan uban su store kuma an cika shi da kayan abinci ga sola haske Kota ina kawu daya ga alatun daka danƙara masa kuka ya saka yana Godiya ga Allah lallai haihuwa mai rana dama akwai ranar daze Huta har haka Ashe rabon arziki ne yasa Farha ta turje seta auri wannan Mutumin Ita ko Umma daran da suka koma gidan kasa bacci tayi alwala tayi ta dinga sallah akan Allah yasa dukiyar Mijin farha ta halak Ce Allah yasa ya kawo farha ta ganta Allah yasa farha tana cikin Ƙoshin lafiya.
Cikin lokaci kaɗan rayuwar Gidan su Farha ta sauya daga Ƙunci zuwa farin ciki daga matsi zuwa wadata ada ana damben abinci agidan yanzu kuwa sema ayi abincin babu mai ci da kuɗin wajan Nura aka sauyawa yaran Gidan makaranta aka kaisu Private school, Babar su Ruƙayya ta koma Gindin Umma wanda Babar su Hadiza kuwa taƙi kwantar da hankalin ta sabida baƙin ciki Kullum fatan tsiya take tare da aibata farha wanda Kuma hakan baya hanata Cin abincin da Mijin farhan ya kawo da Kuma zaman gidan da Mijin farhan ya gyara Yayanta faɗa suke mata amman taƙi Ji ita ko babar su Ruƙayya sun haɗe da umma har wata biyayya take mata shi kansa kawu yanzu ba wannan faɗan idan yana wa Umma magana har ƙasa yake da Murya wani bin idan umma ta damu da wannan Hidima yakan ce yaji ajikinsa mijin farha ba macuci bane ba da wannan yake kwantar wa Umma da hankalinta...........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 61*

Yau saura kwana ki Biyu azumi gaba ɗaya al'ummar Musulmi sun cika da farin cikin gabatowar wannan wata mai daraja watan da Allah yake Buɗe ƙofofin rahmar sa wata mai albarka wata mai daraja yau tun safe su Farha suke ta kwalema a part Ɗin Ammi an fitar da Kujerun falon an sauke labulayen falon duk an fitar dasu sabon Paint ake tayi a part ɗin zuwa azahar an sake sabbin Kujerun falon tare da labulaye Komai ya sauya Falon sai tashin Ƙamshi yake yi.
Gaba ɗaya jikin farha ciwo yake mata haka ta shiga ɗaki ta cire kayanta ta shiga wanka tana wanka tana tunanin Bawan Allah matar sa tace kwana takwas zeyi yau gashi har ya kwana Goma sha huɗu bai dawo ba, Haka tayi wankan ta fito tana zaune a bakin Gado tana shafa mai Safna ta shigo ɗakin ta ɗan kalleta.
"Kizo Ammi tana kiran ki"
Daga haka ta juya bata jira cewar Farhan ba, Farha ta gama shafa man sama sama ta je gaban kayan ta Riga da skirt na atamfa ta ɗauka Sedai data zo saka rigar kaɗan tai mata taƙi shiga Musamman daga wajan Ƙirjinta Seda ta cire bra sannan ta saka rigar skirt ɗin ma da tsalle ta saka shi aikuwa se Nishi take Numfashin ta har sama yake da ƙyar take janyo shi Hijabi dogo ta saka har ƙasa ta fita daga ɗakin zuwa Ɗakin Ammi shima an sauya kayan gadon ɗakin dan bana da bane Ammi ta dubi Farha yau babu wannan Ɗaure fuskar tace mata

"Fati yanzu me zaki yi?"

Farha tana wasa da yatsun hannunta tace.

"Babu komai Ammi, wanka dai nayi"

Ammi ta ɗan dube ta.

"To dan Allah zaku shiga kitchen Keda Hajja, zaku yi girki kamar kala Biyar sabida yau Sadiƙ zezo da iyalan shi, da Bashir da Baba duka yau zasu zo Ina so kuyi girki mai kyau dan Allah"

Farha cikin ladabi ta amsa wa Ammi, sannan ta baro ɗakin sallah tayi sannan ta fita har Hajjo tazo Kayan miya farha ta soma gyarawa ita kuma Hajja tana ɗora sanwa.
"Hajja wai waye Baba ne? naji Ammi tana yawan cewa baba?"
Cewar farha wadda take Cire hancin attaruhu, Hajja tayi dariya tana cewa.
"Nawa zaki biyani na gaya miki waye baba" Itama farha dariyar tayi tana cewa "Hajja zan baki jakaliyan Ɗari" Dukansu dariyar sukai kafin Hajja tace.
"To Alhaji Ali shine Baba Kinsan sunan Baban Hajiya Ammi gare shi" Farha ta cika da mamaki domin sam bata ɗauka shi bane Baban dama yau ze dawo wato shiyasa Aunty mami tun safe tace ta fita gyaran Jiki da ƙunshi da Kitso Ah lallai.
"To Hajja sadik fa naji tace yau zezo da matar sa shima anan yake?".Hajja ta ɗora tukunyar akan gas sannan ta juyo "Eh yayan Alhaji Ali ne yana lagos yana aiki a ɗayan kamfanin Alhaji Ali, Tare akai Musu aure sadik nada mata ɗaya da yara Uku duk zasu zo anjima sabida zasu je umarar azumi ne nan da ƴan kwanaki" Farha bata ce komai ba aikin su suka cigaba dayi Wajan Magariba suka kammala Lokacin Mami ta shigo kitchen ɗin tai kyau ma sha Allah Fuskarta tai fiyau sabida sabon Kitso warmers ɗin abincin ta shiga dubawa tana ta yiwa su Hajja sannu.
"Ina abincin Ammi?"
Cewar mami tana kallon farha.
"Ai gaba ɗaya aka haɗa abincin sabida tace anan zasu yi dinner"
Cewar Farha, Mami ta yatsina fuska tare da cewa

"Da anyi wa Ammi ko tuwon semo ai ina zata iya waɗannan ciye ciyen ai se mu" Hajja tayi dariya tana cewa "Hajiya mami ta ammi wannan soyayya taku har tayi yawa to ni dai na tashi sedai Fati tayi mata" Farha jitai kamar tace wayyo Allah dan ba ƙaramar gajiya tayi ba ga ciwon mara ga zafin hannu wanda gyaran attaruhun data yi ne yaja mata shi ga ciwon baya ga wani yawu da yake tarar mata abaki zuciyarta na tashi tun ƙamshin tafashen naman data yi bata sami sukuni ba.
"To Farhan ɗan yi mata tuwon Before ai magariba" Mami ta faɗa tana fita daga kitchen ɗin farha dan haushi Ko sallamar da hajja ke mata bata amsa ba ta ɗora ruwan tuwon sannan ta fita daga kitchen ɗin ta koma ɗakinta Da gudu ta shiga Toilet ta riƙe Ciki tana sheƙa amai a galabaice ta fito tana Numfashin wahala jagwab ta kwanta a gado hannunta dafe da ƙasan mararta daya ɗaure yana mata ciwo Miyau ne ya tarar mata taje ta tofar ta kuma dawowa Kitchen ɗin ta shiga ta Buɗe Fridge ta ɗauki lemon tsami ta yanka tana tsotsa seda tayi sallar magariba sannan ta tuƙa tuwon ta kwashe sannan ta ɗora Miyar Kuka wani haɗaɗɗan Ƙamshin turare taji wanda kafin ta ɗago mami ta shigo kitchen ɗin taci adon golden lace ɗinkin Bubu wanda yayi mata cif ajikinta ga wasu uban gwala gwalai sarƙa ɗan kunne awarwaro data zuba fuskar nan tata taci kwalliya, Kallo ɗaya Farha tayi mata taji zuciyarta ta motsa wani irin zafin Kishi na taso mata

yanzu fa duk wannan kwalliyar Domin Mijinta tayi ta ko, maganar mami ce ta katse wa farha tunanin da take.
"Farhan nayi kyau kuwa? Yaya yayi min waya suna airport taimaka ki ɗora masa ruwan tea mai kayan ƙamshi amman mai ɗan yawa sabida ta lagos ya biya tare suke da su Ya Sadiƙ Ni bara naje wajan Ammi, amman kafin na ɗauko min wancan Ludayin na sama"
Farha tayi Murmushin yaƙe.
"Kin yi kyau mana Aunty sema ya gani ya bada tukwici"
Ta faɗa tana juyawa wajan Ludayin Mami tana dariyar jin daɗi da sauri tai wuf ta zuba magani a ruwan Miyar da farha ta Ɗora Farha sam bata lura ba ta miƙa wa mami ludayin ta Cigaba da haɗa miyar tata Mami ta fita da Ludayin da babu abin da zatai dashi dama dan ta zuba magani a miyar ne tayi wa Farha dubara

Farha da ɗayan Gas ɗin ta ɗorawa Aliyu tea ɗin Ta raba hankalinta Biyu can tana miya nan tana kula da tea bayan ya tafaso ta zuba a flaks ta aje Miyar na tafasa Ƙamshin daddawa dasu citta na tasowa Farha taji zuciyarta na tashi sabida bata san ƙamshin ɗankwali ta saka ta Toshe hancinta haka ta kammala Miyar ta haɗa takai Falo haɗe da sauran kayan abincin ta gyara dining Ɗin tas ta ɗauko turaren wuta ta kunna.

Ammi ita kanta a ranar seda ta yaba da yadda Farha tayi Ƙoƙarin haɗa komai aikuwa se sannu take mata Ammin ma taci gayu Su safna ma haka.
Ita dai farha data samu ta shiga ɗaki kwanciya tayi a saman gado nan da nan bacci ya ɗauketa............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 62*

Yana saukowa daga step ɗin jirgin yana lumshe idanun shi sabida shaƙar Iskar Jahar sa Abar alfaharin sa da yake yi kano kenan ta dabo ci gari koda me kazo an fika mai mata mai matasa mai malamai mai masoya Manzon Allah ( s.a.w ) mai dala tushen birni mai gwauron dutse mai masauratar da take da tarin tarihi kano jalla babbar hausa kano tumbin giwa!
Da sauri musa ya ƙaraso gaban sa bayan ya bar harabar da jirgin ya sauke su Musa ya amshi ƴar ƙaramar Jakar dake rataye a kafaɗun sa Haka suka nufi inda Musa yayi parking Ɗin Mota yana jiran shi wata haɗaɗɗiyar Black mercedes benz s class, Musa ya buɗe masa Back seat ya shiga ya zauna gaba ɗaya ya gaji tunda yabar lokoja ya tafi lagos bai zauna ba zirga zirga suke shida Bashir wanda jin sadik zezo arewa yasa wa Aliyu kuka akan ko kwana ɗaya ne ya barshi yazo yayi shima tausayin Bashir yaji shiyasa ya bar shi suka tawo tare sedai shi Aliyu ko acikin Jirgi yana Vip section sabida haka jirgin su na landing ya sauko batare daya tsaya jiran su Bashir ba dan su Driver ne yake jiran su.

Sadik da Yaran shi da sakina da jamila ƙanwarta da bashir driver ne ya ɗauko su a wata Farar BMW suma Musa yana tafe yana bawa Aliyu labarin yadda Shari'ar Md ta kaya Shidai ya dafe kai bai cewa Musa komai ba suna isa gida part ɗinshi ya shiga Mami ta tare shi tana masa sannu ya hau sama ya shiga wanka ya ɗauro alwalar sallar magariba a ɗaki ma yayi sallar

sannan ya sauka ƙasa dan yunwa yake ji Jeans baƙi ne a jikinsa se farar Polo shirt se ƙamshin turare yake mai sanyin Kamshi ya ƙarasa gaban dining ya zauna yana kiran mami.
Ta ƙaraso tana rankwaɓo wa jikin shi.
"Yaya gani nayi sallah ne"
Ya ɗan kalleta kaɗan tayi kyau ba laifi.
"Ina abincina?"
Tai murmushi.
"Ammi tasa an haɗa a part ɗin ta acan zamu yi dinner"
Bece komai ba yayi sama da kanshi ya jingina jikin Kujerar da yake kanta yunwa yake ji ba kaɗan ba can ya kuma cewa.
"Ko ɗan ruwan shayi ma babu?"
Mami tace "Eh duk suna can"
Ƙaramin tsaki kurum yaja ya fito da wayar shi ya shiga danne danne seda yayi sallar Isha'i sannan suka jera part ɗin Ammi shida Mami.

Su sadiƙ a part ɗin Ammi suka sauka extra room ɗin dake Kusa dana su ammi Sakina ta saka kayanta shi kuma Sadiƙ ya aje nasa a part ɗin Bashir sabida su ba'a gyara musu part Ɗinsu ba akwai datti sosai Kuma duk aikinne yayi yawa sedai ko zuwa Gobe wanka sukai tare dayin sallah Nan fa suka baje a falo ammi nata tsokanar su Minal ƴaƴan sadik waɗanda suke jin yarabanci don maganar suma bata fita sosai saboda zaman Cikin yare, Intisar ce ma mai magana da hausa amman Minal da Hidaya se turanci se yarabanci nan da nan sun koma kamar ƙabilu.

Zuwan Aliyu da Mami ne yasa Bashir dasu safna suka ɗan shiga Nutsuwar su da dariyar da suke yi dan Sun san Gogan ba wasa Jamila ƙanwar sakina wadda ita kebin ta wadda sakina keson ta haɗa ta da Aliyu shi kuma yaƙi yarda se kallon Aliyu take kamar ta lashe shi lura da kallon da jamila kewa Aliyu ne yasa Mami taƙi sakin fuska tai kicin kicin da ranta ta koma bayan Mijinta ta zauna yaɗan kalli sadik da ke bawa Ammi labari.
"Oga nifa nazo yin dinner ne sabida yunwa nake ji" batare daya jira amsar sadik ba ya gaishe da Ammi wadda ta miƙe tana cewa su sakina.
"Ku taso muje muci abinci seku yi sallar isha'i"
Duk suka tashi ban da Jamila data zauna tana sunne kai ammi ta kalleta da kulawa.
"Jamila taso mana kema ai kin zama ƴar gida" sakina tayi dariya tana cewa.
"Ai Ammi ita haka take, yau fa kwanan ta biyu a lagos taje min hutu shine na tawo nan da ita"
Ammi tayi dariya tana cewa.
"Aiko ta kyauta"
Shikam Aliyu har ya ƙarasa dining ya shiga buɗe warmers ɗin da aka jere duk ba abin da yayi masa se tuwon daya gani marar yawa ya zuba a plate ya ɗauki spoon da sauri Mami ta riƙe Cokalin da Aliyu ze kai cikin bakin sa jikinta har rawa yake wajan ce masa "Yaya kada kaci dan Allah"
Ya aje cokalin ya tsareta da ido Lokacin kowa ya zauna a saman dining kuma kowa ya shiga zuba abin da ze kai cikin sa.
"Sabida me kar naci? idan naci mutuwa zanyi kome?"

Gaban mami ya faɗi ta shiga sosa kanta.
"A,a yaya dama Ammi nasa Farhan taiwa kasan ita bata son girke girken mu na zamani"
Aliyu yayi wani Basaraken Murmushi ya ɗauki cokalin ya cigaba dacin tuwon hankalin sa kwance Ammi kam dariya tayi tana cewa "Ai kema da se kisa ai da yawa Kin san yadda Mijin ki yake son tuwo" Mami sam bata ji mai ammi take faɗa ba ta shiga tashin hankali ko abincin ma ta kasa zubawa taci.
Falon ya ɗauki shuru kowa yana faman cin abinci se ƙarar cokula da Plate ke tashi.
Aliyu ya ɗan kalli mami ya cigaba da cin tuwon shi.
"Ina tea ɗin?"
Sosa kai tayi tare da ɗaga Murya sosai.
"Farhan kawo tea"
Aliyu yabi ta kallo yana tuna wace Farhan ɗin da take ta faman faɗi dan shi ya manta sunan farha farhan dan shi Fatima yake ce mata.
Lokacin Farha ta miƙe daga baccin tana sallah seda ta idar ta fito waje sabida jin Yadda Aunty mami keta ƙwala mata kira.
Gaba ɗaya se ta shiga damuwa sabida yadda taga mutane da yawa a falon kowa kuma ya zuba mata ido sum sum ta wuce Kitchen ta haɗo kayan tea ɗin a tray ta kawo gaban mami ta aje ta Lura da yadda wannan matashin ya tsaida Cin abincin sa tun bayan data fito se kallonta yake kamar maye, Sannan wannan baƙar Budurwar ma kallon ta take, a ɗarare ta shiga gaishe dasu sakina.
Sakina ba sakin fuska ta amsa jamila ma haka Bashir kuwa bai amsa ba se jarababban kallon da yake bin ta dashi Sadik ne ya amsa yana cewa.
"Hajiya Ammi tamu ina kika samo ƴar budurwa haka?"
Ammi murmushi tayi bata ce komai ba sabida abinci take bawa hidaya ƙaramar ƴar sadik.
Sakina ce ta ɗago a gadarance.
"Ke da Allah ɗauki yarinyar can Ki mata wanka" ta nuna intisar Farha ta juya zata ɗauki yarinyar Aliyu daya daskare a zaune yana binta da kallo na mamakin yadda ta kalli kowa ta gaishe dashi amman shi ta kasa koda kallon shine bare ya sami arziƙin gaisuwar ma.
Da sauri yace.
"A,a Sakina Ita wannan ƙanwar taki taiwa Intisar wanka mana, bakya ganin ita aiki take" batare daya kalli sakinar ba yayi maganar da sauri kuma ya cigaba da cin tuwon shi...............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 63*

Cikin son ta cusa masa haushi tace.
"Lah bari nayi mata wankan, meye aikina in ba yiwa kowa na gidannan Hidima ba ai bani da wani hutu se Hidimta Muku" daga haka ta ɗauki Intisar cak tayi hanyar ɗakin ta da ita Bashir da yaji ta burge shi data gwale Aliyu dama cike yake da haushin yadda Aliyu ke hana yarinyar tai wani abun sannan kuma yana nuna kamar shike iko da ita.
Da ɗan nishaɗi Bashir ya ɗaga Murya bayan ya kora ruwa.
"Hy baby zo mana ki zuba min Lemo a cup" cak ta tsaya tana nanata sunan daya gaya mata Anya ta je kuwa murmushi ta saki ta aje Intisar ta juya gaban Bashir se kallonta yake ta tsiyaya

masa Lemon ta miƙa masa tana wani Irin murmushi ta koma ta ɗauki Inti ta shigar da ita ɗakinta ta cire mata kaya ta haɗa ruwa tayi mata wanka sam ta mance yaushe rabon ta da sabulun wanka se yau sabida ita idan zata yi wanka sedai ta ɗauko omo tayi dashi sabida bata son ƙamshin sabulun tana toshe hanci tana wa Inti wankan tana kwa gamawa ta soma sheƙa amai wanda yarinyar ta gudu daga toilet Ɗin ta fita falo ko kaya babu ajikinta.

Lokacin sun kammala cin abincin Shi kaɗai ke dining yana shan bakin shayi.
"Ke Intisar ina kayan naki?" cewar Jamila wadda ta Miƙe zata shiga ɗakin da suka sauka yarinyar tai kalar kuka tana cewa.
"Nanny ɗin amai take tayi a bathroom ɗin shine na fito" Jamila ta kamata suka wuce ɗaki Mami zama tayi a falo duk jikinta a sanyaye har lokacin a tsure take sabida Aliyu yaci wannan tuwo da sauri kuma ta miƙe ta nufi sashin su don ta kira maman ta a waya su san matakin ɗauka.
Bashir wata irin tafiya yake yana ɗaga lemon data zuba mai yana sha ji yake kamar bakin ta yake tsotsa dan jaraba Aliyu ya fuskanci Abin da tai masa yayi wa Bashir daɗi Se kawai ya raka Bashir da idanu har yabar falon domin Aliyu ya gama gano Bashir me yake nufi da yarinyar wannan tasa ya nesan tashi da gida amman yanzun ma ze ɗauki mataki akan Bashir Ɗin daga cikin falo sakina ma ɗaki ta wuce dan ta gaji sosai hutu take buƙata Falon daga sadik se Ammi dasu safna suna ta faman Hira shiko Aliyu be shiga cikin suba kuma bai tafi ba waya yake tayi da mutane daban daban duk da yaji zafin yadda ta yarfa shi ta gwasale shi a gaban ƙannen shi da matar shi amman sabida tsabar Muskilanci bai ko nuna a Fuskar shiba.

Sadiƙ hamma yayi tare dayi wa su Ammi sallama ya ƙaraso wajan Aliyu sukai sallama ya wuce makwancin sa su safna ma wuce wa sukai bedroom ɗinsu ganin haka Ammi ta dube shi.
"Wai kai me kake jira anan ne kowa ya kwanta kai ba hira ba kai ba tafiya ba?" Ya shafa kanshi bai ce mata komai ba ta miƙe ta kama hanyar Bedroom ɗinta tabar shi a wajan.

Ya sauke ajiyar zuciya ya miƙe ya nufi ɗakin marar kunyar can, kamar yadda ya raɗa mata yaja handle ɗin ƙofar ta buɗe ya shiga ya zira key a jikin ƙofar ya kunna hasken ɗakin sabida ta kashe hasken tun sanda ta fito daga toilet bayan ta gama aman ta kashe ƙwan ta kwanta duk da tana tsananin jin yunwa ga yawun ta se tsinkewa yake, amman bata sha'awar shinkafa ko taliya yau ɗinnan wainar fulawa take son taci mai man gyaɗa da albasa da tumatur da yajin tafarnuwa har ƙamshin wainar take ji a hancin ta wannan dalilin ne yasa ta ɗora hannu a saman cikinta tana kuka wiwi dan sosai take muradin cin wainar kuma bata son ƙamshin suyar tafi son kawai ta ganta a gabanta tana ci cikin haka hasken daya kunna ya gauraye ɗakin ta ɗago ta zauna tana kallon shi ya wani haɗe fuska kamar bai taɓa yin dariya ba.

"Ke baki da kunya ko? baki da mutunci baki san darajar aure na da yake kanki ba har Bashir yana ce Miki Baby kina amsawa kin mayar da kanki kamar baki san me kike ba me sakina ta fiki dashi da zata wani daka Miki tsawa! ki mata abu har Kiyi, sannan ince ba zaki ba ki gwale ni bayan rashin gaisuwa dana kasa samu a wajan ki, so kada ki ga na haɗa Ƙirji dake wallahi I will surprise you if you refuse to follow what I told you"
Har ya gama masifar bata ko kalli inda yake ba ita ta kanta take se faman sakin Numfashi take yi Shurun data yi masa ne ya ƙara fusata shi idan da abin da yafi tsana a duniya bai wuce Yayi

magana ai masa banza ba bai wuce yayi faɗa a ƙi bashi haƙuri ba aiko yayi mata kaa cikin hargowa yana daka mata tsawa!
"I talked to you but you kept quiet, you made me crazy or something?"
Ya faɗa yana zuba mata girman idanunshi waɗanda sukai jajir Se tace tunda take bata taɓa ganin Yanayin nan a tare dashi ba rintse idanu tayi Jikinta yahau rawa Bakinta mai cike da yawu ta ɗaga tana cewa

"To ni me kake so nace maka, nayi magana kace nayi maka rashin kunya kome?" Seta saka kuka ta cigaba da cewa "Ni ka rabu dani ka barni haka nina san me yake damuna zaka wani zo kana min Ihu akaina dame zanji da gajiyar aikin gidanku koda Abin da yake damuna kashe kaina zanyi idan ban musu aikin ba, ba jaka ka kawo ba? ai ni jaka ce mai muku hidima kaine kace nida fita sedai naje gidan zoo wajan dabbobi ƴan uwana to meye danna yiwa matar yayan ka Biyayya nayi wa ƙanin ka duk fa acikin aikin dana zo yi muku ne ni baiwa ce daka siyo duk inda kuka kaɗani nan zanyi sabida haka ni kada ka kuma zuwa kana Min wannan ihun idan ba haka zan faɗi tsakanina dakai kowa ma ya sani idan yaso ka sake ni na huta da wannan ƙaddararran auren naka wanda bashi da Ƴanci"
Da gudu ta ƙarasa maganar sabida Aman daya tawo mata tun kafin takai ga shiga banɗakin ma Aman ya gama wanke tsakar Ɗakin a bakin Ƙofar bankaɗin ta tsugunna tare da dafa ciki tana sheƙa Aman yana tsaye yana mamakin furucin ta lallai ta shahara a rashin Kunya shine har yana magana tana mayar masa, Farha ta gama aman ta wanke wajan ta wanke bakinta ta taso zata Zo ta gyara inda ta ɓata ɗin a ɗakin santsin aman ya kwasheta luuu ta tafi zata faɗi da wani Irin sauri ya taro ta, ta faɗo masa saman Ƙirjinsa Allah ya taimaka bata kai ga faɗuwa a ƙasan ba.................*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 64*

Idanu ta rintse ƙirjinta na dukan dum!dum! sabida gaba ɗaya ta bayar data faɗi ma ta gama sedai data tsinci kanta ajikin sa ya tallafe ƙuguntа da hannun shi seta hau sakin ajiyar zuciya mai ƙarfi da sauri ta kuma soma zamewa ajikinshi sabida sabon Aman daya kuma tawo mata amman fafur yaƙi sakinta Lumshe ido tayi tana girgiza masa kanta alamun ya saketa dan ba zata iya magana da baki ba sakamakon yawun daya cika mata Bakinta tana magana zubowa zeyi bata da zaɓi face soma sheƙa masa Aman a jikinsa harta gama bai sake ta ba Mayar da Numfashi take tana dambe da Numfashin ta wanda yake Fita da sauri da sauri.
"Sannu" ya faɗa yana ɗagata cak ya kaita Toilet da hannunsa ya dinga ɗauraye mata Jikinta ya ɗagata cak ya kaita kan gado ya ajeta da kansa ya shiga gyara ɗakin seda ya goge aman duk da yana da masifar ƙyamƙyami amman ikon Allah shiya gyara ɗakin ya tube Rigar sa ya wanke ya shanyata ajikin Ƙofar toilet dan ta ɓaci yayi saura daga shi se dogon wandon Jeans ɗinsa da singlet.
Ya ƙaraso gabanta ya tsugunna ya kamo hannunta duk da yaji zafin abin da tai masa Musamman ƙaddararran auren sa data Furta wannan kalma tai mai zafi ba kaɗan ba amman hakan bai hana shi Jin tausayin halin data ke Ciki ba a yanzun

"Da ina da ina ke maki ciwo sannan kuma shi wannan Aman yau she kika fara?" ya faɗa yana kallonta da kulawa.
"Ni ba inda ke min ciwo amai kuma ban san adadin Lokacin dana fara ba ina ga maleria ke damuna daman haka take min ko a gida"
Bai magana ba ya tashi ya dawo kusa da ita ya zauna.
"Fatima" yaja sunan a hankali.
"Ummh" tace batare data kalle shiba.
"Nifa ba sa'an ki bane bai dace ki dinga min magana yadda kika ga dama ba danna Miki faɗa shine zaki ce da aure na ƙaddara, Yes ƙaddara ne kamar yadda kika faɗa ai daman komai kika ga ya sami bawa ƙaddarar shice sannan idan kika ce zaki fallasa aure na dake Ba damuwata bace Ke nake tausayi dan ba zaki iya rayuwa babu niba danna tabbata daga ranar da Ammi ta sani to seta rabamu shiyasa nake lallaɓawa har Allah ya kawo mana mafita, amman in kika tona shi kece a ruwa ni ina da matata"
Ya faɗa hankalin shi kwance kuka! farha ta fashe masa dashi.
"Nima ba abar tausayi bace tunda idan naje Gida salim ze dawo na aure shi"
Aliyu ya saki Murmushin Na miki illah.
"Ke mai yasa wani bin baki da hankali ne wani mahaukacinne ze aure ki a yanzu to nima jahadi nayi ai dana aure ki Idan ma zaki nutsu ki Nutsu ba wani salim daze aure ki ai ɗan halak ne shi idan kin manta rashin albarkar da kika masa shi bai manta ba"
Kuka take sosai dan ya ƙular da ita da wannan maganar daya gaya mata gwara ya saka bulala ya zaneta.
"Nima Allah ze kawon mafita Kuma wallahi bazan zama abar tausayi ba, dama ko baka gaya min baka sona ba ai na sani haka rannan kace kada naci muku abinci baka san abin yana cimin rai ba ko" Aliyu dariya ta bashi Yadda take acting se yaji duk ta kawar masa da takaicin data ƙunsa masa.
"Eh mana amman dai kin dena cin abincin ko? kin siyo garin kwaki kin mana yajin abincinmu" Pillow ta ɗauka ta kwaɗa masa ya cafe yana haɗawa da hannunta ya janyo ta saman cinyarsa se Kuka take yahau shafa gadon bayanta.
"Shiii to kukan ya isa yanzu gaya min me yake sakaki amai, ki daina min rashin Kunya ni ba sa'an ki bane in ba haka ba Magana ɗaya tak da zan miki zata saka ki kuka ba adadi"
Ya faɗa cikin yin ƙasa da Murya yana laluban zip ɗin rigarta Da dubara Aliyu ya cire mata rigar Jikinta.
"Subuhanallahi Ya Allah........!
Ya faɗa muryar shi a shaƙe Lokacin daya ci karo da cikakken ƙirjinta wanda ya cika ya batse har tsone masa idanu yake.
Ya lumshe ido tare da Buɗewa ya ƙura musu ido babu ko ƙiftawa tabbas yaga sauyi a tare da yarinyar Cikin rashin controling ɗin kanshi ya kwantar da ita yana ɗora fuskar shi a tsakiyarsu yana goga mata sajen shi mai haɗe da gemu a wajan Lumshe ido tayi tana shafa kanshi bata taɓa jin daɗin abin da yake mata ba se yau ɗago kanshi yayi wanda da sauri ta janyo kan nashi ta ƙara mayar wa kamar zata fashe da kuka matso da kan nashi yayi daidai saitin bakinta ya haɗe da nashi ya shiga sarrafa dukkan inda yaci karo wani Irin nishaɗi Aliyu ya tsinci kanshi aciki sakamakon haɗin kan da Farha ta bashi abin da bai taɓa samu daga gareta ba tunda yake

zuwar mata da lalurarshi se yau ada har kuka take tana Raki amman yau tsit kake  ji kuma sun jima suna Tare seda kowannen su ya sami Nutsuwa ya ɗagata duk Jikinta ya saki ya kaita Bathroom da ƙyar tai wanka sabida bacci Shikam zama yayi tare da zabga tagumi bayan ya tsarkake Jikinsa yana kallon yadda take ta baccinta hankali kwance.
Wajan 11 na dare ya gaji da zaman ya miƙe ze tafi Farha ta riƙo hannunshi tana Murzawa Ta kwaɓe Fuska tana kallon shi.
"Cika ni zan tafi dare yayi ba anan zan kwana ba"
Kukan dake taso mata ta danne, dan ƙari take so sedai kunya ta hana ta tai magana kada ya rainata.
"Zan ci wainar fulawa mai mangyaɗa da tumatur da albasa da yajin tafarnuwa"
Ta faɗa tana Lumshe ido ya zuba mata ido na ɗan Lokaci kafin yace.
"Tashin hankali da wannan daren fatima ki bari da safe se Hajja tayi miki amman ni ina zan sami waina"
Aikuwa ta haɗe rai ta soma hawaye tare da sakin hannun shi ta juya masa baya.
Fita yayi daga ɗakin batare daya yi mata magana ba alamunta suna masa yanayi da na masu juna Biyu idan har ya canka daidai dan haka mami ke masa tsurfa kala kala idan tana da ciki shikuma yayi ta Biye mata dan haihuwar yake so.
Hannu ya ɗaga adaidai Ƙofar daze Fita daga falon Ammi yana addu'ar Allah yasa Abin da yake zargi ne kuma Allah yasa rabon sa ne ya inganta masa da wani irin ƙarfin gwiwa ya nufi parking space dan ya samo mata abin da take Muradi ɗin.......

Yana fita farha ta kwanta a saman gado tana kuka wiwi tasan baze samo mata wainar ba kuma ita idan bata ciba ba zaman lafiya Numfashin ta har wani Ɗaukewa yake ta rasa mai yasa a kwanakin nan duk abin da ta ƙwallafa rai akan shi idan bata samu ba se taji kamar zata Mutu, Kuka take tasan ai kawai Morar jikinta yake ba son ta yake ba bare ya damu da abin da take so Kukan da tayi ne ya haddasa mata zazzafan ciwon kai mai zafi wanda kafin kace Me ta dinga karkarwar sanyi zazzaɓi ne mai zafin gaske ya rufeta zuwa wani Lokacin Idanunta ya Lumshe ta shiga jan Numfashi da ƙyar Jita ke kamar Kwananta ze ƙare...............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 65*

Cikin wata baƙar ferari488 ya shiga mai azababban kyau ya kunnata ya tada ita ya nufi bakin gate da sauri yake danna horn masu gadi suka tawo aguje suka buɗe masa ƙaton gate ɗin ya saita kan motar ya fita zagaye yake a saman titin Ƙofar na'isa to shi ina zega masu siyar da waina har wajan 12 na dare yana saman kwalta gaba ɗaya jiyay hankalin sa ya tashi bashi da sauran Nutsuwa idan bai samo mata abin da take so ɗin ba a tal'udu ya tsaya wajan wasu ƴan daudu ya siya mata soyayyar awara daya ga suna soyawa ya tambaye su ko suna saida waina suka ce ta ƙare daya ke da face mask a fuskar shi wadda dama yana da ledarta acikin ko wace mota tashi shiyasa ba wanda ya gane shi seda ya karɓi awarar ya koma mota sannan ya lura ashe shirt ɗin sa ma daya ɗauka a ƙofar Toilet ya saka sanda ze fito a baibai ya sakata dan tsabar yadda ta ɗaga mai hankali Driving yake yawanci Sahu ya ɗauke damma cikin gari ne

suna hirar dare Cikin yakasai ya shiga kai tsaye gidan Umma Suwaiba ƙanwar Babanshi wadda Mijinta ya rasu yabar ta da marayun ƴaƴa mata da maza wanda mazan Aliyu ne ya ɗauke su aiki a kamfanin sa matan kuma ya aurar mata da uku saura biyu ƴammata a gabanta.
A ƙofar gidan Umma suwaiba yayi parking ya fito samarin ƴaƴanta suna ƙofar gida da abokansu suna hira irin ta matasa Daga ƙofar gidan kuma an ɗan karo ƙofar Aliyu ya wuce su ya Shiga gidan bakin sa da sallama Hasken ƙwan solar daya sa aka haɗa musu ya haske tsakar Gidan Falon ya shiga ya zauna Umma suwaiba dake zaune a saman darduma da carbi a hannunta ta Zubawa Aliyu ido bayan ya zare face mask ɗin taɗan saki Fuska.
Ya zamo daga kujerar daya zauna.
"Umma ina yini"
Cikin mamaki take amsa gaisuwar wadda bayan ita yaja baki yayi Shuru yana matsa hannun shi domin ya rasa ta inda ze fara maganar ma.
Umma suwaiba ta dube shi hankalinta a ɗan tashe.
"Aliyu lafiya kuwa da wannan dare ko dai wani abunne mai ya faru a cikin gidan?"
Ta faɗa aɗan gigice, ya shafa kai yana Duba wayar shi sha biyu da kwata har tayi.
"Umma yaran ma sunyi bacci bara naje kawai" da sauri ta katse shi "Kamar yaya lafiya?" cike da jin nauyin ta yace.
"Wai waina aka taso ni nema Umma wainar fulawa da man gyaɗa da tumatur da albasa da yajin tafarnuwa da wannan daren" washe baki umma suwaiba tayi tare da ɗaga hannunta sama.
"Alhamdulillahi Ya Allah ka tausayawa wannan bawa naka Ya Allah kasa wannan rabo tabbatacce ne, Bari na soya mata Allah sarki mami Allah ya raba lafiya kasan mai juna Biyu idan tana son abu in bata samu ba babu zaman lafiya" Shidai bai ce komai ya sunkuyar da kanshi ƙasa gaba ɗaya jinsa yake kamar bashi ba yanzu ya ƙara tabbatar da zargin sa na Yarinyar can ta sami cikin sane amman duk da haka ze ɗauketa suje asibiti Ya lumshe ido lallai Allah Shine tabbataccen sarki a ɗan zaman su wanda baifi na sati Biyu ba har Rabon ciki ya Shiga tsakanin Su wato Rabon haihuwa dashi ne ya haɗa su Rabon haihuwa dashi ne yakai ta aikin jarida Rabon haihuwa dashi ne yasa ta Bijirewa Iyayenta da masoyinta ta zaɓe shi Lallai Rabo dangin Ajali ne Idan Ya Rantse se me shi lallai RABO YA RANTSE! A tsakanin shi da fatima Jiyay yana masifar ƙaunar abin da ke cikinta wata irin murna da farin ciki yake ji jiya ke kamar akan ta ya soma ganin cikin shi yana son duk abin da ke cikin nata wani irin tausayin yarinyar yaji ƴar ƙarama da ita tana ɗauke da cikinsa ta rabu da kowa nata sabida shi gaba ɗaya Jikinsa sanyi yayi har Umma suwaiba ta kawo masa wainar bai gama dawowa daidai ba, komai daya ce ta haɗa a saman wainar yayi mata godiya ya ɗauki kular da wainar ke ciki Umma suwaiba har soro ta bishi tana faman yi masa addu'a da fatan alkairi ya fita se lokacin Yaƴan Umma suwaiba suka gane shi aikuwa suka taso suna gaishe dashi sukai sallama ya shiga mota se Gida Lokacin ƙarfe ɗaya ta kusa yana shiga gida ɗaya nayi Ya kashe Motar ya ɗauki Ledar takeaway ɗin awarar da kular wainar ya shiga sashin Ammi ya buɗe ƙofar falon da key ɗin Jiki tunda an gyara ƙofar falon duhu dum ɗum ya lalubi Kofar ɗakin nata ya buɗe ya shiga ciki har Lokacin da haske a ɗakin Da alamun bata kashe ƙwan ba ya aje kayan hannunsa ya ƙarasa bakin gadon ya zauna ya Sanya hannunsa ya ɗagota Jiyay jikinta kamar gaushin wuta se faman Nishi take.
hankalin shi a tashe ya shiga cewa.
"Fatima ke fatima yaya zaki min haka gafa wainar nan na samo Miki tashi kici"

Lumshe ido tayi tare da ɗora kanta a kafaɗar shi tana jan Numfashi tana hawaye.
Muryarta a hankali take masa magana
"Ni kabani wainar naci yunwa nake ji"
Ɗagata yayi ya saukar da ita ƙasan carpet ya ajeta ya ɗauko wainar da awarar hannun shi har rawa yake ya shiga Buɗe wainar sedai tana jin ƙamshin ta se ta miƙe aguje amai taita sheƙawa a banɗaki ya taimaka mata ya gyarata ta fito tana dafa bango.
"Ka fitar min da ita bana son ƙamshinta"
Aiki ja ya faɗa a ranshi lallai ciki a gaishe shi duk wahalar da yasha kafin ya samo wainar nan amman ance ba'a ci ya fita da ita.
Ya karya muryar shi.
"Haba fatima nasha wahala kafin na samo dan Allah kici ko kaɗan ce"
Ta zauna ajikin gado tai sama da kanta kafin ta saka hannu tana toshe hanci"Ni bana so nace ka fita da ita in ba zaka fitar ba ni sena bar maka ɗakin" da sauri ya rufe wainar ya aje saman madubi "To yanzu me zaki ci?" se faman nishi take daga gani ƙarfinta ya ƙare sabida aman da take ta faman yi awarar ya tura mata gabanta cikin tsoro yana addu'ar Allah yasa taci ga mamakin sa se yaga ta saki fuska ta kalle shi "Dama ita nake so kuma yanzu" bai ce mata komai ba ya zuba mata ido duk ta sauya masa, taja awarar tana ci hannu baka hannu ƙwarya kamar wani ze ƙwace mata duk yawan awarar seda ta cinyeta tsaf tayi hamdala "zan sha  ruwa" ta faɗa tana lumshe ido ya tashi yaje fridge a falo ya ɗauko mata ruwan tana kallon ruwan ta taɓe baki "Ba lemo?" yaɗan kalleta "Wanne kike so Gimbiya?" ya faɗa yana kallonta "Coca cola nake so" da sauri yaje ya ɗauko mata irin babbar nan, ya kawo mata Ruwan ta buɗe ta ɗauki Cup ɗin Kusa da ita ta buɗe coc ɗin ta zuba a cup ta ƙara ruwa ta shanye daga haka se bacci a wajan ta dinga bacci Ya tattare komai data bari ya gyara wajan Ruwa ya taro a bawo da ɗan towel ya ɗagata ya mayar saman gado ya cire mata kayan jikinta ya shiga goge mata Jikin nata da ruwan sabida zafin da Jikinta ya ɗauka ruf da ciki tayi a saman cinyar shi ta saka hannu ta zagaye Ƙugunshi kanta yana daidai cikinsa ta cigaba da baccinta Da dubara ya sauke bawon da towel ɗin ya jingina da jikin bango har asubahi Aliyu bai rintsa ba yana zaune ita kuma tana jikinsa baccinta take hankali kwance..............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 66*

Rasa yadda zeyi ya zareta daga jikin sa yayi sabida baya son yayi Missing Jam'i a hankali kamar mai tsoron kada ta farka ya ɗagata ya ɗora kanta saman Pillow ya kwantar da Jikinta a saman gadon ya sanya ƙaton Devut ya rufe mata Jikinta dashi ya yunƙura ze tashi ta riƙo hannunsa ya leƙa fuskarta Idanunta a lumshe yake sedai ta ɗan turo bakin ta gaba Ya ɗanyi Murmushi wato acikin Baccin ma se anyi tsiwa
Ya zame hannunta daga cikin nasa Ya sauka daga saman gadon ga mamakin sa se yaga ta tashi zaune ta ɗan kalle shi.
"Ina zaka tafi Kuma ni wallahi bazan zauna ni kaɗai acikin ɗakinnan ba ga sanyi ga tsoro"
Ya bita da kallo kafin yaɗan langwaɓe kanshi muryarshi Very cool, yace mata.
"Sallah zan je nayi Kimin afuwa"

Daga haka da sauri ya buɗe Ƙofar ɗakin nata ya fita Cikin sauri ya Karasa masallaci a bakin masallaci Yayi alwala ya shiga ciki Lokacin ana ƙoƙarin tada sallah ya bi jam'i bayan sun idar ya jima yana zaune baya tunanin ya koma wajanta saboda yana son fita Office yasan idan ya koma kuma wata rigimar ce sabuwa sedai kuma ya shiga tunanin abin da zata ci Jikinsa ba ƙwari ga rashin bacci ga gajiya haka ya ƙarasa part Ɗinsa ba kowa a falon da alamun Mami bata tashi ba Saman shi ya wuce yana shiga ɗakin sa ya faɗa wanka ya fito Jallabiya kaɗai ya saka ya ɗan fesa turare sama sama ya kwanta ba jimawa wani bacci mai daɗi ya kwashe shi..

Jikin mami yana wani irin mazari ta shiga ɗakin ta tare da danno Ƙofa ta sanya Key ta shiga Kiran mamanta Tajira tana zaune tare da wata ƙawarta taga kiran Mami ta ɗaga tana cewa
"Yaya aka yi kike ta jera min kira da wannan Lokacin?"
Mami ta share zufar data karyo mata cikin sauri tace.
"Mama ba kanta fa akwai matsala"
Da sauri tajira tace.
"Matsalar me kuma sarkin ƙorafi ba dai za ki barni na huta ba"
Mami ta ji gabanta ya faɗi haka dai ta danne ta soma cewa.
"Wallahi mama aiki ya sami tangarɗa dan Aliyu yaci abincin Ammi yau ni bamma san yadda zan ba kaina gaba ɗaya ya ɗaure"
Zumbur Tajira ta miƙe tare da shiga cikin ɗakinta.
"Me kika ce mami wannan wace irin banzar magana ce maganin da muka tsallake tsaunika sahara Burji muka karɓo shine zaki ce Aliyu yaci dan ubanki asarar Kuɗina nayi kenan kome?"
Kuka mami tasa ta soma cewa
"Wallahi mama nayi iya yina akan kada yaci amman shi seda yaci Ni babban tashin hankalina ma kada Aliyu ya mutu koya sami matsala"
Tajira ta kwashe da dariya.
"Ah lallai laila majnun! tattabara uwar soyayya ai ba zaki gane barno gabas take ba har se ya danƙaro Miki kishiya ni ina ruwana da wani Aliyu yaci Allah yasa ma gaba ɗaya su Mutu gayyar tsiya mu huta"
Mami tai saurin cewa

"A,a mama Ammin dai ta Mutu amman ban da Mijina yanzu Mama meye mafita?"
Tajira tace "Ai cigaba da danƙarawa matsiyaciya dan dai kuskure ɗaya nasan baze hanata sheƙawa barzahu ba kada ma ki damu shima inda rabon ajali yaci can gasu gada"
Mami bata ji daɗin furucin mahaifiyarta ba ita tana son Mijinta kuma tana son su rayu tare saɓanin mahaifiyarta da kawai daula da dukiyar take hange ba komai ba sallama sukai mami ta kashe wayar anan tai kwanciyarta tana saƙa wasiƙar jaki har dare ya raba ta kasa bacci Kuma ta kasa tinkarar ɗakin Aliyu sabida shakkar sa take tunda yace mata idan yaci ze Mutu shikenan taji tana shakkar Tunkararsa a taƙaice anan ta kwana wanda se asubah bacci ya ɗauketa ba ita ce ta farkaba se bakwai na safe tai sallah ta Kuma komawa Baccin nata.

Da ƙyar Farha ta tashi taje toilet alwala ta ɗauro a zaune ma tayi sallah sabida yanzu kuma ƙafafunta ke mata wani irin ciwo jita ke kamar ana sara mata su wainar jiya daya aje a saman madubi ta ɗauka a haka ta dinga cusawa tana ci duk da tayi yami amman ita tai mata daɗi tana

gama ci ta koma gado se Bacci Hajja data zo aikin safe ta leƙo ɗakin ganin Farha na bacci ne yasa bata tashe taba ta shiga kitchen ta soma haɗa musu abin karyawa wajan ƙarfe goma sakina ta fito falon lokacin hajja tana tsaka da jera kayan kari a dining suka gaisa da sakina wadda ta zauna a saman Kujera sakina ta ɗan dubi hajja tana cewa.
"Dan Allah Hajja ina wannan yarinyar ta jiya?" Hajja tai Jimm kafin tace "Oh fati tana ɗaki bacci take dan Jiya tasha aiki"
Sakina ta ɗan kalli Hajja se kuma tayi shuru can kuma tace "Taso min ita tayiwa yarana wanka zamu fita ne Nida Jamila zamu je gidanmu" Da Hajja har zata yi magana se kuma ta fasa ta kama hanyar Kofar ɗakin Farha da ƙyar Hajja ta farkar da ita daga baccin sabida baccine mai nauyi "Tashi fati zaki wa ƴaƴan sadiƙ wanka inji Hajiya sakina tana jiranki a falo" Idanu jajir Farha ta miƙe Jiri ke ɗibarta Wanka tayi sama sama ta fito Doguwar rigar material ta saka tare da yafa ɗan ƙaramin Mayafi a saman kanta wanda ya tsaya iya wuyanta Doguwar rigar ta karbi surar Jikinta domin daga ƙirjinta ta kamata daga ƙasa ne ta buɗe ta ɗan fesa turare kaɗan ta fita falon tunda ta fito sakina ta zuba mata ido haka kawai aranta take jin yarinyar batai mata ba ita dai Farha a gaban sakina ta tsugunna tana gaishe ta a yatsine tace.
"ki shiga bedroom ɗin da muka kwana ki gyara mana shi ki wanke mana toilet sannan kiwa yarana wanka"
Daga haka sakina ta tashi tabar Farha a wajan
Cije baki farha tayi domin yadda ƙafafunta ke ciwo ba zata iya sunkuyon wankin banɗaki ba sedai babu damar ta musa cibi ya zama ƙari haka ta miƙe tayi hanyar ɗakin da sakinar ta umarce ta a bakin ƙofar ma seda ta ɗan tsaya tana cije baki kafin ta tura ta shiga ciki bakin ta da sallama Wannan budurwar da suka zo tare da sakina ce zaune a saman sopa ta bawa ƙofar baya tana waya tana dariya kalma ɗaya Farha taji Budurwar ta faɗa wadda ta sanyata taji ƙafarta ta sage.
"Aunty da alamun nasara fa Aliyu yaje lagos tare ma muke dashi yanzu haka ina gidansu Ku dage Aunty ba mamaki na zama Amarya" Sum sum farha ta wuce Toilet tana wasi wasin maganar Budurwar Giftawar Farha yasa jamila ta aje wayar tabi Farha da kallo kafin ta kirata tana cewa.
"Ke zonan agidan ku ba'a koya Miki sallama bane?"
Farha ko kallon jamila bata yi ba dan ƴaƴan gida ba zasu raina mata hankali ba sannan wata can daga wata uwa duniya itama tazo ta raina mata hankalin ta ɗauka ba Wankin banɗakin ta fara tana gamawa ko kallon Ƴaƴan da sakina tace tayi wa wanka batayi ba tayi ficewar ta dan yadda take jin jikinta idan har tai musu wankan zata iya cutar kanta Tazo ta wuce ta gaban jamila wadda take ta faman Cewa ke! ke! farha tai mata banza tana fita falon sakina ce kaɗai har Lokacin kitchen ta wuce wajan Hajja tai zamanta aciki amman ƙasan zuciyarta tana Allah wadai da munafurcin wasu mazan ashe Lagos ɗin daya biya wajan waccan Guzumar yaje ita kam wallahi ta dena bashi Jikinta sedai ya saketa dan ba zatai Kishi da waccan Guzumar ba ita kaɗai se cika take tana batsewa Ƙiris take Jira ta fashe dan tsananin yadda take jin zuciyarta................*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 67*

Idanunta har wani ruwa ya tara na ɓacin rai bakin ta na mata wani irin ɗaci ita sam bata son Munafurci me yasa baze gaya mata Ƙanwar matar yayan sa Budurwar sa bace amman ko a fuska bai nuna mata ba ita bata Kishin Mami dan matar sace kuma zuwa tayi ta tarar da ita sannan kuma Alkairi yana kore sharri mami ta sota ta jata ajiki dan haka ko a zuciyarta bata jin zafin mami dan ita ya dace ma mamin taji zafi tunda ita ta aure mata Miji amman da Hanan ɗin data ji yana waya da ita rannan da waccan Guzumar wallahi sedai a ƙone muddin yace ze auri ɗaya daga cikin su ba zata zauna dashi ba dama yace Ita yake tausayawa shi yana da mata to taji gwara son shi ya kasheta data yarda ya auro mata su.

"Fati lafiya se faman jijjiga ƙafafu kike yi taso Muci abinci"
Ta girgiza kai tare da cewa.
"Hajja na ƙoshi bar abincinnan" Sabida ko sha'awa ma bai bata ba Hajja ta bita da kallon tausayawa se kuma ta soma rarrashinta
"Fati ban taɓa ganin ki a irin wannan yanayi ba idan ɓata miki rai akai aciki kiyi haƙuri watarana se labari maraici ne duk yaja miki hakan"
Hannu ta sa ta rufe fuskarta nan da nan hawaye ya soma wanke mata Fuskar tata wani irin kuka take mai cin zuciya dan har zafi ƙirjinta ya soma yi mata tunda take kuka bata taɓa mai zafi irin wannan ba Hajja tasowa tayi wajanta tana rarrashinta itama hawayen take yi sabida yadda take ƙaunar Farha jinta take har ranta seda tayi Kukan mai isarta sannan ta miƙe ta wanke Fuskarta ta nufi hanyar fita don ta koma ɗakinta.

"Fati ga ruwan shayin naki ki tafi dashi kya zauna haka baki ci Komai ba" cewar hajja farha ta juyo tace "Hajja bana jin daɗi anjima amman zan sha" daga haka ta juya ta fita falon wanda Yayi daidai da sanda Bashir Shima ya shigo shida Sadiƙ Daga cikin falon Kuma Sakina da jamila ne wadda take faɗawa Sakina rashin Mutuncin da Farha tayi mata.
"Yanzu bata wa su Hidaya wankan ba kome?" cewar sakina
"Bata musu ba yaya ai wannan yarinyar inaga se mun gyarata kafin Mubar gidannan wallahi"
Adaidai nan farha ta Zo zata wuce ta shiga ɗakinta Da wani irin sauri Jamila tayo kanta wani tsalle farha tayi tare daja baya ganin Jamila na ƙoƙarin kawo mata mari.

Cikin sauri Bashir yace
"A,a jamila mai tayi Miki kuma fisabilillahi zaki dakar Musu Ƴa"
Da jin haushi a saman fuskar jamila tace
"Wai wannan kucakar yarinyar harni zan mata magana tai Mini banza dan ubanta" da sauri sadiƙ dake haɗa tea a dining yace "A,a jamila ban da zagin mahaifi Ke kuma shige ki tafi ɗakin ki"
Ya dubi farha Jamila ba yadda ta iya haka ta tsaya tana jan ƙwafa sakina data ji zafin abin da sadiƙ ya faɗa akan farha da sauri ta Taso tayo kan farha tana cewa.
"Tunda An hana jamila taɓa ki Ni bari naji uban daya hana kiwa ƴaƴana wanka komu sa'annin kine?"
Bashir yayi saurin katseta cikin Jin zafin abin da suke wa yarinyar "Haba Aunty sakina wannan ba girman ku bane ina yarinyar nan zata saka kanta ke Kina mata ƙanwarki ta gama mata kuma

kowanne acikin ku mahaifanta yake zagar mata talauci hauka ne Ina ne ba'acin arziƙi dan tazo gidannan aiki ba yana nufin ta zama jaka ba"
Bashir ya faɗa cikin Fushi dan dai bai da hurumin hana sakina ne daya nuna mata ƙarfin namiji da mace ba ɗaya bane.
"Bashir ba zaka gane ba wannan matsiyaciyar yarinyar tun jiya take mana kallon banza bara na nuna mata akwai tazara a tsakanin mu na zaneta na ɓallata na watsar da ƴar iska karnuka su cinye ƙashin Ƴar banza"
Cikin Fushi farha tace.
"Sedai karnuka su cinye ƙashin uwarki da uban ki kuma kece ƴar banza bani ba shasha sha" daga sadik bashir sakina jamila kowa kallonta ya tsaya yana yi se Huci take ta kama Ƙugunta to dama farha ta lafiya ce.
Wani Irin kukan kura sakina tayi tare da shaƙo wuyan farha tana ihu ta cika falon da ihu da ashar.
"Ni zaki zaga dan ubanki baki da tarbiya to bari na gwada Miki bambancin mai kudi da talaka zan karyaki zan La'anta ki dan ubanki"
Sakina tana faɗa ta shaƙe wuyan farha sadik da hankalin sa yayi Mugun tashi ya taso yana jan sakina amman taƙi Sakin farha Bashir kam ya ƙame Sabida takaicin sakina adaidai nan Ammi dasu Safna suka fito falon Da sauri Ammi tayo kan sakina sedai duk Ƙoƙarin ta itama ta kasa cire sakina daga jikin Farha Hankalin Ammi yayi Mugun tashi ganin za'a mata kisan kai agida sam bata san abin da ke faruwa ba cikin ɗaga Murya Ammi take magana.

"Sakina kada ki kashe Musu yarinya In ma wani abun tayi miki sakin ta zaki Muyi magana" Muryar sakina a dashe take cewa.
"Ammi gwara na kasheta nima a ɗaure ni ubana fa take zagi"
Adaidai nan Aliyu da Mami suka shigo falon wanda gaba ɗaya ƙamshin turaren shi na labbra ya cika falon sanye yake cikin Baƙin Boyel mai gidan sukari kanshi ba Hula se haɗaɗɗan Agogo baƙi oyster daya sanya a tsintsiyar hannun shi Ganin Kowa a falon yayi cirko cirko yasa ya ƙarasa ciki da sassarfa jin muryar Ammi yayi tana cewa "Sakina ki cika musu ƴarsu ki rufa mana asiri kada ki mana kisan kai" sakina cikin zafin zuciya ta kuma cewa "Ammi gwara na kasheta nima a kashe ni" se Lokacin ya lura da abin da ya faru da sauri yayi kan sakina ya Finciketa daga jikin farha wadda harta yaga mata Riga zamewa farha tayi ƙasa ta ɗora hannunta a wuyanta tana Wani irin tari kukan kura sakina ta kuma yowa zata kuma shaƙota Aliyu ya taɗeta ta faɗi cikin kakkausar Murya yace.

"Ashe sakina baki da hankali, Ashe baki da tunani kisan kai zaki agidannan kowa yana miki magana kina hauka Okey zoki ƙara shaƙeta ki gani wallahi da sena ɗaure kaf danginku wallahi se kun ƙare rayuwarku a prison marar hankali Kinci darajar auren Sadiƙ wallahi dase na ƙarya ki a wurin nan"
Daga haka ya Sunkuya ze ɗaga farha dan shi idanun shi ma ya rufe dasu ammi na wajan wata irin zabura farha tayi da sauri ta ture masa hannun shi daya kawo Jikinta aguje tayi ɗakinta ta murza key ta faɗa saman gado tari take tayi tana kuka.

Cikin Fushi Aliyu yabar falon Ammi sabida shima idan yace ze tsaya komai na iya faruwa

wannan tasa ya fice daga falon gaba ɗaya yana buƙatar nazari kanshi gaba ɗaya ya Kulle............
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 68*

Cikin Ɓacin rai Ammi tace
"Wato sakina ni ban isa dake ba har na fito ina miki magana ki min banza har kina furta zaki kashe musu yarinya ko, wannan wani irin sakarci ne?"
Cikin kuka sakina data ke zube a ƙasa tun bayan da Aliyu ya taɗe mata ƙafa tace.
"Ammi kamar ni yarinyar can ta kama zagin ubana dan kawai nace tayi wa su hidaya wanka batai Musu ba nazo zan Mata faɗa Abban su ya hana ni har yana cewa ta tafi ɗakin ta to meye tsakanin shi da ita" ta faɗa tana kuka wanda ya nuna cewa Tsananin Kishin maganar da Sadik yayi ce tasa idanun sakina suka rufe take neman halaka farha.
"Innalillahi wa'innah ilaihirraju'un wannan wace Irin annoba Musa ya kawo min gidana tun da nake da sakina bata taɓa min Musun magana ba se yau Tunda Baba yake da sakina bai taɓa Gaya mata magana mai zafi ba seyau har yana cewa ze ɗaure ta wannan wace Irin annoba ce tazo Min gidana ni Amina"

Bashir daya ji daɗin abin da Aliyu yayi shine cikin zafin zuciya yayi magana.
"Ammi ga babbar Annoba nan jamila ai itace Munafukar komai ita ta haɗa har Aunty sakina taso ta kashe yarinyar can wallahi ko yaya Ali bai ɗaure suba ni sena ɗaure su inda sun mata illah"
Bashir ya faɗa a fusace yabar falon Ammi wata irin tsuma ta soma yi tabbas hasashen ta ze zama gaskiya tsakanin Bashir da Aliyu akwai ayar tambaya a tsakanin su da wannan yarinya.
Sadik kam dan takaicin abin da sakina tayi tashi yayi yabar falon Ammi ta kalli sakina cikin sanyin Jiki.
"Ki haƙuri kada ki ƙara Ƙoƙarin Yiwa wani haka nan gaba ita kuma yau zata bar mini gidana base Gobe ba"
Mami takaicin sakina ma ya hanata magana se kawai ta juya tabar falon In ba tsabar hauka ba dan kawai Mijinki yace yarinya taje ɗaki shikenan seki hau Jibgar ƴar Mutane lallai in bata gyara wannan halin zafin Kishin nata ba watarana zata aikata dana sani.

Sum sum jamila ta koma ɗaki Sakina tabi bayanta Shirin fita suka yi ba jimawa suka fito tare da ƴaƴan sakinar sukai wa Ammi sallama suka wuce dama gidansu zasu je dan acan zasu wuni yau suna fita sajeeda taja tsaki.
"Wallahi Ammi Aunty sakina ce bata da gaskiya kuma abin da Yaya Ali yayi shine daidai domin in aka kashe waccan yarinyar harmu abin ze shafa Kishi hauka ne Fisabilillahi daga tashin ta tai mana girkin safe raba kanta uku zata yi ita jamilar uban me take da bazata yi wa su Hidayar wankan ba" Ammi ɗagawa sajeeda hannu tayi alamun bata son maganar kafin ta miƙe tabar falon ɗaki ta shiga ta ɗaga waya ta shiga Kiran Numbern Aliyu.

Kiran duniya Ammi tayi masa yaƙi ɗauka seta shiga kiran Number ɗin Bashir wanda ya fito cikin

shirin fita Office.
"Kazo ina son ganin ka"
Daga haka ta katse wayar Bashir ya ƙaraso ɗakin Ammi tana zaune a bakin gado har Lokacin Numbern Aliyu take Kira Amman bai ɗauka ba.

Bashir ya zauna a gabanta yana kallonta.
"Dan uban ka meye nufin ka akan yarinyar can? har da zaka wa sakina rashin Kunya akan ta?" Bashir ya ɗaure Fuska "Ammi ni fita zanyi idan na dawo mayi maganar Nidai nasan a bayan gaskiya nake ita jamilar bata da gidan uba da zata biyo yayarta nan zata haɗa mana rigima agida" Ammi tayo kan Bashir cikin hargowa "Dan ubanka kai ma nan ɗin gidan uban ka ne ba gidan baba bane Kai idan kana da kunya zaka kalli ƙanwar matar ɗan uwanka ka zageta akan bare To bari kaji idan ma akwai wata manufa a zuciyarka ka cire ina nan yadda nake ban sauya ba" Gaban bashir ya faɗi Dan jin soyayyar yarinyar yake kamar ranshi haka ya miƙe yabar ɗakin Ammi cikin sanyin Jiki.

Aliyu yana fita daga falon ammi waya ya samu daga mai girma gwamna da gaggawa akan zasu shiga meeting duk da ɓacin ran dake cikin zuciyar shi hakan bai hana shi amsa kiran mai girma gwamna ɗin ba cikin wata Red colour mota ƙirar samfirin Mcleran 75os ya shiga yayi revers ya nufi bakin gate da sauri masu gati suka Buɗe masa gate ya fice aguje kamar ze tashi sama Yana driving kiran sadiƙ na shigo masa da ɗayan hannun ya ɗaga wayar ya kara a kunnen shi cikin damuwa sadik yace masa.
"Aliyu dan Allah kayi haƙuri da abin da sakina tayi naga kamar ranka ya ɓaci wallahi tun kafin kazo nake magana amman da yake ta rainani bata jiba"
Aliyu yaja ƙaramin tsaki tare da cewa
"Kada ka damu, Ni dai ka jamata kunne koda wasa kada ta kuma gigin taɓa ƴar mutane dan tana taimakon Ammi baze zama ticket na kowa ya dake ta ko ya zageta ba, Ya sadik wallahi dan dai matarka ce sakina amman da yau seta yi kwanan cikin cell dan ban ga abin da ƴar mutane tayi mata ba da zata shaƙe ta"
Sadik daya cika da mamakin furucin Aliyu wanda yake nuni da kamar yana da wata alaƙa da yarinyar yace.
"Kayi haƙuri zan ja mata kunne, sannan kai ma kayi wa yarinyar faɗa a matsayin ka na uban ɗakin ta ta dena wa manya rashin Kunya dan sakina ba sa'arta bace"
Aliyu yayo wa sadik ka tare da ce masa.
"Dan Allah malam kai min shuru sakina sarki ce da dole seta bita zagi inta zagi sakina So what wadda tafi sakina ma ana zagi bare ita Nidai na gaya maka wallahi ka jawa matarka Kunne kada ta sake Gigin dukan ta in banda ma ɗaukar hakki yarinyar nan guda nawa take dubi sakina ƙatuwa ta shaƙe ƴar cikinta dan Mugunta"
Sadik sakin baki yayi amman sabida tsabar haƙuri irin na sadik bai ce komai ba se can yace.
"Kayi hakuri Ba zata kuma ba, Amman wannan zaƙewa taka tai yawa akan yarinyar anya kuwa?"
Aliyu yayi saurin katse sadik dace wa
"Lafiya lau kasan ni bana Ɓoye al'amurana ni zalinci kaɗai shine bani so dan Allah kada hakan

ta kuma faruwa" Daga haka ya katse wayar yabar sadik cike da al'ajabi Sadik yayi tagumi yana nazarin maganganun Aliyu wanda ko matarsa iya abin da zeyi idan an taɓa ta kenan Yasan Aliyu baya shiga abin da ba ruwan shi but amman yadda yaga yayi ruwa da tsaki akan case ɗin wannan yarinyar abin yaɗan Bawa sadik mamaki duk da shima ko kaɗan bai goyi bayan sakina ba amman yana son itama yarinyar ta dinga saita bakin ta dan gashi nan garin rashin kunya tasha matsa a banza.

Tashi sadik yayi da zummar zuwa ya shatawa sakina Layi akan Yarinyar Tare da gargaɗin ta akan kada ta kuma taɓa musu yarinya sedai yana zuwa Ammi tace masa sakina sun je Gidansu da Jamila A wajan Ammi sadik ya zauna suna maimaita abin da ya faru shidai duk bai ji dadin hakan ba musamman da yadda yaji Muryar ɗan uwan shi cikin ɓacin rai.

Aliyu bayan sun gama Meeting sallah yayi ya wuce kamfanin shi manyan Buhunnan shinkafa tare da katan katan na taliya macaroni maggi manja man gyaɗa shine Aliyu yasa musa ya firfito dasu domin rabawa ma'aikatan kamfanin shi sabida gabatowar watan azumin ramadan wanda za'a shiga Gobe idan Allah ya kaimu za'a tashi dashi har la'asar suna aikin fitar da kayan abincin wasu ankai gidan marayu wasu an kai gidan yari wasu ankai makarantun allo sannan yazo ya ware na gidajen ƴan uwa da maƙota duk aka zuba a mota se bayan magariba ya sami Nutsuwa Lokacin ko driving bayajin ze iya da kanshi, Musa daya dawo daga kai saƙon Gidansu farha wanda suka je da abokin shi kamar yadda yake yi idan Aliyu yace yakai saƙo shiya Ke Driving ɗin Aliyu dan yay droping ɗinsa a gida.

Aliyu dake zaune a back seat ya dubi Musa yana ce masa.............

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 69*

"Musa kun je gidan su Fatiman kuwa Hope everything is going well?" Ya faɗa yana fito da wayar shi tarin Misscall ɗin Ammi reras ya gani yasan kira ne shikuma tunda yabar wayar bai ɗauka ba se yanzu Musa yace "Mun je yallaɓai komai yana tafiya daidai sedai har yanzu mahaifanta sun kasa sakin Jiki da tarin alkairan da kake Musu duk sun tsure kamar yadda Abokina ke Gaya min More especially ma mahaifiyar Fatima gaskiya Abokina yace ta shiga damuwa sosai Duk a tsorace take ga kuma Karin damuwar rashin Yarinyarta"
Aliyu yayi wani murmushi mai sauti tare da cewa "I kon Allah! ka bawa Baba ɗin wayar da sim card?" Musa yace "Eh abokina ya bashi bayan mun sauke musu kayan abincin nasu da na wanda zasu rabawa maƙotan su" Aliyu bai ce komai ba na tsayin Mintuna can kuma yace "Oh bani number ɗin" Musa ya ɗauko wayar shi ya miƙawa Aliyu ya amsa yana copy number ɗin to wayar shi har ya gama ya miƙawa Musa wayar Number ɗin yayi dialing wadda shine yayi ma Musa umarnin daya saya ya bawa Kawu.
Ringing ɗaya tayi kawu ya ɗaga Aliyu ya jingina kanshi da seat muryar shi a hankali yayi

sallama Kawu ya amsa.
"Baba nasan baka gane mai maka magana ba, Aliyu ne Mijin Fatima da fatan kuna nan lafiya?" Cikin farin ciki da kwanciyar hankalin da kawu ya shiga Lokacin daya ji Aliyu yace Mijin fatima ne kawu ya washe baki yana cewa
"Alhamdulillahi Naji dadin jin Muryarka yanzu ina fatiman take?" Aliyu ya jinjina soyayyar da Mahaifin nata yake mata kafin yace "Bana gida, kuna lafiya ko? dama na kiraka ne danna gaya maka ka kwantar da hankalin ka Baba akan kome zaka gani daga wajena Ina ɗaukarku a matsayin mahaifa dan Allah ku saki ranku fatima tana cikin Ƙoshin lafiya kuma zata zo gare ku Very soon cikin farin ciki" Kawu yahau share ƙwalla har Muryar shi tana rawa lokacin da yake cewa "Nagode Nagode Ali Allah yayi maka albarka ada ina ta ɗar ɗar amman jin kamilalliyar Muryarka yasa naji nutsuwa Kuma muna ta ganin saƙo yau ma kayan abinci sun Kuma sauka wasu kan wasu harda na maƙota mun gode ƙwarai" Aliyu yaji Nauyin godiyar kawu seya basar da amsa godiyar yace "Ina mama kuma mu gaisa?"kawu yace bari ya miƙa mata Umma tana ɗaki ta zabga tagumi duk abin duniya ya dameta ita fa kada suje ko kuɗin kan yarsu ake kawo Musu da sunan Kayan abincin kawu yayi sallama ɗakin yana cewa "Ungo Hasiya kuyi magana da Mijin Fatima" umma ta saki ajiyar zuciya ta amshi wayar tun kafin tai sallama Aliyu ya rigata yana kuma haɗawa da gaisuwa cikin ladabi.
Cikin jin nauyi umma take amsa gaisuwar kuma daga jin muryarshi tasan Ba ƙaramin yaro bane dan babu baragada ko shirme a nutse yake gaishe da ita.
"Umma Aliyu ne Mijin fatima na kira ne Mu gaisa kafin nazo Muku da ita dan Allah ki kwantar da hankalin ki wallahi Fatima tana cikin Ƙoshin lafiya kuma komai kika ga na aiko da zummar na kyautatawa mahaifana Nayi muku bada wata manufa ba dan ku kamar iyayena kuke"
Umma ta saki fuska tace.
"Babu komai na Gamsu Kuma in sha Allah zan dena wasi wasi a game dakai nidai ina roƙon ka daka dinga haƙuri da halin Farha yarinya ce mai tsiwa Se an haɗa da haƙuri watarana se labari sannan Muna son zamu turo ƴan uwanta don suga inda take kaga ba abin da akai mata na aure daga cikin abin da ya shafi ɓangaran mahaifa dan haka ina son ƴan uwanta suzo nan su ganta" Aliyu ya Lumshe ido ya buɗe tare da cewa.
"In Sha Allah Mama Fatima ce zata fara zuwa ta gaishe daku,sannan maganar wani abun ɓangaran iyaye kada ki damu komai zan mata ai hakkina ne ina son zanje umara nan da ƴan kwanaki Se bayan sallah inna dawo zamu zo daga nan ma suma zan ɗauke su sesu gano inda take"
Umma cikin Nutsuwa tace

"To angode Allah yayi maka albarka Munga abin arziƙi Allah yasa kafi haka Allah ya raya maka zuri'a"
Cikin alkunya yake amsa addu'ar da umma keyi Masa, Bayan kawu ya amshi wayar Aliyu ya ƙara Kwantar masa da hankali kuma sosai kawu ya sami Nutsuwa da hakan sukai sallama.
Aliyu ya aje wayar ba tare daya kira Ammi ba dan har gabanshi faɗuwa yake inya tuno gida dan yasan Ammi nacan na jiran shi seda ya cewa musa ya tsaya yayi masa siyayyar kayan lashe lashe dana marmari Musa ya fita yaje ya siyo ya dawo mota suka ƙaraso gida A harabar Gidan Musa ya bawa Aliyu keyn motar suka yi sallama da juna seda Aliyu ya tsaya a masallacin Gidanshi yayi sallar Isha'i wadda ake ta kira kafin ya ƙarasa Part Ɗinsa siyayyar ya raba Biyu

ɗaya ya bari a mota ɗayar ya shiga da ita ciki.

Da sallama acikin bakin shi ya shiga Ƙaton falon nashi mami tana zaune a falo tana kallo taci gayu cikin Cgreen material ɗinkin Riga da skirt tasha kwalliya a fuska Jikinta yana tashin ƙamshi da sauri ta ƙaraso wajan shi ta amshi Ledojin dake hannun shi takai dining ta aje tana mai sannu da zuwa

Ya raɓe ta ya haura saman shi mami tabi bayan shi Lokacin data shiga Bedroom ɗinshi yana tsaye yana Cire kayan shi ta ƙaraso gabanshi ta taimaka masa ya cire rigar Jikinshi ta Cire mai agogon dake hannunshi Ta Shiga Bathroom ta haɗa masa Ruwan wanka hatta towel daze tsane Jikinsa seda mami ta aje masa sannan ta fita daga ɗakin

Ƙasa ta sauka ta haɗa masa abinci a dining komai tayi readyn sa sannan ta koma Lokacin ya fito daga wankan yana tsane Jikinsa da ƙaramin towel Mami ta buɗe closet ɗinsa ta ciro masa Jallabiya Brown colour tare da Boxer da singlet ta feshe turare ajikin kayan ta miƙa masa tana tsaye ya saka kayan ta kwashe towel Ɗin daya cire da wanda ya goge Jiki ta kai washing machine ta Gyara masa gadon sa sabida zanin gadon yaɗan yamutse.
"Mamy Allah yayi miki albarka Allah ya Shirya min ke"
Ya faɗa cikin jin daɗin Hidimar data ke masa Don mami mace ce harda ƙari bada ban ya kamata da laifin daya ke binciken ta dashi ba da se yace ko kawo masa ƙararta akai baze yarda ba zece sharri akai mata sabida Halinta na zahiri data nuna masa na Juriya da kirki da kunya.

Gaban mami yaɗan faɗi dan har Lokacin ɗari ɗari take dashi.
"Yaya me nayi kuma da zaka ce Allah ya shirya ni?"
Ya saki wani malalacin murmushi mai sauti.
"Nima kice Allah ya shirya ni zan ce Amin" Ya faɗa yana Lakatar Kumatunta dariya tayi tare da kama hannun shi ta langwaɓar da kanta

"Yaya muje Abincin yana jiran ka"
Ya shafi saman cikin sa.
"Kamar kin san ina jin yunwa"
Yabi ta suka sauka seda Ma suka kai dining sannan yace ta je ta ɗauko mai wayar shi a saman gado ta koma ta ɗauko masa ya amsa ya saka a aljihun jallabiyar shi Sakwara da Miyar ganye wadda taji naman sa irin yankan manya manyan nan ta zuba masa ta tura mai.
Ya yatsina fuska yayi.
"Kin san ban son abinci mai nauyi da daddare kuma ina son sakwara amman dan mugunta baki da da rana ba se dare" Dariya mami tayi tace "To ina ma ka zauna da ranar in da zaka zauna ai da kaga Sakwara" ta faɗa tana dariya ya janyo silver ɗin data zubo masa ruwan wanke hannu ya wanke yayi Bisimillah ya soma ci ƴar kaɗan yaci yace ta haɗo masa Coffee miƙewa tayi ta koma Kitchen ta haɗo masa yasha ya Miƙe ya kalleta.
"Zan je wajan Ammi bana son dare yayi rabo na da ita tun safe"
Dariya mami tayi tana cewa.
"Ai yaya baka taɓa Burgeni ba se yau"

Ya wani zaro mata ido wanda ya ƙara hasko kyansa yace mata.
"Yanzu duk Ƙoƙarin da nake danna Mantar dake komai bana burgeki se yau?"
Mami dariya take sosai har tana Rufe baki kafin tace "Kai yaya kana da fassara marar ƴanci bafa anan wajan ba Ina nufin yadda kayi wa sakina akan Farhan gobe ai ba zata Kuma dukan ƴar mutane ba"
Shima Murmushin yayi tare da cewa

"Okey na gane, to mamy ai abin da sakina tayi bai dace ba, bari naje kada Ammi tayi bacci"
Yayi saurin kawar da maganar sabida baya bawa mami fuskar Kawo masa maganar ƴan uwan shi.
Duk da itama ɗin ƴar uwarshi ce amman kowa ɓangaran shi daban.
"To ka gaida ita nikam yaya Zan kwanta a ɗakina dan Ina Fashin sallah zan sha magani kafin kazo ma inaga nayi bacci"
Ya wani kama ƙugu ya zuba mata ido.
"Kina nufi me kenan ba zaki zo ɗakina ba kome?"
Da gudu tabar wajan tana cewa.
"Bye yaya seda safe"
Sabida tasan nacin sa ko tana Mp ɗin ma seta sha matsa a wajan sa dan seta gwammace kiɗa da karatu..........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 70*

Seda yaga shigarta cikin bedroom ɗinta sannan ya saki ajiyar zuciya mai ƙarfi ya Fita daga Falon bayan ya kashe hasken Falon ya rufo Ƙofar Ko ina haske ne a harabar Gidan ga securities kota ina wani irin daɗi yaji da Mamy ta kawo masa reason ɗinta na ba zata kwana a ɗakin shiba sabida dama a yadda ya tsara ya raba yau ma kwanan Fatima ne sabida Lokacin daze tafiya a ɗakin Mamy yake Yanzu kuma daya dawo Jiya ya kwana a ɗakin Fatima yau ma anan ze kwana Gobe kuma mamy da Jibi dama ya rasa yadda zeyi da Mamy se kuma Allah ya kawo masa mafita Seda ya biya mota ya ɗauko abin da ya sai mata ya shiga falon Ammi a dining ya aje ledojin ya ƙarasa cikin falo Bashir ne kaɗai a falon yana danna waya Aliyu ya kalle shi ya wuce Ɗakin Ammi yana tafiya yaji gaisuwar da Bashir ke masa ya amsa Tare da shiga ɗakin Ammi Ya tarar da ita a zaune a ƙaramin falon ta Tv kunne tana kallon Sunna Tv ya zauna daga nesa da ita yana gaishe ta.

"Ba gajiya baba yaya Isa da kai?"
Ya ji ta faɗa Ya ɗago batare daya gano me take Nufi ba Ammi ta kuma maimaita masa"Nace yaya isa da kanka baka ga Kirana bane Ko har ka kai matakin da zan Kiraka ka ƙi ɗaga wa Baba?" Aliyu ya matso gaban Ammi da sauri ya kama Ƙafafun ta Jikinsa duk rawa yake dajin furucin Ammi  "Ammi kada ki kuma faɗin haka Allah kada ya kaini matsayin da zan Kauce umarnin ki Ammi duk abin da kika ce nayi zanyi muddin bai kauce umarnin Allah ba"
Ammi ta yi dariyar takaici "An ya kuwa Baba nakai matsayin nan tunda inda nakai ba zan ce

kayi abu ba kaƙi yi" da sauri yace "Ammi me kika ce nayi bam miki ba Ammina?" ya faɗa duk hankalin shi a tashe "Cewa nayi ka ce wa Musa yazo ya ɗauki ƙanwar shi dan annoba ce agidannan Tunda nake dakai ban taɓa jin kayi Musayar yawu da matar Sadiƙ ba se akan ta haka kwanakin baya ka kusan kashe ƙannen ka akanta, sannan Shima Bashir naga take taken sa to sabida haka Nidai ba zan sami kwanciyar Hankali ba har se ka ɗauke yarinyar nan daga gidannan In ba haka ba Nida kaina zan sa a samo Min Numbern musa na Gaya masa" ALIYU ya yarfe zufar data ke Karyo masa duk da sanyin Ac'n dake falon Ya kalli Ammi wanda inda ta lura zata hango Tashin hankalin daya shiga amman da yake hankalinta ba anan yake ba sam bata lura ba "Shikenan Ammi in dai matsalar Wannan yarinyar ce kada ki damu, Amman kimin alfarma zuwa bayan sallah kafin nan zanyi mata ɗan alkairi wanda Musa zeji daɗi batare daya San kece kika ce a koreta ba" Ammi ta ɗaga masa hannu "Kada ka raina min hankali Me Yasa ba zaka mata alkairin yanzu ba se bayan sallah kafin nan ta gama min illah a gidana kawai ka sallame ta yau Gobe ta kama hanyarta" Aliyu yaji Gabansa ya faɗi aiko Fatima bata da Cikinsa baze iya korarta ba bare Kuma yanzu da take ɗauke da Gudan Jininsa rabin rayuwarsa Cikin daya Saka rai da shi.
"Ammi ki haƙuri" tayo masa kaa "kai bazan saurare kaba Ai bama kai Musa ya kawowa ba ni ya kawowa dan haka tafiya zatai ba zata zauna min ba" Aliyu yaji ranshi ya ɓaci Mai yasa yawanci Ammi tafi takura shine fiye da kowa "To Ammi duk yadda Kikai daidai ne Allah ya taimaka" daga haka ya Miƙe ya juya zebar ɗakin tasan sarai haushi yaji seta sanyaya Murya "Shikenan amman ana sallace sallah zata bar min gidana" Muryar shi can ƙasa yace "Duk yadda kika ce Ammi"
Yabar mata ɗakin Yana fita falon Jamila ta fito daga ɗakin da suka sauka dan har Lokacin ba'a gyara part ɗin sadik ba sanye take da riga da wando na pakistan kanta ba ɗankwali Zata shiga Kitchen ta tsaya ya ƙaraso zeyi hanyar dining ta sha gaban shi tana wani kaɗa mai Jiki tai ƙasa da murya.
"Aliyu kasan dan kai na sauka a gidannan amman kana ta share ni" Takaici yazo masa wuya wannan wace Irin mace ce marar kamun kai Tun kwanakin baya da sakina tace masa Ga jamila ya aura ko Allah ze sa A dace ta haihu dan su Irin haihuwa ne Buɗar bakin sa ya bawa sakina amsa da cewa Ai mami ma ba Juya bace Allah ne bai tsayar ba Dan Shi gaba ɗaya jamila bata cikin tsarin matan da yake so kwata kwata dan wayewar ta tayi yawa idanunta a buɗe yake shikuma sam baya son macen da idanunta yake Buɗe, bayan nan ma totaly Jamila batai masa ba.

"Idan danni kike zaune anan, Gidan lallai zaki dawwama aciki dan abin da kike Bibiya ba zaki samu ba Idan kika kuma shiga harkata kuma" ya matse yatsun sa suka bada sautin ƙas! ƙas! ya juya zebar wajan ta kamo Gefen Rigarshi tai raurau da ido zatai Kuka ya ɗora hannunshi ajikin rigar tashi ze Cire hannunta adaidai nan farha ta fito yunwa take Ji Kanta har juyawa yake dan azabar yunwa sabida tun da ta Kulle kanta sallah ke tada ita sam bata Leƙo falon ba rabon ta da abinci tun wainar safe idanun farha ne suka sauka akan Shi suna tsaye shida wannan Budurwar Goge idonta take dan ta tabbata abin da ta gani Gizo ne Ko Gaskiya sedai Idanunta ya nuna mata gaskiya adaidai nan Aliyu ya zare hannun Jamila daga rigarshi ya Juya yayi hanyar dining da Gudu ita Kuma jamilar ta Juya ɗaki tana dira ƙafa kamar ƙaramar yarinya se hakan ya Bada style kamar Masoyan da suka rabu cikin shauƙin ƙauna Farha jitai tana neman

faɗuwa wani Irin Kishi mai zafi ne ya taso mata rasa Yadda zatai tayi domin Yunwar ma jitai ta daina Jinta Juyawa tayi ta koma ɗaki wanda adaidai nan kuma Aliyu ya ɗago dan yaji ƙarar Rufe Kofa Ɗaukar Ledojin da ya mata siyayya yayi ya Nufi hanyar ɗakin nata wanda adaidai nan ita kuma ta Jingina da Jikin ƙofa ta ɓare baki tana Kuka kamar Wadda aka cewa Umma ta rasu..............*RABO YA RANTSE! Iittafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 71*

Aliyu Ya Murɗa handle ɗin ƙofar yaji ta a rufe Ya laluba aljihun jallabiyar shi ya ɗauko key sedai koda ya zira shi jikin ƙofar yaji da alamun wani key ɗin ajiki A hankali ya Jingina da jikin ƙofar ya ɗan kara Fuskar shi yana jiyo sautin kukan ta Danna ƙofar yake a hankali yayi magana wadda yake da tabbacin zata jita.
"Fatima ki buɗe min ƙofar wai mene ne hakan?"
Shuru yaji taƙi magana still kukan take yi bata daina yin shiba, Cikin hargowa yace "Wallahi in baki buɗe ba zan sa a ɓalla ƙofar wannan wani irin rainin wayo ne zaki rufe mini ƙofa" Cikin tsiwa tace "Ni bazan buɗe maka ƙofar ba sabida bana buƙatar ganin ka a ɗakina" Murmushi yayi tare da cewa "Please Fatima dan Allah ki buɗe min" turo bakinta tayi gaba tare da Buɗe mai ƙofar da sauri ya tura ya shiga ya maido ta ya rufe tana Ƙoƙarin juyawa da zafi zafi ya janyota jikinsa ya haɗa ta da ƙirjinsa Ƙamshin mayen turaren shi na Labbra ya doki hancin ta wani irin kashe mata jiki ƙamshin yayi har tana neman faɗuwa ƙasa ƙara kamata yayi sosai ya saki ledojin hannunshi ya Turata Jikin bango ya danne mata Kirjinta da ƙarfin nasa ƙirjin Ya kawo fuskar shi dab da tata ya tsare ta da girman Idanunshi Lumshe idanunta tayi dan ko kaɗan ba zata jure wannan Kallon da yake hukunta ta dashi ba Hura mata iskar cikin bakin sa yake mai ɗauke da ƙamshin Mint  a hankali hawaye ya soma fitowa daga cikin idanunta Bai hanata Kukan ba Zubewa tai a jikinsa tasa hannu ta kamo Ƙugunshi wanda ta kasa ritsawa sabida Yadda yayi mata girma Shikuma ya saka Hannu yana shafa gadon bayanta tsawon Minti goma suna a haka kafin ya ɗagota a hankali ya raɗa mata.
"Be quiet and tell me what made you cry, but this cry of yours is too much Fatima" turo masa mitsitsin bakin ta tayi gaba wanda yasa Haƙorin shi yaɗan cije ƙasan lips ɗin nata Kuka ta saka tana dira ƙafafunta ɗagata yayi cak ya nufi gado da ita ya ɗora ta akai tare da sunkuyo wa daidai Fuskarta "Nasan dalilin kukan naki yanzu zan Miki maganin shi" juya mai baya tayi Shikuma yaje ya ɗauko Ledojin daya yar a bakin ƙofa Ya hawo saman gadon ya ajesu Sannan ya miƙe Tsaye tare da cire jallabiyar Jikinshi Rintse idanu tayi sabida yadda Ƙirarshi ta bayyana acikin singlet da boxern daya rage ajikin sa lallai maza ba kunya cewarta cikin zuciyarta Bata tsorata ba seda ya kuma hawowa gadon ya juyo da fuskarta tana facing tashi Fuskar hannu yasa ya shiga buɗe Ledojin ƙamshin kazar data sha gashin Inji ta doki hancin ta Lumshe ido tayi nan da nan yawun bakin ta ya shiga tsinkewa Ya fito da Soyayyan dankali Wanda akai masa ƴar miyar ƙwai a saman shi se tsire wanda yaji Kuli da su Cabbage Haka ya dinga jere mata dukkan kayan ƙwalam ɗin daya siyo mata a gabanta.
"To Gimbiya kici wanda kike so a gado sena ɗauke idan kin gama ci"
Ya faɗa da Murmushi a saman fuskar shi Maƙe kafaɗa tayi tare da turo baki.
"Ummmm ni bazan ciba"

Seta hau masa kuka Yaɗan matsota kaɗan ta kafe shi da ido ko ina na jikinshi gashine kwance hatta cinyarshi wadda take fara ƙar kamar ka taɓa Jini ya fito acikin ta.
"Sabida me ba zaki ciba Pls fati kada ki Hukuntani da rashin Cin abincinnan dan Allah"
Haɗe rai tayi tare da cewa.
"Idan naci damuwar kace, Ba yanzu na ganka da waccan Guzumar ba wallahi an dai Ji kunya"
Ya ɗan ɗage gira se kuma yayi dariya wadda tai masa kyau kafin yace.
"To ina ruwanki niba Mijin mace Huɗu bane, Kika sani ko amarya zan Miki"
Ya faɗa cikin sigar wasa dan yanayin nata ya saka shi acikin Nishaɗi.
"Allah ya kiyaye kayiwa mami dai amman bani ba"
Har Lokacin dariya yake "Ai ke akaiwa mamy Ita kuma ke za'a yiwa"
Juya masa ƙeya tayi tare da cewa.
"Kama sani Wallahi idan ka aureta sena gudu kuma bama gida zanyi ba dan kar ma kaje a maido ni"
Tana faɗa tayi Rub da ciki ta juya masa baya da sauri ya sauke kayan Kwaɗayin daya jere a gabanta Kana ya ɗagota yana cewa.
"Ki daina irin wannan kwanciyar kada na ƙara gani kinyi"
Ya faɗa lokacin daya ɗorata a saman cinyar shi Yana kuma zira hannunshi a ƙasan mararta dannawa yake a hankali yaji ɗan tauri a wajan kaɗan Ta rintse ido tana Cije bakinta a hankali ya sunkuyo da kanshi saitin Fuskarta har Lokacin kuma hannun nashi yana ƙasan marar tata bai cire ba"Akwai zafi?" Rufe ido tayi tana ƙara cusa kanta adaidai saitin Cikinsa Ya kuma raɗa mata "Ki daure ko kazar da yoghurt ɗin kisha Kinji" yadda ya furta Kinji ɗinne ya jefa ta cikin wani hali Kuka take masa ƙasa ƙasa wanda yasa yaɗan susuce kaɗan ya ɗagota yana kallonta "Wai menene haka kita kuka kita kuka tun ɗazu se kace dukan ki nake yi" Cikin Muryar kukan tace "Hannun ka fa naga ka ɗora akan nata Fisabilillahi ba dole nayi kuka ba kwartanci da Mijina da cikin dare" Saka yatsa yayi ya ɗane bakinta kafin yace "Nine kwarton ko ita?" Turo baki tayi "Oho muku nidai aka ci amana ta Allah....." bai bari ta ƙarasa ba Ya ɗora bakin sa a saman nata Ji kake tai Kus tana amsar darasin nashi tsayin Lokuta yana hukunta tata da Kissing lips ɗinta kafin ya ɗauketa ya saukar da ita ƙasan carpet ya shiga yago kazar yana saka mata abakin ta Haka ta dinga amsa tana ci tana Lumshe ido harta ƙoshi takura mata yayi seta sha kankana A wajan shan kankanar seda tayi Kuka dan cikinta ya cika Tana gama sha ya ɗagata Ya kaita tai Brush tare da ɗauro alwala aikuwa tana zuwa ta haye gado se bacci Ya tattare Komai daya zube sannan ya shiga Toilet ya ɗauro alwala Carpet ya shinfiɗa ya soma nafila har wajan ɗayan dare yana saman carpet Kafin ya tashi ya Ninke ya cire jallabiyar Jikinsa ya hau gadon bai takurata ba dan ya fahimci tana jin daɗin baccin janyota yayi Jikinsa ya haɗeta da Ƙirjinsa yaja masu bargo ƙarfe huɗu ya farka sabida sahur dan Gobe za'a tashi da azumin watan ramadan Ba abin da ya iya ci se dabinon daya shigo ɗakin dashi se ruwa marar sanyi sannan ya tashe ta tai sahur Ɗin itama daga falo ma yana jin su Ammi na hidimar yin sahur Ɗin farha Tsire taci da sauran Yoghurt ɗin data rage yaɗan kalleta "Zaki iya azumin amman?" ta ɗaga masa kai Ita dai tana gama sahur wani baccin ta kuma komawa shikuma jiran asubahi yayi ana kiran assalatu ya fita masallaci daga nan kuma bai Kuma dawowa ba part Ɗinshi ya wuce.
Farha da ƙyar ta iya sallah ta koma bacccin ta..........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na

500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 72*

Ganin hasken falon Part Ɗinshi a kunne yasa ya ƙarasa cikin falon da sassarfa Lokacin Mami ta fito daga kitchen hannunta riƙe da cup da shayi aciki tana ta juyawa da spoon Jiyay gabanshi ya faɗi yana addu'a Allah yasa mami bata leƙa ɗakin shiba dan ya manta bai saka key ba ta ɗan kalle shi tana yi mai hararar wasa.
"Shine koka tashe ni nayi sahur ko?"
Ya shafa saman kanshi wanda baya barin suma ko ɗaya tare da cewa

"Ai duty ɗin kine ni me yasa baki zo kin tashe niba, Ko abin da zanyi sahur ɗin ma baki bani ba haka na kusan makara dan kin san bakya azumin ke"
Dariya tayi tare da wucewa saman Kujera ta zauna tana shan tea ɗin nata ajiyar zuciya Aliyu ya mayar bayan ya tabbata mami bata Je ɗakin shi ba ya haura saman shi yayi wanka Wajan 6:00am ya fito cikin shiri ze fita ya ƙarasa ɗakin Mami tana kwance ta dunƙule cikin Bargo yaɗan tsaya akanta yana duba tsadaddan agogon shi Kirar samfirin exporer ya ɗan bugi pillown da mami take kai ta buɗe idon ta tar akan shi kafin ta yunƙura tana cewa.
"Ina kwana har ka fito?"
Ya saki murmushi yana cewa.
"Ehh na fito mamy zani dutse yau sannan kuma zani gidan Alhaji akan case ɗin Hanan"
Mami tai masa fatan alkairi ya fita ya wuce sashin Ammi ba kowa a falon se ƙarar Ac da fanka da suke faman yi da alamun kowa bacci yake yi Sabida dama azumi ya gaji haka Ɗakin Farha ya buɗe ya shiga.

Itama tana kwance kuma bacci take sosai ya zauna a gefen gadon ta ya fito da wayar shi ya kira musa akan yazo su wuce sautin maganar shice ta farkar da farha ta tashi zaune duk fuskarta a kumbure take tashi tayi daga zaunan ta sauka banɗaki ta shiga ta wanko fuska ta dawo har Lokacin waya yake yi ta zauna a ƙasa tana kallon shi ya gama wayar taɗan saci kallon shi kaɗan tare da cewa

"Ina kwana" da kulawa yace mata.
"Lafiya lau yaya azumin?" tace masa "Alhamdulillahi"
Shuru suka yi su dukan su kafin ya miƙe tsaye.
"Zan je dutse daga nan kuma zan shiga Gidan Alhaji"
Bata gano me yake nufi ba tace masa

"To Allah ya tsare hanya" ya zuba hannayen shi cikin aljihun shi.
"Baki buƙatar komai wanda zanzo Miki dashi me kike sha'awa kici idan an sha ruwa?"
Tai jimm tana tunani kafin tace masa.
"Ka tawo min da Nono mai tsami, se Kuma Ɗata da Mangoro" setai shuru tana kuma tunano abin da take so can kuma tace "Yawwa da fara" dariya yayi tare da cewa "Duk zanzo dasu amman ni baza'aci fara ba" Turo baki tayi tana ƙunƙuni "Nidai ina so ka siyo min" Dariya ya

kuma yi mata tare da cewa "Tom shikenan zan duba Miki" ya fita daga ɗakin ta bishi da kallo wani bin yana da kirki Musamman a lokutannan ta rasa mai yasa yake lallaɓata Komai tace masa yana mata batare daya danƙara mata baƙar magana kamar da ba.

Bata koma bacci ba tashi tayi ta wanke Toilet ɗinta dan yau ta tashi da ƙarfin Jiki rahmar Allah kenan, tana azumin amman yau kuma tana jin kuzari sosai ajikinta Bayan ta wanke toilet ɗinta Ta Cire Zanin gadon ta, takai Cikin Injin wanki ta sauya wani Gyaran ɗakin nata tayi sosai ta tattare kayanta dasu kai datti duk ta fitar dasu Ta kunna turaren ƙamshi a ɗakin nata.
Aliyu fita yayi ɗakin Ammi tana bacci se kawai ya fita suka wuce dutse shida Musa.

Gidan Ammi wuni akai bacci kamar babu ɗan adam agidan Farha gajiya tayi da kwanciya ta fita sashin hajja anan tayi sallar la'asar sannan suka rankayo tare kitchen suka shiga Ƙosai suka fara soyawa sannan suka soya dankali Sannan sukai farfesu suka dafa ruwan shayi Nan da nan suka haɗa dukkan abin da za'ai buɗa baki dashi wajan magariba kuma akaita shigo dasu kankana gwanda lemo ayaba Hajja tasa farha Yayyanka su acikin ƙaton Bowl ko wanne daban Farha ta gaji iya gajiya sabida a ƙalla sunyi kayan shan ruwa kusan kala goma hajja tana tsaye da Dabino a hannunta tana wankewa Farha ta ɗago ta dube ta.
"Wai hajja yanzu Kullum wannan aikin zamuyi har ƙarshen ramadan gaskiya zamu sha wahala"
Hajja tayi dariya tare da cewa

"A,a ai nan da ɗan lokaci ma zasu wuce saudiya umara Dukka gidan ina ga Salama ce kaɗai wannan karon babu amman gaba ɗayan su zasu tafi"
Farha ta jinjina kai cikin mamaki tace.
"To Ku kuma ina zaku je?"
Hajja tace.
"Ni gida zan koma sauran ma'aikata ma duka gida zasu wuce se kuma ana gobe sallah zamu dawo sabida ana jibi sallah suke dawowa"
Farha ta jinjina kai batare data ce Komai ba sedai taji daɗin wannan tafiya tasu sabida Ko banza itama tasan zata je Gida ta zauna kafin su dawo.
Ana magariba suka kammala komai farha ta ɗauki kayan buɗa bakin ta taiwa hajja sallama tana shiga ɗakinta wanka da alwala ta ɗauro tazo tayi sallah tunda ta idar da sallah ta kwanta a ƙasan Tiles bayan ta naɗe carpet ɗin ɗakinta ruwa kaɗai take ta sha dan jitayi bata sha'awar Komai haka taita malelekuwa a ƙasa sanyin wajan yana ratsata ba ƙaramin daɗi take jiba dan har wani Lumshe idanu take yi.

Can bayan sallar Isha'i wanda a ƙa'ida se Lokacin mutan gidan suke cin abinci sabida idan an sha ruwa Dabino da ruwa kaɗai suke amfani dashi Safna ta shigo ɗakin Farha tare da ce mata tazo Inji Ammi farha ta Ɗauki hajib ta saka gaba ɗaya iyalin Gidan suna kan dining kowa yana Cin abinci Ta Tsugunna tana gaishe da Ammi wadda ta kalli Farha da kulawa tare da ce mata.
"Ke kin sha ruwan naki ne?"
Farha ta ɗaga kai tana wasa da yatsun hannunta.
"Yawwa to masha Allah, Nan da wajan jibi haka ko ranar sati zamu tafi umara ki haɗa kayanki waje ɗaya Idan Baba yazo zewa Musa magana seki Je gida ana jibi sallah zaki dawo kafin nan

Mun dawo In sha Allah"
Farha ta saki fuska sosai tana dariyar Farin ciki kafin tace.
"Dama Ammi komai nawa ma a haɗe yake ko yau ma zamu iya tafiya gidan Ko musa be zoba Ni zan gane hanyar Gidan Namu"
Ammi tace.
"To shikenan tashi kije sena neme ki"
Miƙewa tayi zata shiga ɗakinta Bashir ya kirata.
Ta ƙarasa gaban shi Turo mata Plate yayi tare da cewa ta zuba masa Soyayyan dankalin dake gaban shi ta ɗauki Plate ɗin ta zuba mai ta tura masa gaban shi ta lura daga Matar yayansu har wannan Budurwar se harararta suke taɓe baki tayi zata Juya ta koma ƙamshin farfesun da sakina keci ya doki hancin ta Wanda nan da nan cikinta ya hautsine da sauri tabar wajan tana zuwa ɗaki ta dinga sheƙa amai wanda shine ya galabaitar da ita a bakin Toilet ta kwanta a ƙasan tiles tana mayar da Numfashi dan bata da Kuzari ko kaɗan.

Lokacin daya shiga Gidan Alhaji Hamishi ana kiran sallar magariba...........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 73*

Sabida haka sauka sukai daga mota suka shiga cikin wani ƙaramin masallaci dake Ƙofar gidan suka yi sallar magariba Ya miƙawa Musa dabino Wanda ya ɗauko daga cikin aljihun farar shaddar dake Jikinsa a tare da Musa suka shiga cikin Gidan marigayi Alhaji Hamishi a Madaidaicin Falon gidan suka tarar da Momcy a zaune tana shan Kunun Buɗa baki zama sukai a ƙasan carpet Momcy tayi juyin duniya akan su tashi su zauna a saman kujera Amman suka ƙi tashi tayi ta shiga Kitchen tray ta fito dashi wanda ke shaƙe da kayan ciye ciye ta dire a gabansu tana cewa.
"Nasan bakuyi buɗa baki ba ga ɗan abin Motsa baki nan"
Haɗa baki sukai wajan yi mata godiya Musa ya ɗauki kankana yana sha shiko Aliyu ruwan gorar faro ya ɗauka ya buɗe ya ɗaga seda ya shanye tas sannan yayi hamdala ga sarki Allah Ya dubi Momcy tare da cewa.
"Dafatan Kun sha ruwa lafiya" da kulawa tace "Alhamdulillahi" falon ya ɗauki shuru na wasu daƙiƙu Musa ya ɗauki Kankana a plate ya fita daga falon dan ya basu guri Falon ya rage daga Aliyu se Momcy Aliyu ne ya katse shurun su da cewa.
"Yanzu yaya ake ciki ne da maganar Hanan ɗin naso nazo to ban sami Lokaci ba ga shi zan je Umara To bana son na kuma tafiya Kuma na dawo ban zoba yanzu ma haka daga Dutse Muke ko gida banje ba"
Momcy ta ɗan kurbi Kununta kafin ta aje a center table ta fuskanci Aliyu.
Cikin damuwa tace.
"Kaga shidai wanda yake zuwa wajanta abokin Shashancin nata Wallahi data masa maganar ya turo yaƙi dan da faɗa ma suka rabu amman bari kaji daga bakin ta"
Momcy ta soma kiran Hanan wadda take ɗaki a kwance ko ruwa bata sha ba se aikin kuka take idanunta sunyi jajir sabida kuka duk sun Kumbura Hijabi ta saka ta fito falon Tunda ta doso

Yaɗan zuba mata ido kafin ya kawar yana kallon ƙasa ta durƙusa a gabanshi Murya a dashe tace.
"Yaya Aliyu ina yini An sha ruwa lafiya?" a taƙaice yace "Lafiya" daga haka ta zauna acan nesa dashi tayi Shuru Momcy ganin Bai ce komai ba yasa tace "To seki gaya masa yadda kuka yi da saurayin naki"
Kuka Hanan ta saka mai fitar sauti tana fyace majina kafin tace.

"Yaya Aliyu kace na fitar da Mijin aure sedai wanda na ƙwallafa raina akan shi tashi ɗaya ya gujeni, Kuma shine silar darwatsa mini rayuwata"
Aliyu ya ɗago da mamaki ya tallafi Haɓarsa yana kallonta kafin yace mata.
"Kamar yaya kenan?"
Hanan ta share hawaye tace.
"Tun bayan rasuwar Dady Na Haɗu da Anwar a school ɗinmu Anwar class mate ɗinmu ne tun bana kulashi har yazo ya cusa mini soyayyarshi anwar ba wani ɗan masu dashi bane amman ni da yake ina son shi sam ban damu ba haka nacigaba da soyayya da anwar wanda Harta kai ga yana taɓa Min Jikina batare da wata shakka ba inna nuna masa Ɓacin raina se yace ai aurata zeyi har takai ta kawo da ina wa Momcy ƙaryar zamuyi Karatu da ƙawayena in fita naje na haɗu da Anwar Kuɗinmu da momcy ta sakar mana dashi nake wa Anwar Hidima harta kai nike biya mai kuɗin makaranta kullum burinmu muyi aure dashi Baya da geji da jikina Sex ne kaɗai bai taɓa yi dani amman a hankali na lura anwar na ɗan shaye shaye wanda shine ya koya min afa ƙwaya wadda nake sha nai ta bacci batare da Momcy ta lura da halin da nake Ciki ba Lokaci ɗaya dana buƙaci Anwar yazo muyi aure nina yarda Komai ma zan masa inze aure ni buɗar bakin sa se yace ai ko ɗan iska tagari yake nema, yanzu ko wayata baya ɗagawa Yama yi Blocking ɗina dama Tunda muka gama school ganina dashi yayi wahala"
Ta faɗa tana wani irin gunjin kuka.

Aliyu yaja tsaki yafi sau goma da ɓacin rai a saman fuskar shi yace.

"Kin cuci kanki hanan mai yasa wasu mazan suke cutar mata ne da zasu aure su suyi ta more albarkatun Jikinsu, dama akwai namijin daze zo maki da maganar taɓa Jikinki kuma ki yarda auren ki zeyi har ma ya koya Miki shan ƙwaya ki yarda son ki yake sabida ke mahaukaciya ce to wallahi wannan Mutumin ya cuce ci kuma kema Momcy kinyi Kuskure mai yasa baki lura da shige da ficen ta baki lura da yanayin ta Kai innalillahi wa'innah ilaihirraju"un"
Aliyu ya faɗa da wani irin tashin hankali.
Momcy kuka Hanan kuka an rasa mai rarrashin wani acikinsu.
"Tabbas nayi kuskure Aliyu wallahi hankalina da tunanina bai taɓa kaini ga na gano Lamarin hanan ba seda abun ya soma ƙwaɓewa Maƙota na suka fara nausar dani halin da take Ciki ranar dana soma shiga ɗakin hanan na ganta cikin halin maye tana surutai wallahi ban rintsa ba, Kuma abin takaicin har yanzu shi saurayin nata bai taɓa zuwa gidannan ba sedai ita ta ɗauki Mota ta fita suje su haɗu wanda ni ƙarya take shatamin tace Min wai karatun jarrabawa zasuyi da ƙawayenta babban kuskuren danai shine kuɗin dana sakarwa Hanan bata da geji duk Adadin kuɗin da zata ɗiba ban taɓa Hanata ba sabida ina ganin nasu ne ashe ita tana can tana Bawa saurayi suna shaye shaye suna shashancin su kaga yanzu da maganar aure tazo ai ya

gudu yama kashe wayoyin sa"

Shuru Aliyu yayi aranshi yana jin Tsananin takaicin halin da hanan ta shiga a sanadin soyayya wai yaushe ne ƴammata zasu farga daga baccin da suke yi ne wani wawan ne zeje wajan mace ya gama taɓeta sannan ya aureta ai in kika bashi jikinki zargin ki zeyi ya ɗauka kowa ma haka yake miki.
"Bani Number wayar shi"
Aliyu ya faɗa yana zaro wayar shi daga aljihun Rigarshi Hanan daka ta dinga karanto mai Number ɗin Anwar Ringing ɗaya Anwar ya ɗaga Aliyu yayi sallama Anwar ya amsa.
"Nine yayan Hanan yarinyar daka ɓatawa Lokaci akan ƙaryar zaka aureta ina son ka turo iyayenka Ni zan baka aiki kuma zan baka gida zan maka lefe sadaki kaɗai Muke Buƙata in ka amince ko gobe ma muna jirank"
Dariya Anwar yayi tare da cewa
"Wasan yara ma kenan, Yarinyar da bata jin maganar mahaifiyarta a wani labarin ma ance baƙin cikinta ne ya kashe ubanta yarinyar da take zuwa ɗakina Duk abin da nake so A tare da ita na samu duk abin da yake Burgeni na ganshi Duk abin da ke tsolen ido na taɓa to me yayi saura Ta yaya zan ɗauko baragurbi na saka cikin Zuri'ata iyayena ma ba zasu yarda ba yanzu haka akwai yarinyar da nake so ɗanya jagwab Zan aura mai tarbiya ƴar manyan Mutane"
Daga haka Anwar ya kashe wayar yabar Aliyu sake da baki.
Kuka Hanan take sabida ta gama Jin komai da Anwar ya faɗa.
"Wallahi yaya ban taɓa zina ba nasan dai yana taɓamin Jikina........
Ai ɓata ƙarasa maganar ba Aliyu ya daka mata wata uwar tsawa wadda ba Hanan ba hatta Momcy seda ta Firgita.
"Kin cuci kanki kin cuci rayuwarki na tausaya miki wannan masifa ita zatai ta Bin rayuwarki Sabida darajar mahaifinki Kinsan ance baka alkairi ka lalace baka sharri ka gama lafiya to Kinci arziƙin mahaifin ki Ni zan samo miki Mijin aure daga yanzu ki fara shiri koda yaushe zaki iya ganin wanda zaki aura sauran Ki nuna masa ke shasha sha ce"
Daga haka ya miƙe beko yi musu sallama ba yabar falon.
A mota ya tarar da musa ya shiga Musa yaja suka tafi Gida........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 74*

Tunda ya shiga mota ƙasa yayi da kanshi baƙin ciki na nausar zuciyar shi bai ɗago da kanshi ba seda yaji Musa yana ce masa.
"Yallaɓai Mun iso gida" Buɗe murfin motar yayi ya fita Yana tafe yana dafe kanshi har ya ƙarasa part Ɗinshi yanayin shi kaɗai mami ta kalla tasha Jinin jikinta tunda ta masa sannu ta Kama kanta ya haye saman shi kwanciya yayi sabida kanshi ciwo yake masa Alhaji Hamishi Mutum mai Mutunci da sanin darajar ɗan Adam ya tausaya masa ya tallafi rayuwarshi Tabbas yana da dama baze taɓa barin Zuri'ar Alhaji Hamishi su shiga cikin masifa ba, Dan ita Momcy sanadin wannan matsala Kullum Acikin hawan Jini take idan ta faɗi ta rasu Yaya ƴaƴanta zasuyi Juyi kawai yake a gado da ƙyar yayi wanka yayi sallar Isha'i ya sanya jallabiya baƙa ya fita Ƙasa ya

sauka tea kaɗai ya haɗa yasha Ya fita part ɗin Ammi.

Falon Ammi babu kowa bedroom ɗinta ya wuce anan ya sami sadiƙ da Bashir gaisawa sukai ya nemi Guri ya zauna yaɗan kalli Bashir daya ke danna waya.
"Ka shirya gobe zaka wuce Abuja sabida wannan karon kai zaka zauna kaga duk Umara zamu je"
Bashir ya ɓata fuska kamar zeyi kuka.
"Dan Allah Yaya Ali ka barni a kano wallahi takura nake a wani garin"
Aliyu ya harare shi tare da ce mashi.
"In ba zaka je ba kai ta zama"
Bashir fita yayi yana ƙananun maganganu Aliyu yayi Murmushi mai ciwo wani abun idan Bashir yana yi kawai mamaki yake Su da suka taso Tun kafin sukai shi suka san rayuwa.
Hira Ammi suke da sadiƙ wanda Aliyu bai saka baki acikin hirar tasu ba sema Pillow daya janyo ya kwanta Sadiƙ yaɗan dube shi.
"Wai baka da lafiya ne?" Ya ɗan kalli sadiƙ "Me kagani?" Sadiƙ yace "Naga sanyin ka na yau yafi na koda yaushe" Girgiza kai yayi bai ce komai ba.
Har wajan 9:00pm sadiƙ na ɗakin kafin daga bisani yayi musu sallama ya tafi ɗakin sa Ɗakin ya rage se shida Ammi.
"Yawwa dama maganar waccan yarinyar fati, Nayi mata magana akan zata je gida sabida zamu tafi umara tace koda kanta ma zata iya zuwa to Zaka bata wani abunne sabida Guzurin Mota Idan yaso Gobe seta tafi Nace mata ana jibi sallah ta dawo"
Shuru yayi mata kamar mai bacci.
"Baba wai ba magana nake maka ba kayi Min banza"
Ya ɗan ɗago.
"Ammi ni me zan bata babu wani abun da zan bata kawai ta tafin kamar yadda kika buƙata dama ai Koba dalilin Umara ba kina son ta tafi kamar yadda kika gaya min Jiya to kuma ga dalili mai ƙarfi nan ya taso to kinga dole ne taje"
Ya faɗa yana Rintse idanunshi kanshi ne ke sara masa ga gajiya ga bacci ga yunwa.
"Wallahi Baba idan ka cire maganar Umara data taso mana Bani da wata Hujja na tafiyarta ai nai maka alfarma ta zauna har bayan sallah, To ɗa na kowa ne zan barta anan ita ɗaya ne tare da masu gadi hajja tafiya zatai sauran ma'aikata tafiya zasu yi Dukkanmu Umara zamu tafi to dawa zata zauna In kuma kaga zamanta shiyafi alkairi ta zauna Ɗin ai ga ɗaki nan ga kayan abinci da komai"
Bece komai ba tunanin inda ze kai ta yake Yi acikin zuciyarsa dan koya sha giyar wake baze bari taje gidansu ba dan bai shirya hakan yanzu ba.

Miƙewa yayi yana cewa "Haka ne Ammi Duk yadda kikai shine daidai amman zan yi shawara da Musa" daga haka sallama yayi mata yabar ɗakin Falo ya fita ya shiga ɗakin farha Tana nan kwance a ƙasan tiles hatta zanin Jikinta ya kunce daga ita se under skirt se Birgima take tana Lumshe ido yaɗan Gyara tsaiwar shi akanta.

"Yanzu dan Allah idan sanyin nan yayi maki illah fa?" tashi tayi zaune ta gyara zaninta tana mai sannu da zuwa kafin ta shiga banɗaki ta wanko bakinta yana zaune a bakin gado tazo ta zauna

a gaban shi.
"Ina farar?"
Shi yama mance da batun fara sam.
"Na manta wallahi amman zan sa a samo Miki ita kinci abinci?" ta girgiza kai tare da cewa "Dama so nake inna je gida na sa Ikram tai min ɗan malele" da rashin fahimta yace "Wace haka?" ɓata fuska tayi tare da cewa "ƙanwata mana ba gida zani ba Inji Ammi dama kayana suna haɗe" Murmushi yayi tare da watsa mata wani kallo "waye ze kaiki gidan a haka?" ta murguɗa mai baki tare da cewa "Ƙafata mana" wayar shi ya fito yana Dannata idanun shi yana kan wayar yace "Babu inda zaki zan kaiki Gidansu Hanan ki ɗan zauna kafin mu dawo" da mamakin shi seya ga ta ɓata rai tai kicin kicin da fuska "Idan ma ka kaini wallahi bazan zauna acan ba"  yaɗan kalleta "Sabida me?" bata ce masa komai ba ya tashi ya buɗe wardrobe ɗinta kaf kayanta ya fito mata dasu ya zuba acikin Trolly ya kalleta "Tashi muje" Hijabi ta saka a fusace tayi hanyar waje Biyota yayi da kayan ta a hannunshi ya rufo Ƙofar Ɗakin nata ya aje kayan ya shiga ɗakin Ammi ya jima aciki kafin ya fito Tana gaba yana binta a baya har zuwa bakin Mota se Fushi take ya Buɗe mata gidan gaba ta shiga ya aje mata kayan a bayan motar ya shiga mazaunin driver Yayi revers ya Nufi gate suka fita daga gidan Se turo baki take yi gaba Ƙiris take Jira ta fashe shi dariya ma ta bashi A wani waje yayi parking ya fita se gashi da fara a ƙatuwar farar roba ya aje mata saman cinyarta yaja Motar suka cigaba da tafiya.
"Kici farar mana"
Hawaye ta soma tana Turo baki.
"Wai zafin rabuwa dani ne yasa kukan ko kuma me?"
Ji rainin hankali ta faɗa a ranta yasan Gidansu hanan daya ce mata shine ya ɓata mata rai sabida tun ranar data ji yana waya dasu a ɗakin ta tashiga tunanin meye alaƙarsu kuma Wacece ita a zuri'arsu amman dan ya rainata shine zece mata zafin rabuwa.
Ɗora hannunshi yayi a saman nata ya shiga matsawa.
"Ni bana son inga kina wannan Fushin Fisabilillahi Na barki ke kaɗai ne agida Ko kuma na barki Kije gidanku a halin da kike ciki ai se a zageni"
Harara ta ɓalla masa.
"To ba a gidan namu ka ɗaukoni ba, Ni wallahi babu gidan wasu da zani ai dama rannan ina ji kana Magana da Hanan ɗin kuma dana tambayi Hajja tace ba ƴar uwarku bace sabida ka rainani bani da daraja a idanunka shine zaka kaini Gidansu Budurwarka ka ajeni"
Seta rushe da kuka, Tunda yake bai taɓa dariya irin ta wannan Lokaci ba dramar Fatima kullum ƙaruwa take yau kuma ta lafta masa Hanan Jiya kuma tace wa Jamila kwartuwa lallai wannan harta fi mami Kishi.
Rage Gudun Motar yayi a hankali ya saka hannun shi ɗaya ya kamo fuskarta ya sa harshe yana lashe mata hawayen nata kafin ya ɗan lashi bakinta yana wani Lumshe ido ji yake kamar ya saki kan Motar ya janyota Jikinsa ya rarrasheta.
Yawun bakinta ta tara ta tofa mai a fuska tana cusa kanta a tsakanin Cinyarta tana wani irin kuka kashe Motar yayi tare dayin parking a gefen hanya ya ɗora yatsansa a wajan yawun nata data tofa masa ya goge shi tare da sanya yatsan a bakinsa ya tanɗe yawun ya ɗagata cak ya ɗora ta a saman cinyar shi.
"Fatima me yasa kike son ɗaga min hankalina ne inda nasan ma zaki shiga damuwa wallahi da fasa tafiyar nan zanyi ina Ƙoƙarin inga ban cutar dake ba amman ke Kullum cikin ɗaga min

hankalina kike hanan ce Budurwata zaki bada sheda ne Kinsan yaya nake da ita harda zaki faɗi haka?"
Ya faɗa yana cusa fuskarshi a saman tata fuskar bai bata damar magana ba bakinsa ya Ɗora a saman laɓɓanta yana tsotsarsu kamar alewa ya ɗora hannunshi a saman Kirjinta yana Yamutsa su wani irin yanayi suka shiga mai wiyar misaltawa kafin ya ɗagata ya mayar saman Kujerar data ke kai ya ɗora mata farar a cinyarta ya tada motar gaba ɗaya Jikin farha ya saki wata irin tsumammiyar soyayyar shi ke ƙara nausarta Jita ke idan bashi ba zata iya rayuwa ba ta ko ina Yayi harya zarta tunani Motar shuru ta ɗauka shi bai mata magana ba itama bata ƙara magana ba Bata ɗago kanta ba se a bakin gate ɗin gidan daya ke faman zuba Horn mamaki ne ya kamata lokacin data ɗaga kanta ta gansu a ƙofar gidan Aunty salama.........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 75*

Me gadi ya buɗe musu gate ɗin ya danna hancin motar shi cikin farfajiyar gidan yayi parking a wajan adana motoci ya kashe Motar ya ɗan dube ta fuskarshi cikin damuwa yace mata.
"Nan yayi miki zaki iya zama a gidan ƙanwata salama?"
Ƙasa tayi da idanunta tana jin hawaye na ƙoƙarin zubowa daga cikin su.
"Kin min shuru fatima, Ni akwai dalilin daya sa kika ga bana son na kaiki Gidanku, Amman idan kinga zuwa gidan ku ɗin yafi Miki sena juya na kaiki"
Lokacin da yayi maganar Muryarshi ta ɗan canza da alamun yana cikin damuwa shima.
"Yanzu kuma idan ka tafi se yaushe zaka dawo?"
Ya tsinci muryarta acikin dodon kunnen shi.
"Saura kwana ɗaya sallah Sabida ni sati Biyu kaɗai zanyi a saudia se na wuce Chaina se ana gobe sallah zan dawo In sha Allah"
Ga mamakin sa seya ga ta saka mai kuka! duk seya susuce ya tarairayo ta jikinsa.
"To kukan na menene wai fatima Lokaci ya ƙure kema dana samar Miki Visa ɗin mun tafi tare amman in sha Allah nayi miki alƙwari In Allah yasa kika sauka lafiya zan kaiki"
Da rashin gane abin da yake nufi na in Allah ya sauketa lafiya tace.
"Ni kenan zaka bari anan dan baka sona amman ka tafi da matar so"
Murmushi ya saki.
"Fatima kincika rigima bana son ki ɗaga hankalin ki, Akan tafiyata in ba haka ba zan tafi ne da damuwa acikin zuciyata zaki ƙara mini damuwa akan damuwa dan Allah ki kwantar Min da hankalinki"
Hannunta ta ɗora a saman Gemunshi tana ja tana hawaye.
"Shikenan ka dena min abin da kake min da daddare?"
Dariya yayi lallai akwai Ƙuruciya a tare da fatima Ya fuskanci gaɓuwa ce ajin farko.
"To shikenan kibi ni bashin duk wanda ban yiba idan na dawo zan rama miki" ta wani zaro ido
"Tab ai sena Mutu ina zan iya ɗaukar Duka na kwanakin da kayi"
Dariya yayi tare da lakace mata Kumatunta.
"Fatima kenan kina da rikici Allah ya shirya min ke"

Daga haka ya ɗauki robar farar tata "Muje ciki to na tabbata zaki sami Nutsuwa agidan nan sabida Bani da matsala da salama, sannan Kuma ban yarda Ko bakin gate ki fito ba kuma ko falo zaki je ki tabbata Kin saka Hijabi zan bawa Musa Kayan sawa sabbi ya kawo Miki naga naki duk sun miki kaɗan ƴar lukuta ashe zaki ƙiba"
Ya faɗa yana dariya fita tayi daga Motar ta Jingina da Jikin motar ta ɗora kanta a saman motar seta fashe da sabon kuka ita fa da gaske Missing ɗin sa take Jitake kamar suje tare ɗan zaman da sukai dashi ta gano Mutum ne mai haƙuri kawaici tare da kyautatawa duk wanda yake tare dashi.
Ya zagayo gefenta hannu ya sanya ya zabga tagumi ya zuba mata ido.
Tai kuka sosai kafin taji Tattausar muryarshi wadda tai rauni sosai Kamar ba shiba.
"Kinga muje mota kawai na fasa tafiyar Tunda Ranki baya so na haƙura"
Kuma seta ga ya kama hannunta yana ƙoƙarin sakata acikin Motar da alamun da gaske yake mata maganar.
Tirjewa tayi taƙi tafiya sedai kuma bata dena kukan ba.
"Allah in baki shiga mota ba zan ɗaga ki cak na shigar dake, wai ya kike so nayi ne Kince Bakya son gidan su Hanan naƙi kaiki bayan gidan kamar Gidanmu yake tunda Mai gidan uban gidana ne amman kin fassara da wata manufa, Gidan Ammi kuma ba kowa duk ma'aikatan ta tafiya zasuyi na kawo ki gidan salama sabida kaf ƴaƴan Ammi babu wanda yakai ta haƙuri sauƙin kai sanin ya kamata nina tabbata zaki ji daɗin zama da ita ba alfahari ba, to tunda nan ɗin ma bai Miki ba Muje gidan nina fasa tafiyar na haƙura mu zauna tare"
Tunda ya ke maganar Kuka take ba zaka gano a wani yanayi yake maganar ba yanayin damuwa ko ɓacin rai ƙarya ne ka gano yanayin tunda suke dashi bata taɓa Jin yayi doguwar magana kamar wannan ba Ta yaya zata So kanta kawai ya fasa tafiyar sa wadda ya kashe Kuɗi akanta share hawaye tayi ta ɗan dube shi ya ƙura mata idanun shi da suka ɗan kaɗa sukai jajir abin ka da farin Mutum

"Muje to ni tayaya zance ka fasa tafiyarka bayan tun bani ka tsarata"
Ƙin tafiya yayi taga ya cigaba da tsaiwar shi.
"Da gaske nake miki tafiyar ma naji tafita a raina kawai Muje gida"
Maƙe kafaɗa tayi tana tuttura baki gaba.
Ya zuba mata ido gaskiya fatima yarinya ce ɗanya jagab yana ganin shagwaɓa da sangarta kala kala a hankali ya sunkuyo daidai Kunnenta ya raɗa mata.
"Wai kece auta ne a wajan su mama?"
Dariya tayi kuma ga hawaye tana cewa.
"Tab wallahi idan kaga ƙannena ma seka ce min ba yarinya bace Ni su Ruƙayya duk se sun goya ni fa"
Dariya yayi kaɗan yana sa hannu yana share mata hawayenta itama hannu tasa tai ɗage tana Goge mai saman idanun shi hannun nata ya kama ya sanya yatsanta a bakin shi yana tsotsa a hankali ta ɗora ɗayan hannun nata a saman sajen shi tana shafawa se kawai ta faɗa saman Ƙirjinshi ta rungume shi ya sunkuyo Sabida ya fita tsayi ya rungumeta sosai yana buga bayanta.
"Fatima kina sona da yawa Ko?"
Ya faɗa muryarshi tana rawa ta shiga girgiza kanta alamun da gaske tana son shi da yawa dan ita bata cikin masu Ƙunbiya Kunbiya duk abin da take so a fili take nuna wa Muryarta na rawa

tace.
"Bamma san adadin soyayyar da nake maka, tunda na ɗora idanuna akan ka na kasa samun Nutsuwa duk abin da kai min bantaɓa Jin haushin kaba sabida ka taimaki zuciyata daka aureni koda zakana yanka naman jikina zanji daɗi ne, sabida ina bawa zuciyata abincin ta na fara son ka tun kafin nasan kai waye tun kafin nasan sunan ka tun kafin Nasan Halaiyar ka Ina son ka kai min alƙawari ba zaka taɓa Juya min baya ba sabida in ka Juya min baya wallahi rasa rayuwata Zanyi na rabu da iyayena saboda kai na rabu da masoyin daya soni Don Allah sabida kai nina tabbata akwai wani Ɓoyayyan lamari da Allah ya ƙaddara a tsakanina dakai"
Tana faɗin haka seta saka mai kuka tana cewa.
"Wannan tafiya taka Jin ta nake har raina Wannan tafiya taka batai Min ba amman bazan hana ka tafiya ba, Duk da na fuskanci akwai abin da kake Ɓoye mini a game da Gidanku wanda basu san ka aure ni ba dan Allah kada ka cutar da zuciyata kada ka wulaƙanta rayuwata Aliyu........
Ta kasa ƙarasa maganar sabida kukan daya ci ƙarfinta........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 77*

"Yaya a iya sanina ba wata alfarma a tsakanina dakai, Umarni ne kawai zaka ce min nayi abu kaza wanda in dai bai saɓawa Allah ba da gudu zan maka shi"
Salma ta faɗa cike da ƙarfin gwiwa, Aliyu yaɗan share zufar data tsatstsafo masa daga saman Goshin sa sannan yace mata.
"Salama wannan alfarma ta shallake dukkan wata alfarma wadda kike zato rufin asiri ne nazo Kimin a matsayina na ɗan uwanki na jini"
Ya faɗi maganar cikin raunin sa wanda ya bayyana ƙarara, wani irin tausayi ya bawa salma cikin kulawa salma tace masa.
"Yaya kome ye ka gaya min in sha Allahu baka da matsala dani"
Ya gyara zaman shi sosai ya soma yi mata magana.
"Salma ga amanar fatima nan na kawo Miki ita ki kula da ita kamar yadda zaki Kula dasu Safna In sha Allahu da zarar mun dawo zanzo na ɗauketa, sabida tana da lalura dole se an kula da ita sosai tana ɗauke da juna biyu amman bana son ita kanta tasan tana da cikin kuma kema bana son ki sanar da kowa, Ina son dai ki dinga lura da ita idan da damar hakan"
Jikin salma ne ya ɗauki rawa hankalinta yayi masifar tashi"Innalillahi wa'innah ilaihirraju'un" take faɗa a fili wato kowani ɗan adam akwai kalar tashi jarrabawar wato shi tashi kalar jarrabawar kenan to fyaɗe yayi wa ƴar mutane ta sami ciki Kome shi kuma sabida masifar son haihuwa ta Shiga ranshi yaƙi Zubar da cikin

"Amman yaya ban gane me kake nufi ba, Allah yasa ba zargin dana ɗarsa bane a zuciya ya tabbata yaya kada kayi mana haka Idan ma Ƙaddara ce ta faɗa muku Ni zanyi shahadar zubar da cikin kafin duniya ta sani dan na tabbata Ammi ma taji zata iya haɗiyar zuciya ta Mutu"
Salma ta faɗa muryarta tana wani irin rawa Tunda ta soma maganar ya kafeta da idanu Ranshi idan yayi dubu ya ɓaci sedai uzirin rashin sani da yayi wa salma shine yasa yaji zuciyarshi tana ƙasa tana sassautawa daga zafi da ƙunar da take masa.

"Wannan shine Kuskure na farko da zaki a rayuwarki, Koda wasa kada ki gangancin zubar Da cikin dake Jikin fatima dan fatima ba Lalata da ita nayi na mata ciki ba, Cikin jikinta na sunna ne Nine Mijinta wanda shedu da sadakina suka tabbatar da hakan"
Wata irin hantsila salma tayi ta Dafe ƙasan carpet ta zaro ido Jikinta yahau rawa lallai biri yayi kama da mutum, shiyasa lokacin data masa waya akan ya bata Number ɗin musa yaƙi yace kada ta bari ta tafi se gashi yazo.

"Yaya Ban gane ba wannan wani irin aure kayi wanda kaf ɗinmu bamu sani ba dan bani tunanin Ammi ma tasan wannan yarinyar matarka ce, Yaya mai yasa kayi hakan wanda ka san Wannan aure akwai matsala gagaruma acikin sa Wanda kuma gashi tun kafin aje ko ina rabo ya shiga tsakanin ku da ita"

salma duk ta faɗi maganar a hargitse.
Ya zuba mata ido yana jin dama bai gaya mata ba domin ya hango ruɗu kala kala a cikin idanunta koda yake dama haka ƴa mace take tana da ruɗewa ba kamar namiji ba wanda shine ze tsaya ya saurare ka har ma kuyi magana ta fahimta.
"To salama na ɗauki kayata na juya kenan dama wannan dalilin ne ai yasa nace Miki alfarma nake nema a wajan ki ba kuma komai ne yasa na gaya miki matata bace kuma tana da ciki sabida zan tafi ban san meze faru a Bayan tafiyata ba ƙila jikinta yaƙi daɗi daga ƙarshe ki dubata kiga tana da ciki wanda ƙila kafin na dawo Kin Koreta kokin sanar da wani shiyasa na gaya Miki gaskiyar lamari, But amman tunda naga kin shiga damuwa kin ruɗe ba wata matsala zan ɗauketa kawai Mu juya Nidai na tabbata Wannan ciki na wane kuma Na sunna bana shege ba"
Daga haka ya miƙe tare da zira hannayen shi cikin aljihun jallabiyar shi da sauri salma ta miƙe tana cewa "Dan girman Allah yaya kada kayi min haka kowa ma kajewa da wannan magana irin wannan yanayi ze shiga ta yaya zaka tsallake Duk gidajen dake garin nan kazo wajena sabida kana ganin ka isa dani sannan na kasa yi maka alfarma wadda bata fi ƙarfina ba in ban rufawa Iyalinka asiri ba wa zan rufawa yaya dan Allah ka zauna Muyi magana ta fahimta dan Allah ba domin niba"

Aliyu yaji jikinsa yayi sanyi sabida magiyar da salma keyi masa a hankali ya zauna salma ta zauna itama tana kallon shi jitai ta matsu taji meye silar wannan aure mai cike da ruɗu acikin sa.
"Fatima matata ce na aureta ne sanadin ƙaddara lokacin da akai Min sharrin nan agidan wata radio kin tuna? to na aureta ne da zummar ɗaukar fansa akan yadda ta jagoranci yaɗa labarin Bogi akaina sedai Kin san shi Allah babu yadda bayayi da bawan sa yarinyar ta soni tun kafin tasan waye ni lokacin dana je mata da maganar aure akwai maganar wani akanta amman haka ta bujure tace ni take so Duk da ni bada Soyayyar gaskiya naje mata ba Ni kawai naje ne akan ɗaukar fansar abin da tayi Min sedai tashin farko mahaifinta yace Kona zo na aure ta ko kuma ya bada ita sadaka tunda tafi sona akan wanda ya bata a daran ranar najewa ammi da bayanin Ina son nai aure amman ammi ta rufe idanu akan ga mami ba zan yi wani aure ba, Ni kuma kawai sena tura su Baba Usman da sadakina aka auro min ita na kawo ta gidan Ammi akan zata ke mata aiki bama nine na kawo taba Musa na saka yace ƙanwar shice Nufi na intai kamar

shekara sena sallameta sedai kwatsam Kuma Allah ya ƙaddara Min tsananin son ta har takai ga wannan rabo ya shiga tsakanina da ita yanzu haka in ba keba babu wanda yasan wannan magana dake tsakanina da wannan yarinya hatta ammi bata san Komai game da ita ba"..............
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 78*

Ya ƙarasa maganar cikin Nutsuwar sa tare da zubawa salma ido wadda duk jikinta yayi sanyi ga mamakin sa se yaga salma ta fashe da kuka wanda bai hanata yin Kukan ba har ta ɗauki Lokuta masu tsayi tana faman yin kukan kafin ta ɗago ta share hawayenta tana kallon shi wani irin tausayi ɗan uwan nata ya bata ba ɗan kaɗan ba

"Nagode wa Allah da Allah ya ƙaddara wannan ciki ta silar sunna aka samar dashi wallahi da ko baka auri yarinyar nan ba dafa seka mata cikin nan sabida akwai rabo a tsakanin ka da ita rabon haihuwar dake tsakanin Kune yayi ta ɗawainiya da ita har taƙi shi wanda mahaifin nata ya bata ta aure ka, sannan kai ma rabo ne fa ya kaika gidan su domin ba da ban haka ba kamar yadda ka ɗauki mataki akan shugaban gidan radio ɗin ita ma haka zaka ɗauki mataki akanta, amman da yake Allah ya ƙaddara ta silar faruwar haka zaku haɗu shiyasa Allah ya tsara Muku hakan Kuma naji matiƙar daɗi nai Farin ciki kuma zan bata duk wata kulawa Kuma zan rufe maka sirrin ka in sha Allahu"

Salma ta faɗa cikin sakin fuska tagumi yayi yana kallon salma yaji ya sami Nutsuwa da maganganun data yi masa.
"Sedai salma ina tunanin ranar da Ammi zata san gaskiyar lamarin nan babban tashin hankalina shine na kasa yiwa ammi biyayya akan abin da bata so nayi wannan shine tashin hankalina dan nasan In ta sani ranta ze ɓaci"
Salma ta bishi da kallon tausayawa Duk ƴaƴan ammi babu mai biyayyar shi babu mai gudun ɓacin ranta kamar shi wannan tasa Ammi tafi riƙe mai wuta fiye da kowa.
"Kada ka saka wannan tunanin aranka dama shi ciki ɗan duma ne dole ammi tasan wannan magana komi daran daɗe wa kuma dama ammi bata da wani dalili na hanaka aure tunda hakan bai saɓawa addini ba dan kawai ta Burge ƴar yayarta ta faranta mata seta Ƙi barin ka kai aure fisabilillahi yanzu in a waje akai Cikin nan yaya zata yi sufa Mutane sun kasa gane cewa Rabo kamar ajali yake Allah ya ƙaddara matar kace Akwai rabo a tsakanin ku dan haka se kawai a barwa Allah ikon shi, yaya kaje kaita addu'a kada ma  kasa ka damuwa aranka In sha Allah akwai nasara acikin lamuranku"
Da ire iren waɗannan maganganu salma tayi ta kwantar masa da hankali har zuwa sanda taga ya saki ranshi Kuma ya sami Nutsuwa tashi yayi yana ce mata shi ze juya amman Musa ze kawowa fatima kayan sawa Sallama sukai dan yace yana gudun Rigimar fatima ne shiyasa baze je suyi sallama ba

Bayan tafiyar shi salma ta rafka tagumi lallai Ammi in batayi wasa ba a kan wannan yarinya zata iya rasa farin cikin Ɗanta mai biyayya dan salma ta hango irin ɗumbin soyayyar da yakewa wannan yarinya.

Miƙewa salma tayi ta shiga ɗakinta Ko Mijinta bata gayawa gaskiyar abin da ke faruwa ba sabida sirrinta ne ita da ɗan uwanta tana Ƙoƙarin fita taji wayarta na ƙara tana duba taga Kuɗi ne masu yawa yayo mata transper ta account Ɗinta fita tayi da wayar zuwa ɗakin da Farha ke ciki tana zaune su Dady sunyi bacci ita kuma farha ta zuba uban tagumi wanda tausayin ta ya kama salma Sallama salma tayi tare da zama a kusa da ita ta riƙe wayar tana Kiran Number ɗinsa yayi rejecting kiran salma shiya kira.

"Assalamu alaikum,yaya ya zaka min haka naga ka turo mini kuɗi na menene?"
Yayi Murmushi lokacin yana driving ze koma gida.
"Ki dinga siya mata abin da take so, Saboda Koni ma tana ce min tana son abu kaza da abu kaza to kada na ɗora Miki nauyi idan kuɗin ma bai isa ba Ki min magana sena ƙaro sannan inda hali ina son ki duba min ita ki tabbatar da akwai cikin nan ma kuwa danni ban kaita asibiti ba kawai hasashe nake yi dan naga Shigen irin yadda take yi mami keyi in tana da juna biyu"
Tausayi da dariya ya bata tausayin na farko shine harda tura mata Kuɗi akan ta kula da yarinyar lallai yana son wannan yarinya da yawa dariyar kuma daya bata ashe shi kaɗai yake shagalinsa ko asibiti ma bai kaita ba lallai se abar yaya.
"Allah ya kiyaye wallahi Ficika ma bazan taɓa ba ta yaya zan ɗauki Kuɗinka kome take so baze fi ƙarfina ba In sha Allah zan mata duk yadda kace"
Ya ɗan sauya murya.
"A,a nidai ki riƙe ban ɗorawa kowa wahala ba Ko ki riƙe koki zubar dasu duka ɗaya nidai na tura yanzu tana ina bani ita"
Salma tayi dariya tare da bawa farha wayar ta fita dan tabar Musu ɗakin.

"Kina jina fatima?"
Ya faɗa cikin wata irin murya mai kama data wanda yake jin sanyi.
"Ummh ina ji"
Ta faɗa sabida yawun daya cika mata bakin ta.
"Menene naji Muryarki ta sauya ko kina cin wani abunne?"
Ta miƙe tsaye taje ta zubar da yawun ta dawo tare da cewa "A,a bakina ne miyau ya cika shi amman naje na zubar"
Ya sauke ajiyar zuciya

"To kinci farar taki ko kina son wani abunne?"
Ta girgiza kai kamar yana ganinta

"A,a wai ka tafi ne?"
Da sauri yace "Na tafi sabida in ma nazo nayi miki sallama Kuka zaki Ni kuma bana son yawan koke koken nan naki"

Ta langwaɓar da Murya tawani shagwaɓe kamar zata masa kuka.
"Shine ka tafi amman koka zo ka min sallama ai shikenan"
Yayi dariya kaɗan "I'm sorry rigimarki nake gudu amman Koda yaushe zannan kiran ki Muna gaisawa harta Vedio call ma, yanzu de ba inda ke maki ciwo ko?"
Ta shafa cikinta "Babu ko ina kawai saman Cibiyata ne inda ka taɓa naji yayi tudu da marata tayi tauri"
Yayi Murmushi mai sauti "Ki dinga cin ayaba sosai ko tsutsar ciki gareki" ya faɗa yana dariya daga haka ya kashe wayar Tabi wayar da kallo aikuwa indai tsutsar Ciki gareta zata dage dacin ayaba dan taita yin kashinta.
Ta jima a zaune kafin salma ta dawo Ta dube ta da kulawa

"Har kun gama wayar?"
Tayi ƙasa da kanta tana miƙawa salma wayar salma dariya tayi.
"Aunty fatima yau kuma kunya ta kike ji"
Yadda salma tace mata Aunty se abin ya bata mamaki.
"Yanzu me kike so Kici na dafa miki?"
Cewar salma Farha ta girgiza kanta.
"A,a wallahi Aunty salama na ƙoshi bacci dai kawai nake ji"
Salma tace mata.
"Taso Muje ɗakin dake kusa dana su Dady seki kwanta acan yafi wannan faɗi"
Salma ta ɗaukar mata kayan suka fita zuwa ɗakin babbane sosai da toilet da tv da komai na More rayuwa acikinsa ga ƙaton gado da Manyan barguna salma ce ta jere mata kayan sawarta acikin Wardrobe sannan ta dube ta.
"Duk abin da kike so ga kitchen nan ki shiga ciki sannan Kome kike buƙata ki gaya min Ni ƙanwarki ce"
Dariya farha tayi kafin tai magana salma ta fice daga ɗakin gadon tahau taja bargo nan da nan wani bacci mai daɗi yayi gaba da ita dama shi take Ji.....

Wani irin missing ɗin fatima yake Ji acikin zuciyar shi da dukkan sassan jikinsa.........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 79*

Cikin sanyin jiki dana zuci ya shiga gida a harabar adana motocin gidan yayi parking tare da shiga sashin Ammi Lokacin daya shiga dukkan su suna saman dinning suna shan shayin dare wanda ƙa'idar ƴaƴan Ammi ce shan wannan baƙin shayi,Ammi ce da bashir da safna da sajeeda.
Sallama cikin bakin sa ammi ta amsa ya nemi guri ya zauna Ammi ta tsiyaya masa Kunu cikin cup ta tura masa ya ɗauka yaɗan kurɓa ya aje.
"Yaya maganar tafiyar tamu ne Banji kace wani abun ba?"
Cewar Ammi yace mata "Gobe in sha Allah zanbi Jirgin ƙarfe Ukun yamma Ku kuma se wajan

Jibi da safe haka Zaku wuce" ya faɗa yana kallon Bashir wanda ya mayar da hankali kan wayar hannun shi yana dannawa sedai sam hankalin shi ba'a kan wayar yake ba yana kan Ƙofar ɗakin waccan yarinyar Burinsa ta fito ya ganta Dan ba lallai Gobe su haɗu ba tunda Abuja ze wuce.
"ka gama haɗa kayan naka kuwa? sabida in sha Allah gobe tare zamu je airport inna tashi kai kuma seka sami ticket ɗin abuja"
Bashir ya sosa kai tare da cewa "In sha Allah dama ban zo da wasu kayan kirki ba"
Daga haka su safna Tashi sukayi suka bar falon Bashir ma daya ƙwallafa rai akan son ganinta daya ga Boss a wajan miƙewa yayi ya tafi Ammi ta dube shi.
"Komai da komai ya kammala Ɗazu Matar kawu ta Kirani tana min godiya da irin Hidimar da ka aika Musu, Ni dan dai Lokaci ya ƙure ne amman da Mun koma da tajira umara, dan rabon ta da saudi tun hajjin Bara da mukai tare"
Bece mata komai ba can kuma yace mata"Ai lokaci ya kure dakin magana da wuri,Wanda ma nake son ya koma baba usman" Jin haka yasa ammi ta sauya yanayin ta yayi saurin kauda maganar "Na bawa musa yarinyar nan sun tafi tun ɗazu" da mamaki ammi ta dube shi"Kana nufin har ka kira musan kenan sun tafi amman baka gaya min ba ai da ko ɗan sabulu na bata" Murmushi yayi me ciwo "To Ammi gobe zan tafi ban san abin da ze faru bayan bana nan ba shiyasa na Damƙa mai ita shine kawai samun masalaha" Ammi ta haɗe rai tamau "Kai baba wani irin masalaha kuma ban gano nufin kaba wai da kake ma wannan Haƙilon uban wa musa ya bawa yarinyar idan bani ba kuma dan Munafurci ai baka gayan zata tafi yau ba ashe bayan kabar ɗakina zuwa kai ka ɗauketa ka bawa Musa to ko na dawo ma kada ta dawo min gida bana buƙatarta" yarasa mai yasa ammi take ɗaukar zafi a duk Lokacin daya sako mata maganar fatima"Ammi ai kece kika ce Kin mata alfarmar zama har zuwa bayan sallah" tayo masa kaaa da maganarta mai ƙarfi "To yanzu na fasa kai nifa bana son wannan zaƙewar da kake akan wannan yarinyar mai kama da igiyar shanya Ni bamma san jarabar data sa Musa ya kawo Min itaba waya sani ma koda wani surkullen nasu na mutan ƙauye tazo min gidana tunda nake dakai baka taɓa Min tirjiya ba se akanta duba dukan dakawa su sajeeda akanta kamar ba ƴan uwanka ba wallahi bana ƙaunar yarinyar nan" Kurawa Ammi ido yayi gabanshi yana tsananin faɗuwa Tun yanzu ma ammi tana irin waɗannan maganganun inaga tasan Matar shice Muryar shi sanyi ƙalau yace mata "Ammi Dan Allah ki dinga kwantar da hankalin ki ni babu wata manufa a tsakanina da yarinyar in kika cire ta dalilin Musa kuma abin da yasa yanzu ma na Bawa Musa ita dan Gobe zanbar ƙasar ne Ku kuma jibi Kinga ba Lokacin Tsayawa akan jiran har se anyi wata shawara akan tafiyar tata, amman inna ɓata miki rai akan hakan Allah ya baki haƙuri Allah ya huci zuciyarki" ya faɗi maganar cikin sanyin Murya se kuma tayi ƙasa da muryarta "Ni kawai shiga hurumin yarinyar ne bana son ka dinga yi Koda yake ma ai Allah ya raba zaman namu Tunda ta tafi shikenan" da sauri yace "A,a ammi in kuka dawo zata dawo In sha Allah haƙuri zaki ɗa na kowa ne kuma kece kika yi alƙwari" shuru tayi masa shikuma seya tashi yayi mata sallama ya wuce part ɗin shi, Ammi tashi tayi bayan ta kashe ƙwan falon ta nufi ɗakin ta.

Jamila ta dawo da baya lokacin data ga ammi ta nufo ɗakinta, Saboda da niya tayi tabi bayan Aliyu Sakina ta dubi Jamila "yana ga kin dawo kuma?" jamila ta zauna jagwab a saman sopa ta saka hannu ta kama Kumatunta"Yaya Ammi nagani zata shiga ɗakin ta shikuma ya fita kin san

shi akwai saurin tsiya" sakina taja tsaki mai ƙarfi "Kina nufin haɗuwar ku ba zata yuwu ba kenan asarar kuɗina zanyi kome?" jamila ta share hawayenta daya ke faman zubo mata "Yaya wallahi kona Bisa nasan yanzu ya shiga sashin sa" sakina ta haɗe rai "Gashi Gobe ze wuce naji abban su yana faɗa ɗazu Mukuma jibi Amman banso Kuka ƙi haɗuwa ba sabida turaren nan malam ya tabbatar min da in ya shaƙi ƙamshin ajikin ki shikenan magana ta ƙare,amman ki san duk yadda zaki a goben ku haɗu ki ƙara goga shi a goshin ki da Jikin ki ya shaƙa Shikenan magana ta ƙare wallahi da tsada na amso shi"
Jamila tace "Naso jiya aka samo shi yaya dan na haɗu dashi a falo Allah ya sa Dai wannan karon aikin namu yayi tasiri akan Aliyu, Dan ina hango mana daular da zamu shiga mu warwasa Muji daɗi" ƙaramin tsaki sakina taja" duk wani lissafina akan ki yake burina naga kin auri Aliyu waccan matsiyaciyar matar tashi bana ƙaunarta sam Yaushe Ina ji ina kallon daular shi ga ƙanwata ai wallahi se inda maina ya ƙare" Jamila tana dariya tana kuka ta kuma damƙe kwalabar turaren Sakina ta kuma ce mata "Wannan shirin nefa yasa nace miki ki sauka anan gidan To kuma ashe tafiyar tamu ma a kusa take, amman Zamuyi amfani da damar Gobe tunda ta yau ta Kufce Ina son ki zama matar Aliyu uwar ƴaƴan shi wannan tasa duk wani ƙoƙarina akan hakan yake tafiya" jamila ta Lumshe ido batace komai ba ita kaɗai take hango wadaƙar da zasu yi in Burin su ya cika akan Aliyu.

Duk zuciyar Aliyu babu daɗi haka ya shiga falon shi mami ta jere masa kayan abinci taci kwalliya tana zaune a falon tana jiran shi yanayin data ganshi ne yasa taji hankalin ta ya tashi ta dube shi a raunane.
"Ga abincin ka na haɗa maka"
"Na ƙoshi" daga haka ya haye saman shi yana shiga ɗakin Rigar shi ya tube ya kwanta Maganganun Ammi suna masa amsa kuwa acikin Kunnen shi na Yadda ta nuna fatima ba zata Kuma zauna mata agida ba,rasa tunani da madafa yayi da haka bacci ya ɗauke shi Cikin dare ya farka sallah yaga mami kwance a gefen shi ya janyota ya gyara mata kwanciyarta Ya miƙe sallah ya jima yana yi har wajan ƙarfe Huɗu da tea yayi sahur ya koma bacci da asubah yayi wanka ya fita masallaci.

Umma ce ta dubi Yaya nafisa wadda zuwanta gidan kenan sabida Jikin umma daya ƙi daɗi a kwanakin nan...............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 80*

"Nafisa na rasa me yasa zuciyata take rawa tunani na yake tsayawa cak hankalina ya gaza kwanciya kullum na kwanta bacci mafarkin farha nake yi wallahi kome nake farha nake gani a idanuna baki ɗaya tsoro ne a tare dani ban san a wani hali take ba ban san a wani matsayi take ba"
Umma ta faɗa idanunta yana kawo Ruwa yaya nafisa cikin sanyinta ta matsa gaban umma tana

share mata hawayen dake zubo mata sabida dama ita yaya nafisa sanyin hali ne da ita kamar halin umma yaya sadiya ce mai zafi kamar na kawu cikin sanyin murya yaya nafisa tace.
"Wallahi umma bake kaɗai ba muma kammu hankalin mu ba'a kwance yake ba ko jiya babansu seda yace Min anya muna bibiyar halin da farha take ciki nace masa kuna waya da Mijinta kamar yadda yaya sadiya take gayan shine yace ai waya ba tabbas bace mu ganta shine tabbas tunda duniya yanzu babu gaskiya acikin Mutanan ta"
Yaya nafisa takai maganar cikin sanyin Jiki umma ta kuma goge hawayenta tare da cewa "Hidimar da Mijinta yake mana tayi yawa, na fahimci shi kuma kawun ku wannan wayar da sukai da mijin nata ya sami nutsuwa Nikam har yanzu hankalina baya kwance ga kuma maganar yaron nan da Ya nemi auren farha Jiya Kawun ku yake cewa Baban sa yace dai basu haƙura ba suna neman iri dai acikin gidannan a ƙara bashi guda ɗaya daga cikin yarannan ni nace ga Ruƙayya ko Hadiza amman kawun ku yace Ikram za'a bashi wallahi Jiya baki ga bala'in da a kwasa ba Nan Babarsu Hadiza tazo tagama cimin mutunci har da cewa waya sani ma ko anyi tsafi da farha kuɗin kanta Muke ci wannan abu ya ƙara ɗaga min hankalina Kin san shi maƙiyi kome zaka masa bazaka Burge shiba nina rasa mai nayi wa matar nan ta tsane ni nida ƴaƴa na wallahi babarsu Ruƙayya ta sakko har nan take zuwa muyi hirar mu wani bin sirrinta ma zata kwaso ta gaya mini"

Yaya nafisa ta numfasa kafin tace.
"Au umma salim ɗin ne dai bai haƙura ba wato yanzu kuma da ikram za'ayi to umma Allah yasa haka ne mafi alkairi sedai Kuma Tana makaranta katse mata karatun zaku yi kenan?"
Umma tace.
"A,a nifa hankalina har yanzu bai gama kwanciya ba, Kin san dai yadda muka ƙare da mahaifiyar shi babu kalar maganar da bata jefe mu da ita ba akan farha bada ban Allah yasa ma Mahaifin nashi a tsaye yake ba ina ga da har gidannan zata zo taci mana mutuncin maƙiya suyi dariya to Se Allah yasa mahaifin sa a tsaye yake shine ya taka mata burki, to kawun kune yaje har gida yana ƙara bawa mahaifin salim ɗin haƙuri dan yadda kawun naku ke faɗa ko a hanya baya yadda su haɗu da mahifin salim sabida yadda yake jin kunyar shi, to shine fa mahaifin salim ɗin kecewa kawun ku Shifa yana ganin acikin ƙannen farha a  sake bawa salim guda ɗaya tunda ya gama ginin shi yayi komai matar dama ake jira"
Yaya nafisa ta katse umma da cewa.
"To shine aka bashi Ikram?"
Umma ta girgiza kanta.
"A,a shi kin san kawun ku in ze magana tara mu yake gaba ɗaya har yanzu shibe san ya ware mace ɗaya yayi shawara da itaba, To shine jiya ya taramu yake gaya mana Shine na buɗi baki nace to tunda haka ne ga Ruƙayya ko Hadiza tunda Wannan shekarar zasu gama makaranta, Amman shi kawun naku se yace a,a ga Ikram nan ƴar ɗakin su Farha in aka bawa salim seya fi jin daɗi, Kuma ma ikram tafi farha sanyin hali da haƙuri to tundaga nan suke ta ƙananun maganganu musamman ita babarsu Hadiza dan ba'a ƙare taron da ita ba tashi tayi tabar mana wajan tana Mita, nifa Nafisa bana Murnar wannan abu saboda Ikram duka nawa take ma da za'a mata maganar aure"

Yaya nafisa ta saki fuska cikin farin ciki tace.

"Umma bafa aja da ikon ubangiji ke dai addu'a zaki muma kuma mu tayaki duk abin da yafi zama alkairi Allah ya tabbatar sabida seta yuwu rabon ikram ɗinne ma Allah yasa akai haka data shiga gidan sa ita farha ɗin ta Mutu Ai da Ikram gwara da Allah ya kawo wannan masalahar sannan in batun shekaru kike yanzu ikram nada shekara kusan sha takwas a jiki fa tafi farha sannan tafi farhan ki Nutsuwa kawai in yana son auren ai yarjejeniya akan ze barta ta fita tai jarrabawar ƙarshe Shikenan sabida umma wata ni'ima Allah yayi miki kina kallo kece kaɗai mai ƴaƴa mata agidannan meye bamu gani ba wani irin hali ne bamu shiga ba, wallahi umma wani bin ko agidana ina son naci abu mai daɗi kona ɗinkawa yara amman inna tuno ku agidannan sena haƙura na ƙullo na kawo muku ranar da Farha taje take gaya min lokacin su Halifa sun sami aiki amman kowa babarsa yake bawa Abin cefane ranar har kuka nayi nace duk dan ke ake wannan sabida baki da ɗa namiji amman ki duba ni'imar Allah kaf ƴaƴanki Farha ce kaɗai takai shekara ashirin da ɗori batai aure ba amman duk ɗinmu muna shekaru kaɗan Allah yake bamu mazaje to ga Ikram ma farhan datai jinkirin a hakan ashe ajikinta za'a huta sabida haka Umma ki godewa Allah su ga ƴaƴan nan birjik agaban su Na gidan Mijin ma ba daɗi suke jiba mu ɗinnan wallahi Munfisu rufin asiri to zuciyarki wankakkiya Allah ya duba shiyasa ya Yaye maki damuwar ƴaƴan ki cikin sauƙi"

Dukkan maganganun yaya nafisa haka suke kuma umma taji ta sami Nutsuwa sosai da maganganun Nafisa sabida dama sune kamar abokan shawarar tata Umma ta dubi yaya nafisa.

"Haka ne maganarki to Allah ya zaɓa abin da yafi alkairi seku soma tari dan dama nace Ikram taku ce kune zaku aurar min da ita ni hutawa zanyi"

Yaya nafisa tayi dariya.

"Da yake kin aurar da farin cikin ki umma masoyiyyar farha oh wannan ƙauna amman umma yanzu kin dena Jin zazzaɓin ko?"

Umma ta wurga mata pillo tana dariya sannan tace.

"Ai wannan zazzaɓi bazan dena ba har se naga auta ta, Sannan kuma da kike batun na aurar da farha babu fa abin da nayi mata na uwa Kina kallon yadda wannan aure yazo abu kamar almara babu wani shiri haka aka tafi da yarinyar nan kamar Marar gata ko sabbin kaya babu"

Umma ta faɗi maganar cikin damuwa Hirar su suka cigaba dayi har zuwa lokacin da Ikram ta dawo daga makaranta ta gaishe da yaya nafisa ta wuce ɗaki ta cire kayan makaranta ta fito ta shiga kitchen ta zubo abinci ta zauna tana ci suna hirar su.

Aliyu daga masallaci fita yayi zuwa cikin gidan su mahaifinsu yayi Musu sallama sannan ya kira Musa Suka wuce office dan ya ɗanyi abin da zeyi kafin lokacin tafiyar shi ya cika dan Jirgin ƙarfe ukun yammaci ne ze tashi dasu in sha Allahu........

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 81*

Tun da ya shiga office ɗin shi yake faman aiki yana damƙawa Musa dukkan wasu abubuwan da zasu gabatar Idan baya nan seda akai sallar azahar a masallacin Dake cikin kamfanin nashi

sannan ya rufe laptop ɗin dake gaban shi suka fita da Musa zuwa masallaci bayan sun idar da sallah Office ɗin dai ya kuma dawowa lokacin ya ɗago ya kalli Musa tare da bashi umarnin ya sai kayayyakin sawa irin dogayen rigunan nan ɗinkakku sabida lokacin ɗinki ya ƙure to ina ma yasan size ɗin ta in ma ɗinkin ne, yakai gidan salama sannan yaɗan yi siyayyar kayan motsa baki ya tafi dasu.
amman yayi sauri ya dawo sabida ze kaishi gidansu fatima kafin Jirginsu ya tashi da ladabi musa ya amsa mai sannan ya fita ya laluba wayar shi ya shiga kiran Layin salama kusan sau uku tana ringing bata ɗaga ba se daya kira na huɗun sannan ta ɗauka da muryar bacci ya hau yi mata masifar baccin me take bata ji kiran shiba Haƙuri ta bashi umarni ya bata akan ta miƙawa farha wayar salama ta miƙe ta shiga ɗakin da farha ke ciki bacci take sosai tace masa bacci take se cewa yayi ta tashe ta, ta bata wayar Salma ta cika da mamakin wannan naci haka amman taja bakinta tai shuru ta shiga tashin farha wadda ta Miƙe bakin ta cike da yawu taje ta zubar ta dawo ta karɓi wayar salma ta fita tabar mata ɗakin.

"Fatima kin tashi lafiya?"
Taji sassanyar muryar shi acikin kunnenta.
Ta turo baki tana wani kwaɓe fuska dan takaicin katse mata baccinta da yayi.
Tayi masa shuru, yayi ƙasa da murya.
"You are angry with me because I woke you up, so I am sorry" ya faɗa cikin ƙasa ƙasa da murya, still shurun nata ne ya kuma biyo baya yaji hankalin shi ya tashi ya kuma yin ƙasa da muryar shi "Kin zaɓi ki hukuntani ta hanyar yi min shuru idan ina miki magana ne kome fisabilillahi me yasa kike son ɗaga hankalina ne?" ya faɗi maganar yana sauke ajiyar zuciya mai ƙarfi a hankali ta kwanta a saman gadon muryarta can ciki tace.
"Ina kwana?" ya saki murmushi me sauti"Se yanzu kika san yaya na kwana bayan da shuru kika min" ta turo baki kamar yana ganinta tare da cewa"Bacci fa nake yi mai daɗi kasa aka tada dani" yayi murmushi "Sallah zanji kinyi and kina azumin?" ta wani yi ƙaramar dariya "Ina yi mana ta yaya zan sha azumi babu wani dalili, sallah kuma tun asubah nayi kaima kasan ba wasa da sallah" yaja ajiyar zuciya tare da cewa "To Alhamdulillahi yaya kike jin zaman naki kuma yaya kike ji ajikin naki?" ta lumshe ido saboda har Lokacin baccin na kanta "Zaman nan yafi na gidanku daɗi sabida Aunty salama tasan darajar ɗan adam kuma tana girmama ni, sannan Jikina lafiya lau sema ƙarin kuzarin dana samu wanda yafi nada" ya Jinjina kai cikin rashin jin daɗin maganarta yasan magana ta faɗa a fakaice wato gidansu ba'a san darajar ɗan adam ba lallai ta riƙi su Ammi acikin zuciyarta seya kawar da maganar yace mata "Jirgin ƙarfe uku zamu bi wace addu'a zaki min?" tayi dariya "Allah ya kaika lafiya, idan kaje kayi addu'a Allah ya baka ƴan uku da ƴan huɗu a wajan Aunty mami" da sauri yace "Kefa bakya son ƴaƴa dani?" ta rufe ido cikin jin kunyar abin da ya faɗa mata sannan tace "Ni ai nai ƙanƙanta da yawa ina zan iya rainon ƴaƴa ai se su karyani ba yanzu ba ita dai Allah ya bata" ya cika da mamakin Furucinta "To idan Allah ya baki fa?" tayi dariya "Zan karɓa amman wallahi sedai kaji da ƴaƴanka dan bazan iya musu komai ba Inji ma da nauyin cikin kai in sha Allah bama zan haihu yanzu ba yadda mata keci wiyar ciki data haihuwa" dariya yayi sosai lallai wautar fatima takai ta kawo tan tare da cikin ma bata sani ba sannan har take faɗin ba zata haihu da wuri ba har sukai sallama dariya yake mata kuma hirar tasu tayi masa daɗi Sabida shirmen data dinga zuba masa Minti kaɗan musa ya dawo Suka wuce Gida wanka yayi ya fito cikin shirin sa har part ɗin

ammi mami ta raka shi addu'a ammi ta dinga yi masa Sadiƙ da Bashir ne suka rako shi duk yadda jamila taso ganin Aliyu abin bai samu ba saboda yadda mami ta liƙewa mijinta sadiƙ da Bashir wata motar suka shiga daban driver yaja su shikuma ya shiga cikin wadda Musa yazo da ita suka wuce Gidansu farha seda ya gyara sosai ya saka face mask sannan ya sauka Yabar Musa a mota ya gane gidan duk da an gyara shi amman Yadda Gano gidan abin har mamaki ya bashi shi kanshi doka gate ɗin yayi ƙanin farha ɗan ɗakin su ruƙayya ne yazo ya buɗe Ya zubawa Aliyu ido yaga fuskar shi a toshe Aliyu ya zame face mask ɗin shi tare da cewa yaron "Ki ramin baba agida" yaron yace "Ai baya nan ya tafi gaisuwar Mutuwa" Aliyu yayi shuru kafin yace "To kace wa maman su Farhan tayi baƙo a waje" Yau ce rana ta farko daya faɗi sunan ta na laƙani dan yaron yafi ganewa aiko yaron ya koma ciki aguje yaje ya gayawa Umma wadda tace wa Ikram taje ta gano mata wanene Ikram ta saka Hijabi ta fita Tana zuwa gaban Aliyu taɗan saki fuska ta tsugunna ta gaishe dashi.
"Wai umma tace waye?"
Yayi murmushi yana kallonta.
"Kema wace koke ce Ikram mai ɗan malele?"
Dariya tayi tana Ɓoye fuska.
"Nice dai ikram amman bana ɗan malele"
Aliyu ya zubawa ikram ido lallai fatima tace yaga ƙannenta seya yi mamaki amman duk da haka Yara ne saurin girma ne sukai.
"Jeki cewa mama Aliyu ne yazo Mijin Fatima"
Ai ikram seta ɗago tana dariya.
"Lahh kaine ina farha to?"
Ya zuba mata ido Tafi fatima fari da kyau ya kawar dakai.
"Tana gida mana"
Da sauri ikram ta juya cikin gida ta sanar da umma wadda Ita kuma umma tayi saurin shiga ɗaki tana murna yaya nafisa ce tace wa ikram taje ta shigo dashi Ikram ta fita ita kuma yaya nafisa ta shiga gyara wajan.
"Wai ka shigo"
Ikram na gaba Aliyu yana binta a baya suka wuce babban falon gidan suka shiga ɗan ƙarami na umma.........
Yaya nafisa na zaune akan kujerun da aka zuba ƙananu a falon Aliyu yayi sallama ya shigo cikin nutsuwa yaya nafisa ta amsa mai sallamar kuma tana nuna masa gurin zama sedai yaƙi zama akan kujerar data ke nuna masa da sauri Ikram ta shinfiɗa mai darduma a saman ƙaramin center carpet ɗin falon ya zauna yaya nafisa se satar kallon shi take Kyau kamar shi yay kanshi Astagfirullah ga Nutsuwa wannan kuwa anya Mijin farha ne.
"Ina kwana yaya mutan gidan?" cewar yaya nafisa ya ɗago ya kalleta bata fi sa'ar bashir ba itama farar ce kuma suna kama da ikram yaya akai basa kama da fatima ya kawar da mamakin shi tare da cewa.
"Lafiya lau Alhamdulillahi"
Yaya nafisa taji yayi mata kwarjini tashi tayi ta shiga cikin ɗaki umma ta tarar da umma zaune a bakin gado yaya nafisa tayi murmushi.
"Umma yana jiranki kije ku gaisa"
Umma dama akwai jin kunyar surukai tace.

"A,a Nafisa jeki kira su Babarsu Ruƙayya su gaisa kafin na kintsa"
Yaya nafisa ta ɓata fuska.
"Haba umma gaskiya ki soma fita in yaso sena kirasu daga baya ai ya shaida kece mahaifiyarta ko"
Ba yadd umma tayi haka ta saka hijabinta har ƙasa ta fita Lokacin Yana ta jan Ikram ta magana tambayarta yake ajin ta nawa Ta dage tana gaya masa sega umma ta fito da sauri ya gyara nutsuwar shi kuma bai yarda sun haɗa ido ba yayi ƙasa da kanshi.
Umma ta sami nesa dashi ta zauna.
Da sauri ya ce mata.
"Mama ina kwana mun same ku lafiya?"
Lokacin ta ɗago da Murmushi da kuma alkunya a saman fuskarta tace.
"Lafiya lau yaya mutan gidan?"
Lokacin shima ya ɗago ya kalleta da sauri yayi ƙasa da kanshi Ko kaɗan ba zaka ce maman fatima bace sabida basuyi kama ba Itama fara ce tas.
Ɗakin shuru yayi.
Har yaya nafisa ta fita domin kiran mutanan gidan.....*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 82*

Ɗakin Babarsu rukayya ta soma shiga ta gaya mata tazo ga mijin farha yazo sannan ta shiga ɗakin babarsu hadiza wadda dan tsananin ruɗewa seda zaninta ya kunce"Nafisa mijin farha ko mijin fa'eeza?" Yaya nafisa tai dariya tare da cewa "Mijin farha dai shine yazo ya gaishe daku"
Da sauri ta juya ta koma falon Umma bata zauna anan ba Ɗaki ta wuce ta sami Ikram a zaune dan tunda Umma ta fita wajan shi Ikram ta tashi daga wajan taba su guri Falon yayi shuru dan duk cikin su babu wanda ya kuma magana tun bayan gaisawar da suka yi.

Aliyu jinsa yake wani iri ita ma umma haka Cikin haka Su Babarsu Ruƙayya sukai sallama umma ta ɗago da far'a ta amsa musu zama sukai suna gaishe da Aliyu Babarsu Hadiza tsabar ruɗewa ma cewa take "Ina farha ɗin?" murmushi yayi tare da cewa "Tana nan lafiya shima sallama yazo yayi musu zeje saudia" daga haka shuru ne ya biyo baya dan ko wacce tasha jinin jikinta Aliyu ba kalar wanda za'a masa baragada a gaban shi bane ba Ko wacce mamaki take ina farha ta samo wannan Miji na kere sa'a falon tsit yayi seda suka ji tashin maganar kawu sannan Babarsu Ruƙayya ta miƙe dan ta gaya masa ga baƙo A babban falo kawu ya zauna Aliyu ya tashi tare da ajewa Umma damin ƴan dubu dubu agabanta yayi mata sallama umma tai kamar ruwa ya cinyeta dan ta kasa Motsi sabida dama ita bamai sake wa bace da surukai wajan kawu yaje a ƙasan carpet ya zauna suna gaisawa.
"Muna ta ganin abin arziki fa Allah ya ƙara maka buɗi ina fatima?"
Kanshi yana sunkuye yace.
"Tana nan lafiya nima sallama nazo muku zan tafi saudia bana son ku shiga shakku akaina danna tabbatar Muku da gaskiya ne yasa nazo"
Kawu addu'a ya dinga zubawa Aliyu wadda tai masa daɗi sosai yaran gidan sukai ta zuwa suna

gaishe dashi su Halifa ne kaɗai basa nan Amman hatta su Ruƙayya seda suka zo suka gaishe dashi kuma duk wanda yazo se Aliyu ya bashi kuɗi.
"Kaga fa waɗannan duka ƙannen fatima ne" cewar kawu yana dariya Aliyu ya zaro ido sabida sosai abin ya bashi mamaki daya ga su Ruƙayya Dan sun fi farha girma.
Kawu ne yace.
"Amman duka tsiran su babu yawa ita fatima tana da shekaru ashirin da huɗu ne, Su Ashirin da biyu na haifa Akwai wasu a ɗakunan su, ita fatima su Biyar ne a ɗakin su sadiya nafisa fa'ieeza fatima ikram ni bana barin ƴaƴana suyi karatu mai tsawo daga sun taso Indai sun sauke kur'ani aurar dasu nake akan Fatima ƴaƴana suka fara cigaba da karatu wadda ashe jinkirin danai ban bawa salim ba kaine mai rabon, yanzu haka ƙanwarta zan bawa salim ɗin nai masa Huce zuciya"
Aliyu dai bai ce komai yaɗan duba agogon shi ya zaro ido dan lokaci ya tafi.
"To baba ni zan koma duk abin da kuke buƙata ka gayawa mai kawo muku abinci Magana in sha Allah, sannan akwai shagon da nake son na saya maka shi anan Wajan Mandawari se a zuba maka kayan abinci ka dinga saidawa ya ɗan fi zaman haka baka komai"
Kawu ya washe baki cikin Murna yace.
"Kamar kuwa ka sani Wallahi bana son zaman nan haka tunda ina da ƙarfina da lafiyata Nagode Nagode Allah yasa kafi haka"
Aliyu yayi murmushi.
"Baba kada ka damu duk abin da zan muku kamar nayi wa mahaifana na ne Allah ya saka muku da alkairi da kuka bani auren yarinyar ku batare da kun duba ni ɗin waye ba, Kuma in sha Allah zan riƙe fatima da gaskiya da Amana"
Ya faɗa yana tashi wanda lokacin Umma ta fito da baƙar leda a hannunta Dambun nama ne acikin wata farar roba wanda Yaya nafisa tazo mata dashi rasa me zata bashi tayi shine ta fito dashi.
Yana ganin umma ta fito yayi murmushi umma ta kawar dakai Tare da cewa.
"To kazo mana babu zato ka ɗan wannan kayi guzuri babu yawa"
Ta miƙa masa Ledar sannan ta ɗan kalle shi.
"To Allah ya tsare hanya ya kiyaye hanya ya kuma karɓi ibada, Koda wanda zeje wajan farha?"
Cewar umma yaɗan yi jimm.
"Mama akwai saƙo ne?"
Shiga ɗaki umma tayi can ta fito da wata ledar daban.
"Maganinta ne Na ciwon ciki da take fama dashi, to ban san a wani hali yanzu take ciki ba nidai na amso mata shi to kuma har yanzu naji shuru bata zo ba" Umma ta faɗa idanunta yana kawo ruwa se kawu ya hau sababi.
"To Asiya in banda abinki Kukan me kuma zakiyi yaronnan dan fa ya kwantar mana da hankali yazo In marar gaskiya ne ta yaya zezo gidannan eye? kuma yace in ya dawo ze kawo mana ita mu ganta dan hankalinmu ya kwanta"
Lokacin hawayen Umma ya gama zubowa.
"Kayi haƙuri dan Allah,ga maganin nata ka tafar mata dashi ka bayar akai mata akwai duk yadda zatayi amfani dashi ajikin takarda ikram ta rubuta"
Aliyu kasa amsar ledar yayi masifar tausayi baiwar Allah'r ta bashi lallai soyayyar ɗa da mahaifi se Allah ya lura gaba ɗaya hankalin mahaifiyarta ba a kwance yake ba yaɗan sassauta Murya

cikin rarrashi Lokacin ya durƙusa a gaban umma ya dafa ƙasa da hannayen shi.
"Mama ki kwantar da hankalin ki, Ina da mahaifiya mahaifin tun muna ƙanana ya rasu, Ina da ƙanne mata wallahi bazan cutar Miki da ƴarki ba naga har yanzu baki gama Yarda dani ba Ni ba macuci bane, amman In hankalin ki baya kwance zanje yanzu na kawo Miki ita inna dawo sena zo na tafi da ita"
Kawu ne ya katse Shi da sauri.
"Jimin maganar banza Haba Aliyu kai kamar ba namiji ba kamanta shirmen mata ne rabu da Asiya soyayyarta da Fatima tayi yawa ban taɓa ganin ɗanda Asiya take so har ta kasa kawaici akan sa kamar fatima ba Inka biye mata ba zaka tafi ba zaman rarrashin ta zakai tayi har Lokacin ka ya ƙure...........*RABO YA RANTSE! Iittafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 83*

Cewar kawu Umma ta share hawayen ta.
"A,a Aliyu wallahi na yarda dakai fa Kada ka dawo min da ita ni ai uwa ce Burina Naga ƴaƴana agidan mazajen su Suna zaune lafiya Allah ya Tsare ga maganin nata"
Ta miƙa masa yasa hannu ya amsa Kawu har wajan mota ya raka Aliyu se hira suke kamar sun saba Aliyu ya shiga mota kawu ya koma gida Bakin matan gidan muƙus ba wanda ya iya magana Umma ta Mayar da Ajiyar Zuciya Allah mai rahma da jinƙai yau dai ya fitar da ita daga Gorin Babarsu Hadiza wadda take caɓa mata magana kusan kullum akan auren farha to yau dai ga Mijin farha yazo Mijin kere sa'a kuma ya cika kowa da abin arziƙi dan kuɗin daya bawa Umma haka ya bawa ko wacce acikin su Ranar Umma ta saki ranta har yaya nafisa kafin ta tafi nata gidan tana tsokanar Umma Su kansu yaran gidan wuni sukai maganar Mijin farha ɗan gayu mai kyau mai Kuɗi ranar dai Abin se San barka shi kanshi kawu ya wuni cikin farin ciki Musamman na kawo ƙarshen zaman shi haka da Aliyu zeyi domin wannan shago daze Buɗe masa ba ƙaramin Daɗi kawu yaji ba.

Aliyu jingine kanshi yayi da Jikin seat ɗin kujera mahaifiyar fatima ta bashi tausayi jiyay ze cigaba da riƙe mata ƴarta Amana Muddin rai, Haka zalika mahaifin fatima ya kwanta masa arai sabida yadda ya nuna yarda a tare dashi har kunyar kanshi yaji lokacin da ya ga mahaifin fatima ya dage yana kare shi a wajan mahaifiyarta, yaja ajiyar zuciya yana cewa "Ya Allah ka tayani riƙon amanar waɗanda suka bani yarda" Musa dake driving yace "Oga kana magana ne?" Aliyu yayi Murmushi tare da cewa "A,a" ya faɗa sanda yake Zazzage maganin da Umma ta bashi zaro idanu yayi Lokacin da yake karanta maganin maganine na ciwon mara na gargajiya shine Umma ta karanta tace na ciwon cikine Murmushin gefen baki yayi tare da aje maganin yana wani Lumshe ido yana tunanin ai ya kawo mata ƙarshen ciwon mararta tunda sun zama abu ɗaya dama yawanci ƴammata na fama da ciwon mara ne saboda rashin aure ƙarfe uku daidai suka ƙarasa airport tuni su sadik sun tsufa a wajan sallama sukai da Juna adaidai Lokacin Jirginsu Aliyu ya ɗaga ƙasa mai tsarki sedai fatan Allah ya dawo dashi lafiya.

Washe gari da Ammi da sadiƙ da sakina da ƴaƴan sadik safna sajeeda Mami suma nasu Jirgin

ya ɗaga bayan su hajjo sun bar Gidan kowa ya tafi kafin su dawo dama shima Bashir Ranar da Aliyu ya tafi shima yabi jirgin abuja na ƙarfe shidda gaba ɗaya Gidan Ammi se ma'aikata maza dan babu kowa.

Zaman farha agidan Salma se son barka sabida zama suke na mutunta juna da alkunya a tsakaninsu Salma tana girmama farha abin har Kunya yake bawa farha dan hatta abinci Salma bata yarda farha taje dinning har ɗaki take kawo mata kuma ta hana ta aikin Komai ita ke yi mata Abin na damun farha Yau kwananta goma agidan wanda ya kama azumi kwanan shi goma Salma tayi mata awon Cikin a dubarance ta karɓi Fitsarin Farha ba tare data bari ta gano komai ba kuma Alhamdulillahi abin da Aliyu ke zargi ya tabbata dan Ciki ne ɗauke ajikin farha har na wata ɗaya da Sati uku wata Biyu ba sati ɗaya kenan tun daga nan kulawar da salma ke bawa farha ta Kuma ninkuwa Kuma Alhamdulillahi Farha tana ta samun lafiya matsalarta kwaɗayi da bacci amman bayan nan yanzu ko amai ba sosai take yi ba Ga wata ƙiba data ke yi kamar bata azumin ga shi ta ɗashe ta koma fara tas kallo ɗaya mai hankali ze mata ya tabbatar tana da shigar yaron ciki wanda ita sam bata san dashi ba kusan koda yaushe ta kwanta inta danna cikinta taji yayi tauri se tace Tsutsar ciki ce seta tashi ta ɗauko ayaba tai ta ci kamar yadda ya gaya mata sabida gaba ɗaya ta manta da wata al'adarta sam batai tunanin Misssing watan data yi.
Kayanta ma sun mata kaɗan basa shigarta yanzu sabida yadda Ƙirjinta ke rinjayarta se kayan da Musa ya kawo mata take sakawa Take harkokinta Daga ɗakinta zuwa falo Tare dasu Dady dasu ka manne mata dan Ko bacci ma tare suke yi.

Salma Farha na bata tausayi sosai haka zalika Aliyu gaba ɗaya tausayi suke bata tunda ya gaya mata halin da suke ciki shida yarinyar taji tsananin tausayin su ya kamata ita kaɗai take juya abin aranta Ta rasa wa zata gayawa Taji dadî Dan shi kansa Mijinta ya lura bata da kuzari yayi nacin ta gaya masa meke damunta tace azumun da take yine kaɗai da kuma yanayin aikin ta dama shi mijin ta bamai sa ido bane koda yaga farha sau ɗaya bai tambayi salma wacece ba tunda yasan ba zata kawo masa wadda bata da alaƙa da ita ba daman ita ma farha ba fita take ba tun da suka haɗu sau ɗaya basu sake haɗuwa ba.

Kimanin kwanaki ashirin da fara azumi rabon farha da Aliyu tun wayar da yayi mata ranar daze tafi abun na damunta sosai na yadda bai taɓa kiranta ko a wayar ƙanwar shi yace a bata ba, wani bin inta kwanta haka zatai tayin kuka har bacci ya ɗauke ta a hankali ta shiga tsananin damuwar rashin Mijinta wanda bata san tana son shi da yawa ba seda sukai nisa da juna Komai dai gashi nan a gidan salma amman baya burgeta har taji tafi son zaman gidan Ammi duk da wiyar da take ci amman ai da sauƙi tunda tana tare da Mijinta Kome tace tana so se salma ta samo mata fara ma da take so Har ta isheta sabida Kullum in salma ta dawo daga aiki seta siyo mata Tsabar yadda ta saka damuwa aranta yasa daga tasha ruwa zazzaɓi yake rufeta haka Zata ƙudundune taita rawar sanyi se cikin dare yake lafa mata sannan ga abin da yake tsorata ta shine Motsin da cikin ta keyi mata Haka zata dafe cikin tana jin yana motsi taita hawaye seta ci ayaba Guda goma arana tana fatan Allah yay gaggawa fitar da tsutsar da take damunta acikinta.

Yau azumi kwana ki ashirin da biyar Salma ce ta shigo ɗakin farha kasancewar week end ce ranar babu aiki ta zauna a bakin gado farha kuma tana kwance Cikin bargo yanzun ma kukan ta gama bayan tayi sallar azahar ta kwanta bacci.
"Aunty fatima bacci kike yi ne dama zaki bani size ɗin kayan kine sabida zan miƙa mana ɗinkin sallah" cewar salma farha ta miƙe zaune sabida bata da nauyin bacci.
Salma ta kalleta tace mata "Subuhanallahi Aunty fatima kuka! kuma kukan me kika yi haka fuskarki duk ta tashi haka kodai kina Missing ɗan uwana ne?"
Salma ta faɗa tana Juyawa Kusa da farha suna fuskantar Juna farha cusa kanta tayi a cinyoyinta tana Ɓoye fuska sabida maganar salma ta bata kunya "Dan Allah ki sanar dani Ko kina Missing ɗan uwa ne?" ga mamakin salma se taga farha ta girgiza kai se kuma ta fashe da kuka Mai ƙarfi tana yarfe hannunta.........
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 84*

"Subuhanallahi abin har ya kai haka Aunty fatima kuka kike yi meke damun ki me nake yi miki zama dani ne bakya so ko wani ke takura miki agidan nan?"  salma ta faɗa duk a ruɗe farha kasa magana tayi kuka take yi sosai wanda hakan ya ƙara tsorata salma Sabida ko jiya da sukai waya da Aliyu seda ya ƙara jaddada mata cewa ta dinga kula da fatima sosai saɓani suke dashi duk sanda ya kira salma Ita kuma bacci take idan yace a bata wayar salma seta ce masa ba'a son mace idan tana da ciki ake tashinta daga bacci wannan tasa tun yana cewa ma a bata in ya kira har yama dena sedai kawai ya kira salma su gaisa ya tambayi lafiyar matar sa ya kashe wayar tunda ya yarda da salma ɗari bisa ɗari yasan ba zata cutar masa da fatima ba shiyasa Ya saki hankalin shi bai damu ba.

Goge hawayen daya wanke fuskar farha salma take da hannunta jikinta duk yayi sanyi muryarta a raunane ta kuma cewa "Kinki min magana fatima dan Allah ki gaya min in da wani abun da yake damun ki, ɗan uwana ya damƙa min ke amana in na bari wani abun ya same ki naci amanar zumuncin Allah Ko baki da lafiya ne duk kin min shuru?" salma ta faɗa kamar zata yi kuka girgiza kai farha tayi tare da sauka daga saman gadon taje banɗaki ta wanko fuska ta dawo ta tarar da salma ta zabga tagumi daga nesa da salma ta zauna muryarta har lokacin bata saki ba tace "Aunty salama wani gagarumin abu ne yake damuna" salma ta ɗago a saɓule tace mata "To fa wani abu ne Aunty fatima wanda har ya sakaki wannan kuka haka wanda ya ɗaga mini hankalina?" farha ta sunkuyar da kanta ƙasa sabon kuka ne yake tawo mata cikin kukan tace "Nina san ƙarshena ne yazo ƙila mutuwa zanyi ma" salma tai saurin matsawa kusa da ita tare da cewa "Subuhanallahi Aunty fatima baki da lafiya meke damunki amman baki gaya min ba?" ta faɗa tana kama hannayen farha, Farha ta kuma fashewa da kuka! kafin tace "Ni kaɗai nasan abin da yake damuna na rasa jin daɗin bakina kullum yawu yayi ta taruwa naita bacci kuma kome naci bana jin daɗin sa ban sani ba ko ƙarshe nane yazo shiyasa Allah ya zaren ɗanɗanon komai" salma ta kusan hantsilawa sabida dariyar data zo mata batare data shirya taba da ƙyar salma ta saita kanta tana sauraran Farha wadda take ta faman kuka can kuma ta

cigaba da cewa "Aunty salma bazan ɓoye miki ba tabbas akwai abin da yake ajiye acikinnan nawa babban tashin hankalina Allah yasa Ba wata masifar bace Dana gaya masa kwanaki yace min tsutsar ciki ce sabida da farko tauri cikina yake min wajan ƙasan marata shine yace mini na dinga cin ayaba tsutsar ciki ce To yanzu fa abun ya gagara yakai maƙura dan motsi sosai nake ji acikina har dafe wajan nake bari ki gani" da sauri salma ta dafe hannun farha wadda take Ƙoƙarin ɗaga mata rigarta duk yadda salma taso danne dariyarta ta kasa tashi tayi ta fita falo ta kwanta a saman Kujera tai dariya ta godewa Allah har cikinta seda ya kusan ƙullewa wato Yaya Aliyu abin da yace wa ƴar mutane kenan ya ɗorata a keken ɓera wai tsutsar ciki gareta.
Wato shi wayo ga mutum halittace wasu ƴammatan suna da wayo da ganewa In wata ce da sauri zata fahimci Halin da take ciki, amman ita wannan sam bata gano kome ke damunta ba yadda mijinta ya ɗorata haka ta tafi, to ta yaya bata gane tai Missing mp ɗinta ba cewar salma a zuciyarta Koda yake in kana cin Damuwa bama ka gane kanka wataƙil tsananin damuwar gidan Ammi da yarinyar ke ciki ce ta hana ta gano Kana lamarin ta salma tashi tayi tare da komawa ɗakin ta tarar da farha zaune ta rafka tagumi.
Zama tayi wata dariyar tana ƙara tawo mata tana danneta "Aunty fatima karki damu babu wata matsala acikin ki ina zaton Kina da ulcer ne kin san ita ulcer Sihiri gareta Yadda takewa Mutum acikin sa seya rantse Ma ciki gare shi" farha ta share hawayenta "Wallahi Aunty salma abin yana damuna sosai, nace to kada naje ko wata gagarumar matsalar ce a tare dani abun yana damuna sosai ban dai gaya miki bane ni naketa fama" salma ta dinga kwantar mata da hankali ta nuna mata wannan motsinfa ba mamaki ulcer ce ke damunta Seda salma ta karɓi size ɗin Farha na kayanta sannan ta miƙe tsaye "bari naje na kai mana ɗinkin kafin ashara ruwa zan dawo in sha Allah" farha taɗan kalleta "Amman Aunty salama sefa an ɗan ƙaran rigata dan waccan tai min kaɗan dama tare muka je aka gwadani kawai dama na jima ban fita ba duk ƙafafuna kumbura suke sabida zaman waje ɗaya" salma taɗan zaro ido "Rufa min asirin faɗan Mijinki ni na isa na fitar dake waje so kike ya dawo ƙasar yau kenan?" farha tayi dariya "Tab ta yaya dan kawai na fita se ya wani dawo wama ze gaya masa babu wanda ya san na fita ai" salma tayi wata dariyar tana cewa "Nidai rufa mini babu ruwana nafi son mu rabu lafiya da mijinki Dan yadda ya kafan sharuɗa akanki Ba zan tsallake ba ina fatan Allah yasa yadda ya kawoki lafiya yazo ya ɗaukeki lafiya" farha ta kalli salma "Yawwa dan Allah Aunty salma shine yace Miki ni matar shi ce?" salma taɗan fito da ido tana murmushi "Tunda ke wancan karon kin Ɓoye mini ai shi ya gaya min be ɓoye mini komai ba" farha tayi ƙasa da kanta "Amman ke ya gaya miki To amman mai yasa be gayawa su Ammi ba? ko lokacin daya kaini gidan cewa yayi kada na bari kowa yasan ni matar sace wannan ne yasa ban gaya Miki ba koda nazo gidannan kwanaki sanda kika ɗauko ni, sabida ya min gargaɗi akan kada na Nuna ko alamar muna da alaƙa dashi Wannan abun yana Ɗaga min hankali dan Allah Aunty salma rayuwar aure zata tabbata a ɓoye ne?"
Salma ta girgiza kai cikin damuwa tace "gaskiya maganar Ɓoye auren ku ma bazata yuwu ba sabida na tabbata kema ai a wajan mahaifan ki yaje ya amso auren ki to sabida me shi ze Dinga Ɓoyewa nasa iyayen ke matar shice bayan auren ku ba haramun bane wannan ba Hujja bace In ma don Kada hankalin Ammi ya tashi yake yin hakan ni a ganina gwara ma tun yanzu ta sani kafin Lokaci ya ƙure naso na bashi shawara amman kuma Bamu sami lokacin hakan ba sabida sanda ya kawo ki sauri yake tayi"*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa

za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 85*

Hankalin farha a ɗan tashe tace "Nima abin da na gani kenan Wallahi Aunty salma in da nasan akwai matsala acikin gidan su da bazan gigin kawo kaina ba na lura shi baya son ko kaɗan asan ni matar sace ke kanki nasha mamakin da naji ya gaya miki ni matar sace shiyasa in kika lura zaki ga koda kike tsokana ta da matar ɗan uwa na ɗan sha jinin Jikina"
Tausayi farha ta bawa salma.
"Ni kam ya gaya min kome hatta sanadin auren ku ya gaya mini Kuma ni kin mini ina son auren ku Kuma ina muku fatan zaman lafiya mai ɗorewa" farha tace "to anty salma har yaushe ne ze faɗawa mahaifiyar shi gaskiya toko hayar iyaye yayi ma aka ɗaura mana auren nifa duk bana hayyacina so nake ya dawo ayi wadda za'ai ma gwara in ba dama nai takai na Kafin zama yayi nisa" salma tayi murmushi tare da cewa "Yaya Ali baze taɓa hayar iyaye ba ƙannen mahaifin mu ya tura gidanku aka amso mai auren ki, Kuma abin da baki sani ba shine Wallahi yana son ki in da baya son ki da baze dinga damuwa da lamarin kiba kada ma kice zaki ɗaga masa hankali yazo yana ɓata miki ranki, Ki barshi da abin da ke damun shi Wallahi Fatima abin da yasa kika ga yana Wannan Ɓoye ɓoyen auren naku matar shi Wadda yake aure yanzu da babarta da Ammi babansu ɗaya ammi ce ta haɗa auren kimanin shekara goma tunda sukai auren In Aunty mami ta sami Ciki kafin ta haife yake ɓarewa anyi maganin har an gaji har ɗaurin mahaifa ammata abin ya faskara wanda kin san ta silar wannan matsala ma har Gidan radio ɗin da kike aiki suka sami Labarin Ƙarya suka watsa akan shi ko?" farha ta ɗaga kanta tare da cewa "Haka ne amman ban san dangantakar shi da matar shiba gaskiya ni iya labarin haihuwar shi Md ya bani yace na watsa" salma taja ajiyar zuciya sannan ta ɗora da cewa "Fatima Mun sha wiya a rayuwa Mun taso cikin rashin gata mahaifinmu maraya ne.............seta fashe da kuka cikin kukan take bawa farha labarin su daya shuɗe seda takai aya sannan tace " Allah shine gatan mu, Ya Aliyu shine gatanmu komai da kika sani shiya tsaya mana har muka kai wannan mataki, Ammi uwace yadda tai mana ne yasa Ya Aliyu baya son ɓata mata rai baya son saɓa mata Sabida mun taso ne a rayuwa bamu da kowa se ita, Ammi ta haɗa auren Mami dashi ne sabida tana ganin mami ƴar yayarta ce sabida yadda muka taso a rayuwa yasa Ammi take tsoron kada Yaya yaje ya auro matar da zata tarwatsa mana zumunci mami kuwa kinga ƴar uwarta ce Bata da matsala a tare da ita, Yaya Aliyu yana da wadda yaso a shekarun baya amman ammi ta hana shi auren Najuwa Ammi bata son Ya Ali ya ƙara aure ko yayi maganar aure in ma haihuwa ce tace ya jira mami zata cika masa gida da ƴaƴa amman maganar gaskiya ammi bata son yaya yayi aure sabida tsoron matan zamani yadda Allah ya ɗaukaka shi tana ganin ko wace mace da zuciya biyu zata aure shi bada zuciya ɗaya ba"

Farha taja ajiyar zuciya lallai inda ranka kasha kallo a fili ta furta "To Ammi ta lissafa ba daidai ba yawanci ma wanda kake zaton bashi da matsala a rayuwarka to daga ƙarshe shi yake zame maka illah, Ai bakawa Allah dubara ƙaddarar bawa kuma bata sauyawa wannan duk ba mafita bace In Allah yaso ya jarabci ɗanta da shu'umar mace wallahi ba wayo ba dubara seya bashi, sannan shi aure muƙaddari ne daga Allah Ni yanzu na taɓa kawowa zan aure shi toni ko a mafarkina ma ban taɓa kawowa ba dan ban sanshiba hasali ma akwai wanda nake so aka

tsaida maganar aurena dashi amman ɗan uwanki ya kutso akai dashi wallahi Ammi tayi ganganci To yanzu bada ban yana da biyayyar ba in yaje yayi zina fa koya yi auren ya aje matar a wani wajan fa?" salma tai saurin cewa "To baga shi ba ma ya auro ki ya ajeki agidan kuma bata sani ba nima dai naga Wannan Ƙudiri na Ammi sam bai yiba wallahi" farha taja ƙaramar ajiyar zuciya tare da cewa "Ai a matsayin ta na uwa addu'a zatai masa akan Allah ya bashi mace tagari bawai ta tsaya akan mami kaɗai ba ita mamin wahayi akai mata aka ce lallai ta garin ce? zuciyar mutum se Allah, Ni dai Allah ya sani ina son Mijina kuma tun kafin nasan asalin shi waye na soshi, amman inna ga da matsala zan nemi ya sakeni dan wallahi nagaji kullum ina ɓoye a ɗaki Kullum ban da ƴanci Koda yaushe Cikin fargaba nake idan Ammi bata san auren mu yanzu ba yaushe zata sani toni nagaji shi ta zamewa dole yayi mata biyayya bani ba kawai ni ya sake ni yaje ya zauna da wadda mahaifiyar shi take so take kuma burin su haihu tare" farha ta faɗa daɗan Ɓacin rai salma ta sassauta Murya tare da cewa "Nifa ban gaya miki maganar nan dan ki je ki ɗagawa mijin ki hankali ba kija min masifa kuma kada ki sake maganar saki dan babu kyau batun Biyayya ga ammi kece zaki ƙara nusar dashi hanyar yiwa mahaifiyar shi biyayya Dan ya gama da ita lafiya abin da ya shafi yaya ke ma ai ya shafeki Bazan Ɓoye miki ba yaya ya auri mami ne dan biyayya ba domin yana son taba kuma auren ku da yaya ze zamewa Ammi izna taga duk yadda taƙi yayi auren daga ƙarshe ya auro mata matar da take zaune da ita batare data san matar sa bace ba wannan ma babbar izna ce gareta dan Allah ki kwantar da hankalin ki kada ma Ki sa damuwa aranki na gaya miki waɗannan maganganu ne dan hankalinki ya kwanta da wasi wasin da kike na hayar iyaye da yaya yayi sannan na gaya Miki ne dan Kisan waye Mijinki dan shi be zama lallai ya gaya Miki ba"
Farha ta kwantar da kanta a jikin Pillow lallai akwai matsala har salma ta gama maganganunta ta fita bata iya magana ba, Gaba ɗaya tunaninta ya tsaya ammi wace irin uwa ce Murmushi mai ciwo ta saki Su a iya fahimtar su kenan akan ammi Amman ita fahimtar datai Ammi ta hana Aliyu yayi aure ne dan kada acika gida da ƴaƴa Mamin ma abin da yasa ta saki hankalinta da ita dan tana samun ɓarin ciki ne amman ita fa a yadda ta Zarga kenan acikin ranta Hawayen tausayin Mijinta taji yana zubo mata lallai suna cikin gagarumar matsala ita dashi dan tun yanzu ta fara Missing ɗinsa dan tabbas data sami dama sedai yaga wayam dan zakara bata sa'a zeyi ita ba zata iya auren rashin ƴanci ba dan a yadda yake shakkar mahaifiyar shi ɗinnan bata hango narasar ƴancin su anan kusa to gwara tai ta kanta Tun wuri kada ma tazo ta sami Ciki Azo a sami matsala, Dama haka yasha wiyar rayuwa dama haka suka taso lallai duk wanda yayi haƙuri ze sami nasara ta tausaya masa a yadda taji tarihin sa lallai Bayan wiya se daɗi tana nan a kwance salma ta shigo cikin shirin fita taɗan kalleta.
"Ni zanje wajan ɗinki su Dady kuma zunje aski da Babansu gashi gidan yayi shuru ga wayata zan baki ko Mijinki ze kira dan ya kikkirani kina bacci ni kuma naƙi tashin ki"
Salma ta faɗa tana miƙa mata wayar ta sukai sallama salma ta fita kwanciya Farha ta kuma yi tunanin mafitar ta cike acikin zuciyarta tabbas ya zama dole ma ta samowa kanta mafita wata sabuwar tsanar Ammi taji acikin zuciyarta Har akai sallar la'asar tana faman tunani tashi tayi lokacin data ji Kiran sallah tayi sallah ta fita falo mai aikin Salma nata Gyaran kayan miya a kitchen gaisawa sukai da Farha wadda ta zauna taɗan kalli mai aikin salma cikin sakin fuska tace "Dan Allah Ko akwai tsakin ɗan malele agidan nan?" Mai aikin salma taɗan zaro ido tana dariya "A,a babu amman in kina so sena Miki da semo shima yana daɗi" farha taɗan haɗiyi yawu tare da cewa "To dan Allah ki sakan salak da tumatur ana shan ruwa shi zan fara sha" mai

aikin salma tana dariya tace to farha tashi tayi ta koma ɗaki se gab da magariba salma ta dawo suko su dady ma seda aka idar da sallar magariba suka shigo Gidan Ana shan ruwa farha da wannan ɗan malele tasha ruwa tasha sosai kuma taji daɗin sa salma se dariya take mata lokacin data shigo ɗakin taga farha ta zage tana ta shan ɗan malele Tana kuwa gama sha gudawa tace salamu alaikum Ta dinga shiga Toilet tana yin sallar Isha'i ta kwanta cikinta se ƙugi yake mata ba komai bane yasa hakan face yaji data danƙara a ɗan malelen wayar salma dake Gefenta wadda har Lokacin salma Bata amsa ita ke Ringing ta ɗauki wayar taga special Number ce bama ta ƙasar nan ba ta mayar da wayar ta aje bata ɗauka ba.

Aliyu yana kwance.............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 86*

A cikin ɗakin hotel ɗin daya sauka Pillow ya danne da ƙafafun shi se ƙaton Bargo fari tas daya rufe jikin shi dashi gefen shi cup ɗin black tea ne wanda yake ta turiri tunda aka kawo mai bai shaba tunda ya dawo daga masallacin harami yake kwance Tunda bai samu wuce wa chaina ɗin ba ya zauna anan saudia addu'a yake tayi sosai akan lamarin shi da fatima da kuma neman Allah ya inganta mai cikinsa dake Jikinta Kuma Alhamdulillahi yaji tana ta kwanta mai aran shi ga kuma damuwar cikin nata da kullum ke manne aran shi ji yake dama da ita ya tawo sabida Baya tare da Mami a halin yanzu ita tana tare dasu Ammi.

Tashi yayi zaune tare da zube dogayen ƙafafun sa a ƙasa shi kuma yana zaune a saman gadon Jikinsa sanye da ƙaramin wando wanda ya manne masa a iya cinyarsa wadda ta cika da tarin Gargasa wadda ta kwanta tai luff baƙa siɗik se singlet fara wadda ta fito masa da gabaki ɗaya halittar dake faffaɗan ƙirjinsa mai cike da kwantacciyar Suma baƙa tai luf Nippy ɗinsa baƙaƙe zagaye da sumar suma kana kallon shi kasan lafiyayyen namiji ne mai ji da ƙarfi da lafiya wanda yake cikin ganiyar shi ta matashin namiji mai jini ajikinsa hannun shi yasa wanda yatsun hannun guda biyu suke ɗauke manya manyan azurfofi masu tsada ajikinsu ya tallafe ƙugunsa ya janyo Ƙasan leɓansa da harshensa yana tsotsa ita kaɗai yake gani a idanunsa Ji yake kamar ze rufe ido ya ganta wata irin wutar soyayyarta ke cin zuciyarsa Number ɗin salma yake ta kira har Lokacin ba'a ɗagaba tsaki yaja yafi kala goma idan baiji Muryarta ba akwai matsala gagaruma a tare dashi Muryarta kaɗai ce zata saukar masa da Azabar da yake ji a gangar Jikinsa.

Tsotsar ƙasan leɓanshi yake yana sake Kiran Number ɗin salma, Farha taja tsaki ƙarar wayar ta hanata bacci Mai yasa ma Aunty salama zata ajemin wayarta a wajena tasan ai ba kirana yake yi ba yau kusan kwana ashirin da Biyar ai bai kirani ba se yau taja tsaki sabo ta Toshe kunnenta da hannunta wayar dai na ƙara Ɗaukar sabon kiɗa na alamar ana kira kamar zata ce wayyo Allah! tai picking call ɗin shuru tayi Aliyu ya ja ajiyar zuciya tunda yaji shuru yasan Gimbiyar tasa ce ƴar rigimarsa dan inda Salma ce da sallama zata ɗaga da gaisuwa.
"Fatima Ina yini" taji Muryar shi Wayyo daɗi Nutso tayi a saman gadon taja Pillow ta matse tana

sakin Numfashi a hankali shuru tayi masa iya muryarshi ma kaɗai ta wadace ta a halin yanzu.
"Fatimahhhh" yaja sunan wanda taji Numfashinta yana ƙoƙarin ɗaukewa yama za'ai ta barshi ai kawai faɗa tayi ba zata iya barin saba son sa a jininta yake tana sonsa kamar Bugun Numfashinta.
"Kina fa jina dan Allah ki kulani Kimin magana Wai meye haka sabon raini kika Ɓullo" ya ƙarasa maganar Cikin faɗa amman bawai mai nuna yaji haushi ba.
Sangarta shagwaɓa ta motsa se kawai ta ɓare masa baki tahau Kuka ƙasa ƙasa mai cike da ɗaga hankalin ma'abocin sauraron shi wayyo Allah! nan da nan ta ɗagawa marayan Allah hankali tashi yayi tsam daga zaman da yake ya shiga sintiri a ɗakin yana yarfe zufa kukan yarinyar ɗaga masa hankali yake tunda can ina ga kuma wannan Lokacin da take ɗauke da ajiyarshi Cikinshi Gudan Jinin shi.
"Shiiiiiiiii wai meye haka Okay so kike nima nayi kukan ko? ko so kike na Shiga cikin damuwa da tashin hankali?" ya faɗa da narkakkiyar Muryarshi mai kama data wanda yake jin tsananin sanyi ga kuma raɓa da tsananin sanyin na Bugun ƙashin sa da Jikinsa to haka muryar tashi tayi kala, "Nifa kawai kukan Daɗi yake min na rasa me yasa Ya zama abokina" ta faɗa tana turo bakinta gaba yayi Murmushi yana jin Nutsuwa da wata kasala tana rufe shi ya koma da baya ya zauna a saman gadon se Kuma ya kwanta tare da ɗaukar Pillow ya ɗauro a saman Ƙirjinsa ya matse shi ya damƙe wayar"Fatima ta rigimar ki se ni ɗin to yaya kike kullum idan na kira salama se tace kina bacci Dafatan kina lafiya?" ya faɗa yana lumshe ido "Lafiya lau Alhamdulillah yaya ibada Allah ya amsa" ta faɗa wayar tai shuru sabida su duka shurun sukai "Tom yaya Kika koma yanzu nasan Kin ƙara girma Ko Jikinki yayi kyau?" kunyar maganar tashi taji dan haka tayi masa shuru se can Kuma kamar wadda ta tina wani abun tai saurin Ce masa "Kasan me?" ya girgiza kai kamar tana gabanshi kafin yace "Sekin gaya min" ta ɗan yi raurau kamar zatayi masa Kuka "Wallahi Abu fa se ta'azzara yake shine nace gwara na gaya maka sabida kana ƙasa mai tsarki kayi mini addu'a" yaɗan Yamutsa fuska duk bai gano mai take Nufi ba "Ban fahimce kiba Fatima?" ya faɗa a hankali "Dama wannan tsutsar ta ciki daka ce nake cin ayaba ka tuna?" da sauri yace "Yes na tina tana girma ne Kokuma yaya ake ciki duk na damu da ita nima" ya faɗa yana toshe baki dan dariya ce taso Kama shi ta gyara kwanciya tare da damƙe wayar da ƙarfi kafin tace masa "To wallahi girma take yi Cikina yay ta Motsi Kullum gashi daga sama Yana kumbura Cibiyata ma Duk ta ƙara Fitowa gashi naita bacci Kullum sena ci ayaba da yawa ɗazu dai nake gayawa Aunty salama shine take cemin Ko ina da ulcer ne wai itama tana haka mutum yayi ta Jin ma kamar yanayin yana da Ciki"  tashi yay ya zauna ya jima bai ji dramar fatima ba A hankali yace "Alhamdulillahi wannan tsutsar ciki mai abin al'ajabi haka ta koma miki kuma kice lallai semun tashi tsaye, to koke ma cikin gareki ne?" da sauri ta wani zaro ido kamar yana gabanta "Ciki kuma angaya maka a ruwa ake sha Daga aure se ciki to ko Yaya sadiyarmu ma seda tai wajan shekara Uku sannan ta haihu fa haka suma su Ya Nafisa ai daga aure ba'a samun ciki da wuri" Da sauri yace "Haka aka gaya miki kenan?" ta wani haɗe rai "Nidai kabar wannan maganar yanzu addu'a zaka min da magani Ko yaya?" yayi Murmushi "Duka zan Miki nima wannan Tsutsar da ita nake kwana nake tashi amman dai kina cin ayabar sosai ko?" Da sauri tace "Eh duk da bana son ta amman haka nan nake daurewa" yayi murmushi fatima da sauranta Shirme ne da ita ace kana ɗauke da Cikin Mutum ka kasa fahimta Lallai da sauranta Shikuma zeta Shigar da ita akan Tsutsar Ciki ce har sanda Cikin ze Fito a Lokacin ta farka daga baccin daya ɗauke ta.

"To Kina cin farar ki kuwa? dame dame kike ci yanzu?" ya tambayeta "Hmm yauma ɗan malele akai Min wallahi naci bakaji daɗi ba Aunty salama tana kula da ni kome nace mata tana Min yau ma ta amsa size ɗin kayana ta kai mana Ɗinkin sallah" Ya saki fuska cikin Jin daɗi yace 'Ai na gaya miki a kaf ƴan uwana ba kamarta wallahi Nasan zatai Miki fin haka Kuma nagode sosai Amman kin san dai ba anan zaki sallah ba" ta wani haɗe rai tana hararar gefe "To a ina zanyi?" ta faɗa kamar zatai kuka "Gidan Ammi nan da kwana Biyu Zan dawo ana Jibi sallah kuma dana dawo ma Ki shirya tanan zan Biyo ƙafata ƙafarki................*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 87*

Ya faɗa batare da wasa a maganar tashi ba, Lokaci kaɗan hawaye suka wanke mata fuskarta "Baki jin me nake gaya miki ne kika min shuru fatima?" turo baki tayi gaba kamar yana gabanta "Ni kika yi wa shuru?" ta kuma jin muryar shi wannan karon a tausashe yayi mata maganar"Toni me kake son nace maka?" ta tambaye shi cikin sigar sakalci ya sauke ajiyar zuciya tare da cewa "Ce maki nayi dana zo zamu wuce gidan Ammi Naji kin min shuru ne baki magana ba" Ta shaƙi hanci tare da cewa "To naji Allah ya kaimu amman ni har ga Allah ana shiga haƙƙina" cikin sauri yace mata"I don't understand you, I am intruding on your rights like that kimin yadda zan fahimta" ya faɗa muryarshi can ƙasa kanta tsaye tace mai "Sabida ni nagaji da zaman gidanku mahaifiyarka bata sona babu sunan da bata haɗani dashi ba har Igiyar shanya ta kirani dashi sabida haka Ni wallahi na gaji Kullum ina ƙunshe a ɗaki Inna fito bauta na fita yi mata ita da marasa kunyar ƴammatannan To yaushe zan sami ƴanci kamar ko wace mace, Ni harga Allah in ba zaka barni anan gidan ba to sedai a rabu danna gaji agaskiya ana ƙwarata" ta faɗa tana murguɗa bakinta Aliyu ya sauke wayar daga Saman kunnensa ya kalli Number tabbas da fatima yake magana wato koda yaushe rashin Kunyar yarinyar ƙaruwa yake ya daure ya danne abin da yake taso masa sabida furucinta na se a rabu ɗinnan ya kaɗa shi matiƙa.
"Fatima"
Yaja sunan a hankali.
"Ina jin ka" itama ta faɗa muryarta babu sassauci.
"Cewa zaki na'am ba ina jinka ba tunda bada yaro ƙarami kike magana ba da Mijinki kike yin magana fatima"
Ya faɗa a hankali.
"To Na'am Mijina" ta faɗa a gatse ya saki murmushi mai ciwo wai kamar shi yarinya ƙarama zata mayar kamar sakarai shi kuma ya biyewa shirmenta lallai haka rayuwa take Kodan akan ta yasan so akan ta ya fara soyayya oho!
"Fatima na kiraki dan hankalina ya kwanta danna sami Nutsuwa amman shine zaki ɗaga min hankalina idan har zan kiraki Na sami ɓacin rai to inda kike ma sena guji zuwa sabida bana son ɓacin rai a rayuwata Kuma na baki haƙuri akan abin da Ammi take yi miki Ammi mahaifiyata ce in kika tayani muka haɗu muka mata biyayya inna gama da ita lafiya kema ribarki ce, Ki barni dan Allah akwai tarin ƙalubale da matsaloli a gabana so nake na ture su tukunna sena sami Nutsuwa" A hasale tace masa "Matsalar ai ba zata wuce Ɓoyayyan Auren da kayi dani ba dan ɗaukar fansa to tunda Dama ba sona kake yiba base ka sake ni ba ai babu wata matsala ni a

ganina tunda dai ba ɗaure ni akai a ƙafarka ba Ka zauna da zaɓin mahaifiyarka wadda take so take ƙauna dan Allah nima abarni nai rayuwar ƴanci kamar ko wace mace" ta faɗa a tunzure Aliyu ya ji hankalin shi ya tashi da irin maganganun da take jefa masa Muryarshi har rawa take kamar ba Aliyu mai saurin fushi da tunzura da rashin ɗaukar raini ba yace mata "Shikenan fatima duk yadda kika ce haka za'ayi tinda kince na sake ki Allah ya sani Bazan cutar dake ba watakil zaman da nake dake akwai cutarwa acikin sa tunda har kike furta kalmar Mu rabu da juna zan baki abin da kike so koda ni zan rasa nawa farin cikin Ki jira zuwana se muyi maganar a nutse" ya faɗa a hankali wanda yasa hantar cikin farha kaɗawa cikinta ya juya inya sake ta ina zata saka kanta Muryarta cikin rawa tace "Nifa baka gane nufi na bane" Ta faɗa a hankali sabida yadda jikinta gaba ɗaya yayi sanyi dajin abin da yace mata.
Cikin sanyi jiki shima yace mata
"I understand your intention fatima duk na gano inda kika dosa kuma duk abin da kike so zan miki koda nine zan cutu Tunda ni bani da ƙima da alfarmar Ki tayani Yiwa mahaifiyata biyayya tunda saki kike so shikenan baki da matsala dashi Amman ki bari na dawo"
Jikinta ya hau tsananin rawa nan da nan tahau kuka.
"Ni yau she nace maka ka sake ni kawai zaka lauya mini magana ta" Duk yadda ta ɓata mai rai seda yaɗan yi dariya ya fuskanci barazana take masa akan ya saketa amman hakan bai kai mata har zuciyarta ba"Kece kika faɗi ɗazu Ki koma ki tariyo me kika gaya min aini kin riga kinga wurin kwanciyata kin raina ni Kince ba zaki koma wajan Ammi ita ma salma da kika ganta ai agidan Mijinta take se kece sakarai zaki ƙi bin naki Mijin nikam in ba zaki koma gidan Ammi a wannan karon za muyi faɗa dake" Kuka ta saka a hankali wanda yake fitar da sautin sa shima hankali "Dama ni ce a ƙasa dole Kome kace sedai kawai nabi dama umma ta gaya min na dinga maka biyayya" ta faɗa tana kuka shima yace "Good Amman umma ta kyauta mini to shikenan zamu gani Zaki bi maganar Umma ko zaki watsar Kuma ai ba Umma ce ta fara faɗi ba Allah ne yace mata tabi Mijinta sau da ƙafa sabida haka Ki zaman shirin Komawa gidan Ammi kema kin kusan shiga naki gidan Ki haƙuri Dai mu lallaɓa duk wanda yayi haƙuri baya faɗuwa nidai nasan ina tare dakeI will never turn my back on you, I will never run away from you unless you want to run away from me,ki saka wannan aran ki fatiman Aliyu" ya faɗa mata hakan Lokacin Jikinta ya ƙara sanyi muryarta na rawa tace "Duk kasan ka gayan waɗannan kalamin amman ka kasa furta kana sona bayan kai ma ka riga da ka kamu da soyayyata kaine kawai baka san na gano kaba" ya saki tattausan murmushi "Fatima faɗin soyayya ga masoyi ƙauyanci ne sedai idan ana so a gani acikin aiki Ki kula min da kanki sosai sannan Kita cin ayaba sabida wannan Tsutsar ta Mutu" murmushi tayi mai sauti "Yawwa to yi dariya naji se muyi sallama babu wani abin da zaki bani wanda ze kwantar Min da hankalina?" ya faɗi maganar a hankali dariyar ta saki kamar yadda yace sannan tace "Hmm kai da kana tare da Aunty Mami To ai baka da matsalar kome" ya langwaɓar da kai kamar tana ganin shi "Mami fa bata nan tana wajan su Ammi Yanzu dai Kimin koɗan Kiss ne se muyi sallama" Ɓoye fuska tayi tana jin kunyar abin da yace mata "Uhmmm ina jira zan sauka ƙasa na ƙara karɓo tea wannan yayi sanyi baze shawu ba" Tace masa "Kai kullum seka sha shayi niko abin da baita ɓa burgeni ba kenan" yayi murmushi "Mu haka muka taso tun Baba yana da rai kuma ni gaskiya yana ƙara min ƙarfi Da kuzari ajikina In ban sha tea ba har Ciwon kai nake kuma bana son asa mai komai se ƙayan ƙamshi da sugar" Ta jinjina kai "Yanzu dai Ayi min Kiss" ya faɗa yana wani ƙasa da Murya "Nifa ban iya ba" ta faɗa yayi Murmushi "Haka ma zaki cemin Kinfi son na fita Compound na hotel

ɗinnan nai ta kallon ƴammatan larabawa Ko?" da sauri tace "A,a zanyi maka" Ya lumshe idon shi "Uhmm tom kiyi yanzu wani kayane ajikin ki kinsa sleeping dress?" ya faɗa da wata kalar Murya "Ai bani dasu duk nawa suna gida" Ta faɗa itama a hankali "Zan siyo Miki sannan zan siyo kayan jarirai na mami ne amman ke zan bawa ajiya sabida inna Nuna mata zata ɗagawa kanta hankalin Rashin samun ciki" ya faɗa tare da kuma cewa "Se kuma me zan siyo Miki Bamma ki lefe ba amman inna dawo zamu je asiyo su Ki zaɓa duk kalar da kike so a saya" tai Jimm tare da cewa"Dabino wannan Curarren na makka shi zaka siyo Mini Allah yasa in ka siyo kayan jariran ma Kuna dawowa ta sami Wani cikin Kuma Allah yasa wannan karon ya tsaya ta haihu" ta faɗa cikin Rashin damuwa da Mami kishiyar tace waɗannan halaiyar nata yana Burgeshi bata zafafawa akan Mami sabida tasan matar shice Kuma ita taje ta samu agidan saɓanin wasu amaren da suke jin kamar su jefa iyayen gidansu a wuta dan tsananin ƙiyayya amman banda farha ita inda zega Kishinta seya yi zance wata a waje amman indai mami ce tana ƙoƙarin yin kawaici.
"Ke bakki son ki haihu?" tai dariya "In Aunty mami ta haihu kamar ni na haihu ne ai" yayi Murmushi "Ke baki son naki?" tai shuru can Kuma tace "kasan me wallahi ni ban fiye jin zafi ko kishin Aunty mami ba sabida Ai Ita ka fara aura kafin ni" da sauri yace "Kina nufin bakya kishina" tai fari da idonta "Ina yi amman na hankali" ta faɗa tana dariya sannan ta ƙara cewa "Yawwa da dabino ɗin zaka zo min sannan In zaka sai Min kayan baccin wallahi kasai manya dan nayi ƙiba sosai yanzu" Ya lumshe ido yana jin daɗin yadda yanzu ta sake tana hirarta cikin walwala "To shikenan Gimbiya Bara naje ƙasa na sha tea ɗin kiyi bacci lafiya" Fatan alkairi sukawa Junansu Farha ta kwanta ba jimawa bacci yayi gaba da ita shiko sauka yayi yaje ya amso tea ya dawo duk yaji baya da damuwa ya tabbata tana masa Musulmin so wanda yake jin Zata iya zama dashi a ko wani hali Jiyay ta ƙara shiga zuciyar shi Yana kammala shan tea ɗin yaja Pillow yayi kwanciyar shi.

Cikin shigar baƙar jallabiya take se ƙaton Glass data rufe fuska dashi ta shiga cikin wani super market zatai siyayya su Koma masaukin su dan su Sajeeda suna mota suna jiranta Da sauri taga wani turare mai kyau ta ƙarasa zata ɗauka seya faɗo shima adaidai Lokacin ya Sunkuya danya ɗauko mata turaren cikin rashin sa'a hannunsu ya haɗe dana junan su Ta ɗago ido ta kalle shi shima nasa idanun ya zuba mata yana kallonta kafin ya saki murmushi.
"Aminci da kusancin Allah su tabbata a gareki ya fara ma'abociyar ƙamshi"
Safna taji wata irin Faɗuwar gaba ta ziyarceta tinda take a rayuwa bata taɓa yin saurayi ba ko fita sukai ba'a cewa ana son su yauce rana ta farko da ɗa namiji ya furta mata magana wadda tai kama data soyayya ta saki fuska tare da cewa "Tare dakai" ya ɗauki turaren ya miƙa mata yana cewa "Naga kamar Siyayya kika zoyi muje nai Miki rakiya ki zagaya" tai murmushi "Nama gama ai tafiya zanyi" Ya zira hannunshi cikin Aljihun wandon shi baƙi ne siriri mai kyau dashi "Okay muje muji bill ɗin naki" batai mai musu ba suka ƙarasa shiya biya kuɗin siyayyar aka zuba mata a leda ya riƙo ledar suka fito yaɗan dakata a bakin super market ɗin yana facing ɗinta "Ni sunana Kamal Ni ɗan najeriya ne nazo yin umara nida sister ɗina nazo siyayya ne sena ganki amman ke ƴar wace ƙasa ce?" safna tai ƙasa da kanta tare da cewa "Nageria Kano state muma umara ɗin muka zo" yayi murmushi "Lahh ƴar garin mu ce okay in ba damuwa ki bani Phone Number ɗinki zan maki magana" safna ta karanto masa Number ɗinta Sukai

sallama Kamal ya juya safna itama ta nufi Motar su.

Da Far'a Ammi ta dube ta.
"Auta muna ta jira kin san Ina da matsalar ƙafa kikai zaman ki" Safna ta tura bakin ta gaba tare da cewa.
"Wanine fa ya tsayar dani wai yana sona shine muka ɗan tsaya dashi muna magana"
Da wata irin Murna Ammi tace mata.
"Haba auta tsakanin ki da Allah? kai Alhamdulillahi Addu'ar dana ke bata faɗi a banza ba Allah nagode maka Allah nagode maka sauran sajeeda dan Allah ya sani wannan zama naku haka babu aure yana tsanani sakani acikin damuwa to yaya kuka yi dashi? Allah yasa nagari ne Allah yasa dashi za'ayi Amin"
Ammi ta faɗa cikin maɗaukakin farin ciki wanda ya kasa ɓuya a fuskarta.
Safna tace mata yace Min.........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 88*

"Ɗan kano ne shi sun zo umara ne shima da sisters ɗinshi yazo yin siyayya ne shima Ya ganni" Safna ta mayar wa da Ammi kamar yadda Ya gaya mata Bakin Ammi ya kasa rufuwa Haka sajeeda itama se farin ciki take dan abun yana damun su sosai ƴammata kamar su ba muni ba, ba talauci ba amman ace Ko na ɗan na rage dare basu da shi.

Har suka koma masaukin su Hirar Abu guda suke yi bayan sunyi shirin Bacci da ike suma Shirin Komawa gida nageria suke tayi Ammi ta dubi Safna"Ki ɗan taɓo yaron nan mana muji ke waya gaya miki haka akewa mazan yanzu in babu kula ai basa zama" daga sajeeda har safna dariya suke Ita ko mami da yake ba da ita aka fita ba tuni ma tayi baccinta dan tunda tazo bata da Lokacin Kowa Kullum addu'arta Allah ya bata ingantaccen rabo mai albarka, sakina kuwa masaukinta daban ita da yaranta Sadiƙ ma ba waje ɗaya suke ba, Safna ta fito da wayarta ta kunna data Tana hawa yana mata sallama da sauri ta shiga mai da masa da replay amai makon ya dawo mata da amsa se ya kira ta voice call, Ta miƙe daga wajan su Ammi ta shiga wani ɗan corridor ta tsaya amaimakon tai masa sallama se cewa tayi.
"Ina jinka"
Kamal ya kama haɓa cikin ɗaurewar kai yace mata.
"Ƙanwata kamata yayi ki fara min sallama tare da cewa yaya naje masaukina amman kince kina ji kamar wadda nai wa dole"
Sam ita safna bata san ba daidai tayi ba seda ya gaya mata sannan ta kama haɓa cike da jin kunya tace.
"Au na manta amman kai haƙuri"
Bai ce komai a wannan gaɓar ba se Magana ta gaba data biyo baya

"Na ganki kuma kin min a matsayin matata kuma ni da gaske ina son ki da aure ni ɗan kano ne, Mazaunin hotoro nine babba agidanmu ban taɓa aure ba ina aiki a Asibitin Malam Aminu kano

Ƙanne na biyu mata se mahaifiyata dafatan kin gamsu dani nai miki bayanin kaina a taƙaice kafin In mun koma nazo har gida"
Safna ta washe baki cikin farin ciki tace.
"Tom shikenan Allah yasa zamu ga lokacin zuwan naka"
Yace.
"Ke ba zaki gayan Taƙaitaccen tarihin kiba?"
Tace.
"Sedai kazo In sha Allah!"
Bai jada tsayi ba yayi mata sallama cikin farin ciki ta koma take sanarwa da Ammi har abin da ya mata gyara akai.
"Kullum dama ina gaya muku ku dinga iya kalami Mazannan da kuke gani se ana lallaɓasu Sabida haka ki dinga saita harshe in zaki magana Bari Mu koma in Allah ya kawo shima mu ashirye Muke"
Har Sukai bacci maganganun suke yi na Saurayin safna ɗin da suka haɗu dashi a saudi'a.

Gabaki ɗaya al'ummar musulmi yaro da babba kowa murnar tawowar sallah ƙarama yake sabida sallah ce wadda ake sada zumunci ake ɗinka sabbin kaya a saka aje hawan idi a dawo a cigaba da zaga gari.

Yau sauran kwana ɗaya sallah har Lokacin Aliyu bai dawo ba kamar yadda farha take Lissafi tuni ta saki ranta domin ta ɗauka baze dawo bama ko se bayan sallah tun safe suka fita wajan gyaran gashi ita da Salma anan akai musu har Kitso sannan aka zana musu baƙin lalle da Farha tana mitar ita baze mata kyau ba amman Cikin Ikon Allah ana mata seya fito a saman fatarta yayi mata kyau gwanin sha'awa Daga wajan Saloon ɗin kuma wajan karɓar Ɗinki suka tafi Farha tana mota salma ta shiga ta amso se suka wuce wajan saida takalma da jaka A tare suka fita salma tace ta zaɓi wanda yayi mata baƙi ta ɗauka tace bata son jaka dan bata dame taba suka je wajan mayafai nan ma ta zaɓa tare da sarƙa da ɗan kunne da turare salma ta biya kuɗin suka wuce Gida a falo suka tarar da mai aikin salma tana ta gyara farar shinkafar wainar da za'ai gobe ga kaji da kayan miya nan Mijin salma ya kawo Ita dai farha kayan Sallar ta buɗe zaro idanu tayi sabida ganin haɗaɗɗan Jan lace da yasha buba mai azababban kyau se material da shadda wadda aka mata aiki dan murna Farha kasa magana tayi data gwada ɗinkin kamar an auna yayi mata cif sedai Ko wanne daga sama ya kamata ta rasa wannan cika da Ƙirjinta yayi har ƙasa ta zube tana cewa.
"Aunty salama nagode da Hidima Allah ya saka miki da alkairi ya raya zuri'a" salma ta kama baki cikin mamaki.
"Kai bari kada ki kuma min Godiya ai ya zama dole"
Farha kwashe kayan tayi duka takai ɗaki sannan tayi alwala tayi sallar la'asar ta fito waje domin kamawa mai aikin salma aikin Sallar da take yi ita kuma salma ta fito Cikin shiri tace zata je Gidan Ammi ta dawo yanzu suka sauka Jin haka yasa Jikin farha yayi sanyi haka dai suka yiwa Salma adawo lafiya ta fita aikin ya kaisu har dare dan har su ƙwaɓin cincin sukai wajan taran dare salma ta dawo Lokacin farha ta bar mai aikin ta ita kuma ta koma ɗaki wanka tayi ta gasa Jikinta dan ta gaji sosai bata kuma fitowa ba bacci yayi gaba da ita.

Su Ammi ne suka sauka da wajan magariba shiko se wajan Goman dare Jirginsu ya sauka Musa yaje ya ɗauko shi Mami kamar gawa ya tarar se bacci take shima dai wanka kaɗai yayi yasha tea ko wajan Ammi bai iya zuwa ba se Bacci washe gari ta kama sallah Gidan Ammi gaba ɗaya ya cika da Hidima sabida su Hajja tun ana jibi sallah suka dawo kuma da yake komai an tsara kafin su ammi subar ƙasar shiyasa gidan ya cika da Hidimar ɗora sauke.
Wajan ƙarfe takwas Aliyu ya fito cikin Babbar rigar shadda fara takalmi da Hula baƙaƙe yayi masifar kyau da dardumar shi a kafaɗa ya ƙaraso falo mami taci gayu cikin shadda turare ta fesa masa ta ɗauko waya tana masa Hoto shi dariya ma ta bashi yadda duk yaga ta ruɗe da shigar tashi Mayafi ta yafa suka jera zuwa sashin Ammi wanda ya cika da ƴan uwan Ammi waɗanda dama duk sallah haka gidan yake cika Suka gaggaisa da juna Lokacin sadiƙ shima ya shigo sabida haka tare suka Miƙe da Aliyu domin tafiya masallaci.
"Ba zaku ci ko waina bane tunda masallacin da kuke sallah se tara suke tayarwa" cewar Ammi Aliyu murmushi yayi tare da cewa "Haba Ammi ai mukai zaman cin waina makara zamuyi Dan Allah yaya sadiƙ kazo Mu wuce" sadiƙ da yake ta tsokanar Safna wadda taci kwalliya wai saurayin da suka haɗu dashi a saudia ne zezo Shine yabi bayan Aliyu wanda tuni ya ɓace daga falon

Musa ne yaja su zuwa babban masallacin Gidan sarki anan sukai sallah Shidai Sadiƙ gida yayo sabida Yadda mutane suka yaɓe Aliyu tun bayan idar da sallar wanda har seda yaje suka gaisa da mai girma gwamna sannan ya samu ya fito daga cikin Taron mutanan da ƙyar matasa se kirari suke masa Da ƙyar ya shiga Mota kansa har ciwo yake masa dan yawan matasan har yayi yawa Har Motar shi tabar wajan Mutane basu dena bin bayanta ba.
"Musa kaini Gidan su fatima na gaishe da mahaifanta kafin mu wuce"
Musa yaɗan juyo tare da cewa.
"Ranka ya daɗe ka manta yau sallah kowa yana gida idan har kaje Gidansu tofa za'a san kaine gwara ma kai shigar dare amman innai ba daidai ba a yafe ni"
Aliyu ya lumshe ido.
"Haka ne kuma musa to kaini sharaɗa Gidan Salama kokuma kaga kawai Ka bani key ɗin motar zanje da kaina kaikuma zan sauke ka a ƙofar Gidana se ka ɗauki mota ka wuce harkokin ka" Musa yace.
"Mai gida duk yadda kace daidai ne"
Musa ya nufi Gidan Aliyu a bakin gate Aliyu ya sauke Musa shikuma yaja motar zuwa gidan salama dan ya matsu yaga ƴar budurwar sa.

"Tsarki ya tabbata ga Ubangijin halitta sarkin daya shinfiɗa sammai Guda bakwai ya shinfiɗa ƙassai Guda bakwai gaskiya yau inda ɗan uwana ze ganki Aunty fatima daya susuce"
Salma ta faɗa lokacin data ga farha ta fito daga ɗaki sanye take Cikin Lace ɗin da suka amso jiya daga Ɗinki, Yayi mata shegen kyau Sabida fuskarta tai fiyau Dalilin sabon Kitson da akai mata ga Fulawar Datai mata kyau a hannunta ga sarƙa da ƴan kunne wanda suka cika mata ƙirji da kunnenta.
Mayafin ta a kafaɗa ta saki Murmushi tana ɓoye fuskarta ta zauna a saman kujera dan salma ta hanata zaman ƙasa Waya salma ta ɗauka ta dinga zubawa farha Hotuna tana faman zuzuta kyan datai Farha Tashi tayi taje Kitchen ta zubo waina ta dawo ta zauna tana ci Dady yace zeci

shima tace yazo suci tare.

Suna cikin cin wainar ne Yayi sallama falon ƙamshin turaren shine ya sanar mata daya ƙaraso tsakiyar falon ƙasa tayi da kanta batare data cigaba da cin wainar ba.
"Oyoyo Uncle" yaran salma suka ɗane shi salma cikin murna tace.
"Sannu da zuwa yaya jiya har na baro gida baka sauka ba har ya sadiƙ na cewa ko se yau"
Zama yayi a kujerar dake kallon farha yana ƙoƙarin ɗora idanunshi akan fuskarta sedai taƙi yarda.
"Se wajan 10 na sauka ay Salama yaya gida ya hidima nafa gode"
Miƙewa salma tayi tashi ga kitchen ganin haka yasa farha taɗan kalle shi akai sa'a shima itan yake kallo.
"Sannu da zuwa anyi sallah lafiya"
Murmushi yayi batare daya amsa ba.
"Kinyi kyau So ma sha Allah"
Ya faɗa yana lumshe ido tashi tayi daga wajan ta nufi ɗaki ya bita da kallo lallai da gaske tayi ƙiba.
Kayan abinci ne salma ta shiga jera masa ɗaga mata hannu yayi.
"Salama so kike nai abin Kunya cin abincin gidan suruki a,a turo min fatima da kayanta ina Mota sauran maganar se Munyi waya naji dukkan abin arziƙin da kikai mata Na kuma gode Allah yabar zumunci"
Kuɗi ne ƴan naira 500 sabbi ya dire mata yace ta saiwa su Dady Sweet salma sakin baki tayi Lokacin shi har yakai Ƙofar falon Ma.
"Yaya to na zuba maka a basket ka tafi dashi amman in baka ci ba ai bazan ji daɗi ba"
Bai ma jita ba Lokacin har ya ƙarasa wajan motar shi ya buɗe ya shiga salma tashi tayi ta shiga ɗakin farha  a kwance ta tarar da ita

"Mai nake gani Aunty fatima Mijinki yana Falo kinzo kin kwanta to yace ki same sa a mota Ki haɗa kayan ki"
Juya baya farha tayi tana tura baki can kuma tace.
"Ni dai Aunty salama dan Allah yabar ni anan nafi jin daɗin Gidanki acan yayta takura min"
Salma haɓa ta kama.
"A,a ni babu ruwana da Rigimar yaya wallahi baze ce nike zugaki ba In ma zaki dena wannan sakarcin Ki dena dan bake kaɗai bace Kina da abokiyar zama In ma babu yaya ƴammata rububinsa suke Sabida haka ki tashi Kibi Mijinki Kije ki bashi kulawa ki tabbatar duk ishirwar ki da yayi ta tsayin wata Kin gusar masa da ita Dan Allah banda gardama Aunty fatima"
Kalamin Salama sun bawa farha Kunya rufe idanu tayi da hannunta tana dariya tare da cewa.
"Kai Aunty salama wace Kulawa zan bashi Muna ɓoye a ɗar ɗar fa muke"
Salama tai dariya.
"Allah ze kawo muku mafita In sha Allah ki tashi yaya baya son jira"
Farha ta miƙe da taimakon Salama ta haɗe kayanta Ta rungume su Dady se hawaye! Ta ƙara zuwa wajan salma ta rungumeta salma ta shiga bugun bayanta.
"Kiyi haƙuri haka sabo yake Allah ya kaiki lafiya"
Cikin Kuka farha tace.

"Bazan manta dake ba Aunty salama Allah yayi miki abin da kikai min Allah ya raya miki ƴaƴanki nagode nagode" kuka ne yaci ƙarfinta itama salama dauriyar take sabida sun shaƙu a ɗan zaman da sukai Yaran salama Kuka suka sa sanda Farha ta ɗauki trolly ɗin kayanta Ledar turaruka salma ta bata har bakin motar suka rakata yana zaune yana jiranta Farha ta sunkuya ta ɗauki Almustapha wanda ya riƙe mata mayafi Kuka take sosai Shikam Aliyu zuba musu ido yayi yana kallon ikon Allah wato haka sukai Muguwar shaƙuwa da yaran Salma ta Riƙo Almustapha taja dady suka koma ciki Ita kuma Farha Tsayawa tayi bata shiga Motar ba se Kuka take.

Ziro kanshi yayi waje ya kalleta.
"Ki shigo mu tafi ki saka kayan ki a back seat"............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 89*

Sautin muryar shi ta fita a hankali bata ko kalli inda yake ba still kukan nata ta cigaba dayi yaɗan tsira mata idanu na wasu Lokuta kafin ya kawar da kanshi bai ko sake kallon inda take ba da alama yau shima ƴan Miskilancin nasa suna kusa Ƙafafunta ne suka fara rawa sabida gajiyar tsaiwa kuma bai sake cewa ta shigo ba sema zuge glass ɗin sa da yayi yana danne danne a wayar shi A hankali taje ta buɗe bayan motar ta saka kayan nata sannan ta zagaya inda ya buɗe mata ta shiga ta zauna Ƙamshin Turaren shi na _Labbra_ ya doki hancin ta Mayar da murfin motar tayi ta rufe har Lokacin be mata magana ba ya tayar da motar yayi revers ya fita daga harabar Gidan Salma Jifa jifa take jin yana magana a wayar shi wanda yawanci Mutanan shi ke kiran shi don yi masa barka da sallah amaimakon taga sun ɗauki Hanyar Gidan Ammi seta ga ya karya kwana yayi hanyar state road ita dai jingine kanta tayi da seat tana gyangyaɗi dan yanzu ya zame mata aboki Ko a zaune take gyangyaɗi take yi Har sukai tafiya mai nisa bata Sani ba sabida baccin daya kamata a cikin harabar wani haɗaɗɗan Hotel yayi parking ya saka face mask a fuskar shi sannan ya fita Seda yaje ya kama musu ɗaki na wuni Guda ya biya kuɗin komai sannan Ya dawo Motar ya buɗe ya shiga Dukan seat ɗin da take kwance a hankali ta buɗe jajayen idanunta waɗanda suka cika da bacci.
"Fito"
Ya faɗa batare daya saki fuskar shiba har Lokacin ta fuskanci kamar haushinta yake ji Fitowa tayi tana ƙarewa wurin kallo bata san wajan ba Kuma bata san ina bane tunda ba hanyarta bace yana tafe a gaba tana bin bayan shi Suka shiga ciki Har zuwa Bakin Room ɗin daya kama ya sanya key ya buɗe ita dai Binsa take Ƙaton ɗaki ne wanda Yake ɗauke da gado da madubi se toilet se sopa da ɗan Center table Ƙamshi da sanyi sun cika ɗakin zama tayi abakin gado shi kuma ya fita Minti Kusan goma se gashi ya dawo Hannun shi ɗauke da fararen Ledoji manya ya zube a Ƙasan carpet Ɗin ɗakin babbar Rigar Jikinsa ya shiga cirewa se wayar shi daya aje a kusa da ita.
"Kinyi sallah? ya kamata kije ki alwala ki sallah dan wallahi a matse nake"
Bata gane me yake Nufi ba ta wuce Cikin toilet ta ɗauro alwala ta tayar da sallar akan carpet ɗin ɗakin bayan ta sanya ɗankwalinta dan bata ga darduma ba.

Tana idarwa ta juya ta dube shi yana zaune daga shi se Gajeran wando iya cinya ko singlet babu ajikinshi ya wani baje takeaway ɗin dayayo musu yana ta cin chips da miyar sauce ga lemo nan da ruwa mai sanyi a gefen shi.
"Ke me zaki ci ni ban ko break ba naji yunwa ne" ya faɗa yana kai Loma cikin bakin shi Tashi tayi bayan ta ɗauki Coca cola ta zauna a saman gado tana kallon yadda yake cin abincin da sauri da sauri harya kammala ya tattare Komai ya shiga Toilet ya jima aciki kafin ya fito da ruwa na ɗiga ajikinshi da alamun wanka yayo Daga shi se gajeran wando ya ƙaraso wajan ta Hannu ya miƙa wajan swich ɗin ɗakin Nan da nan hasken ɗakin ya ragu se Duhu wanda se ka rantse dare ne wajan ta ya ƙarasa ya ɗora hannun shi a saman nata yana shafa lallen hannunta.
"I miss you fatimah wannan lallin yayi kyau" ya faɗa yana shafawa tare da ɗora hannunshi a saman kanta "Wow dama kina da gashi haka baki taɓa Yi min Kitso naga ni ba" ya faɗa yana Shafa ƙananun Kitson dake kanta aranta tace ina kurkukun ta ina zanyi Kitso.

"Nayi Missing ɗin ki Kema kinyi Missing ɗina?" ya faɗa Lokacin da yake ɗagata daga zaunan da take ya shiga zuge mata zip Ɗin rigarta adaidai wajan ƙirjinta tasa hannu ta dafe muryar shi very cool yace "Please karki Min haka" ya faɗa yana ƙarasa yin ƙasa da rigar tata Red bra da red ɗin under skirt ɗinta suka bayyana a idanun shi Breast ɗinta daya ƙara cika mata Ƙirjinta ya tsirawa ido dan yafi ƙarfin cikin bra ɗin a hankali ya saki ajiyar zuciya ya Mayar da hankalinsa ƙasan cikinta wanda Yaga yaɗan Tasa kaɗan Ya saki Murmushi yana janyota cikin Kirjinsa danshin Ruwan daya jiƙa mai Kwantaccen gashin ƙirjinshi ne ya haɗe da fatarta ajiyar zuciya ta ja mai ƙarfi a hankali yakai hannun shi bayanta ya shiga Cire mata bra ɗin kafin ya kwantar da ita ruwan cikinsa Tuni lamarin ya sauya Abin da ke wanzuwa a tsakanin su ya wuce tunanin mai tunani ya wuce zaton mai zato sedai a bar musu su da suka kasance acikin wannan yanayi Kowa a wannan gaɓar Koƙarin nunawa ɗan Uwanshi kulawa yake Aliyu gaba ɗaya ya haukace ya susuce ya gigice bai taɓa jin yanayi irin wanda yake ciki ba babu irin sumbatun da bai yi mata ba Tun tana daurewa har seda ta Ƙosa ta soma kuka tana dukan Kirjinshi Muryarta da ƙyar take fita sabida azaba Numfashinta yana fita da ƙyar take ce masa.
"Dan Allah ka rabu dani haka ji nake kamar na mutu Ishirwa nake ji dan Allah kayi haƙuri" ta faɗa tana kuka ƙasa ƙasa hannun shi ya ɗora a gadon bayanta ya shiga shafawa yana mata magana ƙasa ƙasa cikin raɗa.
"Fatima I miss you, I love you, you are my happiness, I can never live without you, you gave me all the happiness in life, I love you, I love you, I love you fatinahhhhh" ya ja maganar yana wani irin ƙara shigewa Jikinta kamar ze ɓalla mata ƙirjinta nishin azaba ta ƙara saki.
"Dan Allah to ka barni haka na huta dan Allah kaji na gaji wallahi"
Ta faɗa tana wawuro gwauron Numfashi domin duk yadda kalaman shi ke tashi bata jiba sabida takanta take yi don abin tun yana saka ta a nishaɗi har tazo ta gaji lallai Shiɗin gwarzon namiji ne Dole se mace ta shirya zata tunkare shi.
Sake liƙewa yayi ajikinta hannu yasa ya tallafo fuskarta yana hura mata Iskar cikin bakinsa Tare da Ɗora harshensa akan Kunnenta yana tsotsa yana hura mata iska cikin Kunne wata irin Nutsuwa ta samu ta tallafe shi tana Kara tura fuskarta cikin kirjinsa A hankali ya dawo da bakin sa cikin bakinta ya jima yana Kissing lips ɗinta kafin ya saki ya gangara gefe yana sakin Numfashi a tare suka tsarkake Jikinsu A gurguje yayi alwala sabida lokacin sallar la'asar ya

wuce anan cikin ɗakin yayi sallah bayan ya Suturta Jikinsa ita ko tana zaune Ko rigarta ma ta kasa mayarwa saboda yadda gaba ɗaya Jikinta ke mata ciwo Ya jima yana addu'a kafin ya shafa ya juyo yana kallonta.
"Raguwa"
Ya faɗa yana mata Tsadaddan Murmushinsa mai narkar mata da zuciyarta.
Turo mai bakinta tayi gaba sega hawaye nan yana Zubowa daga idanunta"
"Subuhanallahi Mai kuma nayi Miki?" ya faɗa yana ƙarasawa inda take ya zauna kusa da ita ya zube hannayen shi a saman nata hannun yana murzawa.
Ya ɗauki rigar ya maida mata jikinta

"Ki sallah karki Makara"
Ya ɗagata ta saka mayafi ta tayar da sallah tana nan zaune bayan ta idar ya dawo Kusa da ita ya zauna har kafaɗun su na Gugan na juna.
"Ki cire mayafin mana ki sha iska"
Ya faɗa yana zare mata mayafin Jikinta hannunshi ya zira ta cikin Rigarta ya ɗora a saman cibiyarta yana shafawa Lumshe idanu tayi ta ɗora kanta a kafaɗar shi

"Akwai zafi?" ya tambayeta ta girgiza kai alamun babu

"To yana yin motsi har yanzu ko ya dena?"
Ta girgiza kanta "Baya yi yanzu ni yunwa nake ji" Da sauri kuma cikin kulawa yace mata "Me zaki ci?" tai Shuru can kuma tace "Sakwara da miyar agushi" Ya tashi ya fita sabida bai yarda wani ya shigo kawo Musu komai ba yafi gane shida kanshi ya fita ya amso ko ma meye Minti Wajan Goma ya dawo da tray da bowl ƙananu a saman shi gabanta ya ƙaraso ya aje sannan ya Koma ya rufo Musu ƙofar ƙamshin Miyar ya doki hancinta ta lumshe ido ta haɗiyi yawu ta saka hannu ta Gutsiro sakwaran bayan ta fitar dashi daga cikin Ledar ta soma ci Shiko saman sopa ya koma ya kwanta baccine ya ɗauke shi harta gama ci Ta kwashe komai ta haɗe waje ɗaya yana baccin bata tashe shiba se ma Gefen shi data je ta ɗora kanta a cinyar shi ta zauna a ƙasa Nan da nan baccin itama ya ɗauketa Basu Ne suka farka ba se Magariba Sosai yayi mamakin baccin daya yi Shine ya soma tashi ganinta agaban shi kanta a saman cinyar shi yaɗan saki Murmushi ya shiga tashin ta a hankali ta buɗe ido ya sakar mata Murmushi "Munyi bacci har magarib tayi" ya faɗa yana tashi yayo alwala itama ta shiga tayo alwala shine yaja su sallar a wannan karon Bayan sun idar azkar ta shiga karantawa Har akai sallar Isha'i suna wajan haka ya kuma jansu sallar Isha'i Bayan sun idar Ya fita ya kuma shigowa da Baƙin tea cup Biyu ya miƙa mata ya ɗaga cup ɗinsa yana sha Ita kam bata sha ba sauran sakwarar taci tasha ruwa Bayan ya gama shan tea ɗin ya kalleta.
"Zamu wuce Gida yanzu ai kin Huta haka ko?" haɗe rai tayi ta soma kwaɓe Fuska zata mai kuka.
Zama yayi tare da kama hannunta.
"Nasan bakya son zuwa gidan Ammi amman ina baki haƙuri, akan hakan Ki ɗauka taki ƙaddarar auren ce tazo a haka amman a hankali Kome zai sauya Kinji"
Ya faɗa cikin yin ƙasa da murya.
"Yau she zamu sami ƴanci bayan kullum muna ɓoye ka riga ka ɓoyewa duk wani makusancin

ka cewa ni matar kace"
Ta faɗa tana hawaye! ya sa tafin hannun shi yana share mata hawayen

"Ƙannen mahaifina ne suka je wajan Magabatan ki suka karɓa min auren Ki Ko suma Ba su na aiko ba wasu daban na aika?"
Ya faɗa yana sauya yanayin sa.
"Ai baka nuna wa Ammi ni matarka bace ita ma Aunty mami baka nuna mata ba dan kana tsoro"
Murmushin takaici yayi.

"Kina da alaƙa dasu ne? wa kika sani acikin su bani kika sani ba haba Kin ɗaga min hankali da waɗannan zantukan nace Ki kwantar da hankalin ki Kin ƙi sannan inda ina Jin tsoro ke Kin san da bazan taɓa kwana a ɗakin kiba Kuma kina part Ɗin Ammi Ke da kin kalle ni Kin san banyi kala da sakaran namiji ba sedai Tsananin Biyayyar mahaifiyata wadda nake son na rabu da ita lafiya shine silar Komai na rufewar auren mu"
Ya faɗa yana tashi tare da ɗaukar babbar Rigar shi wadda bai ɗorata akan kayan ba Ya saka hula ya ɗauki Wayar shi da key Ɗin mota.
"Taso muje Lokaci yana Ƙure wa"

Ta miƙe Bayan ta yafa mayafin ta.
"Idan kuma zuri'a ta shiga tsakani na dakai fa Shin ta yaya zaka bayyana cewa naka ne bayan baka bayyana ni matarka bace?"
Ya ɗan sosa gemun shi.
"Kina son shiga hurumin da ba naki ba duk waɗannan tambayoyin ba Hurumin ki bane Nidai nine mai Igiyoyin auren ki Ko to please in ba Kina son Na ɓata Miki rai ba Ki rabu dani da waɗannan zantu kan ki bari har Ki sami cikin haihuwar tukunna seki zo min da waɗannan maganganun"
Ta Tura baki cikin son ta bashi haushi.
"Ai wallahi dana sami cikin ma Seya sheƙa rariya dan bazan haifi ƙannen marayu waɗanda basu da tartibin uba ba"
Ya saki Murmushi wanda ta kasa fassara ko na meye

"Lallai daga ranar da Kika sami ciki kika zubar da kin tabbata faɗa da Aljani babu daɗi dan sena baki matiƙar mamaki marar hankali Burin ki koda yaushe ki ɓata Min raina ko hakan nada kyau"
Ya na faɗa mata yabar ɗakin da sauri tabi bayan shi sauri yake kamar ze tashi sama Se Duk Jikinta yayi sanyi ta shiga yin nadamar abubuwan data masa bayan ya gama bata Jin daɗi a ɗazun.

Har suka shiga Mota yaƙi kallonta se yay Kicin kicin da Fuska yana driving yana ɗaga waya har suka ƙarasa Gida yana parking ya ɓalle Murfin Motar ya fice ya barta aciki.

Hankalinta duk a tashe yake da yadda taga ya koma mata Ita bada wata manufa ta faɗi dukkan maganganun ɗazu ba ta faɗa ne dan ya Bayyana ta a wajan mahaifiyar shi amman in ka cire

wannan manufar bata da wata manufa ta da ban akan hakan amman gashi yaji haushin ta sosai.............

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 90*

Gajiya tayi da zaman cikin motar ta buɗe ta fita harabar Gidan babu kowa se hasken daya cika wajan tare da tarin Shuke shuke ko ina tsit Bayan motar ta zagaya ta ɗauko kayan ta da ƙyar take jan Trolly ɗin tata tana tafe tana Nishi sabida akwai nauyi Ko alamun sa bata gani ba har ta ƙarasa sashin Ammi adaidai Bakin Ƙofar gaban ta ya faɗi tayi Bisimillah tare da shiga cikin babban falon Duk iyalan Gidan suna zaune Shi kaɗai ne Da Salma babu a wajan amman akwai Ammi akwai sadiƙ akwai sakina akwai Bashir akwai Su safna se Ammi Se wannan ƙanwar sakinar data kuma dawowa se ƴaƴan sadiƙ kayan abinci ne kaca kaca a falon ko ina kwanukan abinci da robobin lemo dana ruwa Daga nesa dasu ta tsugunna bayan tayi sallama Wanda Sadiƙ kaɗai da Ammi ne suka Amsa mata sallamar amman sauran babu wanda ya dube ta..

Seda ta danne wani malolon abu daya zo mata wuya ya tokare ta sannan tace

"Ammi na same ku lafiya yaya Ibada dafatan Kunyi sallah lafiya?"
Ammi bata amsa mata ba se cewa tayi.
"Fati Yaya baki dawo ba ke se yau? ko da yake dama Mun yi magana da Baba a gaskiya Ni yanzu bana buƙatar Ƙananun ma'aikata irin ki shine ya nace har ya nemi alfarma zaki zauna har bayan sallah Tunda sallah tayi anyi an ƙare shikenan zan sallame Ki seki Koma gida"
Hawaye ne me ɗumi yazubo wa farha batare data san ya zubo mata ba Ga abin da take nuna mai amman sam yaƙi fahimta.
Murya a shaƙe tace.
"To Ammi Ko yan zu ma zan iya komawa tunda dare be yiba"

Sakina ce tai zaraf tace.

"Kaji ƴar rainin hankali da baƙar magana irin ta mutanan ƙauye yanzu Ammi ɗin kike gayawa magana haka?"
Safna ce tace

"Ai da yake ba uwarta bace......
Adaidai Lokacin Aliyu ya shigo falon sanye yake da jallabiya ash colour mai Dogon hannu ƙamshin turaren shine ya soma sanar da zuwan shi Kafin ya bayyana bai ko kalli sai tin da farha ke tsugunne ba Kona ce da ƙyar ma idan ya kula da ita ya ƙarasa wajan Ammi ya zauna yana fito da wayar shi Musa ne Ke kiran shi akan Ko zasu je Gidan su Farha kamar yadda yace ɗazu sukai magana da Musa se Da ya gama wayar sannan ya shiga gaishe da Ammi a nutse suka gaisa da Sadiƙ Sakina da jamila dasu Bashir Suka gaishe dashi.

"Wai Baba yau ina ka shiga sallah Guda kowa se tambayar ka yake Kuma kamar haɗin baki mami ma yau ko leƙo mana batai ba"
Ya ɗan shafi kanshi se Lokacin ya kula da ita ya basar kamar bai ganta ba dan har Lokacin Haushin ta yake Ji dan tayi masifar ɓata mai rai Seda yayi Controlling kanshi ma ya iya zuwa sashin Ammi.

"Ammi na shiga meeting ne mai muhimmanci se yanzu na sami kaina"
Ammi tace "Allah ya temaka" cikin kulawa kafin ta mayar da hankalin ta wajan farha wadda take raɓe a tsugunne se ruwan hawaye ke faman Biyo Kuncin ta.

"Tashi kije ɗaki Ki aje kayan ki seki Fito ki tattare mana falon nan kinga yadda ya koma"
Farha batai Ko Motsi ba dan ji take Zuciyarta kamar Dutse.
"Ba magana nake Miki ba kika sakani gaba" Ammi ta faɗa a hasale

"A,a ni zan koma kawai kamar yadda kika buƙata Inna ɓata Muku rai a iya zamana daku Ku yafe Mini"
Daga haka ta Miƙe Bashir da sauri yayi gabanta ya riƙe Trolly ɗin kamar ze Kuka ya dubi Ammi.
"Haba Ammi Haba Ammi abin da kike sam babu kyau Ammi meye ribar wulaƙanta ɗan adam wanda baka san baiwar da Allah yayi masa ba"
Kafin ya dubi farha a hargitse yace.
"Babu inda zaki je a wannan tsohon dare Koda zaki tafi wallahi se an baki haƙƙin gaɓarki kuma gari ya waye sannan ki tafi"
Aliyu cikin rashin fahimtar abun da ya faru yake Bin kowa na falon da kallo kafin ya dire akan Farha data ɗora hannu a fuska tana Gursheƙen Kuka.
"Bashir ni kake gayawa haka akan wata Ƴar ƙauye yayi maka kyau nike da damar ɗaukar masu aiki a gidannan to nace Na gaji da ita dama alfarmar Baba taci Idan gidan kane seka barta bama a darannan ba a yanzu zata bar Mini Gidana ni wannan masifa ta ishe ni"

Sadiƙ ne ya shiga bawa Ammi haƙuri wadda take masifa kamar ana tinzirata ga bashir ya Tsaya akan Farha ba zata bar Gidan da wannan daran ba Su Safna dariya suke sakina kuma se faman zuga Ammi take Aliyu yaji ranshi ya ɓaci da wannan Cin zarafi da mahaifiyar shi take Ƙoƙarin Yiwa matar shi jiyay gwara ya tauna tsakuwa a wannan karon Ko aya zata ji tsoro. Tashin dayay domin ya Nufi wajan Farha Jiri ya ɗebe shi babu zato suka ji ƙarar faɗuwar shi Aliyu ya faɗi baya Numfashi kwata kwata kanshi ya bugu a tiles ƙafar shi ta daki Katakon Jikin Kujera wanda yatsan ƙafar ya ce ƙass wanda ya bada tabbacin Ya sami tsagewar ƙashi a yatsan nashi ga gefen kanshi da ke zubar da Jini sakamakon faɗuwar da yayi daga Ammi har Su Sadiƙ ƴar Rige rigen zuwa gabanshi Suke yi Ammi kuka kawai take se ta fita a guje tai Compound tana kiran driver agigice suka shigo ammi na cewa

"Sadik ku saka min shi a mota in Baba ya mutu nima bin bayan shi zanyi na shiga Uku Baba Me ya same ka Innalillahi wa'innah ilaihirra'jun Allah ka farkar dani daga wannan Mummunan mafarki dana keyi"
Da sadiƙ da Bashir da ƙyar suka ɗaga Aliyu zuwa mota Su Safna kuka kawai suke yi ammi

kuwa dan Kuka Ko Muryarta bata fita ko mayafi seda aka miƙa mata sannan ta shiga motar da ita dasu sadiƙ suka tafi asibiti.

Farha juwa ce take ɗibarta a hankali take dafe bango tana silalewa ƙasa zama tayi daɓas a ƙasan tiles tana sakin ajiyar zuciya ta saka hannu, ta Shafo hawayen dake Biyo Fuskarta Hankalin ta ya tashi ta kasa Nutsuwa ta kasa tunanin komai akan hakan Lallai akwai matsala kalmar Innalillahi data ke ta faɗa ita ta zama makamin bata Nutsuwa ta ɗaga kai ta hango su Safna nata Kuka in ba idanunta Gizo yayi mata ba tabbas matar sadiƙ ba kuka take ba dariya take tana Wa ƴaƴanta wasa sedai daga taga su Safna sun ɗago zata fara share hawayen ƙarya ƙanwarta bata wajan bare taga a wani hali take itan

Bata da Lokacin Tunanin dalilin dariyar sakina sabida haka tashi tayi a hankali ta nufi ɗakin da aka ware ya zama nata ada ta ƙudiri ba zata kuma kwanan Gidan ba amman yadda taga halin daya shiga yasa dole zata zauna domin kota tafi ma bata da sauran Nutsuwa wato kuka ma se da dama ake yin sa hawayen ta ya ƙafe kawai hango yadda ya faɗi take tana kuma hango yadda aka fitar dashi kamar gawa take Cikinta ya murɗa ta dafe Gefen mararta wanda ke faman juyawa kwanciya tayi a ƙasa bata damu da tarin ƙurar dake ɗakin ba Nishi take tana kiran sunan Allah har Gumi ya soma wanke ta marar ta lafa mata da ciwon Jitai kamar Ihu da kururuwa Hankalin tane ya kuma tashi bayan data tabbata daga falo take Jiyo Ihun! wanda tunaninta ya bata ya rasu Shikenan ta ɗora hannu aka ta fasa Ihu mai ƙarfi tunanin yanayin su na ɗazu yana mata yawo a idanunta da rarrafe ta fita falon Sedai babu su Ammi Mami ce take kukan daya sa taji kamar Ihu take Su safna na taya mami kukan sakina ce ta fito tana musu magana.
"Haba duk kun cika mana gida da Ihu se kace wanda aka ce ya rasu haba da Allah se kace ba Musulmi ba kema mami da Girmanki kinzo kin biyewa ƙananun yara"
Mami ta ɗago ido tana hararar sakina.
"Dole muyi kuka ai kuka muya kama da ma bama su Burin ya mutu suci dukiya ba sakina bari Kiji duk wani iskanci naki a tafin hannuna yake da duk wata gadar zare da kike haɗawa"
Mami ta faɗa tana kallon sakina wata ƴar iskar dariya sakina ta saki tare da cewa.
"Ai duk kanwar jace Ni ma kallon ku nake an gaya miki ana shiga dawa dan ƙarya ne to bari Kiji kifi na ganin ka mai jar koma gwara ma kowa yay takan shi tun kafin ai mutuwar kasko haihuwar guzuma ƴa kwance uwa kwance"

Daga farha har su safna hankalin su bai kai kansu mami ba har sukai suka gama ita mami manufar maganarta akan sakina shine Tana sane da yadda take cusa mai ƙanwarta ya aura sannan kuma taga yadda kowa yake kuka amman sakina batai ba shine dalilin daya sa ta faɗawa sakina haka wanda ita kuma sakina Jikinta seyay sanyi ta ɗauka ko mami tasan shirin tane Shiyasa itama ta yanko tata baƙar maganar ta yaɓa wanda tasan dai Aliyu baya son mami ammi ta haɗa auren amman bata san komai ba bayan haka Dukkan su Jikinsu yayi sanyi kuma sun shiga ɗarɗar kamar wani yasan sirrin wani mami Kukan dai ta Cigaba dayi ganin dare nayi yasa farha ta ƙarasa wajanta tana rarrashinta Mami tace wa farha tazo suje part Ɗinta su kwanta haka tabi mami Ranar farha dai batai bacci ba daga ƙarshe alwala ta ɗauro tazo tana ta sallah duk hankalinta yaƙi kwanciya tai kuka ta gode Allah kanta har ciwo yake mata ga ciwon

mararta wadda ta ɗaure tai gam.

Duk yadda likitoci suka so dawo da Numfashin sa abin yaci tura A taƙaice har ya shafe awanni Biyu yana a tsakanin halin rayuwa da Mutuwa ne Likitan ya fito yana yarfe zufa sadiƙ ya Miƙe da gudu bawan Allah ko takalmi babu a ƙafar shi ya tari Hanyar da Likitan ze wuce.
"Doctor yaya mai jikin da Muka kawo?"
Likitan yaɗan dubi sadiƙ tare da cewa.
"Sorry ka kwantar da hankalin ka"
Bashir ya taso ido jajir yana cewa.
"Kaga malam in kun kasa zamu ɗauke shi a yanzu zamu yanki ticket ɗin ƙasar waje wannan wani irin iskanci ne asibitin kuɗi mai tsada kamar wannan amman Ku kasa aikin ku"
Likitan ya dafa kafaɗun Bashir Lokacin Ammi ta karaso wajan yaɗan kalli sadiƙ yace masa.
"Muje Office"
Bashir yace.
"Wallahi babu inda zaku seka gayan a wani hali ɗan uwana yake ciki idan ya rasu kawai ku gaya mana mu ɗauki gawar shi"
Likitan ya dubi bashir wanda yay kamar baya hayyacin sa.
Kafin yayi magana wata Nurse wadda ya bari a ɗakin ta fito da sauri tana cewa.
"Doctor yana numfashi yanzu"
Da gudu Likitan ya koma dama ya fito ne dan ya ƙaro kayan aiki Taimakon gaggawa suka cigaba da bawa Aliyu har Allah yasa Numfashin sa ya dawo Normal allura sukai masa tare da gyara masa Yatsan sa daya bugu sannan suka manna mai plasta a Kanshi wurin daya fashe Likitan yaja mai ƙofa bayan yace kada wanda yaje Inda yake.

Sadiƙ likitan ya kira Office ai da sauri ammi tabi bayan su.
Likitan ya zauna sadik da ammi suka zauna.
Likitan ya dubi sadiƙ.
"Gaskiya yallaɓai ku kiyayi abin da ze dinga ɓata masa rai dan zuciyar shice ta Buga wanda bada ban Allah ya taimaka ba ze iya rasa ranshi sannan Jininsa ya hau lokaci ɗaya tabbas Allah ne yayi akwai sauran kwanan shi akwai abin da akai agaban sa wanda ya ɗaga mai hankali ya kuma ɓata masa rai se a guda in ba haka ba akwai matsala"

Salati ammi tahau yi tana tunanin me yake damun Baba haka Da har waɗannan lalurori suka far masa lokaci guda.
"Hajiya ai ita ƙaddara ba'a mamaki da faruwarta Amman dai a kula dashi sosai dan Allah in ba so kuke ku rasa shiba" shawarwari likitan ya basu tare da Bawa sadiƙ Bill ɗin su yaje ya biya Ammi cewa tai anan zata kwana Bashir yace a,a shima ya sadiƙ ya koma gida shi seya kwana a wajan Aliyu tunda Likita yace sallama se zuwa gobe da yamma kafinnan ya ƙara warewa. Wajan Sha biyun dare su Ammi da driver suka kamo hanyar gida daga asibitin suka bar Bashir.........

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya

09022260850*

*A LOVE STORY 91*

Lokacin da su Ammi suka shigo gidan tsit yake sabida kowa yayi bacci Ammi ta wuce ɗaki sadiƙ ma ya tafi masaukin sa Gaba ɗaya hankalin Ammi ya gaza kwanciya don ita ma babu mamaki idan aka duba Jinin nata yahau sedai rashin Lafiyar Aliyu Yafi Komai ɗaga mata hankali har Lokacin kuka take idan ya rasu tasan da wuya itama zata ƙara Moruwa Duk ƴaƴanta yafi soyuwa azuciyarta yafi mata biyayya to me yake damun sa haka da wannan matsaloli suka taru sukai masa yawa Haka bata kwanta ba alwala taje ta ɗauro ta dinga Sallar nafila se wajan asubahi bacci yayi awon gaba da ita.

Sadiƙ yana shiga ɗakin daya sauka mamaki ne ya kama shi ganin sakina a zaune cikin shirin kayan bacci tana ganin shi ta saki Murmushi ta miƙe ta shiga banɗaki ta haɗa masa ruwan Ɗumi tazo gabanshi ta shiga cire masa kayan jikin shi bai musa mata ba sabida yadda ya gaji Shima hutu yake buƙata da taimakon ta ya samu yayi wanka ya fito ta kawo mai kayan bacci Catton na maza ya saka yana umartarta akan ta kawo masa ruwan Shayi taje ta kawo mai.

"Abbansu yaya naga duk jikin ka yayi sanyi ka shigo babu kuzari?"
Sadiƙ ya kurɓi ruwan zafin tare da aje cup ɗin a center table ya kalli sakina fuska babu sukuni

"Jikin Aliyu ne ya bani tsoro wallahi duk hankalina a tashe yake na rasa Nutsuwa ta"
Ta ɗan kalle shi cikin zaƙuwa da taji abin da ke damun Aliyu ɗin.
"Mutuwa likitan yace zeyi ko cutar ɓarin jiki ce ta kama shi?"
Sadiƙ cikin tsananin mamaki yace.
"Ban fahimta ba sakina dama akwai wanda yasan ranar Mutuwar wani ne In ba Allah ba?"
Ta ɗan sosa kai tare da cewa "To naga duk ka ɗaga hankali ne In ba haka Likitan yace maka ba to meye zaka wani zo duk ka damu kanka so kake kuyi Mutuwar kasko shi a kwance kai ma a kwance a,a gwara anyi ɗaga shiɗin dai ya kwanta"
Sadiƙ ya zubawa sakina ido cikin Nutsuwa yace "Ban gama gano nufin ki ba Ai ni a tunani na duk abin da ya shafi Aliyu nima ya shafeni kamar duk abin da ya shafe ni shima ya shafe shi"
Ƙaramar dariya sakina tayi.
"Kai dai kake ganin haka Ni jikina  ma ya bani Mutuwa zeyi babu mamaki mutuwar Fuji'a ce Faɗuwar ajali yayi dama abu ne irin nasa ya auri jamila yaƙi da tuni yaga ɗan kanshi to ai yanzu gashi nan ya tara mana dukiyar ze mutu yabar mana ita muyi yadda muka so" wata irin tsawa sadiƙ ya bugawa sakina yana toshe Kunnen sa tunda take bata taɓa ganin sadiƙ a irin yanayin data ga ya shiga a yanzun ba ya shiga girgiza kai yana Hawaye "Ya Allah idan har ka ƙaddara Aliyu mutuwa zeyi Ya Allah ka dawo da wannan ajali kaina ni na mutu domin rayuwar sa tafi tawa amfanuwa ga Al'umma duk da Allah ba wanda ya isa yayi maka dole ba mai saka ba mai hana ka yadda kaso kake yi a lokacin daka so kaga dama"
Sadiƙ ya faɗa yana wani irin kuka wanda ya bawa sakina mamaki zatai magana ya ɗaga mata hannu dan baya buƙatar tace masa komai.

Cikin Tsiwa da rashin Kunya ta miƙe tsaye akan shi.
"Daga faɗin gaskiya zaka hau Kuka, Me yake tsinana maka kai kenan Kullum Yi masa hidima ya mai da kai kamar yaron sa Baka da komai se Masa hidima in da yana ƙaunar ka ya mallaka maka kamfanin sa na lagos mana ai yaƙi Se aikin matar sa kullum taci tai kashi waya sani ma ko mu yake tarawa dukiyar Wallahi bama zan ɓoye maka ina jin matiƙar haushin biyayyar da kake yi masa"

Sadiƙ ya ɗago idanun shi jajir yace mata.
"Wallahi sakina baki isa kin rabani da Aliyu ba naji bani da komai ɗin tun da ke baki da godiyar Allah duk ni'imar da Allah yayi mana kin take ta Aliyu kike hangowa to bara Kiji kamar yadda ci bezo ɗaya ba To ƙoshi ma baze zo ɗaya ba Ko yatsun mu in muka duba ba daidai suke ba, kuma ni bana baƙin ciki da arziƙin Aliyu dan ta hanyar halak Allah ya bashi maganar Matar sa kuma ai bake ce Kike bada haihuwar ba Allah ke bada wa ba ita zaki wa Gori ba don ba ita zata bawa kanta ba jamila kuma ni kaina bana masa sha'awar auren ta dan bata da kamun kan da Aliyu ze zauna da ita a matsayin uwar ƴaƴan shi kema nadamar auran ki nake bada ban darajar ƴaƴana ba da tuni Kinyi gaba wallahi su kaɗai nake dubawa amman ki cigaba da yadda kika  so na baki Lokaci ne kaɗan, Dan babu wata macen da zata shiga tsakanina da ƴan uwana in zuba mata idanu"

Sadiƙ ya faɗa a zafafe Sakina jitai ƙafarta na rawa Lallai ashe akwai sauran aiki a gabanta Duk haƙilon da take dan wa take idan ba dan shiba ashe ma shi bai san tana yi ba Jikinta se ya ɗauki rawa muryarta na karkarwa "Abbansu yau ni kake gayawa haka akan Aliyu? dan wa nake haƙilon nan dan kai nake yi kai ma ka shaƙi iskar ƴanci kai ma ka tsaya da ƙafafun ka, ka fita daga jerin yaran kamfanin sa Amman har ni zaka buɗi idanu ka jefawa waɗannan maganganu to Allah yasa a budurwa ka same ni bare kace nayi yawon ta zubar tun da kace Jamila bata da kamun kai"
Cikin fushi sadiƙ yace.
"Da bana shan iska kenan Look sakina kada ki yarda na same ki da wata manufa akan ɗan uwana na rantse da Allah in kika bari na kamaki da wata manufar ɓoye akan ɗan uwana wallahi senai shari'a dake kuma bari Kiji har yau har gobe babu macen da zata raba mana kai nida Aliyu soyayyarmu daga Allah take Kuma abin da kika kasa ganewa Aliyu yana da kamfanin Mota ne A lagos da sunan sa amman Komai na kamfanin ya sakar Mini se yadda nai dashi In har na cuci Ali kona zalunce shi ba zan gama da kyau ba  sabida babbar nadama ce ka cutar da wanda ya baka yarda da amana In kuma ban godewa Allah akan ni'imar da yayi min ba zan godewa azabar sa Ko yau na mutu nagode Allah dan yayi min dukkan suttura ƴaƴana kuma nina san Aliyu ze aurar Mini dasu Muddin yana raye ze tsaya musu a komai"

Da sauri sakina tabar ɗakin sadiƙ be kwanta ba alwala ya ɗaura yana jero sallar nafila akan Allah ya bawa Aliyu lafiya ya kuma shirya masa matarsa ya cire mata hassada da ƙyashi da baƙin ciki.

Yadda Sadiƙ ammi farha basu rintsa ba haka sakina ma bata rintsa ba asubar fari ta tashi jamila suka bar gidan dan fita tai wajan bokanta akan ya bata maganin mallaka da ɗaurin baki wanda

bata ɗauka sadiƙ ze bata matsala haka ba shiyasa batai tunanin bi ta kan shiba a gidan su suka aje ƴaƴanta ita kuma da jamila suka nausa ƙauyen da Bokan nata yake.

Farha tana zaune a saman darduma a tsakiyar ɗakin mami sabida a ɗakin mami suka kwana tare bayan ta idar da sallar asubahi ta ɗaga hannunta sama idanunta yana zubar da hawaye addu'a take yi akan Allah ya bashi lafiya kafin ta idar ta shafa ta soma karatun azkar Lokacin gari yayi haske mami se baccinta take hankali kwance kamar ba ita ce ta gama kuka jiya ba Ita dai farha jingina kanta tai da Jikin gado Hawaye duk ya bushe a idanunta wajan shiddan safe mami ta farka idanu jajir ta dubi farha cikin mamaki.
"Farhan wai baki bacci jiya bane ni dai duk tashin da zan sena ganki a zaune kina sallah?"
Farha bata ce komai ba mami ta tashi ta shiga banɗaki ta jima aciki sannan ta fito tazo ta shinfiɗa darduma a ƙasa tana sallah Bayan ta idar wayar ta ke ringing taje ta ɗauka ta zauna a bakin gado.
"Hello mama ina kwana"
Shuru ne ya biyo baya da alamun na wayar ke magana.
"Eh mama ya kusan ƙarewa kwana biyu ma Kin san muna umara To kuma mun dawo Aliyu ya faɗi yana asibiti nayi zaton Jiya ma zaku zo nan ɗin ai"
Shuru mami tayi can tace

"Ƙaddara mama  wallahi ya faɗi to shikenan se kun zo nagode"
Bayan ta gama wayar wadda ta bawa farha tabbacin da mahaifiyarta suke yi tashi tayi ta fita farha ta gyara mata ɗakin wajan ƙarfe tara na safe Mami ta kammala girki ta zuba komai cikin Basket lokacin farha ta gama mata gyaran ɗaki mami shiga tayi ta shirya cikin Jallabiya baƙa tai rolling ɗin mayafin jallabiyar a kanta ta fito tana zabga ƙamshi farha datai tagumi ita ko wankan ma batai ba Tun kayan ta na jiya ne ajikinta Hijabi kawai ta sauya.
"Farhan driver ze kaini asibiti sabida yanzu dana shiga ciki Sadiƙ yayi min waya akan na kaiwa Aliyu abinci sabida Ammi ta tashi yau da rashin Jin daɗi tasha magani bacci take Se anjima zata je wajan shi To ba kowa ni zanje na karɓi Bashir"
Zaraf Farha ta miƙe tsaye tana wasa da bakin Hijabin ta Muryarta kamar zatai wani Kukan tace.
"Aunty mami nima zani"
Mami tayi dariya "To a haka zaki baki wanka ba ki bari anjima seki bi su Ammi" hawaye ne ya shiga ziraro mata wanda bata san da suna zubar ba kafin tace "Ni dai dan Allah zan biki" mami taɗan sha jinin Jikinta kafin ta kalli farha cikin nazari "Farhan badai akan faɗuwar Yaya kike ta kuka tun jiya ba?" Jikin farha yaɗan yi sanyi sabida Kada mami taga zaƙewar ta cikin sauri tace "A,a nima bana jin daɗi ne Kuma sannan Kin san babba kamar shi ya faɗi ai duk mai hankali ze shiga cikin damuwa dole" Mami ta wuce ta ɗauki baske Ɗin tana cewa "Haba nidai nai mamakin Kukan naki To Allah ya baki lafiya Shige Mu tafi" suka fita wajan mota suka shiga driver yaja su zuwa asibitin farha ta matsu suje taga wani hali yake ciki ajiyar zuciya farha ta sauke sanda suka shiga cikin asibitin ba kowa Sabida asibitin mai tsada ne sosai ba Mutane se iya ma'aikata haka suka wuce Ciki adaidai Ƙofar shiga suka haɗu da Bashir Suka gaisa da Mami farha kawar da kanta tayi Gefe.
"Yawwa Aunty mami gwara da kika zo Ni bari nabi driver gida na ɗan kwanta dan Jiya ban yi bacci ba wallahi"

Mami data nuna damuwa ƙarara a gaban Bashir tace.
"To yaya Jikin nashi?"
Bashir yaɗan kalli farha tare da cewa.
"Bai farka ba dai har yanzu amman Likita yace zuciyarsa Normal kawai alluran ne basu sake shiba"
Mami tai ajiyar zuciya tana cewa

"To Alhamdulillahi"
Bashir yaɗan dubi farha.
"Cute babu gaisuwa abin ƴar haka ce Ko?"
Farha batai masa magana ba tabi bayan mami suka shiga ciki Ƙofar ɗakin da yake ciki mami ta murɗa handle ɗin ta shiga farha tabi bayanta sanyi da ƙamshi ne sukai musu sallama A hankali suka ƙarasa gaban gadon nashi..........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 92*

Har lokacin bacci yake yi kwance yake samɓal a kan gadon Jikin shi gaba ɗaya a rufe yake da tattausan Bargo fari tas mami ta aje basket ɗin hannunta tare da zama a saman ɗaya daga cikin dogayen kujerun ɗakin farha kuma bata zauna ba hannu tasa ta dafe gadon daya ke kwancen ta zuba masa idanu bata ko ƙiftawa Addu'a take ta yi akan Allah ya tashi kafaɗun sa.

"Farhan ga wajan zama ki zo ki zauna anan kafin ya tashi naga bacci yake sosai" Cewar Mami farha taja ajiyar zuciya jita ke dama ciwon ya dawo mata shiya sami lafiya Jikinta a saɓule taje kusa da mami ta zauna.

Hannayenta duka biyun ta zube a kumatun ta tare da zabga tagumi ita ko mami wayarta ta ɗauko tana danne danne ɗakin shuru yayi wata nurse ce ta shigo ɗakin bakin ta ɗauke da sallama.

Suka gaisa da mami nurse ɗin ta dubi mami

"Amman ranki ya daɗe doctor yace kada wanda ya shigo wajan shi a bari har ya tashi daga baccin"
Mami tayi wa Nurse ɗin wani kallo tare da cewa "Aini ce mafi kusanci dashi fiye da kowa Kije kicewa Likitan matar shi ce a tare dashi" mami ta faɗa cikin gadara Nurse ɗin bata ce Komai ba ta ƙarasa wajan gadon da yake kwance ta duba shi tayi abin da zatai tabar ɗakin mami taja Dogon tsaki ta cigaba da danna wayar hannunta farha tashi tayi ta fita batare data cewa mami komai ba Mami ta bita da kallo amman setai tunanin ko zaga asibitin zatai shiyasa bata ce mata Komai ba harta ƙullewa ganinta farha bin bayan wannan Nurse ɗin ta dinga yi har zuwa bakin Office ɗin da zata shiga Juyowa nurse ɗin tayi tana kallon farha da sauri farha tayi ƙasa da kanta tana wasa da yatsun hannunta.

"Ƙanwata yaya akai?"
Cewar Nurse ɗin farha tai ƙasa da kanta sosai tare da cewa.
"Dan Allah Office ɗin Likitan daya duba wancan marar lafiyan zaki nuna min"
Nurse ɗin tayi murmushi.
"Okay amman yanzu baya nan sabida ba'anan ya kwana ba nasan dai yana hanya can kwanar zaki Miƙe seki hannunki na dama zaki ga office ɗin nashi"
Farha tai mata godiya tabi hanyar data mata kwatancan

Samun kujera tayi a wajan ta zauna zaman jiran Likitan.

A hankali yake motsa bakin sa salati yake yi yana ware idanun shi dishi dishi yake gani maƙogwaron shi ya bushe kanshi se sara mai yake yana masa azababban ciwo ji yake kamar ya rabe Gida biyu ga yatsan ƙafar shi se zugi yake mai kamar ze cire Zazzafan Huci ya saki Yana tariyo abin da ya faru daran Jiya na farko abin da ya ɗaga mai hankali yadda yaga Bashir na ƙoƙarin Cusa kanshi ga lamarin fatima wannan abu ya kaɗa shi wanda tunanin shi ya tsaya ne akan tabbas Bashir son fatima yake gaban shi ya faɗi bai ga laifin bashir ba sabida bashir bai da sani akan alaƙar shi da fatima, A bu na biyu yadda Ammi ta wulaƙanta fatima agaban ilahirin mutan gidansu abin ya ɓata mai ranshi se abu na Uku Shine abin da ita kanta fatima ɗin tayi masa abin ya ɓata mai ranshi a yunƙurin ya tashi ya Bayyanawa Ammi matsayin fatima awajan shi Allah ya ƙaddara masa wannan faɗuwa wadda tasa Numfashin sa ya tafi Hutun wucin gadi wanda bai sake sanin ina kan shi yake ba se yanzu a kuma gadon asibiti wanda shi kanshi bai san Taka maimai awani hali aka kawo shiba Kuma bai san meke damun shi ba yasha fa hannun shi yaji Plastar allura ya taɓa kanshi yaji plasta Ya yunƙura ya tashi zaune da sauri Mami ta ƙaraso tana mai sannu Da taimakonta ya zauna sosai Yana huci dan yadda kan shi kemai Ciwo Abin na dukan shi.

"Sannu yaya Allah ya baka lafiya"
Cewar mami ya cije leɓansa na ƙasa Idanunshi sunyi jajir Jijiyar kanshi ta miƙe tai raɗo raɗo.
"Zanyi sallah zona dafa ki"
Cewar shi mami ta kuma zuwa ya dafa ta suka shiga toilet.

"Ƴammata lafiya na ganki zaune kin zuba tagumi" cewar likitan daya ke tsaye akan farha Ta ɗago idanunta ta kalle shi ta soma motsa bakinta alamun gaisuwa ya amsa yana raɓeta ya Buɗe Office ɗin.
Ta bi bayan shi zama tayi a kujerar dake kallon tashi shima lokacin ya zauna yana aje jakar hannun shi "Likita dan Allah meke damun wancan bawan Allah da aka kawo Jiya?" Likitan yaɗan yi mata kallon Nazari tare da cewa "Wai madaki kike tambaya toke mecece ɗin sa?" tayi ƙasa da kanta tare da cewa "Matar shi" Likitan ya saki baki yana kallon ta bai da damar ƙaryatawa dan bai san komai akan Suba yaɗan dube ta a tsanake "Please karki ɗaga hankalin ki ba wata matsala gagaruma bace kawai ajiya zuciyar shi ta ɗan Buga ne se jinin shi daya hau sabida wata ƴar damuwa daya shiga ko kuma wani abu daya gani wanda yaɗan bugi zuciyar shi

amman Tun jiya numfashin sa ya dawo kuma Jinin nashi ya sauka se Buguwa da yatsansa da kanshi yayi duk mun gyara masa Yanzu haka Nurse tace bacci yake alluran da mukai masa ne masu ƙarfi" Tuni hawaye ya gama jiƙa gaban Hijabin farha cikin wani irin yanayi take kallon Likitan kafin muryarta cikin Kuka tace "To yanzu wani matakin za'abi don kada hakan ya kuma faruwa dashi?" Likitan yace "Kada ki damu Kawai magani ze dinga sha akan Lokaci Sabida jinin nashi kada ya dinga hawa sannan kuma aguji ɓata masa rai ko yaya duk abin da ze ɗaga masa hankali aguji yi agaban shi ai ita lalura ƙaddara ce wata baka tashi da ita ba seka kwana da ita wata bakai farko da ita ba sekai ƙarshe da ita nidai Inda naji dadɗi ma da matsalar zuciyar batai ƙarfi a tare dashi ba" Farha taja ajiyar zuciya Gaba ɗaya ta karaya da lamarin lallai mai rai ba abakin Komai yake ba "To Yanzu wani maganin ya kamata a fara ɗora shi akai?" Cewarta Likitan yace "Duk mun rubutawa Ɗan uwan shi jiya kuma an siyo se a dinga Kula wajan bashi" Godiya tai masa tabar Office Ɗin Likitan ya mayar da ajiyar zuciya yana jin ina ma shine yayi dacen macen da take son shi kamar wannan yarinyar.

Ko gabanta bata gani haka ta nufi Ɗakin da aka kwantar dashi dan ta cika da damuwar lamarin nashi.

Adaidai Lokacin Kuma ya kammala Abin da ze a toilet ɗin mami ta kamoshi mami da taji ƙara kamar an turo ƙofa ta ɗauka ko farha ce cikin sauri tace "Farha ɗan shinfiɗa mana carpet kafin mu fito" duk da halin da yake ciki seda ya dubi mami akaikaice yace "Wace haka?" mami tace "Wannan yarinyar mana ta wajan ammi ai jiya tare muka kwana se Kuka take tama Ki bacci se sallah nina ɗauka ma ko akan faɗuwar ka take Kukan dana tambayeta shine tace Itama bata da lafiya ne Da zanzo nan tare Muka zo to naga ta fita ne ban sani ba Ko ta shigo" Ta faɗa sanda suka fito daga cikin Toilet ɗin Aliyu cikin kaɗuwa yace "Kika barta kuma ta fita?" daga haka ya zame daga Jikin Mami Jiri na ɗibar shi ya Nufi wajan abin sallah duk Jikinsa yayi sanyi alokacin farha ta shigo daidai nan shikuma ya tada sallah.

Ajiyar zuciya ta sauke a ɓoye tana Goge hawayenta.
"Farha daga ina kike?" cewar mami.
Sosa kai farha tayi tare da cewa.
"Na fita ne na zauna a waje" ta faɗa tana Kallon yadda yake sallah bayan ya idar ta nemi guri ta zauna wannan karon a ƙasa ta zauna Kusa dashi so take su haɗa ido amman se taga ya kawar da kanshi Gefe.

Ya jima yana addu'a kafin ya miƙe da sauri mami ta zo ta kamashi yadda suka haɗe da juna shida mami se abin yaɗan sosa mata rai da taimakon mami ya koma saman Gadon ya zauna. "Mami baki zo min da kayana ba wannan sun dame ni wanka zanyi" mami aranta tace ai ko kwaɗo yasha fa ma lafiya wajan yin wanka amman a fili se tace "Na manta amman bari anjima in basu baka sallama ba sena je na ɗauko ma" yaɗan ɓata Fuska "Ni wanka zanyi Kinga kije Ki ɗauko Mini kawai" ya faɗa yana Jingina kanshi da Jikin pillow Ɗin da ke kan gadon

"To bari kayi break" ta faɗa ta shiga haɗa mai tea.

"Ina kwana yaya kwanan Jikin naka?" Yaji Muryar farha amman seyay mata banza yaƙi kulata sema ya Juyar da kanshi Gefe.
"Yaya baka jiba ana gaishe dakai" banza yayi wa mami ɗin itama farha taji wani takaici ya taso mata da ƙyar ta danne ta cigaba da wasa da hijabinta Mami ta tura mai ƙwai da dankali da ruwan shayi Gaban shi ya Tashi zaune Ya ɗauki Cup ɗin shayin

"To sedai nahau napep dan driver yaje kai bashir Gida farha bari naje na dawo"
Cewar mami farha ta Miƙe tsaye "A,a zan biki mu tafi tare kawai" dan ya gama ƙona mata rai yadda ya Nuna halin Ko in kula akanta ai ita jiya ta kasa bacci sabida shi

"A,a ki zauna yanzun nan zan dawo Dana dawo semu koma tare sabida koda Kinje ɗin ma Gidan Ammi ba kowa duk nan zasu tawo" mami ta faɗa tana fita daga ɗakin badan farha taso ba ta Koma ta zauna rannan nata a haɗe ta haɗe fuska babu alamun dariya.

Ɗakin shiru yayi can taji Muryarshi.
"Fatima bani ruwa marar sanyi"
Banza tayi masa.
Ya kuma maimaitawa a zuciye ta miƙe tare da zuwa wajan ƙaramin Fridge ɗin ɗakin ta ɗauko mai gorar ruwan tazo gaban shi ta Miƙa masa amaimakon ya amsa seya haɗa da hannunta. Ƙoƙarin zamewa take yaƙi bata dama sema cicciɓota da yayi zuwa saman gadon ya direta a saman Cinyar sa.

Taƙi kallon shi a yayin da shi kuma ya zuba mata ido tausayinta yana ratsa mai dukkan Ilahirin sassan Jikinsa.
"Fatima kuka kikai tayi kalla Hijabin Ki duk ya yi jirwaye da ruwan hawaye Koma wanka baki ba"
Ya faɗa a tausashe.
Sabon kukan ta soma yi.
"In banyi kuka ba me zanyi tun jiya kana ta fushi dani"
Da sauri yace mata.
"Ko na mutu baki da asara ay tunda Kin zaɓi kita gasa min magana kamar sa'anki Tunda ba zaki bi yadda nake soba ay shikenan" da sauri tace masa "To ni mai nayi maka Kaga in ma danni ka shiga wannan halin ka fita dan wallahi ciwon nan kaɗai ne ajikinka amman nina fika wahala Jiya ban rintsaba gani nake kamar zan farka ace Min ka rasu" ta faɗa tana Goge hawayenta Kusancin su ne ya daɗu Lokacin daya Ke Kusanto da fuskar shi daidai wajan tata fuskar har ƙasumbar Fuskar shi na gogar tata Fuskar Idanu ya Lumshe yana Fesa mata hucin Numfashin sa.

"Kaci abincin se kasha maganin ka"
Ta faɗa tana ɗanyin baya da fuskarta.
Hannunta ya damƙa ya Ɗora a saman Kirjinsa a hankali yace.
"Fatima kina jin yadda zuciya ta take Bugawa? Fatima duk rintsi kada Ki kuma furta kalmar zaki rabu dani Kinjii....Ji nake kamar zan Mutu wayyo kaina" ya faɗa Cikin wani yanayi wanda ya kaɗa hantar Cikin farha Kuka tasa tana Kwantar da kanta a saman Kirjinsa.

"Me yasa ba zaka gaya Musu matsayina a wajan kaba Me yasa ka zaɓi ka Ɓoye aure na dakai Dan Allah kayi wani abu akan hakan" ta faɗa Cikin Kuka

"Fatima Ammi na tsoron ɓacin ran Ammi na nake wallahi fatima ina masifar Gudun ɓacin ran Ammi ne"
Ya faɗa a wahalce zame wa tai zata tashi daga Jikinsa yayi saurin ƙara Rungumota kamar wani ze ƙwace mai ita hannunshi ya zira ƙasan Rigarta.
Yana wani daɗa matse ta ajikinsa.
"Mami tace Min baki da lafiya oya tell me meke damun ki Muji Jikin naki?"
Ya faɗa yana Buga mata Numfashinsa a saman Fuskarta Lumshe idanunta tayi lokacin dataji ɗumin tafin hannunshi a saman Cikinta yana wasa da tsakiyar Cibiyarta.................
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 93*

Jikinta ne ya hau rawa tana wani irin shige masa kamar mai jin sanyi zullewa take tana cusa kanta a cikin Ƙirjinsa a hankali ta riƙo hannun shi dake Cikin rigar tata.
Fuskarta ta ɗago wadda tai kalar tausayi kamar zata yi kuka! ta ce masa "Dan Allah ka dena" Cikin raɗa kuma a hankali yace "Sabida me bayan ni daɗin hakan nake ji" ya faɗa yana Ƙara shigar da hannunshi sosai Ya shiga Murza Ɗan tudun daya ji a ƙasan marartata Huci ta sauke tana kwanciya sosai a jikinsa wani irin wahalallan Numfashi take ja gaba ɗaya ya saukar mata da kasala ajikinta hannu tasa ta kamo fuskar shi ba zato yaji saukar danshin Bakinta a saman lips ɗinsa tana tsotsa a hankali ya Jinginar da kanshi a saman Pillow ya Lumshe idanunshi Ji yake dama zasu dawwa ma acikin wannan yanayi mai wuyar Misaltawa......

"Ammi ya kamata ki kwantar da hankalin ki Jikin Yaya Aliyu da sauƙi sosai dan yanzu haka ma Aunty mami tana tare dashi" cewar Bashir wanda yake tsugunne a gaban Ammi sadiƙ daya Fito cikin shirin tafiya asibitin sabida ya makara sakamakon Rashin baccin da bai samu a daran Jiya ba shine ya dubi Bashir wanda ke gaishe dashi Bayan ya amsawa Bashir ya kuma ce masa "A,a yaya na ganka agida Kuma shi Aliyun da wa ka bar shi ai da kayi min waya dana je in yaso kai seka tawo" Bashir yaɗan sosa kai tare da cewa "A,a Aunty mami taje har da kayan break fast ma shine nace ni bari nazo nai wanka sena koma" Sadiƙ ya zauna a kusa da Ammi yana gaishe ta kafin yace "Okay to yaya ƙarfin Jikin nashi?" bashir yace "Da sauƙi amman har na tawo be farka ba" Cikin wani irin yanayi ammi tace "To kuma shine zaka ce bazan je na ganshi ba wannan wani irin Bacci ne tun jiya har yau Mutum bai farka ba kaga in da wani abun da kake ɓoye Min gwara ka gaya min nasani ni Musulma ce kuma ba mutuwar da ban gani ba tunda naga ta uwata da ubana naga Ta mijina" Ammi ta faɗa tana share hawayen ta! Bashir ya soma rarrashinta "Wallahi Ammi ya sami sauƙi bacci ne kawai yake sabida allurar da akai masa mai ƙarfi ce haba Ammi in akwai wata matsala ai dana gaya Miki Kuma abin da yasa nace Miki ma ba zaki je ba sabida shima nan da Anjima za'a bashi sallama naga kuma kema ba lafiya ce dake ba Ki sha maganin ki kikwanta ki huta" Bashir ya faɗa cikin sigar rarrashin Ammi Sadiƙ ne

ya saka baki Haka suka haɗu da ƙyar dai suka samu Ammi ta dena Kukan Amman ta kafe tace wallahi seta je asibitin Badan ran Sadiƙ Yaso ba yace ta shirya su tafi Su safna ma sun fito cikin shiri sadiƙ ya dubi Sajeeda tare da cewa.
"Ki leƙa kice wa maman Minal ta fito muje asibitin" Sajeeda ta amsa tare da Nufar ɗakin da sakina take Ciki sedai koda ta shiga babu kowa acikin ɗakin dawowa tayi tare da shaida masa cewar basa nan.
Sadiƙ cikin mamaki yace

"Fita sukai amman basu gayawa kowa ba Ko Ammi sun leƙo sun ce Miki zasu fita?" Ammi ta girgiza kai tana tashi ta shiga bedroom ɗinta dan ta kintsa sadiƙ wayar shi ya ɗauko ya shiga kiran Number ɗin sakina sedai koda ya Kira Number Ɗin Bata shiga yaja tsaki aranshi yana ayyana Rashin Mutuncin daze wa Sakina wannan wani irin iskanci ne ta fita ba tare da izinin shiba da ƙyar ya saita kanshi dan kada ƙannen shi su gano akwai wata matsala haka Ammi ta fito suka rufo part ɗin suka nufi compound a nan suka haɗu da Mami wadda ta fito da kayan Aliyu data zo ɗauka masa A babbar Mota suka tafi asibitin sabida ƙananun Motocin gidan ba zasu ɗauki yawan suba.

Gaba ɗaya hannayen shi suna zube a gadon bayanta ya riƙe ta gam ya sakar mata Jikinsa sabida yadda take Kissing ɗin nashi ji yake kamar Numfashin sa ze bar gangar Jikinsa A hankali ta zare harshen ta daga cikin bakin nashi tana sakin wani irin wahalallan Numfashi, Ƙoƙarin sauka take daga jikinsa wanda shi kuma yaƙi bata damar hakan idanunshi jajir Muryarshi ta dashe yace mata.
"Dan Allah kar kimin haka"
Ta ɗan tura bakin ta gaba kamar wata ƙaramar yarinya

"In wani yazo ya gammu fa kuma ma ai baka da lafiya" ya sa hannun shi ɗaya ya shafi gemun shi yama kasa magana gaba ɗaya Jikinsa ya saki Murya can ciki ya furta mata "Kullum ƙara sauyawa kike Ji nake in bamu kasance tare ba kamar zan rasa raina dan Allah fatima" ya faɗa yana wani taɓe baki kamar ƙaramin yaro.
Ita abin ma dariya yake bata se kace wani ƙaramin yaro.

"To ni me zanyi maka kalli fa ƙafarka Tana ciwo da kanka"
Janyo hannunta yayi tare da saka yatsanta guda ɗaya a cikin bakin shi yana tsotsa a hankali kwantar da kanta tayi a saman Ƙirjinshi ta Lumshe idanunta wani irin bacci ne yake kawo mata hari amman tasan nan ɗin ba wajan bacci bane A hankali taji takun takalman Mutane wani irin zullo tayi zata sauka daga saman gadon Ya wani janyota ya matseta kamar zatai masa kuka tace.
"Tawowa fa ake wallahi ga ƙarar takalman Mutane nan dan Allah ka sakeni kada ka min haka"
Duk ta faɗa cikin tsoro.
"To ki sauka a hankali wannan dirar da zaki ai da matsala" bata saurare shiba tai saurin sauka ta Tafi can nesa da gadon nashi ta zauna sedai gamai hankali kallo ɗaya zakai mata kasan Bata da Nutsuwa Tana zama Kuma taji ana murɗa handle ɗin Kofar kafin hayaniyar su Ammi ta cika

ɗakin dukkan su suka shigo kuma babu wanda ya kula da ita gaba ɗaya gadon suka nufa suna yi masa sannu Idanunshi a lumshe yake yana sakin Numfashi sabida idan ya buɗe idanun nashi tabbas za'a fuskanci yana cikin wani hali Cikin Jimami ammi take kallon shi.
"Baba kai mana magana mana kowa ya kasa bacci jiya sabida kai dan Allah kai min magana" ta faɗa muryarta tana rawa a hankali ya tashi ya jingina da pillow yaɗan kalli ammi Yana kama hannunta ya ƙaƙalo Murmushin dole "Ammi dafa sauƙi naji sauƙi" ya faɗa a hankali su safna suka shiga gaishe dashi sannan suka gaisa da sadiƙ Mami tace masa "Ga kayan na ɗauko maka kayi break ɗin Kuwa?" ya jinjin mata kai dukkan su zama sukai sedai sun rage hayaniya sabida shi A hankali Ammi ta jefa idanunta kan farha wadda taji kamar ta saki fitsari dan tsoro "Ke kuma waya kawo ki nan kinyi tsuru kamar shege a rabon gado?" da sauri mami tace "Nice nazo da ita Ammi kin san jiya da ita muka kwana" daga haka ammi bata ce komai ba Farha taja ajiyar zuciya sabida mami ta kareta ɗakin shuru yayi sedai Aliyu da sadiƙ suna ɗan yin magana jifa jifa akai sallar azahar duk suka tashi dan zuwa suyi sallah sadiƙ da Aliyu masallaci suka tafi farha kam bata motsa ba ta matsu subar asibitin bayan sun dawo daga masallaci Doctor ya shigo ya miƙawa Aliyu hannu.
"Ma sha Allah! jiki yayi kyau ko yanzu ma za'a iya sallamarka amman kafin nan zo muje Office na ɗan Gwada jinin ka" Aliyu da sadiƙ suka bi bayan doctor suka fita Wanda adaidai Lokacin da sadiƙ ya gifta ta wajan farha ƙamshin turaren shi mai ƙarfi ya doki hancinta jitai kanta yana juyawa seta fara rufe idanu tana dafe bakinta wani irin amai ne mai ƙarfi ya tawo mata Da gudu ta miƙe ta shiga Cikin Toilet ta tsugunna ta dinga sheƙa amai kamar zata amayar da hanjin cikinta mami tana tsaye akanta tana jera mata sannu ta gama Mami ta wanke mata bakinta suka fito sedai yadda ta wahala a wajan aman ga yunwa dan rabon ta da abinci Tun  jiya se jiri ya ɗebe ta a wajan ta zube tana sakin Numfashi Cikin tausayi Ammi ta dubi Mami dake ƙoƙarin ɗago farha.
"Mami aje akira Nurse su duba ta ko ɗan ƙarin ruwa ne ai mata dama bata da lafiya ne?" mami tace "Tun jiya dama na fahimci bata jin daɗi" Sajeeda ce ta kira Nurse wadda tazo tace Su ƙaraso da farha wani ɗaki dake Kusa dana Aliyu Da sajeeda da mami ne suka kamata suka kaita ɗakin Nurse ɗin ta dubi Farha bayan su Mami sun fita.
"Me dame yake damun ki?"
Farha tace.
"Yawu ke taruwa a bakina se kasala da amai da yawan bacci"
Nurse ɗin tace.
"Yaushe rabon ki da ganin Period ɗinki Ai kina da aure ko?"
Gaban farha yayi mumnan faɗuwa a hankali tace.
"Eh ina da aure sedai rabona da ganin Period ɗina zan kai wajan wata Uku Babu kwanaki Kuma ni hankalina bai kai Lissafinsa ba sabida ban da nutsuwa"
Nurse ɗin tace mata.
"Shiga wancan toilet Ɗin ki fitsari a wata kwalba ki miƙo min"
Jikin farha da matiƙar sanyi ta shiga bayin tayi fitsarin ta miƙowa Nurse ɗin wadda ita kuma ta fita tana fita su mami dake tsaye a bakin Ƙofar suka tare ta da cewa "Yaya jikin nata?" Nurse ɗin tai Murmushi tare da cewa "Ku kwantar da hankalin ku bari naje yanzu zan dawo" Mami ta saki ajiyar zuciya dama ita kaɗai ce ta damu da lamarin Farha ɗin se sajeeda wadda Take tayata tsaiwar ammi kuma da Safna suna cikin ɗaki.

Gaba ɗaya Jikin farha rawa yake hankalinta a Mugun tashe yake Ji take dama bata cewa Nurse ɗin tana da aure ba da seta roƙeta akan ta rufa mata asiri koda gwajin da zatai mata ya bada wani sakamako kada ta gayawa kowa dan gaba ɗaya tunanin farha ya tafi akan tana da ciki dan ta taɓa jin wata rana Yaya sadiya ke gayawa yaya nafisa ita fa wata biyu bata ga al'adarta ba tana zargin Ko ciki ne da ita tundaga nan ta fahimci hakan Sam tunaninta ya gushe ga fahimtar yanayin ta se yanzu da Nurse Ɗin ta tunatar da ita koda yake rashin kwanciyar hankali ma kaɗai wanda take ciki ze hanata fahimtar tana da shigar Cikin wato shiyasa Komai nata ya sauya.

Cikin farin ciki Nurse Ɗin ta fito wanda ta nufo ɗakin da Farha take kwance domin tayi mata albishir da tana da shigar ciki na watanni Uku cif sedai Mami ta kuma shan gaban nurse ɗin tana ce mata.
"Yaya mai jikin tamu amman ba wata matsala bace?"
Nurse ɗin tai Murmushi tare da cewa.
"Ki kwantar da hankalin ki madam Da farko dai ina tayaku Murna dan tana ɗauke da ciki na wata uku cif ajikinta"
Ƙafafun mami ne suka soma rawa sajeeda da rawar Jiki kuma muryarta da ƙarfi tace.
"What Ciki fa har na wata uku ƙanwar musan ?"
Da sauri Ta buɗe ƙofar ɗakin dasu Ammi ke ciki tana cewa.
"Ammi baki ga ta zama ba wallahi yadda tazo sedai ta Koma Kinji ciki ne da ƙanwar musa har na wata Uku"
Ammi da safna agigice suka fito gurin nurse ɗin wadda take tsaye mami kuwa tama kasa magana.
"Ke ƴarnan wake da ciki?"
Cewar ammi Nurse Ɗin tace.
"Mama ku kwantar da hankalinku tana cikin ƙoshin lafiya sannan tunda tace min matar aure ce ita ai No need ku ɗaga hankalin ku haka"
Ammi cikin masifa tace.
"Ƙarya take Munafuka Budurwa ce mai aikina ce Wallahi bazata ƙara kwanar Min agidana ba Safna ku kamo min ita Muje gida ta haɗa kayanta tabar Min gidana bazan ɗauki jaraba ba ƴaƴana basu kwason abin Kunya ba ɗan wani baze kwaso Min ba shegiya munafuka Mami muje Mota kidena mamaki dama ƴaƴan ƙauye wasu ai sunfi na birni jaraba Su Baba sa same mu agida dan bazan kuma zama anan ba Muje Gida tabar Min gidana"

Duk yadda Nurse Ɗin taso ta fahimtar da Ammi taƙi sauraronta Su safna a wulaƙance suka janyo hannun farha suna aibata ta harda ce mata ƴar iska mazinaciya Suka wurgata Mota da ammi da mami suma suka shiga mami Jin komai take kamar mafarki to tayaya farha tai ciki lallai Mutum mugun Icce driver ne yaja Motar suka bar asibitin suka tafi gida..............
Autar manya ce marubuciyar......
*ƁOYAYYAR KAUNA*
*BA SON TA NAKE BA*
*ƊAN MAJALISSA*

*MURADIN ZUCIYA*
*ASHE ZUMA*
*TAURARO*
*KOBA SO*
*RABON WANI*
*FITAR RABO*
*DA IZZATA*
*BAƘON LAMARI*
*AUREN BARE*
*H A S K E*
*RABO YA RANTSE*
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 94*

Doctor ya zare farin glass ɗin dake idanun shi yana miƙawa Aliyu Doguwar farar takardar dake hannun shi tare da cewa.
"Alhamdulillahi Mr Madaki I hope your blood is back to normal, but you should be very careful if something like this happens in the future domin jiya a yanayin da aka kawo ka abin it was very sad Allah ya kiyaye gaba"
Aliyu ya naɗe takardar ya cusa a aljihun jallabiyar Jikinsa dan be samu yayi wankan bama kayan shi da Mami tazo mai dasu suna ɗakin da aka kwantar dashi.
"Nagode doctor And I will keep all the commandments that you told me in sha Allah, Se maganar Bill"
Doctor yayi murmushi.
"Ɗan uwanka tun jiya yayi dukkan abin da ya kamata"
Sadiƙ yace.
"Rabu dashi Likita so yake ya nuna mana shi me Kuɗi ne"
Aliyu Murmushi yayi yana shafa Gemu bai kuma cewa Komai ba dan har Lokacin bai Koma normal ba

Tashi suka yi suka miƙawa doctor hannu sukai sallama Suka fita daga Office adaidai bakin Ƙofar fita Aliyu ya dafa ƙafar shi tare da cewa.
"Washh Allah na!"
Sadiƙ da kulawa yace.
"Subuhanallahi ƙafar ce dai Ko gidan masu ɗorin gargajiya zamu je in mun fita sannu"
Aliyu ya dafe Ƙirjinsa sakamakon wata Mummunar faɗuwar gaba data ziyarce shi.
A fili ya furta.
"Subuhanallahi Innalillahi wa'innah ilaihirraju'un"
Ya faɗa da ƙarfi Kuma da sauri yana dafe ƙirjinsa yana Riƙo kanshi sadiƙ ya zuba masa ido.

"In kana ganin baka jin daɗi har yanzu Mu ƙara kwana ka huta Sosai"
Girgiza kai yayi.
"In ban yi ƙarfin hali ba Ammi ba zata kwantar da hankalinta ba banson ciwon ta ya tashi"
Sadiƙ yaɗan kalle sa tare da cewa.
"Kai kuma seka kashe kanka Ko me? baka warware ba ma karɓi sallama ba gwara ka ƙara zama Normal ba"
Dafa ƙafaɗar sadiƙ yayi suka jera A tare suka Miƙe hanyar da zata sadasu zuwa wajan su Ammi.
Abin mamaki koda suka je Cikin Room ɗin babu kowa acikin sa Aliyu ya saki kafaɗar sadiƙ yana ƙarewa ɗakin kallo.
"Ina su Ammi?" ya faɗa a fili Sadiƙ yace.
"Ko gajiya sukai da jiran mu suka tafi Gida"
Aliyu ya girgiza kan shi.
"Gaskiya su Ammi ba zasu tafi gida haka ba there is something that happened"
Ya faɗa yana fita daga ɗakin Sadiƙ yayi saurin Bin bayan shi a Farfajiyar asibitin yaja ya tsaya ya kama Ƙugu Kamar daga sama kuma ya hango Nurse na tawowa zata shiga Office yasha gabanta.
Ko sallama bai mata ba.
"Da Allah ko kinga wasu mata haka anan ɗakin?"
Wannan nurse Ɗin ce wadda ta gwada farha Cikin sakin fuska tace masa.
"Ƙwarai akwai wadda na duba acikin matan da suka zo Dubaka To abin da yasa ma na duba ta sabida nayi amfani da file ɗinka ne na nan asibitin tunda aikin gaggawa ne tana buƙatar taimako"
Da sauri yace "wacece babbar macece?"
Duk zaton sa ko Jikin Ammi ne ya tashi a lokacin sadiƙ ya ƙaraso wajan Nurse Ɗin tace "A,a wannan Matashiya ce mai ɗauke da Cikin wata Uku amman dai naga dana faɗa musu duk sun Shiga tashin hankali Kuma ita tace Min matar aure ce Nadai barsu sun tafi gida......

Ai ina bai ma ƙarasa Jin sauran ba ya saka kai yabar wajan duk uban Kiran da sadiƙ ke masa bai Jisa ba Har yakai bakin gate ya tari napep Da ƙyar sadiƙ ya cimmasa Suka shiga Ciki Duk uban maganar da sadiƙ ke masa sam bai magana ba Addu'a yake Akan Allah yasa kada Cikin Jikin farha ya sami matsala idanunshi sunyi jajir har wani Jiri yake Ji dan tashin hankali.

Tunda suka hau motar Ammi take cin Mutuncin farha babu kalar aibatatan da batai ba kamar Ammi bata taɓa haihuwa ba Farha ta kasa kuka se ajiyar zuciya take Numfashinta yana kaiwa da Komowa ashe Kuka ma se ana cikin kwanciyar hankali ake Yinsa tabbas Tunda take ganin Ƙaddarar Gidan Miji bata taɓa ganin mai kama da tata ba Mami ke bawa Ammi baki tana ce mata.
"Ammi dan Allah ki mata a hankali Muje Gida a kira Musa duk ai komai Cikin Nutsuwa nina fi zargin fyaɗe akai mata dan Farha tana da kamun kai"
Ammi tace.
"Dallah gafara can rufe min baki wannan mai kama da ɗanwaken ce za'awa fyaɗe babu wani ita

takai kanta dama Jiya tunda na ganta Naji gabana ya faɗi to bazan Goya ɗan shege agidana ba Zuwa zamuyi ta tattare kayanta tabar min Gidana tun ma kafin na waje suji a ɓatawa Gidana suna"
Safna da sajeeda se dariya suke Farha ƙasa tai da kanta Tana Jin Zuciyarta na wani Irin Buguwa tunda take bata taɓa ganin ƙasƙanci kamar wanda Ammi tai mata ba har suka ƙarasa Gidan Ammi tana cin zarafin farha A wannan karon ma Su safna Ne suka janyota har zuwa sashin ammi a falo suka zubar da ita ta dafe Gefen mararta tana rintse Ido ɗakinta Ammi ta shiga ta dinga jido kayanta tana watsa mata a jikinta.
"Ki tashi ki tafi matsiyaciya mazinaciya Kije Ki nemi uban Cikinki"
A wannan karon Mami ta kasa daurewa Kuka ta saka wiwi sabida yadda farha ta bata tausayi Ammi Masifa ta cigaba dayi wadda farha tai Shuru sabida kokawa take da Numfashinta.

"Nace ki tashi ki tafi Ba zaki ƙara zamar Min agida ba makira Mazinaciya Kije ki Nemi uban Cikin Jikinki.......
Cewar Ammi tana tsaye akan farha su safna na zaune suna dariya Mami tana Tsugunne a gaban farha tana kuka tana tattare mata kayanta.

Adaidai nan Ya shigo kamar an cillo shi Kuma lokacinne ammi takai maganarta ta ƙarshe wadda tace mata Kije ki nemi Uban cikin Jikinki.....

"Ammi Nine uban Cikin Kuma Fatima ba mazinaciya bace Nine Mijinta auren sunna mukai"
Daga Ammi har su safna Ƙamewa sukai Mami kuma ta Miƙe tsaye sadiƙ ya ƙame a jikin Ƙofar shigowa Aliyu gaban farha ya ƙarasa da sauri yana Kama hannunta bayan maganar ta gama fitowa daga bakinsa.
"Tashi fatima mu gani babu abin da sukai Miki ko?" Kura mai ido tayi lallai ɗan halak ne kuma yayi mata halacci se lokacin Kuka ya ƙwace mata Ta faɗa Jikinsa tana wani Irin Kuka kamar ranta ze Fita.

"Baba Kazo ka tasheni daga mafarkin da nake Cikin ka matarka duk ina me akai hakan Zaman dadiro Kuke da ita dama shine dalilin daya sa ka hana na sallameta baba sakamakon da zaka Min Kenan zina.........!"
Seta rushe da Kuka.
Da sauri ya saki farha Hankalin shi a Mugun tashe ya Nufi gaban Ammi wadda ta ɗaga mai hannu alamun bata buƙatar Ganin shi a gabanta.
Ya zube Dukkan gwiwowin sa a ƙasa ya kama hannunta ya rintse idanunsa.
"Ammi kada ki jefeni da kalma mafi Muni ga Mumuni ammi ban taɓa zina ba Kuma ba zanyi ta ba In sha Allah"
Tureshi tayi tare da bashi haɗaɗɗan Mari har Guda Biyu ta Miƙe a haukace.
"Ubanka kayi in ba zina ba dan ubanka a ina ka aure ta ban sani ba?"
Aliyu ya dafe Fuskarshi tare da cewa.
"Ƙaddara Ammi ƙaddara ce ta haɗani da ita wadda bana fatan na bayyana ta a gaban kowa Nabar ta tsakanina da ita sedai ƙaddarar mai Kyau ce Tunda ta kaimu ga yin auren Sunna Ammi in kina kokwanto ki Kira su Baba Usman sune suka karɓa Min auren fatima a wajan

mahaifinta Tare da cikakkun shedu da sadaki fatima matatace Cikin jikinta na wane Nina mata kuma nasan dashi Ammi Ki haƙuri na Ɓoye miki ne sabida bakya so na Yiwa mami kishiya Ni kuma ina Gudun ɓacin ranki Ammi"

Ya faɗa a wahale sabida yadda kanshi Ke sara mai.
Da baya ta dinga ja tana dafe kanta.
"Su Usman sun cuce ni Dasu ka haɗa baki Kuka cuce ni kaje kai aure ban sani ba Ka ɓoyewa kowa Na cancanta Da haka a gareka Baba ni zaka yaudara Baba ashe matarka ce To bari kaji wallahi se an zubar da Cikin nan kuma seka saketa"
Da sauri sadiƙ ya ƙaraso Duk hawaye ya Jiƙa masa Fuska kuma bana komai bane ba sena tausayin Aliyu.
"Ammi kada ki yanke Hukunci Cikin Fushi nina gamsu da Aliyu baze Mana ƙarya ba Allah yasa hakan alkairi ne a gare shi"
Ta bugawa sadiƙ tsawa.
"Matsa ka bani waje shasha sha Ni zai ranawa hankali to ya saketa kuma na  Kira salma tazo yanzunnan ta zubar da Cikinnan Tunda nasan ba asibitin da suke zubda Ciki sabida Doka ce"!!

Jada baya Aliyu ya dinga yi yana girgiza kansa.
"Ammi ina son matata babu dalilin da zesa na saketa Kuma Allah ma baya son saki duk da ba haram bane! Sannan Ammi in kika zubar mata da Ciki Wallahi Nima rasa ni zaki dan In kina ƙaunata To Kiso Cikin Jikin fatima nina ɗauka Murnar Cikin Jikinta zata Goge Dukkan wani ɓacin ranki au ashe ba haka bane........

"Dakata baba ni bana son wannan yarinyar ba kuma nason na haɗa zuri'a daga tsatsonta sabida haka koka bi zaɓi na Ko ɓacin rai ya Biyo baya wallahi"

Ammi ta faɗa cikin hargowa.

Farha ta dinga shafa Cikinta tana Kuka Jitai Tana masifar son abin da ke Cikin nata.

Aliyu a hankali ya Miƙe yabar falon yana tafe yana haɗa hanya Ammi ta janyo wayarta ta shiga Kiran salma ta bata Umarni akan tazo Cikin gaggawa Falon Shuru yayi ammi ta bar wajan Su safna Suka Nufi ɗakin su sadiƙ ya Juya ya fita mami da dafe bango Ta bar falon sabida har Lokacin mafarki take.

Falon yayi tsit se Sautin Kukan farha a hankali ya tako ya ƙaraso gabanta.
"Taso"
Ya faɗa babu walwala tashi tayi shikuma ya ɗauki Kayanta Suka fita daga falon Harabar Gidan tsit sabida Lokacin ana sallar la'asar Cikin wata Mota suka shiga da kanshi yaja Motar Har zuwa Bakin titi kafin ya ɗauko wayar shi ya kira Musa zaman Jiran Musa sukai wanda kusan Minti talatin yazo.

Aliyu ya Koma baya kusa da farha Musa yaja Motar tafiya sukai harta kusan awa se gasu a wata babbar tashar Motoci Kaduna Shine abin da kwandastan motar yake faɗa

Aliyu yace Musa ya Tsaya suka fita ya fito da kayan shi da nata Babbar Wayar shi Ya miƙawa Musa tare da cewa.
"Ka aje Min a wajan ka Wannan Kuma takardar ka kaiwa Ammi"
Daga haka ya kama farha Suka Shiga Cikin Motar dama Mutum Biyu ne suka rage yabar Musa a tsaye kamar an dasa shi yama rasa me zeyi sabida bai san Komai akai ba.
Da sanyin Jiki Musa yaja Motar zuwa gidan Aliyu kuma kamar yadda ya faɗa kai tsaye Musa sashin Ammi ya Nufa Lokacin salma ta ƙaraso duk hankalinta a tashe Kusan a tare ma suka shiga sashin ita da Musa Lokacin da suka shiga falon sadiƙ da Bashir suna tsaye se Ammi Dasu safna daga gani kamar magana suke sallama sukai suka shiga falon Musa ya rissuna ya miƙawa Ammi doguwar takardar da Aliyu ya bashi tare da cewa.
"Ammi gashi Inji yallaɓai yanzunan na kaishi tasha"
Har rige rigen Miƙa hannu sadiƙ da Bashir sukai wajan amsar takardar Jikin sadiƙ rawa yake a fili yake karanta saƙon da takardar ta Ƙunsa mai ɗauke da Rubutun Aliyu ajiki.

_Ammi ki yafe Min ko zamu gana ko ba zamu gana ba Ammi na zaɓi na nesanta kaina dake sabida matakin da Kika ɗauka akaina duk ba zan Iya ba Domin Ko a addini haka haramun ne saki halak ne amman Allah baya so Bare Ni fatima batai Min laifin da zan sake taba sannan Kuma in na yarda Kika zubar mata da ciki kamar nai Kisan kai ne bare ma Ni ina son cikina Tunda matata ce ta sunna amman In kina Musu Kije ki tambayi su kawu Ko Musa ma yasan Komai akai Ammi na Tafi duk Inda Allah ya nufa na zauna nai rayuwa na raini Cikin fatima na zauna da ita kamar yadda itama ta yarda dani ta zauna dani ta rabu da iyayenta akaina Na bar Muku komai nawa Ku riƙe Ni fatima da Cikinta sun fimin dukiya da Duk Jin daɗin rayuwa ina fatan Dukiyar dana bar Muku zata baku farin ciki kwatankwacin wanda Nake baku na barki lafiya Daga ɗanki Aliyu Kuma ina roƙon gafarar Ki in nai Miki ba daidai ba_ ...................
Autar manya ce marubuciyar......
*ƁOYAYYAR ƘAUNA*
*BA SON TA NAKE BA*
*ƊAN MAJALISSA*
*MURADIN ZUCIYA*
*ASHE ZUMA*
*TAURARO*
*KOBA SO*
*RABON WANI*
*FITAR RABO*
*DA IZZATA*
*BAƘON LAMARI*
*AUREN BARE*
*H A S K E*
*RABO YA RANTSE*

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 95*

"Innalillahi wa'innah ilaihirraju'un" Ita ce kalmar da sadiƙ yake ta ambata acikin bakin sa kuma da sauri haka zalika a bayyane yake furta kalmar gaba ɗaya Gumi ya jiƙa wa sadiƙ Rigar dake Jikinsa ga wani Wanda yake Kuma biyowa daga goshin sa zuwa fuskar shi Ita ko salma ƙafafunta kasa ɗaukarta sukai Seta zube a wajan tana ambatar Sunan Allah wani irin ɗaukewa numfashin Ammi yayi na wucin gadi wanda seda Bashir ya riƙota dan gaba ɗaya tai suman tsaye ko motsi ta kasa yi Babu abun da kake ji a cikin falon se sautin Fitar Kukan su Safna.

"Ammi kin cuce mu kin cuci kanki wannan wani irin son zuciya ne me Aliyu yayi miki haka? Ammi aduk cikin mu babu mai yi miki biyayyar da yake Miki Yau gashi kin wayi gari babu shi ko tausaya mai baki ba na halin da ya shiga Jiya ke idanunki sun rufe son zuciyarki kaɗai kike hangowa yau gashi kin buɗi idanu babu Aliyu Ya bar miki gidan da komai nashi Seki zuba ruwa a ƙasa ki sha sabida Murna"

Sadiƙ ne yayi wannan furuci cikin Fushi ya juya zebar falon Musa ya riƙo hannayen shi cikin ladabi Musa yace.
"Ranka ya daɗe a sassauta kalma mahaifiya ce in rai ya ɓaci hankali ke Nemo shi kuma kada ka fita dan Allah muyi zaman neman mafita Ba fushi ba ni ban san abin da yake faruwa ba wallahi da bazan bar yallaɓai yay tafiyar nan ba Kuma ko wayar shi bai tafi da ita ba ka ganta a hannuna"

Ammi ta zabura tana furta.
"Na shiga uku ni Aminatu na banu ina zan ganka Baba wallahi dukkan abin da na gaya maka ba har raina ba tsananin ɓacin ran auren da kai ne batare daka gaya Min ba amman in akwai abin da nafi so a duniya shine ɗan ka Baba"

Bashir ne yayi magana cikin haushi.
"In kina son shi mai yasa Kika kasa karɓar ƙaddarar shi mai yasa har kika furta zaki zubar masa da cikin matar shi har kika kira yaya salama haba Ammi duk Ɓoye ɓoyen da yaya Yayi sabida wa yayi?"

Kuka ammi take tana cewa.
"Ko giya na sha bazan iya zubar da Cikin taba ku fahimceni kurari nake masa har Kiran salama dana yi Kuma koda na shiga ɗaki bayan nayi wa salama waya wallahi Kuka nake Na farin cikin wannan ƙaruwa da Muka samu sannan na Jinjina girman rabo Lallai In RABO YA RANTSE se meshi kuma duk inda mai rabon yake se ya same shi har ga Allah naso mami ce ta sami ƙaruwa da baba amman ni Musulma ce nasan ƙaddara kuma nasan Cewa dukkan abin da Allah yayi ya tsara ya ƙaddara ba makawa seya tabbata wannan yarinya ita ce mai rabon Haihuwa da Aliyu......."

"Amman ammi kika tozarta ta kika wulaƙantata tun a hanya kike aibata ta Nai kukan rashin sani wallahi in da nasan matar yaya ce ba zan taɓa cin zarafin taba dan yaya yayi mana a rayuwa komai muka samu shine sila komai muka zama shine tsani ko kashi ya kawo mana wallahi zamu yaɓa ajikin mu sedai kash rashin sani ya kaimu ga yiwa baiwar Allah cin kashi agidannan raini cin zarafi Kaicon Mu"
Cewar safna tana wani irin kuka duk yadda Ammi taso fahimtar da yaran nata sun kasa fahimtar ta kowa ya ɗora laifin akanta a wannan Lokacin  ta kuma tabbatar da cewa kan ƴaƴanta a haɗe yake dan ko wanne acikin su kamar ze haɗiyi zuciya ya Mutu Salma da tunda tazo batai magana ba ita tace.
"Nice shedar cewa matar sa ce dan bai Ɓoye Mini komai ba koda Kuka tafi umara agidana ta zauna Babu kalar wahalar da bata sha a laulayi kuma koda yaushe hankalin sa yana kan matar shi dana zauna nai nazari sena gano cewa wannan aure nasu haɗin Allah ne wallahi nina san duk ranar da ammi tai ƙoƙarin raba shi da wannan yarinya akwai matsala dan mace akewa dole ba namiji ba, Ammi mai yasa idanunki suka rufe kika kasa karɓar ƙaddarar da Allah ya ƙaddarata cikin halak! yau da ace miki ya sami Ɗa ta hanyar zina da wannan yarinya ba farin ciki bane ace ta hanyar aure aka samu ba Ammi duk ɓoye Ɓoyen da yayi na auren shi gudun ɓacin ranki ne ni yasha gaya min cewa salama bana son ammi tasan nai aure sabida bata so salama har fargabar ranar da ammi zata san na ƙara aure nake kuma se Allah ya bashi yarinyar arziƙi wadda take son shi tsakani da Allah wadda take taya shi yi Miki biyayya dan wallahi yadda yake masifar son yarinyar nan wllahi idan irin ƴammatan wannan zamani ce da tuni Ta rabaku da tuni Ta bayyana ita wacece a gurin sa ƙarƙari base dai ki faɗan ki gama ba amman da yake tana da tarbiya ta kwantar da kai ta nuna ita ƴar aikin ce kamar yadda yace tana binki ammi tana bin ƴaƴanki ammi amman ammi seda kika jawo Aliyu yayi nisa dake Kuma ko nice abin da yayi hakan zanyi dan babu irin biyayyar da bai Miki ba wannan son zuciyarki ne Kika so ki aiwatar masa shi kuma haƙurin sa ya ƙare Kinga yanzu ya ɗauke matarsa sun Gudu batare da ya gaya miki kalma marar daɗi ba zeje yayi rayuwar shi ba tare damu ba ze zauna a tsakanin ƴaƴan shi da matar shi Ko zamu gana ko ba zamu gana ba Allahu masanin gaibu"

Da kuka salma takai ƙarshen maganar kafin bashir yace.
"Ammi ke mahaifiyar muce wallahi ammi baki kyauta ba Kuma ina son kawai ki karɓi laifin ki Kuma kiyi nadama wallahi ammi naso yarinyar nan kamar zan Mutu kuma yaya ya gano ina son ta amman bai taɓa nunan cewa Matar sa bace Kuma bai yarda ya sami matsala dani akanta ba seya dinga Nisantani da garinnan wannan Ne silar daya Ce sena zauna a abuja dana dawo yace na tafi lagos da kaina na zauna nai karatun Ɓoyayyar alaƙar dake tsakanin wannan yarinyar da yaya tun daga nan Kuma na fara yakice ta araina domin wata Fuskar tafi gaban mari Kuma ana barin halak dan Kunya cewar bahaushe, maganar gaskiya ammi nadama da gyara abin da ya ɓaci zaki bawai Kita maganar cewa kina so ko bakya so ba domin duk wannan ya wuce Sedai Mu san abin yi wani mataki zamu ɗauka akan wannan matsala ni babban tashin hankalina ma shine kada ƴan Cikin gida suji wannan labari"

Bashir ya faɗa yana share hawayen sa Ammi a raunane tace "Naji bashir wallahi nai nadama ni kaɗai nasan me nake Ji acikin zuciyata Sajeeda bani ruwa bani ruwa na sha" Ta faɗa cikin kuka

tana Jan Numfashi da ƙyar sadiƙ ya Miƙo mata ruwan tasha Musa ya gyara Murya shima duk ya karaya Muryarshi ta sauya kamar zeyi Kukan Cikin Sanyin Murya yace.

"Wato ita ƙaddara haka take tana faruwa ne ga bawa batare daya shirya mata ba Kuma batare daya san zuwan taba Da aure da Mutuwa da sauran dukkan jarabawar da Allah ze saukar wa bawan sa yana saukar wane kai tsaye batare da bawa yasan Lokacin faruwar hakan ba sedai kawai yaji shi acikin wannan yanayin to kamar haka ne ta faru a tsakanin auren Aliyu da fatima Nine sheda Kuma dukkan wanda ze bada shaidar wannan aure bayan Nine seko waliyan sa shaƙiƙan sa dangin mahaifin sa dan bana zaton ko mai Gida sadiƙ ya gayawa sabida yadda abun yazo a ƙurarren Lokaci nine na bincika masa komai na wannan yarinya Kuma nine nasan komai daya danganci ita yarinyar tunda niya ɗora akan Bincikar wacece ita wanda Alhamdulillahi ta fito a cikin zuri'a mai kyawun tushe da asali duk da bama su wadata bane iyayenta amman mahaifinta Mutum ne kaifi ɗaya mai gaskiya da riƙon amana ina fatan Allah yasa Ko bayan bayyanar su ne kada waɗannan Maganganu da kalubalen da wannan yarinya ta shiga agidannan yaje Kunnen mahaifinta dan tabbas ze iya raba auren su dan ba ason ranshi ma akai auren nan ba hasalima  ita akwai wanda take so akwai wanda aka tsaida maganar auren su dashi To wannan Rabon shine yay ɗawainiya dasu dukkan su har Allah ya tsara auren Nasu Fatima ƴar jarida ce Dan ataƙaice ma daga kanta mahaifinta ya soma barin ƴaƴan shi mata su cigaba da karatun Boko domin dukkan yayinta daga sun taso yake aurar dasu don mahaifinta Mutum ne mai yawan zuri'a sun haura su Ashirin ƴaƴan babanta Kuma duk yadda kuke Ji da haɗin kai wallahi sun fiku dan ina mai rantsuwa da Allah inda sun san halin da take ciki agidannan da tuni maganar rabuwar Aliyu da ita ta tabbata Tuni har anyi an gama.................
Sabida mahaifinta babu ruwan shi da Kuɗin suruki in kuna jin ana maganar dattijo to wannan Mutumin dattijo ne na asali mutum ne mai dattako da Gudun duniya kaifi ɗaya mai magana ɗaya! In zaku tuna kwanakin baya akwai wani ƙazafi da akaiwa Aliyu a gidan wata radio! to wannan labari ita fatima ita ce ta jagoranci yaɗa shi sabida yadda mai gidan radi'on yayi mata Kurarin ze koreta in bata yaɗa labarin ba ita Kuma lokacin ana gabda sanya ranar Bikinta tana Buƙatar abin da zatai don hidimar Bikinta sannan mafi ƙarfin yaɗa labarin akwai rashin sanin Illar hakan a hukunce da kuma doka kasancewar ta farin Shiga a wannan harkar Bayan labarin ya bazu Aliyu ya sakani na nemo masa shugaban wannan tasha wanda har takai su gayin shari'a sedai abin da ya bani mamaki Daya ce na nemo masa yarinyar datai labarin amaimakon yaje mata da sigar Ɗaukar doka akanta a,a se yaje mata da sigar Soyayya nidai a yadda yace Min ze aure ta ne dan ya Ƙuntata mata kamar yadda tai jagoranci wajan ɓata masa suna acikin al'umma sedai Shi Allah yadda kake zaton shi ya wuce nan Allah bai ƙaddara hakan ba seya ƙaddara soyayyar gaske azuciyar Aliyu akan wannan yarinya wadda Lokacin da yaje mata akwai ɗan abokin mahaifinta wanda yake sonta yake mata hidima wanda akai magana da mahaifinta da nasa akan Ze kawo mata Kuɗin aure sedai zuwan Aliyu wajanta ya tarwatsa wannan magana yarinyar ta kafe ita se dai Aliyu Abin da ze baku mamaki yadda bata san Ko shi waye ba amman ta kafe tace ita shi zata aura wanda hakan ne ya fusata mahaifinta har yace wa Aliyu koya turo ya ɗaura Musu aure koya bada ita sadaka wannan tasa a daren Aliyu ya je ga ƙannen mahaifin sa washe gari suka amsar mai auren fatima a wajan mahaifinta wanda Ni ma ina cikin shedun wannan ɗaurin aure nasu Kuma nina ɗauko ta daga gidan su na

kawo ta nan bayan Mun Ƙulla cewa Nace ƙanwata ce zatai Miki aiki mata da Miji se Allah kinga ashe har ta samu Ciki ba tare da wani ya sani ba sabida haka Ammi haƙuri zaki ki ɗauki wannan ƙaddara dan mai kyau ce Da Allah yasa akai auren sannan aka samu Cikin Inda a waje aka same shifa ita Kuma wadda kike son ta haihu da ɗan naki Allah bai yarda ta haihu dashi ba har yanzu Kinga rabon fatima ne a gaba kafin na matar tasa sannan maganar da Kike wai abin da Kike tsoro kada ya auro matar da zata rabaku kinga fatima ta ciri tuta kenan tunda har ta iya zaman watanni agidannan tana Miki biyayya dan ba da ban wannan matsala ba da Babu abin da ze faru a tsakaninku da ita Sabida haka wannan ma Izna ce ga wasu iyayen masu takura da sa ido akan sha'anin ƴaƴan su kin ga gashi nan yayi auren Ba tare da sanin ki ba Kuma kina tare da Ita a gida ɗaya har ta sami Ciki duk Allah ya rufe Miki ido ni a ganina ko wannan ma ta ishi ki bar bayin Allah'n nan su sami ƴancin kansu ki rabu dasu dan da ai bayan ranki gwara ayi kina raye ina fatan waɗannan maganganu nawa basu ɓata Miki rai ba kuma zaki saka su acikin Kundin nazari ki ƙara fahimtar cewa idan Allah ya baka babu mai hanaka in Allah ya hanaka babu mai baka Kuma Koda Allah yasa sun dawo gare mu ki gyara laifukan ki ta hanyar so tattali da kyautata wa fatima wannan shine abin da zaki dan ki wanke kanki a wajan Aliyu"

Musa yakai maganar Cikin Nutsuwa Falon tsit yayi kowa ya cika da wannan abun mamaki na auren Aliyu da fatima lallai RABO YA RANTSE se meshi wannan rabo shine silar auren su wanda Allah ya rufe idanun duk wani wanda ze kawo musu cikas akan auren su har seda rabon ya shiga sannan Allah ya bayyana da kansa...

Sautin kukan Ammi ne ya cika falon.

Autar manya ce marubuciyar......
*ƁOYAYYAR KAUNA*
*BA SON TA NAKE BA*
*ƊAN MAJALISSA*
*MURADIN ZUCIYA*
*ASHE ZUMA*
*TAURARO*
*KOBA SO*
*RABON WANI*
*FITAR RABO*
*DA IZZATA*
*BAƘON LAMARI*
*AUREN BARE*
*H A S K E*
*ZUMA A BAKI*
*BAƘAR FATA*
*RABO YA RANTSE*
*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya

09022260850*
*A LOVE STORY 96*
Rabo Ya Rantse
Arewabooks autarmanya

"Sadiƙ bani ruwa mai sanyi na sha Bashir ƙaro Mini ƙarfin Ac innalillahi wa'innah ilaihirraju'un Ya Allah ka farkar dani daga Baccin da nake yi Ni Amina na shiga Uku Mai yakai ni ga shiga Hurumin Ubangiji gashi nan tun kafin aje ko ina ya nunan niba komai bace"
Ammi ta faɗa lokacin sadiƙ ya kuma kawo mata ruwan Bashir ya ƙaro mata ƙarfin Ac Amman gaba ɗaya Jikinta zufa yake Se rawa hannun data riƙe Gorar ruwan yake seda ta shanye ruwan tas sannan ta sunkuyar da kanta a ƙasa ta Kuma fashewa da kuka!
"Tabbas Hurumin Ubangiji na shiga domin Shine ya haɗa waɗannan yara kuma shine yay Nufin bawa auren su kariya Kuma shine yay Nufin sanya Rabon haihuwa a tsakanin su Amman ni da ƙarfina da tasiri na a matsayina na Uwa naso na jijjige auren sedai Allah ya nunan Auren nashi ne ba nawa Ba haƙiƙa bani da ƙarfi bani da wayo ko dubara ya Allah ka yafen Nayi laifi Kuma zan gyara dukkan Kura kurai na"
Ammi ta faɗa Bashir yayi saurin cewa.
"Zuwa yaushe zaki gyara Ammi bayan kin bar kari tun ranar tubani Kin riga kin sa har ya tsallake ya tafi wanda bamu san wace duniyar ya tafi ba sannan Kin jefa zargin ba shi muke soba dukiyar shi muke so tunda gashi nan har yana furta yabar mana dukiyar shi Matar sa da ƴaƴan sa sun fiye masa dukiyar daya tara Ammi Tun asali wannan tunanin ya dace Ki soma kafin ki zartar da Hukunci Amman se idanun ki suka rufe wa ganin daidai da aiki dashi gashi yanzu Kin rasa ɗa ɗaya tamkar da dubu dan wallahi Yaya Aliyu ɗane guda ɗaya tak! a gareki amman abin da yake Miki zaki tara ƴaƴa dubu basuyi miki ba Duk wata fankama da Muke da bazar wa Muke in ba tasa ba tun kafin yakai haka ya hana hawayen mu ya zuba ƙasa da sunan na maraici Yake taimakon mu Ammi bazan manta ba In Yaya yaga ranki ya ɓaci Kuka yake Miki Baya barin wajan da kike har se Yaga kin sami Nutsuwa Kin dena Fushi dashi ai kamata yayi Daga Lokacin daya Nuna yarinyar nan matar shice zaki zubar da makaman yaƙin ki kija ta ajiki Ki rungume ta ki nuna mata ƙauna da soyayya da Kulawa Lokacin ne zesan Shima yana da uwa mai farin cikin samun Ƙaruwar shi gaskiya Ammi baki kyauta ba amman inna miki ba daidai ba a magana ta Ki yafe Min dan ke uwa ce a gare ni"

Bashir ya faɗa yana share hawayen shi!

"Ban ji haushin kaba Bashir Don Dukkan maganganun ka gaskiya ne Kuma suna bisa kan tsari na gaskiya sedai nayi Kuskure kuma babu wanda baya kuskure naso ace mami ce ta soma haihuwa da Baba ada sabida ina zaton Duk wadda ze auro ba zata Min Biyayya kamar ƴar da ƴar uwata ta haifa ba sedai tashin farko na gane ita ma waccan yarinyar mai Biyayyar ce don babu wadda zatai abin da tayi Mini Naci mata Mutuncin Yaƴana suyi mata amman Ko a fuska bata taɓa Nuna tana da alaƙa da Baba ba Ya Allah nasan nayi laifi Ina neman yafiya da gafarar ka sannan ya Allah ka kare Min Baba da matar shi aduk inda ya sami kan shi aduk inda ya ke Kada kasa hawaye da kukan da nake akan shi su zame masa masifa danni Uwa ce Kuma babu daɗi hawayen uwa akan ɗanta Ni nasan Baba ze dawo gare ni yayi ƙaurar zuci ne kawai

amman kaf duniya baba bai haɗa soyayyata data kowa ba In ka cire Allah da Annabi ( s.a.w ) Baba bai da sama dani seko mahaifin sa Ko wannan matar tashi wallahi ba fina tai a wajan saba Bai kuma fi son ta akaina ba Kawai ɓacin rai ne tare da ɗaukin Cikin Jikinta amman Nina san Baba soyayyarshi ɗaya ce tana gare Ni sedai hurumi da matakin Soyayyar matar shi da ɗan shima daban aran shi"
Ammi takai maganar.
"Ammi ki dena wannan kukan ya isa haka addu'a zamu tsanan ta akan Allah ya dawo mana dashi sannan kada ki saka damuwa aran ki Kinga kema lafiya bata wadace kiba"
Cewar salama Ammi ta kuma Goge hawayen daya ƙi dena zubo mata tare da cewa.
"Salama kuka ai ya zama Dole wato ajiya faɗuwar da Baba yayi wallahi bana Ko Tantama akan Abun da nai wa yarinyar ne ɓacin rai yasa ya yanke Jiki ya faɗi salama ke baki san halin da muka shiga ba Baba fa a asibiti ya kwana Numfashin sa ya ɗauke Jinin sa yahau zuciyar shi ta Bugu Amman mai yasa ban duba halin da yake ciki ba nai sanadin ɓacin ran shi ya tafi da ciwo Ga matar tashi naga ƙaramar yarinya ce Tsorona da fargaba na kada ciwon nan ya kuma kada shi a gurin da ba Kowa nasa Ga matar sa ba wata wayayya bace ba Innalillahi wa'innah Ilaihirraju'un"
Ammi ta faɗa hankalin ta a tashe dan se yanzu ma wannan tunanin yazo mata a zuciyar ta.

Salma ta kaɗu da jin wannan furuci na Ammi dan bata da labarin ciwon Aliyu.
"Musa zaka ƙara tsayawa kai da fata fiye da yadda kake ada zamu ƙara haɓɓaka Dukiyar Aliyu da ƙarfin ikon Allah zamu tabbatar da ribar da ze samu yanzu tafi wadda yake samu Ada! sannan zamu toshe dukkan wata hanya da mutane zasu San baya tare damu Zamu Je gidan mai girma gwamna da kanmu tare da Bada Uzirin Saƙo daga Aliyu cewa yaɗan ɗauki Hutu Ya tafi London Dan ya Huta acan wanda In mukai haka ina ganin zamu toshe Duk wata hanya da mutane zasu san abun da yake faruwa sabida Sunan shi ya riga yayi fice muddin Muka bar maganar nan ta fita akwai matsala Bashir bana son naji wannan magana ta fita ka kula ko Cikin Gidan su Baba bana son kowa yaji mu kuma zamuyi addu'a zamu saka ayi masa Akan Allah ya Juyo mana da hankalin sa Gida dan Aliyu shine garkuwar Mu Kuma in sha Allah zamu tsare masa martabar sa da Mutuncin sa yadda ya tafi yabar Dukiyar shi haka ze dawo ya sameta Zamu tabbatar da ƙarfin Zumunci Zamu tabbatar damu zumuncin Mu ba irin na wannan zamani bane daga yau dukkan abincin da Komai da ake a wannan Gida da Kuɗin Aliyu nina soke za'a dinga fitarwa daga aljihunmu nida Bashir har sanda Allah ze Bayyana mana shi ba zamu taɓa mai kwandalar shiba Bashir zaka zauna A Abuja Musa Kana kano Ni kuma Ina lagos zamu tsaya da ƙarfin Ikon Allah"
Sadiƙ yakai maganar Cike da ƙarfin gwiwa dana zuciya Sajeeda tace.
"To Amman yaya sadiƙ kasan fa Yaya Aliyu ba iya gidannan yake ciyarwa ba harda Cikin Gida da sauran Al'umma da yake bawa taimako sannan yanayin yadda Aunty Mami ta fita baka tunanin zata gayawa mahaifiyarta baka tunanin maganar zata fita?"
Sadiƙ ya kalli sajeeda.

Kafin yayi magana Musa yay saurin cewa.
"Nima nasan wasu gidajen da yake kaiwa kayan abinci daga ciki harda Gidan surukan shi Ni na ɗauki wannan nauyi nima da aljihuna zan ke tura Musu da kayan abinci kyauta kamar yadda

yake basu batare dana bari sun san halin da ake Ciki ba Dan Ni kam yanzu Alhamdulillahi Nima ina da Kuɗin dazan Iya tsayawa da ƙafata dan Mai gida Aliyu Bangon sukari ne dukkan wanda ya raɓe shi seya sha zaƙi dan bayan albashina yana Min kyauta wadda take sani nai ƙaramin suma wadda Nima da Ita nake Riƙe iyalina nake ɗaukar Nauyin Ƴan uwana Alhamdulillahi Nima na ɗauke wannan nauyi"

Bashir yace.
"Tun da bani da nauyi Akaina ni zan ke aikawa da cikin Gida kayan abincin kamar yadda yake basu in sha Allah" Ammi tace.
"Ni kuma musa a gayawa masu gadi duk sanda wani yazo Neman taimako a kirani zan Fito na bayar Sannan acewa ma'aikatan Gidannan tafiya ce ta kama shi zuwa London sabida kar suga Ya shafe Lokuta baya nan duk da yana tafiye tafiye amman wannan bamu san ranar dawowar shiba se Allah"

Salma ta numfasa tare da cewa.
"Ni kuma zan ɗauke nauyin biyan ma'aikata albashi In sha Allah tare da Hidimar makarantar su Sajeeda kafin Allah ya bayyana shi Allah ya rufa mana asiri ya ƙara mana zumunci"

Sadiƙ da bai ce komai ba shine yayi magana.
"Sajeeda maganar Mami ki barta yanzu bama tada Nutsuwar Yaɗa maganar ga wani sabida ɗayan Biyu ne Ko dai tana cikin damuwar Mijinta Ko tana cikin damuwar Kishiyar dayay mata Koda ta gayawa mahaifiyarta ma Ba zasu so maganar ta fita ba mafita zasu Nema Ko sakina data dawo Zan kaɗata zuwa Jibi Muyi lagos bama zan bata damar sake wata Fitar ba In sha Allah ina tabbatar Miki da se asirin maganar nan ya rufu babu mai Jinta a waje sannan Ku tuna da wani abu kada kuga Mun ɗauke dukkan Hidimar da Aliyu yake ku ɗauka cewa yanzu Muma mun taka da ƙafarmu zamuyi abin da yake yi to fa ku tuna gaba ɗaya da bazar sa muke rawa Domin dukkan kuɗin da zamuyi amfani dasu Daga wajan sa zasu Fito dan albashin mu da dukiyar da muke da Ita duk a tare dashi Muka samu Ilimin da Muke aiki dashi Shine ya ɗauki nauyin sa Haka kema salma Albashin da Kike ɗauka da kasuwancin da Kike Dukkan su da bazar Aliyu Kike rawa dan shine ya tsaya Miki akai dan haka addu'a zamu cigaba dayi masa Allah ya bayyana mana shi Cikin Ƙoshin lafiya"

Sadiƙ yakai maganar Cikin Nutsuwa

"Haƙiƙa Kun cika ƴaƴan Halak Allah ya saka Muku da alkairi Allah ya ƙara haɗa kanku Allah ya bayyana Mini ɗan uwan ku"
Ammi ta faɗa Lokacin ana kiran magariba Kowa ya tashi ya Nufi masallaci Su Kuma sallah sukai agidan Har akai Isha'i salma tana tare da Ammi tana kwantar mata da hankalinta.
Musa ne ya shigo falon bayan sallar isha'i dan har Lokacin bai tafi ba Yazo dan yayi wa Ammi sallama.
Ammi ta dubi Musa.
"Musa in ban takura maka ba dan Allah ka kaini Gidan surukan Baba nida salama Tunda bata zo da Mota ba In mun dawo ka ajeni seka wuce da ita Gidan ta"

Musa yace.
"To babu damuwa"
A ladabce.

Ammi ta shirya bayan ta Zuzzuba kayan arziƙi acikin ƙatuwar Leda Salama ta ɗauka suka Fita sajeeda ta yafa mayafin abaya akan ta tabi bayan su safna wayar da suke da Kamal sam bata san fitar su Ammi ba.

Harabar Gidan suka Nufa suka shiga Cikin mota Musa yaja Motar suka fita kai tsaye Gidan su farha suka Tafi a bakin layin Musa yayi parking shine yayi wa su Ammi jagora har Ƙofar Gidan sannan ya koma Mota ya zauna Jiran su Fito su Koma gida.

Gate ɗin suka tura suka shiga gidan ko ina hasken farin ƙwan sola ya haske Gidan, Suka shiga Ƙofar Babban falo wanda ilahirin Mutan gidan ke zaune wasu na kallo wasu na cin abinci Salma tai sallama Babar su Hadiza ta amsa tana cewa.
"Maraba lale Ku shigo mana Ku zauna"
Duk su Ruƙayya suka zubowa su Ammi ido suna kallon ƴan gayu akan Kujera su Ammi suka zauna suna gaisawa da Babar su Ruƙayya da Babarsu Hadiza.
Shuru ne ya biyo baya kafin salma tace.
"Yawwa dan Allah Munzo wajan Maman Farhan ne Ko tana nan?"
Da sauri Babar su Hadiza tace.
"Eh tana ciki Bata fiya fitowa waje bane"
Su Ammi basu saurare taba suka Miƙe Babar su Ruƙayya tai Musu jagoranci har zuwa ɗakin Umma.

A ƙaramin falon Umma wanda yasha ƴan madaidai tan Kujeru daidai shi tare da ƙaramar TV'n jikin Bango su Ammi suka zauna Ikram dake zaune tana Cin Tuwo jin sallama da zaman Mutane a falon Yasa ta ɗago tana kallon su.
Kafin tace musu.
"Sannun ku da zuwa ina yinin ku"
Ammi ta zubawa Ikram idanu.
"Lafiya lau ƴammata Ina mamanki?"
Cewar Ammi har Lokacin tana kallon Ikram Kyan yarinyar yana fusgarta wato ita matar Baba Ita ce baƙa a gidan tunda ta lura duk ƴan matan falon farko farare ne masu Jiki kyawawa ma sha Allah.
Ashe ba Ammi ce kaɗai ta shiga mamakin ba har su salma da suka saki baki Tun farkon Shigowar su suna kallon kyan ƴaƴan Gidan So Ma sha Allah!
Ikram ta miƙe ta shiga ɗaki domin Kiran Umma dan Babar su Ruƙayya tun da ta rako su Ammi ta fita daga ɗakin don ta basu Guri.

Ikram ta shiga cikin ɗakin Umma wadda take zaune a saman darduma hannun ta ɗauke da carbi mai Dubu tana jan shi...........Autar manya ce marubuciyar......

*ƁOYAYYAR ƘAUNA*
*BA SON TA NAKE BA*
*ƊAN MAJALISSA*
*MURADIN ZUCIYA*
*ASHE ZUMA*
*TAURARO*
*KOBA SO*
*RABON WANI*
*FITAR RABO*
*DA IZZATA*
*BAƘON LAMARI*
*AUREN BARE*
*H A S K E*
*ZUMA A BAKI*
*BAƘAR FATA*
*RABO YA RANTSE*

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

AUTAR MANYA
Arewabooks autarmanya

*A LOVE STORY 97*
Rabo ya rantse

A gefen gado ta zauna tana jiran Umma ta shafa zaman Kusan Minti Goma tayi kafin Umma ta ƙarasa lazumin ta shafa tana kallon Ikram.
"Har kin gama cin tuwon kenan amman dai ba bacci zaki ba Ko kin san akwai Guga a gaban ki gaba ɗaya kayan ki babu guga"
Ikram tace.
"Ehh umma ba kwanciya zanyi ba baƙi Kikai suna falo suna Jiran ki"
Umma tahau salati tare da cewa.
"Amman anyi sakaran yarinya salon suce na wulaƙanta su shine baki gaya Mini ba su waye?"
Ikram tai dariya tare da cewa.
"Wallahi ban san suba Nima Umma kina lazumi se kawai na katse Miki Kefa kika hanamu Yi miki surutu In kina lazumin Ki"
Umma ta naɗe abin sallah tare da kama hanyar Fita tana ƙara yiwa Ikram faɗa akan mai yasa bata gaya mata ba Har ta ƙarasa fita falon da far'arta da komai.
"Ah maraban ku lale marhaba sannun ku Da zuwa dan Allah Kuyi haƙuri Wai Ikram data tarar ina lazumi shine bata gaya Mini nai baƙi ba"

Ammi da far'arta itama tace.
"Ai ta kyauta sosai Koni bana bari sumin magana In Ina lazumi sabida ɓata nake yi"
Umma tai dariya tana fita daga falon Babban falo taje ta Buɗe Fridge ta ɗauko Ruwa da lemo ta zubo a tray ta Nufo ƙaramin falon sabida yanzu Alhamdulillahi Tunda Aliyu ya Buɗewa kawu ƙaton shago wanda yake sayar da kayan masarufi Shikenan Suka ƙara wadata dan babu abin da kawu baya dire Musu gana Aliyu duk ƙarshen wata gana su Halifa duka shiyasa gidan sedai Godiyar Allah.
Umma da sallama ta shigo falon ta aje Musu ruwa da Lemon sannan ta Kuma fita ta ɗebo Cincin a plate ta kawo Musu.
Zama tayi a ƙasan carpet tare da cewa.
"Ikram zoki kawo Musu tuwo Ki duba sama ɗakin su Halifa Ki ɗauko Babban Fulas ɗin tuwon yana can ɗazu aka kai Musu" da yake ranar Girkin Umma ne.
Ammi data saki baki tana kallon karamcin matar tun kafin tasan daga ina suke su waye su Ammi take haba haba dasu Se wata Kunya ta kama Ammi yanzu wannan mata mai Kirki da mutunta ɗan adam ita ce ta haifi ƴar da ɗanta ya aura Amman ta kasa Riƙe Yar da daraja Lallai Aliyu ya auro ƴar Mutunci dan ba tarin Dukiya ake bi a aure ba ka auro ƴar Daraja ƴar Gidan Girma da tarbiya shine kayi aure.

Kafin kace me Ikram ta fita se gata da kwanukan tuwo da Miya ta aje Musu Umma tace.
"To dan Allah Kuci mana Duk da ban sheda kuba Amman ai baƙo daraja gare shi"
Saboda Umma ba wayewa tai da Aliyu ba shiyasa bata gane suba Amman in da tasan shi sosai data kalli salma taga Aliyu don suna kama sosai Haka zalika Ammi to da yake bawai kallon shi Umma tai ba shiyasa sam bata gane su Ammi ba.
Sajeeda ta ɗauki ruwa salama ta ɗauki Lemo Ammi kam bata ɗauki Komai ba se Murmushi take kawai tana Hamdala a zuciyarta.

"To Nidai sunana Hajiya Amina amman ana ce Min Ammi mahaifiyar Aliyu Mijin fatima dama Mun zone domin Mu sada zumunci waɗannan Duka ƙannen shine su basa nan sun ɗanyi ƴar tafiya"
Ammi ta faɗa Cikin Nutsuwa Se Umma ta Kuma washe baki Cikin farin ciki tana cewa.
"Kai Ma sha Allah abu yayi daɗi sannunku sannunku mungode Mungode Allah yasa ka muku da alkairi Muna ta ganin hidima daga wajan Aliyu Amman Farha ce har yau bata zoba"
Umma ta ƙarasa faɗa Cikin rauni.
"Kallo ɗaya ammi tai mata tasan Tabbas rashin ɗiyarta yana susar ranta"
Ammi ta dafa kafaɗar Umma.
"Ki haƙuri Maman fatima ƴarki tayi dacen Miji ba danni na haifi abuna ba a,a wannan magana ce ta gaskiya nake Yi Miki ita Ki Godewa Allah Surukin ki ɗan albarkana ne Kinji Ki kwantar da hankalin naji duk yadda auren su ya kasance wanda Maƙasudin auren nasu zazzafan rabo Ne don yanzu haka fatiman ki nada ciki har na wata Uku"
Umma setai ƙasa da kanta sega hawaye nan Ammi bata hanata Kukan ba dan daga Umma har Ikram Kuka suka saka wiwi Umma har tana ajiyar zuciya kafin Salma ta soma rarrashin Umma.
Cikin haka kawu ya ɗaga labule yana cewa.
"Asiya zo mana ga kaji nan na kawo ki gyara su Gobe Musha dabge a gidannan Asiya kina

ina......"maganar kawu ta tsaya sanda yaga baƙi a zaune a falon Ga kuma Umma tana share hawaye a ruɗe yake magana.
"Asiya Ke Ikram Kukan me kuke wani abun akai Muku?"
Duk ya faɗa a ruɗe Su Ammi ne suka katse masa tambayar wajan gaishe dashi A mutunce suka gaisa da kawu kafin Umma tace Muryarta a shaƙe.
"Surukar mu ce tazo Babar Mijin Farha"
Se kawu ya zauna ana sabunta gaisuwa.
Ammi na dariya tace.
"Wai fa daga Munce mata Fatima nada Ciki shine take wannan Kukan"
Kawu ya fara tafa hannu yana cewa.
"Ai halin Asiya se ita wallahi Koda yaushe haka nake fama da ita taƙi kwantar da hankalin ta akan auren nan na fatima Kuma na gaya mata dama wani alkairin baya samuwa seda ƙalubale ni kaina na shiga damuwar data kaini ga kwanciyar asibiti bayan dana bawa Ali fatima batare dana san ko shi waye bane sabida zuciyar danai na bijire Min datai akan umarnina na wanda na bata tace Ita Ali take so to daga ƙarshe daya zo nan Ya gaishe ni wallahi se naji na yarda dashi Amman Asiya ita taƙi sakin hankalinta Kullum tunani Kullum Kuka sabida jarabar son da ta ɗauka ta Ɗorawa Fatima kamar ita kaɗai ta haifa a duniya"

Ammi dariya ta saki Sajeeda da Salma ƙasa sukai da kansu Suna dariyar Dramar Kawu lallai mahaifan fatima ba ƙaramin Son ta suke Yi ba.

Ammi ce tace.
"Lallai dole na bawa Fatima kyauta wato akan Babana tai yaƙi ba ɗan kaɗan ba lallai fatima ƴar soce yadda Mamanta ke son ta Nima haka nake Son Baba kaf yarana yafi damuwa dani baya son damuwa ta Allah de yayi Musu albarka bai ɗayan su"
Se kuma aka shiga hira yadda Kawu yake hira da Ammi kai kace sun jima da sanin Junan su, Dan Ammi batai wata alkunya ba sosai ta sake suna hirar su da kawu kafin Umma tasa Ikram ta Kira matan gidan ta gabatar Musu Da Ammi a matsayin uwar Mijin farha wadda nan suma suka zauna suka gaisa dasu Ammi kafin su tashi subar wajan.

Ya Nura ne ya shigo ɗakin Umma yana kiran Ikram ta zuba mai Miya tunda ya shigo sajeeda ta zuba masa ido gabanta yana faɗuwa ta Lumshe ido har wata iska ke kaɗata sabida ganin Nura matashin saurayi fari ɗan dumurmur mai Jini a jika.
"Nura ga Mahaifiyar Mijin farha Ku gaisa" cewar Umma Ya Nura ya tsugunna ya gaishe da Ammi kana ya tashi ya Fita dama shi bamai hayaniya bane ba Kuma ba laifi yana ganin ƙimar Umma sosai.

Har Kusan Goman dare Ammi tana Gidan su Farha kafin ta direwa Umma ledar data zo mata da Ita sukai sallama Suka baro Gidan Aikuwa gaba ɗaya Yara da Manya A gidan suka rako Su Ammi har wajan Mota harda kawu wanda yake tayi wa Ammi godiya yana cewa a gaishe da sauran Na gida haka suka rabu Gaba ɗayan su cike da ɗaukin Juna Kowa na gidan su farha ya yaba da Mutuncin Ammi musamman yadda ta saki Jiki tasha Hirarta sosai ta zama Mutuniyar Kawu.

Ko a mota su Ammi labarin karamcin mahaifan Farha suke yi Musa yana Jin su yana ta Murmushi ya sauke Ammi da Sajeeda wadda gaba ɗaya Jikinta ya Mutu tunda taga Ya Nura shikenan taji kaf duniya bata da namijin data ke masifar so in ba shiba soyayyar shi Bugu ɗaya tayi mata Mugun kamu Ita babu ruwanta da Talaka ne shi kawai Nutsuwar shi da kamalar shine yayi mata Hmm anya sajeeda Kin gano Gidan shiga Kuwa Babar su Hadiza mahaifiyar Nura mace ƴar bala'i bare yadda ta ɗauki so ta ɗorawa Nura sabida shine Babba a ƴaƴan ta Maza!

Koda suka shiga gida ma falon Ammi babu kowa Ammi ɗaki ta shige tana Jin kamar ta sauke wani babban nauyi akan ta wannan ziyarar data Je wa surukanta masu Kirki da Mutunta ɗan adam Alwala ta ɗaura Zama tayi tana addu'a seda ta raba dare tana sallah tana wa Aliyu addu'a dan se wajan Asubahi Bacci ya ɗauketa a saman abun sallah Kuma zuciyarta  ta ɗan rage damuwar Rashin sa sabida zafin addu'ar da take yi akan lamarin.

*****************

Tunda suka shiga mota farha ta Jingina kanta da Jikin kafaɗar Aliyu tana tunanin ina ze kaisu Dama yana da ƴan uwa ko gida a kaduna ne Ita kam bata taɓa zuwa kaduna ba shiyasa gaba ɗaya tafiyar ta dame ta gaba ɗaya Jinta take a takure ga Fitsarin daya riƙe mata mara ga Ƙafarta duk ta dame ta sedai yadda take ganin shi a cikin damuwa mai tsanani ba zata iya gaya masa damuwarta ko guda ɗaya ba.
Shima a nashi ɓarin nazari yake akan jahar ta kaduna wadda bai da abokan mu'amala acikin ta wannan tasa ya zaɓeta a matsayin jahar dayay balaguro zuwa cikinta wadda yake fatan yayi rayuwa tare da fatima acikin Jahar kafin Allah ya kawo masa mafita sabida tunda ya baro Gida babu Fuskar wadda yake hangowa seta Amminsa Yasan tana cikin tashin hankali ba ɗan kaɗan ba se Kuma Mami wadda yasan ya tauye mata haƙƙinta tunda har yanzu matar shice akwai nauyin ta akan shi yasan bai kyauta ba ta wannan ɓarin sedai tafiyar tashi kamar Dole ce dan yana tsoron abin da Ammi zata zartar dan uwa ce baze ja da ita ba shiyasa ya zaɓi yayi mata ƙaura Kafin Allah ya kawo musu mafita akan lamarin.

Tunda dukkan abin da Ammi ta buƙata a tare dashi babu wanda yayi Kuskure dan yaƙi Bin umarninta akan su na farko ta nemi ya zubar da Ciki na Biyu saki wanda duka babu dalili bare Hujja mai ƙarfi abin da yasa ma yayi mata ƙauran dan baya son ja in ja da ita ne tana matsayin mahaifiya a gare shi wannan tasa yayi balaguro.

Tafiya taƙi ƙarewa Har zuwa sanda aka kira sallar Isha'i basu ne suka sauka ba se bayan sallar Isha'i a babbar tasha suka sauka Aliyu ya Fito Musu da kayan su ya laluba aljihun jallabiyar shi wadda ya sako Atm card Ɗinshi aciki se ƴan Kuɗin shi waɗanda basu da yawa sabida bai fiye aje cash ba shine yasa ya ɗauko Atm ɗinshi na bankin da yake ajiyar Kuɗi.

Sedai koda ya laluba aljihun nashi wayam ba Atm ɗin Ga wayar da yake transper da ita ya bawa Musa akan cewa ya kashe masa ita ya aje a wajan shi se ƴan Kuɗin daya cusa cikin aljihun shi marasa yawa.
Duk yadda yaso ya dake seda ya kaɗu sabida babban tashin hankalin shi Fatima yasan mai ciki

da tsara be tsara be ga kuɗin hannun shi ba zasu Riƙe Shiba Dama ya taho da Atm ɗin shine dan yasan koda zasu shafe shekaru ba zasu tagayyara ba dan harda Niyar yasai ƙaramin Gida yazo sedai kash Allah baiyi hakan ba dan yafi zaton a ɗakin shi ya manta Atm Ɗin garin saurin haɗa kaya waɗanda Ko rabin kayan nashin ma bai ɗauko ba.

"Yallaɓai Kuɗin Mota ka tsayar damu"
Kwandastan motar ya faɗa a gadarance.
Drivern yace.
"Haba ɗalha kai masa a hankali wannan bai kama da mutanan banza ba"
Aliyu yayi murmushi tare da Ƙirgo Kuɗin motar ya basu yay Musu Godiya tsugunnawa Farha tayi tana Rintse ido da kulawa ya durƙusa a gabanta.
"Fatima yaya me yake damun ki?"
Ya faɗa mata Cikin kulawa.
"Fitsari nake ji washh bayana ƙafata"
Ya ɗan yi Jimm.
"Ni har ga Allah ban son Kishiga toilet Ɗin tasha sabida toilet  Infection"
Ta hau Kuka! tana cewa.
"To ni a ina zanyi wallahi ya matseni Sosai"
Ya kama Ƙugu kafin yaɗan saka hannu yana matsa mata ƙafar tata wadda ta tasa ta Kumbura Cikin sanyin Murya yace.
"Ki bari Mu fita sena sama Miki inda zaki Kinji"
Yadda ya furta maganar cikin sanyin Murya ne yasa ta miƙe ya ɗauki kayan su suka fita daga Cikin tashar..........

Autar manya ce marubuciyar......
*ƁOYAYYAR KAUNA*
*BA SON TA NAKE BA*
*ƊAN MAJALISSA*
*MURADIN ZUCIYA*
*ASHE ZUMA*
*TAURARO*
*KOBA SO*
*RABON WANI*
*FITAR RABO*
*DA IZZATA*
*BAƘON LAMARI*
*AUREN BARE*
*H A S K E*
*ZUMA A BAKI*
*BAƘAR FATA*
*RABO YA RANTSE*

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806

Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 98*
Rabo Ya Rantse
Arewabooks autarmanya

A bakin titi suka tsaya inda motoci da babura ke ta faman kaiwa da kawowa Farha ta kalli Aliyu wani irin tausayin shi ne ke ratsa mata zuciyarta yana huda mata sassan Jikinta koda bai gaya mata ba tasan yana cikin ruɗani da tashin hankali tare da damuwa sedai da ike namijin duniya ne bai ko nuna mata ba.
"Ka bani wannan jakar na riƙe kayan sun maka yawa a hannun ka"
Ta faɗa a hankali ƙwalla mai zafi tana ƙoƙarin zubo mata.
"Nine nace miki kayan sun min yawa a hannuna?" ta girgiza mai kai tare da Kallon fuskar shi se kawai ya juya ya cigaba da kallon titi bai san ko ina a kaduna ba se yace in ba hanyar wucewa zuwa abuja ba bai taɓa zuwa wani abu cikin jahar ta kaduna ba taka maimai bai san ina zasu sauka ba zufa ce ta soma karyo masa ya duba agogon hannun shi Goman dare ta kusa dan motoci ma sun soma sauƙin wuce wa inda Yana da wadataccen Kuɗi ne daya kama musu Hotel sun kwana sedai yana tunanin in ya kama Musu Hotel yanzu to ze ƙarar da ƴan canjin hannun shi.

"Har yanzu kina jin fitsarin fatima ko ya koma kinga yadda Allah yayi damu bama wajan da zaki samu kiyi anan domin titi ne"
Ta girgiza kai.
"Kada ka damu dani Allah ya duba Mu"
Tana rufe bakin ta suka ga wata tsohuwa zata tsallako titi sedai Tsallakowar ta gagara sabida yadda wata babbar mota tayo kan tsohuwar da sauri Aliyu ya yada jakun kunan hannunsa ya tafi wajan tsohuwar a guje ya kamota suka tsallo Ɓangaran da farha take.
"Jikana nagode Allah yi maka albarka bada ban kaiba da tuni wannan mota ta murjeni"
Duk yadda Aliyu ke cikin ɓacin rai seda yayi Murmushi.
Mai hali baya fasa halin sa aljihun sa ya duba ya ɗauko naira dubu ya damƙa mata.
"Baba gashi Kici goro ba yawa"
Tsohuwar ta washe Gibi tana dariya tare da cewa.
"Kai amman nagode nagode madalla a ina kake jikana na dinga zuwa Muna gaisawa ka ganni tunda nake bantaɓa haihuwa ba dana ganka se naji kamar Nina haifi Mahaifin ka tunda nasan dai na girmi gyatumar ka"
Daga farha har Aliyu dariya sukai na dramar tsohuwar kafin farha tace mata.
"Mu baƙi ne daga kano muke"
Tsohuwar tai saurin cewa.
"Oh amman kuka tsaya a titi ai da kunyi saurin zuwa inda kuka zo sabida Titin nan akwai manyan Motocin dake yawo akan shi Nima daga Bikin Jikar ƙawata nake Shine na biyo tanan da tuni na zama gawa"

Aliyu yace.
"Baba zamu bar nan yanzu kema ki daure ki tafi gida dare yayi"
Seta kama haɓar zaninta ta ɗaure kuɗin tana cewa.
"To ku gaya min inda kuka sauka sena zo gobe wajan ku mu ƙara gaisawa"

Cikin ƙosawa da maganarta Kasancewar shi mutum marar son magana sosai yace.
"Bamu da masauki muna dai duba in da zamu sauka ne dan mu baƙi ne a garin"
Tsohuwar ta kama baki cikin mamaki.
"Baku da masauki fa jikana aikuwa ni ina da shi kaga gidana da Mijina ya rasu ya bari se dangin sa suka tausaya min suka bar mini ni kaɗai suka saka min ɗan haya sedai ganin bani da gata tunda ban taɓa haihuwa ba ga dangina duk sun ƙare yasa ɗan hayar yake Mini iskanci baya Biyana Kuɗin hayar Kuma da Kuɗin nake Cin abinci Jikana alkairin dakai Mini dan Allah nima zan kwatanta zan baka ɗaki guda wanda ke Jikin nawa ka zauna kai da matarka danna san matar kace Amman zance kai ɗan yayana ne kazo Kaga zaka dinga amsar Mini kuɗin hayata ma da baya bani"

Tsananin tausayin ta ya kama zuciyar Aliyu.
"Baba idan na zauna kamar na tauye kine sabida Zaki bani ɗaki ne kyauta Kuma Kinga na shiga haƙƙin ki"
Da sauri tace.
"Ni baka tauye niba kuma kai alkairi ne a gare ni dan Allah jikana in ba raina wa kai ba kazo muje ni har zuciyata na baka kuma bana buƙatar Ficikar ka, ka zauna daga nan har san da zaka tashi dan kanka daga gani bakai kala da Mutanan banza ba akwai Ɓoyayyar baiwa a tare dakai"
Aliyu ya lumshe ido yana hamdala a zuciyar shi na yadda Allah bai tozar tashi ba Godiya yayi mata ya ɗauki kayan suka bi bayanta tafiya suke kamar ta kurame seda suka zo dogon wani layi Gaba ɗaya ginin layin na marasa ƙarfi ne dan ko wutar Nepa babu ko ɗauke wa akai oho.

A bakin wani ƙaramin gida tsohuwar ta tsaya mai Ƙofar katako Aliyu ya ƙarewa gidan kallo aran shi yana hamdala ga sarki Allah.

"Jikana kaga gidana nan sunan wannan Unguwa sabon garin rigasa ni Kuma sunana Inno"
Aliyu yayi murmushi inno ta tura ƙofar ta shiga gidan duhu se kukan yara daga wani ɗaki mai fitilar ƙwai Ta ɗaga murya tana cewa.

"Shafa fito ina sunusi yau ga Ɗan yayana yazo"
Matar dake ɗakin matashiya dan ba wata Babba bace ta fito da sauri tana cewa.
"Maraban su sannun su da zuwa amman Sunusi baya nan yana titi"
Sedai se kallon Aliyu take wanda yay kamar bai ganta a wajan ba dan ko gaisuwar data ke masa bai amsa ba yana masifar jin haushin mace marar aji.

Inno ta nuna wa su Aliyu wani ɗan ƙaramin ɗaki wanda ko Kitchen ɗin part ɗin Aliyu ya ninka ɗakin Sau goma tace musu.

"Ga ɗakinnan dama a share yake Kullum sena share ga tabarma nan ga fitilar ƙwai seku shiga ga gidan namu babu abinci"
Da sauri shafa tace.
"Ina da sauran tuwon dasu Basma basu ci ba bara na kawo Musu"
Ta koma ɗaki Shidai Aliyu kayan su ya ɗauka Farha ta ɗauki Fitilar da Inno ta kawo Musu suka nufi ɗakin Suka Buɗe wayyo Allah Aliyu ya ambata a ran shi sabida ƙanƙantar ɗakin ga Shi duk raɓa ta kama bangon ɗakin har simintin ɗakin sauraye ne suka yo Musu caaa da kuka.

Farha da yake ta saba shinfiɗa tabarmar tayi a ƙasa shi Kuma ya aje kayan su a ƙasa bai zauna ba ya Jingina da bango a saman tabarmar farha ta zauna ɗakin yayi shuru.

"Yawwa baƙi ga tuwon da miya"
Shafa take magana daga bakin ƙofa farha ta yunƙura zata fita ta amso ganin kallon da Aliyu ke ai ka mata dashi yasa ta koma ta zauna jikin ta duk a sanyaye shafa taita magana taji shuru seta koma da tuwon ta.

Cigaba sukai da zaman kurame kuma yaƙi zama ko a saman tabarmar ma.

"Kana jina"
Ta faɗa muryarta a sanyaye kamar zatayi kuka!
Bai mata magana ba.
"In hakan akwai cutar wa a tare dakai wallahi ni ka sake ni bani da matsala Kuma in sha Allah zan raini cikin jikina har na haifa koda daga ranar dana haihu ne kazo kace in baka ɗanka zan baka in yaso se matarka ta shayar maka da duk abin da na haifa amman hakan akwai cutarwa a tare dakai sabida baka saba wannan rayuwa ba kaje kabi umarnin mahaifiyarka in ma zubar da Cikinne mafi alkairi duk se a zubar amman Yau ɗaya jibi yadda ka sauya baka saba rayuwar ba sam batai kama dakai ba"

Shuru ne ya kuma biyo bayan maganar tata wanda harta fitar da ran ze mata magana se Kuma taga ya Nufo inda take ya zauna a kusa da ita Kanshi ya sunkuyar yana haɗa kalmar daze mata magana da ita.

"Fatima! waye yace miki wannan rayuwar batai kama dani ba? kin san yadda nake a da kafin na zama haka? kin san wani ƙalubale na fuskanci kaina wallahi sam ba wannan rayuwar ce ta sakani a wannan yanayi ba kece kika sakani fatima anya ban cutar dake ba na kuma raboki da Jahar ki bayan na rabo ki da iyayenki anya ban so kaina ba? sannan maganar zubar da ciki da saki inda ina ra'ayin su da bamu zo nan ba fatima kun fiye min komai na rayuwa Zaki iya zama da Aliyu a wannan Lokacin da bashi da komai ɗakin ma da ya saka ki aro aka bashi? fatima zaki iya wannan rayuwar dani Tabbas Allah ne yaso jarabtata da hakan dan ya ƙara gwada imanina ina fatan wannan ƙaddarar ma Allah ya bani Ikon cinta dan bani da haƙƙin Ammi akaina sabida haramun ne kai biyayya ga abokin halitta dan ka saɓawa mahaliccinka Kinga dukkan abin da Ammi ta bani umarni akai kamar ya saɓawa ƙa'ida Dan saki halak ne amman Allah baya so Kuma baki Mini Komai ba sannan Tace a zubar da Cikin sunna har na wata Uku

nan ma Kinga ta saɓawa ƙa'ida Ko?"
Ya faɗa a raunane wannan shine karon farko da taga raunin Aliyu.
Bai jira amsarta ba......
"Fatima kada ki ƙara cewa na sake ki kada ki ƙara cewa zaki zubar da cikin Jikin ki in dai ba so kike ki rasa ni ba a yanzu kece garkuwa ta bani da kowa se ke seko Cikin dake Jikin ki"
Ya faɗa cikin sanyin Murya wani irin tausayi Aliyu ya bawa farha wata irin soyayyar shi ce ke ƙara Huda Sassan Jikinta bata taɓa sanin tana mugun son shi bama se a wannan Lokacin.
_Dama shi yasa ka auri macen da take son ka sabida ana zaton ita ce zata iya rayuwa dakai acikin ko wani yanayi haka zalika baka gane wake son ka se kana cikin Ciwo ko halin rashin madafa anan zaka gane wake son ka da gaskiya amman in kana da rai kana da lafiya kana da kuɗi to masoyanka basa ƙarewa_

Ta kwantar da kanta a saman kafaɗunsa Hawaye yana zubo mata daga cikin Idanunta.
"Ka taɓa jin wata rana lokacin ina gida kafin ka aure ni na gaya maka ko a bukkar daji kake rayuwa namin daji na zagaye dakai ni zan iya zama dakai? tom ka saka aranka Ni ba zan taɓa juya maka baya ba Allah ya sani Ina son ka cikin ko wani hali amman dan Allah kai ma kada ka saka damuwa aranka kaga baka da lafiya nima kaine garkuwata In ka shiga wani hali rasani zakai, Dole ka daure Ita dama ƴa mace ai Inda mijinta yake nan zata Bishi ka dena wannan Ƙuncin bana so na ganka cikin wannan yanayi kaji"
Ta faɗa tana ɗaga kanta tasa hannunta tana wasa da Ƙasumbar data taru a fuskar shi

Jinginar da kansa yayi ajikin bango ya Lumshe idanunshi Nutsuwa na shigar masa Jikinsa sabida kwanciyar hankalinta yafi Komai yi masa daɗi da basa Nutsuwa dama duk tunanin rabi akan ta ne a wannan Lokacin

Tashi tayi ta gyara musu tabarmar ta ɗauko mayafinta ta shinfiɗa Musu akai sedai babu Pillow ma.
"Kazo ka kwanta naga duk ka gaji"
Ya tashi.
"A,a bari na fita Ko sallah bamu yi bafa Sannan na samo Miki abin da zaki ci"
Ta kalli yadda gari yayi shuru duhu ya sauka.
"Kana jin yunwa nasan"
Ya girgiza kai.
"Bana jin yunwa fatima Kin san abincin dare bai dame niba"
"To in danni ce kada ka fita Nima bana Jin yunwa kada ka fita baka san yaya yanayin unguwar yake ba kaje ka gamu da macuta"
Ya kalleta da wani irin yanayi.
"Baki ci abinci ba Kuma bake kaɗai bace"
"Wallahi bana jin yunwa Ko tuwon da waccan matar ta ce zata kawo na tashi zan amso dan karta ga Mun wulaƙantata ne"
Ya ja ajiyar zuciya.
Ta miƙe.
"Muje muyo alwala"

Suka fita a bakin Ƙofar Inno suka ɗauki Buta gidan tsit kowa yayi bacci Shine yayi Bisimillah yajan yo ruwan a rijiya ya cika musu Butar Seda ya rakata Bayi tayi Fitsari yana tsaye akanta ta gama tayo alwala Suka fito Seda ta shiga ɗaki sannan Yayi abin da ze yi sannan ya Komo wajanta zanin ta cire a tabarmar Sukai sallah Sannan ta mayar da zanin

Ya tashi ya koma saman tabarmar ya jinginar da kanshi bacci ne yake Kama shi sama sama. Kafin ta yunƙura ta Miƙe tai abin da zatai ta dawo wajan shi har bacci mai nauyi ya ɗauke Shi Zama tayi a kusa dashi Ta kwantar da kanshi a saman cinyarta Ta ɗauko wani kwali dake Gefenta tashiga yi masa firfita Duk da tana Jin Baccin amman haka ta hana Idanunta bacci Aliyu yana kwance a cinyarta se Firfita take masa tana kaɗe masa sauro wanda ta hana sauron Hawa Jikin Aliyu sabida Yadda take kaɗewa da Wannan kwalin dake hannunta......... *Masu Application ɗin arewa books se kuje kuyi serching autarmanya ko kuma ku danna blue link ɗin dake ƙasa, marasa arewa kuma zasu iya siya sena saka su a paid grp ɗina Paidbook 500 naira in to 0078174806 sterling bank evidance of payment 09022260850*

*A LOVE STORY 99*
Rabo Ya Rantse
Arewabooks autarmanya

Duk da ita ma baccin ne a idanunta ga shi duk ta gaji dan ko ina na jikinta ciwo yake yi mata ga nauyin Aliyu dan ji take kamar cinyoyinta zasu rabe gida biyu amman haka nan ta daure ta cigaba da kore masa sauron tana kuma kaɗa masa iskar kwalin wadda take bada gudunmawar Bashi iska shiko baccin sa yake sosai harda Munshari Jiyo da kanshi yayi daidai saitin cikinta yana Saka hannu ya zagaye ƙuguntа ya cigaba dayin baccin sa hankali kwance.
Ta jingina da jikin bangon ɗakin Danshin Jikin bangon na Ratsa saman kanta ga ɗan tashin gansa kuka wanda ya hautsina mata yanayin ta wani irin yawu ke tarar mata ga zuciyarta na tashi Tuni yawun ya cika bakinta Numfashinta yana fita sama sama hawaye ke zubo mata Ta ƙudura azuciyarta ba zata yafe wa Ammi ba kuma ba zata taɓa ganin farin Ammi ba sabida ita ce tikitin jefasu acikin wannan hali mai tayi wa Ammi Tunda take bata taɓa ganin Mutumin daya tsaneta ƙiriƙiri kamar Ammi ba ko sunan Ammi a wannan Lokaci Farha bata ƙaunar taji Tun tana hawaye har Kukan nata ya tsananta amman da yake Aliyu baccin nashi mai nauyi ne sam bai Jita ba baƙar Leda ta ɗauko ta zuba Miyan bakinta sabida Tana gudun idan ta zame shi ta fita zubarwa ze farka Ta Buɗe Ƙofar ɗakin ta jefa Ledar ta rufo Ƙofar A hankali ta komar da kanta ta cigaba da kukan da take yi.

Wani bacci ne mai daɗi ya sureta amman duk da haka kwalin yana hannunta a haka aka kira sallar asubahi Duk da Baccin sa mai nauyi ne amman ana kiran sallah ya Juya Yaji ƙafafunsa a ƙasa ga uban sauron daya cika masa ƙafa se Cizon Shi yake Juyawar da zeyi Cinnaka ya gantsara mai cizo a ƙafar shi.
Tsananin mamaki ne ya kama Aliyu Sanda ya ɗaga kanshi yaji shi a jikin farha a saman cinyarta ya zuba mata ido wato a haka suka kwana ya kalli hannunta kwali ne take masa Firfita dashi wani tausayin ta da sonta ne ya ƙara kamashi wanda Ko zafin cizon Cinnakan ma bai sami tasiri a jikinsa ba ya tashi ya janyota Jikinsa wani irin tarin Cincirindon sauraye ne a saman kanta har

wajan Fuskarta tsoro da tashin hankaline ya kama shi sabida yasan matsalar sauro ga mace mai Juna biyu ya kwantar da ita saman tabarmar ya saka zaninta ya rufe mata har fuskarta sannan ya Miƙe ya fita daga ɗakin alwala yayi gidan Shuru shidai da sauri ya buɗe Ƙofar ya fita Wani masallaci ya hango daga can ƙasan layin ya ƙarasa seda yayi raka'atul fijir kafin a tayar da sallar sannan yayi zaman Jiran a tada sallah bayan sun idar da sallar zama yayi Yana lazumi har wajan shiddan safe yayi addu'oi sosai sannan ya fito daga masallacin dan Shine ma ya rufe masallacin ya tawo Gidan Abin mamaki Lokacin daya shiga Gidan A lokacin yaga ɗan hayar Gidan yana jan ruwa zeyi alwala Babu wani sakin Fuska Aliyu ya masa sannu! sannan ya shiga ɗaki Ba kuma komai yasa haka ba shine yadda Aliyu keda taka tsantsan Baka shigewa jikin mutum tashi ɗaya har se kasan waye shi.

Tana zaune ta idar da sallah ya kama haɓa cikin mamaki.
"Yaushe kika tashi fatima?"
Ya faɗa yana ƙoƙarin zama a kusa da ita.
"Ina kwana"
Yaji muryarta.
"Lafiya lau yaya kwanan baƙon waje?"
Tace masa "Alhamdulillahi"
Yayi Murmushi.
"Amman mai yasa kika kasa bacci jiya kikai ta min Firfita bayan ke ma kin gaji?"
Ta ɗanyi Murmushin yaƙe dan ba ƙaramin ciwo Jikinta yake mata ba amman tasan ta gaya masa hankalin shine ze tashi.
"Nina saba da wannan rayuwar kaikuma baka saba ita ba"
Yaɗan dube ta da rashin fahimtar zancen nata.
"Kimin yadda zan gane"
"Nina na taso gidan talakawa mana na saba kwana cikin sauro da zafi kaikuma ka taso kana da Kuɗi ka saba kwanan Ac da Fanka kaga inna barka a haka zaka cutu duk da nasan yanzun ma dauriya kake"

Ya ɗan kalleta cikin wani yanayi.
"Fatima ki faɗi gaskiya nasan dai duk rashin gidanku ba zaki taɓa kwana a irin wannan ɗakin ba Ko talauci ma da rashi ai mataki mataki ne Wani yafi wani kamar yadda Kuɗin ma yake mataki mataki wani yafi wani"

"Haka ne kam dama ita duniya makaranta ce in kana ganin babunka to baka dubi wani bane kai se kaga kana cikin aljanna Nima dai nasan Mu talakawa ne amman wallahi ɗakunan su Umma babu gansa Kuka Kuma akwai ledar tsakar ɗaki"
Shi dariya ma ta bashi Wato yaro yaro ne.

"Shiyasa aka ce in kana kallon na ƙasa dakai Kullum zakai ta yiwa Allah Godiya Kinga wannan Kwana ɗayan danai anan gidan na ƙara Godewa Allah Kuma na ƙara Jinjina ni'imar daya mani sannan na ƙara Jin tsoron shi Koda yaushe Kana samun Kuɗi kana cin mai kyau ka sha mai kyau ka tashi a mai kyau ashe wani ma wajan baccin ya gagare shi yanzu dai duba saman

ɗakin nan In damuna ce ba zamu Iya bacci ba barina gida wata makaranta ce Allah ya kawo ni"
Ya faɗa yana Jingina da Bangon ɗakin hannu yasa yana cire mata Hijabin tare da cewa.
"To yanzu me zaki Break dashi?"
Ya faɗa sanda ya cire mata Hijabin gaba ɗaya ya tsira mata ido yanayin Kallon yana saukar mata da kasala.
Ta lumshe ido.
"Ko mu kwanta?"
Ya faɗa Muryar shi har sarƙewa take ta gano Nufin shi.
"A,a"
"To me zaki ci na siyo miki?"
"Kai kana da tabbacin tsabtar wanda zaka siyo min a wajan sa nifa Allah ya bani tsirfa wallahi bana son abincin waje"
Yayi Murmushi.
"To Gimbiya duk yadda kika ce"
Ya faɗa yana zira hannunshi a saman rigarta.
Ta Buge hannunshi.
"Dan Allah ni ka rabu dani ba zan iya komai ba yanzu duk Jikina danƙo"
Ya Tashi tsaye.
"To bari na fita yanzu zan dawo"
"Ina ka sani da zaka fita?"
Yayi murmushi tare da cewa.
"To se nai ta zama ma tambayi ai baya ɓata"
Se ta miƙe tana saka hijabinta.
"Nidai Muje tare wallahi bazan je a sace kaba kai baka san ko ina ba gwara ma kome ye ya same mu tare"
Dariya ta bashi.
"Dan Allah Ki koma babu wani abu daze same ni haba kada ki mayar dani mace fa se kace wani ɗan ƙauye"
Ta ɓata rai.
"Zaka fita amman ka bari anjima sabida kaga yanzu safiya ce Koni ce fara ai na haƙura da cin abincin har anjima"
"Inna zauna me zaki bani nifa wallahi a matiƙar Buƙatarki nake to na nuna Buƙatata kince a,a to zaman me zanyi"
Ta kalle shi.
"Kai yanzu har ka sami Nutsuwar buƙatata?"
Yayi mata wani kallon ƙasan idanu.
"Ƙarshen Nutsuwa ma tunda ina tare dake Ko a titi Muka kwana zan sami Nutsuwa bare Muna gida a ɗaki to meye saura?"
Ta koma ta zauna Shima zaman yayi amman ya cire rigar Jikinsa shima zafin na damun sa sosai Gaba ɗaya Kirjinsa Kwantaccen Gashine har ya zagaye Nippy ɗinshi ta kawar dakai sabida bata taɓa ganin shi kamar a wannan yanayin ba.
Ya matso wajan ta ya shiga cire mata hijabin.
"Ki dena min haka babu abun da zan Miki Please"

Ya faɗa yana Cire mata hijabin da rigar Jikinta wadda tun ta lace ɗin data sako ne a gidan salama kai tashin hankali beyi ba sam.
Ta kare Ƙirjinta da hannayenta "Dan Allah ka rabu dani"
Ya janyota ya matseta a ƙirjinsa har Zuciyoyinsu suna Jin bugun junan su.
"Ba abin da zan Miki amman ki barni naji ɗumin Jikin ki" ya faɗa yana sakar mata Hucin Numfashin sa Luff tayi ajikinsa ƙamshin dake manne a fatar shi yana ziyartar hancin ta.

"Jikana baka tashi bane?"
Suka ji Bugun ƙofar Inno tana Kiran Jikanta.
A wahalce ya saki farha yana saka rigar shi Muryar shi wadda ta shaƙe ya ɗan ɗaga.
"Mun tashi Baba Bari na fito"
"To fito ga koko na siyo Muku da Ƙosai maza ku karya Dan gudun wannan shu"umar Cutar kwalsa take ko me"
Farha me zatai In ba dariya ba Kuma dariyar harda Biyu na farko Ulcer inno zata ce na biyu kuma yadda ta hango Ba ze raga mata ba Inno tazo ta katse masa hanzari wannan abu yayi mata Onga rigarta ta mayar tana dariya shikuma ya fita waje.

Suka gaisa da Inno tana miƙo masa kwanan kokon da Ƙosan.
"Ban ji dadî ba kada ki kuma siyo mana abin karyawa dan Allah"
Ya faɗa.
"To ka amshi wannan dai na riga na amso muku"
Ya amsa yana Godiya Girma da tausayin Tsohuwar yana ninkuwa a zuciyar shi.
"Amman jikana kai ƙwara ne ko naga jan naka kamar na ƙosai"
Duk yadda yaso kamewa seda ya dara.
Yayi ƙasa da Murya.
"Keda kika ce Ni ɗan yayanki ne so kike asirinki ya tonu ko me?"
Seta kama baki tana dukan bakin ta.
"Shegen baki Ungozomar bata gasa shi sosai ba, to ai abunne jikana ban taɓa ganin mutum mai kyan kaba anya bakai jiɓi da waɗanda muke gani a talabijin ba kuwa?"
"Inno maganin ciwon kai To bari na fita inna dawo zan baki amsa"
Ya faɗa yana Komawa ɗakin sabida bai saba yawan magana ba Aliyu irin Mutanan nan ne marasa magana haka halittar shi take Ko magana aka cika yi fita yake sabida ciwon kai yana shiga farha tasa dariya.

"Jan ƙosai"
Ta faɗa tana dariya tare da amsar Kwanon ƙosan haɗiyar yawu tayi.
"Kai wannan ƙosai yaji albasa"
Ya kalleta.
"Zaki ci kenan?"
"Harda gudu ma"
Hmmmm
"Keda kika ce bakya cin abincin siyarwa kuma yaya zaki ci wannan Ki bari na fita nazo da abin da zaki ci"

Tai saurin Buɗe kwananon ta ɗauki Ƙosan ɗaya takai bakinta.
"Ko a masai ake tsoma wannan dai se naci"
Shagala tayi da cin ƙosan da shan Kokon wanda ya zame yabar mata ɗakin Fita yayi Cikin Ikon Allah bai sami duhun kai wajan shiga cikin garin sosai ba.

Farha ta duba taga baya wajan wato wayo yayi mata "Allah ya kiyaye hanya" ta faɗa tana cin ƙosan wanda yayi mata daɗi bayan ta kammala ta fita har ɗakin Inno wadda take zaune tana jin Radio.
"A,a jikata Kin fito kenan?"
Farha ta zauna.
"Ina kwana Dafatan kin tashi lafiya yaya hidima damu Allah ya saka da alkairi dama kwanukan na kawo Miki"
Inno ta washe bakinta mai giɓi.
"Kai babu komai ai komai yiwa kai ne Jikata ke Kuma baƙa Ƙirin Ma sha Allah kalar hausawa"
Farha me zatai in ba dariya ba.
"Haba inno Nima ai Jar ce kamar Ƙosai"
Dariya sukai daga ita har Inno tashi ɗaya Jinin farha dana Inno yayi Mugun haɗuwa.
"Inno bari na gyara Miki ɗakinnan naki naga ko ina tarkace dama haka ɗakin Tsofi yake ina abun shara?"
Inno ta washe baki tana cewa.
"To jikine duk babu ƙarfi ga shi bani da mataimaki se Allah haka dai nake karkaɗe makwancin nawa na kwanta kafin Mutuwa tazo Shiyasa haihuwa tayi a rayuwa inda ina da ɗan kaina ai da ban zauna ɗakina babu shara ba"
Tausayin Inno ya kama farha.
Tsintsiya farha ta ɗauka ta shiga sharar ɗakin ta gama ta ninke mata kayanta masu dauɗar ta fitar dasu waje haɗe da kwanukan wanke wanke Har tsakar Gidan farha ta share sannan ta shiga ɗakin su nan ma sharewa tayi ta haɗe Musu kayan su Gefe Guda.
Soson Buhu da ruwa ta ɗauka ta shiga ɗakin dashi ta dinga wanko gansa Kukar data cika ɗakin ta gama ta Wanke tsakar ɗakin ta Koro ruwan tsakar gida ta haɗa ta wanke tas Sannan ta amso omo wajan Inno ta mata wanke wanke

Wankin Inno ta soma yi a bakin Rijiya Inno kuma tana zaune a bakin Ƙofa duk daɗi ya isheta se Hirar su suke.

Shafa ce ta fito da yarinyar ta a hannu tana ganin farha ta saki Fuska tana ce mata.
"A,a ina kwana yaya kwanan baƙunta kuma......? *Masu Application ɗin arewa books se kuje kuyi serching autarmanya ko kuma ku danna blue link ɗin dake ƙasa, marasa arewa kuma zasu iya siya sena saka su a paid grp ɗina Paidbook 500 naira in to 0078174806 sterling bank evidance of payment 09022260850*
*A LOVE STORY 100*
Cikin sakin fuska farha tace wa shafa.
"Alhamdulillahi nagode"

Ta cigaba dayin wankin ta shafa ta zauna a kusa da inno suna Cigaba da hirar su Lokacin Mijin shafa ya fito kallo ɗaya farha tayi masa bata Ko gaishe dashi ba ta sunkuyar da kanta tana cigaba dayin wankin ta.

"Inno waɗan nan ne ƴaƴan naki?"
Cewar Mijin shafa Inno tace

"Ita ce surukar mu ɗan nawa ya fita"
Cikin haka Aliyu yayi sallama a gidan yara ne Guda Biyu ke biye da bayan shi da kaya niƙi Niƙi sukai ta shigo wa dasu har Suka gama ya sallame su shikuma ya dinga shigar da kayan ɗakin su Inno se sannu take masa shafa da Mijinta Kuma suka koma ɗaki dan gaba ɗaya Mijin shafa jiyay Aliyu na bashi tsoro yana shakkar sa ga wani kwarjini daya yi masa.

"Ki aje wankin haka kije wajan Mijin ki babu daɗi ya dawo Kina zaune naga Ko sannu da zuwa baki masa ba"

Farha tayi dariya tare da cewa.
"Rabu dashi Inno gwara na tashi gaba ɗaya Inna je ba lallai ya bari na fito ba Kinga da kaya ya shigo"
Inno tayi dariya tana cewa.

"Haka ne kuma Allah dai ya saka Miki da aljanna" farha ta cigaba da wankin wanda har akai sallar azahar tana yi Lokacin ya fito daga ɗakin ya tafi masallaci tana yi masa adawo lafiya yayi mata banza Gabanta ya faɗi ko ba'a faɗi ba tasan laifi tayi masa shiyasa yayi mata shuru a sanyaye ta ƙarasa wankin ta shanya Lokacin shafa ta Fito zata Ɗora Girkin rana.

"Dan Allah In kin sauke zan ɗorawa Mijina ruwan wanka"
Inji farha tana kallon shafa wadda take haɗa gawayi a kurfoti.
"Lah zo ki ɗora in kin sauke sena ɗora girkin ai ba yunwa muke jiba"
Cewar shafa farha ta cika da mamakin shafa Mace mai Kirki mai rawar Jikin son taga ta kyautatawa wanda ke tare da ita.

"Bara na ara Miki tukunyata naga kamar baku zo da kayan aiki ba"
Shafa ta ɗauko ƙatuwar Tukunya lokacin wutar ta haɗu gawayin yayi rushi sosai Shafar ce ta cika Tukunyar da ruwa har baki ta ɗora farha nata Godiya.
"Wallahi babu Komai ai zaman tare ya wuce wasa"
Mijin shafa ne ya kirata Sabida haka farha seta Koma tayi alwala ta Miƙawa Inno sauran sabulun wankin ta Nufi ɗakin su.

Mamaki tayi sabida ya shinfiɗa sabuwar Ledar tsakar ɗaki wadda ta haska ɗakin sosai ga kuma katifa madaidaiciya wadda zata ɗauke su Harda sabon zanin gado daman kayan data ga yaran na shigo dasu Gidan yawan su ya bata mamaki Gefe ɗaya ya aje babban Buhun shinkafa da galan Ɗin mai da ƙaramin gas da Katan ɗin indomie se tukunya Guda Biyu da Plate da Spoon

da dai sauran kayan Kitchen ɗaiɗaiku se ƙaton bawon wanki da Bokitin wanka da Buta babba da ƙarama da Net wanda ya kafa a saman katifar tasu Ɗakin se ƙamshin turaren room frashner yake kayan su ma ya jere su sunyi kyau duk da bai fito dasu waje ba.

Dardumar data ga ni a Can Lokon ɗakin a shinfiɗe ta ɗauko ta shinfiɗa ta tayar da sallah bayan ta idar ta zauna tana addu'a Lokacin ya shigo ɗakin sallama ciki ciki kamar ammasa Dole yayi.

Ya sami gefen katifa ya zauna ya wani rafka tagumi kamar mara lafiya.
"Sannu da zuwa bari na ɗora maka abinci amman kafin nan bari na wanke maka banɗaki se kayi wanka"
Ta faɗa tana kallon sabuwar tsintsiyar daya jere a bayan Ƙofa da sabon abin zuba shara da abin kwashe sharar Duka a bayan Ƙofa.

Yayi mata shuru.
"Yallaɓai magana nake Inna maka laifi kayi haƙuri nidai"

Ta faɗa tana ɗaukar Bokitin ta fita da tsintsiyar ƙaton Omo daya siyo ta farke ta tsiyaya ta zuba Ruwa ta wanke masa bayin tas ta Juyo masa ruwan wankan ta sirka masa takai masa bayin.
"Na gama ko zaki ɗora Abincin"
Ta leƙa ɗakin shafa amman bata shiga ba shafa tace "To gani nan"
Ta shiga ɗakin har Lokacin yana zaune.
Ta ɗauko sabon kwandon wankan daya zo dashi ta koma takai masa Bayin.
Ta kuma dawowa.
"Na gama Kaje kayi wankan"
Ya tashi a saɓule ya fita ya shiga banɗakin Kafin ya fito harta Fito masa da kayan daze saka Ta ɗauki gas Ɗin ta fitar dashi bakin Kofa Ta ɗauko Tukunya ƴar ƙarama ta zuba ruwa ta ɗora masa Indomie.
Tana zaune a bakin Kofar ya fito daga wankan Ya shiga ɗaki Lokacin data gama dahuwar ta juye masa a plate sannan ta Ɗora masa Baƙin shayi.

Ta kammala Komai ta Shigar da gas ɗin bakin ƙofa sannan ta shiga wanka ta fito ɗaure da zani da Hijabi yana zaune Amman ya shirya ya sauya kaya.
Ta shafa mai sama sama ta sanya Doguwar riga marar nauyi Bata saka ɗankwali da Hijabi ba ta zauna a gaban sa ta Janyo plate Ɗin

"Ga abincin nasan baka karya ba amman ka fara shan baƙin shayin"

"Kin zuba wa Mutanan Gidan?"
Ya tambayeta.
Kunyace ta kamata.
"Ni ban zuba Musu ba"
Ya ɗan zaro mata ido.
"Amman ke kika ari tukunyar su Kika ɗora ruwan wanka bazakiji Kunyar Ki girki ki hanasu ba To

Ki ɗora musu wani Musamman Tsohuwar nan Koki ɗiba Musu Ɗanye ki basu"

Ta zumɓuro mai baki.
"Kai fa ka saba kyauta Amman ka tuna yanzu rayuwar ta canza dole mu tattala inya ƙare waze bamu?"

Yayi Murmushi.
"Allah ne ze bamu kamar yadda ya bamu wannan sannan ka bayar baya hana ka ƙi samu sema Allah ya buɗa maka ni gaskiya ban saba rayuwar baƙin hali ba shiyasa naji hakan wani Iri"
Aiko seya ƙular da farha nan da nan tahau fushi.
"Nike nan nina saba da rayuwar baƙin hali kake Nufi Kome?"
Dariya yayi tare da ɗaukar tea spoon yana Juya tea ɗin yana kurɓa

Har ya gama sha ƙunci take Ya ja plate yana cin Indomie.

"Lahhha dama haka kika iya Girki ma sha Allah Alhamdulillahi nayi farin ciki"
Ya faɗa yana cin Indomie ɗin hannu baka hannu ƙwarya kaɗan ya rage ya na Hamdala ga Allah gefe farha taja dan ita bata ma bata sha'awa ba Indomie ɗin.
"Ke me zaki ci yanzu sannan Kuma Nidai Ki dena wankin da kike sabida yanayin lalurar dake tare dake"

Banza tayi masa sabida ta Lura Namiji ne Shi mai masifar Kishin Iyalin shi dama tasan banzar daya yi mata ɗazu nada nasaba da wankin daya ga tana yiwa tsohuwar.
"To in ban mata ba yaya za'ai kenan matar data yi mana karamci me zamu saka mata dashi?"
"Zan ke bawa almajirai suna yi mata Nima ai bance wani abu ba"

Ya faɗa lokacin da yake janyota saman Cinyar shi yana cusa kanshi a wuyanta.
Idanunshi a lumshe yace

"Baki gaya min abin da zan siyo Miki ba Nasan Kema kina jin yunwa"
Ta zame.
"Ka siyo mana gawayi dan yafi sauƙi akan gas Sannan ka siyo min tsakin masara in ka tambaya za'a nuna maka wajan masu awo suna saidawa"

Yana lasar Saman Kunnenta yace.
"Bana son ki wahalar min da kanki Ki bari Allah ze Hore mana Muna siyan gas Ɗin"
Ta girgiza kai.
"Nasan kawai ƙarfin haline irin naka Ni ba wani wahala da zan sha ka siyo in Allah ya hore maka"

Bai bata amsa ba sabida yadda yake tsotsar ramin Kunnenta yana hura mata iskar cikin bakin sa.
"Fatima na ina son ki kamar raina"

Ya faɗa a birkice yana Kwantar da ita a saman katifar ya Ɗora kanshi a saman Ƙirjinta Kusan Mintin su goma a haka kafin ya Haɗe bakin shi da nata wata irin tsotsa yake yiwa laɓɓanta kamar ze cire mata su.
Bata hana shi ba sabida ta fahimci a buƙace yake da ita a hankali ya Tura hannunshi Cikin rigarta.

Subuhanallah lamarin akwai Girma sirrin nasu ne na Masoyan Juna wata irin soyayya mai cike da tsabta da Nutsuwa yake Aika mata Farha tun tana basarwa itama ta ware iya abin da ta sani take yi masa wanda ya birkice har ya Kusan tona Musu asiri sabida sumbatun sa Sun shafe lokuta suna Bawa Junan su farin ciki da Nutsuwa kafin Ya zare Ta daga Jikinsa yana shafa sumar kitson kanta.

"Allah yayi Miki albarka zumata Kullum ƙara Birkitani Kike wai meye sirrin?"
Ta cusa kanta a kirjinshi tana wasa da gashin Kirjin sabida Tuni yayi fatali da sutturar su.
Ya kuma rufeta da zanin gadon yana shafa gadon bayanta.
"Yanzu ta yaya zaka Kuma wanka?"
Yaji tambayar tata cikin Kunnen shi.
"Kema ta yaya zaki wanka?"
Dariya tayi shima dariyar yayi a hankali ya Miƙe ya gyara jikinshi ya ɗauki Bokiti yabar ɗakin ga mamakinta kuwa se gashi bayan wasu Lokuta ya dawo kanshi a jiƙe da alamun wanka yayi Yana tsaye yana Goge kanshi Itama ta fita bayan ta dawo ya shirya ze fita dole ya ce taiwa Inno Girki ta miƙa mata Yayi mata sallama ya fita daga ɗakin sabida bai saba zaman Gida ba.
Lokacin da yabar Gida miƙar hanya yayi batare daya san ina zashi ba Kawai kuma dama ƙarfin hali ne irin nashi kuɗin sa gaba ɗaya yayi siyayya dashi Babban tashin hankalin sa gawayin da tsakin data buƙata bai da Kuɗin kuma baya son ya nuna mata gazawar shi sabida ya fahimci tana Ƙarfafa masa gwiwar shine akan Komai.

"Bawan Allah lafiya ka takani baka sani ba?"
Cewar wani mutum wanda ze wuce ta kusa da Aliyu Jikin Mutumin duk ya ɓaci da baƙin Mai alamar bakani ke ne.
"Dan Allah kayi haƙuri"
Aliyu ya faɗa yana ƙoƙarin wuce Mutumin.
"Bawan Allah dan Allah ko zaka gaya Min damuwar ka dan akwai tarin mamaki ga mutum kamar ka kana tafiya kana tunani har ka takani baka sani ba kuma dai gashi ras kake"
Aliyu ya juyo tare da cewa.
"Lafiya lau Alhamdulillahi Amman kai haƙuri"
"Dan girman Allah ka gaya min Ni naji ajikina kana da damuwa Kuma musulmi ɗan uwan Musulmi ne duk da akwai nagari akwai mugu"
Cewar Mutumin.

"To ni baƙo ne ina zaune a sabon garin rigasa na fito neman abin yi"
Dariya Mutumin yayi.
"Ban yarda ba ranka ya daɗe sabida bakai kama da kalar wahala ba"

Aliyu yaɗan ware ido

"Dama wahala akwai kalar ta Tab"
Mutumin yace.
"To koma dai da wasa kake Ni sunana Dini ina zaune a hayin rigasa Kaga waccan titin Ƙaton ginin da kake gani To tsohuwar tasha ce da aka dena Lodi da ita To se Muka mayar da wajan Gareji ana gyaran motoci sannan ana sauke ƙarfen gyaran Mota wanda Kullum Mota sama da ashirin na kawo ƙarfen daga lagos Indai zakai aikin sauke ƙarfan zan maka hanya duk da basa buƙatar ma'aikata Ni bakani ke ne gyaran Mota nake aciki Muna mutunci da masu kawo ƙarafan"
Aliyu yace.
"Da gaske malam Dini?"
Dini yayi dariya.
"In sha Allah ta yuwu inna taimake ka nima Allah yayi min abin da zato bai taɓa zato ba"
Aliyu ya cika da mamaki.
Jerawa sukai da Dini bayan Dini ya karɓo abincin daya siyo ƙaton gareji ne sosai Mutane nata kaiwa da kawowa Suka shiga wajan Ogan wanda Dini ya gabatar da Aliyu abin mamaki Ogan da Mutunci ya karɓi Aliyu dan har suna wasa da Juna yace masa aikin daga ƙarfe Bakwai na safe ne zuwa shiddan yamma kullum za'a baka Dubu Goma sannan Kuma kawai dan yaga Aliyu ne yaji yana ƙaunar shi amman ba da ban haka bama sun rufe ɗaukar ma'aikata akwai riga da wando masu tambari da sunan wajan ya ɗauko ya bawa Ali yace dasu ze ke zuwa.
Aliyu yaji komai kamar a mafarki yayita Godiya lallai Duniya babu tabbas yau Shine da aka ce za'a ke bawa dubu Goma yaji kamar an saka shi acikin aljanna wanda shi kafin faruwar hakan yana iya bawa Mutum kyautar Da se Mutum ya gigice da ita ma'aikatan sa nawa ne suke cin abinci a ƙasan sa

Bayan sun Rabu da ogan Godiya yayi tayiwa Dini har Dini yace godiyar ta isa haka Kayan a hannun shi ya tawo Gida gaba ɗaya mamaki da al'ajabin wannan alkairi daya haɗu dashi ya sanyaya masa Jikin sa

Kayan kawai ya aje ya fita masallacin sallar la'asar sabida Lokacin daya zo farha bata ɗakin Bayan  ya dawo ya tarar da ita ta shigo.
Se ɗaga kayan daya zube a saman katifa take tana kallo.
Bayan yayi mata sallama yace.
"Ina kika shiga nazo bakya ɗaki Nifa bani son yawo"
Tayi Murmushi.
"Naje kaiwa Inno Shinkafar dana dafa mata ne tana ta Godiya"
Ya nemi guri ya zauna.
"Wannan kayan fa na Menene?"
Cewar farha cikin sigar tambayar shi........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE 101*

kwanciya yayi a saman katifa ya tallafe kanshi da hannunshi yana kallon rufin ɗakin.
"Kana jina ina maka magana kai Min shuru shikenan"
Ta faɗa cikin rashin Jin daɗin yadda yake yi mata shuru wani bin idan tana yi masa magana.

"Fatimah nifa wani lokacin bana son yawan magana kaina har ciwo yake min in ana magana sosai Ki haƙuri Har na huta" ya faɗa a hankali Tashi tayi zata fita daga ɗakin ya Damƙo mata hannunta, "Ni ka cikani mai zan yi maka bayan na dameka da surutu"
Ta faɗa hawaye na zubo mata daga cikin idanunta.

"Subuhannallahi Why are you crying? Fatima, after I was with you, stop crying. I don't want you to be quiet" ya faɗa yana sa tafin hannunshi yana cire mata hawayen nata Kukan take sosai "Tausayin kaina nake" ta faɗa cikin kuka da sauri kuma a ruɗe yace "Kamar yaya tausayin kanki wani abun ke damun ki?" ta girgiza kanta "Idan banyi hira dakai ba da wa zanyi daga maka magana kace kanka na ciwo in ana magana" ta faɗa muryarta na shaƙewa ya marairaice tare da cewa "Bazan kuma faɗin haka ba Me kike so nace yanzu?" ta kalle shi da gaske yake gaya mata maganar Shi haka halittar shi take Mutum ne marar yawan son magana.

Ta ɗan matsa daga kusa dashi.
"A,a shikenan kawai a bar maganar" Yace "Fushi kikai dani ba kyau Saurin fushi" "Niba fushi nake dakai ba to mai kayi min"
Ya gyara zaman shi "Fita nayi Neman abun yi kinga kina da Juna biyu Dole akwai abubuwan Buƙata ga asibiti da zaki fara zuwa ina son In kaiki ganin Likita dan a duba Lafiyar Babynmu Kinsan abin da ya bani mamaki?" ta girgiza kai tana tsira masa idanunta.
Labarin dukkan yadda sukai da Dini da kuma Ogan tashar Ya bata ya ƙare da cewa "Gaskiya abin ya bani mamaki yadda Komai yake zuwa mana cikin sauƙi haka ɗan sauyin rayuwar Da muka samu kaɗan Ne"
Farha tayi Murmushi tace.
"Ai tunda ka ji ƙan Al'umma kai ma Allah zeji ƙanka sannan kuma Ka saka ɗumbin Mutane a farin ciki Ko kasan Allah yana son bawa ya saka bayin sa a farin ciki Ni dama naji ajikina Allah baze tozarta kaba"
Ya zuba mata ido.
"Allah yasa mudace"
Ya faɗa yana tashi lokacin ana kiran sallar magariba.
Ya shiga tattare hannun rigar shi.
"Bari nayi alwala"
Ta tashi da sauri ta ɗauki Buta ta cika masa da ruwa sannan ta komo ɗaki ta Ɗebi gishiri ta shiga bayin ta barbaɗa ta kora ruwa sannan takai masa Butar bayin

Ta dawo lokacin ze fito daga ɗakin.
"Na kai maka Butar Bayin"
"Nagode" ya faɗa yana fita daga ɗakin Ya Shiga bayin yayi abin da zeyi ya Nufi masallaci Da gaske bamai son maganar bane ta Lura haka yanayin sa yake se Dole yake mata magana doguwa.

Bayan tayo alwala tai sallah tayi azkar sabuwar Fitilar Batir daya zo da ita ɗazu Cikin kaya ta Buɗe ta kunna Ta fita waje da gas Ruwan Shayi ta ɗora masa tasan baya cin abincin mai nauyi da daddare kamar yadda yace mata Sauran indomie ɗin ɗazu Kuma ta ɗumama farar sauran Shinkafar data dafawa Inno ta ɗumama taci da ƙyar ta Kammala Komai ta shiga ɗaki Tayi sallar Isha'i bayan sallar Isha ya dawo tai masa sannu ta gabatar masa da tea ɗin da sauran Indomie Ɗin Tea ɗin ma kawai yasha yace ya Ƙoshi Fita tayi ɗakin shafa ta Miƙa mata Indomie tace ta bawa yara shafa taita Godiya har Mijin shafar ma seda ya Leƙo yace angode farha ta juya ɗaki Lokacin harya Cire kayan shi ma daga shi se Singlet da Gajeran wando yana kwance Ya lumshe idanun shi amman ba bacci yake ba Rage kayanta tayi itama ta raɓa Gefen shi Nan da nan bacci ya ɗebe su naji ya wanda basu sami damar yin shiba.

*KANO*

"Nidai ranka ya daɗe so nake ka bani ɗaurin bakin Mijina sabida dukkan abin da nake dan shi nake dan ya sami ƴan cin kanshi amman sam bai gano ba sannan Shi ma ƙanin Mijin nawa Ina son ai Masa Haɗaɗɗiyar Mallaka wadda zeji kaf Duniya ba wadda yake so sama da Jamila ta, Kaga in ya aure ta Dukkan Komai nashi ya dawo ƙasan Mu Inda hali shima a ɗaure masa bakin sa"
Sakina Kenan Gurfane a gaban tsohon Bokan ta wanda ta yarda shi bayan ta sami sabo wanda take waya dashi rannan da daddare ganin aikin sa bai mata yadda take soba yasa yau ta dawo wajan tsohonta nada wanda ta taɓa zuwa wajan sa amman bai taɓa mata aiki ba ta sauya waje se yau suka dawo ita da jamilar ta.

Ya janyo madubi ya zuba ƙasa akai ya fara zanawa yana bajewa.
"Mijin ki ze mallaku Zan baki baƙar laya wadda zaki sami sabuwar gawa wadda ba'ajima da Binnewa ba ki cusa a bakin ta yadda wannan gawa ta Mutu haka bakin sa ze Mutu Se yadda kikai dashi"
Ya ƙara baje wata ƙasar kana yace.
"Bana ganin Komai a tare da ƙanin Mijinki se haske Kwata kwata taurarin sa basa kawo bayani se haske kawai Gaskiya aikin sa yafi ƙarfina Ke Bama zan Ɓoye Miki ba Duk wanda yace Miki ze iya yi Miki aiki akan shi ƙarya yake Kuɗin ki kawai zeci bawai asiri bane baya kama shi a,a Wani irin Murɗaɗɗan Mutum ne mai taurin kai da kafiya uwa uba addini ya ratsa shi Da wuya aiki ya Huda shi nan Kusa A lissafin masana taurari ma za'a iya kai wa shekara hamsin ana masa asiri amman bai huda Jikin sa ba wannan shine gaskiyar Bincike na amman In kina Musu Kije wajan wani ki tambaya"
Sakina ta share zufa tare da cewa

"Ranka ya daɗe Nafi shekara biyar ina aiki akan sa da matar shi"
Da sauri ya ɗaga mata hannu yana zana ƙasar sa.
"Kin san kaf Bincike babu wanda yakai na ƙasa gani! To wallahi waɗanda kika kaiwa Kuɗin ki akan shi sun cuce ki dan babu wani abu naki a tare da wannan Mutumin matar shi Kuma ɓarewar Cikin Jikinta ya samo nasaba ne da yawan Bin malamai ita ma da suke Yi bata sani ba sheɗanun da suke turawa surukarta akan suyi aiki akanta sune suke Shiga Jikinta suna lalata

mata Cikin da take samu yanzu haka mahaifarta ta fara saki In batai wasa ba ma Zata iya samun matsala"
Sakina tai wata zabura tare da gyara zama sosai
"Ban gane ba kai min yadda zan fahimta?"
Yace mata "Bani sunan matar Kanin Mijin naki" sakina ta gaya masa ya Cigaba da zana ƙasa yana gogewa har yakai Minti ashirin a haka.
Sannan yace.
"Na bincike ta tas Itama ai ba don Allah ta auri ƙanin mijin naki ba, mahaifiyarta bata ƙaunar surukarku sabida manufar ma ta tarwatsa farin cikin surukarku ta shiga ta fita ta haɗa auren ƴarta da ƙanin Mijinki Kullum faɗi tashin su akan Su kawar da surukarku suke sabida ana musu bincike ana gaya musu surukarku Ke Ɓarar da cikin ƴarta to basu sani ba sheɗanun da suke aiki dasu sune In suka raɓi Surukarku da ƙanin Mijinki In basu sami nasara ba sabida tsarkin dake tare da surukarku da ƙanin Mijinki to sesu Huce takaicin su ajikin ita matar ƙanin Mijin naki wadda a ƙasan mararta suke dira su lalata ɗan tayin Cikin Jikinta su sakar mata Jini ana ta aikin banza a asibiti ne amman ga ainihin inda matsalar take tattare yanzu haka mahaifarta ta fara gajiya ko wani lokaci zata iya fuskantar matsala"
Sakina tai Huci tare da cewa.
"Lallai dara taci Gida wato aljanun da suke aiki dasu don su Shiga Jikin Aliyu Ko Ammi in an turo su Jikin su Ammin basu sami Kofar shiga ba sabida tsarkin dasu ammin ke tare dashi wato se su Huce ajikin Mami su ɓarar da Cikinta su lalata shi kenan?"
Ya jinjina kai.
"Kinsan aisu sheɗanu haka suke sam basu da gwani zafin takaicin Raɓar da sukai Jiki mai tsarki Konewar da sukai Shine suke Huce haushin ajikin Ita yarinyar"

"To sun jima suna Aiki da Sheɗanun Kenan?" cewar sakina.
"Ita dai surukarki tun farkon auren ne da suka Neme ta asirin ya Huda ta amman yanzu kam jikinta akwai tsarin addu'a duk abin da suke baya tasiri gaskiya Kuma ita a yanzu ma abin da yasa bata son ɗan nata yayi aure sabida sharrin matan zamanin nan ba don wata manufa ba sedai ana zaton wuta a maƙera seta Koma masaƙa labarin tane ya faɗo nan"
Ya faɗa yana dariya.

Sakina ta tsorata dasu mami ashe suma a tafe suke.
"To ni yanzu kace Ba abin da ze tasiri a jikin ƙanin Mijina to meye amfanin na ɗaure bakin Mijina kuma yaya batun auren shi da jamila?"
Ya cigaba da binciken sa.
ya ɗago tare da cewa.
"Idan kika ɗaure bakin Mijinki zaki sami Haɗin kanshi ta yadda zaki tarwatsa Komai na ƙanin Mijin naki sabida Ƙanin nashi ya bashi yarda sosai Mijin ne ze zama garkuwarki Duk dukiyar ƙanin Mijin taki dake wajan Mijin ki seku tattare ku hana shi In ma kika ɗaure bakin Mijin baki da buƙatar auren ƙanin Mijin naki da ƙanwarki Sakina nasan ki Muguwa ce Ke ita ƙanwar taki ai ba don Allah kike son ta auri ƙanin Mijin naki ba dan dai kawai Ta samo Muku dukiya ne" da sauri sakina tai masa Inkiya da hannunta murya can ƙasa tace "Rufa Min asiri ta tashi ta fita tana waya kar taji abin da kake faɗa ka ɓatan aiki"

Yayi Murmushi.
"To mubar batun auren su mu gama da wannan ɗaurin bakin"
Ta langwaɓar dakai..
"To yanzu ina zan sami gawa?"
Yayi dariya.
"Gaskiya da wannan don yanzu yawanci maƙabartu an saka Masu gadi sabida Irinku masu sakawa gawa laya da Kuma masu yankar sassan Jikin gawa shiyasa aka saka tsaro sosai"
Sakina tai jimmm.
"To ko biya zanyi a saka"
Ya girgiza kai "Gaskiya wannan aikin naki ne ba'a buƙatar hannun kowa"
Sakina tai Murmushi.
"Akan biyan buƙatata ba abin da ba zan iya yiba Sabida haka Nina san yadda zanyi Duk yadda zanyi danna sami gawa zanyi" adaidai nan kuma jamila ta gama wayar ta shigo ɗakin Lokacin sakina ta ɗauki jakarta ta Buɗe ta zuba masa Kuɗi a gaban shi sukai sallama suka yo Gida A gidan su suka kwana sabida dare yayi washe gari sakina ta sako yaranta gaba suka dawo gidan Ammi tun daga falon farko ta gano gidan babu lafiya jakarta ta aje tare da nufar ɗakin Ammi sabida Ko ina na gidan tsit hatta Kayan kallo suna kashe sallama tayi ta shiga ɗakin a hankali Ammi ta miƙe daga kwanciyar da tayi tana amsawa sakina sallamar tata.
Cikin ladabi sakina take gaishe da Ammi ta karyar da kanta tana cewa.
"Ammi waya ce ta gigita aka Min Jiya maman mu bata da lafiya, Shine Muka tafi ko sallama bamu yi Muku ba"
Ammi tace.
"Allah ya bata lafiya jikin girma ne se a hankali ai"
Shuru ɗakin yayi Lokacin sadiƙ ya shigo Cikin shirin fita kamfanin Aliyu dan ya gudanar da abin da ze dan cikin satinan yake son su wuce lagos sabida ya mayar da hankalin sa kan Kula da kamfanin Aliyu nacan.
Sadiƙ ya kalli Ammi cikin kulawa.
"Ammi har yanzu baki break fast ba dan Allah Ki barwa Allah Komai In sha Allahu Yana cikin Ƙoshin lafiya"
Kamar jira Ammi take seta fashe da kuka.
"Sadiƙ ta yaya hankalina ze kwanta tun Jiya nake Kiran Numbobin baba duka a kashe"
Sadiƙ yace.
"Kema ammi kina da maido da magana baya kin manta ya bawa Musa wayar tashi"
Ta share hawayenta "Ba Numbobin nasa da yawa ba ai wayar shi ba ɗaya bace ya Allah kasa Babana yana cikin Ƙoshin lafiya"
Sadiƙ ya kwantar da Murya yana bawa Ammi haƙuri har dai ta dena Kukan.
"Abban su baka ganni bane?"
Cewar sakina sadiƙ bai Ko dubi Inda take ba yasa kai zebar ɗakin

"Sadiƙ dawo Mahaifiyarta ce babu lafiya shine ta fita bata gaya maka ba kai mata alfarma mahaifi ya wuce wasa"
Cewar Ammi dan ita yanzu bata son ɓacin ran kowa tsoron Tafiyar Aliyu ma kaɗai bala'i ne a

gareta.
Sadiƙ ya dawo jikinsa a sanyaye Jin Abin da Ammin sa tace masa Ya kalli sakina tare da ce mata..........
Autar manya ce marubuciyar......
*ƁOYAYYAR ƘAUNA*
*BA SON TA NAKE BA*
*ƊAN MAJALISSA*
*MURADIN ZUCIYA*
*ASHE ZUMA*
*TAURARO*
*KOBA SO*
*RABON WANI*
*FITAR RABO*
*DA IZZATA*
*BAƘON LAMARI*
*AUREN BARE*
*H A S K E*
*ZUMA A BAKI*
*BAƘAR FATA*
*RABO YA RANTSE*

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*A LOVE STORY 102*
"Kodan gaba bana son ki ƙara fita baki gaya min ba wannan ai Ba daidai bane"
Ya faɗa cikin nutsuwa sakina tayi ƙasa da kanta tare da ce masa.
"In sha Allahu......"
Ɗakin Ammi yayi shuru na wani Lokaci kafin sadiƙ ya yiwa Ammi sallama ya tashi ya fita sakina ta miƙe tabi bayan shi ya juyo ya kalleta.
"Yaya jikin Maman Inna tashi da wuri zan biya Mu gaisa na duba ta"
Sakina tayi saurin cewa
"A,a bama se kaje ba sabida Sun koma asibiti tun ɗazu ita da jamila"
Sadiƙ yace.
"Okay to Allah ya bata lafiya Inna dawo Ko zuwa dare se Muje dake Ina su Minal?"
Tace.
"Suna ɗaki suna Break fast ko a kira su?" ya girgiza kai har bakin Ƙofa ta raka shi Ya kama hanyar Office.......

*Mami*
Tunda tabar falon Ammi ta koma part Ɗinsu take faman safa da marwa kamar wata zararriya seta zube a ƙasan carpet tana rusa Kuka!
"Wannan wace irin baƙar rana ce tazo Mini na shiga Uku yanzu ashe duk yadda naso wannan

yarinyar Kishiya tace Duk yadda na jata ajikina Kishiyata Ce Aliyu me yasa kayi Mini haka me yasa kayi Min bazata Ko a fuska baka taɓa nuna Min kana da alaƙa da wannan yarinyar ba?"...........
A haukace ta miƙe ta ɗauko wayarta ta shiga Neman layin Hajiya tajira mahaifiyarta idanunta a rufe suke Bata Ji bata gani haka taita Kiran Number Mahaifiyar tata.
"Mami wannan Kira haka na lafiya ne yaya akai?"
Cewar Hajiya tajira wadda daga ɓarin ta tana zaune ne tana Cin Abinci.
"Mama babu lafiya mama bokayen Mu maƙaryata ne mama duba ƙarya ne ba gaskiya ba Mama babu Mai sanin abun da ze faru yau ko gobe se Ubangiji mama wannan abun yasa naji na tsani Bokaye da duk ma mai binsu.......
"Dakata mami Ki fara sanin da wa kike yin magana Ki Nutsu kafin ranki ya ɓaci Farko tunda Kin tsani mai bin bokaye har dani Kenan da kanki dan ba da ban aikin bokayen ba da baki kai matakin zama matar Ali ba"
Mami ta share majina tare da cewa.
"Dama can Allah ya ƙaddara ni matar shice ba mahalukin daya isa ya hana Ko ya saka Mune dai idanunmu suka rufe Muke zaton aikin Bokaye ne yasa Aurena da Ali ya tabbata"
"Dakata mami Ni zaki wa butulci Nida naci kashi da Fitsarin Ki......
"Mama ba zan taɓa yi Miki Butulci ba ke mahaifiyata ce amman mama ina Roƙonki da cewa dan girman Allah daga yau Mu rabu da biye biye don ƙarshen alewa ƙasa! bakin alƙalami kuma ya riga ya Bushe Bokayen mu basu gano mana faruwar Auren Aliyu ba domin zancen da nake Miki tsayin watanni Uku Aliyu yayi auren shi da matar shi Muke zaune har tana da Cikin watanni Uku daga ni har Ammi da mutan Gida bamu san da wannan aure ba ashe Ammin da Muke zargin da hannunta a matsalar da cikina yake samu har Bokan da Muka je yana tabbatar mana yana bamu maganin kawar da ita ashe Ita ke faman yin faɗi tashi akan Aliyu kada ya ƙaran Kishiya wannan dalilin Ne ma yasa ya Ɓoye mata auren Shi sabida haka iya wannan kaɗai Mama ya dace Mu kama kammu Mu gane In Allah ya baka babu mai hanaka in Allah ya hanaka babu mai baka Kinga Munje wajan maƙaryata suna Cutar damu suna karɓar Kuɗin Mu abanza suna haɗa mu da makusantan mu.......
"Ke dallah gafara can Marar hankali se soki Burutsu Kike Min kin kasa fahimtar dani takai maimai ɗin abin da yake faruwa?"
Mami a nutse take gayawa mamanta dukkan abun da ya faru.
Tajira cilli tai da plate Ɗin abincin wanda har ya fashe a ƙafarta Jini ya ɓalle amman bata damu ba seta hau ashar! tana cewa.
"Na rantse da Allah da wanda ya haɗa auren da shi mai auren da ita yarinyar da ita Aminar gaba ɗaya Sena ɓatar dasu aduniya harni za'a kawowa maganar banza harni Amina zata rainawa hankali Kece yarinya ƙarama To bari Kiji Kitimurmura ce Ba wani tasan da batun auren nashi dani suke magana ki haɗa kayan ki da safe zanzo Mu tafi gida daga nan Kuma dole Na koma wajan Bokan daya haɗa auren Ki dana Ali shine kaɗai ze Min yadda nake so dan na nijar Ɗinnan na Kasa gane kan aikin shi sabida yadda gaba ɗaya naga Komai bai tafi yadda nake soba"
Bata jira cewar mami ba ta katse wayar.
Daran ranar mami batai bacci ba Komai ya tsaya mata cak ta kasa tunanin Komai akan wannan lamari sedai kaso goma na cikin Zuciyarta yafi gasgata cewar Duk abin da Bokaye da ƴan

Tsubbu suke faɗi ƙarya ne ba mai yi se Allah ba mai hanawa se Allah da asubahi ta samu bacci ya kwashe ta wajan tara da wani abu Bugun Ƙofar mahaifiyarta ne ya tashe ta
Ta miƙe taje ta Buɗe mata Ƙofar falon ba ta tsaya jiran Gaisuwar mami ba ta tattare mata kayanta iya waɗanda zasu ci manyan akwatunan da suka Fito dasu Suka kama hanyar waje suna tafe Tajira tana tijara har zuwa sashin Ammi wadda suka tarar a ɗaki dan sadiƙ bai Jima da fita ba suka shigo a tsaye tajira ta tsaya ta kama Ƙugu tana cewa.
"To tsuhuwar Munafuka Ni zaki yaudara Kici amanar zumunta ashe aure kika wa Aliyu amman zaki wayance da Borin Kunyar banza wai bakya son ya ƙaro aure Gudun shu'uman cin matan zamani munafuka to ƙarya Kike da hannun ki a auren Aliyu har barin gidan da yayi da saka hannun ki"
Ammi ta ɗago a ɗimauce tare da cewa.
"Ki fahimce ni Yaya tajira wallahi bana da sa hannu akan Komai Yadda kowa yaji maganar auren shi Nima haka naji ki barni da tashin hankalin ɓatan yarona kaɗai ya isheni"
Tajira tai wata girgiza tare da cewa.
"Ai sha Allahu ya tafi kenan Kuma yadda kika tarwatsa min shirina kema ki kwana da shirin kinyi bankwana da farin cikin ki matsiyaciya Munafuka"
Mami ta saka kuka tana cewa

"Haba mama haba mama ammi bata da laifi akan hakan Please karki abin da zakiji Kunyar shi gaba"
Seta juyo wajan mami.
"Dama batun yau nasan tasono na haifo ba kekam Baki gadoni ba To shikenan duk abin da nake dan wa nakeyi Tunda kin zaɓi amina dani gata ga kinan Ku zauna"
Mami cikin kuka tace.
"Ba haka bane mama Yanzu Lokacin gyara kura kurai ne ba Lokacin wani abu ba rayuwar bata da faɗin da zamu ce se Munga komai daidai in ada munyi ba daidai ba yanzu akwai damar gyara"
Tajira ta juyo.
"In kika ƙara cewa tak Allah ya isa.......
Mami taja bakin ta tai shuru Ammi tace.
"Mami Allah yayi Miki albarka kuma Allah yana son bawan daze laifi yazo yayi nadama ya tuba duk da ban san mai Kukai ba amman Kije Ki tuba akwai ragowar damarki sannan Kibi mahaifiyarki Ku rabu lafiya daman Allah yana sako rayayye acikin matacce ya sako matacce acikin rayayye ba tun yau nasan Wasu abubuwan tirsasaki mahaifiyarki take akan yin su ba, kamar nice da Aliyu da dama wasu abubuwan danni yake Yinsu dan ya gama dani lafiya daga ciki harda auren ki Aliyu bai taɓa son ki ba sanadin biyayyar uwa yasa yake zaune dake amman mahaifiyarki bata ga haka ba nina sadaukar da farin cikin ɗana danna Ƙara ɗanƙon zumuncin mu Allah yana kallo wallahi banda gudun sharrin matan zamani babu wata manufar Ɓoye data sa na hana Aliyu ƙarin aure sedai kash yaya tajira Kin bani mamaki yau se gashi akan abun da duk ya shafe mu Kinzo kina Kumfar baki kina aibatani Kina jawa yarona jafa'i lallai Ɓoyayyan Nufin ki akaina da zuri'ata ya bayyana Kuma kin saka min shakkar auren da kika nace akan se ɗana ya auri ƴarki tabbas akwai manufar hakan dan Inda Kina ƙaunata baza kice Aliyu yayi tafiyar da baze dawo ba, sannan Sekin tarwatsan farin cikina mai nayi Miki tajira in ba alkairi ba

dama alkairi yana zama sharri? Allah ya sani bani da Mugun Nufi akan ƙara auren Aliyu se Gudun kada ya auro mana ɓata gari wanda nasan Inzan haɗiyi kur'ani sabida rantsuwa ba ko wa ze yarda ba wani ma cewa zeyi sabida naga matarshi bata haihuwa ne yasa na hana shi ƙarin aure gudun kada ya auro wadda zata haihu Ya sami ɗan kanshi yanzu ma haka daya bar Gida nasan Ko ita matar tashi Kusan tunanin hakan zatai aranta Ni kuma nasan Ko kaɗan bani da wannan manufar manufata ɗaya ce Kuma na faɗa Nasan mami ba juya bace Ko min daɗewa zata haihu tunda Allah yana bata cikin zama ne kawai bayayi Shiyasa duk sanda yazo Min da batun Ammi zan ƙara aure nakan ce masa Baba Ina gudun sharrin matan zamani kai haƙuri ka zauna da mami sabida kada ka auro ɓata gari wadda zata tarwatsa mana zumuncin Mu da zaman lafiyar mu mami kuwa Jinin kace In ma haihuwa kake so mami zata cika maka gida da yara To ashe gwara ma da Allah yake ƙaddara Dukkan Cikin da mami take samu yake zubewa shi kaɗai yasan abin da ya ɓoye da ban haɗa zuri'ata daku ba sabida jiya kaɗai dana je Gidan su yarinyar da ya aura ban sani ba na gano lallai akwai wata Rahma da Allah ya ƙaddara Aliyu ya auri wannan yarinyar har rabo ya shiga tsakanin su"
Ammi ta ƙare maganar a nutse wata irin dariya tajira tayi.
Tare da cewa.
"Ranar wanka ai ba'a ɓoyen cibi komai ya ƙare ai tunda har Kika haɗa munafukin auren ɗanki har ya sami ƙaruwa da amaryar shi sedai ki sani yadda Kike zubar da Cikin mami Nima sena zubar dana amaryar shi sabida nasan kece Kika haɗa wannan aure amman dan Gulma kince bake bace ba Kuma Ki san nasan kece Kike Zubar wa da mami dukkan Cikin da take samu sabida Kina baƙin cikin kada ƴata ta haihu itama ta dandali arziƙi to ta Allah ba taki ba Amina"
Ammi tai dariyar takaici.
"Haka Mashirikan naki suka gaya Miki? to na fiki da sauri na faɗi Allah! wanda shine yake bawa Mami ciki Kuma shike Rabata dashi wanda Duk Ɗinmu bamu san manufar Allah akan yin hakan ba, Kuma Alhamdulillahi dama ya ƙaddara hakan da ban haɗa iri daku ba, An gaya Miki Nima irin kice mai bin mashirikai Sabida dukkan kalaman ki sun yi Nuni da zahirin Kina Biye Biyen banza dana wofi Toni ba haka nake ba na dogara ga Allah Kuma In sha Allah da kaifin addu'ar mahaifiya Ɗana ze sami kariyar Allah Kuma cikin matar shi zezo duniya lafiya Allah baze baki wannan sa'a ba"
Ammi ta faɗa babu tsoro!

"Amina yadda kika ɓatan shirina kema Ki kwana cikin shiri ko yau ko gobe ko anjima zancen wanin ki ake ba naki ba Wallahi ni tajira sena ga bayanki yadda mahaifinmu ya firfita uwarki akan uwata ya soki fiye dani Kika auri Mijin daya fi nawa Kika haifi ƴaƴan da suka fi nawa to wallahi sena rabaki da sauran farin cikin dayay saura a rayuwarki wannan manufa tawa ita ce jagaban haɗa auren mami da Aliyu"

Ammi tayi dariyar takaici.
"Mahaifiyata tafi taki mahaifiyar biyayya shiyasa taci ribar zaman aure! Sannan soyayyar mahaifina dani ina zaton soyayyar mahaifiyata ce ta dawo kaina Mijina Kuma Sunan shi Mijin marainiya Allah yay masa rahma ƴaƴana kuma sunan su ƴaƴan albarka ita zatai ta Binsu Kinga Illar sharri kenan Yadda kikai haka ze Koma Miki Nufin ki Allah ya duba shiyasa yaƙi bawa Mami zuri'a da Aliyu Kuma Ni yarda da Allah danai na tsarkake zuciyata Shine yasa yaketa bani

kariya daga dukkan sharrin ki se wahala Kike taƙi ƙare Miki lallai Kin shiga Jerin ƴan caca Tunda har kike ja da mai tashi tsakar dare ta Roƙi Allah kariya da dukkan Buƙatun ta lallai dukkan wanda ze tashi cikin dare ya roƙi Allah tabbas se yafi ƙarfin Dukkan wata matsala sannan yayi azkar Allah ne ze sauko mala'iku don su zame masa kariya dukkan wata ƙaddara Ko Jarrabawa daze gani wannan fararriya ce Kuma a hakan Allah ze sauƙaƙa masa Ita Nina yarda Allah shine ya haɗa auren Aliyu da mami don ya zama Izna gare ni Nina janyo ku ajikina kuna Jinina ashe bina Kuke da sharri nida zuri'a ta har Kina furta sekin rabani da farin cikin dayay Min saura a rayuwata To Allah ya baki sa'a"
Ammi tana faɗin hakan ta Miƙe tabar Musu falon tai Cikin Bedroom ɗinta Tajira fita tai mami tabi bayanta sabida tace Intai magana Allah ya isa Kuma inda tana da magana da bazata wuce Neman yafiyar Ammi ba amman mamanta ta hanata tai mata Furuci mai zafi.
Haka suka fita daga gidan tajira na Tijara har kuma suka kai Gida masifar take yi alokacin mami tayi mata magana

"Mama nidai nasan nayi laifi har da na biye Miki mukai ta tafka ɓarna a baya Babbar rahmar da Allah yayi Mini shine daya sa maganin da Muka amso dan Ammi ta Mutu bai tasiri ba yau da Ammi ta mutu ta sanadin mu da yaya zamuyi da tarin zunubi bayan ga wanda Muke abun dan shima tuni yay auren shi mama bazan Ɓoye Miki ba nidai wannan auren nashi ya sanya na zubda makaman yaƙi na ada na yarda nai Laifi nai kuskure Kuma ina roƙon Allah ya yafe Mini Kuma duk ranar dana Koma zan nemi yafiyar Ammi data Aliyu akan abubuwan da Mukai Musu Sabida Nina san Ammi ba lallai ta Kuma barina da auren ɗanta ba a irin abin da kikai mata a yau, Sannan mama in danni kike Bin Mashirikai akan ganin bayan ƴar uwarki mai son ki da alkairi da Kuma Mijina daga yau ki dena Dan Allah mama zan zauna agida Ina roƙon gafarar Allah har zuwa sanda zanji matakin aurena da Aliyu"
Mami ta faɗa tana Kuka Tajira salati ta saka tana cewa.
"In sha Allahu Dana fita wajan Bokana ze duba Mini ke anya amina bata mallake Min keba Tabbas an sauya Miki tunani Mami ba yin kanki bane Kuma maganar Fita neman Nasara yanzu na fara ke baki san ciwon kanki ba"
Mami tabi mamanta da kallo tana mata addu'ar shiriya lallai wanda yayi nisa baya taɓa Jin kira iya wanda Allah yaso da rahma kaɗai yake ganar wa idan yay laifi ya gyara!

Ammi tai Kuka tai kuka a wannan rana na nadamar auren Aliyu da mami data haɗa daga ƙarshe ta Miƙe tana addu'ar Allah yayi mata tsari da sharrin tajira lallai ɗan adam abun tsoro ne wanda kai wa Alkairi ne ke Binka da zagon ƙasa.

Dukkan abin da ya faru akan Kunnen sakina............*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank, idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*A LOVE STORY 103*
Sabida tun Lokacin da Mami da Tajira suka shigo Gidan Sakina ta fito Ta tsaya a bakin Ƙofar Bedroom Ɗinta dama gidan ba kowa daga ita se Ammi Su Safna sun tafi makaranta, Sabida

haka Dukkan abin da ya faru acikin Kunnenta ya faru sedai ta kasa gane meke faruwa sabida bata da masaniya akan Dukkan abun da ya faru don batai kwanan Gidan ba bare ta sani Sabida haka Cikin sanyin Jiki wanda ta aro shi ta Saka a cikin yanayin ta taƙarasa Cikin Bedroom Ɗin Ammi bayan su tajira sun tafi waɗan da sam basu Lura da Sakina ba.

Ammi bata ƙaramin falon ta tana Bedroom sabida haka sakina seta zauna a falon Tana jiran Ammi wadda bayan ta idar da addu'ar Neman kariya daga sharrin tajira ta shiga toilet ta wanko Fuskarta datai jajir sabida Kuka ta fito falon se taga sakina a zaune Cikin Nutsuwa Ammi ta zauna sakina Kuma ta Matsa tana mata sannu da Fitowa.

"Ammi wai meke faruwa ne? duk na kasa samun Nutsuwa sabida naji Dukkan abun da ya faru keda Maman Mami Kuma banji daɗi ba duk da ban san meya ke faruwa ba, Amman idan tambayata ta ɓata Miki rai dan Allah Ki haƙuri sabida ba Hurumina bane ba"
Sakina ta kai maganar kamar gaske Ammi ta share sabon hawayen da ya zubo mata muryarta a shaƙe tace wa sakina.
"Ai ba maganar Hurumin ki koba Hurumin kiba sabida an haɗu an zama ɗaya abin da yayi sadiƙ shine yayi baba........
Tas ammi ta kwashe duk abin da akai ta gayawa sakina wanda bata nan akai abin

"Ammi Aliyu yayi aure batare da sanin kowa ba har matar nada Ciki?"
Sakina ta faɗa cikin zare idon mamaki.
"Haka ne sakina yanzu haka baba baya gida shida matar tashi"
Cewar Ammi tana share sabon hawayen ta sallamar Bashir ce ta katse Musu maganar wanda ya fito Cikin Shirin Komawa Abuja Suka gaisa da sakina wadda ta miƙe ta basu waje

Sakina sabida Murna rawa ta dinga yi a ɗakinta bayan ta koro su Hidaya falo ta ɗauki wayarta Numbern Bokanta ta kira bayan ya ɗauka ta ce masa.
"Ranka ya daɗe ina dawowa kuma na tarar da labari Biyu ɗaya mai daɗi ɗaya marar daɗi mai daɗin shine Ƙanin Mijin nawa yabar gida bayan yace yabar wa Mijina da mahaifiyar shi da ƴan uwan shi dukkan dukiyar shi sabida auren dayay a ɓoye wanda mahaifiyar taƙi aminta da matar wanda Labarin marar daɗi shine matar na ɗauke da juna Biyu"
Daga cikin wayar ya kece da dariyar Mugunta tare da cewa.
"Sauƙi ya samu kenan sabida haka ki maza Ki Kai layar nan Sabida zaki ji daɗin mallaka da ɗaure bakin Mijin ki tunda yanzu shine akan Komai da wannan damar zaku Raya kanku"
Sakina tai dariya tare da cewa.
"Ƙwarai kuwa wannan abu yayi Mini daɗi ba ɗan kaɗan ba wallahi yau ɗinnan zan fita da kaina asai da rai a nemo suna ai ba Komai bane ba a wajena"
Sallama sukai ta katse wayar Tana wata Irin dariya.
Wayar sadiƙ ta kira tace masa zata je Gidan su amman zata bar yara a wajan Ammi.
"Kin san ammi bata jin daɗi gasu safna basa gida dan Allah kada Ki jima"
Tace masa to seda aka idar da azahar sakina ta Nufi Gidan su mahaifiyarta tsohuwa tukuf Mutuniyar arziƙi tana kwance a tsakar Gidan su tana Shan iskar hanyar soro sakina tayi sallama

Suka gaisa.
"Ina jamila?"
Ta tambayi babar tasu wadda tsufa ya Cimmata dama mahaifinsu ya rasu Kuma Su uku ta haifa daga Anty babbar yayar su se Sakina se Jamila Ko kaɗan sakina batai halin mahaifiyarta ba dan Mahaifiyarta Mutuniyar arziƙi ce Ko kaɗan bata da hannu akan abun da sakina take yi, Ita ko Anty babbar yayar su ƴar abi yarima ce asha kiɗa kaf Cikin su bamai jin maganarta sabida talaka ce Maganar Sakina tafi ƙarfi a tsakanin su dan Hatta ita ma Antyn se abin da sakina tace Kuma duk abin da suka ce mata bata ja da tsayi kwantar da kai take taci arziƙi bambancin ɗaya ne ita bata Binsu Biye biyen su sedai In sunje Sun dawo su bata labari Dan jamila da sakina team Ɗin su guda ba'ajin kansu Shiyasa Anty yayar su ke Binsu sabida suna ɗan bata.
Hira suke tayi da mahaifiyarta wadda rabi Hirar faɗa da nasiha mahaifiyarta ke mata a fakaice har akai la'asar akai magariba duk sakina tana gidan su dama tana fashin sallah ana idar da sallar Isha'i tai wa mahaifiyarta sallama Lokacin Jamila ta dawo daga inda ta fita ita ta rakota har Titi Bayan sunyi sallama da jamila ta koma gida ita ko Sakina Hanyar sabuwar maƙabartar da aka Gina ake kai gawarwaki anan kusa dasu ta nufa Cikin Ikon Allah bakin maƙabartar babu kowa da jimawa sun taɓa wucewa ta wajan Lokacin sun zo sallah take tambayar sadiƙ shine yake ce mata sabuwar maƙabarta ce wannan Ne Tunanin daya faɗo mata harta Tuno maƙabartar shine tazo Ta buɗe Ƙofar shiga Ciki ta tsaya a kan kabarurrukan tana tunanin to ta yaya zata gano sabon kabari Duhu da kukan tsuntsaye ne a maƙabartar amman sam bata damu ba Ko ta saka tsoro aranta  sabida yadda idanunta suka Rufe da son Duniya Hango wani Kabari tayi mai Tudu da alamun sabuwar gawa ce aciki ganga ganga ta nufe shi sedai ta Ɗora ƙafa dan tai taku taji wata Gigitacciyar ƙara ta cika maƙabartar ga kuma wani irin Duhu daya mamaye mata idanunta ƙarar Kuma ta cika mata kunnenta ta cikin duhun take ganin wata irin halitta mai kama da jemage tana nufo ta Aguje sakina ta juya jikinta yana wata irin Tsuma gudu take Jikinta yana rawa da ƙyar ta Karasa gida tana Buɗe Ƙofar falon Ammi suka ci karo da sadiƙ wanda yake riƙe da key zeje ya zo da ita dan daya dawo ya tambayi ammi tace bata dawo ba yanayin da sadiƙ ya ganta abin ya bashi mamaki amman bai magana ba sabida yadda Sakina ta ture shi ta shiga ɗaki aguje tayi saman masai se Gudawa sadiƙ ya Bita yana tambayar lafiya? sedai Jiyo sautin Gudawar dayay a toilet yasa ya koma da baya yana zaton ita ta Korota Bayan ta fito zama tai har Lokacin bata dawo daidai ba layar ta mayar jaka ta kwanta..

A wannan dare sakina bata rintsa ba sabida daga ta rufe idanunta Wannan baƙin da halittar take gani suna Nufo ta Seta Miƙe tana Rawar Jiki ta Kutsa Cikin ƴaƴanta tana rungume su sedai ƙarar na Binta Har asubahi tana faman abu ɗaya gaba ɗaya se zabura take Ranar Ko falo bata iya fita ba ga ciwon kai daya sakata gaba kamar kanta ze rabe Biyu sedai duk da haka tunanin yadda zata sami Wata maƙabartar take Sedai Sadiƙ ya ɓata mata shirin ta sabida yace ta haɗa kaya Gobe zasu wuce lagos Tasan Kuma data tafi can ba fita take ba kuma ba Ko ina ta sani ba Amman dai haka ta haɗe kayan su Ta ƙudiri aniyar koma ta yaya ne zata san yadda tai da wannan layar sedai abin mamaki awannan daran ma tsorata da zabura sakina ta dinga yi dan abun har yafi na farko dan daga ta rufe idanunta gawarwaki take gani suna Biyota acikin Likkafani seta toshe baki tana Kuka dan gudu take tai ƙara asirin ta ya Tonu.

Washe gari Sukai sallama da kowa suka wuce lagos dan sadiƙ Ta gidansu sakina ya biya sukai

wa mahaifiyarta da jamila sallama Ya dubata kamar yadda sakina tace bata Jin daɗi ita ko babar sakina ta amsa sabida ta ɗauka Ko jikinta na Tsufa yake dubawa Haka suka Wuce Lagos Don gaba ɗaya sadiƙ yafi son yaje can dan ya Mayar da hankalin sa wajan kula da dukiyar ɗan uwan shi.

*KADUNA*

Yau sun sami bacci mai daɗi sabida Gidan sauron da suka ƙulla wanda ya basu kariya Wajan cizon sauron Gaba ɗaya Cikin dare Aliyu Ƙamƙame Farha yayi kamar ze mai da ita Cikin sa Haka sukai baccin su se asubahi Kiran sallah ya farkar da shi a hankali ya zare ta daga Jikinsa ya fita ya ɗaura alwala yazo ya tayar da ita dan itama tayi alwalar yau ya Ƙudiri aniyar seya tashi Mutan gidan sallah sabida ya lura kamar basa tashin asubah sabida haka Buga ƙofar ɗakin Inno yayi yace ta tashi tai sallah sannn yaje Jikin windown su shafa nan ma yace Wa mijinta ya tashi yayi sallah ya fita masallaci Bai dawo ba se wajan shiddan safe Lokacin farha ta Koma bacci Bakwai saura yayi wanka ya shirya bai tashe taba yayi tafiyar shi wajan aikin shi Alhamdulillahi bai sami matsala da kowa ba a wajan sema Girma da Mutunci da mutan wajan sukai ta bashi sedai rashin sabo da irin aikin ne yasa kafin Ya tashi wani Irin zazzaɓin gajiya ya rufe Shi Ƙarfe shidda aka sallame su bayan an basu Kuɗin su a hannu Haka ya tawo Gida duk jikinsa ya ɓaci da baƙin mai sabida ɗaukar ƙarafe.

Farha koda ta tashi bata ganshi ba tasan ya fita ne gyaran ɗaki tayi ta Ɗora abin karyawa ta gama ta zubawa Inno da shafa ta miƙa Musu suna ta Godiya ta haɗa wanke wanke Tayi ta share ɗaki ta ɗauko kayan sa Daya cire na jiya dana yau da nata ta fita ta wanke su ta shanya a tsakar gida suka zauna Inno ta fita dubiya Se ita da shafa wadda tai wake da shinkafa da manja da yaji ta zubawa farha wadda tace ba zata ciba Ran shafa ya ɓaci Sosai ganin haka yasa farha ta Ci waken Kuma yayi mata daɗi Hira suka Soma yi da shafa kamar dama can sun saba.
"Wallahi fatima naji daɗin zuwan ku sabida baban su baya son na shiga maƙota yanzu kuwa na sami ƴar tayin Hira"
Farha tayi dariya haka sukai ta Hirar su shafa tace.
"Na iya Kitso In naki ya tsufa Ki zo Nai Miki sabo Har da Ƙunshi sabida Kin san mazan yanzu se kana gyarawa Musamman Mijin ki na ga ɗan gayu Ne sekin da gaske"
Dariya suka sa tare da tafawa farha tace.
"Shiyasa nake Ririta abina Sabida ƴammatan yanzu"
Shafa tace.
"Ban Hanaki ba wallahi Ki gyara Ciki da waje yadda ze ƙara rikicewa ya gigice sabida Wasu matan da ƙyale ƙyale suke janye wa mazajen mu hankali Kalli hannuna da kaina Koda yaushe akwai Ƙunshi da kitso ga kuma ƙamshin Humra masu daɗi dana ke siya da kayan gyaran Jiki Duk da Mijina talaka ne ban bari kaina ya Kulle ba"
Farha ta fuskanci shafa sosai tare da cewa.
"To yanzu maman basma dame dame Ni ya kamata nai amfani dasu amman Ina da Juna Biyu"
Shafa tai Murmushi.
"Mace mai juna biyu ma ko batai Komai ba ita kanta Ni'ima ce dan yanzu Mijinki se yafi Jin

daɗin ki fiye da ko yaushe amman duk da haka Ki dinga shan Kayan marmari Irin su ayaba Kankana kwakwa Dabino ki markaɗa su ki zuba madarar ruwa kina sha,Koki dinga cinsu a haka Zasu saukar Miki da Ni'ima sosai ga cukwi da dabino da Kwakwa Ni gaskiya nafi amfani dasu akan cushe cushen kayan matan nan waɗanda ban san garantin suba amman kowa ce mace akwai ra'ayinta nidai nawa na gaya Miki Kuma Alhamdulillahi Mai gida yana yabawa sannan Ki dinga kama ruwa da ruwan Ɗumi In kin gama al'ada kuma ki dinga tafasa Samfarerar lalle da ganyan magarya Kina tace wa ki zuba a ƙaton baho Ki dinga zama aciki, sannan Kuma Ki dinga amfani da turaren ƙamshi na Jiki mai kama Lungu da saƙon Jikin ki dan namiji baya son ya kawo Jiki yaji wari Ki tabbatar da tsaftar shi da taki In kikai haka kika haɗa da Ladabi biyayya ƴar shagwaɓa Kirsa da saka ƙananun kaya to In sha Allah Kin siye zuciyar Oga"
Dan dariya farha harda ƙwalla! anan suka ɓata Lokaci Sallah kaɗai ke tayar dasu Har akai la'asar shafa ta Miƙe don ta Ɗora sanwar Dare Farha Kuma ta shiga ɗaki ta Ƙudiri zata dage wajan gyara Lungu da saƙo na Jikinta dan faranta ran Oganta.
Tana zaune tana azkar ya shigo yanayin sa ta kalla ta gane kamar baya Jin daɗi tayi masa barka da dawowa ya zauna yana cewa
"Washh fatima ya wunin dafatan dai Kinci abinci ko?"
Ta ɗaga masa kai tana kallon Shi idanunshi yayi ja sosai kamar mai ciwon Ido ga kayan duk sun ɓaci.
"Mai zan dafa maka abin da yasa ban maka girki ba sabida bamu da fulas Kuma nasan baka son abinci mai sanyi"
Ya kwanta yana cewa.
"Fatima bar abincin nan bana Jin daɗin Jikina"
Ya kwanta sosai yana Ɗora hannunshi saman ƙirjinshi.
"To kaci wani abun acan ne?"
Ta faɗa tana matsa mai ƙafafun sa ya Lumshe ido yana sakin Numfashi sabida ya gaji ga zazzaɓi ga ciwon kai tashi tayi ta ɗora masa ruwan wanka ta Juye masa a bokiti takai masa bayi.
"Ka daure kai wanka se a siyo magani"
Ta shi yayi ya fita wankan ta Bishi da jallabiyar shi Bakin bayin ta Miƙa masa Koda ya fito alwala yayi kayan daya cire ta jiƙa da Omo shi kuma ya fita masallaci.
Itama sallar tayi Tana zaune ya shigo da leda a hannun shi ya aje ya zauna yana Kwantar da kanshi a kafaɗunta.
Jikinsa zafi zau amman haka ya miƙe ya fita waje wajan kayan daya ga ta jiƙa ya Nufa ya sunkuya yana wanke wa dan in ya barta ita zata wanke bayan yaga wankin data sha jiya da wanda tai yau rabon shi wanki har ya manta amman haka ya tirje kayan tas ya shanya Yana Wanke Bokitin ta leƙo.
"Au wankin kayi Nifa zan yi kai da ba lafiya ba"
Yayi Murmushi suka shigo ɗakin gaba ɗaya hannun shi ya fashe Duk yayi jajir abin ka da ba'a saba ba kamar zatai kuka ta riƙe hannun

"Dan Allah ka dinga bari ina yi kalla fa hannun ka"
"Fatima ina tausaya Miki ƴar ƙarama dake Allah ya jarabce ki da abubuwa kala kala a gidan auren ki"

Hannu tasa ta toshe bakin ta.
"Kada ka kuma faɗin haka Kaji"
Ledar ya janyo kankana ya siyo se Biredi da kayan tea Shine yasha kankanar kaɗan dan yace kada tayi girki shi iya kankanar ta ishe shi Bayan sunyi sallar Isha'i suka kwanta tsakar dare zazzaɓin ya Rufe Shi sosai farha ta gigice ta riƙe shi gam tana kuka tana masa sannu xuwa asubahi ya sami bacci itama baccin tai dan bata san ma ya tashi ya fita ba se tashi tai taga baya nan.
Haka rayuwar taita tafiya Tun Aliyu yana zazzaɓin rashin sabo har ma yazo ya saba Suna rayuwar sune Cikin rufin asirin Allah dan duk inda ake Neman matar Rufin asiri farha takai ta wuce Don komai in ya kawo tattalawa take, Duk tsurfa irin ta mai ciki farha tana mugun kawaici da cewar yayi mata kaza ko Ya sai mata kaza in da tayi Lokacin suna da shi yanzu rayuwar ta sauya Tuni ya yankar mata kati a wani asibitin Kuɗi ƙarami anan take zuwa awo Inno ke rakata Suna zaman su lafiya da shafa haka Mijin shafa ashe rashin abinyi ke saka wa baya Biyan Inno Kuɗin haya sabida magini ne se kuma sanda Ginin ya faɗo seda Aliyu yasan yadda yayi ya samarwa Mijin shafa gyaran Mota anan Tashar da yake sabida shi ya iya gyaran Mota ranar su shafa kamar xasu ari baki dan Godiya Zaman su Yayi daɗi Cikin farha na daɗa Girma yana cikin wata na bakwai sedai in ka kalle shi zaka ce a ranar zata haihu sabida yadda cikin yayi Mugun Girma gaba ɗaya ta Koma ƴar ƙarama Se Girman ciki wanda idan ta zauna shima Cikin zama yake dan girma Ma Sha Allah.
Watan su Huɗu a kaduna sedai Koda Wasa Aliyu bai taɓa mancewa da Ammin sa ba Koda yaushe tana ran shi Wanda Lissafin Cikin farha ya kama wata na bakwai kenan.

*KANO*
Haka al'amura suke ta faruwa Ammi gaba ɗaya ta rame ta Koma wata iri Koda yaushe Likita yana kan zuwa duba Mata lafiyarta sabida Koda yau she jinin ta hawa yake Tun su sadiƙ na Mata Nasiha har sun Zuba,mata ido sadiƙ har kano ta zame masa Gida koda yaushe yana hanya sabida Jikin Ammi daya tsananta wanda Har Likita ya kafa dokoki akan dole seta cire damuwar ranta.
Koda yaushe kukan ta Ina baba ya shiga tayi nadamar abin da tai wa baba da matar shi.

Tun washe garin da mami ta koma gidan su Tajira.........*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*
*RABO YA RANTSE 104*
Ta shirya fita wajan Bokanta.
"Mama dan girman Allah ki haƙura da biye biyen nan mu Nemi yafiyar waɗanda muka zalunta har yanzu fa muna da sauran dama nidai babu ruwana Allah ma yasani in har danni zaki Fita wajan boka Akan ki cutar da rayukan da suka yi mana alkairi dan Allah mama ki bari sabida ni Jikina yana bani Ba lallai Na ƙara zama da Aliyu ba"
Tajira ta juyo a fusace.
"Dallah gafaracan matsa ki bani waje wadda bata san abun da take yi ba to in kin ga na aje makaman yaƙin yaƙar Amina da zuri'arta sedai kwana ne ya ƙare"
Ta figi mayafinta tabar gidan Hassana ƙanwar Mami tai murmushin takaici tare da cewa

"Aunty mami addu'a ce kawai mafitar mu Allah ya shirya mama danni ban ga amfanin Bin Bokayen nan ba basa ƙarar ka da komai se Cin kuɗi yanzu dai ki duba tsayin shekara Goma kuna abu ɗaya amman babu wani sauyi Da aka gani daga ƙarshe ma dai Jiba yayi auren shi tuni har matar nada Ciki inda duba gaskiya ne mai yasa ba'a gano muku ba sabida haka abin da Allah yaso kaɗai yake bayyanawa bawan sa Amman abin da ya ɓoye babu wanda ya isa ya gano shi"
Hassana ta faɗa a nutse.
Mami taja ajiyar zuciya.
"Nidai Har ga Allah na tuba wallahi ba zan kuma kai ƙafata wajan wasu mashirikai ba laifin dana ɗauka ma Zanje na nemi yafiyar su Ammi amman yanzu kam wani tsoron Allah ne ke yawo adukkan sassan Jikina in Allah ya baka bamai hanaka in Allah ya hanaka babu mai baka Ya rabbi Mun tuba"
Wuni sukai suna tattaunawa Ita da Hassana sabida Hussaina ta fita makaranta Itama tana dawowa suka ɗora Kuma dukkan su Sunyi Allah wadai da halin Mahaifiyar su.
Tun suna sa ran dawowarta har suka rufe gida dan ba baƙon ta bane kwana a wajan Bokayen ta.

Tajira cikin wani ƙauye dake jahar katsina wajan Bokanta taje wanda tai Imanin Aikin shine yaci sanda Aliyu ze auri Mami Ta sami damar ganin Bokan wanda ya haɗa mata Mugayen ayyuka wanda daga ciki harda haukata Farha matar Ali sabida tace base da lafiya zatai rayuwar auren ba sannan Ita kuma Ammi a sakar mata Cutar shanyewar Jiki Aliyu Kuma a birkita masa tunanin sa ya zama baya daji ko gani se Mami a duniya waɗannan zafafan ayyukan aka haɗowa tajira ta zube masa manyan Kuɗi Ta kamo hanyar gida tare da sharaɗin nan da kwana uku sheɗanun da Bokan ze tura Jikin su zasu fara aikin sedai ya bata wani baƙin magani yace ta saka A kusurwa uku ta Farha data Ammi data Aliyu wanda shine kan Aikin Kuma yace lallai ta saka wannan magani in ta kuskura to aikin ze juya kanta

Sedai a hanyar dawowar ta Allah yayi Ikon sa akan motar su wadda ta ɗebo mutane daga wannan ƙauye zuwa kano wata ƙatuwar Motar katako tabi takan Motar tasu wanda motar ta gangara Gefen hanya Mutanan ciki duk sun sami raunika Wanda Har da tajira acikin waɗanda suka sami Rauni wanda nata yafi Na kowa shahara dan ta karye a cinyarta Ƙashin kwankwasonta ya ɓalle Kanta ya fashe da ƙyar aka haɗa wayarta data yashe can Ƙasa aka kira Numbern da aka gani acikin wayar tata. ALLAH KENAN!

wajan ƙarfe Ukun Dare wayar Hassana ta fara Ringing wadda ta manta Bata kashe taba.
Cikin magagin bacci ta ɗaga wayar Muryar wani namiji ce yace.
"Da Allah da Hassana Muke magana?"
Hassana ta watsake tare da cewa.
"Nice"
Se yace mata.
"Mun sami Numberki a wayar wata mata naga kece ƙarshen Kiranta to bamu san dai halaƙar ku

ba Sabida bata hayyacinta Motar su ta sami hatsari ne a tsakanin Hanyar dawowa katsina zuwa kano yanzu dai Mun samu an saka su a wata motar Muka tawo dasu babban asibitin murtala dake Cikin kano yanzu haka muna sashin ƴan gaggawa"
Wayar ce ta Mutu hassana ta ɗora hannu aka tana cewa.
"Innalillahi wa'innah ilaihirraju'un mama kin jawa kanki Babu wa'azin da Aunty mami batai Miki ba Amman kika Murje dama in baka godewa Allah akan Ni'imar saba zaka godewa azabarsa"
Maganganun Hassana ne suka tada mami da sauran ƴan uwan haka suka fita da ƙyar suka ƙarasa Asibitin dan akwai tazara tsakanin fagge zuwa asibitin Murtala sabida dare ne babu abin hawa Koda suka je asibitin ma seda suka sami ɗan sanda sannan suka sami ganin tajira wadda sam bata gane Kowa Mami kuka tasa a haka suka zauna har asubahi taimakon gaggawa aka bawa tajira Wanda ta samu ta dawo hayyacinta sedai Likita ya tabbatar wa su mami sedai su ɗauketa su kaita asibitin ƙashi ai mata Hotuna a wajan data samu rauni kan Mota suka samu aka sakata zuwa babban asibitin ƙashi dake Dala Iya kuɗin Hoton Cinyar Tajira dana kwankwasonta seda ya saka mami ƙaramin hauka dan basu da wannan Kuɗi duk bokaye sun cinye Musu kuɗaɗan su hatta Motar da Aliyu ya sai Musu sun siyar basu da komai se Gidan da suke Ciki se ɗan Kuɗin Cin abinci Suna kuka suka mayar da ita Mota tana wata Irin ƙara sabida da an taɓa mata jikinta ji take kamar zata mutu dan azaba.

Zubawa sarautar Allah ido sukai akan lamarin tajira dan basu da hanyar Kuɗin hotunan ta bare aje ga batun aiki Kashi da fitsari a kwance take dan tun da suka dawo Gida ko zama bata iya yi. Abin al'ajabi da mamaki bayan kwana uku Tajira ta soma wani Irin Gurnani tana Ihu tana zabure zabure Ga shi gaba ɗaya Ko wace Gaɓa ta Jikinta ta dena aiki Sedai taita ihun tana zabura amman babu damar tashi Kafin sati tajira har haushin kare yi take tana wata irin dariya tana xare ido maƙota na shigowa dubata Tuni magana ta cika unguwa kowa da fassarar da yake ganin haka yasa su mami suka dena Buɗe Gidan su Kuma suna Koƙarin gyara mahaifiyarsu sedai fa a tsorace suke mata Komai dan Gudu suke kada ta musu Illah.
Yau da gobe se Allah gaba ɗaya rayuwa ta sauyawa su mami duk kayan mami dana tajira na alfarma masu kyau haka ta kwashe ta siyar saboda suci abinci damma su Hassana na Koyarwa da wannan suke Ganɗawa su sami na abinci rayuwa ta sauyawa tajira Da iyalanta Kullum gidan kamar na makoki duk ƙawayen tajira sun janye ƙafarsu sun dena zuwa Inda take Tana son magana amman babu dama sabida bakinta ya shanye ga wani yawu da yake zubo mata mai Mugun Ɗoyi bada ban ɗanka ɗanka bane babu yadda za'ai ka iya zama da tajira na minti Goma amman haka Ƴaƴanta ke hidima da ita a hankali Mami itama ciwo ya soma Cinta Koda taje asibiti aka duba ta aka tabbatar mata da mahaifarta ce ta soma Ruɓewa sedai a yanke mata gaba ɗaya Mami tayi Kuka ta gode Allah ranar da wani ƙanin mahaifinsu yazo duba tajira yaga mami tana cikin ciwo seya tausaya mata Shine ya tafi da ita wani asibitin Kuɗi mai kyau anan akai mata aikin aka cire mahaifar ya biya Kuɗin harda na magani mami tai kuka tai kuka shikenan ita ba zata Kuma haihuwa ba aduniya bayan ta dawo Gida still dai ciwon Bai daina ba ta kira ɗan uwan mahaifin nasu a waya shine yazo da wani malamin addini yace Kona Islamic za'a gwada Koda malamin yazo ya kalli mami kawai yayi murmushi yace mata ze mata tofi a zamzam Kafin taci Komai kullum ta fara sha yace sheɗanu ne Suka taɓa mata mahaifar tata inda ba'ai gaggawar Cire mata mahaifar bama da zata iya Gamuwa da babbar Illah.

Mami ta kalli malamin tace masa.
"Malam mun aikata laifuka a baya nida mahaifiyata kuma ni abin ya dameni...........
Tas ta kwashe komai ta gaya masa malamin ya jinjina Abin da su mami sukai amman bai Nuna mata ba.
"Kya iya zuwa ki nemi yafiyar waɗanda Kika zalinta tinda suna raye sannan Ki nemawa mahaifiyarki tunda ita bata da bakin magana Ita kinga taka maimai ma ba'a san abun da yake damunta ba amman kodan gaba kada Ki ƙara bawa maganar Boka gaskiya bare har ki aiki da abin da zece Miki sabida aljanun da suke turawa bama su amana bane In suka je gurin wanda aka tura su basu sami nasara ba to dawowa suke Jikin Wanda ya tura sun su masa Illah dan babu Ko tamtama ciwon mahaifiyarki nada nasaba dasu harma da ciwon dake marar ki amman sha Allah kina shan wannan Tofin zakiji daɗi"
Mami ta fashe da kuka.
"Malam ni nafi zaton Koma sune suka lalata min mahaifata ya Allah na tuba"
Malamin yace.
"Allah masanin gaibu koma dai meye Ki godewa Allah zaki ƙarasa rayuwarki cikin yarda da tabbatuwa da tuba ga Allah ki duba mahaifiyarki mana Ki gani ita ba'a ma san ta ina matsalarta take ba"
Shawarwari ya bata suka musu sallama suka tafi mami ta dage wajan shan zamzam ɗin Kuma Alhamdulillahi tana jin daɗi Kuma tana godiya ga Allah daya sa a haka sakamakonta ya tsaya wanda ya ƙara tsoratar da ita tare da gudun zalunci ko cutarwa ga wani dan ta tabbata hakki ne yake bibiyar su.
Haka rayuwar ta cigaba tsayin wata Huɗu tajira tana cikin Jinya dan mami kam ta warke ras Ciwon ta ɗaya in ta tuna da an yanke mata mahaifarta wannan kan sakata kuka dan ɗa rahma ne koga su yadda suke Hidima da mahaifiyar su, wadda ta rame tai baƙi Fuskarta kamar gawayi Ta koma fiyau kamar ba tajira ba lallai Duniya abar tsoro ce.

LAGOS.
Cikin damuwa sadiƙ daya haɗa kayan sa ze tawo kano sabida yanayin jikin ammi wanda har takai ga tana kwance a asibiti ne salma tayo masa waya safiyar yau ya dubi sakina wadda duk ta koma kamar tsakuwa se rama take tana baƙi sabida wannan tsoratar da take fama da ita Kimanin watanni Huɗu tun sanda taje maƙabarta kai laya da aka firgitata har yanzu bata daina tsoratar ba Kullum dare bata iya bacci ita kaɗai tasan a wani hali take Ciki.
"Zan tafi kano ban san Lokacin dawowa taba sabida Jikin Ammi daya takura ta"
Tai kamar zata ɗora hannu aka tai kuka.
"Abban su dan Allah ka tafi dani"
Ya kalleta sabida shima kanshi yanayin nata yana bashi mamaki gaba ɗaya ta koma wata iri duk ta susuce daidai da Girki bata yi sedai Kullum su fita cin abinci Yaƴanta bata gyarasu Shima kanshi rabon data bashi haƙƙin sa tun Suna kano abin dai se Godiyar Allah.
"Sakina wai me yake damunki dan Allah ki gaya min amman bazaki kano ba sabida makarantar yara"
Sakina ta daki kanta da ƙarfi sabida wani abu mai kama da Kiyashi dake Bin kanta yana yawo

kamar tsutsa aciki ta fara sosa Jikinta.
"Babu komai Hmm babu komai"
Ta faɗa tana maimaita magana ɗaya sadiƙ yayi mata sallama sabida Jirgi zebi ya baro Gidan Koda ya fita daga Gidan se sakina ta ɗauki wayarta ta kira jamila tana roƙonta akan tazo kodan kula da yara Jamila tai dariya.
"Haba yaya sakina ai Kifi yana ganin ka mai jar Koma! tun ranar da Mukaje wajan wannan Mutumin naji dukkan abun da kuka ƙulla ashe Ba don Allah kike so na auri Aliyu ba dan ki samu ajikina ne Ki amfani dani dan ki cika Burin ki Nikam yaya tsoronki nake sabida wannan layar da Kika amsa ba mamaki In kika rasa gawar da zaki sakawa Ki Zuban guba nasha na Mutu ki sami Gawar da zaki cusa layar aciki dan yadda idanunki ya rufe ason duniya ba abin da ba zaki ba Ni yanzu yaya na nutsu yanzu haka maganar aurena ta taso Ni na yarda dake ashe Ke da wata manufar taki ta daban akaina wato Ke ƴaƴanki da Mijinki kaɗai Kika sani wallahi yaya kin bani mamaki"
Sakina tasa kuka.
"Wallahi Ni kaina ban san ina layar take ba jamila kema tsayin wata huɗu ta yaya zan ajeta har sekin zo na saka Miki Ni na san abin da yake damuna wato tunda naje maƙabarta kai layar nai gamo se firgita nake Kullum bana iya bacci ƴar uwata kizo Ki Tayani Kula da ƴaƴana"
Jamila tai dariya.
"Yaya sakina an fa kai Kuɗin aurena tun bayan tawowarki dama ina da wanda yake sona Yadda Kika dage sena auri Ali ne yasa nake ta zabga masa wulaƙanci to Allah ya nunan manufarki sena bawa mai sona dama yanzu haka shirin aure nake Nina hana kowa ya gaya Miki wato Ni na ƙare a bauta Miki keda ƴaƴanki kada nai aure ai Firgita da bala'i yanzu kika fara gani tunda kin kasa gane Cewar Allah ɗaya yake bai da abokin tarayya Nikam In sha Allah na dena zuwa wajan Kowa zanyi aurena na cigaba da istigifari babu ni'imar da Allah bai Miki ba amman ke kin raina wannan Ni'imar taki ta wanin ki kike hange wanda wani Irin takin yake nema bai samu ba lallai kin ɗaura ƙafa da masifa Tunda baki yarda da Allah ba"
Jamila tana gama faɗa mata hakan ta kashe wayarta tana tsaki domin tun sanda suka je wajan wannan Boka da jamila taji maganarsu lokacin da ta fita waya taji Komai ya sire mata lallai mutum bai da tabbas.
Sakina tai Kuka har ta gaji haka ta aje wayar sedai tun bayan tawowar sadiƙ take wasu irin Muggan mafarkai wanda abin har yakai ga tana ganin wata irin halitta mai kama da ƙadangaru manya baƙaƙe a zahiri sosai sakina take Firgita ita kaɗai taita sosa jikinta daga yaranta sun zo inda take ta rufe su da duka ga ƙananun zance ita kaɗai taita magana tana dariya kaɗan kaɗan abun na sakina fa se du'ai.
*KANO*

Autar manya ce marubuciyar......
*ƁOYAYYAR ƘAUNA*
*BA SON TA NAKE BA*
*ƊAN MAJALISSA*
*MURADIN ZUCIYA*
*ASHE ZUMA*
*TAURARO*

*KOBA SO*
*RABON WANI*
*FITAR RABO*
*DA IZZATA*
*BAƘON LAMARI*
*AUREN BARE*
*H A S K E*
*ZUMA A BAKI*
*BAƘAR FATA*
*RABO YA RANTSE*

*RABO YA RANTSE! littafin kuɗi ne 500 naira zuwa  wannan asusun bankin 0078174806 Sterling bank,  idan kuma kati ne mtn card na 500 hoton sa za'a ɗauka a turo,shaidar biya 09022260850*

*RABO YA RANTSE 105*
Duk yadda sadiƙ yake zaton yanayin Jikin Ammi abin ya wuce tunanin sa sabida gaba ɗaya Jikin nata ya rikice bata da magana se ta akira mata Baba kada ta mutu bata nemi yafiyar shiba wannan tasa Likita yace a dena zuwa wajan ta aka barta ita kaɗai a ɗakin se Likitan dake zuwa dubata dan koda yaushe Jininta baya sauka ga ciwon kai mai tsanani dan bata yin bacci ganin haka yasa Sadiƙ yaje ya shaidawa ƴan uwanta da kuma dangin mahaifinsu ƴan cikin Gida ranar asibitin ya cika da ƴan uwa Sosai su Baba Usman sukaiwa sadiƙ faɗan mai yasa bai gaya musu abin da  yake faruwa ba nan da nan Baba Usman yasa aka fara roƙon Allah akan Allah ya juyo da hankalin Aliyu gida a duk inda yake sannan ya sa aka sallami Ammi daga asibitin Gida suka dawo aka fara rubuce mata alkur'ani ana wanke mata da ruwan sama tana sha waraka ne ga dukkan damuwa ko ciwo ko wata matsala Cikin Amincin Allah ta fara dawowa daidai Jikin nata ya soma sauƙi Ammi kuka ta sanya tana roƙon gafarar su Baba Usman suma Kuma haka suka nemi gafararta Suka shirya kamar ba su taɓa Yin gaba ba zaman su yay daɗi dan koda yaushe Ilahirin zuri'ar cikin gida suna wajan Ammi suna Kula da ita Dan tuni baba usman yace wa salma ta koma gidanta Umma suwaiba ce ta dawo Gidan sabida ta dinga ɗebe wa Ammi kewa ga kuma su Hajja dama ance Shi ɗan adam rana gare shi Kuma Alhamdulillahi a wannan karon dangin mahaifin su Aliyu sun nuna bajintar su domin sunyi zumunci akan matsalar Ammi da kuma tafiyar Aliyu dan har masallatai Baba Usman yakai Barar addu'a akan a taya su da addu'a Allah ya juyo da hankalin ɗansa Gida.

Acikin wannan ƙadamin Iyayen Kamal suka zo wajan Baba usman akan maganar auren safna wanda ada mahaifiyar kamal taso ta dakatar dashi ta hanashi auren safna sabida akwai wadda taso ta bashi Amman yadda yake son safna yasa mahaifiyar shi ta amince masa akan ya aure ta ɗin tare dayi Musu fatan alkairi haka aka kawo kuɗi da saka ranar safna da kamal watanni Biyar masu zuwa

Al'amarin soyayyar Sajeeda da Nura abin Kullum gaba yake daga wajan ta amman ta Rufe ba

wanda ta sanarwa addu'a take wanda ita ce ta zama garkuwanta don sosai take Komai kan hankalinta tana jin Nutsuwa na saukar mata tare  da neman zaɓin Allah akan lamarin Domin haka mahaifiyarsu ta koyar dasu akan Komai nasu su nemi zaɓin Ubangiji.

Kimanin sati Guda da faruwar Komai yau da safe Jikin Ammi ya motsa Wanda gaba ɗaya kowa ma ya karaya da ita dan se Neman gafarar kowa take sadiƙ daya haɗa kaya ze Koma lagos se Zama yayi ya sakata a gaba yana Kuka zuwa yanzu Ji yake inda yasan inda Aliyu yake daya Je yazo wa Ammi dashi dan ya shaida wata irin soyayya ce a tsakanin ta da Aliyu Zamzam Baba usman ya ɗauko yana tofa mata addu'a aciki ya bata tasha wanda anan ta samu bacci.

ALIYU
Gaba ɗaya Aliyu jinsa yake wani iri acikin waɗannan Lokuta sanyin Jiki da faɗuwar gaba sun sako shi a gaba Tun farha na tambayar shi har Tai masa shuru dan itama ta kanta take yi.
Yau tunda ya tashi yaƙi ma fita Aiki ba wadda yake son gani se Ammin sa kawai seya tashi yahau haɗa kayan su Seda ya haɗe kaf sannan yace wa farha.
Ta tashi su tafi kano ta kalle shi tare da cewa.
"Kamar yaya Kano kuma nidai gaskiya ba zan iya doguwar tafiya da wannan cikin ba"
A fusace ya kalleta.
"In ba zaki tafi ba seki zauna Ni mahaifiyata nasan tana buƙatata a wannan Lokacin Jin Garin nan nake kamar wuta"
Dama addu'a ai bata faɗuwa ƙasa yadda ƴan uwanshi da Mahaifiyar shi suke addu'a Allah ya juyo da hankalin shi gida ne yasa yaji kadunan tai masa zafi.
Farha taji takaicin wannan magana daya yaɓa mata wato ya mayar da ita sakarai.
"Nima ƴan uwana da mahaifana suna buƙatar ganina  dan haka kona koma kano ba zan zauna Kamar da ba wallahi a wannan karon Sedai ai wadda za'ai Koka sake ni Koka Sama min Gidan da zanzauna cikin ƴan cina dan ba zan Kuma Irin zaman danai a baya ba na gaji ni ma ƴace kamar Kowa kuma mace kamar kowa"
Bai kula taba dan ya fuskanci a sama take ya saɓi kayan a kafaɗar shi Suka fita dan jaraba ko wanka babu wanda yayi acikin su daga Inno har su shafa basu Ji daɗin wannan tafiya ba dan Inno harda Kukan ta Aliyu yace su kwashe kayan abincin da komai da suka rage Kuma ze waiwaye su komin Bajima komin ba daɗe haka Suka rabu duk babu daɗi dama bahaushe yace sabo turken wawa suna zuwa tasha suka sami Motar kano Haka suka shiga ya biya Kuɗin Mota tafiya sukai har zuwa garin kano gaba ɗaya ƙafafun farha sun Kumbura Duk ciwo suke mata Har suka sauka Da ƙyar take taka ƙafafun Napep ya samu sukai tsada zuwa gida bayan ya zuba musu kayan su acikin napep ɗin farha ta Tsaya taƙi shiga napep Ɗin a wahalce ya juyo ya kalleta sabida Shima ba ƙaramar gajiya yayi ba.
"Fatima muje mana"
Ta juya fuskarta wadda ta haɗe ta tamau tace.
"Ni gidanmu zani danni ma mahaifana suna Buƙatar ganina Rabon umma dani Har wata nawa dan haka kowa yayi Gidan su kafin asan abin yi dan ba zan ƙara zaman rashin ƴan ciba wallahi in ada nayi haƙuri yanzu ba zan iya ba"
Ta faɗa da iyakacin gaskiyarta.
"To shikenan Indai ni nake riƙe da igiyoyin auren ki ban amince Kije gidan kuba In kuma kika je

keda Allah ai seki bari muje Gidan Ammin tukunna kiga wace irin karɓa zasu yi Miki kafin ki Ɗauki mataki Kuma ke ai sheda ce tunda can ban yarda an taka mutuncin kiba"
Kuka tasa tana cewa.
"Dan kawai kana aure na seka haɗa ni da Allah bayan kasan tsoron sa ze hanani tafiya gidanmu nidai na cuci kaina dana zaɓi auren ka"
Murmushin takaici yayi bai iya magana ba Ya shiga napep Ɗin haka ta shigo itama tana ta Kuka ya sassauta Muryar shi.
"Dan Allah fatima ki shuru kinga a condition ɗin da kike ki rufa mana asiri ki haihu lafiya"
Da ire iren maganganun nan yayta kwantar mata da hankalinta har ya samu ta dena Kukan se ajiyar zuciya ya kama hannunta ya riƙe tare da cewa.
"Inna Cutar dake Allah baze barni ba haka zalika inna juya Miki baya Na zama butulu fatima ba irin wannan zuwan nake so kiyi wa mahaifan kiba Duba duk kin rame Kinyi duhu kowa ya ganki yasan bakya cikin kwanciyar hankali Na fison ki zuwan da kowa ze sha'awarki mahaifan ki suyi alfahari da aurena da kikai dan Allah ki Nutsu mubi komai a sannu"
Ko kula shi ma tayi banza tai masa dan zafin Ammi take Ji sosai dan se yanzu ma take ƙara tuno Cin mutuncin data sha wajan Ammi a zamanta.
Har Bakin gate mai napep ɗin ya dire su Ya sallame shi ya shiga sauko Musu da kayan su Hohoho Masu gadi Ma'aikatan gida Ihu suka sa suna Wa Aliyu barka da zuwa dan basu da labarin Dalilin tafiyar shi sudai sun san sunyi Missing Uban gida nagari mai tausayi da Jinƙai Kayan nasu Suka amsa suka Nufi Cikin Gida gaba ɗaya Falon Ammi cike yake sabida yadda Jikin nata yau se a hankali ganin ana shigo da kaya yasa Bashir daya zo Shima daga abuja yake tambayar su na menene kafin ya rufe bakin sa Aliyu ya turo Ƙofar falon hannunshi Riƙe dana farha wadda da ƙyar take taka ƙafafunta.

Ai Ammi dake kwance kanta yana saman Pillow tana hango Aliyu ta miƙe a guje ta Nufesu su dukan ta haɗe ta rungume seta fashe da kuka tana cewa.
"Baba ina ka shiga baba da tuni na Mutu baka tare dani nayi nadamar abin da nai Muku fatima ki yafe Mini na tuba"
Seta hau kuka wanda duk dauriyar Aliyu shima kukan ya saka farha ma Kukan take seda ƙyar aka rarrashe su Suka ƙaraso falon Hannun Ammi cikin na Aliyu yau ciwo ya ƙare Su sadiƙ se farin Ciki Shikam Aliyu Yana ta kallon ammi duk ta rame tai duhu Se sannu take wa farha kamar zata mayar da farha cikinta wanda nan da nan tausayin Ammin ya rufe farha nan fa aka shiga mayar da zancen abin da ya faru bayan basa nan Cutar Ammi ta ɗagawa Aliyu hankali se kallonta yake Yafiyar farha Ammi ta nema wadda tace ba Komai ai ita mahaifiyace a wajan ta sabida haka Komai ya wuce Har dare falon yana cike shidai Aliyu zamewa yayi ya tafi yayi wanka bai shigo ba se wajan taran dare Lokacin mutane sun ragu kowa ya kama gabansa farha tana can gadon Ammi tana baccin gajiya bayan tai wanka an bata sabbin kaya ta sanya.
Ammi da kanta ta haɗawa Aliyu abinci ranar ciwo ya ƙare seda ya gama cin abincin sannan take sheda masa mami bata nan mahaifiyarta tazo ta tafi da ita sedai in ya huta yaje ya dawo da ita.
Aliyu yayi Murmushin takaici.
"Ammi kawai mami tai zamanta Na sake ta saki Biyu dan na kama mami da tarin laifuka kafin nabar Gidannan kona zauna da ita ma akwai zargi Sabida dumu dumu na kama ta da laifin

Yunƙurin kasheki ta hanyar zuba Miki magani agirki Kuma ban tabbatar ba seda na kamata da manyan Hujjoji wanda ni ban san dalilin ƙudirin hakan gare taba"
Ammi ta share hawaye nan take gaya masa Dukkan abun da ya faru wanda tajira tazo tai mata agida Tsaki yaja yana Allah wadai da wasu mutanan to mai wani ya isa yayi maka In ba Allah ba.
Ya jima suna hira da Ammi wanda washe gari yacewa Ammi ta shirya suje har gidansu mami ya miƙa mata takardar sakin nata tare da bayyana dalilin sa na sakin a gaban mahaifiyarta Sedai koda suka je Gidan su mami yadda suka ga tajira abin babu daɗi se ɗagawa Ammi hannu take amman ba damar Neman yafiyarta.
Mami ta bawa Ammi tausayi dama shi Aliyu tunda ya bata takardar ta ya bayyana mata laifukan ta wanda bata Musa ba ta saka Kuka tana neman yafiyar shi yace ya yafe mata Allah ya yafe masu gaba ɗaya ya fita Ko kallon ɗakin da tajira take beyi ba Ammi da tunanin tajira ta dawo Gida seta ƙara Jin tsoron Allah lallai Mutum ba abakin Komai yake ba.

Kuma a ranar Sadiƙ ya gabatarwa Aliyu riba da ci gaban da kamfanin nikan shi suka samu bayan baya nan Aliyu kuma bai ƙasa a gwiwa ba wajan tara ƴan uwan shi a wannan rana ya sheda cewa ya mallakawa Sadiƙ kamfanin shi na Lagos halak har abada ya mallakawa Bashir kamfanin shi na Abuja har abada shi Kuma ze mayar da hankali ana kano da wanda ze Buɗe a garin kaduna dan mutan kaduna sun zame masa dangi Ranar Ammi tai Kukan daɗi sadiƙ Kuwa yama kasa magana haka Bashir bayan gama Murna Aliyu ya kuma yiwa Bashir albishir da yaje ya Nemi auren Hanan ƴar Gidan Alhaji hamishi wadda yace se a haɗe dana Safna Bashir yayi Godiya sosai haka taron ƴan uwan ya tashi Cikin farin ciki.
Wata irin kulawa Ammi take bawa farha tun farha na jin kunyar Ammi har ta ware ta mayarta kamar umma dan shagwaɓa take zubawa Ammi wadda Komai tace Aliyu ya sauya na ɓangaran shi in farha ta haihu seta tare acan dan haka sabbin gyara aka soma yiwa part Ɗin Aliyu Daidai da sutturar farha ammi ta bawa masu aiki sabbin kaya aka ɗinka mata akwati akwati masu kyau da tsada Su safna Sun Haɗe kai da farha sun koma ƴan ukun Ammi.

Musa daya zo Aliyu ya karɓi wayar shi ya kunna tarin saƙonni Yayta bi Haka yaje Gidan gwamna ya sheda ya dawo dan sadiƙ ya gaya masa sunje Sun bada Uzirin yayi tafiya har gidan su farha seda yaje anan Su kawu sukai ta masa Godiya da mamaki ya kalli Musa bayan sun fito yake tambayar shi bayan baya nan ana aika masu da saƙo ne Musa yace Shiya ɗauki nauyi Aliyu yay wa Musa Godiya sosai Nan fa harkokin Aliyu da tafiye tafiyen sa suka dawo acikin satin Ya aika Musa kaduna dan ya Fara duba in da zasu siya su gina kamfanin su ma acan.
Sadiƙ ya koma lagos sedai yadda yaga sakina fa abin babu  sauƙi nan Minal babbar ƴarsa ke gaya masa abin da maman su take lokacin da baya nan Abin ya ɗagawa sadiƙ hankali dan washe gari suka dawo kano Gidan su sakina ya wuce Ya sanarwa da mahaifiyarta dan sosai sakina hauka take da sumbatu jamila ce ta warware wa sadiƙ Komai na abin da Sakina ta aikata sadiƙ yayi Takaicin abin ya kalleta yace.
"Mai na rage ki dashi sakina gashi nan kin ɓata rayuwarki a banza abin da Kike so Gashi na samu dan Aliyu ya mallakamin kamfanin sa cikin sauƙi bayan Kin fita daga hankalin ki sakina Kin cuci kanki Kuma ni sadiƙ na sake Ki Saki ɗaya kuma ba zan bar Miki yarana ba"
Ya kwashe ƴaƴansa suka bar gidan sakina se dariya take Suna fita Jamila ta samo mota ta saka

sakina sukai dawanau gidan mahaukata dan tace ba zata barta agida ba ta kashe su haka kawai Mahaifiyar sakina tai takaici da halin ƴar tata haka jamila takai sakina gidan mahaukata aka bata ɗaki guda dan A soma duba ƙwaƙwalwarta dan hauka take Tuburan tana Tone tonen asiri.

Sadiƙ duk yadda yaso seda yay Kuka sanda yake shedawa Ammi abin da yake faruwa Ammi ta tafa hannu tana cewa.
"Lallai Mutum mugun icce sakina tabani mamaki dama abin da ka shuka shi kake Girba Allah ya zaɓa maka tagari wadda zata riƙe maka yaranka yanzu Ka huta zuciyarka tai sanyi kafin ka koma lagos ka bar Min yaran a gabana kafin muga abin da Allah ze mana"
Nan take bashi labarin su tajira ma Sadiƙ yaji labarin tajira da Kuma abin da ya gani akan sakina ya ɗaga masa hankali Kuma ya ƙara Jin tsoron Allah aran shi.

Wayyo Allah Kaine mai iko akan kowa zuwa wannan Lokaci abin ya ƙazanta ga tajira dan takai tana ɗoyi tsutsa tana fita daga gabanta kwanan ta Biyu cikin wannan hali rai yayi halin sa an Mutu da Mugun Nufi arai Allah ka rabamu da irin ƙarshen su tajira Babu wani taro da akai haka tsirarun Mutane suka kaita Gidanmu na gaskiya aka gama addu'a aka watse su tajira an gama na duniya sauran nacan.

Seda akai kwana bakwai mami ta kira ammi ta sheda mata Ammi batai ƙasa a gwiwa ba wajan saka salma dasu safna a gaba suka Je gaisuwa harda abin arziƙinta takai Musu mami se Godiya take.
Sadiƙ ya koma lagos.
Cikin Farha nata Girma kullum Aliyu na Kuncin taƙi Zuwa inda yake ai tasan yana buƙatarta Ita ko dan rashin Kunya taje wajan Miji da wannan ƙaton cikin ta Tsallake mahaifiyar shi Dan haka tai masa banza duk da ba haram bane hakan amman ai da kunya.

Bayan wata biyu farha ta tashi da naƙuda wadda Nan da nan Ammi tasa aka ɗauko Mota suka tafi asibiti basu Jima da zuwa ba Allah ya sauketa lafiya ta haifo yaranta mace da namiji masu kama da Aliyu sak kafin kace me asibitin ya cika da ƴan uwa Aliyu da yaje kaduna dan Buɗe kamfanin shi albishir da Salma tai masa ba sanya yayo Gida yabar Komai wajan Dini wanda ya taimaka masa ya sami aiki a tasha to shi Aliyu ya Nema akan Harkokin kamfanin nashi na kaduna kuma ya ɗora shi a babban matsayi a kamfanin.
Zo kaga murna wajan Aliyu duka ya haɗe yaran nashi yana Musu addu'a yana farin ciki da yake bata sha wahala ba nan da nan aka sallamo su suka dawo Gida Ammi ta haɗa ruwa da kanta taiwa Farha wanka ta gyarata tsaf Aliyu se kallon farha yake yanzu da kanta ta haifa masa waɗannan manyan yaran kyawawa.
Musa ya aika gidan su farha aka sanar wanda Yaya sadiya da Nafisa da Umman zage yayar umma dasu babarsu Hadiza suka shigo Motar Musa suka tawo Gidan farha Hoho Duniya da duniya se a wannan Rana su Yaya sadiya suka san wa farha ke aure ashe Hasken matasa take aure wanda A kamfanin sa ma su Halifa suke aiki.
Sun sami karramawa daga wajan Ammi da su safna Farha kuwa harda Kukan murna ta rungume yaya sadiya wadda ta saki baki tana kallon farha Su yaya sadiya na gidan farha ta

Koma sashin ta ashe basu ga komai ba domin sashin farha se ka rantse ba a ƙasar nan aka tsara shiba Umman zage aka bar mata su Kuma suka tafi Gida da labarin mijin da farha ta aura da kuma Duniyar alatun da suka gano.
Umman zage kewa farha wanka da yara wanda Koda yaushe se farha tai kuka in za'a mata wanka Umman zage taita tsokanarta Aliyu Kullum yana rungume da yaran shi yana kallon su yana jin farin ciki aran shi haka aka gudanar da taron suna gagarumi yara sunci Suna Amina ( Ammani ) da Abdullah ( Dady ) haka akai taro lafiya aka gama lafiya Se bayan suna umma tazo shima da ƙyar Su yaya sadiya suka takura tazo dan koda tazo a part Ɗin Ammi ta sauka Hmm zoku ga soyayya wajan farha da Umma dan ɗane jikin umma farha tai tana Sangarta kala kala Shikam Aliyu koda yazo gaida Umma yaga yadda farha tai abin ya bashi mamaki duk yadda yake zaton farha ta wuce nan.

Yara nata girma dan suna samin kulawa ta kowane ɓangare kwanaki arba'in umman zage tayi tanawa farha wanka wanda Aliyu ya mata gagarumar kyauta sanda zata tafi Hajja ce ta dawo ɓangaran dan ta taya farha raino da ƙyar yabarta taje Gida tai kwana Uku yadda taga an sauya gidansu tai murna taiwa Aliyu fatan alkairi taji ya ƙara ƙima a idanunta ashe haka ya kyautatawa mahaifanta kaji masu yi domin Allah amman bai taɓa gaya mata ba seda suka ƙulle da Umma ma take ƙara gaya mata abubuwan da yake musu tace wallahi Umma bai taɓa gaya Mini ba lallai ma Abban su ba Komai.
Ta zaga gidan yayinta kaf dan haka ta ɗauki Ikram sukai ta ziyara Wanda Aliyu yayta Mitar tana fitar masa da yara suna shan rana in yayi waya dasu har Gidan su Shema'u ƙawarta taje anci dariya ba ƴar kaɗan ba da suka Tuno aikin su na gidan radio Shema'u ta bawa farha labarin zuwan musa gidan su Farha ta bawa shema'u labarin komai har auren da sukai da Aliyu bayan ta bata Numbern wayarta suka baro Gidan su shema''u gida daɗi kamar kada su baro gida haka suka dawo washe garin data dawo Aliyu ya ɗauke ta da yara sukai kaduna abin mamaki ya bata dan ya gyarawa Inno Gidanta har mai aiki ya ɗaukar mata Ya kuma saiwa Mijin shafa gida ɗan ƙarami anan Kusa da na inno kuma ya ɗauke shi aiki a kamfanin sa nacan agidan Inno suka kwana cikin Ac da haske dan ya gyarawa Inno Gidanta ya sauya mata Komai washe gari sukai sallama da Inno da su shafa ta kamfanin sa nacan suka biya suka gaisa da dini ta zaga kamfanin Sosai sannan suka kamo hanyar kano tana Jinjina halaccin Aliyu wato Shi baya manta alkairi sabida duk waɗanda suka taimaka masa a kaduna seda ya koma ya taimake su.

Bayan sun dawo Gida ta kafa masa nacin maganar Mami wanda se Lokacin ya gaya mata Halin da ake Ciki tai Kuka dan bata ji daɗin rabuwar suba haka ta kafa masa nacin ya kaita gidan su mami ba dan yaso ba yakai ta wuni tai agidan su mami wadda bata Ɓoyewa farha Komai ba farha ta tausayawa mami haka suka wuni da daddare yazo ɗaukar su Tana masa ƙorafin halin da Mami da ƴan uwanta suke ciki yana mita yana Komai haka dai yasa Musa yakai Musu Kuɗi da kayan abinci kuma tunda ga nan Duk ƙarshen wata yana sawa akai Musu.
Mami nata wa Farha godiya a waya farha tace mata ba komai.
Rayuwa na tafiya bikin su safna yana ƙaratowa sajeeda ganin zata cutu ne yasa ta gayawa farha halin da take Ciki akan Nura kuma ta roƙi alfarma da ta taimaka mata akan shawo kan shi farha tai dariya tace ta kwana gidan sauƙi aikuwa ta kira Yaya Nura wanda tuni Aliyu ya sauya masa wajan aiki yana kaduna bayan ya sami ƙarin girma shaida masa tai halin da ƙanwar

Mijinta ke ciki akan shi ashe shima tunda yaga sajeeda sanda suka je da Su Ammi kullum tana manne aran shi kawai gani yake kamar tafi ƙarfin shine Cikin Lokaci kaɗan Soyayya ta Kullu a tsakanin Su Wanda ba jimawa manya suka shiga maganar babar su Hadiza murna take nura ze auro ƙanwar Mijin farha itama ikram maganar aurenta da Salim tai ƙarfi sosai dan Lefe za'a kawo ma Bashir yaje Gidan su Hanan tuni sun sasanta Kansu Har an kai Kuɗin aure da saka rana.

Cikin wannan Lokacin akai Bikin jamila ƙanwar sakina wanda bayan auren nata ta sami Kira daga dawanau cewa Jikin ƴar uwarta ya tsananta naka nakane haka jamila da Mijinta suka ɗauko sakina yadda suka ganta abin babu sauƙi ta haukace Hauka take Tuburan agidanta ta ajeta sedai kwanan sakina Biyu ta rasu waya jamila taiwa sadiƙ washe gari yazo kano Ya ɗauki Aliyu suka je wajan ta'aziyya sannan yakai yaran sakina se Kuka suke har dare suna can Kafin su dawo Gida washe gari shema'u tazo wajan farha sun Fito farha zata rakata sadiƙ yaga shema"u bai wani yi Ɓoye Ɓoye ba yacewa farka surukata naga ƙawarki in ba wani ni ina ciki farha tai Murna sosai kafin sadiƙ ya koma akai maganar auren shi da shema'u ana bakwan sakina sadiƙ ya koma Lagos.
Shirin auren sadiƙ da shema'u Safna da kamal sajeeda da nura Bashir da hanan ya kankama kowani ɓangare Shiri ake dan Gidan su Farha Nura da Ikram za'a haɗa shiyasa Duk farha ta zama Busy ga kuma shirin Buɗe ƙatuwar Plaza wadda Aliyu yayo mata order kayayyakin sawa irin su dogayen riguna  da takalma  harda kayan jarirai dan ta dinga sai dawa Sunan Plazar fatiman Ali plaza tana nan kan babban Titin Hotoro anan ya buɗe mata ya zuba mata ma'aikata mata don su dinga taimakon ta to shirin Buɗe plazar da Kuma shirin Bikin da zasu yi duk ya sakata ta zama se a hankali dan hatta su Ammani watsar dasu take wajan Ammi Tun ubansu na mita har ya gaji damma yaran akwai haƙuri.
Alhamdulillahi anyi bukunkunan lafiya an kai amare gidajen su anyi shagali na ban mamaki dan hatta shafa seda tazo daga Kaduna ita da Inno haka zalika Mami ma da su Hassana sun zo dan farha seda takai Musu katin Biki har Gida a sabuwar motar daya bata wadda ya koya mata da yake tana da ƙwaƙwalwa tuni ta Iya ta ƙware a tuƙi dan da ita ta dinga shige da ficen Biki.
Farha tai rawar gani sosai dan ita taiwa Ikram komai wanda uwa da uba keyi sannan ta haɗawa Nura Lefe duk kuma a lalitar Oga Aliyu kuɗin suka fita Babar su Hadiza ta dinga wa farha Godiya kamar zata ari baki.

Mami ta sami Miji wani bawan Allah anan maƙotan su matar ce ta rasu da yaransa Biyu Har gida ta kawowa Ammi da farha katin Biki Kuma sunje harda abin arziƙin su anan Gidan su ta zauna sabida ƙannen ta waɗanda suma duk sun sami mazajen aure Shirin Bikin su ake kuma farha tace Aliyu ya taimaka yayi Musu kayan gado Bai Musa ba yace yadda kika ce haka za'ai ƴar amanata.

Rayuwa mai sauyi komai ya sauya a rayuwar farha wadda ta koma Babbar Mace Dan Allah ya sawa kasuwancin ta albarka Tana taimako sosai da wannan sana'a tata wadda nan da nan Sunan plazar ta yay suna a kano sabida yadda kayanta keda sauƙi da aminci.
Aliyu nata mitar taƙi yiwa su Ammani ƙanne shifa Seya ƙaro aure dariya take in taji ya faɗi wannan magana dan tasan ita kaɗai ce amarya uwar gida a gare shi.

Yanzu haka su Ammani nada shekara biyu suna Gudunsu ko ina haka ya ɗebe su harda Umma da kawu Da hajja suka Nufi makka dan suyi aikin hajji sabida yayi wa hajja alƙwari Kuma Allah bai yiba sabida tafiyar dayay kaduna.
Ita dai farha taje umara har sau biyu se kuma makkan daya kaisu a wannan Lokacin haka sukai aikin Hajjin su suka dawo Gida lafiya.
Bayan shekara shidda farha ta sake haifar yara Biyu duka maza Safna da ta haihu sajeeda ta haihu shema'u da suka haɗe kai da farha itama ta haifi ɗa namiji kuma ta riƙe ƴaƴan sadiƙ tsakaninta da Allah Hanan ma ta haifi Ɗanta namiji Wadda Itama Gidanta ke Abuja Ikram ma ta haihu dan seda ta haihu farha ta iya zuwa gidanta sabida kunyar salim wanda bai ko nuna mata wani abu ko a fuska ba, Anyi auren su ruƙayya Haka zalika anyi auren ƙannen mami.
Rayuwa na tafiya abubuwa masu daɗi da marasa daɗi Sun faru domin Inno ta rasu Haka zalika kawu ma ya rasu Se Cigaban da Aliyu ya ƙara samu dan koda mai Girma gwamna ya sauka daga kujerar dayay shekaru takwas ta zarce akan ta, jam'iyya tai masa tayin koze tsaya takarar gwamna seda yay shawara da Ammi da farha sannan ya amince aka fara yawon yaƙin neman Takarar Kujerar wadda Cikin Hukuncin Allah bayan kaɗa ƙuri'oin dubban jama'ar dake jahar kano Allah mai kowa da komai ya bawa Alhaji Aliyu Abdullahi Madaki nasarar lashe zaɓan Zama Cikakken gwamnan kano.
Anyi murna anyi shagali haka su farha sukai ƙaura zuwa gidan gwamnati Mulki yake cike da adalci da jin ƙan talakawa Farha An zama first lady abin se Godiyar Allah dama dukkan wanda yay haƙuri a rayuwa yana tare da nasara.
*ALHAMDULILLAHI*
Nan na kawo ƙarshen Littafina mai suna *RABO YA RANTSE*
wanda na fara saki da rubuta shi on 22 august na kuma kammala shi a on 10 act 2023 abin da nayi daidai Allah ya bani ladan shi kuskuren danai kuma Ya Allah ka yafe mini.
Waɗanda suka ɓatan a wannan tafiya na yafe muku waɗanda na ɓatawa a wannan tafiya nima su yafe mini Allah ya yafe mana gaba ɗayanmu ina roƙon ku da kuyi aiki da abu mai kyau da darasi da saƙon alkairi na wannan Littafi Kuyi watsi dana dukkan sharrin ciki.
Godiyata ga Allah maɗaukakin sarki daya bani rai lafiya kwanciyar hankali basira hazaƙar Rubutu nagode maka Allah baka taɓa gajiya da dukkan lamurana ba nagode Maka Ya rabbi!
Godiya  ga tarin masoyana mabiyana masu Jimirin bina Ya Allah ka sakawa dukkan wadda ta sanya Kuɗinta tasai wannan Littafi nawa da dubun alkairinka.
Godiya ga ƴan private Allah ya biya Muku buƙatunku na alkairi.
Godiya ga ƴan paid grp Allah ya biya Muku buƙatun ku na alkairi.

Se mun a haɗu a wani sabon  kuma da ikon Allah.......   *09022260850*

Autar manya ce marubuciyar......
*ƁOYAYYAR ƘAUNA*
*BA SON TA NAKE BA*
*ƊAN MAJALISSA*
*MURADIN ZUCIYA*
*ASHE ZUMA*

*TAURARO*
*KOBA SO*
*RABON WANI*
*FITAR RABO*
*DA IZZATA*
*BAƘON LAMARI*
*AUREN BARE*
*H A S K E*
*ZUMA A BAKI*
*BAƘAR FATA*
*RABO YA RANTSE*